*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

*FREE BOOK*

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

_Bisimillahir Rahamanir Rahim dukkan yabo da godiya su tabbata ga ALLAH madaukakin sarki tsira da amincin ALLAH su ƙara tabbata ga shugaban halitta cikamakin annabawan ALLAH, annabin farko annabin ƙarshe shugaba jagaba annabi muhammad s.a.w Amin…._

_My fans yauma gani tafe da sabon littafi mai suna a sama da fatan zaku biyoni domin jin yadda labarin nawa ke tafe! labarin nawa ƙirƙirarre ne banyi domin cin zarafin wani ko wata ba duk wanda yaga yayi dai dai da tasa rayuwa tofa akasi aka samu._

_Labarin nawa ne nina tsara abina kuma na rubuta shi banyarda wani ko wata su juyamin shi ta kowace sigaba ba NAGODE_

*001*

_GARIN KANO UNGUWAR SHARAƊA_

Yammaci ne mai ɗauke da wani irin lullumi mai dadɗin gaske, hadarine yaketa faman haɗowa kota ina garin yay wani irin luf har wani duhune ke kawo kai, sabida yadda garin yagama gamewa da wannan hadarin, ƴan matane, guda uku suna tafe kowacce hannunta riƙe da bokiti mai ruwan garai wanda hausawa ke masa laƙabi da ɗan ballasa.
Seda na ƙarasa gabansu sannan idanuna ya ganemin ashe ba kansu ɗaya ba, domin farar cikinsu itace mai ƙiba amman ba canba tana da cikar halitta irin ta ɗiya mace, kallo guda zaka mata kagane ƙarancin shekarunta domin daga gani bazata haura shekaru goma sha shidda a duniya ba, se ragowar biyun suma sunada haske amman dai basu kai wannan ɗin ba, sukam kallo ɗaya zaka musu kagane ƴan biyune sabida yadda suke tsananin kama da juna, waɗanda bazasu haura shekaru goma sha takwas aduniya ba, kuma kana kallonsu kasan sun girmewa wannan farar sedai kuma daga ganinsu kaga jini ɗaya sabida tsananin kamar dasuke da ita, abin da zata fisu shine girman jiki da cikar halitta gami da hasken fata.
Ɗaya daga cikin ƴan biyun ce ta dubi wannan farar yarinyar tare da cewa "Haba Bebi! bakya ganin yamma tayi sosai yakamata mu koma gida hakan nan dan ALLAH kinsan halin mama da ruɗewa wallahi nasan yanzu haka tana ƙofar gida tana faman zagaye". Takai maganar tana

kallon ɗayar wadda batai magana ba tare da cewa "Koba haka ba hassana?" tafaɗa tana kallonta,cafkewa hassanar tai tare da jan tsaki! kaɗan"Bebi kiwa ALLAH ki rabu da bin ƴan bashin nan mutafi gida ai gobe ma ranace, wallahi mu dukke kike jamana ana ƙin sayan awararmu sabida jarabar faɗanki" takai maganar cikin ƙufula. wannan farar yarinyar wadda ita nake tunanin itace bebin ita ta dubesu cikin fitsara kana tace"Nifa karku uzzuramin wallahi saina koma na amsowa mama kuɗinta aini ba baiwar ubansu bace" takai maganar tana huci kamar taci gudu, wadda aka kira da hassana ita tai rau-rau da idanunta"Dan ALLAH bebi kiyi haƙuri mutafi nai miki alƙawari gobe zan karɓi kuɗin da kaina". wani kallo bebi ta watsa musu tare da dire bokitin hannunta batama tsaya jiraba ta arta aguje, ko nauyin jikinta bata ji.
Baki ɗaya baki da hanci su hassana suka saki suna kallon yadda ƙanwar tasu ke gudu amman babu yadda zasuyi sabida halin bebi se ita bata tsoron kowa ko kaɗan bebi bata da kunya ga faɗan tsiya da taurin kai da mita, ganin an soma ruwa kaɗan kaɗan yasa suka ƙara sauri, domin nufar gida sedai cikin zuciyarsu tsorone fall na yadda basu san halin da bebi zata shiga a hanya ba.
Cikin wani irin zafin nama take gudun baki ɗaya tagama jigata kanta harseda takai dai-dai jection ɗin sharaɗa kai da ƙafa, sannan taja ta tsaya ta huta, lokacin ruwan harya soma saukowa, hijabin jikinta ta cire tare da ɗaurawa a ƙuguntа, baki ɗaya manyan breast ɗinta waɗanda suka zame mata kaya, masu bata tsananin haushi duk sun fito waje, ta saman rigarta amman haka ta kurmutsa cikin kan dakalin da matasan samarin ke zaune cikin zafin nama da masifa ta dubi ɗan baƙin cikinsu "Kai siba dallah kabani dari biyun awarata idan ba haka ba wallahi zamu kwashi ƴan kallo anan wajan dakai" takai maganar tana riƙo ƙugunta tare da jijjiga jikinta wanda ya baiwa albarkatun kirjinta damar kaɗawa kamar da gayya wanda ita ko kaɗan batai wannan tunanin ba, wanda aka kira da siba ne ya taso daga cikin samarin yana ɗan shafa gemunsa tare da lasar ƙasan lip's ɗinsa kaɗan yana binta da wani mayen kallo, wanda kafin ya furta wani abu ruwan dake zuba kaɗan ya kece da ƙarfi, cikin tsananin zalama yake dubanta"idan har kika bari na taɓa nan" ya nuna saman kirjinta,"Nikuma zan baki ninkin kuɗinki, amman idan kika saka taurin kai na cinye kuɗin inga uban daya isa ya karɓa miki" yakai maganar yana dariya wadda baki  ɗaya mazan wajan suka haɗe baki wajan sakin ta suna mara masa baya kamar da gayya, cikin tsananin ƙufula bebi ta dubeshi "Kai! dakata gaja da kai dawani ƙazamin hannunka mai datti kakeson taɓa min jikina lallai da uwarka ta haifi mai yankakken hannu kuwa" takai maganar tana mayar da hijabinta jikinta, dariya ya saki kana ya kai hannunsa dai dai wajan wuyan hijabinta wanda tunma kafin ya ɗago hannun yaji saukar mari! tas!tas!!tas!!, har sau uku, baki ɗaya idanunta ya juye ya koma kamar banata ba"Dan uwarka dan ubanka shege bunsuru jikina yafi ƙarfin gaja irin........" bata ƙarasaba taji saukar yatsunsa a fuskarta, kafin ta ɗago taji muryar okasha yana magana"Haba baba kafayi kwafsi tayaya zaka bari mace taga weak ɗinka haba dallah wuce kabarta da yawarta" yafaɗa yana watsa mata kallon banza, sam bebi tama kasa furta komai illa maganar siba wadda ke cike da borin kunya ta karaɗe mata kunnenta"hakane fa oka bara nabar wannan wawiyar wadda bata da arabi bare boko ƴar matsiyata masu gidan buhu, ƴan makarantar tallah........." yafaɗa yana bin bayan okashat abokinsa, tsaye suka bar beby wadda tai saƙare kamar doluwa still kuma ruwan yana kuma zuba ajikinta su basu bata  kuɗin bashin taba gashi kuma sun barta da dukan ruwa.
Wata ƙwallar takaici ta saki wadda takejin zuciyarta na mata suya kamar zata faso ta fito abinda

tun tasowar ta bata yarda dashi ba kenan kuka! sam bebi bata yarda tai kuka akan abu sabida tsabar kafar kanta tare da yawan faɗanta, jan ƙafafunta tai tare da barin wajan tanajin yadda ruwan sama ke sauka ajikinta.
Kanta tsaye sharaɗa police station ta nufa dukkan kayan jikinta suna ɗigar da ruwa domin sun riga da sun jiƙe jagaf da wani ɗan sanda taci karo ɗan gajere baki, yana ganinta ya washe baki yaga ƴar fara kyakykyawa"A,a madam lafiya na ganki cikin ruwan nan?" yafaɗa yana ɗan matsowa gabanta, da baya taja kaɗan tana ayyana yadda wasu mazan suke hali kamar na kwartaye, kana ta dubeshi"Officer na kawo ƙara ne akan ina son abimin haƙƙina" yadda ta kame kanta tana kora masa bayani seka rantse babbar macece mai hankali, seda ta gama yi masa bayanin duk yadda sukai dasu siba hatta marin daya mata bata ɓoye masa ba sabida tun asalinta ita bamai yawan ƙarya bace, sannan ta ɗora da cewar"idan da hali officer ina son ku ɗauko mota aje na nuna muku har inda yake domin a karɓar min naira ɗari biyuta". takai maganar da iyakar gaskiyarta, wata iriyar dariya officern ya kece da ita, da kallo ya bita yana nazarin ko ta samu taɓin hankali sedai kuma tsaf take babu alamun ƙazanta ko rashin hankali agareta, dai dai ta nutsuwar sa, yay tare da ɗan haɗe ransa kaɗan"Ke yanzu ƙanwata idan banda abinki haka ake kawo ƙara wama yace miki muna aiki da kane?" ya jefa mata tambayar yana kallonta tsaki! taja kaɗan tare da ɗan sharce ruwan daya zubo mata saman fuskarta"Kaga ni daman wajan shugaban wajan nan nazo idan bazaka tai makamin na karbo mana kuɗinmu ba kaban wuri kawai malam ruwa yana faman jiƙani" tafaɗa tana murguɗa masa baki, haɓa officer ya kama sannan yace"To muje naga wasu tsagerun samarin ne base kin shiga cikiba sabida ba kowa ne ze fahimce kiba", babu musu bebi taja ƙafarta suka jera da officer seda takai har kan dakalin ƴar rumfar dasu siba ke ciki sannan taja ta tsaya tana nunawa officer siba, wanda yaketa faman zaro idanu tamkar yay ma sarki ƙarya.
"Officer wannan ne kadai san bayanin dana maka tun acan ko?" tafaɗa tana makawa siba harara, da kallo officer yabi siba tare da ce masa "Kai kuwa abokina tayaya zakaci kuɗinta na sana,arta kaƙi bata abin kuma yakai ga cin zarafi harda mari?" yafaɗa cikin sigar tambaya, duk ruwan da ake bai hana siba sharce gumi ba wato duk jarabar yarinyar nan da ake faɗa masa bai taɓa tabbatarwa ba se yau, inda yasan akan ɗari biyunta zata kaishi ƙara ai da tuni anwuce wajan ya bata abinta, basar da tunanin yay kana ya ɗago "Officer ai min aikin gafara Bebi kiyi haƙuri insha ALLAHU hakan baze kuma faruwa ba, gama 500 nan wallahi ki riƙe duka" yafaɗa cikin sauri kana ya zaro sabuwar ɗari biyar daga pocket ɗinsa wanda daman can iya shege ne yasa ya hanatan, wani watsatstsen kallo ta watsa masa tare da murguɗa bakinta gaba"Ni ai bana buƙatar kuɗin ƴan tasha haƙƙina kaɗai zaka bani na kama gabana nasan inda dare yay min" tafaɗa tare da kauda kanta gefe, mamakine ya kama ƴan wajan harshi kansa officer sannan ya dube ta,"Haba ke kuwa an miki alkhairi ai kya amsa ko?"........wawan kallo ta masa tare da cewa"officer na gode da taimako kaga siba bani ɗari biyu ta nai gaba bana son ɓata lokaci". a wajan okashatu siba ya amshi ɗari biyun ya bata hannunsa na rawa, bata tsaya kallon kowa na wajan ba bare taiwa officer godiya taja jikinta tabar wajan, har taje titi ruwan bai bar dukantaba....................

*AUTAR MANYA*👉👈

_LITTAFIN KYAUTA NE BANA SAIDA WA BA AMMAN RASHIN COMMENT ZE SAKA YA KOMA NA KUƊI, INA MATA MASU SON A TALLA MUSU HAJARSU, ZASU IYA NEMANA TA WATSAP NUMBER TA_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*002*

Tsaye tayi abakin titin ruwan yana kuma jiƙa mata jikinta, ganin yamma tana kumayi magariba tana kawo kai, yasa ta yanke shawarar bita lunguna, hakance ta faru ta lunguna tabi har zuwa cikin layinsu wanda yake da tazara sosai a tsakaninsu da wajan dasuke kai awarar.
Nufar bakin wani ɗan ƙaramin gida tayi wanda katangar gidan take ƴar ƙarama domin batafi taku uku ba, yaye labulan buhun da aka rufe ƙofar gidan dashi tayi, tare da ɗanyi ƙasa da kanta gudun bugewa domin tsayinta yaywa. ƙofar kaɗan, karo sukaci da wani ɗan matashin namiji wanda baifi shekaru goma sha bakwai ba, kallo ɗaya zaka masa ka gane shiɗin yayanta ne, da kallo ya bita"Kedai kinji kunya wallahi kullum cikin saka mama a damuwa kike, to yanzu ma wai daga gidan ubanwa kike, kin ɗagawa kowa hankali?" yafaɗa yana kawo mata hannu kamar ze bugeta, da gudu tai baya tana watsa masa harara" wai kai shahid ɗin nan meya ruwanka dani ne kuɗin awarar uwata akacinye shine naje nabi bashin tunda ƴan biyu su baxasu iya ba".......,"Seke tsagera?" yafaɗa yana zabga mata harara, bata bi takansa ba tai cikin gidan, shima sabida yasan bazata raga masa ba yasa yay wajan gawayin sa dayake saidawa acan bayan layinsu.

Wani ɗan mitsitsin tsakar gida ta shiga tare da fara kiran "Mama! mama!! mama!!!, kina ina ga ƴar albarkarki ta iso" tafaɗa da ƙarfi tare da tsayawa ƙyam a tsakar gidan batare data shiga ɗakinsu ba.
Cikin sauri wata farar mace tas ta fito daga cikin ɗakin dayake ƙwaya ɗaya tall acikin gidan, kallo ɗaya zaka mata kagane ita ɗin mai kyauce kuma mahaifiya ga bebi domin ga kama nan kamar an tsaga kara,da sauri ta ƙaraso gabanta tare da riƙo hannunta tajata zuwa cikin ɗakin data fito daga cikinsa , wanda yake shinfiɗe da ledar, tsakar ɗaki tare da ƙatuwar kafita se sip ta kaya, ƴan biyu suna zaune akan katifar suna kallo a ƴar wayar mama, se arfa da ihsan a gefe suna cin taliya, suna shiga ta saki hannunta tare da haɗe ranta kaɗan "Yanzu bebi kullum sekin ɓata min raina kike jin dadi?" tafaɗa muryarta tana karkarwa, da kallo bebi.
tabi mama tare da cewa"Mama kuɗin awararmu fa na tsaya na amsar mana idan kuma ƙarya nake gobe muje dake wajansu"girgiza kai mama tayi tare da cewa"Bana son jin ba,asi kullum ina gaya miki cewar duk wanda yaci awarar nan bai baku kuɗi ba to ku barshi da ALLAH, ke mace ce bebi bana son wannan faɗace-faɗacen naki sabida baki san bakin wani ba".dira ƙafafunta tafara a ƙasa tana ƙoƙarin sakin kukan shagwaɓa, "Haba mama idan nabar musu kuɗin dame zamu dinga cin abinci wallahi mama indai akan haƙƙina ne se inda ƙarfina ya ƙare", da kallo mama ta bita tana mamakin halin ƴar tata, sam batayo halin kowa na gidanba, mama bata ƙara shan mamakin bebi,
ba seda ta zayyane mata yadda sukai har zuwa wajan ƴan sandan datayi sannan ta fito da ɗari biyun data amso ta miƙa mata sannan tai rau rau da idanunta"Mama dan ALLAH kibani ɗari aciki anjima na siyo nama wallahi miyauna har tsinkewa yake sabida ƙwaɗayi". cikin mamaki mama tace"Kice zuwa kikai wajan maza kika nuna rashin tarbiya harda tube hijabi wato haka na baku tarbiya?,haka kikaga ƴan uwanki sunayi BILKISU soki ke kijamin maganar dangin ubanku ko?, dasuka zuba mana ido suga gudun ruwanmu?" tafaɗa tana kokarin kai mata hannu, da baya tai waje tana furta"Mama bazan kuma ba" tana yarfe hannayenta.
Zama mama tayi a bakin katifa tare da kallon ƴan biyu dasukai tsuru batare dasun cigaba da kallon da sukeba suna sauraran dramar bebi da mama, suna kuma tsoron suyi magana tai musu rashin kunya.
"Ya salam ni Aishatu ALLAH ka kawomin sauƙi cikin lamuran wannan yarinya, na haifeki ban haifi halinki ba" ta faɗa a fili, hassana ce ta dubi mama, tare da ɗan matsowa gabanta kaɗan bayan ta taso daga kwanciyar datayi, dafa hannun mama tayi tare da cewa.
"Mama kiyi haƙuri haƙiƙa Bebi tana buƙatar addu'arki, ta uwa mama ki ɗora akan wadda kike insha Allahu babu abinda ze faru se alkairi".
Tafaɗa cikin nutsuwa, ɗan murmushi mama ta saki, kaɗan tare da kallon hassana tana yaba irin baiwa tare da hankali irin ta ƴan biyun, nata, kana tace.
"Hakane Allah ya rufa asiri". daga haka ta miƙe ta fita zuwa tsakar gidan tsugunne taga Bebi, ga ruwan yanata faman dukan jikinta, sabida da yaɗan tsagaita amman yanzu ya dawo da ƙarfinsa, ruwan taɗan sharce daga fuskarta, wanda yake faman zubowa tamkar da bakin ƙwarya, itama mama duk yabi ya jiƙa mata jikinta.
"Watakam so kike ki sakani cacar siyan maganin zazzaɓi ko Bebi?" tafaɗa tana kallonta.
Cikin tsoron dukan mama Bebi ta ɗago idanuwanta da suka firfito tare da cewa"Dan Allah mama kada ki dakeni, wallahi yunwa nakeji rabona da abinci tun safe". tausayin Bebi ne ya kama mama.

Da kallo tabi ƴar ta'ta tare da cewa.......
"Bazan miki komai ba bebi maza ki tashi ki shiga cikin ƴan uwanki, amman ki tuɓe kayan jikin naki tukunna".
Mama ta faɗa tare da shiga cikin wani ɗan ƙaramin kicin wanda baze ɗauki mutum biyu ba, ko mutum ɗayan nema seyay da gaske, irinsu bebi masu ƙiba kuwa ma yay musu kaɗan.

Cikin rawar ɗari Bebi ta ƙarasa cikin ɗakin nasu harara! ta watsawa hussaina wadda take baje a katifa tana kallo, sannan ta bugawa su ihsan tsawa! "Dalla ku rufe idanuwan ku zan tube kayana".
Cikin sauri yaran suka rintse idanuwansu, janyo marufin sip ɗinsu tayi tare da kare rabin jikinta, sannan ta tube kayan jikin nata waɗanda sukai sharkaf har ɗiga suke.
Ko ɗaɗɗiyar atamfa riga da zani ta ɗauko wadda da ƙyar ta saka rigar sannan ta ɗaura zani ajikinta wanda kayan ya sami damar kama mata jiki ɗam ɗam.
Hijabi ta ɗauka ta saka sannan ta ɗebe kayan data cire ta fita waje, igiya taje ta shanya duk da ruwan har yanxu yana sauka.
Bayan ta kammala ta nufi cikin ɗan madai daicin banɗakinsu wanda yake wanke ƙar ƙar, kama ruwa tayi tare da fitowa ta dauro alwala, shiga ɗakin ta kumayi ta shinfiɗa sallaya tare da tayar da sallar la'asar wadda ta makare mata.
Bayan ta idar ko hijabin bata cire ba tayi waje lokacin an ɗauke ruwan dan duk su hassana suna tsakar gidan har sun gyara shi sun goge ruwan daya jiƙa tsakar gidan.
Duk suna zaune hussaina tana tankaɗen garin tuwan dare wanda shahid ke fita dashi can cikin kasuwar sharaɗa kai da ƙafa.
Hassana kuma tana daka kayan miya danginsu daddawa da sauransu, ihsan wadda bazata wuce shekaru goma sha biyu ba, tana faman wanke ƴan kwanika a bakin rariya.
Kanta tsaye ƙofar kicin ta nufa tare da tsayawa"Mama abani abinci yunwa nakeji".
Juyowa mama tayi duk fuskarta tagama haɗewa da gumin haƙayin itacen dayabi ya addabi kicin ɗin, ni kaina seda nabi fuskar mamansu bebi da kallo sabida yadda take da tsananin kyau ɗan gaske farace jajur kamar ka taɓa jini ya fito sedai kuma wahala ta saka duk jan maman ya du sashe sedai kuma tsantsar kyanta ɗan gaske! har yanzu yana nan bai gushe ba.
"To Bebi baki ga yanzu nake kici-kicin na haɗa ruɗen tuwan ba?, ai kya jira na gama ko?".
Zaro idanu Bebi tayi waje wanda hakan yake acikin al'adar rayuwarta muddin zatai magana seta zaro su duka waje, sannan ta haɗe ranta tamau kamar kace mata kat! ta fashe, sannan ta soma magana muryarta tana rawa kamar zatayi kuka!.
"Mama yunwa nakeji wallahi tun safe dana sha koko har yanzu ban kuma kai mai ɗumi cikina ba".
Ta ƙarasa maganar tana zubo da hawaye! shaaaaaaaa, kamar famfom.
Mama bata kula Bebin ba illa cigaban datayi da tuƙa ruɗenta harta kammala sannan ta fito waje ta wuce Bebi wadda take ta faman kukan yunwa.
Abakin ƴar tabarmar da su hassana ke kai mama ta xauna sannan ta ɗan ɗaga murya kaɗan.
"Wai ke! Yaushe zaki hankaline?, Nace yaushe zaki hankaline?, idan da abincin nan me zanyi dashi dazan aje naƙi baki?".
Ta kalli Bebi cikin jin haushinta.
"Wallahi tunda kuka tafi tallah ban ɗora ko ƙwayar hatsi acikin gidan nan ba, ina zaune ina jiran

ikon Allah, shahid ne yazo da taliya leda ɗaya, ita na dafa na zubawa, su ihsan shima na zuba masa, ina jiran ku dawo naga abinda Allah ze mana, sam hankalina ya tafi ga inga na haɗe kuɗaɗan nan na shahid ya zana jarabar wannan kema na baki kuɗin jarrabar shiga aji huɗun nan amman har yanzu abin yaƙi tafiya, seki zauna kijira in gama tuwo kici tunda ke har yanzu baki san abinda yake dai dai ba".
Mama ta ƙarashe maganar tana jin ranta na mata suya na halin kunci da rashin da suke ciki.
"Mama dan Allah ki rabu da ita, ga ruwa can a randa tasha ta jira tuwo".cewar hussaina wadda taɗanfi hassana zafi.
Wata uwar harara! Bebi ta makawa hussaina tare dajan tsaki! batare datayi magana ba taja ƙafafunta zuwa cikin ɗakinsu.
Rufda ciki tayi tare da sakin kuka! "Ya Allah ka kawo mana ɗaukin ka na alkairi a wannan zamanin talaka yana cikin matsala...............

*AUTAR MANYA*👉👈

I just published "PART 3" of my story "AUREN BARE".
https://www.wattpad.com/1108841932?utm_source=android&utm_medium=com.gbwhatsapp&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=autarmanya&wp_originator=bsm2ItCjiW55IJsHzofKCWd8CydFozsfYKQa7U9xGL1jQ%2FhrrdK5oQwC4rs2G7%2BoX4QJAH5q707c64tTT%2FmpkbNfQ2wSnU4X6BxVTXhnlwp%2BWq%2FYvdr1K7g%2BWUDCRuMu

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*003*

Bebi ta faɗi maganar tana share hawayen dayake faman zubo mata kamar famfo.
Miƙewa tayi daga kan katifar datake kai tare da cire hijabin jikinta, ta ajeshi a waje guda, fita tayi tsakar gida lokacin anata faman doka kiran sallar magariba sakamakon lokacin yayi.
Mama tana kan kujera ƴar tsugunno tana kwashe tuwo tana mulmulashi cikin farar leda tana kuma ajeshi acikin robar da ake fita da ita tallan tuwon.
Su hussaina suna kan tabarma suna buɗe mata ledojin ita kuma ihsan tana miƙa mata,arfa kuma tana bakin rariya tana kuma wanke ƴan kwanikan da suka ɓaci.
Wucewa tayi gaban rijiya ta zira guga ta ɗebo ruwa ta zuba a buta, sannan ta shige cikin banɗaki ta kama ruwa.
Fitowa tayi tare da ɗaura alwala hakan nan ta kuma wucewa ɗaki, zama tayi a bakin katifa tare da ɗaukar carbi azkar ɗin data haddace da kanta, ta soma gabatarwa, tana idarwa ana tayar da sallah a masallacin cikin unguwarsu, wanda ƙarar! lasafikar cikin masallacin har cikin gidansu, shinfiɗa darduma tayi a tsakar ɗakin ta soma tada sallar, cikin nutsuwa, bayan ta idar ta jima tana addu,a akan Allah ubangiji ya kawo musu ɗauki na alkairi, sannan ta shafa, tare da naɗe dardumar, duk abin Bebi bata yarda tai wasa da addininta wanda hakan ba komai yaja mata shiba face jajurcewar mama akan su.
Sam bata yarda ɗanta yayi wasa da addini, haka zalika duk talaucin su bai saka mama ta hanasu zuwa makarantar islamiyya ba, domin yanzuma haka makarantar magariba zasu tafi, wanda tun waccan shekarar su hussaina suka sauke alqur'ani mai girma, haka zalika sun sauke littattafan addini da dama, sannan kuma suna zuwa makarantar hadda ranar asabar, yanzu haka itama bebin saukarsu ya rage wata uku ciff itada shahid, makarantar bokoce kawai, basu bata muhimmanci ba, sabida rashin kuɗi, yasa su hussaina tunda suka kamallama aji uku a jiniya basu cigaba ba.
Haka zalika shima shahid yanzu ake shirye shiryen biya masa ya zana neko, wadda rabin kuɗin nasa ne na gawayinsa itama bebin yanzu zata zana jarrabawar shiga aji huɗu ne  asakandire.
Sedai kuma itama ɗin ba cigaba zatai ba sabida rashin da suke ciki.
Buɗe sif ɗinsu ta kaya tayi, wani ruwan tokar hijabi ta ɗauko wanda yasha karin guga, turare ɗan shafa,  ta buɗe a ƴar kwalbarsa, ta shafa kaɗan ajikinta.
Sannan ta zira hijabin, tare da rufe sif ɗin.
Gaban inda suke rataye jakunku nan su ta nufa, wata ƴar jakar leda ta ɗauko wadda alqur'aninta ke ciki, sannan ta fita tsakar gida, duk su mama suna sallah, lokacin.
Ɗan dakatawa tayi tare da jingina a jikin bango, cikinta yana murɗawa tanaji wata iriyar yunwa wadda bata da misali.
Bayan sun sallame addu'a suka shafa sannan mama ta juyo tana kallonta.
"Mama natafi makaranta".
Da kallon mamaki, mama tabita jin yau Bebi za,atafi makaranta da wuri, wadda wataran seta haɗata da duka sannan take tafiya ɗin.
"To ki tsaya mana kici tuwon".
Mama ta faɗa. tana kallon Bebi ɗin.

Kamar bazatayi magana ba sekuma ta tuɓe hijabin nata.
Tare da zama a gefen tabarma sannan tace.
"Mama azubo min wallahi yau malam Hadi yace zeyi dukan makara".
Cikin azama mama ta miƙe zuwa kicin suma ƴan biyu, haramar makarantar suka  yi, babban kwano mama ta ɗauka tare da zubo musu wadataccen tuwon gari miyar kuka wadda tayi daɗi duk da lami ce.
A tsakiyar iyalan nata ta zauna tare da saka hannu cikinsu, suka zauna sunaci bayan kowannensu yayi Bisimillah.
Shima shahid wanda ya shigo gidan yanzu wanda da alamar ma daga masallaci yake.
Ƙofar kicin ɗin yaje ya ɗauko nasa tuwon a roba, tare da zama a gefe yanacin nasa, kuma duk cikinsu babu wanda yayi magana.
Hassana ita ta soma ta shi tare da furta.
"Alhamdulillahi, Allah nagode maka, Allah ka ƙara bamu na kullum, Allah ka ƙarawa mama buɗi tare da dukkan musulmi baki ɗaya Amin".
Sannan ta nufi bakin rariya ta wanko hannunta, jakarta ta ɗauka.
"Mama natafi makaranta".
Ɗan kallonta mama tayi tare da cewa.....
"Ai kya dai bari ƴan uwan naki su gama kutafi tare ko?".
Batare data ce komai ba taja ta zauna tana jiransu su kammala ɗin.
Kowa fa seda ya tashi ya wanko hannunsa amman banda Bebi wadda take faman zare idanunta waje alamun bata ƙoshi ba.
"Mama dan Allah muyi gaba kada a soma ƙari bamuje ba, itafa Bebi setai biye-biyen gidansu ƙawayenta, daganan kuma sunje sunyo tsokanar su sannan su tafi".
Maganar hussaina kenan wadda ta take tsaye tana saka takalminta a ƙafarta.
"Eh wallahi mudai gaba zamuyi".
Cewar ihsan mai bin Bebi.
"To dalla kutafin mana Allah yasa niba makauniya bace ba".
Cewar Bebi tana siɗe hannunta sannan ta dubi mama wadda bata ce komaiba tanajin diramar yaran nata.
"Mama a ƙaramin harga Allah ko babban hanjina baije ba".
Tafaɗa tana karya kanta kamar wata abar tausayi.
"Dama haka kika iya shegiya mai cikin zani".
Cewar shahid wanda yake ƙoƙarin ɗora robar tuwan daze fita da ita a kansa.
"To kaikuma meya ruwanka dani ne kamar ansaka baki dashi".
Takai maganar tana zabga masa wata ƙatuwar harara kamar idanunta ze faɗo waje.
"Wallahi nidai karya ƴa zanyi abanza  na watsar ko shara bata iya ba se aikin cin tsiya daga ci se bacci sekin fita tallah, kiyo tsokana babu abin da ta iya".
Yafaɗi maganar yana ficewa daga gidan kansa ɗauke da robar tuwon hannunsa riƙe da bokitin miya.
Wata gigitacciyar ƙara! bebi ta ƙwala wadda seda ta saka mama zabura, cikin masifar faɗanta ta soma magana.
"Wallahi zaka dawo ne wallahi bazan yarda ba, mama kina fa kallon abinda yace min na rantse bazan yarda ba".

Tafaɗa tana Cilla ƙafarta ƙasa kamar wata ƙaramar yarinya tana faman ihun da babu hawaye!.
Ganin zata ɓata musu lokaci ƴan biyu suka wuce makarantarsu.
Itama mama tashi tayi, zuwa kicin ta ƙaro mata tuwon tare da dire mata gabanta.
"Gashi nan idan kin gama ki wuce ki tafi makaranta, ai gaskiya ya faɗa wallahi Bebi bansan irinki ba, ko shara ta ƴa mace senai da gaske, haka kikaga ƴan uwanki sunayi, se aukin ci kamar gara,kullum cikin rainuwa kike idan zan cika miki roba da abinci sekin share sannan kizo kina baki ƙoshiba tallan nan bazaki mayar da hankali kiyiba...................,
Aikin gida kina kallon arfa ƙanwarki ce ta biyu amman haɗuwa muke tare ayi, amman ke sam sedai yau faɗa da wancan gobe tsokanar wancan, hatta ƙofar gida idan kika taho aguje! ta bugeki sekin bita kin rama wannan wace irin rayuwace Bebi?".
Mama takai maganar tana kallonta.
Sannan ta cigaba da cewa.............
"Narasa wannan hali naki jiya haka malam sadi mai kayan miya yazo har nan yana cewa kin buge ƴarsa harda cewa Wallahi ze kai hukuma dame zanji Bebi".
Takai maganar cikin jin susar rai.
"Lah mama wallahi ƙarya........., bata bari takai ba ta buge mata bakinta.
"Dan gidanku babbane yake ƙaryar haka na baku tarbiyar ƙaryata babba?".
Takai maganar cikin zafin rai matuƙa.
"Mama nifa bashi zanceba, wallahi salisa ƙarya takemin itace fa kullum nazo wucewa setace min budurwar habu mai itace,nikuma bana so wallahi mama kije ki mata magana idan ba haka ba zan fasa mata kai watarana".
Takai maganar tana turo bakinta waje.
"To maye idan ta gaya miki hakan tunda aishima habun mutum ne, bana son maganar banza maza gama ci ki wuce kitafi makaranta".
Mama takai maganar tana shiga cikin ɗakinta.
Tana cin tuwon tana mita tana kuma ayyana yadda zataci uban salisa.
Tana kuma murguɗa bakinta kamar agaban salisan take.
Nikuwa nace.
"Hoho Bebi daru kenan".
Tana gama cin abincin ta dauke kwanon takai bakin rariya tare da wanke hannunta.
Aguje ta fita daga gidan tana rungume ƴar jakar ledar qur'anin dake hannunta.
Harta ƙarasa makarantar magariban.
Lokacin malam hadi yana tsaye hannunsa riƙe da dorina yana faman jibgar ƴan makara.
Tunma kafin ya ganta ta laɓe a bayan sadiya ƙawarta cikin sanɗa tabi gefe ta saje da ƴan ajin sabida ita aduniya babu abinda taƙi jini kamar adoketa.
Ƙasa ƙasa take raɗawa sadiya labarin irin dukan da zasuma salisa gobe a filin kaci uwaka.
Wanda ita kuma sadiyar take kuma zuga Bebi hartana zata ɗauko mata wayar wutar da yayansu yake dukansu da ita.
Sam hankalinsu baya kan malam hadi wanda yake bayani sunata hirarsu yadda zasuma salisa dukan tsiya.........

*ASALIN LABARIN*

Yana da kyau makaranci ya tsaya sosai yaji yaya asalin su Bebi yake dama Asalin labarin namu

baki ɗaya.
Kudai kuyi haƙuri kubiyoni a sannu domin har yanzu shinfiɗa muke a labarin bamu shigeshi ba.

*WAI WAYE ADON TAFIYA*

AUTAR MANYA👉👈
*COMMENTS*
*SHARE DOMIN ALLAH*🙏

I just published "PART 4" of my story "AUREN BARE".
https://www.wattpad.com/1108997175?utm_source=android&utm_medium=com.gbwhatsapp&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=autarmanya&wp_originator=wi7huBHWJ%2B5vI6y2TtE8NXp4yNS2NheTEBOWdGsVA%2FMsofq%2BYcMI0duvNSudokhBppbo6YX5Z0IR5IjfVeQqBBYg4U%2FLU6gjCjp67xDLnIiZheyApp4xToH52kSL8tqE

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*004*

*ASALIN LABARIN*

Sunan mahaifin su Bebi  musa mai katifa haifaffen garin kanon dabo.
Cikin ƙaramar hukumar kumbotso anan wata ƴar alƙarya gidan iyayensa yake mai suna ƴan kusa.
musa ya taso cikin halin maraici tare da  tsangwamar matan mahaifinsa kasancewarsa maraya marar uwa, mahaifiyar sa Bilkisu Allah ya jiƙanta da rahamata tun wajan haihuwarsa ta rasu.
Rayuwarsa ta koma wajan matan mahaifinsa waɗanda suke azabtar dashi, inna hasiya matar Alhaji mai katifa ta farko tana da yara biyu maza sabi'u da Rabi'u se autar ta mariya,ita kuma inna suwaiba tana da yara guda biyu maza, sani da tasi'u  se amaryar Alhaji mai katifa Bilkisu wadda ta kasance ƴar uwarsa ta jini wadda aka haɗasu auren zumunci kuma itama ɗin dai duk anan cikin ƴan kusan iyayenta, suke, waɗanda suka haifeta ita kaɗai bata da yaya bare ƙani ga kuma maraici domin Bilkisu bata da uwa bata da uba duk sun rasu, wannan ce ta saka Alhaji mai katifa yake mugun jin tausayinta tare da tsananin sonta.
Tunda Alhaji mai katifa ya auro bilkisu su inna suwaiba suka haɗe mata kai suda yaransu tsangwama xagi da hantara harta kai ga bata iya fitowa ko tsakar gida, cikin haka Allah ya bata ciki zokiga murna wajan Alhaji amman wajan su inna suwaiba kamar zasu kasheta sukeji, sabida baƙin ciki.
Tunda cikin nata ya taso Alhaji ya hanata koda girki, kasancewar Alhaji mai ɗan rufin asirine yasa yake tafiya wasu garuruwan kan harkokinsa na saida katifa, wanda kuma cikin hakan Allah ya nufi Bilkisu da fara naƙudar tsaye.
Ita bata san tana naƙuda ba,sabida ƙuruciya da kuma wauta amman su inna suwaiba sarai sun gane tana halin naƙudar sedai babu wadda ta kulata bare ta saka ran zasu tai maketa.
Kullum daren duniya setai kuka! sabida ciwon baya ciwon mara ga Alhaji baya gari bare ya taimaketa ranar dazata haihu tun safe take murƙususu a ɗaka amman an rasa wadda zata leƙo ɗakinta kodan taga halin datake ciki.
Tun tana ganewa hartazo hankalinta ya gushe, wanda A wannan lokacin Allah ya kawo Alhaji mai katifa gidan wanda zuwansa kenan yay cikin ɗakinta.
Ganin halin datake ciki yasa ya fito ya rufe matan nasa da faɗa har yana kiransu da marasa imani, fita yay zuwa cikin gidan mahaifansa waɗanda suma suke babu rai, se dai akwai yayansa da matarsa agidan,matar yayansa ya kirawo suka nufo gidan nasa cikin sauri da ita.
Ganin halin da Bilkisu take ciki yasa matar yayan Alhaji cewar yaɗan basu wuri domin zuwa wannan lokacin har faya ta fashe kan ɗa ya taho.
Bayan fitar Alhaji bilkisu ta soma nakuda ta gaske.
Wadda cikin mintuna goma ta haifi ɗanta ƙato dashi sedai yana cikin riga, seda matar yayan Alhaji mai suna gwagwgwo aya! tai da gaske sannan  ta yaga rigar ɗan kuwa ya canyara kuka! kallo ɗaya Bilkisu tayiwa jaririn nata Allah ya  karɓi ranta.
_Kullum nafsin zaikatul maut_
Mutuwar Bilkisu ba karamin girgiza Alhaji tayiba wanda seda akai da gaske ya koma walwalarsa.
Kwanci tashi babu wuya wajan Allah  yanxu haka musa ya cika shekaru goma da haihuwa wanda kawai sedai ace ikon Allah ne ya yarashi sabida yadda ya taso cikin halin tsangwama da hantara hatta ƴan uwansa cutar da shi sukeyi.
Awajan Alhaji kawai yake jin sauƙi wanda daman tunda ya taso bai sha nonon mahaifiyarsa ba

sedai shayar da shi da ake da madarar shanu har Allah ya kawoshi waɗannan shekaru, bayan yaɗan soma zama saurayi ya soma fuskantar halin rayuwa  ganin babu wani sauƙi sena ubangiji yasa Alhaji ɗaukeshi ya kaishi can garin rimin gado makaranatar almajirai anan ya sami saukar alqur'ani mai girma, bayan yazama matashin saurayi alokacin ya sauke alqur'ani seya dawo nan ƴan kusa alokacin ne ya soma bin Alhaji kasuwa duk da su sabi'u na cutar dashi da haɗa masa sharri wajan Alhaji.
Amman shikuwa tsakani da Allah yakeson su kuma baitaɓa ƙullinsu acikin ransa ba.
Aisha ƴace a wajan baba sale yayan alhaji mai katifa, waɗanda suka fito uwa ɗaya uba ɗaya, wadda mahaifiyar aisha itace gwagwgwo aya mace mai kirkin gaske, kuma itama gwagwgwo aya daga kan aisha Allah bai basu wata haihuwar ba, tun tasowar aisha ta kasance kyakykyawar gaske nitsatstsiya marar son hayaniya, aisha tana da shekaru goma sha bakwai, Allah yaywa malam saleh rasuwa ,yayan Alhaji, wanda tsananin dukan rasuwar yasa Alhaji kwanciya rashin lafiya lokacin su musa sun girma domin dik su sabi'u sunyi aurensu shikuwa musa ya zama saurayi amman dai bai auren ba, bayan addu,ar sadakar bakwai Alhaji da kansa ya kirawo musa ya damƙa masa kyautar auren Aisha ɗiyar yayansa marigayi atake anan musa ya amsa batare dayay musuba, haka zalika itama aya dataji labarin tai matukar farin ciki.
Shirye shirye ne ya cigaba da gudana Aisha ma tai farin ciki sabida daman ɗan uwan nata yana burgeta cikin gidan Alhaji kuwa kamar ze ƙone sabida ashe tasi'u yana son aisha amman yay ƙauron baki har aka baiwa musa, wannan dalilin yasa su inna suwaiba sukai kamar su ƙona gidan seda Alhaji yay da gaske sannan suka nutsu.
Kwanci tashi babu wuya wajan Allah, an ɗaura auren musa da aisha suma sun tare anan gidan Alhaji inda sauran ƴan uwansa suke zaune da matansu zaman gidan Alhaji da Aisha da matan ƴan uwan musa zamane na faccalanci marar dadɗi.
Sosai aisha take kurɓar ruwan baƙin ciki awajan matansu sabi'u musamman wajan shafa'atu matar Rabi'u wadda take yin wani abun ma da gayya.
Haka dai aisha take haƙuri kuma koda wasa bata taɓa gayawa musa ba kasancewar ta mace mai kawaici, shekarun su Aisha biyu da aure da Musa Allah yaywa aya mahaifiyar aisha rasuwa wanda tsananin damuwa yasa seda musa yayta karɓowa aisha ruwan tofin dangana sannan ta sami nutsuwa.
Kwanaki naja lokaci na gudu katsam shima Alhaji aka wayi gari ya rasu wadda waɗan nan rashe-rashe ya girgiza musa tare da matarsa aisha amman ga sauran matan Alhaji da su tasi'u da matansu duniya ce ta buɗe musu sabuwa tare da buɗe shafin cin dukiyar alhaji wadda sukai kane kane kamar jira suke.
Abinda ze baka takaici shine kwanan Alhaji arba'in da rasuwa suka raba gado!...........

*MANAGE*🙏

*SHARE DOMIN ALLAH*

I just published "PART 5" of my story "AUREN BARE".
https://www.wattpad.com/1109368451?utm_source=android&utm_medium=com.gbwhatsapp&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=autarmanya&wp_originator=FJq4nmGqNChIpjzeCYUID6TOo%2B5ljX4M5WXUf22BCkGUbwyUKvCCue%2F6EcHksmXWEzFi9umRgUcl0ZsLrIVeEGk1fro%2B%2BIba%2BwJwOWtHBuBCg6Xs%2BOukMT17%2BB5t45Dv

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*005*

Abinda ze baka takaici guda ɗayane kwana arba'in da rasuwar Alhaji mai katifa, su sabi'u da tasi'u da sani da rabi'u harma da mariya wadda take aure acan gaida suka ɗauko alƙali wanda suka gama siyansa da kuɗi yazo yay rabon gado.
Wanda inda kaga yadda aka raba aka bawa musa nasa kason sekai kuka! sabida ko arziƙin soron gidan Alhaji mai katifa musa bai samu ba.
Duk da kasancewarsa ɗansa na jini amman hatta mariya datake mace taci wani kasafin acikin gidan amman musa dan tsananin ƙinsa bai sami arziƙin zaman cikin gidan mahaifin nasa ba.
Kwana uku da kammala rabon gadon Rabi'u ya fito gadaga yacewa musa yakamata tunda an bashi kasonshi ya tattara shida matarsa ya bar musu gidansu.
Se asannan musa ya sami zarafin zubda hawayen takaici tare da baƙincikin yadda zumuncin yanzu ya kama uban ɗakinsa.
Lokacin Aisha tana tsaka da laulayin haihuwar farko haka ya haɗe musu tarkacensu suka baro cikin unguwar ƴan kusa cike da baƙin ciki.
Koda sukazo fita ma daga gidan amai makon su Rabi'un su rakosu da addu,ar fatan alkairi a,a ina se fatan tsiya tare da mugun baki ne ya rakosu, wanda bada ban musa da Aisha sunada

haƙuri ba dase anyi ɓatacciya sabida yadda ƴan uwan musan suke jifansu da muyagun kalami.
Anan cikin gaida ya kama musu hayar ɗaki guda a wani gida waishi gidan sabil, abinda kuwa yasa aka sawa gidan wannan suna sabida yadda yawanci masu zaman gidan masu ƙaramin ƙarfine haka zalika shi kansa mai gidan yana dai saka mutane ne kawai sabida Allah amman kuɗin gidan yafi haka.
Zaman Aisha da musa sedai muce zamane na haƙuri, saboda komai na musa ya tsaya cak! kasancewar daman ƴar kasuwar dayake zuwa ta ƴan katifa wajan mahaifinsa ne to tunda ya rasu kuma sesu sabi'u suka rufe shagunan dan tsabar mugunta ma basu sakasu a rabon gado ba, ko da Ado abokin musa wanda sukai karatu a rimin gado tare yazo yaga halin da suke ciki kuma yaji komai se ransa ya ɓaci haryana ƙiƙi rarin cewar musa ya ɗaukaka ƙara.
Shi kuma ze tsaya masa duk inda za,aje aje, amman ga mamakin ado se musa ya buɗi baki yace.
"Haba Ado dawani idon zan dubi alƙali nace masa nakawo ƙarar ƴan uwana akan gado?, Nikam na haƙura na barsu da sakkowar rana da faɗuwarta".
Numfasawa ado yayi tare da kallon abokin nasa cikin tsananin damuwa mai cin zuci sannan yace.
"Amman banji daɗin hakan ba, amman babu komai insha Allahu bazaka zauna haka ba, ni zan koma ƙauye zan haɗo kaddarata, tas nazo nan na sama mana abin da zamu dingayi muna rufawa kammu da iyalanmi asiri".
Sabida tsabar jin daɗi musa seda yay ƙwallar farin ciki, daman haka rayuwar nan take bare can seya rufa maka asiri amman ɗan uwanka yakasa rufa maka shi.
Koda sukai sallama musa yana zuwa gida ya shaidawa Aisha wadda tacika da tsananin farin cikin da seda tai ƙwallah.
Malam Ado abokin musa yana zuwa ƙauyen rimin gado ya samu dukkan kaddararsa ta ƙauye ya siyar daman mahaifansa sun rasu kuma shi kaɗai suka haifa kuma sun tafi sun bar masa tarin dukiya mai yawa, matarsa guda ɗaya, Hansatu se ƴaƴansa maza guda biyu Aminu da nura.
Haka ya sakosu agaba, sukayo nan cikin kano, agidan musa suka soma zama ɗakin Aisha shikuma suke kwana da musa a wani shagon maƙota har Allah yasa komai ya dai-daita.
Dayake musa yana da fuska kuma yasan jama'a a nan kasuwar ƴan katifa hakan yasa basuyi ƙasa a gwiwa ba wajan garzayawa kasuwar, cikin hukuncin Allah suka sami baba lado aminin Alhaji mahaifin musa wanda daman yasha zuwa gidan Alhajin neman musan amman baya samunsa se su Rabi'u waɗanda suke jifansa da baƙaƙen maganganu saboda yazo wajan musa kamar ba abokin mahaifinsu, ba anan musa ya kwashe komai ya gayawa baba lado wanda tsananin tausayin musa yasa baba lado zubda hawaye.
Anan baba lado ke basu labarin ai satin daya wuce ma su Rabi'un sukazo da dillalai suka sayar da shagunan Alhajin baki ɗaya.
Sosai musa ya kaɗu da wannan lamari, amman seya share haryay wa ƴan uwan nasa addu,ar shiriyar Allah domin duniyar ba madauwa ma bace ba.
Abinda ya kawosu kasuwar suka gayawa baba lado, wanda anan take baba lado yay musu garanto wajan kama hayar shago ɗaya wanda zasu dinga saro katifa suna sayarwa.
Seda suka kammala komai sannan suka bawa baba lado kuɗin sarin sabida musa ya yarda da baba lado kasancewar sa kamar amini ne wajan Alhajinsa.

Koda baba lado ya rakosu hanya anan yake tambayar musa yanzu yana ina, anan musa yake ce masa aishi bai sami arziƙin samun kaddarar mahaifin nasa ba se kuɗin da suka bashi waɗanda basu ishe shi koda yankar farcan susa ba.
Sosai baba lado ya tausaya masa.
Kuma anan take yay masa albishir daya bashi kyautar gida guda wanda yake cikin sharaɗa sedai gidan ɗaki ɗayane tal se shago a waje.
Tare da kicin da banɗaki amman yanzu haka ƴan hayane aciki se nan da wata biyu zasu tashi idan yaso idan suka tashin seya shiga, wanda daman daga gidan da baba ladon ya bashi zuwa gidan baba ladon layuka ukune tsakaninsu.
Sabida tsabar farin ciki musa harda kuka! haka zalika ado shima seda yay hawayen murna.
Wanda shima ya nuna yana buƙatar  idan da hali baba ladon yay masa hanyar siyan gida anan kusada abokin nasa musa.
Ganin garin yana yamma yasa baba lado ce musu su koma gida gobe sa dawo hakan ce ta kasance musu suka koma gida anan musa yake gayawa Aisha abinda ya faru, sosai Aisha ta shiga murna harda kukanta itama hansatu taimurna  ranar kwanan zaune sukai dan farin ciki.
Washe gari tun wuri suka iske baba lado acan sharaɗan gidan sa wanda har seda suka shiga ciki suka gaida baba matarsa mace mai kirki haka tai ta jan musa ajiki tana masa wasa,kasancewar baba lado bashi da ƴaƴa maza se mata kuma duk sunyi aure yasa baba jin tsananin son musa aranta.
Anan baba ta shiga zayyanawa musa irin taimakon da Alhaji yaywa baba lado aduniya, seda suka sha kokon da baba ta tilasta musu sannan baba lado ya ɗaukesu suka shiga cikin unguwar cikin ikon Allah suka sami gida wanda tsiran layi guda ne tsakanin gidan da ado ya samu ze saya dana musa ciniki akai cikin sauƙi aka kammala wanda su zasu ma riga musa tarewa.
Komai ya kammala sedai gidan ado yafi na musa girma kaɗan.
Cikin satin suka kammala komai ado ya dawo nan sharaɗa da zama haka suka soma tafiya kasuwa komai yana tafiya musu dai dai misali.
Kwanci tashi babu wuya wajan Allah yanzu haka shima musan ya dawo nan gidan da baba ladon ya bashi kuma suna tafiya kasuwa a tare da ado kuma babu laifi suna samu rufin asirin Allah dai dai misali.
Lokacin cikin Aisha ya tsufa, cikin wannan lokacin su Rabi'u sukaji labarin yadda Allah ya rufawa musa asiri wanda basuyi ƙasa a gwiwa ba wajan zuwa ciwa musa da ado da baba lado mutunci tas harda cewa insha Allah se gayyar ta watse.
Ko da wasa baba lado yaƙi barin su musa suyi magana har su Rabi'u suka gama cin mutuncin su suka tafi.
Zumuncin ne ya ƙarfafa a tsakanin hansatu da aisha da kuma baba matar baba lado wadda suka maidata uwa haka zalika ƴaƴan baba mata guda uku dasuke aure suma baƙaramin zumunci suke dasu Aisha ba.
Sukuwa su musa da ado sun zama kamar yaya da ƙani wanda suka ɗauki baba lado uba domin duk ƴan unguwama sun ɗauka cikinsu guda.
Ranar wata laraba Aisha ta haifu wanda ta haifi yaranta mata masu kyau tabarakallah.
Guda biyu baba da hansatu sune suka gyarata tsaf haka aka cigaba da zaman biƙi wanda baba ita take kula da Aisha.

Har tsawon kwana arba'in sosai musa yake kula da matarsa da yaransa waɗanda sukaci suna Hassana da Husaina.
Ƴan biyu suna da shekara ɗaya ta kuma haifar namiji mai suna muhammad ana ce masa shahid saboda sunan Alhaji mai katifa yaci.
Ƴan biyu sun taso cikin kulawar uwa da uba wanda suke cewa Aisha ( mama) musa kuma ( abba ) hansatu kuma ( iya ) kamar yadda ƴaƴanta ke gaya mata ado kuma ( baba ado ) baba lado kuma ( malam ) baba kuma matarsa sukan ce mata ( baba ) ƴan biyu sunada shekara biyu shahid yana da ɗaya mama ta kuma haifar ƴa mace sabida haihuwar kwanika take.
Yarinya ta haifa fara tas kyakykyawa ajin farko, lokaci ɗaya ta shiga ran Abba wanda atake anan ya saka mata suna BILKISU wadda suke ɓoye mata da BEBI saboda sunan mahaifiyarsa ne.
Abba ya ɗauki son duniya ya ɗorawa BEBI..............

*VOTE*
*COMMENTS*
*SHARE*

I just published "PART 6" of my story "AUREN BARE".
https://www.wattpad.com/1109538150?utm_source=android&utm_medium=com.gbwhatsapp&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=autarmanya&wp_originator=ikpMILhK1zeHxV6QZZRcPLMlWp3agsPzqCYNmA9e%2FIr1pMRPEIDwqDYFHx678GsZUFu89NFvDx2V8kClj9MowWZ2YZGRT49eaLvHxUCfU2RB6QQ1iZHpLSXGr09bVAPw

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*006*

Abba ya ɗauki son duniya ya ɗorawa Bebi wadda ta taso cikin gata, Bebi tafi duk sauran ƴan uwan nata kyau gata da shiga ran mutane sedai fa tun tana ƙarama ta taso a son rigima rashin haƙuri da faɗa.
Sedai kuma tana da son ƴan uwanta musamman abbanta da mama, lokacin da aka haifi Bebi tana da wata biyu iya hansatu matar malam ado wadda tun daga kan mazan ƴaƴanta biyu bata kuma haihuwa ba, se a wannan lokacin Allah ya bata ciki ta haifi ƴarta mace wadda taci suna sadiya wadda suka taso kusan kai ɗaya da bebi.
Bebi ta bawa ihsan mai sunan gwagwgwo aya shekara biyu, daganan se arfa wadda taci sunan mama aisha wadda da cikinta ne Allah ya ɗauki ran Abba shida amininsa malam ado wanda agarin tafiyarsu ta hanyar saro katifa Allah yay musu rasuwa ta hanyar hatsari.
Baƙaramin girgiza waɗan nan iyalan bayin Allah'n sukai ba Bebi batafi shekara huɗu ba lokacin amman har suma ta dingayi tana kiran abbanta, abinda ze baka mamaki shine kaf su Rabi'u babu wanda yazo wa mama ta'aziya se ƴaƴan baba ado ne maza awajan da dangin sa tare dasu malam se ƴan uwan mahaifiyar mama dasuka zo daga ƙauye.
Haka akaci gaba da ƙarɓar gaisuwar Abba tare da amininsa baba ado kowa yaga halinda mama da iya hansatu suka shiga tare da ƴaƴansu seya tausaya musu, sabida tsabar tausayi yasa baba lado ( malam ) ya ɗauki nauyin dukkan abinda za,aci na waɗannan gidaje biyu har zuwa tsahon kwanaki bakwai.
Cikin kwana na bakwai Allah ya nufi  su Tasi'u zuwa gidan ɗan uwan nasu waɗanda sukaita ɗaga kai suna watsawa, mama da yaranta kallon banza.
Mariya ƙanwarsu ita ta dubi mama a sheƙe tana cewa....
"Kukuwa a wannan matsiyacin gidan kuke rayuwa kamar dab.......,
Bata ƙarasa ba Bebi wadda take raɓe a bayan mama tana kuka ta cafketa tare da katse ta hanyar furta.
"Ai seki kawo mana na ƴan gay......, itama bata ƙarasaba mama ta kwaɗa mata mafici da kallo mariya tabi Bebi wadda lokacin take ƴar micila tare da maka mata harara gami da jin tsanar yarinyar tashi ɗaya hartana ƙudurar wani abun aranta.
Haka suka gama habaicinsu mama bata tanka musu ba har suka tafi wanda Bebi seda tasan yadda tai tabi bayansu ta watsa musu ƙasa ta ɓuya haka suka juyo suna masifa amman basuga kowa ba.
Lokacin nema mama takejin wai ashe baba suwaiba bata da lafiyar ƙafa yanzu ita kuma inna hasiya bata da lafiyar idanu.
koda bebi ta shigo gida jin ranta take sakayau ko banza taci uban masu gayawa mamanta magana duk da lokacin bata sanma kosu waye ba.
Su abba sunada kwana ashirin da rasuwa mama ta haifi arfa haka tacigaba da raion ƴaƴan nata cikin tsananin dauriya sabida bata da matallafi se Allah.
Malam yakan ɗan tallafa mata to kuma shima ga tsufa yasoma kamashi gashi baya da ɗa namiji bare ya sami matallafi.
Haka zalika itama iya hansatu take fama sedai ita nura da aminu sun kawo ƙarfi kuma bata kai

mama yawan iyali ba sedai itama ɗin maleji take sabida nura da aminu karatu suke dole wani abun setai da gaske kuma duk da haka tana ƙoƙarin ganin ta tallafi maman ƴan biyu da wani abun haka xalika suma su nuran suna tallafawa mama, ita daman Bebi ƴar gidan iya hansatu ce bacci kaɗai ke kawota gida sabida shaƙuwarsu da sadiya ƴar baba hansatu.
Rayuwa tana tafiya waɗanda cikin amincin Allah mama ta soma saida kayan miya ganin babu wata riba ta koma yin adashi wanda shiya jamata yin suna acikin unguwar wanda anan tasan mutane sosai kuma suna zaman mutunci da kowa.
Su hassana sun shiga  makaranta waɗanda iya kacinsu jss 3 ta ciresu sabida halin rayuwa sedai kuma sun sauke alkur'ani mai girma.
Shahid ne yanzu ze xana neco ita kuma Bebi tana jsss three ita da sadiya su arfa kuma suna primary.
Ganin yadda jama'a suke cinye mata kuɗi ga rigima yasa ta soma yiwa ƴan biyu awara tana kasa musu suna kaiwa can kasuwar kai da ƙafa ada Bebi take ɗorawa to ita kuma Bebi da zarar an kasa mata seta wuce wajan sadiya suje suyo tsokanarsu daganan a zubar suci taci, ta dawo tana raba idanu, gata da mugun tsoron duka sedai tsabar rashin ji.
Ganin haka yasa mama ta soma haɗata da ƴan biyu kuma ba dan taso ba inda asonta ne tafison yaranta su zama masu ilimi kamar kowa amman babu hali,da magariba kuma zata kasawa shahid tuwo shima ya fitar da rana kuma in babu makaranta ya tafi wajan gawayinsa.
Su ihsan kuma tana ɗora musu kayan miya still su kai cikin unguwa da wannan mama take samun na cefane harma taiwa malam alkairi sabida ya tsufa, su Bebi sun ɗauki malam kakansu ada kafinma su san komai sun zata shiya haifi abba seda suka girma suka gane komai wanda Bebi taji duk duniya bata da maƙiya kamarsu Baba tasi'u.
Su Aminu da Nura kuwa ƴaƴan baba ado su suka zamewa su Bebi yayye kuma dan dai suna karatune basuda yadda zasuyi amman sam basa son wannan tallan nasu Bebi.
Rayuwa tana tafiya lokaci yana ja Bebi yarinya ce mafaɗaciyar gaske gata da rashin kunya se tsabar tsoron duka se nace tunda mama take bata taɓa ganin abunda ya baiwa Bebi tsoroba haka zalika bata da saurin kuka duk abinda Zebawa Bebi kuka abun babbane amman ko dukane sedai ka gaji amman bazatai kuka ba sedai fa da zarar taga abin dukan zata gudu.
Gata da mugun kwaɗayin nama haka zalika ko ciwo take bata kasa cin abinci sabida Allah ya zuba mata baiwar son kai loma abaki wataran idan mama batai girkiba haka zata sakata agaba tai ta mita, itafa Bebi ko ƙofar gidane ya bugeta setaje ta rama haka xalika ko arfa ƴar autar mama ce ta bugeta bata saniba seta rama bata da haƙuri ko kaɗan.
To gwarama ƴan biyu takan ɗan raga musu amman ba can ba shahid kuwa yazama kamar sa'anta dan wataran har dambe ake sedai kuma idan suna ƴar daɗi dashi watakan wajan dahuwar idomin dayake kawowa ta dafa masa anan xakaga bebi tana yaya shahid sabida ze bata lasar tukunya.
Batada aminiya kamar sadiya, Bebi yarinyace mai garin jiki dan idan ka dubeta sekace gaba take dasu hussaina sabida tun tana ƙarama can kirjinta ya soma cika dalilin haka yasa kullum mama cikin zulumin fitar Bebi take sabida ɓata garin samari, shiyasa ta dafe mata da saka hijabi koda yaushe.
Sedai kuma inda Allah ma ya duba mama sam hankalin Bebi bayaga kula saurayi ko an biyota xagi ke rabata da mazan kota saka gudu! itafa haushi maza ke bata sam idan taji su sadiya suna zancen samari setai ta ƙunci wannan dalilin ne yasa suke faɗa da salisa sabida tana

haɗata da habu mai itace wai saurayinta wannan kalmar har ƙwalla take saka Bebi dan tsabar takaici.
Haka zalika suma su hassana mama bata barinsu zance sabida acewarta komai dama ne bata son yaran nata su buɗe idanu da soyayya sabida gudun matsalolin rayuwa tafison koda ma auren ne Allah ya kawo musu kwatsam batare dajan lokaci ba.
Su siba a wajan saida awara suka san su Bebi sabida wani zubin suna kai musu wajansu su siya to sabida tsaftar su yasa daga sun fita da ita ake siyeta wani zubin ma har gida ake zuwa To ashe shi siba akwai wata aƙasa domin tunda ya ƙyalla yaga Bebi yaji yana sha'awarta wannan dalilin yasa yaci awararta ya hanata kuɗin toya zata irinsa ce ashe rabon a ɗauko masa officer ne, wannan dalilin yasa kukaji yadda Bebi suka ƙarke da siba agaban officer tun a shafinmu na farko.

*DAWOWA LABARI*

*COMMENTS*
*VOTE*
*SHARE*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*007*

_Dawowa Labari_

Duk irin yadda Bebi takewa Sadiya raɗa akunnen nata ashe malam hadi yana kula dasu seda ya gama dukan ƴan makara tas sannan ya juyo garesu tare da haɗe fuska tamau kamar bai

taɓa dariya ba.
"Bilkisu Musa Mai katifa! Sadiya Ado Rimin gado". yafaɗa tare da haɗe ransa..........
"Dukan ku kufitomin nan tunda Ku bakwajin magana kullum cikin surutu kuke".
Cikin tsananin tsoro sadiya ta soma raba idanu amman mutuniyar kuwa ita ko ajikinta sema fitowar datayi gaban malam ta rissuna tana tura baki gaba tare da yatsine fuska.
"Gani".
Abinda Bebi ta faɗa kenan tana tsare malam hadi da idanunta babu alamun jin tsoro ko kaɗan a idanun nata.
"Wai ke kuwa Bilki aljanu  gareki ne?, kullum burinki kiyi surutu a aji har ki shafawa wasu".
Muryar malam hadi kenan wadda ta saka ƴan ajin yin tsit sunajin gulma.
Seda Bebi ta juya ta makawa ƴan ajin harara sannan ta juyo.
"Nidai Malam sunana Bilkisu idan yay maka yawa kace Bebi amman ubana bai raɗamin suna da Bilki ba, kukuma munafukai ubanku kuke kallo?" .
Gaba ɗaya ajin shuru ya ɗauka ita kuwa sadiya wata gudawa ce ta zo mata sabida kowa yasan halin malam hadi yau shikenan Bibe ta ja musu jaraba.
Ran malam hadi yayi mugun ɓaci cikin zafin rai ya kira monita tare da ce masa yaje ya ɗauko masa dorina mai baki biyu a ofishin shugaban makaranta.
Jiki na rawa monita ta tashi hartana dariya sabida Bebi ta addabi kowa a ajin babu wanda take ragawa daman ta jima tana jin haushin Bebin shiyasa ranta yay fes dajin hakan.
Mintun Biyu monita tazo da dorina jiki na rawa ta rissuna ta miƙa wa malam hadi.
Wani kallon zamu haɗu dake Bebi ta mata tare da sunkuyar da kanta a ƙasa duk da tana da jin tsoron duka amman batajin zatai kuka! kuma batajin xata bashi haƙuri bare aga galabar ta.
Muryar sadiya ce ta karaɗe wajan.
"Malam dan girman ubangiji kai haƙuri wallahi Bebi ce ke magana bani ba, dan Allah malam karka dakeni".
Tafaɗa jikinta yana rawa.
Wani irin haushine yazowa Bebi wuya da kallon ɓacin rai ta dubi sadiyan amman bata iya ce mata komai ba.
"Jeki zauna ki barni da wannan tsagerar marar kunya".
Da sauri sadiya ta koma ta zauna tana godiya.
Tabar Bebi tana gunguni tana mitar zuci wadda sautin har waje yake fitowa.
Tattare hannun rigarsa yay tare da zuba mata dorinar agadon bayanta wanda dukan har wajan fuskarta haka  ya zage ya dinga lafta mata bulalar ajikinta seda yay mata guda goma sannan yace ta miƙe hakan nan ya kuma zuba mata guda biyar a ƙafafunta.
Wata iriyar banƙara Bebi tayi tare da kurma wata shegiyar ƙarar! data amsa makarantar baki ɗaya tare da zubewa a ƙasa tana wata iriyar haniniya tana fidda dafara.
Kallo ɗaya zaka mata ka gane tana fama da bugun iskane wanda kuma hatta mama data haifeta bata san da wannan aljanun na bebi ba haka zalika kowa ma, bai sani ba se yau ɗinnan da malam hadi yay wannan dukan.
Cikin sauri ragowar malaman suka shigo ajin kasancewarsu maza yasa suka nemi ƴan ajin mata akan su ɗagata wadda take kamar gawa su kaita offishinsu.
Mutum kusan biyar ne matan ajin suka xo kan Bebi zasu ɗagata amman duka seta ta watsar dasu.

Sadiya kuka! take aguje tayi ajin su ƴan biyu tana gaya musu cewar suzo Bebi ta mutu.
Hassana mai saurin kuka! tuni ta ɗora hannu akanta tana ihu hussaina kuwa gudu ta saka zuwa ajinsu Bebi tana share zubar datake yanko mata.

Ganin ƴar uwarsu cikin halin rai ko mutuwa yasa hassana fita aguje tayi hanyar gida.tana gaf da kaiwa ta haɗu da ya Aminu. cikin sauri yake tambayarta ina xataje a ahaka atake anan take gaya masa abinda ya faru baiyi ƙasa a gwiwa ba wajan binta makaranta yace karta gayawa mama lokacin da sukaje har an kori ƴan ajin sabida an kasa ɗagata dan haka malaman sukace kawai ai mata roƙiyar anan ajin nasu.
Daga sadiya se hussaina tare da sauran malamai hassana da ya aminun suka shigo ganin halin datake ciki yasa hassana ƙara volume ɗin kukanta!
Seda malama hadi ya buga mata tsawa sannan tai shuru.
Karatu malam najahi ya shiga rerawa akunnen Bebi wanda seda ya shafa mintuna biyar sannan ta soma tari wata iriyar banƙara take tare da kaiwa malam najahi shaƙa, wadda da ƙyar su malam hadi suka ɓambareshi sannan malam najib ya amshi karatun tare da ɗaga murya da ƙarfi, kowa ya dubi Bebi yasan bata hayyacinta sabida wannan uban ƙarfin ansan bana ta bane sabida aljanun nata irin masu mugun ƙarfin nan ne duba da yadda suka taki kanta da mugun ƙarfin gaske.
Birgima ta fara a tsakar wajan kafin ta dage iya ƙarfinta ta yaga kayan jikinta ganin suna ƙoƙarin fidda mata da tsiraici yasa hussaina nufarta a guje ta rungumeta tsam ajikinta ahaka sukaita birgima tare suna kaiwa hussaina yaƙushi da ciwo amman taƙi sakinta harseda karatun yagama jigata su sannan suka soma magana da ƙarfin gaske.
Alokacin malam hadi yacewa hussainar ta cikata, duk da haka seda hussaina ta saka mata hijabin jikinta ita kuma ta warware ɗankwalinta ta yafa sannan taja baya, tabar malaman da mamakin ƙarfin halinta tare da zumunci irin nasu.

Tambayar farko da malam hadi ya somawa aljanin dayake magana shine yaya sunansa? sannan wani jinsi ne shi tare da addininsa.
Amsa ya bashi sunansa musa kuma shi musulmine kuma anan birnin sin yake, kuma dalilin shigarsa jikin Bebi kawai tana burgeshine yadda bata barin kota kwana amman shi ba macuci bane ƙarewa ma akwai dalili mai ƙarfi dayasa ya shiga jikinta wanda hakan yazama sirrinsa.
Ɗaga murya malam hadi yayi.
"Babu wata soyayyya a tsakanin ku da bil adam, sabida haka mu bamu gamsu da bayaninka ba dan haka ka fita daga jikinta".
"Nifa ba tun yau nake jikinta ba, hasalima najima ajikinta nagaya muku inada dalilin dayasa na shigeta, yanxu ma banyi niyyar haurowaba dukan dayake matane naga ze cutar da ita shiyasa nazo dan na kare dukan".
Yakai maganar cikin wani irin sauti.
"Bamu yarda da zamanka ajikinta ba, domin hakan cutarwa ne dan haka tunda kai musulmine kasan girman Allah, to karabu da ƴar mutane".
Cewar malam hadi.
"Nasan girman Allah kuma zan tafi insha Allahu, amman dan Allah kuma ku dinga haƙuri da halinta tunda ita a haka Allah yayota dukan da kuke mata ze iya sakawa mazumuntan mu su

sami faragar shiga jikinta".
"Insha Allahu, Malam musa Mungode".
Cewar malam hadi wata iriyar birgima tayi tare da banƙara tare da sakin atishawa nan ta koma luff ta kwanta kamar gawa.
Ruwa malam najib ya umarci sadiya ta samo, data kawo yay addu'oi cikinsa sannan ya bawa hussaina ta shafa mata harma ta bata abakinta, domin ita hassana bata aikin komai sena kuka!.
Seda sadiya ta taimaka aka ɗagata aka shafa mata sannan ta buɗe idanunta da sukai wani irin jajur kamar gauta.
"Sadiya lafiya kuke shafamin ruwa?".
Tafaɗa cikin rashin sanin halin data faɗa a ɗazun.
"Lafiya ƙalau suma kikai".
Cewar yaya aminu wanda yake tsaye, ganin ya aminu awajan ya bata mamaki watakan dukan malam hadine ya sumar da ita.
Ganin batada lokacin tambaya yasa ta nufi ta miƙe tsaye anan ƙafa tace bata san da wannan ba.
Domin fafur taƙi takuwa wani irin rintse idanu tayi tana salati da sauri da sauri.
Ganin haka yasa malam najib ya sunkuya dai dai ƙafar tata ya tofa mata addu'oi sannan fa aka samu ƙafar ta miƙe amman da duk da hakama tana mata zafi dan seda ta dafa su hassana, suka nufi gida.
Kowa se binta yake da kallo.
Suna fita bakin gate ɗin makarantar sukaga mama cikin sauri duk hankalinta atashe sadiya wadda take gabansu mama ta tara.
"Sadiya ina Bebin take?,yanzu ihsan tazo tana min kuka! agida wai Bebi ta rasu?".
Tafaɗa duk hankalinta a matuƙar tashe seda sadiya ta matsa sannan mama ta hangosu da sauri ta ƙarasa ta rungume Bebin tana shafa kanta.
Malam hadi wanda ya biyosu a baya shiya ɗan yiwa mama magana akan yana son ganinta mintu biyu.
Sakin Bebi tayi ta nufi wajansa.
Bayani yayi mata yadda zata gamsu.
"Allah gani gareka ni Aisha Bebi da aljanu, Allah ka taimakeni kada ka jarabci wannan yarinya bata da wani gata se naka".
Tafaɗa muryarta na rawa amman kana ganinta kasan ta kaɗu amman haka ta daure taiwa malam hadi godiya suka  nufi gida tare da sadiya ya aminu dasu hassana, cikin nutsuwa su hassana ke tallafe da Bebi ajikinsu haka suka nufi gida da ita..........

*HAR YANXU DAI AKWAI TAFIYA BAMU SHIGA CIKI BA, KUDAI KAR KU ƘOSA DANI..............*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*SANARWA!*
_Assalamu Alaikum barkanku da wannan lokaci naga saƙonku akan cewar ni na shiga gasar marubuta sabida kunga sunana a cikin group na 1 jerin suna na 4 To Alhamdulillahi bani bace an ɗan samu mistake ne wajan rubuta sunan inda aka saka *AUTAR MANYA* toba ni bace ƴar uwatace marubuciya mai suna *AUTAR MAMA* wadda itama nake mata fatan nasara fatan alkairi tare da fatan cin nasara acikin wannan gasar har da sauran ƴan uwana marubuta dake ciki dukansu Allah ubangiji ya basu nasara da sa,a Amin ina fatan kuma zakuje kuyi mata voting sabida marubuci ɗan uwan marubuci ne nagode_

*008*

Tunkafin suje gida jikin Bebi yagama ɗumama da zafi wanda atake anan ze baka tabbacin cewar zazzafan zazzaɓine ya shiga jikinta.
Suna gab da shiga cikin gida sukaci karo da iya hansatu wadda ta taho cikin tashin hankali mayafinta aka kamar ma batasan ta yafoshi ba dai dai ba.
Mama ta tare tana tambayarta.
"Maman ƴan biyu, wai mai yasami Bebi ne yanzu naji labarin wajan salisa tazo aguje tana cemin Bebi ta faɗi?".
Iya hansatu ta faɗa duk jikinta yayi sanyi.
"Hmm kedai bari iya wallahi tsautsayi amman dai mushiga gida tukunna bama tsaya anan ba".
Cewar mama wadda taya fito iya da hannunta akan su shiga cikin gida.
Ranka yawa sukai atare zuwa cikin gidan da sauri sadiya taje ɗaki ta ɗauko tabarma ta shinfiɗa musu sannan ta taimakawa su hassanar suka aje Bebi wadda zuwa lokacin ta soma rawar ɗari.
Dukkansu zama sukai a tabarmar in banda ya Aminu dake tsaye yana bin hassana da kallo ganin har zuwa lokacin bata bar kukan! datake yiba.

"Hussaina samo min maganin zazzaɓi acikin kwabar kayan kwalliya seki zo ki samo mata ruwa abata".
Cewar mama wadda take tube mayafinta daga jikinta.
"To mama".
Hussaina ta faɗa tare da tashi da sauri tayi cikin ɗakin.
Fita yaya Aminu  yayi  batare daya cewa kowa komai ba,lokacin daya dawo har anbata maganin hannunsa ɗauke da baƙar leda miƙawa hassana yay wadda ta daina kukan! yanzu sannan yace mata ta bawa mama magunguna ne ya siyowa bebi a chamist harda tsire gashashshe.
Bayan mama ta buɗe ledar godiya ta masa sannan yai musu sallama yabar gidan.
Mama ce ta kuma duban iya a karo na biyu.
"Wallahi iya nima ina zaune ihsan tazomin...............,"
Tass! ta kwashe komai ta gayawa iya wadda take tafa hannu tana salati.
Sannan tacewa mama.
"Allah ya bata lafiya ai baxamu zauna ba sabida aikin iska yafi karfin tunani dole zamuje rimin gado dake gidan ƙanin mahaifina ya taimaka mana da roƙon Allah"..
Cewar iya wadda take kallon mama domin taji me zatace.
"To iya insha Allahu bari ƙarshen wata yazo semuje ɗin kafin nan kuɗin adashin dana saka na amsa".
Mama ta faɗi tana kallon iya.
"To babu damuwa Allah ya sawwaƙe ya nuna mana lokacin Amin".
Cewar iya wadda take ƙoƙarin miƙewa tsaye.
Bayan iya ta miƙe duban sadiya tayi wadda take gyangyaɗi.
"To Auta tashi maza mutafi gida anfara taskar labarai darefa yayi".
Tura bakinta tai gaba tare da cewa...
"Ni dai dan Allah iya ki barni yau ɗaya nai jinyar Bebi".
Tafaɗa kamar zatayi kuka! mamakin shaƙuwar Bebi da Sadiya iya take kullum suka haɗu se anyi faɗa amman ɗaya baya ƙaunar yaga ɗaya cikin damuwa.
Ko cuta Bebi take tofa sadiya setayi aminai ne na ƙut amman duk wannan amincin nasu baya hana aci uba idan ta ɓaci.
"To masu jinya Allah tashemu lafiya".
Iya ta faɗa tana dariya! mama ce tabi bayanta domin ta mata rakiya suka nufi kofar soro.

Sun jima suna tattaunawa akan lamarin lalurar Bebin sannan iya taiwa mama sallama, ta nufi gidanta.
Mama tana ƙoƙarin zama Shahid na doko sallama gidan.
Turus yay da baho akansa sabida ganin Bebi lulluɓe tana rawar ɗari ƙarar sautin kuma har kunnensa.
"Mama meya sami wannan yarinyar?"
Yafaɗa yana aje bahon a bakin rariya sabida tuwon ya ƙare tas.
"Hmm aika zauna tukunna kodaga tsayen zakaji mai ƴar uwa?".
Mama ta faɗa tana mamakin shaƙuwa irinta ƴaƴan nata.
Jiba kamar ba,aci uba ita dashi ba ɗazu amman jiba dayazo ya tarar ta ahaka duk yabi ya ɗaga

hankalinsa.
Motsin! zaman shahid  akusa da mama ya dawo da ita daga tunanin data afka na lamarin ƴaƴan nata.
"Mama kimin shuru lafiyarta ƙalau kuwa?"
Yafaɗa yana yaye lullubin Bebi yana taɓa jikinta dayay zafi rau kamar gaushin wuta.
Da sauri ya janye hannun nasa yana yarfewa.
"Kai mama ai wannan babu lafiya zazzaɓi ne bara na siyo mata magani inada kuɗi ajikina".
Yafaɗa yana miƙewa tsaye jikinsa yana rawa!.
Wannan kalamin na shahid shiya saka mama hawaye.
Nima kaina mai rubutun seda naiwa yaron hawayen tausayi.............

_GUNTUN PAGE KUYI HAƘURI PLS_

*AFUWAN YAU INA UZURINE WALLAHI DA ƘYAR NAI MUKU WANNAN SHAFIN AMMAN KU TARENI ZUWA DARE INSHA ALLAHU RABBI, NAGODE DA BIBIYATA DA KUKE*🙏

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*009*

Kamo hannayensa mama tayi tare  da jawoshi jikinta.
"Zauna ɗan albarkata, ka kwantar da hankalinka, yanzun nan yayanku Aminu ya siyo mata magani insha Allahu babu wata matsala".

Tafaɗa bayan ta zaunar dashi daga gefen jikin nata.
Zama yayi amman duk jikinsa yayi mugun sanyi, ciro kuɗin cinikin  tuwon yayi tare da miƙa mata.
Ƙirgasu tayi cif suke babu ƙwandala data ɓata koda yake daman tasan shahid baya ɓatar da kuɗi, ko Bebi ma kawai tsabar sakarcin tane.
"Allah yay maka albarka ɗa ɗaya tamkar da goma, maza tashi kaje shago ka kwanta kaga gobe munada sammakon safe".
Shahid na ƙoƙarin tashi seya fasa ganin Bebi tana yunƙurin tashi daga kwanciyar datayi.
Gaba ɗayansu zuba mata idanu sukai harta miƙe batare datayi musu magana ba, gaban rariya taje ta wanko bakinta sannan ta dawo duk jikinta yana mata zafin zazzaɓi, amman ina bata damu ba, hankalinta yanaga wannan baƙar ledar data ƙyallah idanu ta hangota gefen mama, daman ita ciwo baya hana ta kai loma.
Hannu ta saka tana kici-kicin janyowa cikin ɗunbin mamaki hassana take kallonta.
"Ke BEBI yanzu duk nauyin dakika zuba mana ɗazu garin ɗauko ki kina makyar kyatar zazzaɓi baze saka ki mana godiyaba, sedai ki ɗauki leda burinki kenan?".
Cewar hassana wadda haushin ko in kular data musu yaɗan bugeta.
"Hmm kema dai hassana da ɓata bakin ki, kike kin manta da wadda kike magana kenan?".
Cewar hussaina wadda take hararar
 Bebi domin gabaki ɗayansu tayi mugun basu haushi.
Ko kallonsu batayi ba sema zazzage ledar datayi.
Ganin tayi idanu Biyu da tsire a fake a baƙar leda daban yasa ta zabga wata shegiyar shewa! Kafin muryarta ta karaɗe ɗan tsakar gidan nasu.
"Ahayye! shagali ni ai wannan duka na malam hadi da goshi yazo mini ko banza nayi brush da tsire".
Tafaɗa tana buɗe ledar wadda har yawunta seda ya ɗiga a saman takardar.
Sosai ta basu dariya da mamaki har seda mama ta dara afili tabbas ta yarda ɗiyar tata nada iska, duba da yadda watarana take acting ɗinta kana gani kasan seda uzuri.
"Kekuwa Bebi meyasa wataran baki da kan gadone, daga ganin abu babu tambaya har kin ɗauka gakuma dare yayi amman kike wannan shegiyar shewa kamar tsohuwar bazzawara".
Cewar mama wadda take kallon Bebi ɗin.
"Toni mama meye ruwana da dare, amman dai nasan wannan garar babu ta kowa face tawa, wayyo! ni ƴar abbanta yau zanyi ƙaramin party da tsire".
Tana faɗin haka ta ɗauki ɗaya ta saka abakinta ta lumshe idanu tana luma haƙora tana tanɗewa kamar wata kura.
"Wayyo Allah na masu kuɗi suna shagalinsu, aini Allah yay min arziƙi tofa kullum semunci tsire mun donge ƙullinki mamata daban".
Tafaɗa tana kuma ɗaukar wani gudan ta afka abaki tana tanɗewa tana lashe hannayenta.
"Waike wace irin yarinya ce?, watakan ke ɗayace mai rai agidan kenan kanki kaɗai kika sani, wallahi ina jiye miki wannan halin naki na sonkai ai ko ƙannenki kya sanwa amman kiketa faman ci ke ɗaya".
Mama tafaɗa tana warce ledar seda ta bawa kowa sannan ta miƙa mata yanka biyu.
"Ke amshi wannan tunda kinci biyu".
Tura baki tayi gaba nan da nan idanunta suka sauya kala.

"Ni wallahi wannan yamin kaɗan haba mama jibi fa dan Allah ki ƙaramun anaki".
"Bazata ƙaraba malama idan bakya ci ajeshi anan banza marar hankali"..
Cewar hassana cikin ƙufula.
"Nidai ba banz........,
"Kull ɗinki Bebi inji kin rama, kekuma ban hanaku zage zagen nan ba?".
Cewar mama ta juya tana kallon hassana.
"Yi haƙuri mama wallahi Bebin ce da abin haushi komai ita kanta ta sani kina kallon jiya da malam ya aiko mana da fura da nono kafin kizo ki fiddawa kowa tasa itafa harta sha fiye da rabi".
Tafaɗa cikin jin haushin abinda Bebin ke musu wataran.
"To hassana tunda haka Allah yayota aise haƙuri wataran se labari ina gaya muku a kullum cewar kada ku ɗauki wannan rayuwar da muke a madauwamiya wataran komai ze zamo tarihi idan babu mutuwa akwai aure kowacce rayuwarta ba mai ɗorewa bace ba anan gabana nafi muku fatan kuje can kuyi rayuwa da mazajenku lafiya".

"Hakane mama amman wallahi idan har wannan yarinyar tace haka zataje taiwa mijinta kullum kuwa seyaci  ubanta".
Cewar shahid wanda haushinta yagama cikashi.
"Kaikuma ina ruwanka sarkin baƙin baki ni bama zanyi auren ba sedai duk kutafi ku barni da mama ina cin daɗi na".
Kallon ƙuruciya mama takewa Bebi tare da ayyana yanayin girman jikinta wanda tsaf idan aka kalleta za,a iya ɗauka itace gaba da ƴan biyu.
Sannan tace.
"Kema ƙuruciya ke ɗibanki bana miki fatan zaman gabana kema Allah ya kawo miki mijin arziƙi na aurarki na huta".
Tsirenta ta lamushe tare da miƙewa tai ɗaki tana gunguni itafa bata son aure inama take da saurayin bare wani aure tabb bata ma san maye soba bare auren.
Kwanciya tayi aɗaki tana tunanin gobe yadda siba ze kalleta awajan sayar da awarta sabida rashin m ɗin data karta masa.
Tanajin sautin hirar mama dasu hassana ganin baccin baizo mata ba yasa ta miƙe zuwa gaban sif ɗinsu kayanta ta cire tai tik, tare da ɗauro zani a kirjinta sabida anyi ruwa garin yaɗanyi sanyi ita kuma bata kaunar kwanciya da kaya.
Harta koma kan katifar xata kwanta sekuma ta kuma komawa gaban sif ɗin tare da ɗaukar wata ƴar shimi wadda tsayinta ya kaimata dai dai ƙwaurinta.
Tube zanin jikin nata tayi domin aranta take faɗin gwara ta saka rigar sabida mama ta hanata kwanciya da zani domin tsakar dare zanin kama gabansa yake.
Ƙurawa farar fatar jikinta idanu tayi musamman wajan cinyarta inda har wani jajur tayi sabida farin wajan fatar ta irin lugwi-lugwi  ɗin nan ce wadda idan ka dubeta bazaka taɓa zaton ta taso gidan wahala ba, sabida gogewa tare da murjewar fatar jikinta.
Bebi tana da wani irin baiwar kyau mai fisgar hankali, farace ita tas mai ɗauke da wani irin kyau mai ƙayatarwa matsagaiciya ce itaba doguwa can ba, kuma ita ba gajeraba, gashin kanta, irin mai curewar nan ne wanda yake bawa mutum wuya wajan kitso, domin mugun taurinsa shiyasa bata ƙaunar taɓa wannan kan  ko kaɗan, kuma babu laifi tana da cikar sumar sedai rashin

tsahonta.
Tana da gashin idanu zara-zara haka zalika girarta acike take,halittar kirjinta acike take sabida nononta irin mai ƙasan ƙwaryane waɗanda suke a tsaye ƙyam babu alamun zubewa atare dasu, gasu cikakku farare tas sedai ko kaɗan basu fidda kai ba saboda ƙarancin shekarunta.
Daga ƙasanta tana da cikar hip's wanda idan zata saka skirt wani zubin seda tsalle.
Bebi tana da kyawunta dai dai misali mai ƙayatarwa.
Saka rigar tayi ajikinta tare da nufar katifa tai kwanciyarta bata jimaba barci mai daɗi ya fisgeta.
Ko shigowar su mama bataji ba seda Asuba dataji mama tana tashinta a barci.......................

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*10*

Tsadaddiyar motace ƴar gaske black colour haka zalika window ɗinta ma tinted ne, irin wadda ake cewa sedai na ciki yaganka badai kai ka ganshiba, Fake take awani tangamemen bakin gate wanda aka rubuta *MAI ATAMFA INVESTMENT NGR LTD* da manyan harufa, cikin sauri tare da zafin nama irin na cikakkun maza masu jini ajikinsu matashin saurayine wanda baze gaza shekaru talatin da bakwai da haihuwa ba, dogone sosai mai murɗaɗɗan jiki irin na majiya ƙarfi hasken fatarsa baƙar fatace,mai ɗauke dawani irin gogewa tare da ɗaukar hankali, kallo ɗaya zakayi masa kaji ya kwanta maka acikin zuciyarka, sabida yadda Allah yayi masa baiwar cikar haiba tare da kamala, da ƙaton tabon abin sallah nafara cin karo shinfiɗe a saman goshinsa wanda har wani irin kurji kurji yayi sabida bayyanarsa.
Yana da manyan idanuwa masu haske tare da ɗaukar hankali, waɗanda kallo ɗaya zewa marar jin magana dasu ya hukuntashi hancinsa dogone mai ɗan faɗi kaɗan tare da ɗan baki ma daidaici, mai ɗauke da fararen haƙora tarr gwanin sha,awa, saman sumar kansa irin askin nan yay na manyan maza wato saisaye seɗan gemun daya bari kaɗan tare da sajen daya ƙara ƙawata masa kyawun fuskarsa,Sanye Cikin wata azabbiyar shadda wadda ta amsa sunan ta

shadda mai kalar golden yake batare daya saka hula akansa ba, se takalminsa mai buɗaɗɗan sama wanda ya bada kala da ruwan shaddar jikinsa, cikin sauri ya buɗe marufin motar ya fito kunnensa kare da wata tsaddiyar waya mai mugun kyau, Hannunsa nabi da kallo wanda yaji manyan zobunan azurfa guda biyu gawata irin kwantacciyar gargasa databi saman hannun nasa har wajan tsakiyar yatsunsa ta lafe gwanin sha,awa da ita.
Cike da zafin nama yake taka ƙafafunsa wanda yabani tabbacin cewar cikin wannan kamfanin ze shiga duba da yadda ya nufi ƙaramar ƙofar datake kusa da gate, ɗin,fuskarsa babu wata far'a yake doka ƙaramar ƙofar da ɗayan hannunsa wanda bai riƙe wayar dashi ba.
Cikin sauri wani security yazo yaɗan leƙo da kansa ta ɓular datake tsakiyar ƙofar ganin wanda ke buga musu ƙofar yasa jiki na rawa yazo ya buɗe masa ƙofar tare da rissunawa yana masa barka da zuwa, cikin sauri ya wuce security ɗin batare daya amsa masa ba sedai hannunsa ɗayan daya kuma ɗaga masa still alamun baze iya magana ba, sabida wayar dake kare a kunnensa.
Tunda ya shigo cikin kamfanin ma'aikatan cikinsa ke kawo masa gaisuwa kowa ya gansa seya rage tsayinsa sedai kaji ana "OGA ALIYU barka da fitowa" wannan kalamin yana matuƙar ɓata masa ransa tayaya zasu dinga masa haka, bayan sunsan cewar duk ɗaya suke, wallahi jiyake aransa inda yanada yaddaze ya datse wannan girman da suke bashi dase yayi sabida sam bayaso amman rashin maganarsa da tsabar miskilancinsa yasa yagaza furta musu abinda yake ran nasa, to inama yake da lokacinsu bare ya tsaya yi musu bayani.
Wata ƙofa yabi mai girma wadda take ɗauke da wani ƙaton office wanda aka rubuta *MD ALIYU IDRISS MAI ATAMFA* da manyan baƙi, cikin sauri sakataren sa ya tawo gabansa yana zubewa tare da fara gaisar dashi cike da tarin ladabi hannun dai yakuma ɗaga masa tare da raɓewa yanufi cikin wannan office wanda yake ɗauke da table ɗin takardu daban wajan system daban ga kuma wani ɗan medium room nan duk acikinsa, saman wata one seater ya nufa tare da zama, yana cigaba da saurararan wayar dayake har seda ya ɗauki mintuna kafin yay sallama.
Ɗago idanunsa yay waɗanda nima kaina seda nakusan yada abin rubutu na saboda kyawunsa daya gigitani, zubawa sakatare idanu yay wanda yake gurfane gabansa yana jiran yaji meze ce masa.
Cikin nutsatstsiyar muryarsa mai ɗauke da kamala, wadda sam baya ɗagata wajan fidda magana yace.
"Am sorry nura inaiwa baƙinmu bayani ne".
Yafaɗa ataƙaice.
Sosa kai nura sakatare yay tare da kallon ogan nashi kana yace.
"Haba dai oga wani irin nai haƙuri ai kafi ƙarfin haka,Yau ai naga baka shigo office da wuriba nace ko lafiya sabida oga usman ma yazo kusan sau biyar bai gankaba yace ya kira wayoyinka swich off".
Lumshe idanunsa yay tare da mayar da kansa baya kaɗan yana ɗan sosa saman kan nashi da key ɗinsa dabai riga ya ajeba.
Tsaki yaja kaɗan.
"Motana ta samu problem ne yanzun haka tana bakin gate nima banso nai lates ba saboda nasan akwai new vistors dazamuyi yau".
Yafaɗa tare da zira hannunsa acikin pocket ɗinsa, counter ya ɗauko ya saƙala yana motsa baki a hankali wanda yabani tabbacin tasbihi yake ga sarki buwayi gagara misali.

"Haba nidai nasan oga inba wannan matsalar ba baka kaiwa har 12 baka shigoba Allah dai ya tsare mana kai".
Nura sakatare ya faɗa tare da kuma russuna kansa ƙasa.
Bai tankawa nuran ba kamar yadda nuran yasan da haka, sema ƙara mayar da kansa baya dayay sabida ko kaɗan shi mutum ne marar magana yafi buƙatar yayta istigifari a fili dazuci akan ya zauna yayta maganar da bazata amfane shiba, shiyasa yake mamakin jarabar surutun usman.
"Nura shigomin da files".
Abinda ya faɗa kenan tare da rintse idanunsa yana cigaba da tasbihinsa.
"Angama oga".
Nura yafaɗa cikin sauri ya tashi ya fita zuwa office ɗin kusada dana ogan nasa.
Mintuna uku nura ya shigo hannunsa shaƙe da manya manyan files asaman table ya zubesu tare da rissunawa kana yabar office ɗin.
Wayarsa dake gefe itake ringing!
Da kallo yabita ganin mai kiran yasa ya danna busy.
Sannan yay dial number.
"Assalamu Alaiki, Eh naje Ammi ok, zan kira letter I'm busy now!"
Yafaɗa cikin tattausar murya kana ya datse kiran ya nufi gaban kujerar dake fecing ɗin wannan table ɗin ya zauna tare da soma abinda ke gabansa.
Yajima yana gudanar da ayyukan dake gabansa.
Kafin yaji ana knocking dorr ɗinsa.
"Yes come in"!yafaɗa idanunsa kan takardun dake gabansa.
Wani magidancin mutum ne ya shigo bakinsa dauke da sallama.
"Haba tuzurun Ammi yau ina kashige ne kaƙi fito mana aiki da wuri gaskiya semunci tararka".
Cewar wannan magidancin daya shigo office ɗin yanzu.
Wata harara ya zabga masa tare da haɗe rai tamau saboda ya tsani sukirashi da wannan sunan, baya so ko kaɗan amman yaga alamar yayyen nasa so suke su mayar dashi wani bitacan dan jiyama yana jin ya abbakar yana gaya masa hakan but amman bai tankaba.
"Kaga malam rabu dani in gama aikina wallahi gobe Abba ze dawo kada ka haɗani dashi".
Dariya magidancin ya saki tare da furta..
"ALIKON ABBA kaima kasan abba baze maka komai ba, yau inda dai mune da mun banu".
Bai tanka masa ba kuma bai ɗagoba illah cigaba da aikin gabansa dayake sabida yasan ya biyewa ɗan uwan nasa USMAN sesu wuni ba,ai uwar komai ba.
"Oga Aliyu.................

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*11*

"Oga Aliyu" yaji an kirawo sunansa gabaki ɗayansu basuji sallamarta ba bare suji buɗewar ƙofarta illa ganin ta dasukai akansu.
Wani irin wawan tsaki yaja tare da mayar da kansa ga aikin gabansa, Usman ne ya dubeta tare da cewa, "A,a lina har kun tashi kenan haka da wuri hope dai babu wani matsala?" matsowa tayi gaban table ɗin daya sada kansa tana aika masa da wani irin shu'umin kallo tamkar zata lashe shi tunda take bata taɓa ganin haɗaɗɗan namiji kamar *HAIDARA* ba tana kwaɗayinsa tana buƙatar sa ajikinta tana son taji ta rabu acikin faffaɗan kirjinsa wanda take ayya irin raɓar dazata kwasa a wajan sedai kash ta makaro domin shi ko kallo bai yarda ya haɗasu ba.
"O.g.a.A.l.i.y.u" ta kuma faɗi a rarrabe batare data baiwa usman amsar tambayar dayake mata ba, ɗago idanunsa yayi a karo na biyu tun bayan shigowarta tare da zaro mata manyan idanunsa waɗanda suka kuma firfitowa fuskarsa babu alamun sassauci bare taga waje.
"Ke! stay out from my office"! yafaɗa yana watsa mata wani banzan kallo, ganin tana binsa da idanunta yasa ya kuma ɗagowa "I say get out!"yafaɗa tare da dukan table ɗin da ɗan ƙarfi kaɗan yanajin zuciyarsa tana bugawa da ƙarfi kamar wanda yay gudu.
Jiki na rawa ta raɓe fitt ta fice a office ɗin cikin jin haushi.
Tana fita yaja ajiyar zuciyar tare da lumshe idanunsa ya mayar da kansa jikin kujerar yana jin kansa yana sara masa wannan wani irin masiface agida ba,a barka ba a office ma haka yarasa me mata ke gani a tare dashi suke liƙe masa.
"Tuzurun ammi yakamata ka dai naiwa lina hakafa sabida kaga ba musulma bace kada taga kamar kana jin ƙyamar addininta ne".
Yaji muryar usman cikin dodon kunnensa.
Ɗago idanunsa yay tare da zubawa usman batare daya ce masa komai ba amman tabbas! bada ban usman ɗan uwanshi bane daseya gaya mashi magana mai zafi.
"Wannan tsarin naka bai ba, shin waikai bakada feeling ne kamar sauran mutane?".
Still usman ya kuma jefa masa wannan tambayar.
"Eh bani da dutse ne ni, ko angaya maka kowa sarkin kwashe, kwashe ne kamar kai?, Ok ba matsala xaka iya ƙarama zainab ay da wannan ɗin".

Yafaɗa tare da mayar da kansa ƙasa.
Wata shegiyar dariya usman ya saki tare da cewa.
"Aikam kaima kasan gaf nake danni senai huɗu ciff waya gaya maka kowa irinka ne ai wallahi senasa ammi ta ɗauko maka mai roƙiya kai ace baka da abinki se wadda tace tana sonka, yanxu dai ai abba ya gama komai nan da ƴan kwanaki kaɗan kazama na khadija".
Yafaɗa yana dariya........
"Ni wallahi dama ni aka haɗa da ita dase nai tsalle amman kai ka samu kana yanga".
Wata harara ya zabga masa tare da miƙewa cikin wannan ɗan room ɗin ya shige yabar usman a tsaye sake da baki.
Mintuna kamar biyar ya fito hannun rigarsa a tattare kansa jiƙe da ruwa da alamun alwala yayo.
Batare daya kula usman ba yabar masa office ɗin.
Fita yay daga section ɗin nasu baki ɗaya ɗayan section ɗin ya shiga inda anan ma'aikatan kamfanin ke da office kuma sannan anan ake fidda komai a shigo da komai, haka zalika masallacinsu shima duk anan yake kasancewar section ɗin yanada mahaukacin girma.
Tunda ya fito suke masa barka da fitowa harya ƙarasa cikin babban masallacin abin mamaki yawanci ma'aikan duk suna zaune aciki yana zuwa suka miƙe gabansu ya shiga yaja musu jam'i cikin daddaɗar muryarsa cike da nutsuwa yake jansu har suka iddar da sallar, bayan anyi addu,a an shafa ya gaggaisa da jama'ar masallacin kana yabaro nan ya taho wajan daya kasance muhallinsa anan ma'aikatar.
Baiga usman ba dan haka ya ƙara gudun AC'n cikin office ɗin yacigaba da aikin gabansa.
Ƙarfe huɗu ya kuma kowama cikin masallacin sukai sallah sannan ya dawo office aiki yake da ƙarfinsa da lafiyar da Allah ya bashi.
Ƙarfe biyar da kwata usman ya shigo tare da azalzalarshi akan yazo su tafi gida shi yana da wadda take waiting ɗinsa..
Murmushi kawai yay bayan yagama jin tabakin usmanɗin  wanda murmushin yay mugun yimasa kyau batare dayace komai ba, yaɗauki laptop ɗinshi daya bari jiya tare da wayoyinshi.
Gaba yay yabar usman batare daya kulashiba da nura sakatare sukaci karo wanda yake ƙoƙarin amsar laptop ɗin cikin kulawa ya dubi nura.
"No barshi jeka kulle office akwai key a saman table and pls kaje gareji ka amsomin motana ka kawomin gida pls".
"Angama mai gida".
Nura ya faɗa cikin kulawa sannan shikuma Aliyun ya wuce da ƙyar usman ya cim masa acan farfajiyar kamfanin sabida Aliyu yana da zafi shiyasa komai nasa yake da zafi zafi baya sanya namijine na gasken gaske.
"Kai dallah ina can sake da baki ashe kayo gaba ka barni".
Usman ya faɗa cikin ƙufula bai kula shiba illah gaban daya kumayi cikin sauri.
Gaban wata ash corolla, suka nufa usman ya zauna a driver seat shikuma ya zauna a front seat batare da ɓata lokaciba security's suka buɗe masu gate ɗin tare da ɗaga musu hannu.
Usman kaɗai ya maida musu shikam ƙasa yay da kansa yana danna wayarsa.
"Amman yakamata ka fito kaiwa su abba bayani sabida gudun matsala".
Cewar usman wanda hankalinsa ke kan titi, wanda kai tsaye titin yahaya gusau ya ɗauka.
Ɗage girarshi yay ta ƙasa alamun bai gane ba tare da kumayin ƙasa da kansa.
"Ina nufin kacewa abba baka da lafiya a nema maka magani, gudun kada ka cutar mana da

ƙanwa".
Usman ya faɗi yana guntse dariyarsa.
Hannunsa yasaka yaɗan shafo gemunsa kaɗan yana sakin wani irin killer smile wanda na kasa gane na komaye batare kuma daya tankawa usman ba........

*INA MASOYANA MASU BIBIYAR LITTATTAFAINA YAUMA TAFE NAKE DAWANI ALBISHIR GAREKU KO SHIN KUNSAN NA SAKI ZAFAFAN LITTATTAFAINA GUDA BIYAR AKAN FARASHI NAIRA DUBU ƊAYA? WAƊANDA SUKE HAƊE COMPLT A DOCUMENT ƊINSU DA KIN SIYA SE KARATU*
*ƊAN MAJALISSA*
*KOBA SO*
*HASKE*
*RABON WANI*
*DA IZZATA*
*DUKKANSU AKAN FARASHIN NAIRA DUBU ƊAYA COMPLT GAMAI SO YA KARANTA SEYAY MIN MAGANA TA WATSAPP NUMBERTA KAMAR HAKA 08142105218*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*12*

"Hmmmm kaji wasan yafi ƙarfin kanka ko?, aidaman nasan bazaka ce komai ba tunda kai dai bakada kuzari anan wajan".cewar usman wanda gabaki ɗaya hankalinsa yana kan titi amman tsabar jarabar surutunsa yasa yana tuƙin yana magana, tsaki *Haidara* yaja kaɗan tare da mayar da hankalinsa bisa kwalta yana kallon yadda motoci da adai dai ta sahu da babura ke shawagi akan babban titin sharaɗa yahaya gusau.
Tabbas kano tacika babban birni gari mai tarin albarka kano ta dabo cigari kano ta dabo tunbin

giwa kodame kazo anfika, lumshe manyan idanunsa yay yana ayyana yadda yake matuƙar son wannan gari mai tarin albarka.
"Wai ni kamayar ɗan iska inata surutun banza ko?, kayimin banza sabida rainin wayo waikai dan Allah bakajin bakinka yana wari?".
Cewar Usman wanda yake kallon Haidara cike da takaicin wannan muskilancin nasa.
"A,a to mezan ce maka?, kayi tambayarka kuma kabawa kanka amsa to kuma maiyay saura, nikam surutu baya cikin tsarina gwara naita yiwa ubangijin girma tasbihi ana taramin ladan akan naita surutun da baida amfani, wanima idan nayi zunubi xa,a rubutamin".
Yafaɗa tare da jingina kansa ajikin seat yana motsa bakinsa alamun tasbihi yake ga sarki buwayi gagara misali maikowa mai komai maƙagin sammai da ƙassai wanda mulkinsa baya ƙarewa.
"Kai masha Allahu wallahi Kanafa burgeni mutumina ɗabi'unka abin koyine ina godiya ga sarki Allah dayasa kazo acikin zuri'armu Allah ya ƙara mana suttura da'ima".
Cewar usman ya faɗi hakan yana maijin daɗi acikin ransa shi kansa ɗabi'un Aliyu yana burgeshi mutum ne nutsatstse mai hankali da kamala sam baya da hayaniya bare yawan magana idan yana office zaka gansa zaune yana aikinsa, idan yana gida zaka ganshi a ɗakinsa riƙe da alkur'ani mai girma yana karatunsa, kokuma ka ganshi zaune akan sallaya yana nafilfilunsa, sedai fa akwai tsare gida da miskilanci haɗi da mugun taurinkai da saurin zuciya abu kaɗan kesaka ALI fushi musamman akan ƙannansu suna mugun shakkarshi hatta yayyenma suna shakkarsa sabida bai cika sakin fuskarsaba bare ka, kawo masa raini, amman ga wanda yasanshi shiɗin mutum ne mai daraja ɗan adam sam baison yaga wani ya wulaƙanta yana da mugun tausayi da rauni, shiyasa sam abin hannunshi bai rufe mashi idanunshi ba idan ya maka wata kyautar wallahi sekai kukan daɗi sabida bai iya kyauta kaɗan ba.
Da kallo Haidara yabi usman ganin yay shuru kamar yana nazari, ɗan taɓoshi yay kaɗan"Hy malam kada ka zubda mufa, gwarakai ana shirin juye maka nikam banga komai ba". yafaɗi maganar a fusge kamar ba shiba.
Jan ajiyar zuciya usman yayi tare da kallon Haidara kaɗan sannan yace"Wallahi Man kawai tunanin irin kyawun ɗabi'unka nake wallahi kaji daɗinka fa".Usman yafaɗa yana mai karya kwanar dazasu shiga tare da danna hancin motarsa cikin kwanar.
"Hmmm ɗabi'una idan har masu kyaune to ba burgeka nake son suyi kaɗai ba No ina son ka koyesu, musamman ma wannan surutun naka dan Allah ka rageshi haba mutum kamar aku" Yafaɗa yana ƴar dariya kaɗan.
Wani irin kyau dariyar tayi masa musamman yadda dimple point ɗinsa suka lotsa kaɗan ga fararen haƙoransa sun ƙara wani haske tamkar ƙanƙara.
Sakin baki usman yay sabida daman idan kaji Haidara na irin wannan dariyar tofa yaɗan kunno usman ne.
"Aikuwa kayimin one zero wato nikeda surutu ko?, hmm zamu haɗu next wallahi sena rama" usman yafaɗa tare da karya wata kwanar still wanda cikin layin da suka shiga ya kasance tsitt babu alamun hayaniya ko kaɗan tafiya mai ɗan nisa sukai tare da nufar wani mahaukacin tangamemen baƙin gate wanda aka rubuta *ALHAJI GIƊAƊO MAI ATAMFA ESSTATE* da manyan baƙi tundaga nesa da gate usman kefaman zuba uban horn cikin sauri wasu ƙartin sojoji suka tawo cike da ƙarfi da zafin nama suka wangale ƙaton gate ɗin aguje motar usman ta faɗa cikin farfajiyar wannan gate wanda cikinsa yay kama da wata anguwar sabida girman

esstate ɗin.
Wajan adana motoci ya nufa waɗanda su kansu motocin gasunan burjik kamar banxa kowacce da kalarta parking ya gyara tare da kashe motar sannan ya dubi Haidara,"Malam seka sauka ka ƙarasa part ɗinku da ƙafarka dan wallahi bazan ƙarasar da kaiba anan parking lot ɗin naga damar ajeka" batare daya tankawa usman ba ya buɗe ya fita yana mai shaƙar iskar waje ƙafafunshi ya taka har cikin part ɗinsu hannunsa riƙe da system ɗinsa wanda daga parking space ɗin zuwa cikin part ɗin akwai ƴar banxar tafiya anan na fuskanci ashe esstate ne ƙaton gaske mai ɗauke da part kusan bakwai, daga gate ɗin farko kenan wanda ya kasance na iyaye domin shi Haidara  part ɗin farko ya shiga shikuwa usman  gate na biyun ya nufa wanda nake tunanin ko anan sukesu.
Gaban wani ɗan medium size gate ya tsaya tare da saka hannu yaja shi ya buɗe ya shiga babban gidane wanda ya tsaru ya haɗu ƙofar farko ya buɗe wadda ta kasance kana shiga xakaga katon falo wanda yasami nasarar lamushe manyan saitin kujeru kusan uku, zube ƙafafunshi yayi asaman lallausan carnies carpet ɗin dake malale a tsakiyar falon bai tsaya anan ba wani corridow yabi wanda yayi ƴar tafiya kaɗan daga gefan corridow ɗin ƙofar wani falonce still, sekuma step ɗin bene wanda nan naga ya haye yana tafiya da zafi-zafi hannu ya saka ya buɗe ƙofar falon saman tare dayin sallama abakinsa ƙaton falone wanda yaci kujeru saiti biyu se babbar tv plazma, ƙatuwa akan tv stand se two bedroom dake cikin falon tare da ƴar wata ƙofa a gefe wadda nake zargin ko ɗakin da furji yakene.
Room ɗin farko ya tura ya buɗe ƙofar tare dayin sallama sannan ya shiga ciki wani irin ƙamshine mai sanyi ya shige masa jikinsa tare da daddaɗan sanyi mai ratsa ɓargon jiki.
Kan ɗan medium table ɗin dake tsakiyar ɗakin ya aje system ɗinshi tare da wayoyinshi, se asannan nabi ɗakin da kallo babbane sosai babu wani shirgi cikinsa daga ƙaton close set se wani lafiyayyan bed mai girman gaske wanda aka ƙawatashi da white bedshit da pillows masu kyau, ɗan dressing mirrow ne a gefe wanda aka aje hand drayer tare da cream, se sopa da wannan table ɗin se Bathroom ɗin dake gefe daga wani ɗan kwana.
Botiran gaban rigarshi ya fara buɗewa...........

*BONONZA BONONZA ZAFAFAN LITTATTAFAI 5 AKAN FARASHIN 1000 COMPLT DOCUMENT*

*ƊAN MAJALISSA*
*RABON WANI*
*KOBA SO.......*
*H A S K E*
*DA IZZATA*
_Idan kin shirya biya hanzarta nemana anan 08142105218_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*Assalamu Alaikum ina yiwa ɗaukacin ƴan uwana musulmi barka da shigowa cikin sabuwar shekarar addinin musulunci ya rabbi ka sadamu da alkairin cikinta kasa mun shiga acikin alkairi da sa,a amin, ya rabbi ka yafe mana laifukanmu kai mana tsari daga dukkan sharri amin barka dai ƴan uwana musulmi 1443AH*🥰

*13*

Ya shiga ɓalle botiran gaban rigarsa dagashi se singlet da wandon shaddar dake jikinsa ya shiga bathroom ya haɗa ruwan wanka sannan ya fito waje arayuwarsa shi mutum ne mai kunyar wani ya ga jikinsa wannan dalilin yasa da wuya kaga Haidara zaune da singlet ko 3qrt sedai tsananin zafin gari ke sakashi hakan kasancewarsa mutum mai yawan gargasar jiki shiyasa yake ma'abocin jin zafi,janyo bathrube ɗin dake hangar cikin bathroom ɗin yayi tare da suturta jikinsa da ita sannan ya jefa kayan daya cire cikin washing machine, ɗin dake bathroom ɗin, Ya jima acikin bathroom ɗin wanda ga dukkan alamu shiɗin yana ɗaya daga cikin maza masu daɗewar wanka, kafin kuma naga ya fito jikinsa rufe cikin rigar wanka tare da ƙaramin tawul akansa gaban wannan madubi ya tsaya tare da goga mai agurguje turare ya fesa cikin mintuna kaɗan ya shirya kansa cikin jallabiya ruwan toka mai yankakken hannu, bayan ya kammala shirinsa ya jefa rigar wankan a acikin injin wankin dake banɗakin tare da fitowa ya nufi falonsa yana faman zuba uban ƙamshi mai sanyi da daɗin ji, gaban Tv yaje ya kunna tare da kamo tashar saudi karatun shaik Abubakar sudais ne ya karaɗe falon, yana tafe yana bi har zuwa jikin wannan ƴar ƙofar dake tsakiyar ɗakunan barcin nan nashi.buɗewa yayi ya shiga babban furjine ƙato a ɗakin se coffee machine dake gefe se jerin cup's dake lulluɓe da farin hanky se sink na wanke-wanke, gaban wannan farin hanky ɗin yaje ya fito ya ɗauki glass cup guda tare da wankeshi acikin sink ɗin sannan ya nufi coffee machine ɗin ya murɗo coffe cikin cup ɗin tare da saka spoon medium bayan ya ɗaurayeshi kana ya fito yana juya coffee ɗin har

zuwa cikin falon nashi, xama yayi akan ɗaya daga cikin sitocin falon yana kurɓar coffee ɗinsa yana bin suratul baqra dake tashi ta cikin speaker's ɗin Tv'n.
Yakai kusan mintuna goma a falon kafin aja ƙofar a shigo ciki, sallamar mace ce ta bayyana cikin garɗi da gwalli tare da iyayi, sanin daraja da muhimmancin sallama yasa ya amsa a ƙasan laɓɓansa batare daya ɗago idanunsa dake bisa tv'n sa ba.
"Yaya barka da wuni yaya ka taso daga office" wata ƴar farar budurwa marar jiki ta faɗa tana mai tsugunnawa agabansa tare da tsira masa ƙananun idanunta tana kallonsa kamar zata lasheshi sabida yadda take kallonsa.
"Lafiya Alhamdulillahi, khadija nagode".
Yafaɗa batare daya dubeta ba.
Sunfi ƙarfin muntuna goma ahaka har ƙafar khadija ta sage amman miskilin bai kuma dubanta ba.
Gajiya tayi da tsugunnen ta miƙe ta masa sallama ta fita tanajin kamar ta kurma ihu! daman tasan kozasu shekara ahaka baze tanka mata ba tarasa wannan musibar son datake wa Aliyu amman shikam kullum hango baƙar ƙiyayyarta take acikin idanunsa.
Share hawayenta tayi tare da sauka ƙasa ta shige ɗakinsu tanajin komai ya fita akanta ita dai shiɗin take muradi har xuciyarta.
Ɗan tsaki yaja kaɗan tare da furta "Yara tunkafin ku tafasa zaku ƙone mtssss se son auren tsiya wanda idan aka musunma basu san yadda zasuyi da mijinba".yafaɗa a fili tare da faɗawa tunani na daban.
Shi haryau baiga muradin ransa ba, ma'ana wadda tai dai-dai da tsarinsa shi baya son auren yarinya ƙarama sabida gani yake bazata iya da buƙatarsa ba, yafi son babbar mace wadda tasan metakeyi wadda zata kula dashi wadda zata kular mashi da yaransa domin shi burinsa yaga ya tara zuri'a mai yawa da albarka, khadija babu laifi tana da shekaru domin takai kusan 27 da haihuwa dan yanzun haka tana shekarar ƙarshe a BUK amman yanayin tsarin jikinta da yadda take yasa shi sam batai masa ba ace mace kamar tsinke kullum se tsabar iyayi da jida kai amman kamar ka hureta ta faɗi shikam sam khadija baya mata kallonso sedai kallon ƙanwa kuma shi har yanzu baitaɓa jin wani alamun feeling akan soyayyar wata budurwar mace ba, kodan batasu ɗin yake ba oho?
Katse tunanin daya faɗa yayi tare da miƙewa bedroom ɗinshi ya shiga xama yayi akan bedset drowwer ɗin dake gefen gadonshi tare da ɗaukar wayarshi guda, number dr jalal ya shiga nema ta jima tana ringing kafin ya ɗaga,dr jalal abokinshine school guda sukai sedai bam bancin course haka zalika kuma cousins bro ɗinshine kuma surukinshi domin yana auren ƙanwar Aliyu mai binshi Nusaiba yanzun haka suna Abuja da zama sabida aikin daya kaishi can ɗin, ɗaga wayar dr jalal yayi tare da fara yiwa haidar tsiya"A,a tuzurun amminmu barka da warhaka".haɗe ranshi yayi tamau "Kai banson shirme nifa surukin kane yakamata ka dinga darajani, hope ya yarana suna lafiya?" yafaɗa cikin barkwanci, atakaice dai sun gaisa cikin barkwanci kasancewarsu abokan wasa, sannan Aliyu yaɗan nisa"Dr babu wasu tablet ɗin da suka fi waɗancan ƙarfi wallahi jiya da ƙyar nayi barci yanxun haka still ƙasan marata ciwo yakemin sosai ataƙaice yau ko break wallahi banyi ba kawai ina daurewa ne".yafaɗa yana lalubar leɓansa na ƙasa yana tsotsa tamkar sweet.
Dariya dr jalal ya saki kaɗan"Haba bro kaida naji ance an maku baiko da dija kawai kacewa su abba su ƙara yo maku zooming ɗin aurenku sabida kaifa sparm yay maka yawa".yafaɗa yana

dariya,haɗe rai Aliyu yay"Malam kaga in bazaka gayamin ba wallahi zan katse wayana banson shirme yadda kuka ƙaƙabamin ita haka zaku gaji ku rabamu".yafaɗa cikin tsantsar takaici.
"Gaskiya Aliyu wannan karon bansan wanda xan kuma tura maka ka siyaba tunda wanda na baka yafi kowanne ƙarfi amman ina baka shawara kawai kai aure shine kaɗai solution ɗinmu,kokuma a wannan karon wallahi i will tell to su abba su san komai kawai tun kafin ka kai kanka lahira".
Furzar da zazzafan huci yayi tare da rintse idanunsa yana kuma tsotsar laɓɓansa shikansa wannan lamarin ya ishesa, kullum daren duniya da ƙyar yake barci sauƙinta ma ɗaya azumin dayake yawaita yi shine kaɗai yakejin ɗan samun nutsuwa amman yana adduar Allah ya rabashi da faɗawa halakar kusantar zina domin muninta.
"Hellow bro kana jina kuwa?" cewar Abdul-jalal ta cikin wayar"Eh inajinka bara kawai zan cigaba da shan wannan ɗin kafin muga abinda Allah zeyi Tnx".yafaɗa tare da katse wayar zubeta yay bisa gadon tare da sauka ƙasa wajan Amminsa.............

**********

"Bebi ke Bebi tashi kada kiyi lattin sallar asubahi".cewar mama wadda tafi mintuna biyar tana tashin Bebi a bacci amman Bebi ko gezau.............

*BONONZA BONONZA!*
*ƊAN MAJALISSA*
*RABON WANI*
*H A S K E*
KOBA SO*
*DA IZZATA*
_Dukkansu akan farashin naira 1000 document complt mai so seya tuntuɓi 08142105218_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*14*

"Bebi kada fa ki makara a sallar asubahi nasan sarai kina jina Bebi".Cewar mama wadda ta miƙe daga wajan datake tsugunne domin tashin Bebi daga bacci, fita tsakar gida tayi domin haɗa sanwar awarar da tun ɗazu shahid yatafi kai markaɗanta bayan layi, Hassana ce ta idar da sallarta cikin sauri tayo tsakar gida ganin har gari ya soma haskawa ruwa mai sanyi ta ɗiba a randa cike da zafin nama taje ɗakin ta juyewa BEBI ajikinta shi tass, wani tsalle BEBI tayi tare da kwallah ƙara "Wayyo mama wannan wani ɗan.........", Sam hassana bata bari ta ƙarasa ba ta maketa "wai ke dan ubanki bakisan nagaba dake ba? toni na tasheki idan nima shahid ce",cewar hassana wadda ta zarewa Bebi Idanu daman hassana ita ba magana gareta ba sannan kuma bata fiye shiga sabgar bebi ɗinba sanin batada mutunci yasa bata bita kanta. Tsitt tayi sabida tasan idan ta yadda muryarta tafi ta hassanar ɗaguwa tofa mama xata shigo haka kurum a zaneta da wannan sanyin safiyar shiyasa tai tsitt tare da tashi tana gunguni tayi waje, banɗaki ta shiga tafi mintuna goma aciki sabida jarabar kashin safiyar da Bebi take fama dashi kashin safe ya aureta duk safiyar duniya setayi aikuwa wari ya cika tsakar gidan sabida rashin wadatuwar faɗinsa, seda ta gama kashin sannan ta fito fuska jage-jage da hawaye wanda ba komai ke kawo matashiba se tsabar cin yaji shiyasa yake saka mata kashin ya riƙe yaki fitowa ta daɗi makilin ta lakata ta ɗora saman brush ɗinta tare da soma wanke baki sannan tayi alwala tayi cikin ɗaki aguje sabida sanyi.
Shinfiɗa abin sallah tayi tare da tayarwa tana idarwa tai azkar sannan taja hijabi ta koma baccinta hankali kwance.
Tsakar gida babu wanda yabi takan Bebi sabida idan da sabo sun saba da halinta, idanma suka tsaya tashinta tofa ransune ze ɓaci sannan ta ɓata musu lokaci a banza, shahid yana kawo markaɗan ya shiga wanka ita kuma mama tata ta somayi kafin ta ɗora tukunyar awara hassana tana dakan yaji hussaina tana wanke kayan da aka ɓata na abinci, su ihsan sukuma shirin makaranta suke ganin bakwai saura na safe, shahid yana fitowa shima shirin makaranta yayi, ragowar sauran tuwon jiya mama ta zubowa kowa amman banda su hassana sabida su ba fita zasuyi ba, iya shahid dasu ihsan ne kawai ta zubawa.
Suna gamaci sukaiwa mama sallama suka wuce makaranta.
Bayansu shahid sun fita, Hussaina dake kwaso kwanuka tana kaiwa kwando ita ta dubi mama tare da cewa.
"Mama wai ita Bebi ta daina zuwa makaranta kenan?,naga duk su sadiya suna xuwa".cewar hussaina wadda take kallon mama.
"A,a hussaina bata daina zuwa ba kuɗin jarrabawar datace nake son haɗa mata seta koma tukunna", mama ta faɗa tana yarfe gumin hayaƙin dayake keto mata idanunta yay jajur sabida zafin wuta.
"Lah wallahi mama ƙarya take babu wasu kuɗin jarrabawa kawai ita daman tace wai bazata

kuma zuwa makarantar ba domin wai duk tafi ƴan ajin tsaho".
Cewar hassana wadda tagama daka yajin yanzu kuma albasa take yankawa.
"Au haka tafaɗa?,cewar mama wadda tsabar mamaki yasa ta miƙe daga sunkuyon datake."Eh wallahi haka naji tana faɗa jiya, amman nace zan gayawa yaya nura ko yaya Aminu". cewar hassanar.
"A,a barni da ita, jeki tasomin ita daga baccin datake".cewar mama tafaɗa cikin takaicin abin.
Koda hassana ta shiga ɗakin seda suka kai ruwa rana kafin Bebi ta miƙe ta fito tana hamma fuskarta duk tai wani irin alamun bacci.
"Mama ina kwana?,Gani angama abincin safe?".tafaɗa tana tsugunnawa agaban mama,
"Ban gama ba uwata nace baiwar bata gama ba, yanzu abinda kikai kinmin daidai Bebi rana zafi inuwa ƙuna ina tsaye dan ganin na rufa mana asiri ashe ke dan gidanku ƙarya kike ba,ace kuzo da kuɗin jarrabawa ba kika ƙi zuwa makaranta kinfison kullum kina ɗaukomin maganar jama'a?".
Cewar mama tana kallon Bebi cikin tsananin ɓacin rai.
"Nifa Mama nafi ƴan ajin tsayi, rashin kunya sukemin suna min dariya idan na daki ƴa seta kaini malaman suyita dukana", tafaɗa tana danna baki gaba dan bebi taƙi jinin zuwa makaranta sam arayuwarta.
"Aiseki zauna anan ɗin ko kiyita zaga layi ɗaukar awarar ma bawani abin kirkin kike ba".
Murmushine ya suɓuce mata sabida taƙi jinin makaranta tafi son tai zamanta gida wannan kalamin na mama baƙaramin daɗi yayi mata ba.
"Mama haka zaki barta, dan Allah mama kada kibiye mata wallahi seta koma ai ba ita ta haifi kanta ba".cewar hussaina cikin ƙufula tayi wannan maganar sabida bakaramin haushi Bebi ta bata ba.
"Dama Hussaina ai bazanbi ta kanta ba ita ɗin banza nadai saurari tatsuniyarta ne kawai kuma tayi ƙurun ƙus saura dame kuma?".
Mama tafaɗa tare da juyawa gaban tukunyar awararta tana buɗewa sabida yadda yayo sama alamun tafasa.
"Kekuma ina ruwanki idan nai karatun hala ba kaina nayiwa ba?".
Tafaɗa tana tura bakinta gaba.
"Malama rufe mana baki anan in ba hakaba Wallahi in zubdar miki da haƙora banza wadda bata san mutuncin kanta ba,ke kodan maƙiya bakya zauna kiyi karatuba.kinfison kullum fita tallah ana kallonmu ana zinɗanmu, ai kema kya samu ko candy ne kiyi kamarmu".duk wannan maganar hussaina ce kewa bebi ita cikin tsananin jin haushinta.
Mama tana jin hussaina tana mamakin kaifin hankalinta tabbas tasan yaran nata na tsananin son karatu sedai kuma ana takai waketa kaya.
Bebi batace komaiba illah juyawar datayi gaban tukunyar ɗumame batare data tambayi nawa dana wa bane ta tsoma hannu ciki tana ci, "Lahh! mama wallahi bamuci bafa kinga harta kusan cinyewa".cewar hassana wadda tazo aje albasar hannunta wadda ta wankota,juyowa mama tayi tare da tafa hannu tana rafka salati, "Kubarta ana ranarta dan wannan tuwon rai ukune kinci harna rana kuma kika fita tallan awara kikaci Wallahi sena zane miki jikinki".Ko ajinkinta dan wannan tuwon jinsa take har cikin ranta daɗinsa yana mata mugun yawa,tafarar ɗaya tagama dashi tayi bakin rariya ta wanke hannu taje gaban randa ta ɗebo ruwa a kofi ta kafa baki tahausha gyatsa!tayi tare da hamdala ga sarki Allah kana ta juya zata tafi cikin ɗaki.

"Dawo malama ubanwa kika aje ya wanke tukunyar?".mama wadda take zuba awara a mataci dan ta tsaneta itake wa Bebi wannan maganar,sanin batada gaskiya yasa ta juya tafi minti goma akan tukunya ɗaya harseda mama ta kuma magana sannan ta ɗaurayota ta zo ta ajeta"Hahaha cikin muka kawo duniya kasa uwar ƴan bacci acici kenan babu abinda ake saurin ganin himmarki akai, kamarci".cewar mama kenan tana kokarin ɗora ɗan murfin tukunya akan awarar sabida ta tsane ta yanka ta soma suya ganin lokaci yana ja kada su makara a tallan nasu.
Tana ƙoƙarin shiga ɗaki tajiyo muryar mama tana magana"Yau dai babu lokaci amman gobe ki shirya dan Aminu ko Nura zasu rakaki makaranta kimaji da kyau"! turo baki tayi "Nidai mama gwara an mayar dani aji huɗu kawai ko asamarmin aikatau natafi can na dinga kwana tunda bakwa sona".tana faɗi ta shige ɗaki tare da birkito da kayan kwalliyarsu tana son shafa powder ne domin tayi shirin fita tallansu...............
Hoda ta shafa asaman fuskarta tare da jan baki raɗau da kwalli acikin idanunta tayi kyau babu laifi, kaya ta sauya tare da saka hijabi ja ajikinta fitowa tayi tsakar gida lokacin mama harta fara suya, cikin sauri ta ƙarasa gaban ɗan bokitin da mama ke tara awarar zata ɗauka mama ta doke hannunta, cikin lokaci kaɗan ta kammala suyar tare da bawa su hassana wadda zasu karya saboda su basu sami tuwonba suma shiryowa sukai cikin hijabinsu tare da fitowa kowacce ta ɗauki tata awarar sukaiwa mama sallama suka tafi.
Bayan su hassana sun fita tattare gida mama, ta somayi tare da ɗan gyara inda ya ɓaci.
Bayan ta kammala komai zama tayi akan tabarma tana, tsince waken dazatayi abincin rana dashi, sallamar mace ce ta karaɗe ɗan tsakar gidan nasu.
"Assalamu Alaikum mutan gida sannunku".cikin sakin fuska mama ta juyo ta amsa sallamar tare da saurin tashi ta kawowa matar tabarmar tana cewa.......
"A,a Rahane barka da zuwa yau agari ai rabona dake tun wancan adashin seda mukai magana da baba kwanaki tace wai kinje kauyene".mama ta faɗawa Rahane wadda ta shigo gidan yanxu:Rahane ɗiyar malam lado ce ta biyu wadda take aure anan wajan fanshekara,
"Eh wallahi maman biyu, munje garinsu mijina ne,babarsa ce bata da lafiya yanxuma daman wata magana ce ta kawoni wajanki Allah yasa zaki fuskanceni".rahane tafaɗa tana kallon mama cikin nutsuwa.
Wuri-wuri mama tayi da ido"Kai gashi ba yara bare asayo miki pure water munan na randa muke sha keko baƙuwace".murmushi rahane tayi "A,a in xansha kya bani sabida nasha agidan baba yanxudai kibani hankalin ki nan kusa". tafaɗa tana kallon mama,"To ina saurarenki".mama tafaɗa tana baiwa rahane dukkan nutsuwarta.
"Yauwa kinsan babansu naxir yana aiki a kamfani ko?,to kinga da yana tsohon kamfanin mai atamfa ne yana musu aiki, yanzu kuma kwanan nan da yaran mai kamfanin suka dawo nan kano seya kuma, buɗewa anan sharaɗar kamfanin nika, da yaran nasa suna legos ne a ɗayan reshensa nacan, tsohon kamfanin sa na nan kuma babban ɗansa ke wajan to wannan sabon daya kuma buɗewa shine ya kwaso ƴaƴansa guda biyu suke riƙe dashi, to kuma se aka rago ma'aikatan wancan tsohon na mundaɗu, to daga cikinsu harda babansu nazir kinsan ya jima yana musu aiki, yanzu haka a wannan sabon sun ƙara masa matsayi, to matsalar abinda ke damunsu yanxu shine abinci, wajan yay ciki da yawa babu masu abinci, ma'aikatan wajan suna buƙatar masu kai musu abinci kinsan kamfanine na sarrafa atamfofi suna fitarwa ana kuma shigo musu da ita daga ƙasashen waje anan kuma suna hulɗa ne da manyan diloli na ƴan

kasuwa daga jahohi kala kala, kin gane?".ta tambayi mama "Eh nagane mana haba waye bai san kamfanin mai atamfa ba, haba ai inajin sa a redio sosai".cewar mama wadda take sauraron rahane.
"Yawwa to shine babansu nazir ya tambayi ogansu akan suna son kawo mai cinikin abinci wajan, sabida su sami sauƙi kinsan aikin kamfani babu hutu kuma su manyan wajan babu ruwansu tunda su order suke yowa ko akawo musu daga gida, tokinga matsalar tana wajan ƙananun wajan tunda su babu wanda ze basu yace wallahi watarana sedai su sha lemo da biscut ko dai wani abun babu abinci ko kaɗan awajan, to ogan nasu ya amince yanxu haka da nice zan dinga kaiwa amman ya hana shine nace meze hana ki gwada sa,arki ma'ana ƴan biyu suna kaiwa can inkin dafa wataƙil Allah ya buɗo muku ciniki sosai kinga yafi wannan saida warar da batada ribar kirki............ amman ya kika gani dan seda na tambayi baba kuma tai murna babansu nazir kuma yana wajan kinga baze bar wata ɓaraka ba insha Allahu".

"To babu komai rahane insha Allahu semu gwada can ɗin, sedai kuma dole mu sami abin hawan dake kai musu kayan abincin, zan dinga dambu da wake da shinkafa, amman dai Bebi banda ita sabida makaranta".tafaɗa cikin gamsuwa da maganar rahane tare dajin daɗin hakan takuma tabbatar da cewa baban nazir ze kula da ƴan biyu sosai sabida gudun wata ɓaraka.
"To shikenan nagode bara na ƙarasa idan yaso ranar asabar seku fara kinga yau laraba sabida su koda yaushe suna aikine har ladi". ta muskuta zata miƙe"To babu komai amman yanzu dai vara na baki wayata ki sakamin lambar baban nazir sabida idan sunzo su nemeshi koya kikaga?".tafaɗa tare da janyo wayar ta mika mata ita kuma ta karɓa ta saka mata tare dayi mata sallama ta fita.
Har soro ta bita tana mata godiya...........

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*15*

Har soro mama ta bita tana zabga mata godiya, juyowa rahane tayi tare dayin murmushi "Haba maman ƴan biyu irin wannan godiya haka kamar wadda naiwa babbar kyauta, ai komai da kikaga mutum yana yi tofa yiwa kansane".tafaɗa tana saɓa mayafinta a saman kanta, tare da tura labulan buhun soron sannan suka kuma sallama a karo na biyu rahane ta fita, mama cikin gida ta dawo, ta shiga kicin domin ta ɗora musu abincin rana ganin azahar ta kawo kai.
Shahid ne yayi sallama bayansa su ihsan ne kamar haɗin baki, mama ce ta leƙo da kanta daga cikin kicin ɗin tana musu barka da dawowa seda ta ɗora sanwar dafa dukan, shinkafa, sannan ta fito tsakar gida duk tagama haɗa uwar zufa ajikin nata, shahid wanda ya cire kayansa na makaranta yana shirin fita mama ta kirawo tana mai neman wajan zama a saman tabarmar tsakar gidan, dawowa yayi da baya.
"Gani mama".yafaɗa yana tsugunnawa a gabanta..
"Yawwa shahid wajan maman farida mai adashi zan turaka wannan dubu goman tawa danake haɗawa Bebi kuɗin magani zata bani".
Da kallo ya bita yana nazarinta.
"Mama dan Allah mezaki dasu? wata matsalarce ta faru?".
Yafaɗa a nutse tare dayin tsam da ransa yana sauraranta dan yaji mezata ce masa.
"A,a shahid wata damace Allah ya kawo mana.........",tass! ta kwashe komai ta gaya masa sannan ta ɗora da,"Shine daman nakeson kazo kaje kasuwar jan guza anan komai xefi mana sauƙi amman ya kagani?".tafaɗa tana tsira masa ido dan taji ta bakinsa.
Sunkuyar da kansa yayi ƙasa tare da saka hannu ya share hawayen dayake zubo masa.
Sannan ya ɗago yana kallonta still wani ruwan hawayen bai daina zubo masa ba, sosai mama takebin shahid cikin zuciyarta da tarin tambayoyin dalilin hawayen nasa, amman setai shuru ta zuba masa idanu tana kallonsa.
"Mama Allah ubangiji ya bamu nasara, acikin wannan sana'a dazamu fara, mama! haƙiƙa hawaye baze bar zubarmin ba harse naga lokacin dani kaina zan xame miki Garkuwa, insha Allahu mama senai miki abinda zakiyi alfahari dani, kullum ina takaicin ganin ɗan kowa ya kama hanyar makaranta da safe, amman ni ƙanwata da yayyena sedai su ɗora bokiti aka sutafi tallah! ya rabbi ka kawo mana ɗaukinka dukda hakan ma muna godiya gareka".
Yafaɗa yana miƙewa tare da kallonta.
"Bara naje na karbo na dawo".
Bata iya bashi amsa ba, harya juya ya kama hanyar wajen sabida yadda yaron nata ya karyar mata da zuciyarta, tabbas ko yanxu tana alfahari da shahid kai bama shi kaɗai ba dukkan ƴaƴan da Allah ya bata tana alfahari dasu fatanta a kullum Allah ya raya matasu cikin amincinsa Amin.
Su ihsan sallah sukai suka ɗan kwanta baccin gajiya tana cikin wanke shinkafa shahid ya shigo a tsaye ya tsaya tare da cewa."Mama kawai lissafamin nai sauri naje kinga garin akwai hadari sosai".
Hannunta ta wanke tare da nufar kicin ta zuba shinkafar sannan ta kuma dawowa.
"Kadai bari kaci abinci ko?".
Tafaɗa tana zama, akan tabarmar datake wajan.
"A,a mama nidai nafison naje na dawo tukunna".
Lissafa masa komai tayi cikin nutsuwa sannan tai masa fatan alkairi ya kama hanyarsa ta tafiya, ita kuma ta miƙe tayi kicin danta duba sanwa.

_Sharaɗa ƴar kasuwa_

Tunda su Bebi suka fita yau take ƙunci hatta kallon arziki bataiwa kowa ba haka sukaita cinikin awarar tasu duk jikinsu hussaina yayi sanyi sabida ƙuncin da bebi takeyi ƙarfe uku awararsu ta ƙare, tawajan dasu siba suke suka wuce wanda siba yayi saurin sada kansa ƙasa yayin dayaga Bebi ta zo giftawa ta wajansun sabida tsoro! danshi yanzu Bebi mugun tsoro take bashi bawai ɗan kaɗan ba sam yarinyar tariga data firgitashi tun ranar data ɗebo masa police.
Suna tafe hassana ta dubeta"Waike yau wani salon iskancin ne yau narashin magana ya motsa miki?".tafaɗa mata tana tsareta da ido tura baki tayi gaba tana tafe tana gunguni.
"To duk baku bane zaku cewa mama ƙarya  nake akan exam, wai idan nayi karatun nan ku xanyiwa?".tafaɗa tana jan kafarta cikin sauri sabida bakaramin haushinsu takejiba, yadda suka zaƙe awajan mamaa ɗazu musamman hussaina.
Gaba tayi tabarsu abaya tana mita"Kema dai da ɓata baki nidaman nasan abinda yake damunta shiyasa kikaga nai banza da ita".cewar hussaina wadda take kallon hassana cikin dariya,"Hmmm ai halin Bebi se ita Allah dai ya shirya mana ita, ashe duk akan makaranta take wannan ƙuncin" hassana tafaɗa itama cikin dariya tafiya suke suna kuma mai maita halin Bebi harsuka iso gida wanda ita tana gaba su suna bayantane...........

*************************

Cikin nutsuwa ya saka ƙafafunshi akan lallausan makeken carfet ɗin dake malale acikin falon, wanda babu komai na tarkacen kujeru acikinsa face TV tare da wasu irin tum-tum da aka jera se uban kamshin dake tashi tare da wani irin sassayan sanyin AC'n dake faman ratsa cikin falon.
Sallama yay can cikin ƙasan maƙoshinsa tare da kallon wasu ƴan mata farare masu kyau kana ganinsu kaga tagwaye.
Tunma kafin yace komai sukai saurin rissunawa "Yaya Aliyu barka da fitowa yaya aiki?".da sauri suka bar wajan har suna rige-rige sanin baze tanka masuba.
Se asannan nabi bayansu da kallo babu laifi ƴammatane cikakku waɗanda kana ganinsu kasan ansha boko domin ba yara bane ba, kuma kallo ɗaya xakayi musu kasan ƙan nansane sabida sunɗanyi kama ta jini sedai su farare ne.
Tsaki!yaja afili tare da neman waje ya xauna, still wata budurwar ce ta kuma fitowa cikin nutsuwa wadda kallo ɗaya zaka mata ka gane itama ɗin kanwarsace sabida kamarsa da ita harta ɓaci hatta kalar fatarsu gudace sedai ita ɗin daga gani ta girmewa waɗannan tagwayen.
"A,a yaya harka dawo ina yini ya aiki?". tafaɗa tare da nufar wani ɗan kwana anan cikin falon, ruwa ta ɗauko masa tare da glass cup, sannan ta kawo masa gabansa tana zama agefensa.
"Lafiya ƙalau Amina yanaki office ɗin?" shima ya tambayeta.
Dariya taɗanyi kaɗan"Hmm wallahi yaya yau ɗin nan se a hankali".tafaɗa tana gyara zamanta agabansa, wadda daga gani ana good time atsakanin ƴan uwan juna nan.
"Ok, ina Ammi?". yafaɗa murya can ƙasan maƙoshinsa,"Tana bedroom ɗinta amman naga tana shirin fitowa nan ɗin sabida ya abbakar yace tayi masa dambu yana hanya".wara idanunsa yay waje,"Aikam nima kamar tasan banci abinci ba yau".................

*MANAGE BA CAJI*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Albishirinku makaranta littattafan hausa shin ko,kunsan shararriyar marubuciyar nan *FEENAR MATAR SOJA* wadda ta saba gwangwajeku da zafafan littattafanta masu matuƙar ratsa zuciya ta ƙara zuwarku muku dawani zazzafan littafin, Mai suna *AUREN GADO* kadafa ku manta Feenar tayi fice wajan baku nishaɗi faɗakarwa ilimantarwa acikin littattafanta, Kamarsu *MUKADDARI AUREN SOJA*, *ZANYI BIYAYYA* *WANAKE AURE* dama sauransu toyau ma gata nan tafe da wani sabon wanda ta shirya tsaf domin ta nishaɗantar daku acikin sabon littafinta mai suna *AUREN GADO* na kuɗine akan farashin Naira 500 ga wanda ya shirya biya seya nemeta ta wannan number 09011251444 maza ku hanzarta koda kuɗinka seda rabonka_

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*16*

Dariya Amina ta saki ahankali tare da kallonsa"Yaya kaima dai Allah ya yanke maka haka, musha biki ai wallahi nayi farin cikin wannan haɗin dasu abba sukai". tafaɗa cikin farin ciki, Haɗe rai yayi sosai fiye da yadda yake da tare da kallonta da idanunsa waɗanda suka saka ta sami kyakykyawar nutsuwa akan dariyar datake yi,"Ke ni tsaranki ne?".yafaɗa cikin serious magana babu alamun sassauci, Gintse dariyar tayi tare da haɗe hannayenta waje guda. "Allah ya baka haƙuri".tana faɗin haka ta miƙe tayi ɗaki da gudu sabida tsoron karya kai mata mari tasan halinshi da zafin zuciya tare da saurin hannun tsiya, tsaki yayi a fili batare daya ce komaiba ya lumshe idanunshi yana tasbihi ga Allah buwayi gagara misali, wani irin sassanyan ƙamshi ne mai ratsa zuciyar ma'abocin jinsa ya ratsa ilahirin falon, sallamar wata farar macece tas! marar jiki kallo ɗaya zakayi mata kaga bafulatanar asali sanye take cikin shigar jan legos

less wanda yaji uban kuɗi mai tsada se zobuna da sarƙa dayaji a wuyanta da hannunta jikinta rufe da farin mayafi mai tourching ja ajikinsa, ɗago da lumsassun idanunshi yayi tare da ƙawata fuskarshi da murmushin dayayi masa kyau fiye da tunani, "Amin wa'alaikissalam Ammina" yafaɗa tare da ɗan karkatowa ya tashi daga kishingiɗen dayake, yana kallonta cikin so da ƙaunarta.
Itama faɗaɗa far'arta tayi tare da janyo tum-tum guda marar tudu ta zauna akansa tare da kallonshi, "Yau dai lafiyarka naga duk jikinka amace?".ta tambayesa cikin kulawa, Ɗan langwabar da kanshi yayi tamkar ƙaramin yaro tare da matsowa gabanta ya ɗora kansa akan cinyarta, tura bakinshi yayi gaba kaɗan wanda yay matuƙar bani mamaki ganin yadda yakewa, Ammi kamar ƙaramin yaro, cikin nutsuwarsa wadda tagama bin jikinsa ya furta"Wallahi ammi yau jina nike duk babu daɗi, amman inaga yanayin aikin yau ɗinne".yafaɗa yana ɗago idanunshi yana kallonta,Cike da kulawa ta kuma dubansa itama,"Kaje kiran Alhaji babba kuwa tun ɗazu yake aikosu fahad dan Allah dan Annabi babana kaje kada ka kuma jamin cin zarafi akaro nabiyu tunda sunce ninake ɗaure maka gindi kowa ganin laifina yake".tafaɗa cikin nutsuwarta. Tashi yayi daga saman cinyarta tare da aro nutsuwa sosai sannan ya dubeta"Zanje Ammi amman dominki bada ban keba na rantse babu wani zuwan dazanyi haba wallahi abinda ake acikin gidannan baya dacewa" Riƙe baki ammi tayi cikin ɗunbin mamakin halinshi sam baya da rufi maganar data fito masa a baki ita yake yafaɗi baya rufa rufa musamman idan ranshi yana ɓace."To naji dan Allah karaba kanka da wannan zafin ran babana bana sonka dashi, sannan kuma idan kaje  kasan maganar dazaka faɗa musu sabida daga ƙarshe dai kasan meze biyo baya" tafaɗa itama fuskarta babu daɗi, Lumshe idanunshi yayi tare da furzar da zazzafar iska daga cikin bakinshi.
"Naji Ammina Amman harga Allah bana son wannan yarinyar har zuciyata".Haɗe ranta tayi sosai,"Kace muma duka baka sonmu, Nikuma duk duniya banida kamar khadija tunda ta iya buɗar baki ta furta maka so naji ina sonta".Ammi tafaɗa tana kauda kanta gefe,Dariyar gefen baki yayi, batare dayace komai ba, ni mamakinshi ma nayi yadda naga ya sake sosai da mahaifiyar tashi suna magana kamar ba wannan miskilinba,"Ammi kin sauke dambun?".taji amon! Muryarshi acikib dodon kunnenta, "A,a da saura na saka Habiba ta dubamin".Haɗe rai yayi"Ammi dan girman Allah kidaina baiwa masu aiki suna taɓa mana abinci, gwarama su baba amman waɗancan yaran duk ƙazamai ne".dariya! tasaki "To baban ƴan ƙyamƙyami naji wannan dai na bata tayi sabida inada uzuri, inxakaci to idan bazaka ciba kai kasani" girgiza kanshi kawai yayi tare da ɗaukar wayarsa wadda ya mayar da ita slient, ganin misscall ɗin Abbansu yayi wajan 5 jikinshi na rawa ya fara neman layin ringing! 1 abban nasu ya ɗaga, Sallama yay cikin nutsuwa tare da furta "Afuwan abba wallahi banji kiranka ba".daga cikin wayar abban nashi ya ɗanyi murmushi"Naji Babana babu komai, yaya gida da aiki?",yafaɗa cikin kulawa, cikin nutsuwa shima ya basa amsa da "Lafiya ƙalau alhamdulillahi, Abba ya legos ɗin?". shima daga nashi ɓangaren numfasawa yayi"Lafiya ƙalau Abubakar bai gaya maka saƙona ba?. ya lumshe ido tare da warasu akan Ammi wadda take kallonshi"A,a abba bai gayamin ba, amman yana hanyar gida, sabida bamu haɗuba yau"."Ok daman sonake kazo nan legos ranar saturday akwai kayan dazasu biyo jirgi, sabida umar ze tawo gida week end sekai ka karɓeshi nima kuma gobe zan wuce chaina kaga baze yuwu abarsu bilal su kaɗaiba semuga ba dai dai ba". shafo sumar kansa yay wadda bata cika yawa ba sabida askin dayake mata na saisaye tare da furta"To babu komai Allah ya kaimu zan biyo jirgin dare ranar friday".yafaɗa cikin bin umarnin

mahaifin nashi.
"Allah yayi maka albarka Aliyu bantaɓa neman abu wajanka kayi musuba koda hakan bai maka daɗiba, yadda kakemin biyayya kaima Allah ya baka masu yi maka" Amin ya Allah" yafaɗa cikin jin daɗin addu,ar mahaifin nashi wadda idan da sabo yasaba jinta wajan dukkan mahaifan nashi guda biyun.
Katsewa yayi tare da kallon Ammi,"Pls ammi ki ɗan zubomin naci na tafi ɗaki kinji nan da jibi zan wuce legos".murmushi tayi tare da kallonshi "Toya zakai da baƙin dazasu zo muku ranar lahadin naji kace kuma sabbin costumers ne?"shafa kanshi yayi tare da ɗan jim kaɗan"Babu komai xan haɗasu da ya usman duk da dai ni suka sani awajan". yafaɗa cikin comfidance,"A,a ba,a haka kaga dai suɗin baƙine meze hanaka kace masa yabari ranar lahadin ko da daddare seka tafi can ɗin?".waro idanunshi yayi"Haba ammi ai babu wani uzirin daze katse naku awajena kedai ki sakani acikin addu'arku kawai".yafaɗa cikin ladabi, "Addu,a kullum cikin yi maka ita muke tare da ƴan uwanka baki ɗaya Allah yayi muku albarka amin".Ammi ta faɗa cikin jin tausayinshi sabida kaf ƴaƴanta yafi kowa ƙulafucin iyaye yana da mugun rauni akan iyayenshi yana sansu over.

Tashi tayi da kanta taje ta haɗo mashi dambun cikin madai daicin flate sabida shiɗin ba ma'abocin cin abinci da yawa bane, zaman ammi kaɗan wani magidancin namiji ya shigo wanda ya girmi Aliyu nesa ba kusa ba sedai shi baikai Aliyu kauriba kuma shi yana da hasken fata kamarta Ammi, sallama yayi hannunshi riƙe da wata farar Beby mai kyau, da sauri yarinyar tayo gaban Aliyu ta rungumeshi "Uncle ina yini kasiyomun choculate ɗin?.tafaɗa cikin shagwaɓa ɗagata yayi yana mata wasa "A,a Afrata har an dawo daga school da wuri haka".yafaɗa duk hankalinshi yana kanta yama manta da wanda ya shigo ɗin seda yaji muryarshi yana mashi magana"A,a tuzurun ammi kaine anan?".yafaɗa yana dariya kaɗan ɗan haɗe ranshi yayi"Ya Abbakar dan Allah kudaina wallahi bana so".dariya wanda aka kira da ya abbakar ɗin yayi"Ai yanzu nasaka ka magana miskilin banza".yafaɗa yana neman wajan zama"Ammi pls kibamu abinci yunwa yau kowa yakeji agidan",yafaɗa cikin kwantar da kai"kai nifa nagaji kaje can kana siyo muku wannan laulayin na matarka inaga vaze barni na huta da dahuwa ba".ammi tafaɗa tana kiran "Amina ko hassana wani yazo".Cikin sauri ƴammatan ɗazu sukazo ganin ya Abbakar yasa suka tsaya awajan amman babu wadda tai gigin kallon saitin gadanga wanda ya ɗora afra akan cinyarsa yana cin dambun yana bata batare daya kalli kowa ba, yana gama cin abincin ya tashi baki ɗaya kafaɗarsa ɗauke da afra.
Wadda tayi bacci miƙawa amina ita yayi ganin yadda suka cika falon suna hira da ya abbakar kamar wani sa'ansu bakaramin bashi haushi hakan yayiba dan haka fita kawai yayi batare daya kula kowa ba.
Yana kokarin kai kanshi part ɗin Alhaji babba yaga usman na kokarin kutso kanshi cikin part ɗin nasu ɗan dakatawa yayi harya karaso"Kai kuma ina zuwa haka?" usman ya tambayeshi cikin barkwanci"Wajan wancan tsohon zanje wallahi ya riƙe wuta".yafaɗa rai ahaɗe Dariya usman ya saki"Aikin Alhaji yana kyau shine maganin manyan tuzurai maza jeka na khadija bada kanka asare" yafaɗa tare da maƙe dariyarsa, batare daya dubi usman ba yaja ƙafarsa yabar wajan cikin hukuncin Allah yana kokarin kai kansa cikin part ɗin alhajin ya hango tashin motar fahad ɗan gidan alhajin wanda yake zaton tare dasu Alhajin suka fita ƙila wani wajan zasuje.
Ajiyar zuciya ya sauke tare da barin part ɗin Alhajin baiyi gigin bita part ɗin Abban bauchi ba,

sabida gudun yawan magana sulalewa yayi ya koma part ɗinsu
Tun daga farkon falon kakejin hayaniyar su ya abbakar da usman wanda dagaji tsabar hirace tai daɗi a falon ammin amman shikam baiyi gigin shigaba haka yaja kafarsa ya haura samansa, Alwala kurum yayi tare da nufar masallacin dake cikin gidan nasu.

*******

Da gudu Bebi ta hankaɗa buhun soron gidansu dasukai labule dashi tayi tsakar gida bata tsaya anan ba banɗaki ta tafi wanda tundaga bakin masan take faman fesa gudawar data kwaso daga wajan tallansu............

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*17*

Tajima acikin banɗakin tana faman abu guda kafin ta gama ta wanke jikinta ta fito waje idanunta yayi wani mugun yin ja, ɗaki ta shiga ta cire kayan jikinta tai saura daga ita se ɗaurin kirji, tsakar gida ta kuma dawowa ta tarar da mama, tana buɗe kayan miya dasu shinkafa ga su shahid a zaune dasu hassana duk sunata taimakawa mama wajan kunce kayan wurin. zama tayi tana hamma tare da kallon mama"Mama kice yau zata fashe?".da kallo duk suka bita"Zata fashe a ubanki, maman kike gayawa haka shegiya uwar ƴanci" cewar shahid wanda yayo kanta kamar ze daketa"A,a badole nafaɗi hakaba irin wannan gara dazamuci yau wani ɗan albarkar ne yayo mana wannan taimako kamar yasan damunace akwai ci".wannan karon seda mama ta dara watakan matsalar Bebi dai ɗayace arayuwarta itace ci indai ita zata samu taci tofa hankalinta ze

kwanta.
"A,a Bebi kiyi mana addu,a wannan wata damace rabbana ya kawo mana".........tas ta kwashe komai ta gaya mata kamar yadda ta gayawa su hassana, amai makon mama taga Bebi tayi farin ciki setaga ta miƙe tsaye tare da nufar hanyar kicin abinci ta lodo a kwano tazo ta zauna ta soma ci batare data ce komai ba secan kuma ta ɗago.
"Mama kin amince ƴaƴanki sutafi can kamfanin masu kuɗi su kai abinci?, mama bakya gudun wulaƙancin masu kuɗin nan na yanxu da wasun su basusan darajar ɗan adam ba?".da kallo kowa ya bita cikin mamaki,"Nifa gaskiya nafi ganewa awarar nan yadda duk wanda yay min naci uwarsa a sauki amman wannan kamfanin sam raina bai bani da alkairi akansa ba dan haka ban dani acikinsa".dukansu kallonta suke cikin mamaki jikin mama yayi sanyi sosai.
"Bebi kamar yaya babu alkairi ban fahimceki ba, duk da bakida wata nutsuwar kirki amman hakan baze hana na baki haƙƙinki anan ba".mama ta faɗa duk ranta yayi wani iri"Haba mama kema dai kin manta halin fatan tsiyar ƴar taki musamman idan ranta baiso abu ba,mudai zamuje Allah ya karya bakinki mai fuskar tumatur".cewar hussaina tana hararar Bebin.
"To Allah baku sa,a nidai kar ace wataran naje, ni wallahi mama banyi murna ba gwarama na koma skull ɗita ma baki ɗaya".
Tafaɗa fuwww ta mike da abincinta tayi ɗaki, murmushi kawai maman ta saki tana addu,ar Allah ya zaɓa masu abin da yafi xama alkairi akan hakan amin.
Sosai suka fitar da komai tare da adana waɗanda zasu lalace shawawarsu kuma ta tsaya akan zasuna yin dambu da alala kawai kafin suga kuma abinda Allah zeyi, har dare suna faman aikin shinkafar dambun sabida ƴar hausace, Ita kuwa bebi bata fitoba se alwalar sallar magrib koda ta fito tayi ta koma ɗaki tayi sallah hijabi ta ɗauka tayi gidan iya a ɗaki suka kulle da sadiya,suna labaran shirmansu wanda babu komai a labarin se yadda zasuyiwa su salisa dukan tsiya.
"Ke bebi bakiji wata maganar danaji jiya ba?" cewar sadiya tana kallon Bebin,"Ina jinki bani nasha Allah yasa dai ba wani abun bane?"."Hmm kedai bari wai ashe yaya aminu da yaya nura ƴan biyunku sukeso jiya naji suna gayawa iya amman baza,ai maganar ba se nan da ƴan watanni kafin nan sun kare skull ɗinsu" wata kara Bebi ta saka"Wayyo ni harna hango yadda nake hararar su salisa a rabon kayan fati kuma wallahi bazamu gayyacesu iyayen gayyaba saboda kada su cinye mana kayan partyn mu".dariya sadiya ta saki"Kedai Bebi bakida wata magana setaci yanzu dai bana son ki gayawa kowa wannan maganar amanatun amana inkinci taciki babu ruwana", wata harara ta zabga mata"Wazan gayawa kema dai hmmm kenifa zancen makaranta naxo miki gobe zan koma dan wallahi bana iya wannan tallan kamfanin da mama ta samo mana ba nan ta zauna ta kwashe komai ta gayawa sadiya. dariya sukai atare sadiya tace"tabb wallahi nima na goyi da bayanki gwara tallar awarar akan kai dambu can sabida wajan fa naji ance akwai maza da yawa nikuma kinga bana son yawan maza awaje". tagumi bebi tai tana jin yadda sadiya ke shato sharri tana likawa wannan kamfanin wanda ko hanyarshi bata saniba.
Seda iya ta gama tuwo ta kwaso musu shi fall nan bebi ta lanƙwashe ƙafafu tana kai loma bakinta, seda suka share tuwon tsaf sannan sukai sallar isha'i kana Bebi taiwa iya sallama suka wuce gidansu Bebin.
Lokacin da sukaje duk gidan nasu yana hargitse sabida yadda su mama suka baje kayan aiki, da kallo kawai mama ta bita tare da cewa"Bebi zoke ki wanke ƴan kwanikan can tunda naga dare bai yiba", da taimakon sadiya sukai wanke wanken sannan ta kuma raka sadiya hanyar

gida, se ita kuma ta juyo.
A hanya taga habu mai icce"A,a Bebi se ina haka?" bata sami zarafin kallonshiba sabida tai mashi wata muguwar tsana sanin halinta yasa yaja kafafunshi ya koma inda zeyi ita kuma ta nufi gida, kanta tsaye ɗaki ta nufa ta fito da uniform ɗinta na makaranta tai pillow dashi haka ta kwanta da shirin skull gobe.

_YAHAYA GUSAU_
Yajima a masallacin yana addu'oinshi daya saba kafin liman ya shigo a tayar da sallah, koda aka idar ya jima anan ɗin har aka kira sallar isha'i yana yi ya fito kanshi tsaye ɓarin Alhaji babba ya nufa babban falon ɓarin ya shiga tare da sallama, matar alhaji babba hajiya tana zaune tana kallon saudi jin sallamar Aliyu yasa ta rage tare da faɗaɗa far'arta tana kallonshi tare da amsa mashi sallamar.
"A,a babana kaine awajan namu sannu sannu" tafaɗa cikin sakin fuska ɗan zama yay yana gaisarta a saman carpet ɗin, cikin sakin fuska dattijuwar matar ke amsa mashi"Alhaji yana nan kuwa?" yafaɗa yana kallonta"Eh yana ciki bara na sa akira shi".tafaɗa tana kiran"Nuratu!nuratu!!"wata budurwace ta fito tare da riisunawa "Yaya barka da dare".kana ta juya wajan hajiyar "Hajiya gani".bai amsa wa wadda take gaisar dashi ɗin ba sema kurawa tvn wajan dayay idanu yana nazarin labaran da ake,"Yawwa je wajan alhaji kice masa Aliyu yazo".cikin sauri nuratun ta juya mintuna biyu ta dawo"Yace ya samesa a sitroom".tafaɗawa hajiyar kana ta juya ta koma inda ta fito, tashi yay tare dayiwa hajiyar godiya yabi ta ɗayar hanyar ya shiga sitroom ɗin.
Babban mutum ne sosai mai yawan shekaru zaune akan kujera hannunshi dauke da carbi,sallamar Aliyu tasa ya ɗago cikin sakin fuska yana kallonshi"A,a babana sannu da shigowa" zama yayi a kasan carfet yana gaisar da tsohon tare da sada kanshi a kasa yana jin maganar tsohon.
"Yawwa abinda yasa na ce kazo shine, maganar bikinka da kanwarka shin meka shirya akan hakan?". wani irin takaicine yazo masa kirjinsa amman ya danne tare da ɗago kansa har yanayinshi ya sauya"Alhaji duk yadda kukai yayi".yafaɗa a dake, ɗan jimm Alhajin yayi"To madallah tunda kace haka babu komai zamu zauna da sauran ƴan uwana abinda muka yanke za,a sanar maka, amman kasan dai nan da sati biyu bikin naku babu ɗagi ko?".girgiza kanshi kawai yay batare daya iya furta komai ba,"Wai kamarshi za,aiwa Auren dole lallai bada ban iyaye iyaye bane da babu abinda ze da waccan yarinyar.

"Bakace min komai ba Aliyu?"! Alhajin ya faɗa yana kallonshi"Alhaji babu abinda zance Allah ya kaimu".yafaɗa tare da mikewa yana sosa keyarshi kana yaja ya bar sitroom ɗin bai kuma bi takan alhajin ba.
Murmushi Alhaji yayi tare da mayar da kanshi ya kwantar yana jan carbinshi.
Shikuwa kai tsaye ɗakinshi ya koma ya watsa ruwa again tare da kwanciya saman gado yana naxarin abinda ke gabanshi har wajan 12 bai rintsaba alwala ya mike yaje yayi kana ya tada sallah har wajan 3 sannan ya sami bacci, kiran sallar farko ya tashi ya bada raka'atul fijir kana ya sauka zuwa masallaci har wajan 6 yana can daga nan wajan dayake motsa jiki ya nufa

wajan 7 ya gama komai ya sauko sanye cikin yadin kufta yana zuba kamshi ammi ya gaisar rannan a hade tare da mikewa ze fita"Bazakai break ba?" ciki ciki ya bata amsa daya makara sabida yana son yay landing komai sabida tafiyar dazeyi, "OK Ga Khadija nan zaka ajeta a skull tana shirin fitowa yanzu".harya mike ya koma ya zauna tare da dafe kanshi mintuna uku ta fito jikinta sanye da after dress ammi taiwa sallama kana ta gaisar dashi, bai amsa mata ba"Ammi na wuce office" "Nace zata bika ka sauketa a skull".girgiza kanshi yayi"Ammi nai latti sedai ta nemi driver".yana gama faɗin haka ya dauki car key ɗinshi ya kama hanya ze futa,"Yaya pls ko a jection ka saukeni zan sami napep" tafaɗa tana mikewa da jakarta a hannu ta bishi, adai dai corridow ya tsaya yana aika mata da mugun kallo"Ni sa'anki ne dan ubanki ɓacemin anan" yabuga mata tsawa kana yabar wajan yana huci wata motar ya shiga sabida tasa tana wajan gyara koda yaje aikin rannan nashi a hade yake wajan 4 ya tashi zuwa yay wajan bokking na jirgi kana ya koma gida ya soma shiri, wajan magrib yay wa su ammi sallama ya wuce airport jirgin dare yabi zuwa garin na legos wanda yabarwa usman ragamar komai na kamfaninsu na kano.

Washe gari bakwai Bebi tai makaranta, wanda hakan ya baiwa kowa mamaki agidan haka rayuwar bebi tai ta tafiya cikin wannan satin bata wani magana seta skull sabidama kada mama ta sakata a lissafin tafiya tallan kamfani, yau takama asabar tun wuri mama ta kammala komai ta haɗa musu abin bukata cikin tsafta ƴan biyu suka shirya kansu haka shahid ya samo musu mota har ƙofar gida ta ɗauki kayan nasu zuwa bakin tafkeken kamfanin na mai atamfa dake sharaɗa, da taimakon baban nazir suka shigar da komai cikin kamfanin daga gefen masallaci dakwai wata ƴar rumfa mai dauke da bencina  da tebur a saman teburin ya aje musu kayan abincin nasu wanda tsananin mamakin girman kamfanin da yadda yake a tsare ya daskarar dasu hassana, zamansu da kamar mintuna uku ciniki yace salamu alaikum domin tuni har an cinye damubun har ana neman kari.
Kayansu suka haɗa wajan karfe 3 sukayo gida cike da tarin nasara.

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*18*

Abakin layi mai baburin adai daita sahu ya sauke su, saukar da manyan kulolin dasuka fita dasu sukai zuwa waje kana suka biyashi kuɗinsa, sannan suka dauki kulolin suka shiga layin gidansu, a soro suka aje suna mayar da numfashi sannan suka kuma ɗauka sukai sallama acikin gidan, "A,a har kun dawo?" cewar mama bayan ta amsa musu sallamar, tare da matsowa ta kamawa hassana babbar kular dake hannunta wadda aka zuba dambu acikinta, jinta sakayau yasa mama mamaki, seda suka kai kulolin gaban rariya sannan mama ta kawo masu tabarma ta shinfiɗa musu, kana ta kawo musu ruwa a moɗa tare da abincin ranarsu data aje musu, Hassanace ta mika wa mama kuɗin dake hannunta waɗanda zasukai kimanin naira dubu huɗu,"Mama wallahi akwai sa,a acikin wannan sana,a duba fa gaba ɗaya mun siyar da dambun alalan ma haka kumafa har ƙari suketa nema".murmushine a saman fuskar mama tana karbar kudin tana lissafasa su,"Masha Allah ai inaga gobe semu ƙara kaɗan koya kukaga?" ta tambayesu cikin kulawa, abincin data kawo masu sukeci sannan hussaina ta dubeta"Eh amman fa amfi son dambun kada ki daɗa alalan barshi a na rabin kwanon kawai", tafaɗa tana kai loma bakinta"to shikenan babu komai Allah ya kaimu bari shahid ya dawo seya koma janguzan ya siyo mana abinda babu nacikin kayan haɗin dambun".tafaɗa tana mikewa ta shiga ɗaki.Abincin suka cigaba daci har suka kammala sukai sallah sannan suka nufi ɗaki ƴar hutun tana kwance saman katifa tana sharar bacci ranta fess, da kallo suka bita kowacce ta kama sabgar gabanta. Se yamma ta tashi tana raba ido sabida rashin sallar la'asar ɗin da batayiba cikin azama ta mike tana musu barka da zuwa sannan tayi tsakar gida tayo alwala, sallah tayi sannan tahau tambayarsu harsun dawo da wuri haka, ganin basuda wani aiki yasa suka zauna suna bawa Bebi labari."Hmm Bebi bakiga yadda kamfanin yayi kyau ba, wajan aje motoci daban wajan aje babura daban , gefen masallaci muka zauna awajan wani tebur bakiga yadda ake ciniki ba, sabida mukaɗai ne masu abinci awajan, amman inaga zamu sayi pure water muna saidawa dan naga babu mai kawowa" cewar hussaina kenan"A,a da akwai kanti fa daga bayanmu kuma nasan ƙila yana saida ruwan".cewar hassana tana dariya,sosai suke hira awajan har wajan magariba sannan shahid ya dawo wanda daman daga dawowarsa daga skull mama ta aikasa janguza, shinkafa dasu zogale da mai ya siyo masu, a tsakar gida ya dire wanda su mama suka fito suna masa sannu, da zuwa harda Bebi ake aikin zage zogalan shinkafar mama ta haɗawa ihsan  ta bata ta kai mata ɓarza, sukuma suka cigaba da haɗa kayayyakin dambu da alalan gobe, har zuwa magariba sannan, suka ɗora abincin dare kana kowa ya tafi yay sallah yaudai bebi akwai abin arziki sabida ta xage ta tayasu aiki sedai ko aranta batajin zata je wannan waje sabida bataji ranta ya kwanta dashi ba.
Har dare suna ƴan aikace aikacensu, abinci sukaci suka wuce makarantar dare bayan sun dawo suka kwanta bacci dabida shirin fitar gobe.

Tunda ya sauka A legos yake gudanar da ayyukanshi cikin nutsuwa sabida ya riga ya saba da nan ya kuma san jama'a sosai, agidan abba nacan wanda suke zama ya sauka, da safe ze fita

office da yamma ya tashi, ya umar daman tunda Aliyu ya je shikuma ya dawo gida, waya kawai yake da ammi wadda kullum zancenta akan lefe yake wanda tuni tabayar da order kayan lefen nashi sabida bikin harda na Amina za,a haɗa.
Yau takama sunday wanda ya rage kwanaki biyu ya dawo kano zaune yake a saman sopa system ɗinshi aje bisa cinyarshi, jikinshi sanye da jallabiya milik aikine gabanshi sabida yana turawa wani kamfani achaina wasu samfur waɗanda sukeson a shigo masu dashi, wayarshi dake yashe a gefece take faman ringing! wajan sau biyu yana dubawa baya ɗauka ana ukunne ya ɗaga"Assalamu Alaikum" yafaɗa batare daya duba sunaba, jin muryar lina yasaka shi dawo da wayar ya katse tare da wullata saman gado ya jima yana aiki akan system ɗin tashi kafin ya gama ya ɗauro alwala ya fita.

_YAHAYA GUSAU_
"Nagaya miki kidinga kame kanki agabanshi shifa namiji muddin yaga zaƙuwarki akanshi kin bonu".cewar wata babbar mace fara, wadda take gaban wannan budurwar Khadija, tura baki khadija tayi"Wallahi umma a kullum son yaya ƙara ruruwa yake araina ina sonshi har cikin zuciyata wannan dalilin yasa naji banson part ɗinku na koma na ammi sabida ina ganinshi kurum kodan naji sanyi araina".murmushi wadda aka kira da umma tayi"Ai Aliyu abinso ne ga kowa bake ba na tabbata kowace mace zataso yazama mijinta kodan tarin dukiyar da Allah ya bawa mahaifinshi wanda kaf cikin gidan nan arxikinsu mukeci nima wannan dalilin na matsu ki aureshi kodan kishiga jerin manyan matan masu kuɗi".haɗe rai tamau khadija tayi"Nifa wallahi umma banson irin wannan halin naki, sabida Allah nikeson shi wallahi umma badan komai ba Kuma Allah ma yasani son ya Ajinina yake".tafaɗa tana lumshe idanunta,"hahaha yaro yarone ai shikenan tunda kin kasa gane karatuna nan gaba da kanki zakizo kina cewar na kuma yi miki bita"tafaɗa tana tashi daga wajan da khadijan take.
Tana fita khadija ta mike hotonshi dake saman wayarta ta tsirawa ido hartana hadiyar miyau tana kallon hoton tana lumshe idanunta ahaka bacci mai dadi ya fisgeta cike da tarin soyayyarshi acikin ranta.

Ɓangare gidansu Bebi kuwa washe gari da wuri su hassana suka fita tare da taimakon motar da shahid ya samo musu kai tsaye a bakin kamfanin motar ta tsaya suka fito suna haɗo kayan su zuwa waje.........

MANAGE

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*19 & 20*

Cikin nutsuwa suka gama fitar da manyan kulolin, da taimakon drivern daya kaisu suka shigar da kayan abincin cikin kamfanin, baban nazir ne ya kai musu har kan teburin da suke zama, sabida yadda yake jin tausayin yaran, kuɗin motar hassana ta bawa drivern tare dayi mishi godiya sannan itama ta ƙarasa inda zasu zauna, bayan sun gaisa da baban nazir ya wuce office sabida yana sauri zasuyi meating.
Yau kamfanin babu yawan shige da ficen mutane kodan sabida safiyace tsuru sukai akan bencin dasuke zaune duk jikinsu yayi sanyi suna tunanin kada Allah yasa dai abarsu da kwantai yau.
Shigowar wata farar mota cikin wajan shine yajawo hankalinsu hussaina, cikin nutsuwa motar ke tafiya harta karasa wajan da ake adana sauran motocin kamfanin, tsirawa motar idanu sukai sabida tsabar yadda ta haɗu, sun jima basuga fitowar na cikintaba, dan har hassana ta mike tana zubawa wani security dambu tana komawa zata zauna, sukaga wani magidancin namiji kamilalle cikin shigar manyan kaya farine tass goshinsa dauke da tabon abin sallah, wayace kare a saman kunnenshi dan da ƙafama ya tura marufin motar yana tafe yana cillah key ɗin hannunshi yana dariya yana magana a wayar.
Da sauri sukai ƙasa da kansu ganin yana kusanto inda suke.
Cak ya tsaya agaban kulolin dake gabansu yana cigaba da wayar, cikin harshen turanci..
Yakai kusan mintuna goma a wajan yana wayar kafin ya kammalata yana mayar da ita cikin aljihun wandonshi.
Ƙarasowar baban nazir yasa suka ɗan sauke ajiyar zuciya domin su da sunɗan firgita da yadda sukaga wannan mutumin yana kallonsu.
Cike da far'a baban nazir ya ɗan rissuna gaban wannan mutumin yana gaisar dashi cikin ladabi.
"Oga Usman barka da safiya, wallahi yanzu su manager suketa tambayar ko lafiya baka shigoba duk an hallarafa kai kawai ake jira". yafaɗa yana sadda kanshi a ƙasa.
Cikin sakin fuska wanda aka kira da oga usman ya dubi babansu nazir kana yace.
"A,a fa ni ai ba wancan bane inada iyali dole se nagama sharafin gabana, watakan kun saba

aiki da wancan mai fuskar zakunan shiyasa kuka saba dako sammako kamarshi toni fa wannan satin dole se kamfanin nan ma yasan dawa Allah ya haɗashi" yafaɗa cikin barkwanci yana dariya.
Shima baban nazir dariyar yayi sabida kowa yasan halin Usman mutum ne mai tsananin barkwanci shiyasa yakeda da jama'a sosai awajan shifa kowama janshi yakeyi.
Hankalinshi ya mayar kansu ƴan biyu waɗanda tun fara maganar sukai ƙasa da kansu suna dai sauraran wannan dramar da ake agabansu.
"A,a kai kace kwana biyu Allah ya hutashshe da madam ɗita masu abinci muka samu ashe?,kasan jiya friday banzoba shiyasa ban gansuba" yafaɗa cike da kulawa.
Dariya baban nazir yayi kana yace"ƙwarai kuwa wallahi ƴaƴan yayan matata ne da Allah ya masa rasuwa nine ma na kawosu nan ɗin kasan rayuwar seka mike ƙafa yanzu".
Cikin tausayi usman kebin ƴan biyu da kallo yara kyawawa tubarkallah dasu amai makon a basu ilimi mai kyau shine za,a dinga ɗora musu talla damma yaga yaran sunada nutsuwa sosai. Muryarsu ce ta katse shi suna faman gaisar dashi cikin nutsuwa, shima cike da sakin fuska yake amsa musu idanunshi akansu yana jin tausayinsu har cikin ranshi domin yaran abin a tausayawa ne.
Cikin mintuna uku yagama nazarin su daga gani za,a sami cikakkar tarbiya wajansu duba da yadda suke a kame babu baragada daga gani mahaifiyarsu ta tsaya akansu sosai wajan basu tarbiya.
"Toni ai kun sakani a duhu dan babu yadda zanyi na shaida wace hassanar wace kuma hussainar?" yafaɗa yana murmushi kaɗan.
Cikin nutsuwa hassana tace.
"Nice hassana wannan kuma hussaina" tafaɗa tana yin kasa da kanta.
"Masha Allah koke fa kunga yanzu idan naganku zan iya shaidaku to bara mu shiga ciki kunji Allah ya baku sa,a dafatan zaku ɗan sammun ladan ganin ido" yafaɗa yana dariya dukansu dariyar sukai tare da furta "Mai ze hana". zaro idonshi yayi waje"A,a kuce ƙannan nawa masu kirkine a,a ni bazan karya ba sedai na ɗora kada umma ta dakemu".yafaɗa yana murmushi.
Shikam baban nazir tsananin mamakin yadda usman ya sake da yaran yakeyi duk da yakasance mutum mai barkwanci amman dai kam bai taɓa sakewa da kowa kamar hakan ba. Wayarshi dake aljihunshi ita ta katse masu dariyar dasuke yi.
"Ya salam gafa alhajin faɗa nan yana kira" yafaɗa har yana wani rike baki kamar wani yaro karami.
Aikuwa tunda ya ɗauki wayar suke jiyo sautin wata dakakkar murya wadda sautin fitarta har waje amman yanayin maganar da yadda ake sauri wajan fadinta baya barin na waje yaji taka mai man akan abinda ake faɗan sedai kuma kana dai ji kasan faɗa akewa wanda ya dauki wayar.
"Yau inaganin tujara yanzu kai dan ubanka ni yayanka kakewa wannan masifar! to ai seka dako sammakon dare kazo kanon agogo sarkin aiki ai kaine namiji mu duka matane" yafaɗa yana dariya tare da katse wayar.
Baban nazir ya duba.
"Kaga zo muwuce ciki tun kafin wancan mai bakar zuciyar ya zagen, wai kaji faɗa yake akan wai baki zasu zo tun ɗazu ake zaman jirana nai sing naki fita office wai aikin minake agidana, kajifa ni mai iyali har ze gayawa haka?" yafaɗa yana dariya.

"Ai kasan halin yallaɓai shi baya son sanya wallahi mu kammu mu ringa mun saba da horanshi" cewar baban nazir yana kallon usman.
Gaba usman yay yana cewa su hassana anjima ze aiko masinjanshi ya sai mashi dambu kana ya kama hanyar shi yay gaba sabida sanin halin tujarar Ali kada yaje ya haɗa masa bom wajan abba.

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

*Siyan nagari mayar da kuɗi gida ga arha ga ƙarko kudai maza ku garzaya ku nemi taku Suna sayar da MTN data akan price Mai sauki 1gb 300 2gb 600 expire 30 days ga masu bukata suna iya tuntuɓarsu akan wannan number din 08066268951*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*21&22*

Hassana ce ta juyo wajan hussaina tare da ce mata"Hmm wannan bawan Allah baya da matsala jiba kamar ba mai kuɗiba yadda ko ƙyamatarmu bai ba".tafaɗa tana ɗan kaɗa idanunta kaɗan,"To ai daman wasu mutanan zakiga Allah ya zuba musu sauƙin kai tamkar bamasu kuɗiba aidaman ba duka aka taru aka zama ɗaya zakiga ai ko a talakawan akwai masu izza to kuma suma haka masu dashi ɗin akwai masu izza da ƙi faɗi", hussaina tafaɗa tare da mikewa sabida zuwan wani ma'aikaci zesai dambu bayan ta zuba mashi ta dawo ta zauna tana cigaba da hirarta da ƴar uwarta, cikin ikon Allah ahaka akaita zuwa wajan siya wasu sukan zuba musune a packet wasu kuma anan zasu zauna saman bancinan wajan suci su ƙara gaba abunsu.
_CIKIN BABBAN ƊAKIN TARO NA MUSAMMAN DAKE CIKIN KAMFANIN MAI ATAMFA_

Sosai suka zauna tare da manyan cikin kamfanin suka tattauna akan abubuwan cigaban da kamfanin nasu ya samu duk da kasancewar kamfanin sabone amman kuma ikon Allah haryaso yafi na *mundaɗu* samun jama'a sosai kuma duk ba kowane yay silar haɓɓaka wannan kamfaninba kamar *Aliyu Idiriss Mai atamfa* wanda shi kanshi usman ɗin ya jinjinawa ɗan uwan nashi yakuma san dukkan wata nasara da kamfaninsu na nan dama sauran suke samu tofa tare da taimakon ɗan uwan nashine saninsa mutum mai ɗan banzan naci tare da mayar dakai akan dukkan abinda yasaka agabanshi tofa da zarar ya kafe babu zancen bari, duk da kasancewarshi mutum mai wuyar sha'ani amman hakan bai saka ya samu miskila wajan iya hulɗa da mutane ba wanda hakan ya kuma jawo mashi ƙara samun tarin mutane yadda ba,a zato sosai mahaifinsu yake alfahari da Aliyu sabida yadda yake bashi gudunmawa fiye da sauran ƴan uwanshi.
Sun kammala taron su cikin awowi biyu kacal wanda aka tashi cikin farin ciki gami da fahimtar juna, anan usman ya ƙaddamar da abinda ze ƙaddamar kafin kuma mai gayya mai aiki director manager ya dawo, sosai.

_BAYAN KAMMALA TARO_
Zaune yake cikin offishinsa, asaman kujera irin wadda take kaɗa mutum tana juyashi batare dayay tsammani ba.Kiran masijanshi yayi tare da bashi umarni akan yaje yazo mashi da Salihu( baban nazir ) cikin mutuna biyar masinjan nashi ya shigo bayanshi baban nazir ne wanda wannan kiran na oga usman ya firgitashi addu,a yake kada Allah yasa oga usman yace.
Su hassana su daina kawo abinci kamfanin, sabida yaran suna bashi matukar tausayi ba ɗan kaɗanba, sannan kuma su kansu sunajin daɗin taimakon abinci ko banxa ka huta shan lemo da burodi.
"Haba kaiko kamar ba namiji ba, daga aikawa kazo kazomin kana muzurai nanfa ba office ɗin dodonku bane".
Muryar usman ta sauka cikin dodon kunnen baban nazir wanda tun zuwanshi daya rissuna yake faman tunani shi ɗaya bai kuma ɗagoba seda yaji muryar usman ɗin data katse mishi tunaninshi.
Sosa kanshi yay kaɗan tare da kallon oga usman ɗin tare da cewa.
"Ai oga bansaba jin kana kirana haka kurum bane harga Allah naji wani abu acikin zuciyata har ina addu,a Allah yasa ba dakatar da yarancan zakai ba".
Yafaɗa kanshi tsaye sabida duk tunaninshi ya riga ya tafi akan hakanne.
Da hannu usman ya sallami masinjanshi dake tsaye awurin batare daya juya ba.
Sannan ya gyara muryanshi tare da kallon baban nazir.
"Malam salihu idan babu damuwa ina bukatar daka zauna akan ɗaya daga cikin waɗannan kujerun mana".
Yafaɗa tare da zube dukkan hannayenshi asaman teburin gabanshi yana kallon baban nazir da tausayawa.
Cikin sauri baban nazir ya miƙe tare da komawa saman emty chair ɗin dake cikin office ɗin wadda ta kasance ta silver, sannan ya mayar da hankalinshi kan oga usman ɗin.
Gyaran murya oga usman yayi tare da  kallon baban nazir.
"Ai malam salihu ina zaton kai da kanka zakaje kana bada labarin halinmu kaf! bama ni kaɗai ba wallahi ko Aliyu da kuke ganinshi haka bani zaton ze iya wulaƙanta ɗan adam bare kumani,

saboda me?, dukkaninmu bamusan me rayuwar zata kaimu gaba ba.to dan haka ina son ka cire kokonton wani abu daban acikin ranka wallahi ka ɗauka kamar nan ɗin kaima wajanka ne, sabida haka ina musu fatan nasara acikin sana'arsu ni babu ruwana da wani danyazo yaci arzikinmu nai masa ido ko bakin ciki,
Sabida haka ni ba wannan tasa na kiraka ba, daman tambayar ka zanyi idan babu damuwa. Kasan madam ɗita se ahankali kwana biyu bata cika lafiyaba wallahi kullum problem ɗina abinda zamuci, na break na lunch dinner, kuma kaga dai rayuwar yadda take kuma kasan mata nan idan sunada juna biyu se addu,a shine nace idan babu damuwa kozaka tambayamin mamar yaran nan akan tabani guda ɗaya inje gida da ita sabida ayyukan gidana da girki?".
Zubafe ta ketowa baban nazir wannan shine ga ƙoshi ga kwanan yunwa yasan ko ana yaki bayajin maman ƴan biyu zata bada yaranta aikatau sabida tunba yauba ake wannan mujadalar amman tace ita bata yardaba tafison ko tsakuwa a misali zataci tofa taci tare da yaranta.
"Ban musa makaba oga amman gaskiya mahaifiyarsu ce batada ra'ayin hakan amman zan tambayeta ko Allah zesaka ta yarda".
Cewar baban nazir wanda kawai yafaɗi hakane amman yasan hakan bamai yuwuwa bace.
Cikin ilimi tare da nazari usman yagama fahimtar baban nazir shi daman bawai matsuwa yay sosaiba tunda akwai masu aikin sedai kawai yadda yaga tsarin yaran da tsaftarsu yakeson ya daukesu ko girkine kodan ya sami kafar taimaka masu amman tunda abin bazai yuwuba kawai ze hakura.
"No Salihu karka matsa kanka amman pls dan Allah inason ka tabbatar min da tsaftarsu kawai sena dinga order dambun ma kawai is ok domin madam tana son dambun sosai".
Dariya baban nazir yay.
"Tabb oga ai wallahi ko madam baxata nunawa maman biyu tsaftaba amman kaima zaka tantance ko yadda kaga yaran da yadda komai nasu yake a tsaftace".
Yafaɗa yana dariya shima usman ɗin dariya kurum yay yana cewa"watakan dannafi yadda yasa ka haɗa harda madam ɗita lallai malam salihu ka rainani da yawa" yafaɗa yana kiran masijanshi.
Wata babbar kula wadda yake zuwa da abinci cikinta ya baiwa masinja sabida daman kwana biyu ba,a zuba komai cikinta sedai ai masa take away a waje,"Je wajan yarancan su bani dambu" yafaɗa wa masinja tare da buɗe locar ya fiddo sabbin kuɗi ya bashi"Kada ka tsaya amsar canji kaji kavar masu duka kace inji yayansu" yafaɗa yana dariya"Malam salihu ka iya tafiya kawai, bama seka je ka gaya mataba barshi na dinga siya kasanmu ƴaƴan ammi Allah ya ɗoro mana san dambu kaf ɗinmu" yafaɗa yana fiddo wayarshi daga aljihun wandonshi sallama baban nazir ya mishi ya fita.shiko madam ya kira ya sanar mata maganar dambu aikuwa abinka da mai ciki tahau murna nan da nan tace zata aiko driver ya bata kasonta.

_DAGA WAJANSU HASSANA_
Lokacin da masinjan usman ya kai musu flaks ɗin sosai sukai mamaki ganin dalla dallan kuɗin daya zaro ya miko musu tsorata..........

*MATA DA MAZA YAN KASUWAR DAKESON NA TALLATA MUSU HAJARSU A SAMAN

SHAFUKAN LITTAFINA CIKIN FARASHI MAI SAUKI ZASU IYA NEMA NA TA NAN 08142105218*

*MASU SON LITTATTAFAINA DANA KAMMALA KAMARSU*

*ƊAN MAJALISSA*
*HASKE*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*DA IZZATA*

*DUKKANSU AKAN FARASHIN NAIRA DUBU ƊAYA,1000 IDAN KUMA ƊAI ƊAI KIKE BUKATA 300 DOCUMENT A HADE SE KARATU ZAKI TUNTUBEN ANAN 08142105218 DOMIN KI BIYA KI MORE KARATU*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

*ƊAN ƊANO DAGA LITTAFIN SIRRIN MU*

Yadda kake tunanin rayuwa ba haka take ba,da lokota da dama kana iya gane SIRRIN wasu, Amma wani lokaci naka SIRRIN dake bibiyar Rayuwarka wahalar gane masa kake,Yau Uban daya haifesa ya kawosa Duniya shine da gansa ya masa sharri,Shi ne ya saka za'a kai shi gidan yari,Matar da yafi so fiye da komai nasa,wacce ta zame masa Uwa,Uba,Yaya,Kanwa,Aboki yau itace Mahaifinsa ya kwanta da ita har ta ɗauki cikinsa,Kuma yanzu shine ake cewa shi yay mata CIKIN,da me zaiji? Da nakasar da take damunsa?ko kuma

da BAƘON YANAYIN daya tunkaro sa?Wannan SIRRIN MU ne bai kamata ace kowa ya jishi ba,SIRRIN MU ne nida mahaifi na,SIRRIN MU ne nida Matar da nakeso, SIRRIN MU ni da Aljanun da suke tare da ita.

_JAMA'A WANNAN MARUBUCIYAR CE DAI WACCE TA NISHAƊANTAR DAKU A LITTAFIN *MOON* DA *UNCLE NE* GA KUMA *THE NEW EMIR* SBD NIN DAƊIN MASOYA YASA SAI TA GAMA PART ONE ZATA FARA SAKINSA WANDA ZATA NA BAWA ƳAN *VIP* POSTING 2 KULLUM A RANA ƳAN *NRML GRP* KUMA POSTING ƊAYA A RANA NASAN KUSAN *NIMCYLUV* TAURARUWAR MARUBUCIYA MAI TASHE😂

ZAKU IYA PAYMENT TA WANNAN ACCOUNT ƊIN

0116886423
Sulaiman Naima s union bank evidence of payment 08119237616

400 for nrml grp
600 for vip

*23&24*

Cikin mamaki mai ɗauke da tsoro hassana ta dubi masinjan ayayin dayake Miƙo musu kuɗin hannunshi tare da cewa,"Gashi inji oga usman yace ku zuba masa dambun, amman kada a saka yaji".Karɓar flaks ɗin hassanar tayi ta soma zuba masa harse da ta cikashi damƙam har baki sannan ta rufe, kuɗin ta amsa a hannunshi ta ƙirga iya wanda tasan yakai adadin na dambun ne sannan ta mikawa masinjan ragowar canjin, wanda shi harya soma tafiya tai saurin binshi, sakato yayi tare da cewa"Ai yace kada na karɓi ragowar na baku duka", ɗan jim kaɗan tayi tare da kallonshi"A,a dan Allah kace masa yabarshi sabida mamammu zata mana faɗa idan taga kuɗin ya haura".tafaɗa tana miƙa masa kuɗin kana ta koma wajan sana'arsu, miƙawa hussaina kuɗin tayi tana mata bayani, zaro idanu hussaina tayi tare da cewa,"Lallai wannan mutumin yau soyake mama tai yanka yanka damu kenan",dariya sukai atare "Aidaman shiyasa nayi saurin dakatar dashi tun wuri" cewar hassana wadda ta mike zuwa wajan zubawa wani alala.
Shiko masinjan usman yana komwa office ya tarar da ogan nashi yana amsa waya, dakatawa yayi harya kammala sannan ya rissuna ya mika mishi tare da cewa...........

"Oga wallahi fafur sunƙi karɓar kuɗin wai mamansu zata musu faɗa idan taga kuɗin ya haura, wallahi oga babu yadda banyi dasu ba, amman sunƙi amsa".
Yakai maganar yana rissunar da kanshi a ƙasa.
Ƴar dariya kaɗan usman ya sauke tare da jinjina wannan lamarin.
Daman ana samun yara masu tarbiyar nan har yanzu? tabbas duk lalacewar zamani ba'a taɓa haɗuwa a zama ɗaya dole akwai nagari sannan kuma akwai ɓata gari.
Sau tari wasu yaran tsananin babu takansa su sallama kansu wa  mazan banza domin su sami abinda zasu ci, wasu kuwa tsabar kwaɗayine ke rufe musu idanu, harsu faɗa halaka, wasu kuwa laifin iyayen sune.
Amman su waɗannan yaran kana kallonsu, dai kasan bamasu wadata bane, amman daga gani sunada tarbiya sannan kuma mahaifiyarsu a tsaye take domin ganin ta basu tallafi ta ko'ina.
"Oga ga dambun fa".
Yaji muryar masinjan a saman dodon kunnenshi.
Ɗagowa yayi fuskarshi ɗauke da murmushi kamar koda yaushe sannan ya dubi masinjan nashi.
"Ok ka ajemin saman frij nagode kaje da ragowar canjin kasayi wani abun".
Cikin rawar jiki masinjan ya dubi usman tare da rissunawa sosai gabanshi.
"Kai oga bansan dame zan maka godiya ba, amman ina roƙon Allah daya saka maka da mafificin alkairinshi amin nagode ƙwarai".
Daɗine ya kama usman na wannan godiya murmushi ya saki tare da ɗagawa masinjan hannu batare daya ce mashi komiba.
Aikin dake gabanshi ya cigaba dayi batare daya kumabi takan zancen ƴan biyuba, amman yana ji aranshi tabbas ze duba lamarin yaran yanajin ze tallafesu da wani abun.
Ya jima a office ɗinshi yana aiki har aka kira sallah, bai samu fita masjid ba amman yayi acikin office ɗinshi sannan ya ɗauki flate ya zubo dambun da masinjanshi ya aje masa shi bisa frij, Tun kafin ma ya kai lomar cikin bakinshi yaji wani sihirtaccen kamshi mai ɗaukar hankali ya shiga cikin hancinshi.
Wani irin ƙamshin attaruhune tare dasu albasa, ga gyaɗa tabi lafiyar saman dambun ga wadataccen zogale malam, tuni usman ya soma haɗiyar miyau jikinshi yana mazari, ya koma saman raising chair, ya zauna kana ya ɗora ƙafafunshi ɗaya kan ɗaya,  ya fara da bisimillah a cikin bakinshi sannan ya ɗauko spoon ya soma ɗibar dambun.
Wayyooo! tuni usman ya soma mazari kunnenshi ya soma rawa at list usman seda yay flate biyu na dambun da ƙyar madam ɗinshi ma ta samu ɗan kaɗan wai hakan ma sabida darajar cikin jikinta ne yasaka ya rage mata shi,Sosai yaji daɗin dambun seyace idan ba ammi ba babu wadda takai wannan matar iya dambu,ruwa ya buɗe yasha tare da hamdala ga sarki Allah kana ya koma gaban aikinshi yana ayyana yadda ze ringa bada kuɗin nashi na mussaman sabida matukar daɗin da dambun yayi mashi.

Wajan karfe ukun rana Allah ya taimaki su hassana dambun nasu ya ƙare tas! har ana nema shima alalen babu laifi ya kare yau ɗin sedai baikai dambun kasuwaba.
Na baban nazir dasuke ware mashi hassana ta ɗauko tana kallon hussaina"Tomu yanzu yaya zamuyi da dambun baban nazir kinga har mun tashifa bai zoba", cikin kulawa hussaina ta dubeta tare da cewa"Ki bawa mai gadi idan ya fito seya bashi kawai" wannan shawarar ta karba haka ta kaiwa mai gadi dambun baban nazir sannan ta koma wajan ƴar uwarta suka haɗa

kayansu, aka suka ɗora kulolin har zuwa bakin gate yau sun ɗanyi jinkirin samun abin hawa, kafin kuma Allah ya basu iko wani yazo sukai ciniki suka hau suka wuce gida.

Cikin mintuna talatin suka isa gida a bakin layi suka tsaya tare da sauke kayansu, yauma kamar kullum shahid ne ya taimaka musu da ɗaukar kayan zuwa gida, bayan suma sun sallami mai napep ɗin suka wuce cikin layin su.
Cikin farin ciki mama take musu barka da zuwa yauma kamar kullum ta taresu da ruwa tare da abinci,"Mama banga Bebi ba tana ina?" cewar hussaina, murmushi mama ta saki"Tunda ta dawo daga makaranta ta shige ɗaki ko hijabi bata cire ba naga dai ta kwanta". tafaɗa tana mikewa zuwa bakin rariya"Mama kodai mutanan natane zasu hauro?".cewar hassana,"A,a inaga ko baccine yaci ƙarfinta kinsan fitar sassafan data tsira gudun karta fita talle".dariya hussaina tayi"Aikuwa mama ta shirya inaga ranar lahadi tunda basu da school ita zatabi hassana".juyowa mama tayi tare da kallon hussaina"Akan wani dalilin ke zaman me zakiyi agidan? tunda ku kunyi Candy base ku fita ba ita kuma da Allah yasa yanxu ta mayar da hankalinta ga karatun nata seku barta taje kafin mugani itama idan ta gama ɗin me Allah ze mana".
Turo baki hussaina tayi sega hawaye nan shaaaa! sun wanke mata fuskarta"Haba mama yanzu tsakani da Allah ita kullum  sedai taci tai kashi ta kwanta mu zamu fita ita bazata iya kama mana ba", tsame hannunta tayi daga ruwan wankin shinkafar gabanta ta dawo gaban yaran nata, tagumi tayi tana kallon yadda hussaina take kuka!
Hassana kuwa tai kicin-kicin da ranta kamar kace mata kat! tasaka ihu! daman tasan halinsu tun tana goyonsu ɗaya baya abu ɗaya yay shuru.
"Kinga daina kuka! akanme zakiyi kuka? indai akan tallan Bebine yi haƙuri kuma ku daina gaba ɗaya mu haɗa kai mu zauna semuci abinda zamuci a ahaka, kunsan dai halinta bana son ta fita taje ta ɗauko mana abinda  yafi karfinmu ko, kuma bawai bana sonku ko neba bakuma bam-bamci yasa nake cewa kukai ba duka-duka idan kuka kwantar da hankalinku kwana nawane kun daina ma gaba ɗaya, bana son Bebi taje musu waje tai abinda ze jamana matsala, tunda Allah yasa ta koma makaranta shikenan zancen rashin aikin da batayi agida kuma wannan kanta dan akwai lokacinda setai kuka da takaicin haka bawai ina mata baki bane, Ai ita ƴa mace indai tace son jiki da rashin aiki xatai wallahi to tana tare da muguwar matsala Allah ya gani ina yi kokarina akanta amman tunda ita haka Allah yayita ina nan ina addu,ar Allah ya haɗa ta da miji mai tsafta.
Mai kuka ce ta fashe da dariya hartana kifawa"Mama miji mai tsafta fa?", cewar hussainar tana dariya kamar ba ita ke kuka! ba.
"Eh mana, ba shine maganinta ba".
"Daman mama tun ɗazu mukai maganar da hassana ranar lahadi su fita da BeBi nikuma senayi mana wanki sabida ko hijabin fita bamu dashi gobe, wallahi duk sunyi datti amman idan baki so mama na hakura sena fitan Allah ya baki hakuri".
Kallon su tayi da kalar tausayi sannan tace, "Nifa duk ba wani abu bane hakan kuma banji haushinku ba sabida kuma mutanene kamar kowa sabida Ki zauna Allah ya kaimu se taje ɗin"
Tafaɗa tana tashi daga wajansu.
Aguje sukaga Bebi ta fito daga ɗaki tana rike cikinta.
Bakin rariya ta tafi tana sheka amai! tana dafe da mararta wadda take kokarin tsinke mata

sabida azabar ciwo.
Cikin azama hussaina tayo kanta"Ke BeBi miya sameki haka?,
"Marataaaaaaa wayyo zan..za....zan.............

_Awanke hannu a tadani glass_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

SADAUKARWA GA
*Kausar Salis Usman aglannissa*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*26&27*

"Wayyo! zan mutu marata ciwo takemin mutuwa zanyi wayyo Allah nahhhhh", taja maganar da ƙarfi tana dafe marar tata zubewa tayi a wajan numfashinta yana fita kaɗan-kaɗan, cikin firgici ƴan biyu suka ɗagota da ƙyar sabida yadda take da girman jiki, saman tabarma suka kwantar da ita ihsan ce ta wanke bakin rariyar, Sosai suka firgita ga yadda take cije bakinta, Cikin nutsuwa mama ta taso daga gaban murhun kicin duk jikinta yayi wani irin mugun sanyi ƙalau. Gaban ta tazo ta xauna tana kallon yadda ƴan uwan suka zagayeta"Hussaina miƙomin ruwa a

kofi", cikin azama hussainar taje ta ɗebo mata ruwan ta kawo mata, karɓa tayi ta fara tofa mata addu,a acikinsa sannan ta tallafe kanta ta bata a bakinta wani ya shiga wani kuwa bai shiga ba ragowar ta ɗaga rigar uniform ɗin jikinta ta shafa mata,Janyo numfashi tayi kaɗan. tare da juya kanta gefe tana ɗigar da hawaye daga cikin idanunta, "Sannu Bebi, Sannu Bebi".haka ƴan uwan nata keta faman faɗi gaba ɗayansu idan ka cire shahid wanda bai san miyake faruwa ba yana can wajan gawayinshi.
"Kunga kutashi kuje ɗaki ta samu tasha iska kunga nan ɗin baya da wadata sosai".cewar mama wadda takeson taɗan buɗewa Bebi jikinta tasha iska sabida gumin dake zubo mata, Babu musu suka miƙe dukkan su tare da shiga cikin ɗaki jikinsu sanyi ƙalau.
Tube mata hijabin jikinta mama tayi, tare da ajeshi gefe guda sabida daman tunda ta dawo daga makaranta, taje ta kwanta bata tube kayan makarantar ba.
Share mata gumin dake yanko mata ta goshin nata tayi tare da ƙara karanto addu'oi ta tofa mata a saman goshin nata.
Buɗe idanunta tayi tare da mirginawa saman cinyar mama tana cije laɓɓanta kaɗan kaɗan, buɗe matsakaitan idanuwanta tayi waɗanda suka rine sukai wani irin jajur daga gani kasan tana shan wahala.
Ahankali ta furta,"Mama marata kamar zata cire wallahi" a yadda tai furucin maganarma kaɗai ze baka tabbacin tana jin jikinta sabida sam Bebi bata magana a hankali sedai kaji maganar tata tamkar daga nesa amman yau tayi magana cikin nutsuwa.
"Garin yaya hakan Bebi ko zaki soma al'ada ne, shiyasa ya zo miki da haka?" mama ta faɗa tana saka hannunta tana gogewa Bebi zubar saman goshinta.
Wata iriyar damƙa takaiwa mama tana furta salati cikin wani irin yanayi kuma jikin nata yay lakwas, kamar mai bacci.
"Mama wani abu yana bimin jikina yana fitomin daga cikin pant ɗina",tafaɗa tana mikewa zaune, duk fuskarta ta jike da hawaye, take mama ta gane baƙon watane ya zowa Bebi, wanda take tunanin ita nata mai azabar ciwon mara ne.
Cikin azama mama ta taimaka mata takai mata ruwan zafi banɗaki bayan ta surka mata shi, ɗaki ta shiga ta ɗauko mata zani da Vest, sannan ta ɗauki naira ashirin ta bawa ihsan akan taje ta siyo mata maganin ciwon mara a chamist, ƙaton fallen zani mai kyau mama ta ɗauko ta fito dashi tsakar gida lokacin Bebi harta tube kayanta ta shiga wanka, hannunta dauke da wandunanta waɗanda suka.ɓaci da jini, itama ƙyamar jinin ne ya kamata gefe ɗaya kuwa tsorone fall ranta ganin yadda wai wannan jinin daga jikinta yake fitowa, aikuwa kafin tagama wankan ta zubar da hawaye yafi kwando sabida tsoratar dake shake a zuciyarta.
Muryar mama taji daga bakin kofar bayin, tsumman data yanka da pant take miko mata ta ɗan bular jikin kofar bandakin,"Maza kiyi ki gama wanka ga shinan na ninka miki seki saka tadai gaya mata yadda zatai a takaice sannan ta dawo ta zauna, itako Bebi acikin bandaki kukan ta cigaba dayi da ƙyar ta iya saka tsumman a jikinta tanajin duk ya cika mata hq, haka ta rufa zani ajikinta sannan ta ɗauraye wandunan dasuka ɓaci kana ta fito waje tana harɗe ƙafafunta kamar ƴar........, Seda ta zo gaban mama sannan ta ɗauki Vest ɗin ta saka batare data saka bra ba sabida daman ita ba damunta tai ba, sallamar ihsance ta katsewa mama hanzari amsa mata tayi sannan ta karbi sakon maganin, hassana ta kira daga ɗaki tazo tace ta zubowa Bebi ɗan ruwan shayin da ake ajewa arfa ƴar autar mama sabida tana sonshi sosai, zubowa tayi acikin kofi tare da cokali, ta mikawa Bebi sannan ta kuma mata sannu ta koma ɗaki, bayan ta amshi

kofin ta kafa abakinta tana kurɓa tana hawaye, ƙura mata idanu mama tayi tana addu'a acikin ranta Allah ya kawowa Bebi miji ta aurar da ita sabida koga yanayin girman jikinta kaɗai ka gani seta baka tsoro kullum ka ganta kamar hurata ake seka ɗauka rainon madara ce duba ga yadda tsarin cikar halittarta yake bazaka taɓa ɗauka anan gidan takeba, kirjinta kamar na ƴar shekaru ashirin babu mai kallon Bebi kace mata shekarunta sha shida sabida yadda take kamar zata fashe, wannan girma na Bebi yana ɗagawa mama hankali, musamman idan ta duba taga yadda rayuwar nan ta koma wasu mazan basa tsoron Allah suna ganin yarinya kamar Bebi wadda babu laifi tana da kyan sura tofa idan mai kwaɗayi ce xasu ribaceta ne suyi lalata da ita, wannan yana ɗaya daga cikin abinda yasa take ɗan tsawaita tsaronta akan Bebi fiye da sauran sabida ita Bebi surarta a bayyane take komai zafa ta saka danta rufe jikinta sefa ta bada sharp,duk da ita bata isa ta hana Allah ikonshi akan ƴar tata ba amman tana iya kokarinta dantaga ta killaceta bama ita ba harma sauran ƴan uwan nata wallahi wannan tallan dan babu yanda zatayi ne amman da tuni ta yanke shi amman tana addu,a Allah ya kawo masu mafitar alkairi baki ɗaya.
Kukan! Bebi dake fitowa da sauti a wannan karon shiya dawo da mama daga duniyar tunanin data afka, cikin sauri mama ta furta"Ciwon marar ne ya dawo?". girgiza kanta take tana kuma zubar da hawaye kamar ba Bebi ba wadda kafin kaga kukanta se antona ko ciwo take bata kuka ammam wannan karon kukan! take sosai.
"Mama jinine fa ke zubomin ga wannan tsumman sukarmin jikina yake na shiga ukuna!!!" tafaɗa tana zubar da hawaye!.
Dubanta mama tayi da nutsuwa ganin yadda taɗan faɗa yau ɗaya tabi ta ɗagawa kanta hankali, wanda ba wai iya ciwon marar kaɗai bane ya sakata yin hakan harda ma tsoro wanda ya bayyana a saman fuskarta.
"Kinga ki kwantar da hankalinki kinji ko ina anyi muku karatun jinin al'ada a makarantar islamiyya?, ko.wace mace tanayi bake ɗaya ba, sedai wadda Allah bai ƙaddara zatayi shiba yana xuwar mana ne a kowani wata wata tsakiyar wata, wata farko wata kuma karshe, watama batayi baki ɗaya wanda wannan kuma anfi danganta hakan da lalura..........., Sosai mama ta xauna tana nunawa Bebi yadda zatai tare da yadda zata gyara jikinta komai dai ta zauna ta nuna mata hartana mata misali ga su hassana wanda tsabar tashin hankali ya hana Bebi fahimta ada, sam tama manta anyi musu wannan darasin a makaranta seda nutsuwa tazo mata sannan ta kwantar da hankalinta amman dai har yanzu marar tana yi mata suka, dama kuma taga Sadiya tana ce mata wataran bata azumi dadai sauransu, sam bata ɗauka haka abin yake ba seda yazo kanta anan karatun malam hadi na islamiyya ya dawo mata kanta, wanda ya bayyana musu hukunce-hukuncen jinin haila, dai dai sauransu.
Sosai mama ta zauna ta kuma yi mata nasiha mai ratsa jiki hartana tsoratar da ita akan nisantar wani namiji sabida gudun shigar ciki, daman kuma tasan Bebi inda Allah ya tai maketa ko ƴan yaran da suke cewa suna sonta bata kulasu bare kuma ta tsaya da wani amma me yanzu baka shaidar mutum, Gwara dai ta kuma tsoratar da itan kamar yadda take haɗasu tai musu hakan tun kafin wannan lokacin yazo, sannan  kuma ta kara yi mata nasiha da kula da sallah sannan ta nuna mata dukkan abubuwan da suka halarta akanta sosai ta nuna mata jin tsoron Allah fiye da komai a rayuwa sabida littafinta yanxu a bude yake dukkan abinda tai xa,a shigar dashine.
Jikin Bebi ne yay luɓus wata irin nutsuwa tazo mata haka sukaita hirar fahimta da mama har lokaci yaja sannan tace mata ta koma  wajan ƴan uwanta ita kuma tayi kicin wajan aikin

gabanta.
Koda ta shiga ɗaki kwanciyarta tayi a saman katifa tana tsuke jikinta waje ɗaya tana jin yadda mararta take ɗan lafa mata a hankali hankali sabida karfin maganin datasha kafin kuma bacci ya kamata wanda aikin wannan maganin data sha ɗinne.

_LEGOS_
Safiyar asabar kwance yake............

_MUTARA A NEXT PAGE FANS_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*29&30*

Babu laifi Bebi ta sami bacci sosai domin se dama aka kirawo sallar magariba sannan mama tasa ihsan taje ta tasota, murza idanunta tayi tare da mikewa zaune duk jikinta yayi sanyi ƙalau haka ta tashi ta fito tsakar gida, seda ta shiga bayi ta wanke jikinta sannan tazo gaban mama saman tabarma ta zauna.
"Ke malama tashi kije ki ɗauro alwala ki gabatar da azkar ɗinki, bana son sakarci ta haka shaidanu ke shigar macen datake haila bata yawaita alwala da addu'oin tsari".
Babu musu ta mike taje ta ɗauro alwala ta wuce ɗaki sabida tsakar gidan duk su mama sun

shinfiɗa katuwar tabarma suna sallah.
Zama tayi tare da fara gabatar da karatun azkar ɗin maraice, tana kammalawa ta fito tsakar gida lokacin suma sun idar da sallar bataiwa kowa magana ba taja ta zauna tare da zuba tagumi, itafa Bebi wannan tsumman na jikinta duk shine ya dugunzuma mata hankali( wayyo! cikina dariyar bebi karki kasheni ) da kallo mama ta bita kana tace.
"Waini yau meya sami uwata ne?, naga tun ɗazu taƙi magana ya Allah ya ubangiji kasa sanadin wannan girma dayazo miki yasa sanadin samun nutsuwarki ne kamar haka".mama takai maganar ƴan biyu suka cafe da "Amin mama wallahi yau gidan sakayau".murguɗa baki tai hartana danna shi gaba"Nifa mama wannan tsumman ya ishan wallahi yarda shi zanyi na huta haba abu se soken.........",Batara ƙarasa ba mama tace.
"Kull nakuma jin kin faɗi haka wallahi kika yarda se ranki ya ɓaci dan ubanki haka zaki dinga yawo jini na ɓata miki jikinki Eye?"tafaɗa mata fuskarta a daure domin tasan halin ƴar tata da wauta zata iya yardawa ɗin.
"Nidai Allah kuwan".ta faɗa fuww ta mike tayi cikin ɗaki tana gunguni itafa ya dameta da haka wani baccin ya kuma fisgarta sabida har yanzu jikin nata bai wani yi garau ba, ko abincin dare bata ciba mama tace su barta kawai tasan halinta tana tashi tsakar dare setaci.
Suma sunayin sallar isha'i sukai cikin ɗaki sabida hadarin daya haɗo a garin koda suka shiga ɗaki hussanai  ce ta dubi mama tare da cewa.....
"Mama goben dai sedai ni inje ɗin naga ƴar taki babu lafiya?".
Tafaɗa tana kwanciya gefen hassana.
"A,a idan ta warke sesuje ai babu wani damuwa Allah dai ya nuna mana goben".
Mama ta faɗa itama tana kwanciya a gefensu hassanar abinka da jikin talaka na gajiya ko cikakken minti goma basuyi ba bacci yay awon gaba dasu.
Shahid ne kaɗai ke budurinshi a tsakar gida yana ɗan dafa indomie ɗinshi harya kammala yaci shima ya kwanta a ɗan shagonshi na soro.

_YAHAYA GUSAU_
*GIƊAƊO MAI ATAMFA ESTATE*
Cikin harabar estate ɗin motar usman take danna kanta wanda ya baiwa masu tsaron gidan damar tawowa aguje! zuwa gaban mahaukacin katon gate ɗin gidan suka budewa usman gate ɗin cikin barkwanci yake gaisawa da sojojin waɗanda sune ke tsaron gidan sannan yaja motarshi a hankali har cikin parking space, revars yayi kafin ya gyara parking ɗinshi sannan ya kashe motar tare da fitowa yana xagayawa ta baya ya ɗauko jakarshi ta office tare da kular dambu, ya dauki hanyar gate ɗinsu wanda shine daga gefe, turashi yay tare da bude kofar part ɗinshi ya shiga cikin babban falonshi bakinshi dauke da sallama.
Matarshi Zainab tana zaune a ƙasan carfet tana kallo a tv shigowarshi yasata tashi da ƙyar tana mishi barka da zuwa cike da tattali da kulawa.
Cikin wani irin salo ya jawota hade da cikin yawani rungume batare daya aje kayan hannunshi ba, seda taɗan zame tare da karbar kular dambun da jakar hannunshi ta shige gabanshi tai masa jagora zuwa ɗakinshi, yanayin yadda usman yakewa zainab dolema ya dinga baiwa Ali haushi konima nace anya.....!
Bai samu tayin wankan ba yau, illah haɗa mishi ruwan dumi datayi kaɗai sabida hankalinta na wajan dambu wanda tun a cikin  ɗakin ta soma kaishi bakinta tana yi tana lumshe ido jitake

kamar karya kare amman lomarta batafi biyar ba taji wayam babu dambun babu alamunshi.
Cikin kwaɗayin shi taja ta zauna ta rafka tagumi har seda usman ɗin ya fito ganinta babu yadda take yasaka shi saurin karasowa gabanta.
"Sweet heart what wrong with you?".
Yafaɗa yana tallafota zuwa jikinshi har yana goga mata ruwan daya rage jikinshi na wanka.
Turo bakinta tayi gaba sega hawaye nan shaaaa!!
"Ni wallahi wannan dambun bai isheni ba Allah senaci zan iya bacci, kuma bana ammi kona hajiya ba, na waɗanda naci yanzu nikeso".
Dum!Dum kirjin usman ya bada sautin tare da zamewa ya zauna.
sunayen Allah ya shiga jerowa dama haka mata masu cikin suke?.
Shi yanzu an riga anyi sallar magariba ta ina ze, iya tunkarar gidan wasu?, infact ma ta ina yasan gidan.
Marairaicewa yayi tare da cewa.
"Kiyimin hakuri Cwt gobe insha Allahu zanxo dashi mai yawa amman yanzu kinga Aliyu zanje na ɗauko a airport sannan kuma banje na gaisa da abba ba".
Tashi tayi daga wajan tana jin wani iri aranta batajin zata iya kai haƙarƙarinta gado in bata kuma kai wannan dambun bakinta ba
Agurguje ya shirya kanshi cikin manyan kaya tare dayin alwalar magariba ya fita masallaci.
Koda ya dawo ma part ɗinsu ya koma anan babban falon ammi ya sami abbansu yayi mishi barka da hanya sannan ya nemi guri ze Zauna sabida ammi ta dakatar dashi akan maganar bikin Aliyu wanda za,ai next week.
Ganin ankusa kiran sallar isha'i ga maganar taki ta kare tsabar complain ammin ke mashi akan halin ɗan uwan nashi,yasa abba katse wa ammi hanzari"Kai shehu maza ni kaje airport ka ɗaukomin babana idan yaso ka dawo kucigaba daga inda kuka tsaya".
Murmushi usman yayi tare da mikewa yana jinjina girman soyayyar abbansu da Aliyu.
Sallama yay dasu ammi kana ya koma part ɗinshi ganin yadda zainab matarshi ta hade kanta da gwiwa yay matukar girgizashi, cikin sauri ya karasa gareta yana yi mata magana kasa kasa, duk yadda yakai ga dadin bakinshi taƙi bashi haɗin kan magana itafa dambun nan dai zata kara ci.
Aranshi jaje yakewa kanshi na kaika jawa kanka amman a fili, lallaɓata yake yana kuma ce mata insha Allahu zega yadda zeyi ta samu taci ɗin da ƙyar ya samu ta saki ranta sannan ya ɗansha tea kana ya dauki keyn motarshi ganin 900:pm ta kusa kuma jirginsu Aliyu sauran mintuna kaɗan ya sauka.
Har waje ta rakashi.
Sannan ta jawo jikinta ta koma falon shikuma ya karasa parking space ya shiga motarshi.

_AYI HAƘURI A ƘARA HAƘURI A KUMA YIN HAƘURI AKAN WANDA MUKE BAKI ƊAYA ALLAH YA ƘARA MANA HAƘURI DA JUNA AMIN_

_MASU MIN MAGANA AKAN BOOKS ƊINA DANA GAMA COMPLT DOCUMENT GASU KAMAR HAKA_

*RABON WANI*

*H A S K E*

*KOBA SO*

*DA IZZATA*

*ƊAN MAJALISSA*

_DUK ƊAYA DOCUMENT AKAN FARASHIN NAIRA 300 AMMAN MAI SANSU BAKI ƊAYA ZE BIYA 1000 MAI BUKATA SEYA TUNTUBENI 08142105218_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

*Alhamdulillahi dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah buwayi gagara misali, haƙiƙa naga ruwan ƙauna a wajan masoyana, yadda naita cin karo da saƙonninku ta ko ina wasu na kirana wasu na turomin ta watsapp akan rashin jin daɗin danai na kwana biyu, nagode nagode! Allah yasaka da alkairi, HAIDARA YACE AGAI SHEKU* 😜

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*33&34*

Cikin mintunan da basu gaza ashirin ba usman ya parker Motarshi a bakin layin gidansu ƴan biyu.
Ɗan kallonshi Ali yayi tare da cewa"Malam sefa ka ɗaga ƙafafu sabida naga garin akwai hadari sosai, murmushi usman yayi tare da kallonshi.
"Ai fitowa zakai mu ƙarasa tare wallahi unguwar babu nepa nikam tsoron layin nake yacika

duhu, bazanje a sokan makami ba".
Yafaɗi hakan da iyakar gaskiyarshi, cikin zuciyar Aliyu dariyace fall tayaya usman ze daina bashi dariya a rayuwane.
"Kaga malam nifa daga nan babu wani inda zanje, to inda babuni yaya zakai? waikai kullum kamar ba namiji ba".
Yafaɗi hakan yana jan site ɗin kujera ya jingina kanshi, yana lumshe idanunshi yana jin jikinshi yay mugun gajiya sosai.
"Plsssss ɗan uwa kaiwa girman Allah mu karasa wallahi tsoron layin nakeji bazan iya shigaba, idan kuma bazaka rakani ba, mutafi kawai na hakura".
Usman yafaɗi hakan tare da haɗe hannayenshi waje ɗaya alamun roƙo.
"Wuce muje amman gaskiya ka takurani",yafaɗi hakan yana balle marufin motar ya fice.
Wata sassanyar iska ya shaƙa wadda take gab da zubo da ruwan sama.
Gaba yayi yabar usman yana wa motar key shikanshi lokacin daya shiga cikin layin yayi mamaki sosai sabida yadda sekai da gaske zakaga abinda ke gabanka seda ya fiddo da wayarshi ya kunna tourch ya haska yana ƙara mamakin manyan kwatocin dake layin, cike da zafin nama yay tsalle ya tsallake kwatar gabanshi yay gaba tare da juyowa ya haskawa usman, shima ya ƙaraso wata kwanar suka kuma shiga a ƙarƙashin direction ɗin da usman yake masa, Abakin wani ƙaramin gida usman yaja ya tsaya tare da riƙe ƙugunshi yana ayyana wanne ne gidan, domin a kwatancen da mama tayi mishi, wannan gidan ya gane shima dai dan yanada mugun kai ne da baici ace ya shigo layin nan ya gane ba.
"Kaga wai ina ne nifa nagaji ka saman a mota", yaji muryar Aliyu a saman kunnenshi.
"A,a dan Allah kada ka barni a wannan layin wallahi bazan iya fita ba", yafaɗa cikin sauri tare da fito da wayarshi ya shiga neman layin mama, cikin mintuna biyu tace mishi bara shahid ya fito seya ganshi, shagon shahid ta shiga na soro ta sanar dashi sannan ta koma gaban dambun wanda ya kusan karasawa kaɗan.
Ƙarar buɗe ƙofar da sukaji ya basu tabbacin, ainihin gidan, baki ɗayansu baki suka saki suna karewa gidan kallo shikam Aliyu tsananin mamakinsa yahanashi ma ɗauke kanshi daga wajan. Gidan dake gabansu ne ashe ma bawanda suka tsaya agaban nashi bane, sosai yake mamakin tayaya mutane zasu rayu acikin wannan ɗan ƙaramin gidan wanda ko girman store ɗinshi na aje lemo bai kaiba,sallamar ɗan matashin yaron daya bude wannan gidan shine ya dawo dashi daga duniyar tunaninshi.
"Ina yininku wai mama tace ku shigo daga ciki kafin a gama". muryar yaron ya faɗa musu cikin nutsuwa.
Ƙura mishi ido usman yayi yana ganin kamannin ƴan biyu a tare da yaron sannan yay murmushi.
"A,a jeka ce xamu ɗan tsaya anan ta karasa dare yana kumayi".
Babu musu shaheed ya koma ya sanar da mama wadda take tsaye a bakin gaushin tana firfitawa.
Ɗan tsaki Aliyu yay kaɗan tare da kallon wayarshi, ƙarfe goma da kwata lallai dare yasomayi. Tsaiwar mintuna biyar sukai a wajan kafin iska mai karfi ta soma tashi mai ƙasa-ƙasa. Hannunshi ya saka ya kare fuskarshi yana jan tsaki akai akai sabida yadda usman ya ɓata musu lokaci akan shirmensa.
Ganin garin yana kuma narkewa yasa mama ta yafo mayafinta, waje ta leƙo cikin nutsuwa ta

ƙarasa gabansu.
"Assalamu Alaikum".
Sukaji muryar babbar mace a cikin kunnuwansu.
Cikin sauri suka ɗago atare suna kallon matar wadda duhun wajan bai saka sun tantance ainihin kammaninta ba.
Cike da mutuntaka suka gaisa da mama konace suka gaisa da usman wanda ya saki fuska sosai amman shi Aliyu tunda ya amsa mata gaisuwar bai kuma cewa ƙala ba.
"Kuyi haƙuri ku shigo ciki kuɗan jira ai bai kyautu ku tsaya daga waje ba, layin namu akwai sauro ga iska".
Tafaɗa tana ƙoƙarin juyawa.
"Tom mamanmu mungode fa ƙwarai".
Usman ya faɗa tare da fusgar hannun Aliyu yay gaba.
Agarin kokarin su shiga gidan seda Aliyu ya bige ƙeya sabida tsahonshi yaywa kofar soron yawa, sannan sukai sallama suka shiga ciki.
Tabarma ta baxa musu a ƙasa suka zauna, konace usman ya zauna danshi gogan tsaye yay yana naɗe ƙafarshi ajikin garu.
Yana mamakin kankantar tsakar gidan sedai kuma akwai ainihin tsafta wadda ita ta bashi damar tsayawa domin inda baiga tsaftaba da bazai tsaya bama.
amman cikin ranshi yajawa usman tsaki yafi dubu tabbas agarin kwashe kwashen usman wallahi seya kai kanshi inda baze fitaba.
Mama ɗaki ta shiga saman siff ta saka hannu ta ɗauko babbar kular abinci sabuwa data saiwa su hassana ta tari guda biyu, ɗayar ta ɗauka sannan ta fito hannunta dauke da fitila wadda ta bawa tsakar gidan damar gauraya da haske.
Kallo ɗaya Aliyu yaywa mama yay ƙasa da kanshi sabida tsananin mamakin ganin ainihin kyau ɗan gaske a tare da ita, sosai yaji tausayinta ya kamashi mace kyakykyawa amman sedai babu wadata, sunkuyar da kanshi yay kasa yana ayyana lamarin wannan rayuwa, shima usman lokacin da haske ya bashi damar ganin fuskar mama yayi mamakin madarar kyawunta sedai rashin wadata atare da ita amman jajur mama take tabbas dole ƴan biyu suyi kyau wannan kyanta su sami wadata a tare dasu da babu abinda ze hana murjewarsu tafi ta da.
Akan kujera ta aje fitilar tare da cewa.
"Waini kam dawa nai waya acikinku ne har yanxu ban shaida ɗan nawa ba?" tafaɗa tana karasawa gaban rariya ta zuba ruwa cikin kular tana wanketa.
"Nine mama bakiga muna kama dake ba?  nifa farine wancan kwa ƙanina ne yanxu na ɗaukeshi daga airport" usman ya faɗa yana dariya, takaicine ya kama Aliyu wannan zubda mutuncin na usman har ina, amman bai ce komaiba sema wayarshi daya fiddo jin sako ya shigo, khadija ce ta turo mishi msg wai akan tana jiranshi bai shigoba tsaki yaja tare da mayar da wayar aljihunshi.
Murmushi mama tayi tare da nufar gaban gaushin da dambun ke kai tana furta"To Allah ya muku albarka baki ɗayanku".
Tare da bude murfin tukunyar tana duba dambun.
Sosai usman kewa mama labari akan yadda xainab ta rike mishi wuta akan son dambun nan yana daga zaune yana mata bayani tana amsa masa yadda ya kamata cike da kulawa gefe guda kuma tana mamakin sabo irin nashi amman kuma tana daɗa mamakin miskilancin ƙanin

nashi wanda tundaga gaisuwa bai furta komaiba dantaga ma yanayin shi kamar a takure yake da gidan nasu ma baki ɗaya.
Gefen Bebi wata mahaukaciyar yunwace ke cin cikinta domin har wani irin murɗa mata yake tun tanajin dadin barcin harta dira aguje tayo tsakar gida, jikinta sanye da ɗaurin zani se Vest ɗin data saka tun lokacin da tana ciwon marar ɗazu kanta babu ɗan kwali se kitson kalabar daya zubo mata wajan keyarta ya rufe mata fuska sabida kasancewarta bamai yawan sumar kaba. Bakin rariya taje ta ɗebi ruwa ta wanko fuskarta sam idanunta bai ga wasu mutane  a tsakar gidanba..................

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Albishirinku iyayen yara dama yaran baki ɗaya, shin ko kinsan shararriyar tashar nan ta youtube mai suna *Abdur-rahman* ta shirya tsaf domin baku gudunmawa wajan tayaku bitar karatun ƴaƴanku cikin sauƙi?, Kai dai/ kedai maza garzaya wannan shararriyar channel ɗin domin ki dannawa yaranki dansu karu da zazzaƙar ƙira'ar da *Abdur-rahma* ke gudanarwa wajan bitar karatun alkur'ani mai girma acikinta daman sauran littattafan addinin islama kada ki manta da danna *SUBSCRIBE* tare  da ƙararrawar sanarwa mungode_
https://youtu.be/PFTnz8JGFfQ

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*37&38*

Saman kwalta yahau ɗoɗar yana fafaka uban gudu, saboda zuwa wannan lokacin har ansoma yayyafi kaɗan-kaɗan ga kuma dare yayi motocin ma jefi-jefi ne suke wucewa, yana wajan kwanar ganduje, goslow ya rikesu har lokacin bai cewa Ali ci kanka ba shima kuma Aliyun bai tankashiba dama ya lafiyar kura.............
Seda aka sakesu usman ɗin ya kuma jan motar dawani irin gudu azuciye kamar ze zubar dasu sannan ya ɗago yana kunshe dariyarshi.
"Haba angon zee baban ƙarnin gobe, meyay zafi ba wuta ba? zaka nemi ka zubar damu, dan kai kanada wanda ze maka addu'a aciki".
Yafaɗi hakan cikin tsokana.
Aikuwa kamar jira usman yake yahau sababi.
"Yanzu dan tsabar baka da mutunci har ka iya fitowa kabarni a wannan bakin lungun inda ƴan sara suka sunmin illah fa?, mezaka cewa my zee kai mata asarata kome?".
Murmushi yayi yana sauke ajiyar zuciya"kagama? daman akan wannan ɗan abin kake tada jijiyoyin wuya?".
Yaja fasali tare da furzar da hucin cikin bakinshi.
"Wai nikam anya kaiko ɗan ammi ne? kai ina tantama, idan banda wauta irin taka kai baka san mata ba, baka taɓa ganinta ba daga ɗorin ɗosano ya haɗaku zakaje gidanta da wannan tsohon daren kamar kwarton daya rasa katanga..............,
Abin nakama bai tsaya a waje ba shine harda shiga gidan tare da zama kana zuba kamar famfon daya rasa maɗauri, kasan girman Allah! bada ban kajani ta ƙarfin cin tuwo ba babu abinda ze shigar dani cikin gidan mutane dan Allah ka dinga kintsa kanka wallahi wannan kwashe kwashen naka wataran seka ɗauko mana aljanu, haba kaga yanzu ka duba kagani ita kanta matar taji babu dadi da yarta ta fito ta samemu, amman kai ko ajikinka amai makon kabaro musu gidan ka fito waje a,a sema sake bajewar dakai nidai nagaya maka ka sauya halinka wallahi, kawai dan tsabar shirme zage zage damu muwani shige gidan mutane da wannan tsohon daren nikam ka cuceni wallahi ka cuceni".
Yafaɗa cikin daure fuska tamau kamar betaɓa dariya ba.
Wata shegiyar dariya usman ya saki sannan ya dubeshi.
"A,a nida gidanmu aini kuma naga wuri aiko nemata kukai baku ganni ba to kutafi can cigiyata wallahi tun tasowata bantaba ganin mace mai kirkin mamanmu ba".
"Sabida tai maka dambu, koko sabida jarabarka zaka dinga shige mata kana kalle mata ƴaƴa a sadaka?".
Yafaɗa batare daya kalli side ɗin usman ba.
"Kai kasan wannan baya tsarina inada mata kamar zee aiduk mata fankone awajena, kaine ma dai nake ganin wannan ta ɗazun taso tada maka da tsohon tuzurancika".
Wata shegiyar dariya ya saki ta rainin hankali sannan yace.
"Wa kenan? au ashe da wasu matan bayan ita mai dambun ai ban sani ba tell me plsss" yaja maganar yana haɗe hannunshi.
Haushine ya kama usman daman yasan rainin hankalin Aliyu seyay abu yay kamar bashi yay ba shariya tana ɗaya daga cikin halin sa wadda take mugun batawa usman rai ayau Aliyu ze ganka gobe ze iya nuna kamar bai taɓa ganinka ba.
Amman hakan yafi yiwa mata kodan yaga yanada farin jininsu ne oho.
"Bazaka gane abinda nike nuna maka ba harse wataran kaje ta liƙa maka wata acikin yaran

nata tunda har tana ƙirga maka su, Allah yasa abaka wannan ballagazar marar kamun kan da kunya".
Yafaɗa idanunshi rufe.
"Ban gane ba? kamar yaya kai harka zauna dasu duka kasan halin kowa?".
Murmushi yayi.
"Ko ɗaya hasalima bani da sanin gaibu wannan Allah kaɗai keda iliminshi".
yaja ajiyar zuciya ya furzar da iskar cikin bakinshi yana shakar sanyin motar.
"Amman kasan komai yana da alama, bana da tabbas ɗin rashin kamun kai agareta amman akwai karancin tarbiya da kunya".
Yafaɗi maganar kamar an fusgota.
"Akwai karancin kamun kai da kunya?"!!!
Usman ya nanata yana mamakin wannan maganar ta Aliyu, shifa baiga wani illah wajan yarinyar ba amman jibi uban ƴan sharrin nan shi harya fassarata.
"Baxaka gane ba, matar ta bani tausayi a wannan zamani a rasu a barka da waɗannan yara ai tamayi wallahi".
Usman  yafaɗa yana karya kwanar gidansu sabida harsun karaso ma.
"Seka aureta ka rike mata ƴaƴan baki ɗaya ubansu! Mtswwwwww ina familynsu sekai zarbai?".
Yafaɗa yana ɗaga kanshi sama yana kallon saman motar.
"A'uzubillahi nasan ba haramci amman ita ɗin uwace agareni yakamata ka adana waɗannan bakaken maganganun agabana domin na hango tsana acikin idanuwanka daman kai katsani mutum ai yabanu, pls ka lafa musu".
Bai tankawa usman ɗinba har suka shiga cikin gidan da taimakon masu gadin dasuka wangale musu gate ɗin.
Cike da sauri ya fice a motar baiko tsaya ɗaukar kayanshi ba usman ya bashi haushi over yadda yake wani xagewa akan waɗancan mutanan shi sam baison shigewa mutum.
Tundaga bakin kofar falon ammi ya watsar da maganganunsu domin ya dauki abun shirme dan haka ranshi sakayau ya nufi cikin main falon ammi yana yin sallama abakinshi..............

_KUYI MANAGE DA WANNAN BADAI YAWA AMMAN ZE TAYAKU HIRAR DARE_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Albishirinku iyayen yara dama yaran baki ɗaya, shin ko kinsan sharariyar tashar nan ta youtube mai suna *Abdur-rahman* ta shirya tsaf domin baku gudunmawa wajan tayaku bitar karatun yayanku cikin sauki?, Kai dai/ kedai maza garzaya wannan sharariyar channel ɗin domin ki dannawa yaranki dansu karu da zazzaƙar ƙira'ar da *Abdur-rahma* ke gudanarwa wajan bitar karatun alkur'ani mai girma acikinta daman sauran littattafan addinin islama kada ki manta da danna *SUBSCRIBE* tare da ƙararrawar sanarwa mungode_
https://youtu.be/PFTnz8JGFfQ

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*39&40*

Cikin haɗaɗɗan takunshi irin na cikakkun maza, yaywa falon ammi dirar mikiya, Ammi zaune a saman carpet tana ɓarewa Abba banana ta juyo fuskarta tana ɗauke da ƙayataccen murmushi take amsa mishi sallamar dayayi, Abba wanda yake zaune daga saman one seater idanunshi sanye cikin medical glass sabida hasken computer dake aje asaman cinyarshi yana dannawa shima ɗagowa yay tare da aje computer a gefenshi fuskarshi ɗauke da murmushi shima yana yiwa Aliyu barka da zuwa.
Cikin wata iriyar sangarta wadda tai matuƙar bani mamaki takuma ƙamar dani har na tsawon wasu daƙiƙu, naga Aliyu ya nufi gaban abba da sauri shikuma abban yajawo hannunshi ya ɗagoshi ya mannashi ajikinshi cike da tarin farin ciki yake furta "Babana sannunka da zuwa! Babana yau ka sakamu cikin damuwa tun wajan 9 muke jiranka wallahi yanzu nake ayyana zan kira wancan yaron yabimin kai( abbakar kenan yayansu wanda su abba basa faɗin sunanshi sabida karar ɗan farko ).
Zame jikinshi yayi tare da jada baya kana ya tsugunna har ƙasa, ya juya gaban ammi wadda itama fuskarta take shaƙe da ɗunbin murmushin dake nuna zallar missing ɗin ɗan nata datai na two days sannan ya soma gaisar da ita cikin ladabi, yana kuma tambayarta yaya gidan?, sosai ta sake tana amsa mishi sannan ya juya gaban abba shima ya gaisarshi tare da tambayarshi yaya ya baro chaina cikin farin ciki abban yake amsa mishi da Alhamdulillahi, yana yi yana tsokanarshi.
Zama yayi a ƙasan carper tare da tanƙwashe ƙafafunshi yana jin gwara sunyi wani lissafi da abban yanzu tunda yana available akwai order ɗin dayakeson kamfaninsu na nan zeyi, cikin

wannan watan daze kama to daman ya jima yana dakon abban bai sami ganinshi available ba kamar yau shiyasa yakeson yay amfani da damar daya samu ayanzun.
"Am abba daman zancen.......,
Bai barshi yakai ba.
"No babana kaje tukunna ka huta ai ina nan har zuwa satin daza,a ɗaura maka aure, bazan koma ba. takanas na sami wannan hutun sabida auren ka, maza tashi kaje ka huta abincinka yana falonka na sama zuwa gobe semuyi maganar Allah yayi maka albarka kaida sauran ƴan uwanka baki ɗaya".
Ƙayataccen murmushi ya sauke wanda yake bayyana tsantsar kyawunshi sannan ya mike yana kallon iyayen nashi.
"To Allah ya bamu alkairi nagode ƙwarai".
Yafaɗa yana rissunawa kaɗan sannan ya zira takalmanshi daya aje su a bakin falon tun sanda ya shigo hanyar samanshi ya nufa yana jin wata gajiya tai mashi caaa!
Abba ne ya dubi ammi cikin farin ciki yana cewa....
"Banida ra'ayin bambanci acikin ƴaƴana amman har ga Allah wannan yaron yafi kwanta min araina".
Fuskantar shi ammi tayi kana ta miko mishi bananar ya karba ya luntsumata abakinshi yana saurarantar tana cewa.
"Daman bambanta ƴaƴa aishike kawo rabuwar kai, sedai kuma zakaga akwai wanda yafi faranta maka tokoda kana jin dadin hakan seka bar abin aranka kasan ƴaƴa da kishi yanzu sekaji kai ya rabu, amman kowa yana son mai kyautata mishi ai abinda wasu iyayen basa ganewa kenan sakaga kiri kiri suna nuna bam banci acikin ƴaƴansu wanda hakan bakaramin tarwatsa kan zuri'a yake yi ba, nikaina Aliyu ya shiga raina fiye da tunani sedai ina dannewa sabida banson ƴan uwanshi suga na nuna musu bambanci a tsakaninsu, sabida yaron nan iya gwargwado yana nuna mana mahimmancin mu na iyaye kasan girman Allah ko kaɗan baison wannan aure amman yadda yaga mun dage akai tuni yabi ya hakura da ita".
Ammi takai maganar tana kuma baro wata bananar, amman a wannan karon nata bakin taiwa masauki da ita.
"Haka ne Bilkisu! Allah yayi musu albarka baki ɗayan su".
Da amin ta amsa sannan sukaci gaba da hirarsu ta fahimta ita da mijin nata wadda rabinta akan ƴaƴansu suke yinta.

Shiko Aliyu tundaga step ɗin bene yake rage kayan jikinshi sabida matukar gajiyar dayay, wadda bayajin zata barshima ya iya tsayawa cin abinci yafi bukatar ya soma gasa jikinshi da ruwan ɗumi tukunna kafin komai ya gudana.
Bakinshi dauke da sallama ya nufi cikin babban falon nashi wanda yaci gyara mai kyau har wani turare aka zuba irin na ƴan maiduguri babu abinda ke tashi cikin falon nashi se tsabar kamshi mai kashe jiki.
Mamaki yay gani ƙwan falon a kunne amman seya basar sabida, yana tunanin sister ɗinshi amina wadda take gyara mishi wajanshi ko ita ce data kammala gyaran ta manta bata kashe ƙwan falon ba, sabida amina kaɗai ya yarjewa tashigo tai masa gyara amman ƴan biyu ya hutashshesu ganinsu yake kamar babu wata uwar dazasu mashi se tsabar shirme da shiririta.
Shirt ɗin jikinshi ya ɓalle ya ajeta saman seater falon sannan ya zame trouxer ɗinshi tunda

daman yabar jacket ɗin daya ɗorota samansu acan motar usman.
Dagashi se single and boxer ya nufi hanyar bedroom ɗinshi yana ɗan miƙa kaɗan sabida mugun gajiyar dayaci karfinshi.
Hohoho! Umma ta iya ɗura, sabida ta afka khadija cikin uku bala'i!!! sabida tunda ta soma ɗura mata maganin mata masu ƙarfi tare da gyara na mussaman kasancewar gabatowar bikinsu yasa takejinta acikin wani irin feeling condition wanda kusan kullum setayi zazzaɓi mai zafi tare da ciwon mara mai ɗan karen azaba wanda bai barinta tai katabus dan hatta schoolma ta daina zuwa, kana ganinta kasan tana samun gyara mai kyau domin taɗan ciko ta goge ta murje tai fresh babu abinda yanzu khadija ke bukata kamar namiji cikin dare har kuka! take idan jarabarta ta mikarta sedai inda zata godewa Allah dayasa ita  ɗin bata fito cikin jerin mata mabiya mazaba, hasalima yawan tara maza baya cikin tsarinta tun tasowarta ita dai barta da ɗaukar kai da iyayi da yanga tare da ɗan banzan kishin tsiya mussaman akan gwarzon nata Aliyu wanda tun wajan sallar isha'i tagama hadewa cikin tsadaddun kayan kanti masu matse jiki tai ɓarin manyan turarurruka masu kama jiki, wanda ummanta ta bata abinci da abinsha ta kawo masa amatsayin nata na tarbarsa wanda cikin dabarar da umman tai mata tafaki idanun ammi harta samu damar hayewa saman nashi, wanda ita kanta tasan a tsananin dokar ammi bazata barta ta keɓance  dashi a part ɗinshi ba, shiyasa ta faki idon kowa tayo nan ɗin, tunda ta shigo taji kamshin turarensa wanda yake kame cikin kujerun falon shiya haifar mata da kasala mai zafi tare dajin wani mugun feeling!.
Tun shigowarshi idanunta yake kafe akansa wadda itan take kwance saman Threeseater tai ringine hannunta dafe da mararta ganin surar jikinshi bakaramin firgitata yayba wanda har wani zullo zuciyarta ke mata wajan angizata zuwa gareshi, lumshe idanuwanta tai tare da dirowa gadan gadan ta nufi wajanshi.
Cikin zalama ta ɗora hannunta a tsakiyar west ɗinshi take kuma tasoma murza wajan kaɗan kaɗan tana lumshe idanunta tana furzar da huci, kamar wata mahaukaciya ta ɗora kanta agadon bayanshi tana shakar kamshinsa.
Yana kokarin murɗa handle ɗin kofar yaji ɗumin hannu a kwankwasonsa cike da dakiya ya cigaba da bude kofar batare daya juyoba.
Tsananin mamakine ya kamashi lokacin dayaji kwanciyar kan mutum agadon bayanshi bai jiyoba ya zira jikinshi zuwa cikin katafaren ɗakin nashi.
Mamakine ya kasheshi lokacin dayaji anjawoshi da ƙarfi zuwa gaban kofar amman dayake namijin duniya ne ko gezau sema jin datai kamar tajawo dutse!
Kuka take a wannan karon tana murza kanta gadon bayanshi.
"Plsssss yayahhhhhhh dan Allah ka jiyoooooooo ina bukata yayaaaaaaaa"
Takai maganar da wani irin rawar murya.
"Kutumar uba! yaja wata ashar wadda bata saba fita a bakinshi ba, cike da zallar mugunta ya juyo da ita yana kare mata kallo idanunta lumshe suke ruff kamar ƴar maye,  cike da mugunta ya tureta yana watsa mata wani firgitaccen kallo amman dayake hanakalin nata yay nisa batajin kira yasa take kara ƙokarin kai kanta gareshi.
"Idan kika yarda wannan ƙazamin jikin naki ya kuma raɓar jikina wallahi!".
Bai karasaba sedai yaja ƙwafa! tare da matse yatsunshi.
"Shasha sakarar banza".
Yafaɗa yana bude kofar bathroom ɗinshi ya faɗa.

Sosai ya shiga wani irin firgici wannan wani irin masiface yarinya zatai masa fyaɗe har cikin ɗakinshi lalllai tarbiyar yanxu ta kama uban ɗakinta, to wannanma fa agidansu take inaga ƴan waje kuma se abinda hali yay.
Tabbas yanajin ze kara saka idanu akan kannenshi fiye da'da dukda yasan su basu isa sunyi ba se Allah.
Acikin matukar tashin hankali yay wanka yana aiyana rashin kamun kai na khadija, wanda lokacin daya fito bai ganta aɗakin nashi ba.
Babu yadda zeyi da mahaifanshi amman bada ban hakaba da bayajin ze iya auran khadija sabida baisan maza nawa tabi a waje ba, wata sassanyar tsanartace yaji ta ƙara tabin jikinsa da zuciyarshi baki ɗaya.
Dan haka bai sami sukunin cin abinci ba ruwa kawai yaketa ɗaɗakawa cikinsa haryay nafila ya haye saman bed yana faman serching cikin ransa.

Itako khadija wannan tsawar daya daka mata ita ta dawo da ita hayyacinta aguje ta sauka ƙasa inda Allah ya sota babu kowa a falon farko dan haka kanta tsaye part ɗinsu ta wuce, aguje umma tana mata magana amman ina kuka kawai take bathroom ta wuce taita sakarwa kanta ruwa har komai ya lafa mata sannan ta haye kan gado tai lamo kamar wata marar lafiya.

Da tsananin damuwa ya kwana har zuwa wayewar gari rannan nashi a haɗe yake tamau kamar an aiko mishi da saƙon rasuwa.................

Tunda asubar farko Bebi ta mike kanta tsaye bandaki ta nufa domin ta gyara jikinta kamar yadda mama ta koyar da ita.............

*ƘARAMARSU* ✊

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Albishirinku iyayen yara dama yaran baki ɗaya, shin ko kinsan shararriyar tashar nan ta youtube mai suna *Abdur-rahman* ta shirya tsaf domin baku gudunmawa wajan tayaku bitar karatun ƴayƴanku cikin sauƙi?, Kai dai/ kedai maza garzaya wannan shararriyar channel ɗin domin ki dannawa yaranki dansu karu da zazzaƙar ƙira'ar da *Abdur-rahma* ke gudanarwa wajan bitar karatun alkur'ani mai girma acikinta daman sauran littattafan addinin islama kada ki manta da danna *SUBSCRIBE* tare  da ƙararrawar sanarwa mungode_
https://youtu.be/PFTnz8JGFfQ

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*41&42*

Sosai ta gyara jikinta tas ta wanke ko ina sannan ta fito waje tai alwala ta shiga cikin ɗaki lokacin duk su mama suma sun tayar da sallah kasancewar ita batayi tana fashi yasa ta bude sif ɗinsu ta kaya ta dauki wanda zata saka tare da pant da tsummanta taɗan ja gefe ta shirya kanta, suna idarwa su mama suka fita waje domin haɗa sanwar dambu ita ko kwanciyarta tai tana karatun azkar ɗinta na asubahi wanda ta haddace shi daka.

Ɓangaren ALIYU rannan baƙiƙƙirin ya kwana dashi koda asubahi ma daya tashi watsa ruwa kawai yay tare da nufar masallacinsu wanda ke cikin harabar gidan.
Ana idarwa ya fito sabida yana son yay sammakon office domin akwai abubuwa masu yawa dake gabanshi.
"Hy mr man barka da asubahi' Yaji muryar usman wanda shima kusan atare suka fito daga masallacin, ɗan dakatawa yay har usman ɗin ya karaso sannan suka jera ciki sabida daman ƙa'idarsu ce duk safiya sesunje gaisar da mahaifansu.
Ahanya usman yake bashi labarin rainin hankalin da zee tai mishi domin ko daya koma jiya tare da dambun nan ya tarar tai barci koda ya tasheta seta saka masa kuka! wai damme tana baccinta mai dadi ze tada ita da ƙyar ya lallaɓata ta koma baccin batare dataci dambun nanba, amman tace yau da safe zata ɗumama taci ya saka mata a frij.
Yaƙarasa gayawa Ali yana dariya, shikam Ali murmushi kurum yay sabida damuwar dake cin ranshi daman ai shima usman ɗin ya saka kanshine amman shikam bayajin ze tsaya mace ta dinga bashi order irin haka.
Sallama sukai cikin babban falon abbansu wanda suka tarar da sauran ƴan uwansu azaune kowanne gabanshi ɗauke da medium cup wanda aka shaƙeshi da ta'tacciyar zuma mai kyau wadda suke shanta aduk wayewar asubahi wannan al'adar mahaifinsu ce tun suna ƙanana yake musu hakan kuma gashi har girmansu basu dainaba domin hatta su ya abbakar dasuke manya suma sesunzo shan zuma kullum ta Allah.
Gaisawa sukai dasu abba sannan suka gaisa da ammi da ya abbakar, usman ne ya  miƙa

hannunshi ya ɗauki zumar gaban Amina ƙanwarasu wadda take gaishesu cikin respect, shiko Aliyu mikewa yay tare da kallon usman.
"Nifa zanje nai shirin office dan Allah karka mana delay kaga motana har yau tana garage, pls ka shirya da wuri".
Da kallo ammi ta bisa.
"Kai bazaka sha zumar ba kenan ɗazuma nahau samanka yadda najera maka abincin nan haka nasaka su hassana suka kwasomin shi baka ko taba shiba".
Ɗan shafa kanshi yayi tare da kallonta kaɗan.
"Ammi banji kai komai bakina yanzu da sassafan nan, sauri nakeyi kinga yau ko morning training ma banje ba sabida nai latti".
Abbane ya cafe maganar.
"To bara a haɗa maka break seka tafi dashi office ɗin ko? ai baka tafi haka ba".
Cikin sauri usman ya amshi maganar.
"Dan Ammi kubarshi akwai masu dambu wallahi ƴan gayu kawai ma siya muci".
Hararar da Aliyu ya watsawa usman ita tasaka usman ɗin babu shiri yaja bakinshi yayi gum.
Ammi dariya abba dariya ya abbakar dariya su amina da ƴan biyu ko suna son yin dariyar amman suna tsoro.
Fuww ya wuce samanshi yabarsu anan, seda ya tafi sannan ya abbakar ya dubi usman.
"Kaima kasan wancan miskilin baze iya cin abincin waje ba tsokanace kurum irin taka".
Hirarsu suka ɗan taɓa kaɗan sannan sukaiwa iyayen nasu sallama kowanne ya nufi yin abinda ke gabanshi, ƴan biyu shirin schl amina shirin office, suma su usman nufar part ɗinsu sukai domin suyi shirin fita office.
Ammi da abba kaɗai ne a falon suna kallon labarai a tashar CNN.
Cikin kuzari da zafin nama yagama shirya kanshi cikin fari ƙal ɗin yadin tisue baƙar hular zanna tare da bakin takalmi mai rufaffan sama, se baƙin agogon rolex daya ɗaura a tsintsiyar hannunshi, fitinannun turarukanshi masu azababban ƙamshi yaywa jikinshi ɓarinsu.
Da hanzari ya ɗauki jakar laptop ɗinshi tare da tarkacen wayoyinshi, bai saka komai acikinshi ba ya kullo ƙofar bedroom ɗinshi tare da saukowa zuwa ƙasa yana zuba uban kamshi, bakaramin kyau wannan shigar tai mishiba ta ƙara masa ƙwarjini da haiba tare da tsantsar kyau irin na asalin yaren hausa fulani.
Still ya kuma samun iyayen nashi a falo hankalinsu yana kan TV sabida labaran da suke kallo na safiya.
Ƙarasawa yay gabansu tare da tsugunnawa har kasa yana gaya musu cewar xe tafi office.
Ammice ta dubeshi.
"Aliyu! wai miyasa kakeson jamin magana ne agun mutan gidannan kullum ɗauka suke ninake ɗaure maka gindi hatta mahaifinka gayanan duk sangartar dayake maka amman wataran idan idanunshi ya rufe seyace nike shagwaɓaka".
Ta numfasa sannan ta cigaba da magana.
"Jiya ka dawo daga legos amman ka gaza zuwa ka gaishe dasu yanxu ma haka fita xakai amman bazaka iya zagayen gaishe da mutan cikin gidan nan ba ko?"
Kansa yana kasa yana wasa da carfet ɗin falon da hannunshi guda, bai tankawa ammi ba kuma baya tunanin harta gama faɗan ze iya tankawa sabida baisan meze ce mata akan hakan ba.
"Ba magana ake maka ba wai babana! ɗazunnan Alhaji babba yagama yimin faɗa akan yadda

kazo bakaje ka gaishe dasu ba, kaga nifa bana son abinda ze dinga kawon matsala da ƴan uwana".
Cewar abba kenan wanda hankalinshi ke kan tvn gabanshi.
"Ayi hakuri xan gyara insha Allahu".
Yafaɗi hakan yana jin ransa na suya shifa abubuwan gidan nasu sam sun soma fitar mishi daga kanshi
Mikewa yay yana kuma yi musu sallama batare daya nufi inda ammi ke nausar dashiba.
"Daman nasan wannan shegen taurin kan nashi wallahi bazeje ɗin ba yadai faɗi hakan ne danya amsa maganar tawa, ya Allah ya Allah ya yayewa wannan yaro wannan kafiya da taurin kai amin".
Cewar ammi tana kallon abba wanda yay kamar baijita ba.
Aparking space ya tsaya suna gaisawa dasu fahad da sauran ƙannenshi waɗanda suke cousins kafin ya ɗauko wayarshi acikin aljihun wandon farin yadin jikinshi yana kokarin niman layin usman sema gashi nan ya fito cikin shigar black suite wadda tai mishi kyau babu laifi.
Batare da ɓata lokaciba usman yaywa motar key suka shige tare da nufar bakin gate.
"Ni wallahi daga yau bazan kuma dropping ɗinka ba, nagaji da wannan takurar haka kurum da aurena fitar office a wannan duku, dukun".
Usman ya faɗa yana ɗagawa masu gadi hannu lokacin yana kokarin fita daga gate ɗin gidan.
Har suka hau kwalta yanawa Ali sababi wanda shi sam baima ɗago ba bare usman yasaka ran ze tankashi sema bude datar shi dayay ya shiga face book, abinshi.

Itako Bebi babu laifi ta ɗan samu baccin da tai fashinsa jiya, muryar ihsan dake faman kiranta itace tai mata caa a dodon kunnenta ɗago idanuwanta tai waɗanda sukai jajur sukai wani irin girmaɗ sabida bacci tana makawa ihsan harara"dan ubanki ubanme zan miki dazakizo kina tashina?" bata karasa ba taji muryar mama daga tsakar gida wadda takejin yadda bebin ke zagin ihsan ɗin"Ubanki zatai miki maza tashi daga wannan baccin ga dambu ya hadu ki ɗauraye fuskarki kutafi da hussaina"..................

_Wallahi har yanzu ina zazzaɓi bana jin daɗi dan dai nai alƙawarine ma amman da bazaku samu update yauba amman gashi nayi da ƙyar Allah ya bamu lafiya amin_ 🙏

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Albishirinku iyayen yara dama yaran baki ɗaya, shin ko kinsan shararriyar tashar nan ta youtube mai suna *Abdur-rahman* ta shirya tsaf domin baku gudunmawa wajan tayaku bitar karatun ƴaƴanku cikin sauƙi?, Kai dai/ kedai maza garzaya wannan shararriyar channel ɗin domin ki dannawa yaranki dansu karu da zazzaƙar ƙira'ar da *Abdur-rahma* ke gudanarwa wajan bitar karatun alkur'ani mai girma acikinta daman sauran littattafan addinin islama kada ki manta da danna *SUBSCRIBE* tare da ƙararrawar sanarwa mungode_
https://youtu.be/PFTnz8JGFfQ

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*43&44*

Da gudu ta fito daga ɗakin zaninta a hannunta bakin nan kuwa fall da miyon bacci seda ta wankeshi sannan tayo gaban mama ta wani baje, tare da haɗe hannayenta waje guda sannan ta soma zuba magiya,"Mama dan Allah ki barni agida wallahi ni haka kurum jikina baya bani alkairi atafiyata wannan tallan, gwara na zauna nayi musu wankin kawai" tafaɗa idanunta na kaɗawa suna yin wani irin jajur.
"Eh daman haka zaki ce mana, kuma nasan muddin na barki agidan bazaki musu wankinba, illah daga ƙarshema ki gudu gidan iya, nagaji da wannan halin naki wallahi yadda ƴan uwanki basu zaunaba kema kindaina min wannan kwanciyar wallahi sekin fita".
Mama takai maganar tana mikewa daga wajan damma karta sagar mata da ƙudurinta datai niyya.
Cike da jin haushi ta mike buja-buja ta shirya kanta cikin wata doguwar rigar yadi amman mai roba-roba bakaramin muhalli rigar ta samu ajikinta ba, tsabar matsetan datai yasa bata iya ƙwaƙwƙwaran juyi ma acikinta daga sama kuwa tai mata mugun sharp wanda ya baiwa kirjinta damar yowa sama ya fito sosai, ƙaton hijabi ta ɗauka mai kalar pink har ƙasa ta saka, shima kuma irin na yadin nan ne mai shara-shara, sedai bai nuna shatin jikinta ba matsalar ɗaya sedai idan tana tafiyane ze iya bayyana komai na jikinta.
Turare ta fesa ajikinta batare datai kwalliyaba ta kama hanyar waje sabida jin kiran mama datai akan motar dasuka tsadance da ita zata dinga zuwa tana ɗaukarsu har mai motar ya karaso

anma fitar da kayan Bebin kawai ake jira.
Fuwww tai waje batako tsaya jiran hussaina ba.
Da ƙarfi taja marufin motar ta shiga tana danna baki gaba.
Seda ihsan tacewa mama ai Bebin tana mota sannan mama ta sallami hussaina da tana kicin ma tana nanatawa hussaina lissafin duk abinda suka tafi dashi daki-daki ita kuma hussainar tana gefe tana karashe cin tuwonta ɗumame na karin safe, itako daman Bebi tai kaurar zuci yau bakin cikin talle yahanata karyawa.
Bayan hussaina ta gama ta wanko hannunta taiwa kowa sallama na gidan nasu sannan ta fita.
Aiko ta tarar da Bebi kamar xata fashe  bata kulataba daman hussaina bata ragawa Bebi tuncan wannan yasa tafita a harkarta har mai motan yaja suka ɗauki hanyarsu.
Tafiyar mintuna kaɗan ya kaisu sharaɗa ƴan kamfani, kamar kullum a bakin tangamemen gate ɗin kamfanin _Alhaji idrissa mai atamfa_ motar taja ta tsaya cikin azama drivern ya taimaka musu wajan fiddo da kulolin dambun da kular alalen, sannan sukai sallama yaja motarshi yabar wajan, aiko driver yana tafiya babu yadda hussaina batai da bebi ba akan ta taimaka mata su shigar da kayan ciki amman yarinyar nan taki harseda wani security yazo ya saka baki sannan ta ɗauki robar manja ta wuce shikuma ya taimaka musu da kula ɗaya sabida yana ganin kirkin ƴan biyu yasa yay musu hakan.
Lokacin da Bebi ta saka ƙafafunta cikin shahararen kamfanin mai atamfa seda tazama ƴar ƙauye sabida yadda taga ginin glass da glass wanda aka kuma ƙawata ko'ina na kamfanin da wasu irin filawowi masu birgewa gawajan adana motoci daban kai kowanima dai sashe ( word )akwai inda xakabi ka taddashi sosai kamfanin ya ƙawatu gakuma girmanshi daya baiwa Bebi tsoro lallai waɗannan ma'mallaka wannan kamfanin akwai ruwan kuɗi duba da yadda taga ma'aikata kota ina wasu na shiga can wasu na fita banda zafafan motocin dake fake can gefe, sannan data ɗaga kanta sama kusan shidewa tai sabida yawan hawan benen ciki a ƙalla akwai kusan hawa uku, to ita inata taɓa ganin hakan indai ba'a film ba shima kuma film ɗin takan shafe shekaru bata gani ba sabida basuda kayan kallo.
Cikin jin haushi hussaina ke kiran Bebi amman madam tai nisa harseda hussaina taje tagama haɗa komai sannan Bebi tasami damar gama kallon nata ta soma karasawa can inda taga ƴar uwar tata tayi tofa ko a wajan dazasu zauna ɗinma seda bebi tabaiwa idanunta abinci sannan taja ƙafafunta, ta karasa gaban hussaina amai makon ta zauna a benchin dataga hussainar nakai, a,a seta koma can gefen wata bishiya ta zauna a saman tudun wajan tana kuma juya idanunta kallon ko ina take sosai sabida itafa ganinta take ba'a wannan duniyarba ta ɗauka awata ƙasa take wai a shirmen bebi shiyasa tace gwara ta kalli komai ta more kafin ta koma gida.
Habawa baƙin ciki kamar xe kashe hussaina har wani ruwane ya tarar mata a idanunta wannan wani irin sakarcine inda tasan hakane wallahi da gwara tazo da ihsan yanzu jiba ƴan siyan dambu sun soma zuwa ga ƴan alale tama rasa yadda zatai dasu sabida babu mai taimakonta.
Cikin ikon Allah baban nazir yazo domin su gaisa kamar kullum.
Sallama yay mata lokacin tana zubawa wani staff dambu a leda seda ta kammala sannan ta ƙarasa gabanshi ta rissuna tana gaisar dashi, cike da farin ciki yake amsa mata kafin yace.
"Ke nifa ban ganeku ina ɗayar take naga yau aikin duk yay miki yawa?".
Sunkuyar da kanta tayi ƙas sosai tana zana kasa a ƙasa sannan tace.
"Wanki mama tace tayi amman munzo da Bebi".

Ɗan jimm yay kana yace.
"Yoni ai bana rabewa daku kusan duk kamanninku guda wacece haka?".
Ya tambayeta yana ɗan waige kozega Bebin.
"Bilkisu! fa gata can"!
Ta juya ta nuno mishi bebi wadda take kallon saman benen wajan.
Sakin Baki yayi cikin mamakin ganin yadda Bebi ta girma masha Allah sannan ya soma kiranta.
"Bilkisu! Bilkisu!! yaki nan dan gidanku ƴar ƙauyen banza kina can a zaune kinbar yayarki tana aiki ita ɗaya ko".
Wani sanyi hussaina taji hartana murmushi.
Wanda adai dai wannan lokacin itakuma Bebin tazo wajan kiran nashi  sabida ta ganeshi domin tana ganinshi gidan baba.
Gabansu tazo tare da rissunawa tana gaida shi.
"Toni aike Bilkisu idan zanganki a hanya bana shaidakiba, sabida girmanki harkinfi ƴan uwanki masha Allah".
Yafaɗa yana rike haɓa, burus tai dashi bata ce komaiba harya gama mata nasiha akan tabar wajancan ta koma wajan ƴar uwarta ta taimaka mata suyi sugama sutafi gida.
Ciki-ciki ta amsa masa da "To" sabida itafa haushima ya bata amman sabida ba,a basu tarbiyar musuwa babba ba yasa ta miƙe zuwa saman benchin dataga ƴar uwar tana kai.
Zamanta yayi dai-dai da ƙarasowar usman wajan lokacin ita kuma hussaina tana gaban baban nazir yana yimata ƴan nasihohi akan hakuri da ɗan uwa kada taga bebi nayin haka taji wani abu kuruciya ce kowa da irin tasa.
"Assalamu Alaikum ƴar ƙanwata barka da safiya ya mamarmu?".
Yafaɗi hakan cikin barkwanci dukshi ya ɗauka hussaina ce ko hassana sabida lokacin tai kasa tana gyara zamanta.
Ɗago da dara-daran idanunta tai tare da zuba masa su batare sata saki fuskarta ba.
"Tsarki ya tabbata ga ubangijin halitta"!
Abinda ya fito daga cikin bakin usman kenan yayin dayay tozali da fuskar Bebi wadda tai tamau da ranta.kamar an aiko mata da sakon mama ta rasu.
Basarwa yay amman cikin ransa yay santin kyawun halittar Bebi amman santin bana soyayyaba sedai yaji yarinyar ta shiga ransa lokaci ɗaya.
"Ina ƴan uwan naki suke?"
Yafaɗa yana saita nutsuwarsa.
Amai makon ta bashi amsa setai saurin tsugunnawa.
"Ina kwana?, gata can wajan baban nazir".
Tafaɗa kanta a ƙasa still kuma tana tsugunnan.
"Kai masha Allah! rabbi ya sakawa da uwa mahaifiya da alkairi, bisa jajurcewa wajan tarbiyantar da ƴaƴanta waɗanda suka tashi cikin halin maraicin rashin bango! agidansu wato mahaifi amman hakan bai hanata jajurcewa wajan basu tarbiya ta ƙwarai ba".
Yafaɗi hakan yana numfasawa.
Lokacin hussaina ta karaso itama ta rissuna ta gaisarshi.
Cike da tsantsar farin ciki ya amsa sannan ya mayar da hankalinshi ga Bebi wadda har yanzu bata mike ba.
"Kanwata kekuma maye sunanki?".

Miƙewa tai ta zauna.
"Bilkisu"!
Wata ƴar zabura yay kaɗan.
"A,a kice mamarmu ce wallahi sunan amminmu kenan masha Allah suna mai kyau".
"Eh amman akan cemin,Bebi".
Ta bashi amsa kanta tsaye.
"Ok masha Allah nice name momynah! oh jiya kece muga gani kenan?"
Yafaɗa yana duba wayarshi "Eh"!
Tabashi amsa tana mamakin ashe daman jiya sune sukaje gidansu? wato idan ta fuskanta wannan shine mai surutun nan na tsiya! shiko ɗayan waye? sanin batada mai bata amsa yasa ta watsar da maganar tanajin yana tsokanar hussaina har yana cewa tabbas wataran dole ammi taga bebi takwararta anan yake baiwa hussaina labarin jiya ai yaje gidansu amman baigan suba.
Sosai taga suna magana da hussaina kamar sun jima har lokacin da masu siyan dambu suka zo.
"Ƙanwata zan koma office amman banyi break ba, pls ki bawa momyna ta mikomin yau masinjana bai nan, tahau sama hawan ƙarshe daga hannunta na dama ta duba room 2 nan ne office ɗina, amman yau alale zanci sabida manjan nan ya burgeni".
Yafaɗa yana dariya cikin sauri kuma ya juya yay tafiyarshi batare daya tsaya jin mai zasu ce ba. Murmushi hussaina kurum tayi aranta tana yaba kyawawan halaye irin na usman gashi dai mai kudi amman sam baida girman bare izza kullum ƙara jansu ajiki yake tamkar daman can yajima da saninsu.
Cigaba sukai da zubawa jama'a dambun wanda har Bebin taɗan saki sabida faɗanda baban nazir yay mata da kuma zuwan usman wanda hussaina taga Bebi tai na'am sosai da usman ɗin.
Ƙarfe ɗaya da rabin rana suka dakata da cinikin  famfon dake can baya hussaina ta nufa tayo alwala kamar kullum akan wani ɗan dakali ta shinfiɗa dardumar dasuke zuwa da ita ta soma yin sallah, itako Bebi da wannan damar ta sami ƙaton flate ta shaƙe da dambu harda pure water sabida azabar yunwar datake ji, ganin babu yawan mutane a wajan duk suna masallaci suna sallah yasa ta ɗorashi a saman cinyarta tahauci hannu baka hannu ƙwarya.
Tana gab dagama ci, Shikuma Aliyu ya dawo daga masallaci saboda duk hanyar ɗayace kusan a haɗe sedai kwanonin da suka rabu wanda yabaiwa kowani ɓangare damar nufar hanyarshi, Tundaga Nesa yake kallon duk abinda yarinyar takeyi sosai yake mamakin yarinyar mace budurwa ta zauna a center jama'a tana kai abinci cikinta, seda yakusan shiga corridow ɗin daze kaishi word ɗinsu yagane masu dambun nan ne da usman ke santi, to tayaya tsafta ta samu anan wanda harze saka yay gangancin kai dambun cikin bakinshi, Baiga fuskar yarinyar ba amman ya shaida hijabinta, harya karasa office ɗinshi mamakin wannan al'adar yarinyar yake wadda tsananin rashin kamun kanta ya bashi mamaki domin babu kamunkai ga maicin abu a hanya,Watsar da zancen yayi sabida tarin aikin dake ganshi wani file ya ɗauko wanda ya saka dole seyaje office ɗin usman yay masa bayaninshi kafin ya saka hannu kasancewar kwana biyu bai nan shi.
Tashi yayi da ganshi batare daya nemi sakatarenshi ba, domin daman shi ba komai yake zama seyay aike ba, kasamcewarshi mutum mai zafin nama yasa baya zama kusan dakanshi yake gabatar da komai.

Fita yayi zuwa office ɗin usman anan ya sami usman ɗin suna waya da zee seda ya gama sannan ya nemi waje usman ɗin ya soma yi mishi bayani kan file ɗin wanda harya shafe lokuta wajan usman ɗin.

Riƙe haɓa hussaina tayi tare da kallon Bebi, "Malama wayace ki zuba dambu?".
Ta jefa mata tambayar cike dajin haushi.
"Babu wanda yacemin na zuba nice nai niyya sabida motama bata tashi seda mai bareni kuma ƴar adam".
"Ai shikenan shegiya jaka ko kunya bakyaji ki xauna kina cin abu a bainan nasi sabida kawai kija wani yace bamuda tarbiya mtswwwwwww!".
Tafaɗa cikin jin haushi sannan ta  nemi gu ta zauna.
"Duk wanda yay min wannan kallon yaje can dayawarshi haka kurum yunwa zata halakamin hanjina kurum senai sanya kema kinsan babu amana a tsakanina nida yunwa".
Miƙewa hussaina tayi ta soma zuba alalen a wani ɗan madaidaicin flate mai ƙaras, yaji ta zuba agefe tare da wadataccen manja.
"Ai sekiyi Bebi, ni banida lokacin shirmenki mike kibi waccan hanyar zakiga step ɗin bene kibishi sosai zakiga hanyoyi sun raba akwai lifter daga hannun dama babu ruwana idan kikai gangancin shiga kika maƙale danta manyan wajan nan ce kaɗai".
Tafaɗa tana nuna mata hanyar
"Idan kika hau saman benen sosai ze kaiki har inda yay mana kwatance ɗazu inma baki gane ba ki tambaya ko a reception ne".
Tafaɗa tana miƙo mata flate ɗin data rufe mata shi.
"Nidai kawai ke kije mana seni nifa bazan gane ba".
"Aidaman baxaki gane ba, sabida bakya gane komai ke! seci dan haka wallahi sekin ɗauka kinkai konaci ubanki".
Hussaina tafaɗa cikin daure fuska wadda tasaka Bebi ɗaukar alalen sabida tasan halin tijarar hussaina wataran daman batada daɗin sha'ani.
Ɗauka tayi ta  riƙe da hannu biyu ko kallon ƴar uwar batai ba ta soma tafiya seda tai nisa hussaina tai dariya "Ja'ira aike zuma ce naga seda wuta" tafaɗa tana cigaba dayin cinikin kafin Bebin ta dawo.
Tsorata bebi tayi da yadda taga tanata ratsa hanyoyi konace ƙofofin glass manya kafin ta hango step ɗin daga can gefe yawani raba hanya baki ɗayanshi yaji wani irin tiles kamar ruwa ga wani abu nan wanda shitake tunanin koshine lifter ɗinma.
Hanyar step ɗin tabi ta hau saman benen sosai take nishi sabida tafiyar tai mata yawa, da taimakon masu tsaron ƙofofin wajan ta kai har babban reception ɗin saman kafin ta kuma miƙar hannun daman dayace mata ɗazu dayana mata kwatance.
Ita sam bataga wani office ba se guda ɗaya jall, cikin hanzari taga wani mutum kamar security ya taso daga saman wani chair zuwa gabanta.
"Hy meya zo dake nan ko baki san dokar wajan nan ba?"
Murguɗa baki tayi.
"Toni ina ruwana dawani dokarku,ni gafara na wuce ogan naku dakanshi ne yace na kawo mishi abinci".
Tafaɗa tana tureshi.

"Ke! Ke!! Ke!!!".
Yake faman faɗa bayan yabi bayanta amman ina Bebi bata jiyowa ba sabida harta kai ga buɗe ƙofar ma tuni ta kutsa kanta.
Shiko sakataren Aliyu mamakine ya kamasa yasan badai Yallaɓai bane zece da wannan tsagerar yarinyar ta kawo mishi abinci ba.
Yasan halin ogan nasu da kamewa baya tunanin yanada lokacin ma kula wasu matan a waje bare wannan, kuma tunda yake dashi baitaɓa siyan abincin waje ba, soyake yay mata bayani ko wajan oga usman tazo seyay mata direction ɗin office ɗinshi tunda nan site ɗin office ɗin MD ne kaɗai a wajan wato Aliyu, wanda yake da comfirm ɗin bashi da yawan surutunma daze jawo wannan mara kunyar wajanshi, komawa kawai yay ya xauna yana mamakin jimawarta bata fitoba tunda yaga ogan bai nan yana son yaje ya fito da ita yana kuma tsoron karyaje koshi ɗinne dai ya ce takai masan tunda yaga yarinyar mai kyau ce, duk da yasan ogan nasu kula mata baya cikin tsarinsa dan kullum lina da kuka take fitowa daga office ɗinshi idan ta shiga to yanzuma ya hana shi barin lina wucewa bare ta shigar mashi office.
Zuwan Aliyu wajan shiya dawo da sakataren daga dogon tunanin daya faɗa.
"A,a bala yada wannan nazari haka?" yafaɗa yayin dayake kokarin kai kanshi bakin ƙofar office ɗin nashi wadda inda bebi ta lura zataga an rubuta MD ALIYU IDRISS MAI'ATAMFA! a saman kofar, amman sauri da tsautsayi bai barta ta fahimta ba.
"Yallaɓai amman akwai bakuwa fa aciki".
Yafaɗa yana sada kanshi a ƙasa.
"Bance kada ka kuma bari wannan yarinyar ta shigarmin office ba"! ya faɗa ranshi a matukar ɓace.
Sosa kanshi yay tare da rissunawa.
"A,a ba ita bace wannan wata marar kunyace babu yadda banyi da ita akan kada ta shigaba amman kamar zata zagen ta wuce".
Yafaɗa muryarshi tai kasa sosai.
"Kai miya xaunar dakai anan miye amafani office ɗinka na farko kafin a shiga nawa inda kana zaune wata ƙazamar bazatai gigin shigar min office ba, Bala! wannan yaxama first and last dazaka kuma barin wata ta shigar min office with out my permission"!!
yafaɗa yana wucewa daga wajan fuwwww! yakai bakin kofar ya murda handle ya shiga cikin katafaren office ɗin nashi.
Akan desk ya aje tarin takaddun hannunshi tare da file ɗin daya fita dashi, ƙoƙarin nufar special room ɗinshi na ciki yake wanda yake hutawa acikinsa, idan ya gaji, wanda kuma yay dai-dai da lokacin da Bebi ta gaji da tsaiwar jira ta ɗago ƙafafunta zata fita sabida tun zuwanta tana tsaye a bakin frij ta kafe duk tunaninta ko wani uzurinne ya hana usman fitowa shiyasa ta dakata sabida karta koma hussaina ta balbaleta tace mata batada hakurin jira.
Duk sanyin Ac ya gama kashe mata jikinta gefe ɗaya kuma tsananin santin kyan office ɗin take wanda taga tarin computer's kamar me a zube a saman desk kai haɗuwar office ɗin kaɗai ta shagalar da itane harta kasa yunƙurin fita akan kari.wanda hakan ya hanata jin bude kofar tashi, ɗago idanunta, tai waɗanda take kokarin kaisu ga ƙofa sedai mugun ganin datai yasa jikinta yahau rawa harma da mazari.
Cakk! ta tsaya ganinshi tsaye hannunshi aje bisa kan wata system yana kokarin ɗauka xe wuce cikin wannan special room ɗin, hannunta rawa yake wanda ya bata damar sakin flate ɗin dake

hannunta jin ƙarar dayay yasashi ɗagowa shima karaf ya sauke idanunshi akanta, kafin kuma tallatsin manjan ya sami damar fallatsa har zuwa saman wandon farin yadin jikinshi.
Cike da wani irin mugun tsoronsa wanda ya kusan sakata suman wucin gadi tai ƙasa da kanta sam baxata iya jurar wannan kallon ƙasƙancin dayake mata ba, tabbas! ta shaidashi wannan shine wannan na jiyan daya bata tsoro ɗan uwan wannan mai kirkin sabida tanada rike abu wannan dalilin yasa bata manta shiba dukda bata da tabbacin kamanninshi amman dai ta shaidashi shine dai!.
Wani irin kallo yake aika mata dashi wanda duk yadda naso na haskoshi nakasa fahimta.
Kafin ya aje system ɗin hannunshi  bisa desk ɗin.
Takowa yake zuwa gabanta idanunshi  bisa kanta inda ita kuma take ƙara yin ƙasa da kanta tana kuma jada baya, jikinta yana rawa kamar xata shiɗe, seda takai ƙarshen bangon wajan sannan ta dakata jikinta yana kuma kaɗawa kamar kirjinta ze fito ya faso wani irin mugun fitsarine taji ya kunno mata kamar ze zubo mata tsabar tsoronsa ya saka numfashinta sauka da sauri da sauri, a iya tashinta zata iya cewa bata taɓa ganin  mahalukin dataji tana mugun tsoronsa kamar wannan bawan Allahn ba wanda tun daren jiya data ganshi taji batada sukuni gashi yau ma tsautsayi ya kawota har inda yake.
Saukar hannunshi a gefen hijabinta yasa tai wani irin juyi tare da ɗago da fuskarta ta sauke. akan tashi kallo ɗaya tai mishi tai ƙasa da kanta sabida yadda ta hango tashin hankali da rashin mutunci acikin fuskar tashi,  rannan nashi a haɗe yake tamau babu alamun sassauci, hannunshi ya kange a gefe da gefenta inda gabaki ɗaya yay mata wani irin rumfa da jikinsa, jitai duk ya cika office ɗin tsananin kamshin mayen turarenshi shiya kuma haifa mata da jin wani iri adukkan ilahirin jikinta.
"Bakida kunya ko?".
Yafaɗa cikin wani irin murya can cikin maƙoshinsa wanda bada ban tsananin kusancin dasukai ba da baxata taɓajin abinda yace mata ba.
Sabida yadda sauran kaɗan ya rungumeta, mamakin wannan iskancin nashi take yawani xo yay mata wannan rumfar sekace ya sami ƴar iska amman tsoronshi ya hanata tanka mishi.
Ɗago idanunta tai sega hawaye shaaaaa!!
Duk jitai ta shiga matsi wannan shine farkon kusancinta da ɗa namiji a rayuwarta, Rintse idanunta tai wanda ya bashi damar kare mata kallo musamman lashish ɗin, daya kwanto saman idanunta, matso da fuskarshi yayi gab da ta'ta har yana fesa mata ɗumin numfashinsa wanda yake ɗauke da wani irin mayen kamshi na musamman.
Ajiyar zuciya ta sauke mai ƙarfi jikinta ya kara rawa fiye dana da, wani irin ɗaurewar mara taji wadda take gab da sakin xawo aranta tana dana sani tafi cikin kwando wannan horon nashi yafi duka zafi!
"Waya baki izinin shigomin office? ko nan ma wajan rashin ɗa'a ne"!! taji saukar muryarshi acikin kunnenta ƙoƙarin zamewa takeyi tai ƙasa amman yaƙi  bata damar aiwatar da hakan, sema kurawa kirjinta idanu dayay yana kallon yadda yake fat! fat!! alamun takai ƙololuwar ƙarshen jin tsoronsa.
Murmushin geben baki yay yana kuma hukuntata da idanunsa kafin ya kuma cewa.
"Nisa'anki ne banson nai maimaicin magana wallahi maganata ta biyu bara tai miki dadɗi ba".
Cikin rawar murya wadda take rarrabewa.
"Dan...dan...Allah....kai....kai...ha...ha..ƙu..ri..".

Tafaɗa tana janyo numfashinta  wanda takejin ya gauraye danashi, zuwa lokacin kukanta ya soma fitowa fili.
Nikaina mai rubutun nayi mamakin kukan bebi mai taurin zuciya amman takewa kallon Aliyu kaɗai kuka! wanda ko ciwo take bata masa kuka amman yau iya kallon Aliyu kaɗai ya ɗaga mata hankali lallai Ali mazan fama ne!
"Nibance kimin kuka ba malama tambayarki nike maye ya shigo dake office ɗina, har ana miki magana a waje kikai rashin kunya ko?"
Yafaɗa yana ɗan jada baya kaɗan yana kuma kallon yadda take faman sheko hawaye kamar famfo.
"Kayi haƙuri wannan farinne yace na kawo mishi alale".
Ya fahimce ta tsaff amman seya basar.
"Ai office ɗin baƙin kikazo ko baki kula ba, to danma ke sakarai ce tayaya baki san waje ba zaki shigo kanki tsaye agarinku na marasa kan gado ake haka? keba mace bace koko haka kikaga mata na shiga wajan namiji kansu tsaye?".
Yafaɗa yana matsawa daga inda take sosai ya basu tazara yana kallon yadda taki ɗago idonta.
"Ɗago ki dubeni shashasha wannan yazama karo na karshe dazan kara ganin wannan jar fuskartaki anan arean"!!
Saurin ɗagowa tai sekuma tai saurin mayar da kanta sabida ganin yadda ya zaro mata manyan idanunshi duka waje waɗanda suka kusan sumarta.
kafin taga ya juya bayanshi cike da zafin nama yabar wajan ya shiga ɗayan ƙofar wanda hakan ya bata damar tattare rigarta ta bawa wondonta iska aguje ta fita daga office ɗin tana haki, hamdala tai ganin bataga wannan na ɗazun ba, seda ta sauka ƙasa sannan ta sami wata kwana ta zauna dabar tana mayar da numfashi mai haɗe da hawaye da majina sabida takai kololuwar tsorata.......................

_karkusa ran ganin wani anjima gaya nan har na dare_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Assalamu Alaikum my fans saƙon godiya marasa adadi gareku haƙiƙa naji daɗin yadda kuke nuna min ƙauna kuma alhamdulillahi jikina ya samu sauƙi masu kirana da masu ajemin msg ta inbox ina godiya Allah ya bamu lafiya da abinda lafiya zataci amin summa amin ONE LOVE_

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*45&46*

Jikinta har rawa yake sabida tsorata a iya tasowarta bata taɓa ganin wanda take mugun jin tsoro kamar shiba, sassanyar iskar dake kaɗawa awajan ga kuma gajiyar gudun datayi daga saman benen zuwa nan da kuma kukan! datayi shiya bata damar jin wani shegen bacci wanda batai tsammaninshi ba kuma daman jiya batawani samu baccin kirki ba, uwa uba kuma yadda tacika cikinta da dambu kunsan mai hali bai fasa halinshi, daman ita tun fil'azal idan ta ƙoshi tofa seta matse takejin daɗi wannan dalilin yasa kallo ɗaya zakayi ma Bebi kaɗauka daga gidan manyan mutane ta fito sabida fatarta kalar hutuce sabida babu laifi tana bawa jikinta haƙƙinshi, daɗi kuma da jikin nata bamai son wahala bane ba.
Domin aiki kaɗan zatai jikinta yahau ciwo,Waigawa tayi gabas yamma kudu arewa taga babu kowa wajan wannan dalilin ne ya bata damar tube hijabin jikinta ta shinfiɗa a wajan tare dayin kwanciyarta sam tama manta dawani zancen alalen usman data ɓarar a office ɗin yallaɓai ALI! Cikin mintunan da bazasu haura biyarba bacci mai daɗi ya sureta wanda iskar dake kaɗawa awajan itace takuma bata goyon bayan sake bajewa ranta fes take sharar barcinta babu sanya.

Daga cikin kamfani ko, tun hussaina tana ƙirga lokuta hartazo tana ƙirga awanni lokacin da wani staff yazo siyan alale takuma tambayarshi don Allah karfe nawa?Cemata yay karfe biyun rana da rabi, Cikin fargaba tagama zuba masa alalen wanda inda staff ɗinma ze kula tofa dase yaga hannu hussaina yana rawa sabida lokacin ilahirin jikintama rawa yake sabida kaɗuwar jin shurun Bebi datayi.
Bayan wannan staff ɗin mutum ukune sukazo siyan dambu babu ya ƙare dan haka alalen dayay saura suka siye sabida shi daman na rabin kwano mama keyi domin anfison dambu awajan fiye dashi.
Hannunta ta wanke tare da haɗe kulolinsu, waje ɗaya sabida tasan duk inda drivern dake kaisu ya ɗauko su gida yake yana hanya domin bai wuce ƙarfe ukun yamma kamar yadda mama ta gaya musu baki ɗaya tace koda abincin bai kareba kawai idan uku tayi suyo gida domin yanayin garin yadda yake, idan yaso sesu cinye abinsu da daddare to barema kuma cikin hukuncin Allah tunda suka soma bai taɓa kwantai ba.
Hasalima duk inda biyun rana tai zuwa da rabi sedai kaji ana cigiya domin abin kamar wawarsa ake Allah ya saka musu nasibi acikin sana'ar tasu, _daman munsan shi Allah haka yake Arrahamar-Rahimin neshi mai rahama maijin ƙai ga kowani bawansa dan haka komai na rayuwarmu idan muka miƙa masa toshi ɗin yasan yadda zeyi damu domin shine mahalicci ma'mallaki wanda babu kamarshi tsarki ya tabbata agareka ya ubangijin halitta Allah muna

godiya agareka_   Bayan tagama haɗe komansu waje ɗaya sintiri tahauyi a tsakanin hanyar word ɗin da office ɗinsu usman yake dakuma hanyar wajan da kulolin su suke ganin time yana ja yasa ta leƙa har wajan masallaci wajan da provision store ɗinsu yake amman still babu Bebi babu alamunta.
Sosai hankalinta ya tashi zuwa lokacin babu tunanin ma dabai zo cikin brain ɗinta ba.
Hawaye ta soma wani nabin wani tayi data sanin zuwa da Bebi yafi cikin kwando ganin babu wani alamun Bebi wajan yasa ta nemi guri adai dai saitin step ɗin Benen ta zauna ta rafka tagumi tana kuka kan jiki kan ƙarfi kuɗin cinikinta yana hannunta tanajin komai ya fice mata akanta takai lokuta masu tsaho awajan tana kuka har fuskarta tai jajur abinka ga farar fata.
Shiko Ali yana nufar cikin special room ɗinshi direct madai daicin toilet ɗin ciki ya shiga ya sami sabulu mai kyau ya wanke ƙafar wandonshi aranshi yana raya irin haukan yarinyar tare da giggiwarta sedai akwai ɗan banzan tsoro, tsaf ya gane ƴar gidan mai dambun jiyace marar kunyar nan dasuka gani jiya, fitowa yay yana yarfe wajan da man ya ɓata mishi, gefe ɗaya hannunshi namasa masifar zugin rashin sabo da wankin, ya jima yana yarfe wajan kafin ya gama shan iska, da kanshi ya fito zuwa wajan data ɓata ya sami mopar ya goge wajan ya ɗauke fasashshen plate ɗin ya zuba a tousbin, sannan ya koma ya cigaba da aikin dake gaban shi na tarin takaddun daya shigo dasu ɗazu daya zube akan desk.
Sakataren shi daya aika tun ɗazu garage shike faman danna nocking alamun, yana niman izinin shigowa.
Ɗago da kanshi yay a miskilance tare da cewa.
" Yes! Come in".
Sannan ya cigaba da aikin dake gabanshi.
Cikin ladabi tare da nutsuwa wadda duk wanda ze raɓeshi tofa koda baya dasu seya arosu dan Ali mutum ne wanda baya shiri da mutum mai baragada ko rashin nutsuwa, Sakataren yay sallama daga ɗan nesa dashi ya rissuna tare da miƙo masa keyn hannunshi.
"Yallaɓai an kammala gyaran yanzu haka motar tana can wajan adana motoci".
Fuskarshi kamar koda yaushe kadaran kada hakan ya ɗan dubi sakataren tare da cewa.
"Ok thanks, ajemin nan".
Yafaɗa yana cigaba da rubutunshi.
Ɗan sosa kanshi yayi sannan ya kuma cewa.
"Yallaɓai madam lina tana reciption tace wai don Allah tana son ganinka to........",
"Stop!".ya buga mashi tsawar data saka nakusan yarda birona cikin ɗan zafin rai kaɗan yace.
"Mena gaya maka? nace kada ku kuma barin wata mace ta shigomin office ko? duk abinda zasu ce su gaya maka tun a office ɗinka na falo kada ka kuskura wata ta kuma shigomin nan dafatan kaji abinda nace?".
Yafaɗawa sakataren yana zaro masa fitinannun idanunshi masu girman da kyau.
Rintse idanu sakataren yay kana ya soma bashi hakuri in full respecting, bai sami zarafin magana ba illah hannu kawai daya ɗaga mishi domin wannan maganar dayake harya soma haddasa mishi ciwon kai mai zafin gaske.
Cikin sauri sakataren ya fita inda shikuma ya koma baya ya lafe yana dafe kanshi.
Wannan rayuwa tana bashi tsoro ta yadda wasu matan ke tallan kansu wa mazan waje, waɗanda wasu tsantsar so kan saka suyi hakan wasu ko tsabar son kuɗin jaraba ne ke saka su yin hakan.

Cikin haka usman ya turo ƙofar ya shigo inda bada ban sallamar dayay ba da Alin bazeji shiba sabida zurfin tunanin daya faɗa na lamarin wannan rayuwa da wasu matan suka jefa kansu irinsu lina masu tallar kansu wa mazan waje dan parsonal issue nasu.
"Man yane na ganka haka lafiya ko tunanin dije ake ne?"
Yafaɗawa Alin haka yana dafe saman desk ɗin da Alin ke rubutu akanshi.
Bai tanka mishi ba sema aikinshi daya cigaba.
"Kai bakajin yunwa?"
Ya kuma jefawa Alin tambaya?.
Se a sannan ya ɗago kanshi yana kallon usman da idanunshi dasukai ja kaɗan.
"Banjin yunwa nasha coffee, halan ƙureni kazoyi?".
Yafaɗa muryarshi aɗan kausashe amman kaɗan.
"okey nima tun ɗazu nacewa waccan ƙanwar tawa ta, kawomin alale amman najisu shuru kuma nama leƙa naga bangansu ba duka ƙilan ko sun mantane dan nagama kamar sun haɗe kayansu".
Yafaɗa yana wucewa gaban frij ɗin dake office ɗin Alin tare da budewa ya ɗauko molt guda ɗaya ya balle saman ya soma sha batare daya zauna ba yace.
"Zan koma office sabida xanyi sending cash ɗinnan da mukai maganar da abba na waɗancan ƴan kasuwan, yaufa inaga baxanyi off da wuriba yaya zamuyi da tafiyar kenan?".
Yafaɗa yana ƙoƙarin kai kanshi ga waje.
"No karka wani damu ai nasa an kawon mota ta, ni ina sallah ma zan wuce gida wallahi duk jikina ciwo yakemin".
Aliyun ya faɗa tare da ɗan juya idanunshi kaɗan.
"Aikam gajiya yanzu ka somata malam domin nan da kwana uku mun soma shagali kaga ango ina yaga ta zama" usman ya faɗa aguje yabar office ɗin sabida yasan yay tsokana.
Shiko Ali murmushin da baida ma'ana a wajena yay kana ya miƙe jin ana kiran sallah.
Alwala ya ɗauro acikin toilet ɗinshi kana ya fito, hularshi ya ɗora a saman kanshi tare da haɗe system ɗinshi cikin jaka tare da key da phone's ɗinshi kiran masinjanshi yay in few minutes ya shigo bayan ya rissuna agabanshi sannan yace "Yallaɓai gani", umartarshi yay akan ya kai mishi tarkacen shi mota haɗi da miƙa mishi keyn motar sannan shima yay abinda ze sannan ya fita waje hannun rigarshi a tattare alamun a wajan alwala ya tattareshi, kwantaccen gashin dake gefen fuskarshi ( saje ) duk ya jiƙe da ruwa yay wani irin luff hakama na hannunshi duka ya jiƙa da  ruwa cikin sauri yake tafiya akan ƙafafunshi ko ina yay staff suna zubewa suna gaisar dashi cikin ladabi da ban girma.
Lipter ya hau wadda ta taimaka mishi zuwa ƙasan benen hawa na ƙarshe sannan ya sauka ya taka da ƙafafunshi har zuwa ƙasan daga bakin step yaga matashiyar budurwa zaune ta cusa kai tsakanin cinyarta tana kuka! domin ga sautin kukan! yana fita a fili.
Harya yi gaba sekuma ya duba agogon rolex ɗin dake ɗaure a tsintsiyar hannunshi, ganin da sauran wajan 30 minutes kafin a tayar da sallah dan haka yaja ya tsaya cikin nutsuwa ya ƙaraso gaban ta.
Ƙamshin mayen turarenshi shine ya baiwa hussaina damar ɗagowa da sauri tare da saka hannu ta share hawayen dake zubo mata.
Binta da kallo yay na ɗan wani lokaci yana noticing ɗinta sannan yay mata sallama.
Acikin ƙasan maƙoshinsa kamar anyi mishi dole fuskarshi babu alamun dariya bare sassauci

yake kallonta kafin ya fara jefa mata tambaya akan kukan datake a ƙasan ransa yana mamakin ƙarancin shekarunta.
"Ƙanwata ce mukazo tare tunda na aiketa ta kaiwa yaya usman alale har yanzu ban ganta ba, kuma na koma gida nasan mamammu faɗa zatamin". ta ƙarasa maganar tana sakin kuka!sabida haka kurum taji mutumin yay mata wani irin ƙwarjini a idonta taji tana ganin ƙimarshi da girman shi infact ranta ya aminta dashi sabida nutsuwarsa tare da tsantsar kamala da kamun kansa datagani acikin tsakiyar idanunshi, wanda kallo ɗaya tai mishi ta iya ɗauke idonta sabida tsabar ƙwarjininshi.
Tsaff yagama gano komai kasancewar sa  mai saurin ɗaukar abu aranshi, amman yay mamakin ina yarinyar nan tayi wadda yake da comfarming ta fito daga office ɗinsa tuni to ina tayi? yafaɗa aranshi.
Amman afili seya dubeta yana jin ransa yana taɓuwa da kukan nata................!

_Alƙwari na cika sabida nace zan baku na dare amman ban so na tsaya ananba dan dai karkuji shurune_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Wannan shafin na sadaukar dashi ga duk wani ɗan team Bebi da Ali, da kuma masoyana kuyi yadda kukeso dashi kai sekunga damar bawa ma wanda kuke so musamman ƴan comment box ɗin auren bare_ 💃

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*47&48*

Cikin mamakin yadda tace ƙanwarta ce waccan ɗin yake dubanta tsaf yaga basa wani kama idan bata jini ba, sannan kuma yaga hussaina ƴar ƙarama ba kamar waccan marar kan gadon ba.
"Ok to kije gida mana ko ƙila tayi gaba tabarki sekima mamar bayani tunda ita bataji".
Ya fusgo maganar  kamar an tilassa mishi dole yayita.
Hussaina ƙasa tayi da kanta sosai kamar maijin sanyi sabida yadda ƙwarjininshi ke ƙara ratsa mata jikinta sannan ta soma magana a sanyaye.
"Ai faɗa zatamin akanme na barta wallahi ni tsoron mama nakeji, yanzuma nasan duk inda take hankalinta yana kammu sabida tace kada mu wuce ƙarfe uku koda bamu siyar duka ba, to muyo gida".
Tunda ta fara maganar yake kallonta amman tacan ƙasan ido irin kallon nan wanda kaida akewa shi bazaka fahimta ba seshi wanda yake makan ne ze gama kallonka tsaf.
Haka kawai yaji ta bashi tausayi ganin yadda take  kuka! yana son yaga mutum mai son nashi, uwa uba kuma yadda yaga ta firgita da tsoron faɗan mahaifiyarsu tabbas! yaji tausayi mai girma aranshi.
"Jirani anan zanyi sallah ina zuwa karki damu".
Yafaɗa batare daya jira cewarta ba sabida jin ana ƙoƙarin tayar da sallah wanda yawanci shike jagorantar limancin amman yau ya makara ta dalilinta cike da wani irin sauri kamar ze tashi sama yake tafiya harya samu damar ƙarasawa cikin masallacin yahau sahu shima yabi jam'in sallar.
Bayan sun idar addu'oinshi yay kamar yadda ya saba sannan ya fito sabida hankalinshi dayay gida yana sauri sabida wannan lissafin daza suyi shida abbansu gudun yawan gaisuwar staff ɗinsu yasa yabi ta ƙofar bayan masallacin.
Cikin wani mugun shorck yay saurin jan birki tare da goya hannunshi a gadon bayanshi.
Jada baya yay tare da tsugunnon dabai shirya ba.
Gurfane yake agabanta wadda take kwance tana baccinta ranta fess har wani munsharin daɗin iskar wajan takeyi.
"Innalillahi wa'inna ilahirraju'un"!!! kalmar data fito a bakinshi kenan yawun bakinshi ya ƙafe ƙaff babu alamun danshi cikin bakinshi tsananin firgici da mamakine suka rifushe, wanda seda yayta ambaton sunan Allah sannan ya dawo dai dai.
Wannan waccen irin hatsabibiyar yarinyace? ya jima baiga sakarai irinta ba gabas yamma gudu arewa ya duba akwai ciyayi wajan bata gudun wani mugun ƙwaron bata gudun ɓata gari? tunda ko ina akwai nagari akwai mugu.
Watsar da wannan tunanin yay yana aiyana ballagazancin ta.
Wani irin shu'umin kallo yake aika mata dashi wanda nakasa ganeshi sabida yadda ranshi ke a haɗe tamau.
Ilahirin rabin kirjinta yana waje baccinta take babu alamun damuwa tsira mata manyan idanunshi yay yana kallonta a wannan karon ya mata kallon tsaf ya kuma fahimci ƙarancin shekarunta, wadda ko sa'ar ƴan biyun ammi bata kai ba, wato wannan ita ake kira da girma ya riga hankali, miƙewa yay ya taka zuwa gaban famfon da ake ɗiban ruwa akai cikin toilet ɗin masallaci  hannunshi ya tara ya ɗebi ruwan cike da zallar mugunta ya nufo inda take kwancen wadda alamu suka nuna ma bata san da wanzuwarshi a wajan ba, zube matashi yay tass asaman fuskarta tare da ƙara tsugunnon agabanta yana kallon yadda ta zabura tana wata iriyar

miƙa wadda sauran kaɗan ta sumar dashi, bakinta ta turo gaba kamar wata ƙaramar yarinya kafin kuma tai wani irin juyi wanda ya bata damar samun babban muhalli a saman jikinshi ta saka hannunta ta janyoshi kamar pillow, batare data buɗe idanunta ba take yawo da hannunta zuwa saman face ɗinshi jin gashi kwance bisa fuskarshi ya bata tabbacin a jikin namiji take wani irin tsalle zuciyarta ke mata kafin ta samu ta juyo da ƙyar tare da kici-kicin neman tsira sedai ta makaro sabida ya riga yay mata riƙon tsauri kasancewar shi namijin duniya yasa ya gama janyota zuwa saman cinyarshi ba tare kuma daya zauna ba, a yadda yake a tsugunnen haka yake riƙe da ita ajikinshi saboda idan ya saketa tabbas xatai mummunar faɗuwar da setaji mugun ciwo, jin ƙamshin shu'umin turare mai azababben ƙamshin da tunda mama ta kawota duniya bata taɓa jin irinshi ba yasa ta soma ƙoƙarin bude madai daitan idanunta waɗanda suka ɗan kumbura sabida bacci.

Karaf ta sauke akanshi wani tsalle cikin zuciyarta yay wanda hatta shi seda yaji yadda bugun zuciyar tata ke mugun tsallen, kafin ta soma ruwan hawaye kamar famfo tana kuma ƙoƙarin dira sedai ta makaro, abinda ya bata mamaki sema ganin datai ya miƙe da ita a tsaye a hakan, ilahirin jikinta rawa ya cigaba dayi, kafin ta sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi ganin ya direta a gabansa wanda ta koma ƴar firit agaban nashi sabida yanayinshi na ingarman namiji, taga-taga ta somayi zata faɗi sabida yadda kanta yake neman juyewa, karaf ta kumajin taci karo da tattausan kirjinshi wanda babu abinda take shaƙa se ƙamshi gefe guda kuma ta sami guri mai kyau domin har wani nutso tai acikin kirjin nashi.

Wani irin zirrrrrrr yarrrr zuuuuuuuu!! yaji adukkan ilahirin gangar jikinshi har zuwa yatsun hannunshi tun sanda ya ganta a haka yaji wani zazzafan zazzaɓi yana son rufeshi batare daya shirya ba, lokacin daya karata jikinshi tabbas yay namijin ƙoƙari kafin ya sami nutsuwarshi ta dawo dai dai, still yanzu datake maƙale a ƙirjinshi jin wani mugun fitsari yake yana taho mishi wanda bai san dashiba, cikin tsantsar kamewa ya sami damar tureta daga jikinshi nashi tare da maka mata wata razananniyar tsawar! data saka Bebi zubewa tai zaman da bata shirya ba, tare da saka hannunta tana rufe kunnenta, baki ɗaya ta firgice ta susuce ta tsorata kamar xata shiɗe.

"Dan gidanku haka aka koya miki, rungumar maza!! ya daka mata wannan tsawar tare da furta mata wannan maganar wadda baisan da fitowarta a bakinshi ba.

Bai jirata ba yaci gaba da cewa........

"Kinzo nan kina shashanci da daƙiƙanci kinbar ƴar uwarki tana bilayin nimanki sabida ke bakkida nutsuwa ko?".

A wannan karon sosai yayo gabanta kamar ze duketa cikin sauri tai baya tanajin wani irin mugun tsoro aranta tana ayyana wannan wata sabuwar jarabarce kenan babu dangin uwa bare na uba daga haduwa yau ze nemi shiga rayuwarta.

Amman a fili kuka take sosai tana haɗe hannunta guri ɗaya tana boyesu a bayanta dan duk tagama tunanin zaneta zeyi wata muguwar faduwar gaba takeji har shakewa take sabida tsabar kuka!.

Jada baya yay yana kallon tsoronshi  a saman fuskarta, murmushin da bansan ma'anarshi ba,naga yayi tare da kallonta da fitinannun mayun idanunshi dasuka ɗanyi ja! kaɗan.

"Maza biyoni wawiya, idan kika batamin lokaci zan saka karnukan bayan can na masu gadi sumin kaca-kaca da naman jikinki".yafaɗa yana juyawa tare da gyara jikinshi sosai yawani tamke fuska kamar koda yaushe.

Lokacin daya karasa inda yabar hussaina yay mamakin rashin ganin ta dabai yiba, wanda ita hussaina ganin ya jima bai dawo ba yasa kawai tai tunanin maganarshi ta farko wadda yace ko Bebi tai gida, shiyasa tai tafiyarta tana ayyana yadda xata karta ma bebi rashin m.
Tsaki! yaɗan ja baison mutum marar yarda, kafin ya karasa gaban motarshi wadda taci black tinted, a window's ɗinta yay mata key ya bude tare da shiga ya xauna yana addu'a kafin ya kunnata, haryay revars yana kokarin tada motar bata karasoba seda ya juyawa  sannan  ya hangota yaga yadda take tafe kamar wadda ƙwai ya fashewa aciki duk ta cure kanta da hijabin jikinta dayake tunanin bayan tawowarshi ta sami zarafin sashi, tsayawa tai cike da tsoro! tana waigen hussaina amman wajan wayam haka zalika bataga hussainar ba, jin ƙarar horn a gabanta yabata tabbacin wancan masifaffen ne kamar yadda ta saka mishi, cike da firgici ta karasa gaban motar ganin, yadda motar take da wani irin kyau kamar babu gobe yasa  taja  ta tsaya jikinta yana faman rawa.
Cike da masifa ya turo marufin kofar tare da firfito mata da manyan idanunshi yana mata nuni data shigo cikin motar.
Cike da tsabar tsoro ta shiga wajan daya bude mata inda yake emty site na kusada  driver site hannunshi ya ɗora saman cinyarta ya tura murfin ya rufe motar kafin yaja ya tafi wanda yabata damar sakin wawiyar ajiyar zuciya............

_Nima na saki malam Ali yada haka_ ?

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*49&50*

Tura kanta tayi a tsakanin cinyoyinta kirjinta yana wani irin tsalle yana harbawa sabida yadda tagama tsorata da lamarin nashi wani irin mugun tsorone ke ziyartarta wanda bata shirya mishi ba, Tuni Bebi ta koma wata irin abar tausayi kamar ba wannan marar kunyar yarinyar ba, Har yaja motar ya tafi bata ɗago kanta ba, sabida duk ta riga ta saduda tagama yankewa zuciyarta cewar shikenan itafa ta'ta tagama ƙarewa ƙila zuwa ze ya siyar da ita tunda ba ƙaunarta yake ba, duba da yadda tun ganinta na farko dashi acikin rayuwarta taga yadda yake aika mata da wani irin shu'umin kallon data kasa fassarashi ƙwaƙwalwar kanta ta kasa aunashi a mizani fahimta, amman ita kawai ta barshi akan cewa na ƙiyayyane da tsana mai zafi! tare da ƙyama da rashin haɗuwar jini a iya ta'ta fassarar datai daga daren jiya data kasa bacci har zuwa yanzu datake cikin motarshi.
Shiko Cikin nutsuwa yaja motar tashi har zuwa gaban tafkeken gate ɗin, horn ya danna masu tsaron gate ɗin suka bude mishi, shi aguje suna ɗaga mishi hannu, kan babban titi yahau idonshi tsaye bisa kwalta, Batare daya dubi inda take ba, bare ta saka ran ze mata magana sema Redion cikin motar daya kunna tare da ware ƙira'ar sheik abdur-rahman sudais cikin surarul baqrah,yana driving ɗinshi yana bin karatun jin tafiyar tai yawane yasa ta saka tafin hannunta ta goge hawayen datake, sannan ta ɗan ɗago a tsorace tana kallon titi, tsananin mamaki tare da tsabar kaɗuwa sune sukai mata dirar mikiya, tayaya yay saurin shaida anguwarsu haka? harya iya kawo kansa tabbas wannan bawan Allah banda tsantsar miskilancin dayake dashi yanada wata baiwa ta fikira da basira acikin kansa domin mutane da dama suna cewa suna kasa gane hanyar gidansu domin ita kanta tasha ɓata da a hanyar talle amman shiko jibi daga jiya da daddare zuwa yau harya kawo kanshi cikin anguwar lungunsune kawai basu ƙarasa ba, wanda bata fatan hakan tafi addu'ar Allah yasa yace ta sauka, sabida munafukai suna ganinta ta fito a mota za,a soma talle da ita, sannan ita kanta a mugun tsoro take sabida wannan shine karon farko a rayuwarta data taɓa shiga motar wani namiji dakuma ta'taɓa keɓewa dashi wanda ba muharraminta ba.
Cikinta ne yay wata irin kaɗawa ganin yana kokarin shigar da hancin motarshi ɗan gefen layinsu inda yawanci dama anan ake tsayar da mota domin layin nasu mota bata shiga cikinshi ko mai kaisu hassana kamfani shima anan yake tsayawa se shahid ya kawo mashi kulolin wurin. shikuma ya shigar dasu motar, rau-rau tai da idanunta hango dandazon mazan data gani a gefen inda shahid ke saida gawayi da alamun ko wani abun ake, sotake tai mishi magana akan ya daure ya sauketa anan kada ya karasa da ita can ɗin domin ta hango shahid zaune wanda yake wajan gawayin shi kasancewar motar wadda kai na cikinta xakaga na wajene tas amman shikam na waje baze taɓa ganin kaba sabida tinted ɗin dake glases ɗinta.
Duk yadda take haɗe hannu tana turo bakinta gaba yana kule da ita amman yay biris soyake yaga ƙaryar taurin kanta, sabida ya riga ya hango ƙalubale kala kala a saman fuskar tata,"Dan....ALLAH.....ka'ajeni anan kar shahid ya hangoni" taja maganar a farko a karshe ta haɗe kamar mai saurin baki.
Shuru yay mata amman ya saka hannu ya kashe redion still yana cigaba da driving ɗinshi bai tanka taba.
"Kajiiiiiiiiiiiiii"! ta faɗi hakan daɗan ƙarfi kaɗan sekuma ga hawaye suna bin saman fuskarta.
"A,a da zuwa zanyi na miƙawa mahaifiyarku ke! sannan nai bata bayin banzan sakarcin tallen jikinki da kike a kamfani, shasha sha wadda bata san inda ke mata ciwo ajikinta ba, se yanzu kika san da tsoron da kinbar yayarki tana kuka! akanki......................."

Yakai kusan 10mint yana faman zazzaga mata masifa kamar ya sami wata ƙanwarshi, Bebi bata aikin komai se kuka! tai data sanin wannan baccin data tayi wanda take da tabbacin harda takaicin yadda yaganta kwance acikin masifar tashi,"Nidai dan girman Allah kai haƙuri ka saukeni na rantse bazan kuma ba".tafaɗa tana haɗe hannayenta waje ɗaya, azuciyarta tana jin tsabar haushinsa kamar ta makeshi.
"Bafa zan sauke kiba Allah sena kaiki wajan m......." bai kaiba ta ɗago idonta wanda yake cike da hawaye cikin halinta na rashin kunya ta soma magana"Kaifa ka isheni wannan jaraba haka babu dangi uwa bare..........", Bata kaiba taji danshi agefen bakinta gefe guda wani sihirtaccen zafine a wajan shafo wajan tai wanda ya bata tabbacin ya fasa mata bakinta da dukan daya kaiwa bakin nata a ɗazu alokacin datake masa tsiwa.
"Oh no wonder ashe da fitsararra nike magana marar kunya, halan bakki da tarbiya dan ubanki! bakisan nagaba dake ba?"!!!taji amon! muryarshi yana zaginta sosai yake mata masifa kamar ze ƙara mata wani dukan akan wanda yawa bakinta.
Sada kanta tai a ƙasa tana ɗigar da hawaye masu zafi! wannan wace irin masiface? miye haɗinta dashi daze nemi shiga cikin rayuwarta? hawayen ta share cikin takaici tana ayyana yadda ta taso ko bango ne ya bugeta sefa ta koma ta rama sabida faɗanta bata ragawa kowa hatta ƴan biyunsu bata bari amman daga jiya Zuwa yau wanda bata sanshi ba batasan da rayuwarshiba ya shigo tata rayuwar ze uzzura mata banda ɗan banzan tsoronshi daya saka mata acikin zuciyarta.
"Fitar min a mota shasha sha tun kafin na cire miki haƙoran bakinki! yakamata ki adana wannan rashin kunyar taki idan zan haɗu dake........." bata jira sauran ba ta balle murfin motar ta fita aguje............!!

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*51&52*

Da wani iri mahaukacin gudu taga yaja motar yabar wajan kamar ze tashi sama, jan ƙafafunta

tayi, waɗanda sukai mata wani irin mugun sanyi ta soma nufar cikin layinsu abinda yay matuƙar bata tsoro shine yadda ta hangi shahid tare da wani babban mutum fari, suna tsaye da alamun magana suke sedai kuma duk hankalinsu yana gurinta,Cikin sanyin jiki ƙalau take sarrafa ƙafafunta, tanajin wani bakon lamari atare da ita, tunda take bata taɓa ganin irin kallon da wannan farin mutum yake mata ba, kallone mai cike da tarin ma'anoni kala-kala, cikin tsananin dauriya wadda tai mata saura ta wuce ta gabansu batare data yiwa kowa magana acikinsu ba.
"Habawa ga irinta nan! ai nafaɗawa su Rabi'u sunƙi ganewa nace daman Aisha ta riga ta nunawa ƴaƴan musa, bariki kai! babana wannan ba Bilki bace ba?".
Wannan farin mutumin ke tambayar shahid cike da zaƙuwa.
Cikin rawar jiki tare da tsantsar mamakin Bebi shima shahid ɗin yake ɗagawa wannan mutumin kansa alamun Eh itace.
Gefe ɗaya kuma ga ƴan siyan gawayin shahid duk sunyi tsuru suna sonjin meke faruwa, ganin haka yasa shahid ya soma nufar hanyar gida.
Cike da wani irin tsoro Bebi take tura buhun kofar gidan nasu, da mama da hassana suka kusan cin karo, kusan a tare mama da hassana suka sauke wata ajiyar zuciya hassana batai wata sanyaba ta wankawa Bebi wani bahagon mari a saman fuskarta, cikin kuncin zuciya mama taja hannunta ta wurga cikin gida.
"Daga motar ubanwa kike Bebi na shiga uku! ni aishatu Allah ka dubeni"!!
"Ai bakiga komai ba bala'i da masifa! yanzu kika tsoma ƙafa cikinsu munafukar Allah daman anjima ana kawo mana maganarki munyi biris dakene muga iya gudun ruwanki! to wallahi baze yuwuba dole mu dage akan ƴaƴan ɗan uwanmu, domin baxaki maishe su karuwan gida ba, tabbas yau inda wanine yaga yamin zanyi karya.amman da idona naga Bilki ta fito daga wata sheɗaniyar motar da duk garin nan bantaɓa ganin irinta ba, Dan haka ina son ki tattare dukkan kuɗin karuwancin ƴaƴanki ki sai musu gado dan daga nan zuwa kowani lokaci zamuzo da taron ɗaurin auren su da duk wanda mukaga dama"!!!
Yana gama faɗin haka ya baza babbar rigarshi yabar gidan.
Zubewa mama tayi awajan tana kuka! maicin rai wanda yay mugun ɗagawa yaran nata hankali.
Cikin gigita hussaina ta fito daga ɗaki tana riko mama.
"Dan Allah mama kibar kuka! babu wanda ya isa yay mana abinda Allah bai mana ba, ita kuma Bebin data jawo mana zubewar mutunci wallahi sedai abin ya ƙare a iya kan........", "Kull hussaina kada na kumajin wannan maganar daga bakinki", mama ta faɗi hakan da sauri sannan ta miƙe gaban Bebi taje ta riko hannunta sukai ɗaki.
Su hassana ma ganin haka yasa sukabi maman ciki, Zaunar da Bebi tai agabanta.
Tare da daure fuska tamau wadda bebin bata taba ganin irin haka daga wajan mamar ba.
"Bebi waya sauke ki daga cikin mota, kuma daga ina kike har ƴar uwarki ta dawo ke baki dawo ba?" mama ta buga mata wata shegiyar tsawar data mayar da ita ƙasa babu shiri.
"Mama wallahi babu abinda ya faru kawai.............", tas ta kwashe komai daya faru ta gayawa mama, amman bata gaya musu cewar ga wanda yay mata hakan ba, kuma bata nuna cewar Aliyu ɗan uwan usman bane ba, sannan duk bidirin da sukai nan ma bata faɗa ba, sabida gudun zargi wanda ita dakanta tasan cewar bawai da gangan komai ya faru ba face tsabar son jikinta daya ja mata baccin daya kaita ga faɗawa cikin wannan matsalar abinda yasa kuma bata nuna ɗan uwan usman ne yay mata hakan ba nan ma gudun wata matsalar wadda tasan mama xata iya yin wani tunanin na daban akanta.

"Idan banda sakarci da wawanci ina ke ina bacci a wajan sana'a yanzu shiɗin bada ban na Allah bane ba kina tunanin baze iya yin lalata dake ba?" ta inda mama take shiga bata nan take fita ba seda tai wa bebi faɗan da bebin da sauran basu taɓa zaton mama nadashi ba.
Kallon ƴan biyu tai tace suje su gyara tsakar gida ita kam zancen fita tallen nan ma tana tunanin zata ɗagashi.
Suna fita ɗakin ya rage daga mama se bebi, kallon bebi mama tayi tare da cewa.....
"Zonan Bebi".
Tafaɗa fuskarta babu alamun wasa bare sassauci.
Tasowa tai jikinta yana wani irin rawa tana ayyana cewar ita kam taga takanta yau am!
Tsira mata idanu tai tare da nazarinta cikin hikima.
Tagama caje jikin Bebi bataci karo da komai ba seda mayen ƙamshin daya sa tajawo Bebin saman cinyarta babu shiri, hawayene ya soma zarya a saman kuncin mama.
"Bebi waya rungumeki? wannan sauyin ƙamshin bansan shiba daga jima wannan turaren daga duk inda yake na manyan mutanene dawa kika haɗa jiki a kamfani?".
Mama ta faɗa tanajin tsoron kar wani abu ya sami ɗiyar tata wanda bata fatanshi insha Allahu.
"Nacewa ƴan uwanki su fitane sabida gudun sumiki kallon bai bai! nai miki bahaguwar tambaya a gabansu domin na karkatar dasu ga mugun zargi kinsan zuciya, a wannan karon Bebi kada ki ɗauke ni a komai face mahaifiya mai fahimtar ƴaƴanta kiwa girman Allah ki gayamin dukkan abinda ya faru nai miki alkawarin zan miki fahimta mai kyau! Bebi bana son rayuwar waninku ta sauya daga irin tarbiyar danai muku bani da uwa bani da uba babu yaya bare ƙani mahaifinku danake so Allah ya rabani dashi kune kaɗai sanyin idaniyata idan wanin ku ya shiga matsala ina ganin bazan dena zubda ƙwalla ba, kina kallon irin sharrin da ɗan uwan mahaifinku yazo yay muku wanda ni bata tasa nakeba a ɗazun face ta rudewar fitowarki daga cikin motar damuka ga kinyi a ɗazun nida hassana mun leƙo muna hangen dawo warki".
Tafaɗa idanunta still dai yana ɗigar ƙwallah.
"Mama wallahi baimin komai ba, wannanfa ɗan uwan wanda suka zo jiyan nan ne ɗaukar dambu, shine hussaina ta bani alale na kaiwa wancan ɗayan, to ban saniba naje ofishin sa............." komai seda ta gayawa mama bata rage ba, hatta faɗan dayay mata harma da buge mata bakin dayay akan rashin kunyar datai mishi bata rage ba.
"Alhamdulillahi!, cewar mama sannan ta dubi Bebi da kyau.
"Kiramin hassana da hussaina duka har shahid ma naji muryarshi a waje".
Sum sum ta mike taje tazo dasu dukkansu sunka zube gaban mama suna sauraranta ganin ta tsaida hankalinta garesu.
"Ina son dukkanku kujini da kyau! Ke hussaina ban yarda daga yanzu idan kunje wajan talle da wani acikinku kice masa yaje kaiwa wani abinci office ba, kina jina duk wanda yakeso ze iya zuwa ya siya idan kuma baida lokacin karba ku aje mishi harya gama abinda yake yazo ya ɗauka, tabbas inda inada yadda xanyi wallahi baku kuma tallah amman babu komai ina mikawa Allah lamuranmu baki ɗaya...........Se abu nagaba kuma bana son kuyiwa yar uwarku bahaguwar fahimta kunsan dai halinta da sakarcin tsiya ke ashe dataci dambun ɗazu kwanciyar ta tai a bayan masallaci tai sana'ar tata ta bacci shine fa lokacin da usman yazo shigewa ya ganta anan yasa aka tasota ya bawa drivern sa makullin mota ya kawota gida, kunsan ita bebi bata rabe da usman ba seda taimin kwatance yanzu na gane nima, dafan kun fahimta insha Allahu yadda na baku tarbiya ina fatan kujewa mazajenku da ita in sha Allah".

Mama tafaɗi hakan domin ta kuma wanke bebi cikin ƴan uwanta gudun zargi kunsan zuciya ba ƙashi.
"Insha Allahu mama zamu kiyaye".
"Gobe ma ku zauna kawai bazamuyi ba ku huta hakan nan inada shinkafata harta jibi insha Allahu babu wani inda xaku kuma zuwa, ni babban tashin hankalina ma wannan dangin mahaifin naku Allah yay mana tsari da sharrinsu".
Sannan ta juya gaban shahid.
"Ina ka haɗu da tasi'u sannan kuma waya nuna mishi nan unguwar ma?".
Tafaɗa cike da mamaki.
Sosa kai shahid yay kana yace.
"Wallahi mama yadda kika ganshi haka naganshi ɗazun yazo wajena ina bawa wani gawayi sedai alamun ma bashi ɗaya bane, seda na gama sannan yazo yana cewa wai ban ganeshi ba sabida uwarmu bata nuna mana suba, murmushi nayi sannan nace masa haba baba naganeka mana sedai ban san sunanka ba sabida rabona daku tun ana goyon bebi, shine yake tambayata wai inane gidanmu nikuwa na nuna mishi to muna tsaka da magana bebin ta fito daga mota shine ya kureta da idanu yana kallonta harzata gifta yake cemin wacece nace masa bebi ce shine fa ya biyo bayanta haryay miki wannan cin zarafin".
Shahid yakai maganar yana kallon mama.
Murmushi tayi sannan ta dubesu.
"Tabbas yau naga tasi'u gobe ko anjima xanga sani da rabi'u kuma zuwan nasu babu alkairi sedai sharri ina fatan Allah ya tsallakar damu ai daman yanxu kun zama mutane na tabbata akwai wata a ƙasa zuwansu akwai lauje cikin ɗani, maza kumu fita muyi aikin gabanmu".
Mama tafaɗa cikin dakewar zuci.
"Mama mekuma yay saura seda muka zama mutane sannan zasu nememu nifa ko a hanya na gansu bazan shaidasu ba"..
"Kull hussaina banson maganar raini ta shiga tsakaninku da ƴan uwan mahaifinku iko akeson nunan na dangin uba nikuma zan nuna musu Ni uwace maba da mama"!!!
Mama tafaɗi hakan tare da mikewa.
Seda takai kofa sannan tacewa Bebi taje tai wanka ta sauya tsumman jikinta sannan tazo ga abincinta kana suka fita suna cigaba da mai maita maganganun da baba tasi'un ya gayawa mama.
Suna fita bebi ta koma ragwaf ta kwanta baki ɗaya tunaninta ya tsaya cak!
Abinda ta iya faɗa shine.
"Duk inda xanyi sena nema ka na gaya maka magangun son raina ɗan iska kawai babu gaira babu dalili yazo yajazamin masifa".
Tafaɗi hakan tare da shafa gefen bakinta wanda ya kumbura sumtum.
"Bebi gafa ruwan wankan nan kada ya salance".
Tajiyo muryar mama wadda yasa tai maza ta tube kayanta tare da fita tsakar gidan a ɗarare.

Shikuwa Aliyu dawani irin mugun gudu yaja motar...............

_duk sanda kuka ga banyi update ba akwai uzurin daya risken musamman a yanzu danake cikin rashin jin daɗin jikina sakamakon zazzaɓin malerian dake damuna wannan ma nayi sabida masu bibiyata ne amman wlh bana jin daɗi kwanan nan_ 🙏

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*52&53*

Da wani irin mugun gudu Aliyu kejan motar wanda cikin mintuna kaɗan ta kaishi cikin unguwarsu ta yahaya gusau,Cikin zafin nama da kuzari yake danna uban horn abakin tafkeken gate ɗinsu cikin mintuna ƙalilan sojojin dake tsaron gate ɗin sukai saurin zuwa gaban gate ɗin tare dajanshi suka bude mishi cikinsa.
Hannu suke ɗaga mishi cikin girmamawa alamun suna mishi barka da zuwa kenan,Shiko baima kula da yadda suke ɗaga mishi hannunba, danna hancin motarshi yay zuwa cikin harabar adana motoci tare da fitowa daga cikin motar phone ɗinshi kaɗai ya iya rikewa se keyn motar yana tafe yana hade hanya cikin ƙanƙanin lokaci ya isa part ɗinsu wanda yay amfani da ƙofar baya wajan ɓulla zuwa samanshi domin baison hayaniya a halin yanzu
Acikin ƙayataccen falonshi ya zube saman one seater yana dafe kanshi wanda ke faman sara mishi, duk jijiyoyin kan sun tashi alamun yana damunshi sosai mikewa yay kamar an tsikareshi ya nufi gaban frij ruwa mai sanyi ya ɗauka tare da ɓalle marufin gorar ya kafa kanshi yana faman kwan kwaɗa kamar ze shanye dukkan ruwan frij ɗin haka yakejin maƙogoronshi na faman suya.
"Why Aliyu mike damunka?" haka yake faman faɗi a fili bayan ya aje gorar ruwan dake hannunshi wadda take emty domin bai bar komai ba.
Nufar cikin bedroom ɗinshi yay batare daya dubi inda ya watsar da phone ɗinshi ba.
Sintiri yake acikin bedroom ɗin nashi tare da saka hannunshi yana yamutsa sumar dake kanshi wadda batacika yawa ba se saisaye kaɗan dayayi.

Tunanin shi ya zurfafa akan wannan ƙaddararran auren daza'ai mishi wanda bai murnarshi ko kaɗan, Wanda damuwar hakan ta haifar mishi da mugun ciwon kai mai zafin gaske ya fuskanci kowa son wannan aure yake amman shikam baiko jin abin a farcen susanshi.
Zama yay saman soparshi tare da kokarin tube rigarshi se a sannan yake tuno wannan yarinyar ta ɗazu tsintar kanshi yay da sakin wani murmushi na daban wanda ban san ma'anarshi ba.
Tubewa yay jikinshi yay saura dagashi se dogon wondon rigar daya cire sekuma singlet faffaɗan kirjinshi wanda yake shaƙe da kwantaccen gashi bayyane,ɗora hannunshi yay a saman sopar idanunshi lumshe haƙiƙa yanada damuwa a ranshi amman baida wanda ze fuskanta da ita, gefe guda ga wani haɗaɗɗen ciwon mara dake kawo mishi cafka sakamakon body contact ɗin dayay da wannan ƴar yarinyar amman haka kawai jikinshi ya tashi wanda tun a mota yake faman haɗeshi amman hakan ya faskara, da ƙyar ya mike hannunshi dafe da west ɗinshi gaban cabet ɗinshi yaje tare da janyo drowwer wadda drugs ɗinshi ke ciki ɗaukosu yay tare da komawa ɗan ragowar ruwan dake tsakiyar table ɗin shi ya ɗauka ya balle drugs ɗin ya watsa tare da afa ruwa bisa bakinshi sannan ya koma saman sopar still kwantar da kanshi yay yana saƙe saƙe acikin zuciyarshi.
Ganin time yanaja yasashi tashi tare da nufar bathroom domin yaɗanji releife babu laifi ruwa ya watso ajikinshi tare da ɗauro alwala, zube kayan daya cire yay acikin washing machine tare da fitowa jikinshi daure da faffaɗan blue tawul wanda kuma ya ɗauro karami a saman kanshi yana goge saman kanshi dashi.
Ko cream bai shafa ba turare kawai yaɗan fesa kaɗan tare da nufar gaban close set ɗinshi shirya kanshi yay cikin ash jallabiya tare da fita zuwa falo lokacin anata kiran sallar magrib dan haka phone ɗinshi kaɗai ya ɗauka.tare da sauka ƙasa, Falon ammi ya shiga bakinshi dauke da sallama wadda yayta ciki-ciki, Ammi ya samu zaune akan sallaya tana lazimi gyaran murya kawai tai mishi dan haka bai zaunaba seya fita domin yaji ana kokarin tayar da sallah ya bari idan ya dawo ɗin suyi magana.
Har zuwa sallar isha'i yana cikin masallaci kasancewar shike jan limancin masallacin time to time idan yana available, bayan an idar da sallah tare suka jero da usman suna tafe usman na addabarshi da labarin yadda ɗazu sukaje wajan da zasuyi taron wunin bikin Aliyun wanda shi baima san da hakanba bada ban usman ɗin ya gaya mishi yanzu ba.
Taɓe bakinshi yay batare dayace uffan ba, kusan a tare suka shiga cikin babban falon abbansu wanda yake a farko kafin ka kai ga shiga ainihin falon ammi.
Usman ne ya zube a ƙasan carpet yana faman mayar da numfashin gajiya kamar wanda yay wani abun sakamakon ƴar ƙibar dayake da ita, shiko Aliyu daga ɗan wani saman stoll na table ɗin tsakiyar falon yaja ya zauna yana ɗaukar wani ɗan littafi daya gani a saman table ɗin, idanunshi kafe akan littafin har abba yay sallama ya shigo bayanshi yaya abbakar ne, se nusaiba wadda take biwa Aliyu, tare da ƴan ƴaƴanta ƴan biyu a bayanta.
Cikin sauri ya juyo cikin ɗubin mamaki yake bin nusaiba da kallo na yaushe kikazo? amman seya bar abin can ƙasan ranshi tare da mayar da hankalinshi kan yaranta ya saka hannu ya ɗagosu yana manna musu kiss a saman goshinsu.
Gaba ɗaya ya mayar da hankalinshi kan yaran seda ya gama wasanshi da ƴan biyun waɗanda basufi shekaru ukuba, kuma dukkansu matane masha Allah, kyawawa dasu, sannan ya riko hannunsu sukai wajan abba wanda ya zauna akan lallausar darduma yana bawa ya abbakar umarnin ya haɗa mishi tv,gab da ƙafafun abbansu ya xauna yana aje yaran a saman carpet

tagumi ya zuba tare da ƙurawa abbansu ido kamar bai taɓa ganinshi ba.
Sarai abba yana lura da yadda yakeyin ɗin kuma yasan da abinda yake bukata sedai zurfin ciki bai barinshi ya fadi abinda ke ranshi, sedai abba da ammi suna yawan gano idan yay hakan tabbas yana cikin damuwa wanda daman can tun yana ƙarami da haka suke gane yana da matsala ko damuwa cikin ranshi.
Nusaiba ta zauna daga ɗayan side ɗin cikin girmamawa tace.
"Yaya haidara ina yini kai kaɗaine yau ban gani ba, yaya aiki ya shirye shirye?" tafaɗa cikin mutuntaka.
"Lafiya alhamdulillahi! ina su amir?" ya bata amsa idonshi na kan abba.
"Suna school kasan ba,ai hutu ba, na barsu da abbansu kawai se masu aiki".
Zaro idanunshi yay waje waɗanda suke ƙara mishi madarar kyau ɗan gaske, yana mata kallon bakida wayo.
"Kina nufin kin barosu acan tare da wasu kika kwaso ƙafafu kika tawo ke?".
Murmushi tai tuna yadda yake mutuwar son yara tasan idan shine baze iya ba.
"Eh! mana bikin yayana guda wanda nakeji dashi duk duniya aiko cikine idan da damar na aje sena aje bare kuma yaran dazasu iya yiwa kansu tsarki".
Dariyar usmance ta karade wajan.
"Gaya masa dai ƴar nusai angaya mishi kowa mayen yarane irinshi".
Wannan karon murmushi yay tare dajan bakinshi yay shuru.
Ya abbakar ne yagama haɗa kallon bayan ya kamo tashar CNN zama yay shima daga gefe tare da ɗaukar remote control domin ya rage volume ɗin tv'n.
Ammi ce tai sallama ta shigo se ƴan biyunta da amina waɗanda hannayensu yake ɗauke da manyan farantai na sliver guda uku waɗanda aka jero kayan abinci a samansu ajewa sukai daga gefe bayan sun gaisar da yayin nasu guri suka nema suka xauna, kowa ya halarta a wajan idan ka cire umar wanda ke legos, amman akwai abbakar, usman, aliyu, nusaiba, amina, hassana,hussaina, se ammi tare da abba, se ƴan jikokinsu waɗanda nusaiban tazo dasu daga birnin tarayya.
Gyaran! murya abba yay sannan ya dubi usman.
"Shehu fara bude mana taro da addu,a".
Yafaɗi hakan cikin bada umarni.
Batare da bata lokaciba usman ya mike ya jagoranci addu,ar kamar yadda abban yace bayan ankammala aka rufe da salatin annabi (s.a.w) se suka shafa sannan usman ya koma ya zauna, kowa ya bada hankalinshi akan abba.
"To Alhamdulillahi! muna godiya ga Allah mai kowa mai komai tsira da amincin Allah,su ƙara tabbata ga annabi muhammad ( s.a.w ) amin, kamar yadda kuka sani ban taraku anan domin komaiba sedan murnar sha'anin bikin ɗan uwanku dazamu fara nan da kwanaki biyu, to Alhamdulillahi ranar da kowa acikin wannan zuri'a yake fatan tazo tofa gatanan Allah ya nuna mana fatanmu Allah ya basu zaman lafiya da iyalai masu albarka".
Yaja fasali wanda ya bawa iyalan nashi damar amsawa da.
"Amin".
Sannan ya cigaba.
"Muna fatan Allah ya sanya alkairansa acikin wannan zama ya ƙara mana danƙon zumunta da kaunar juna amin, Aliyu kamar yadda ka sani, ina son kaima ka zauna anan cikin gidan acikin

ɓangaren dana mallaka maka bana son zuri'a ta tabar cikin gidan nan dan haka kowannenku na sama masa inda ze zauna, sedai kuma bayan aurenku da wata guda, zan turaka legos kucigaba da xama da umaru nan kuma ze koma hannun usman da fahad da mansur insha Allahu".
(fahad da mansur ƴaƴan Alhaji babbane yayan abba).
Nisawa ya kumayi inda falon yay tsit kamar babu kowa se saukar numfashinsu.
"Abbakar ya baka gudun mawarshi amatsayin shi na babban yayanku magajina, yayi maka lefe akwatuna seti biyu, umar ya ɗauki nauyin yiwa ita wannan yarinya jeren kayan ɗaki shiko shehu ya ɗauke nauyin komai wanda za,aci za,a sha acikin wannan taro, nusaiba, ta ɗinko maka kayan dazaka saka tundaga ƙasar sinigal, amina ta cika muku store da kayan abinci suko ƴan auta, lemuka da ruwa suka siyo maka, nagaya maka hakane domin kaiwa ƴan uwanka godiya sannan kuma kaima ka ƙara akan alkairin da kake musu na zumunci fatanmu Allah ya ƙara haɗe mana kanku".
Gaba ɗaya kanshi ya ɗauki zafi inama auren so yay da anga rawar kai duk da yaji dadin yadda ƴan uwan nashi sukai mashi amman abin bawani ratsashi yay ba sabida baya ɗaukin auren ze daurene kawai dan kyautatawa mahaifanshi.
"Bakace komai ba, babana?".
yaji saukar muryar ammi akanshi.
"Hajiya kinsan ɗan nawa da kunya fa, yaudai burinki ya cika ɗanki ze aure sekibar yimai lissafin shekaru".
Abban ya faɗa cikin barkwanci.
Murmushi ammi tai tana nazarin ɗan nata wanda yaƙi koda ɗago kanshi bare yay godiyar da aka ce.
Kamar ze kuka ya ɗago jan idanunshi yana fesar da zazzafar iskar baki.
"Nagode Allah ya saka da alkairi".
Abinda ya iya faɗi kenan murya a shaƙe kamar wanda yaci wani abun ya tsaya mishi a makoshin sa.
Hirar yadda lamarin bikin ze kaya ita tacigaba da wakana acikin falon wanda Aliyu yay gum kamar ba shi za,a yiwa bikin ba.
Har wajan 9 suna faman tattaunawa kafin amina ta mike ta soma zuzzuba musu abincin da sukazo dashi acikin flate, koda ta mikowa Aliyu girgiza kanshi yay bai amsa ba, sema saɓar ƴaƴan nusaiba da yay yabar musu falon.
Zama sosai su ammi sukai suna hirarsu tare da yaransu kamar wasu abokai daman wannan ce al'adar abba yana son yaga ya tara yaranshi tare da ƴan jikokinshi sun xauna suna hirarsu kamar babu gobe, haka xalika suna da kyakykyawar fahimta da surukansu matansu ya abbakar waɗanda suma suke kyautata musu sosai musamman anty zee matar usman wadda take ƴar ɗakin ammi.
Sun jima kafin mazan suyiwa su abba sallama suka bar falon suko su nusaiba zama sukai suna hirarsu da abba da ammi har zuwa wani lokaci kafin suyi sallama sabida dare yaɗan ja.
Aliyu yana fita bedroom ɗin ammi yaje kwantar da ƴaƴan nusaiba yay sannan ya fito cikin falonta ya xauna ƙafafunshi zube bisa table, hannunshi ya ɗora akanshi.
Har tsawon lokuta yana xaune seda yaga shigowar su ammina sannan ya ɗaga kai ya dubi agogo wajan karfe goman dare dan haka ya mike ya koma falon abba.

lokacin dayay sallama ammi tana zubawa abba black tea a cikin cup, da hannu abba yay mishi alamun dayazo gareshi.
Babu musu ya nufi gaban abba ya ɗanja baya kaɗan ya zauna yana tanƙwashe ƙafafunshi.
"Babana waya taɓamin kai naga tun ɗazu ran ƴan mazan a haɗe yake gajiyar office ce ko?".
Abba ya faɗa cikin kulawa.
Sunkuyar da kanshi yay kasa yana ayyana damuwar auren nan tafi gajiyar office dubu amman sabida tsabar zurfin cikinshi seya cewa abba.
"Naxo muyi wannan lissafin wallahi baccine a idanuna abba daman na jira kane harka nutsu".
Murmushi abban yay.
"Kai wannan baban nawafa akwai tsabar kaf kaf da kudi wato ashe kai zaman jira kai to maza ina jinka".
Abba ya faɗa yana mayar da hankali kansa lokacin ammi ta mikowa abba cup ɗin tea, sannan ta kuma haɗo wani ta miko wa ali.
"Amshi maza shanye ban kofin domin nasan bakaci komai ba ka tsaya bakin rai".
Cikin damuwa ya amshi kofin yakafa bakinshi tass ya shanye sabida babu zafi sosai.
Sannan ya mike tsaye mintuna biyu yaje  gaban frij saman yaɗan laluba ya ɗauko white papper wadda ya ajeta gaban abba yazo da ita dalla dalla yake zayyanewa abba abinda yake cikin takaddar wadda babu komai cikinta face tsantsar lissafi na cigaban da aka samu acikin kamfaninsu na wannan watan.
Abba yay farin ciki yaji daɗi sosai wanda murnar harta kasa buya.
Duk yaranshi babu wanda yakejin daɗin tafiyar da business ɗinshi kamar Ali sabida yasan kanshi abba yana jin dadinshi yana kuma alfahari dashi over.
"Haƙiƙa ina godiya ga Allah daya azurtani dakai babana Allah yaywa rayuwarka albarka kaji".
"Amin abba sedai kuma......., yakasa karisawa.
"Sedai me? faɗi mana komeye zan maka matukar baifi karfina ba, kuma matukar ba zancen fasa aurenka da khadijaba domin kasan wannan aure babu fashi sedai idan babu raina kona alhaji babba".
"Abba seda safe Allah ya bamu alkairi".
Yana faɗin hakan yay saurin tashi yabar wajan ranshi na suya.
"Amman Alhaji yakamata fa aduba lamarin yaronnan".
Muryar ammi ta karade falon cikin nutsuwa.
"Dakata! Balkisu banson zancen banza duk duniya bamuda kamar alhaji babba tunda ya bada umarni bamu isa muce damme ba, dama naga take takenki wallahi harda hannunki wajan kara tunzurashi a ƙin wannan aure".
Yafaɗa yana huci.
"Allah ya baka hakuri ni ban isa na hanashi aure ba tunda nima fatana kenan kullum Allah ya sanya alkairi amin".
Tana faɗin haka ta mike tabar falon sabida tasan halin abba yanzu se iya rufeta da faɗan tana ɗaurewa Aliyu gindi.
Ɗakinta ta koma tai kwanciyarta tana addu,ar Allah ya basu zaman lafiya.
Washe gari dawani irin ciwon kai aliyu ya tashi wanda ya hanashi fita office sannan ya kulle kanshi a ɗaki,  sabida hayaniyar ƴan biki da suka soma cika gidan.
Se wajan dare ma ya kunna wayoyinshi anan yayta cin karo da sakon taya murna wanda

abokanshi da sauran jama,a ke mishi wanda yasan usman ne yayta yawo da zancen auren nashi.
Wajan taran dare gidan yay tsit saukowa yay xuwa falon ammi wanda babu kowa ciki se masu aiki,yana kokarin fita sabida tun jiya da daddare rabonshi da wajen ko sallah ma yau a ɗaki yaytayin abarshi wayarshi dake cikin aljihun wandon jeans ɗin dake jikinshi ce take faman ringing dubawa yay yana kokarin fita ganin bakuwar number yasa yay banza da ita haka aka cigaba da kira kamar babu gobe.
Khadija wadda taci kwalliya ta alfarma tana gidan make up tana jiran angon nata yazo su wuce wajan event ɗin da tun ɗaxu suka ɗai ake jira ita ke faman doko mashi kira da ɗayan sim ɗin nata, gefe guda ƙawayenta na familyn su, sun zagayeta suna faman zuba mata hotuna sabida khadija ita sam bata da yawan kwashe kwashen kawaye yawanci ƙawayen nata ƴan gidane sa'anninta na familynsu.
Ido jajur take kallon jawa ɗiyar alhaji babba.
"Jawahir kinga yaya bai ɗauka ba kodai bazeje vane tun ɗazu su umma kemin waya".
Murmushi jawahir tai tana cewa.
"Haba dai yayafa usman ya bamu tabbacin xuwansa kinga kawai mukira ko yaya fahad ne yazo muwuce tunda time yana ja kawai ma hade acan".
Tura baki khadija tai.
"Nikuwa nafison naga gani gashi muna tafe ana ƙyasamu a hoto".
Tafaɗa tana lumshe idanu.
Seda jawahir tai da gaske sannan khadija ta yarda suka kira fahad yazo ya daukesu lokacin da sukaje waje ya cika makil da ɗan adam.
Hotuna akaita faman yiwa amarya da kawayenta.
Zama tai a high table tana kuma kiran layinshi sedai wannan karon swich off usman ma bata sami damar ganinshiba sedai matarsa zee take faman barin kudi, haka akai taron aka gama khadija na kukan zuci.
Ganin an dameshi da kira se kawai ya kashe wayar ya koma ɗakinshi tea ya haɗa daɗan biscut ya zauna yasha sannan yay wanka ya kwanta.
Rana bata ƙarya sedai uwar ɗiya taji kunya.
Yau ta kama ranar juma'a ɗaya ga watan ɗaya dubban manyan mutane na cikin kasarnan dama kewayenta suka shaida ɗaurin auren ALIYU IDRISS MAI ATAMFA! DA KHADIJA YUSUF MAI ATAMFA! cikin sadaki mai daraja can na hango usman yana faman baza babbar riga kamar angon, se faman baje baki yake ransa fess kamar shi akewa bikin.
Sanye ike cikin ɗanyen boyel royal blue anmasa ɗikin half body, se hular daya saka wadda tai marching da kayan jikinsa yay mugun kyau duk da rannan yana haɗe amman bai gaza fita da tsantsar kyawunshi ba.
Zamewa yay sabida kanshi daya soma ciwo yabar usman da tarin abokanshi ya gudu gida samanshi ya hau yasha magani ya kwanta.
Sosai akai taro na bikin wanda ya cika da manyan mutane ammi ma tai rawar gani sosai wajan kawata bikin ɗan nata sedai hankalinta yan wajanshi sabida ta jima bata ganshiba.
Se dare Jama,a suka ɗan lafa sosai umman khadija tai mata huduba wadda sam khadija bata hau kan ko guda ba, haka anty karima kanwarsu abba tazo taja hannun khadija har part ɗin alhaji babba yay mata nasiha mai ratsa jiki, sannan aka kaita wajan abba shima, zaunar da ita

sukai, gabansu sannan abba ya dauki waya ya kira gogan.
Yana zaune ya dafe kanshi yana mamakin waishi akawa auren dole, kiran abba ya dawo dashi daga duniyar tunaninshi.
Babu yadda ze haka ya zira black jallabiya akan boxern jikin nashi, sannan ya ɗauki wayoyinshi ya sauka zuwa falon abba.
Ammi da abba zaune se wadda yagani tana zaune gabansu ta rufe fuskarta.
Sallama yay tare da zama gabansu kana ya gaisarsu.
Cikin tsanaki abba ya dubi Aliyu tare da fara yi mishi nasiha mai ratsa jiki wadda rabinta akan rayuwar aure take tare da rikon amana na aure, daga karshe ya riƙo hannun khadija ya damƙawa Aliyu.
"Ka riken ita amana da mahaifinta dani uwarmu ɗaya ubanmu ɗaya ka rikemin ɗiyar yusufa da kyau! domin katayamu rike amanar daya rasu yabar mana kaji babana".
Abba yafaɗa idanunshi yana kawo ƙwalla.
Sannan ya juya ga khadija itama yay mata nasiha sosai wadda babu abinda take se faman kuka!
Yana kammalawa ya dubi Aliyu.
"Tashi kuje ɓangarenku akwai key jiki komai yana kintse office daman nace ka huta duk sanda kai ra'ayi ka koma".
Haɗe ranshi yay tamau.
"Abba ko kayana banyi parking ba pls ta kwana anan gobe insha Allah semu koma can ɗin".
A zafafe ammi ta ɗago kanta.
"Ban amince da shiga haƙƙin iyaliba,a matsayina na mahaifiyarka wadda take da hakki akanka wallahi idan yau baka saukewa marainiyar nan ta gabanmu hakkinta na auratayyaba ban yafe maka ba, sabida nasan halin taurin kanka ƙila yadda zaka jeda ita haka xaka barta ko kallo".
Dum! Dumm!! yaji gabanshi yay mugun faɗuwa akanta mahaifiyarshi ke faɗin haka.
Amman ammi ta ɗora mishi mugun nauyin daya xama dole ya saukeshi.
Ita kuwa ammi ta faɗi hakanne sabida kwaɗayin kota dalilin hakan Allah ze karkata hankalinshi kan khadijan su zama masoya na hakika amman har cikin ranta kawai tafaɗi hakanne da wannan manufar bada wata ta daban ba.
Shikanshi abba yay mamakin furucin ammin amman baice komai ba.
Itako khadija shiwa ammi albarka take sabida ta matsu matuka.
Da sauri yace.
"Zanyi ammina kimin gafara karki sake dan Allah kimin mugun baki".
Nisawa tai.
"Allah yay maka albarka maza tashi kaja matarka kutafi Allah ya sadamu da alkairinshi amin,".
Wuff ya mike yabar falon yana tafe yana hada hanya.
Ta kofar baya yabi sabida har yanzu akwai ƴan biki.
Daga part ɗin ammi zuwa nasu akwai tafiya yana tafe kamar marar lakar jiki.
Ita kuma tana bin bayanshi kamar cingam ranta fari fess yau xata kwana kan faffadan kirjinshi datake mugun marmari.
Ƙayataccen part ɗinsu ya tura gate ɗin ya shiga da sallama sannan ya karasa gaban katuwar kofar glass ɗin da aka kawata, babban falonsu ya shiga yana sallama abakinshi.
Sosai yay mamakin yadda aka kashewa part ɗin kuɗi ba kaɗan ba,sama ya haye inda

bedroom's ɗin gidan suke still tana biye dashi abaya.
Cikin bedroom guda ya shiga tare da faɗawa daman babban bed ɗin dayaji white bedshit yay mugun kyau.
Akanshi ta tsaya tana xare idanu batare data xauna ba.
Zumbur ya mike ya nufi hanyar bathroom alwala ya dauro tare da fitowa sumar kanshi jike da ruwa.
Tsareta yay da idanunshi.
"Jekiyo alwala muyi sallah"
Musgutawa tai a tsayen
"Inada alwala sabida banjima da sallar isha'i ba".
Murmushin xakici uvanki yay mata sannan ya ɗauko dadduma ya shinfiɗata.
Sallah yajasu raka"a biyu bayan sun idar ya jima yana addu,a sannan ya juya ya mata tambayoyi akan addininta sosai ta bashi amsa wadda daman bayada haufi akan hakan sabida babu laifi sun sami ilimin addini mai kyau.
Tashi yay tare da hayewa saman gado yana kallonta cikin muguntа.
"Naga kina matse har kina kokarin yimin fyaɗe  last time ok maza zona baki karki saka uwata ta tsinan".
Yafaɗa yana janyota ya zare mata mayafin jikinta.
"Baki isa kinga jikina ba sabida mai tsadane amman xan baki abinda kike muradi".
Yafaɗa yana fisgo bakinta da karfi cikin mugunta yake sucking lip's ɗinta hannunshi duka biyun suna aje kan mitsi mitsin boobs ɗinta yana murzasu cike da xallar mugunta tun tana kukan zuci harya fito fili babu abinda yake mata se xallar mugunta hatta numfashi da ƙyar take fisgoshi, lokacin daya tubeta ya ɗora bakinshi saman kirjinta, Ihu ta saka sabida harga Allah cizo kawai yake kaimata akan nippy ɗin nata sabida mugunta, rage hasken ɗakin yay yana karanto addu,ar saduwa da iyali kafin ya ɗauki hanyarshi ɗoɗar bai tunawa da itan budurwace haka ya gama sha'aninsa batare da armashiba sema ƙaro wutar jarabarshi dayay domin takasance mishi babu wani test ko kaɗan agaretan, sabida irin matan nan ne masu mugun sanyin daya musu illah har suke rasa ni'imarsu, itako tsantsar azaba ta saka ta suman wucin gadi kafin ta farfaɗo a cikin ruwan daya ɗagata ya sakata aciki bayan yagama bidirinsa, ɗan stain ɗin jinin daya bata bedshit ɗin yasa ya tattareshi ya watsa a washing maching lokacin karfe biyun dare ya kusa dan haka ya barta a bathroom domin ta kintsa shiko  ya shiga na ɗayan room ɗin domin bayajin ze iya nuna tsiraicinshi gavanta.
Allah ya taimakeshi ya sami jallabiya acikin Carbet sabuwa dall fara dan haka yay using da ita bayan ya fito, alwala ya dauro ya kwanta sabida duk jinsa yake wani iri duk da ya sameta a ɗiya mace amman sam baiji wani dadin da abokanshi kecewa ba sema jarabar zafin da abarshi ke mishi adaddafe bacci ya kwashe sa.
Itakuwa khadija tai kuka kamar babu gobe kasancewarta ba yarinya ba yasa ta gyara kanta wajan ruwa biyar tai na xafi ta shiga sannan taɗanji dadi kana ta futo tana ɗingishi ta sauya kaya ta haye gado tana curewa waje guda.
Koda asubahi daya tashi ya shiga ɗakinta da gyar ya ita tada ita tai sallah sannan shima ya wuce masallaci daga nan kuma yaje yayta jigilar kwaso kayanshi nacan part ɗin yana fiddosu ta kofar baya, har wajan 7am yana faman abu ɗaya seda yay setting close ɗinshi tsaff a bedroom ɗin dayake can gefen na khadijan wanda yake nasa sannan yay wanka ya shirya cikin bakin

yadi mai farin xare wajansu abba yaje suka gaisa sannan yaje ya gaisar da mutan gidan, daganan bai koma part ɗinshi ba parking lot yaje tare da karbar mukullin motar wata black prado 018 ya shiga tare da bata wuta yabar harabar gidan tare da nufar gaban gate masu gadi suka bude mai ya fice.......

Bebi tana fitowa daga wanka ta shige ɗaki ta kwanta zazzafan zazzabine ya rufeta washegari basu fita tallale ba, haka xalika ɗayan washe garin ma basu fita ba suna gida abinsu wanda zuwa wannan lokacin zazzaɓin bebi yay zafi yaudai mama ta sakata agaba domin suje ganin likita.........

_SAƘON GODIYA GA MASOYANA KUSANI IDAN HAR KUKAGA BANYI UPDATE BA SEDA DALILI MAI ƘARFI AFUWAN JINA KWANA BIYU DA KUKAI SHURU_

*NOTE EDITING AFUWAN FOR THE TYPING ERROS* 🙏

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*54*

Ƙarfe takwas na safiya taiwa su mama da Bebi acikin asibitin shaka tafi na sharaɗa, wajan yankar kati mama ta nufa bayan ta samawa Bebi ɗan dakalin da marasa lafiya ke zama kafin layi yazo kansu.
Kwanciya tai akan dakalin tana cure hijabinta wuri guda, bayan ta naɗe ƙafafuwanta dik ilahirin jikinta rawa yake gawani zazzafan hucin dake fesowa ta jikinta sabida zafin zazzaɓin malerian

datake kwana dashi take tashi  dashi acikin ƴan kwanaki biyun nan.
Wajan mintuna goma mama tana tsaye bakin windown da nurse ɗin dake bada katin ke ciki, seda layi yazo kanta sannan ta faɗi sunan bebi tare dana mahaifinta da shekarunta sannan aka bata katin ta'tawo gaban Bebin ta tsaya tana kiran sunanta.
"Bebi tashi muje can wajan acan zamuga likitan kinji".
Tafaɗa tare da ɗan jan ƙafafun Bebi dasuke cure cikin hijabi kaɗan.
Ɗagowa tai idanun nan nata yay jajur tana kallon mama dasu kafin kuma ta yunƙura ta miƙe tana jawo slipers ɗinta ta zirasu cikin ƙafafunta sannan tabi mama suka tafi wajan bin layin ganin likita.
Nan ɗinma sun ja lokuta masu tsawo kafin akira sunanta yunƙurawa sukai mama ta kama hannunta har zuwa cikin ɗan madai daicin ofishin da likitan ke ciki wadda ta kasance mace'ce taci farin glass tana zaune akan kujera irin mai juya mutane, Sallama mama tayi, Cikin kulawa da mutuntaka wannan likitar ta ɗan zare glashin idanunta kaɗan tana amsawa mama sallamar. Nuna musu kujerar dake kallonta tayi tare da cewa.
"Bilkisu Musa Ko?"
Bebi ce ta ɗaga kanta tana ɗan matsawa gaban likitar tare da katin ta a hannunta.
"Bayan zazzaɓi sekuma me yake damunki? Kina ciwon kai? koko amai?".
Likitar ta faɗa, idanunta tsaye akan katin tana rubutu cikin sauri biro ɗauke a hannunta.
"A,a nidai kawai zazzaɓi nake senaita jin sanyi baya nan bana jin komai".
"Okey".
Likitar ta faɗi bayan ta gamajin abinda Bebin tafaɗa.
Tajima tana rubutu sannan ta miƙowa mama katin tana cewa.
"Maleria ce ke damunta a daure asai waɗannan magungunan sannan ga allurai nan, daza,ai mata na tsawon kwana uku, Allah ya sawwaƙe".
Tafaɗa tana ɗaga murya tana kiran next daze shigo.
Godiya mama tai mata tare da kamo Hannun Bebi suka fita daga office ɗin likitar.
Abakin asibitin mama ta zaunar da Bebi jikin wata bishiya ita kuma ta shiga wani chemist, mintuna biyu tazo da magungunan da aka rubuta musu acikin bakar leda, sannan tasaka bebi agaba suka hau napep zuwa gida.
Acikin napep ɗinne mama kecewa Bebi.
"Ga alluran bara mukoma ko asiya ƴar gidan malam ya'u muka kira setai miki agida".
"Nidai mama bara kawai nasha maganin base anyi alluran ba, naji sauki".
Tafaɗa murya can ciki tana rawa alamun rashin lafiya, daman can Bebi bata kaunar allura tun tana ƙaramarta, haka xalika koda ta girman ma yanzu bata sonsa ta koɗan.
"Sefa an miki dan bazaki zo tsakar dare ki hanamu rintsawa ba nasanki da ɗan banxan rakin ciwo".
Mama tafaɗa idanunta bisa kwalta.
"Wallahi mama bazanyi ba nikam banson allura dan Allah mama kar amin".
Mama bata kulata ba tanajinta tana faman rakin magiyar kai ai mata allura amman tai mata fumfuris taƙi tanka mata.
Adai dai bakin layinsu mai napep ɗin yatsaya sakamakon dakatar dashi ɗin da mama tayi. Saukowa sukai, mama ta bashi naira saba'in tana mishi godiya, tunma kafin maman ta fito, Bebi tai maza ta sauka cikin sauri tai cikin layinsu sabida gudun kar mama tace su biya gidan malam

ya'u ai mata allura.
Tana yaye bugun soro mama na biye da ita kusan atare sukai sallama.
Hassana tana tsakar gida tana ɗaurin kayan miya hussaina kuma tana bakin kicin tana ɗaurin alalen leda wanda zasuyi shi na abincin ranar yau.
Amsa sallamar sukai sunawa mama barka da dawowa sannan suka juyo sunawa Bebi yaya jikin, da ƙyar take amsawa sabida yadda kanta ke mata mugun ciwo.
Hijabin jikinta ta cire,ta rataye a jikin ƙofar ɗakinsu jikinta sanye da wata doguwar rigar atamfa ko ɗan kwali daman bata ɗauraba, janyo tabarmar gefen da hassana take tayi ta shinfiɗa ta kwanta tana jan numfashi kaɗan-kaɗan ido jawur take kallon mama.wadda itama take kokarin zama agefen hassana bayan ta sauke gyalen jikinta.
"Mama zansha kunun aya mai sanyi".
Tafaɗa tana juya musu baya ta kalli ƙofar ɗakinsu.
"To Hussaina ina ihsan ne ko arfa ban gansuba tunda na shigo, suzo su karmo miki gidan hadiza".
Mama ta faɗa tana ɗan matsawa gaban Bebi tare da shafa kanta.
"Mama sunje siyo barkono amman bara nina siyo mata".
Tafaɗa tana tashi daga kan aikinta.
"A,a zauna bara suzo ɗin cigaba da aikin gabanki".
Maman tafaɗi sannan ta ɗan ranƙwafo saman bebi tana mata magana.
"Uwata bayan kunun ayan mekuma zakici, nifa wallahi duk kin sakani acikin damuwa sabida ke duk zafin ciwo bakya ƙin kai loma bakinki amman wannan karon ina naga ko ruwa baki shaba ko nama zan siyo miki na dafa miki uwata?".
Mama tafaɗa tana ɗagota tare da ɗorata saman cinyarta.
Hawayene yake faman zubo mata hannunta saman kirjinta.
"Mama nidai kunun aya zansha don Allah".
Tafaɗa muryarta tana rawa, itafa ba xafin ciwon nan ne kaɗai ya hanata cin abinciba harda cin zarafin da wannan guy ɗin yamata wanda take jin mugun zafin abin har bargonta burinta a kullum ta ganshi domin ta rama zagin ubanta dayay wanda yake ƙasa bai taka ba kuma bai zubar ba amman ze zagar abanza.
"To kuma kukan na maye nifa banson ciwo da kuka keda kike jaruma bari suzo su sayo miki kunun ayar yau har kaza xan dafa miki kici ki koshi kinji uwata banson damuwarki".
Mama tafaɗa cikin rarrashinta.
Cikin haka su ihsan ɗin suka dawo suma da sallama suka shigo gidan sunawa mama sannu da zuwa sannan sukaiwa Bebi yaya jiki.
"Ihsan maza ɗauko ɗari a saman madubi kije gidan hadiza ki sayo kunun aya kuna hamsin Bebi na hamsin maza ƴar albarkata ki dawo".
Mama tafaɗawa ihsan haka wadda ta amsa da to bayan ta mika barkonon hannunta.
Shiga ɗakin tai ta ɗauko kudin ta fita ita kuma arfa ƴar autar mama ta ɗauko turmi ta haɗa kayan daka yaji tayi hanyar soro domin daka barkonon.
Mintuna kusan biyar ihsan ta shigo hannunta ɗauke da jarkar kunun gyaɗa har guda biyu, nasu ta mikawa hassana tana cewa.
"Anty hassana ga namu".
Amsa hannasa tai sannan ta mikawa Mama na BEBI.

Tun kafin mama tai magana Bebi ta amshi kunun a hannun mama ta kafa kanta ta shanye tas.
Sannan ta amshi maganin da mama ta ballo mata xata sha.
"A,a keda bakici komai ba ai bakyasha magani ba".Mama tafaɗi hakan tana kallon Bebi.
"Nifa mama na koshi kibani nasha wallahi babu komai".
"A,a bazan bakiba ai na ɗauka zaki haɗa da sauran biredin safene shiyasa na ballosu".
Dole tasa seda taɗan cusa bread sannan mama ta bata maganin tasha seta jingina ajikin bango batare data kwantaba.
"Mama ɗazu Uncle usman ya kira waya wai kwana biyu bamuje kamfani ba sannan kuma baban nazir ma ya kira shima dai korafin rashin ganin namu ya faɗa".
Cewar hussaina wadda ta gama.ɗaurin alalen zata ɗora akan wuta.
"Ke rabu dani kozaku koma senan da sati ɗaya haka kafin nan na ƙara jari tunda wannan ɗin muncinye, yaufa inaganin ma shinkafarmu zata kare kuma kuɗin hannuna na kwashe na siyo maganin Bebi".
Cewar mama wadda ta mike xata shiga ɗaki.
"Mama Allah ze tallafemu karki damu".
Cewar hassana wadda ta kammala ɗaura kayan miyan dake gabanta.
"Hakane daman Allah ya rufa asiri".
Mama tafaɗa tana shigewa ɗakinta....................

*********************
Cikin nutsuwa yake driving ɗinshi hankalinshi kwance babu wani damuwa acikin ranshi, kai tsaye nasarawa ya nufa can cikin wata anguwa wai ita ƴan majalisu, wajan wani mutuminsa yaje wanda sukai xancen zasu ƙulla wata sabga duk dai akan kasuwancin sane kasancewar shi mutumin, babban ɗan kasuwane wanda baima cika zama acikin garin nan ba, to tuni Ali keson ganin mutumin se saɓani ya shiga tsakaninsu se jiya Allah yay sukai magana ta waya wanda suka aje yau xasu haɗu wajan ƙarfe 8:00am wannan dalilin yasa yay sammako daga gida zuwa nan ɗin.
Abakin gate ɗin gidan mutumin yay parking tare da fito da wayarsa, ya kirashi cikin ƙanƙanin lokaci mutumin ya fito wanda ze ɗan girmewa Aliyu da kaɗan domin shi ze sa'an ya umar, gaban motar Aliyun ya bude ya shiga tare da sallama cikin mutuntaka sukai gaisuwar girma sannan suka soma maganar data shafesu wadda kusan duk akan harkar kasuwancin sune.
Sun kai kusan a wannin biyu sannan sukai sallama Alhaji Aminu wanda Alin yaje wajansa ya fito daga motar shikuma Aliyu yaja motar ya tafi.
Seda ya biya ta wajan Abokan kasuwancinsu na wasu garuruwan da usman ya gaiyata ɗaurin aure to suna nan basu tafi ba, se zuwa anjima wanda usman ya kama musu wani hotel anan dai duk hanyar nasarawar, ya ɗan ɓata lokaci a wajansu suna gaisawa sannan ya kamo hanyar gida bayan sunyi sallama.dasu.
Agajiye ya shigar da motar wajan adana motoci lokacin wajan ƙarfe ɗayan rana dan anata kiraye kirayen sallar azahar a wasu masallatan.
Da harya nufi hanyar sashen ammi seya tuna seya juya ya nufi hanyarshi yanajin ranshi duk

babu wani daɗi sallama yay a babban falon gidan nashi bayan ya bude kofar falon.
Tsitt gidan yake kamar babu bil adam acikinshi.
Daman ita khadija tunda tai sallar asubahi ta koma ta kwanta bata farkaba seda yayarta anty Ruma, da sauran dangi suka shigo wajan nata sannan ta yunƙura taje bathroom ta kuma gasa jikinta sannan taɗanji dama, kaya ta sauya sannan ta fita falon anan suka gaggaisa da ƴan uwanta, cikin haka ammi ta aiko su hassana da kayan break fast, tare da yayarta da sauran ƴan uwanta waɗanda suke cousins ne sukai break ɗin sannan suka taimaka mata wajan gyara gidan abinda ya dace a fitar suka fidda, har wajan 12 suna gidan sun jima kafin suyi mata sallama akan zasu wuce, duk da yawancin su ƴammatane kuma duk anan gidan suke sedai bam bancin part dakuma ƴar tazarar tafiya.
Seda kowa ya sauka sannan anty ruma ta dawo da baya.
"Dija ina Haidar ɗinne ai ya leƙo mu gaisa dashi tunda yasan ni ba,a nan nake ba, anjima kaɗan abbansu nasma zezo mu wuce".
Rau-rau tai da idanunta.
"Nima ina nasan inda yay"
Tafaɗawa Anty ruman haka kanta tsaye.
( Take Note: dan Allah ƴan uwa mata ku dinga rufa asirin aurenku ba komai xakana budewa ba dole akwai rufin asiri tare da riƙe sirrin juna sabida kowa yasan mata da miji se Allah, kar ƴan uwanki ko ƙawarki suzo ki kwashe sirrinki da oga na daɗi da rashin sa ki gaya musu sabida gudun husuma Allah rufa asiri amin )
Gyara tsaiwa anty ruman tayi.
"Kar dai kicemin bai ratsaki ba jiya, a ƙa'ida kowani ango yana ririta amaryarsa idan ankawota kada kicemin baki sami hakan daga wajanshi ba?".
Kukane ya tawo mata still tana kallon anty ruma.
"Wallahi anty jiya yaymin cin kaca amman tunda ya sakani acikin ruwan ɗumi bai kuma waigena ba, shima kuma nasan dan uwarshi tace yayi ne da baze ba".
Turo ɗankwali gaba Anty ruma tai.
"Aikin banza yagama haukansa dan ubanshi semun saitashi waya gaya mishi ɗiyan hajiya rabi suna boranci".
Tana faɗin haka ta kwashe da dariya.
"Nifa babban burina ki haihu dashi a farkoma kisami maza ƴan biyu fatanmu kenan sabida arzkin ya shigo zuri'ar marigayi yusufa mai atamfa amman dan jaraba akaf dangi su kaɗaine masu dashi komai sedai su".
Share hawaye khadijan tai.
"Nima dai anty ada bana kawo wannan tunanin wanda umma take nunan amman tundaga ranar da mukai.kamu da kuma jiya dana shigo cikin gidannan naga yadda aka narka dukiyar bati wallahi se komai ya sauyamin tabbas anty zuri'ar abba idiris akwai kuɗi wallahi bakiji yadda kaina ya girma ba jiya danaji wai dani aka ɗaura auren Aliyu shalelen abba wanda nasan komai na abba Aliyu ne a farko, kai Allah ya saka Alhaji babba acikin aljanna firdausi amin".
Dariya anty ruma tai.
"To ba wannan ba mudai fatanmu kiyi ciki hajiya ki aje komai ki kamashi da kirsa kinsan tafi bin malamai ci a yanzu karki sake ki nuna fushi akansa ki dinga nuna masa kefa sonshi kike kamar ki zauce insha Allah nan da ƴan satikai zamu somajin kakarin amai".

Tafaɗa tana buɗa!!!
"Anty ammanfa akwai matsala".Tafaɗa tana kallonta.
"Tame kuma?".
Ruman ta faɗi a gajarce.
"Anty inaganin fa wannan infection ɗin bai barni ba, daman nagayawa umma nace mata mu soma maganin sanyi kafin na matan nan amma umma taƙi wallahi jiya tunda ya soma babu wani show se azaba gabana kamar an saka reza yanzu haka ƙaiƙai nakaji".
Tafaɗa cikin rashin kunya da tsantsar jaraba.
"Wannan babu matsala ki dinga jiƙa kanunfari kina sha sannan xan haɗo miki wasu, daman ai gangancine yanzu ƴammata su fara amfani da maganin mata batare dasun nemi na sanyiba ayayin gabatowar biki,sabida duk maganin matan dazasu sha matsawar sanyi bai kauba tofa akwai case".
Anty ruma ta faɗa tana ƙoƙarin fita daga falon.
"Kindai ji duk huɗubata karnaji karnaga kinji ko?".
Tafaɗa tana fita daga falon ta sauka ƙasa khadijan na take mata baya, ko aƙasan ma sun jima suna tattaunawa anty ruma tana kara hau da ita kan network kafin suyi sallama, akan ragowar zancen sayi a waya, tana komawa samanta kwanciyarta tai, bata tashiba seda akai kiran sallar karfe ɗaya sannan ta mike ta shiga toilet tai alwala tazo tai sallah, sannan ta shirya kanta cikin haɗaɗɗun kaya tai ɓarin turaruka ta xauna gefen gado tana latsa wayar hannunta data ɗauka a gefen madubi.
 Jin kamar sallamarshi a babban falon saman yasata ƙara gyarawa sosai, tare da fesa turare cikin yauƙi ta fito muryarta kamar zuma tana amsa mishi sallamar.
Sanye take cikin haɗaɗɗen leshi wanda yaji uban stone har ƙasa anyi mata ɗinkin bubu, bakaramin kyau tai ba, abinka da farar fata, gabansa ta nufa wanda yake kokarin jan handle ɗin bedroom ɗinshi ze shiga, hannunta ta ɗora akan nashi tana ɗan jan gashin saman hannun nashi cike da salo.
"Barka da zuwa my cwt man amman wallahi nai fushi se yanzu ka dawo".
Tafaɗa a raunane kamar xatai kuka dan tsabar kirsa.
Mamaki yarinyar ta bashi ahaka bazaka ɗauka ko (A)khadija zata iya faɗi ba, idan ka cire tsabar iyayinta wanda tun tana karama take da shi amman seya basar yana mata.kallon ƙasan ido mai cike da izza, aranshi yana jinjina kawaicinta.
Ƙarasa buɗe ƙofar yay ya shiga ta bishi a baya tana ɗan dira kafarta alamun shagwaɓa"baka cemin komai ba?".
Tafaɗa.
Haɗe ranshi yay tamau tare da tsareta da idonshi wanda yay ja kaɗan.
"Ina neman afuwanki akan abinda nai miki jiya a ƙa'ida ya dace na zauna na baki kulawa a matsayinki na amarya kuma wadda ta kawo budurcinta cikin daraja, sedai wani uziri daya sha kaina yasa banyi hakan ba, ina fatan zaki fahimceni".
Yafaɗa idanunshi kafe akanta.
Wani irin sanyi taji har ranta jitake kamar su dauwama ahaka.
"Na yafe maka yayana daman can ban rike kaba".
"Nagode".
Yafaɗi hakan yana nufar ƙofar bathroom tare da shiga ciki ya rufo kofar yabarta anan a dashe.

Cike da ƙwarin gwiwa itama ta fita daga ɗakin tare da shiga kicin domin sarrafa masa abinda zeci...............( Tofa   anya khadija xata bar kofar Bebi muje zuwa  )

*******************

Se wajan ƙarfe uku hussaina ta sauke alalen daga wuta..............

[ _afuwan jiya nai mistake number xan saka 53-54 sena saka 52-53 se kawai na soke na bar na jiya a 53 kaɗai yau ga 54 kuji daɗinku ina yinku my fans_ ]

*INA ƘARA GAYA MUKU DUK SANDA KUKAJI SHURU KUMIN UZURI INA TARE DA MARAR LAFIYA TO LOKACIN TYPING BAI DA YAWA AFUWAN MASOYA WANNAN LABARI YA WUCE INDA KUKA KAISHI KUDAI KUCIGABA DA SUBURBUƊO MIN CMNT KOTA INA KUCIKAMIN WAYA NIKUMA IN CIGABA DA BAKU NISHAƊI INSHA ALLAH*

*AUREN BARE !!*🌹
{  _HOT LOVE_  }

NA
*AUTAR MANYA*

_Writter of_
*ƊAN MAJALISSA*
*H A S K E*
*KOBA SO DA AKWAI KAUNA*
*RABON WANI*

*DA IZZATA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*55*

Juyoshi tayi baki ɗaya acikin madai-daicin farin bokiti sannan ta juye manjan cikin ɗan kwanon suyar mai, ta ɗorashi akan gaushin wuta, minti biyu manjan ya soyu, seda ta fara miƙowa mama alalen sannan ta koma ta ɗauko kwanon suyar man wanda seda tayi amfani da ƙyalle kafin ta ɗauko sabida gudun ƙonewa.
Kwanikan cin abincinsu, ta ɗauko duka acikin ƙaton faranti ta jero sannan ta koma gaban mama ta ajesu itama ta nemi guri ta zauna.
"Sannunki Allah yay miki albarka ya baki masu yi miki kamar yadda kikai min".
Mama tafaɗa cikin nutsuwa, kana ta buɗe marufin bokitin.
"Bani farantin ku, seki bani kwanika biyu".
Cikin bin umarninta hussaina ta miko mata ƙaton farantin da sukecin abincin, sannan ta kuma miƙo mata wasu kwanikan guda biyu, kamar yadda ta buƙata.
Dai-dai yadda zasu ƙoshi ta zuba musu sannan, ta zubawa shahid nashi,itama ta zuba, Bebi ta sami bacci dan haka seta bar mata nata cikin bokitin.
Manja ta zuzzuba musu wadatacce yaji ko, tura musu tayi tana cewa............
"To dai kuyi a hankali wallahi babu ni a rakiyar ban ɗaki".
Dariya! dukkansu suka kwashe da ita musamman hussaina wadda har ƙwarewa take dan dariya, kafin kuma ihsan tace.
"Daman mama aimu bama zabga yaji acikin abinci wannan se Bebi gata kuma da ɓataccen ciki daga taci  se gudu zuwa masai".
Dariya duka suka kuma kwashewa da ita.
"Nidai babu ruwana kinsan ta sarai kotana ciwo bata raina masifa dan haka kiyi kina sani".
Mama tafaɗa cike da barkwanci, wannan hali na mama yana burge ƴaƴanta sabida mama mace'ce wadda tasan haƙƙin yaranta sam bata nuna bam-banci ko wariya, a tsakaninsu tana bawa kowannen su haƙƙinshi, bata matsa musu wajan ƙwauran abinci, ko suttura muddin kaga mama bataiwa su Bebi abu ba tofa sedai, bata dashi, amman ankon maulidi kayan sallah, duka basa wuce su haka nan kuma idan tana camama zata ɗan siyo musu namansu ko kifi adafa kowa yaci, mama takan hana kanta wani abun domin ƴaƴanta, wani zubin har tausayi take basu idan zatai musu wani abun wannan dalilin yasa basa takura mata akan tai musu kaza-ko kaza sabida sun san tana iyakacin bakin ƙoƙarinta indai Allah ya hore mata.
Danma yanzu Alhamdulillahi shahid yana ɗaukewa kanshi wasu abubuwan dan wataran da ribar gawayinshi ma suke cefane, da sauran sabgogin cikin gida,wannan dalilin yasa kowanne acikin yaran nata burinshi ya taimaketa sabida yadda itama take zage damtse wajan tallafa musu duk da maraicinsu amman bata  bari sunyi kuka! ba sannan bata bar rayuwarsu ta salwanta ba, domin inda wata uwarce yadda ƴaƴan nata suke duk mata kuma.masu kyau da tuni ta bude hannun jari dasu Allah ya kyauta.
"Mama aini yadda naga Bebi ma jiya tana rawar ɗari wallahi ban ɗauka yau xata iya zuwa asibiti

ba".
Hassana tafaɗi tana kokarin kai loma bakinta
"To kuyi shuru muci abinci kar amanta da ambaton sunan ubangiji mai girma tare da korar shaiɗan".
Mama ta faɗa cikin bada umarni.
Tsitt tsakar gidan yay babu abinda kakeji se sautin taunar su cikin nutsuwa.
Sun ɗan jima suna cin abincinsu kafin su kammala arfa ƴar ƙarama ita ta ɗauke farantin takai gaban rariya ta zuba omo ta wanke tass.
Suko su hussaina wanko hannayen su sukai tare da nufar ɗaki sabida yau zasu kaiwa gidan baba lado( malam ) ziyara sabida kwana biyu talle bai barsu sunje gaidasu baba'ba.
Hassana ita ta fara shiga wanka bayan ta fito ta ɗauro alwalar sallar la'asar  sannan hussaina itama ta shiga.
Saman tabarma hassana ta zauna tana shafa mai.
Mama kuma tana kuncewa ihsan ɗaurin zanin datai na baya wanda yaƙi suntuwa ta sauƙi, sabida itama maman tagama cin alalen nata harta wanke hannunta tasha ruwa tare da godiya ga sarki Allah.
Sallama sukaji daga soro cikin ɗan ɗaga murya kaɗan mama take amsa sallamar kafin taga yara kimanin guda uku.
Suna shigowa da manyan buhunan shinkafa guda biyu, juyawa sukai cikin sauri sega wasu kwalayen nan na macaroni guda uku taliya uku jarkar manja data man gyaɗa manya ɗai ɗai, se manyan ledoji,guda uku abinka da ƙaramin gida nan da nan tsakar gidan ya cika da kaya.
Mama sakin baki tayi tana kallon ƙudirar ubangiji haka zalika sauran ƴaƴanta ma haka.
Yaran dasuka shigo da kayan abincin ne suka juya suka fita.
Cikin izza da taƙama baba tasi'u da rabi'u suka shigo gidan ko sallama babu, gaban mama ne ya faɗi amman seta daure bata nuna firgicinta a fili ba.
Seda ƙyar kamar an musu dole tasi'un yay sallama tare da tsayawa a tsakar gidan yana bin ko ina da kallo yana ƙyafe bakinshi kamar yaga gashi.
Cikin gadara da nuna isa irinta wasu dangin uban  Rabiu ya laluba aljihun wandon jikinshi.
Sabbin ƴan dubu dubu ne ƙarr kamar yanzu aka bugosu kimanin naira dubu ɗari biyu, ya fito dasu waje tare da watsawa mama su a saman fuskarta, "ga sadakin gantalalliyar ƴarki nan a matsayin mu na dangin mahaifinta shaƙiƙansa, mun zauna munyi nazari da yawon ta zubar ɗin datake gudun karta ɗauko mana abin kunya yasa mukai mata miji nan da sati ɗaya tall rana mai kamar ta yau zamuzo nan ƙofar gidan mu ɗaura mata aure, suma waɗannan ƴan biyun na gabanki mun baki nan da wasu gajerun lokuta maza ki nemo musu mazajen aure idan ba hakaba tabbas  zamu haɗasu da koma suwaye , ga kayan abinci nan inji sirikinmu uban mijin ƴarki yace abaki mota guda ya bamu muka raba gida biyar muka baki kaso ɗaya dan kici arzikin, sannan abu nagaba ki saita ƴarki sabida yaron ze zo anjima ya ganta duk abinda ya nema wajanta kartai masa musu domin shiɗin ɗan madarane baison wahala ba babu kuma irin gatan da ubansa Alhaji isa mai gwal bai mishi ba dan haka ku taka a sannu mun barki lafiya".
Gaba ɗaya kan mama ya daure tunaninta ya tsaya cak, wasu keson yiwa aure da ɗan gidan Alhaji isa mai gwall wanda babu wanda bai sanshi ba afaɗin anguwar sharaɗa mutumin da baida mutuncin baisan darajar talaka ba, koda ba shige shige take ba amman labarin shaiɗancin yaron Alhaji isan babu kalan wanda basaji a wajan matasan anguwar hatta shahid

yana yawan bata labarin ɗan gidan alhaji isan dan ma tana taka masa burki ne to tayaya ma suka san alhaji isan har suka haɗa ɗanshi aure da ƴarta sannan su yaya basu bawa ƴaƴansu sun aura ba se nata ƴaƴan?
"Nifa ban fahimta ba wai dawa kuke son haɗin wannan aure ne tasi'u karku saka ƙafa a ƙofar gidan nan harse kun ɗauke waɗannan kayan dan ban bukatarsu".
Dariya ya kece da ita.
"Dawa kwa xasu dace ban da BALKI wadda nagani ta sauka daga mota rannan ai tunda tambaɗɗɗiya ce to ga dai dai itanan na samo mata sabida haka idanma bakida labarin Khaleefah Mai shanawa! kije ki nema sabida ki shirya yadda yarki xata zauna dashi mudai mun gama namu sauran ke"!
"Dakata! Tasi'u!!!"
Mama tafaɗa da ƙarfi wanda sautin muryarta ya tayar da Bebi a firgice ta mike tana raba idon rashin sanin abinda yake faruwa su hussaina ko kuka kawai suke duk jikinsu yay sanyi.
"Babu wanda ya isa yay wa BeBI auren dole ama rasa da wa za,a haɗamin ƴa seda wannan ragowar cutar ƙanjamau ɗin waye bai san maishanawa ba tayaya zaka ɗaukoshi ka haɗashi da Bebi na rantse duk toshiyar bakinda macucin ubansu ze baku bata isa tasa na bashi ƴata ba kuma ku ɗaukemin waɗannan kayan daga gabana tun kafin mu raba abin faɗa".
mama tafaɗa cikin ƙaraji!

"Hahahaha"!!
Sautin dariyarsu.
"Bamuda lokacin ki Aisha inma zaki mike muci arziki tare to in kuma zaki tsaya gaddama ne to muzuba mugani kinsan taƙadirancin mu haka zalika kinsan muɗin kosu waye mu zuba mudake rana ita yau zata bayyana kanta"!!

Kaɗa babbar rigarsu sukai suka fice tare da turo yaran ɗazu suka kwashe masu kayan da suka zo dasu.
Da baya tasi'u ya dawo ya kwashe kudin auren.
"Bazama mu baki komai ba matsiyaciya kuma wallahi semun ɗaura wannan aure kozaki mutu...................

_MEKUKE TUNANI_ ?

*INA JIRAN SHARHINKU*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*56*

Da baya mama taja tana dafe bango kafin kuma ta zube a ƙasa tana fidda numfashi sama-sama, tanayi tana jan wata irin ajiyar zuciya mai ƙarfi,cikin tashin hankali duka yaran nata sukayo kanta suna kuka! ɗagota hassana tayi tare da aza kanta bisa cinyarta, Bebi wadda taji dukkan zazzaɓin jikinta ya sauka sabida ganin halin da mamansu keciki ita take kiran sunan maman.
"Mama dan Allah kidaina wannan ajiyar zuciyar kar wata cutar ta kama mana ke mama ke kaɗaice garemu".
Kuka! Suke suna kallon mahaifiyar tasu wadda babu abinda take face faman sakin ajiyar zuciya ta jima ahaka kafin tabi hussaina da kallo.
"Maza ki ɗebomin ruwa nasha innalillahi'wa'inna'ilahirraju'un"! maman ke faman faɗi afili tunma kafin takai Bebi tariga hussaina isa gaban randa kofi ta saka ciki ta kindimo ruwa tazo gaban mama ta tsugunna tana zubar da ƙwallah ta miƙa mata.
Seda tasha sosai sannan ta miƙe daga jikin hassana ta shiga ɗaki minti ɗaya ta fito ɗauke da mayafi da kallo tabisu.
"Zanje gidan malam ku gyara gidan kafin na dawo".
Tana gama faɗin hakan ta fita ranta duk babu daɗi duk jikinsu babu daɗi suka bita da "to".
Da sauri Bebi taja mayafin ihsan ɗan ƙarami ta yafa a saman doguwar rigar jikinta tabi bayan mama cikin ɗaga murya hassana tana kiranta akan tazo ta sauya mayafin sabida ko bayanta bai rufe ba amman sam taƙi dawowa.
Abaya abaya takebin mama ko tafiyarta ma a hankali takeyinta har mama ta shiga gidan malam wanda lokacin ana gab da kiran sallar magariba ne domin malam lado ma yana kofar gida yana alwala ze shiga masallaci dalilin dayasa mama bata kulashiba ma kenan dan haka ta shige gidan.
Sallama mama tayi acikin gidan bayan ta shiga.
Babace ta fito daga banɗaki hannunta rike da buta tana amsawa mama sallamar cikin karamci.
"A,a maman biyu kece da magaribar nan to lale maraba shigo kiyi alwala malam ɗin yana waje".
Baba tafaɗa tana kokarin ɗaukowa mama tabarmar dake jingine a gefe ɗaya.
"Eh! Naganshi ai awaje shiyasa banyi mishi magana ba nima bara nayi alwalar"
"To ƙaraso a,a wanake gani kamar mai gado? kice tare kuke da ita?".
Cewar baba......

Se asannan mama ta lura da bebi wadda take buya a lokon tsakar gidan.
Girgiza kai kurum mama tayi tarasa wannan ƙulafuci na bebi.
Zama Bebi tayi akan tabarma sabida tana fashin sallah gobe dai take saka ran wanka tunda ya ɗauke, ita kuma maman ta ɗauki buta ta shiga banɗaki domin ɗauro alwala.
Bayan ta fito ta shiga ɗakin baba tai sallah.
Bayan sun idar  baba ta fito musu da fitila ta aje itama maman ta fito waje kusada bebi ta zauna, mintuna kaɗan baba ta dawo hannunta ɗauke da kwano wanda ta zubo musu tuwo a saman kwanon se miya a ƙasa.
Direwa tai tana cewa..........
"To mai gado ga tuwon baba tunda kwana biyu kinƙi zuwa bare kici abokiyar faɗa".
Dariya! mama tai kaɗan.
"Ai mutuniyar taki babu lafiyane kwana biyu anyi zazzaɓi gakuma makaranta data koma sabida, taƙi bin ƴan uwan nata".
Ɗan sauya fuska baba tai.
"Allah sarki ai banida labari da banzo dubiya ba, abinka da mai garin jiki bata faɗa ba sedai idanunta daya zurma ciki kaɗan".
Nan dai suka cigaba da tattaunawa ita kuwa Bebi jan kwanon tai gabanta, tare da tashi ta wanko hannunta tazo ta zauna ta bude tuwone miyar kuka babu wata wata tasoma cin abinta sabida daman kwana biyu bataci abinci ba, duk da bata ƙaunar tuwo amman tana son tuwon bana yana mata daɗi.matuƙa.
Sallamar malam lado ita tasaka suka tsagaita da hirar tasu.
Cikin sakin fuska tare da mutun taka malam ya ƙaraso suka gaisa da mama sannan tace.
"Daman wajanka nazo".
Murmushi yayi irin nasu na manya sannan yace.
"To'to shigo daga ciki Aishatu, Ince dai yaran duka lafiya?". yamike ya shiga ɗakin nashi tare da kunna fitilar wayarshi.
Miƙewa tai tana cewa "Lafiya ƙalau muke wallahi".
Ta bishi cikin ɗakin.
Zama tayi agaban malam suka kuma gaisawa sosai sannan ta kalleshi cikin nutsuwa ta wassafa mishi duk abinda ya faru tass bata raga ba kuma bata ƙara ba.
Seda yagama jin duk abinda ta faɗi sannan yace.
"Banyi mamakin abinda sukai ba sabida suɗin marasa kunya ne to inba rashin kunya ba tayaya, se bayan da kika gama wahalar ƴaƴanki sannan suzo suce zasu miki ƙarfa-ƙarfa akansu ina baze yuwu ba, wannama maganar banza da wofi ce Aishatu".
Yafaɗa yana hucin takaici.
"Ni duk bama wannan ba malam kasan dawa suke kokarin haɗata?, wai ɗan gidan Alhaji mai gwall na nan bakin sharaɗa".
Cikin sauri malam ya xaro idanunshi.
"Wannan yaron mara kunya Allah ya kiyaye ki bari gobe insha Allahu zanje can ƴan kusan wajansu muyi magana duk yadda muke ciki sena gaya miki".
Da kallon tausayi tabi dattijon.
"A,a malam ka bari zan nemesu ai bakaje da tsufanka canba haba ai kaine gaba damu".
Murmushi yay.

"Babu komai ki bari dai Aishatu Allah ya shiga lamarin namu amin, sekuma maganar ƴan uwan nata ina dai kinsan da wasiyar marigayi ko?".
Jim mama tai cike kuma da ƙarfin gwigwa tace.
"Na sani malam hassana daman ita Aminu aka baiwa ita kuma hussaina nura ai maganarsu tana nan mun bari zuwa karshen shekarane kafin nan kaga duk yaran sun kammala bautar ƙasarsu se ai magana, tunda kaga iya mazan nema suka sani amman ƴan biyun ma basu sani ba".
Cikin gamsuwa yace.
"To madallah babu komai Allah ya kaimu lokacin Allah ya rufa asiri amin".
Sallama sukai sannan ta fito tsakar gida tanaiwa baba sallama Bebi harta soma bacci mama ta tayar da ita "Karfe takwas na dare kin soma bacci maza muje gida".
Sallama sukai da baba suka fita bayan sun ƙarƙare da malam akan gobe  zeje can ƴan kusan ainihin gidansu mahaifin Bebin inda su tasi'un suke ciki yaje akan soke maganar  auran da suka zo dashi.
Tafiya suke ga garin babu nepa ko ina duhu adai dai gidansu sadiya Bebi ta coke"Mama dan Allah zanje gidan iya sabida maganar ankon maulidinmu kinga kwana biyu banje makaranta ba kar naje ko an fitar bana nan".
Tafaɗa tana kokarin shiga gidan.
"To kada ki daɗe kinji ko sannan kar kicewa iya tare muke sabida ni bazan shiga ba nasan na shiga gidan se wajan goma zan fito".
Mama ta faɗi tana wucewa, ita kuma Bebi ta shige gidan aguje!.......

***********
Yajima acikin bathroom ɗin yana wanke jikinshi..........

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*57*

Kafin ya ɗauro babban tawul a ƙugunshi, kayan jikinshi kuma daya tube ya zubasu acikin washing maching, fitowa yay jikinshi na zubda ruwa sabida baiyi amfani da ƙaramin tawul na

goge jiki ba,gaban ƙaton dressing mirrow'n shi ya tsaya tare da miƙa hannu cikin jerin cream's ɗin dake shaƙe bisa gaban mirrown agurguje ya ɗauki wanda yake using dashi ya goga a saman golden skin ɗinshi mai ɗauke da wani irin laushi da sulɓi, body perfumes ya fesa ajikinshi, gaban close set ɗinshi ya ƙarasa tare da ɗauko wani milk ɗin yadin tisue tare da singlet and boxer, shirya kanshi yay cikin yadin mai ɗauke da ɗinkin tazarce wanda yazo mishi har gaba da ƙwaurinshi, sabida shara-sharan yadin yasa har ana iya hango white singlet ɗin dake jikinshi, seda ya kuma yiwa kanshi ɓarin perf kana ya zira black shoe mai rufewar sama ya ɗibi wayoyinshi tare da makullin motarshi ya fita daga cikin bedroom ɗin lokacin ana ƙoƙarin tayar da sallar azahar domin yaji ƙarar loudspeaker masallacin cikin gidan nasu.
A daining area ya aje makullin haɗi da wayoyinshi da sauri ya sauka down stair har yana gudu sabida jin ana tayar da sallah, abakin famfon ƙofar part ɗinshi yay alwala da sauri ya nufi cikin masallacin tare da bin sahun jam'in sallar, Cikin nutsuwa suka gabatar da sallar azahar, bayan sun idar yajima yana addu'oinshi kafin ya nufi part ɗinshi upstair ya haye bakinshi ɗauke da sallama, Cikin azama khadija dake cikin kicin taɗan leƙo da kanta cike da mamakin yaushe ya fita? amman se bata nuna mishi mamakin nata ba, ganin saman goshinsa da ƴar ƙasa alamun sallah yayi yasa ta fito baki ɗaya daga kicin ɗin hannunta ɗauke da ludayin datake juya miyar cabbage ɗin datakeyi sannu da zuwa tai mishi kafin ta koma kicin ɗin.
Tunda ya hauro saman mayen ƙamshin girkinta yagama cika mishi hanci sosai ƙamshin girkin nata yay mugun fisgar tunaninshi, wata irin muguwar tsohuwar yunwar dayay ta dakonta ce take taso mashi, Cike da kasala ya ƙarasa gaban daining site ɗin ya ɗauke makullinshi da wayoyinshi saman three seater yazo ya baje yana shaƙar ƙamshin girkin nata wanda azahiri ka dubi face ɗinshi bakka cewa wai shaƙar ƙamshin yakeyi amman shi can cikin zuciyarshi shikaɗai yasan yadda yake son yaga mema take dafawar, daman last time bayan dawowarshi daga uk usman ya taɓa cemasa khadija ta iya girki sabida time to time tana kamawa ammi, amman seya gwasale usman ɗin bai bawa maganar mahimmanci ba, To seyanzu daya shigo ya tarar tana girkin dakuma yadda mugun ƙamshin girkin nata yagama kashe mishi hancinshi yasa yasoma gasgata zancen usman ɗin duk da baya tunanin ko ze iya kai lomar abincin nata cikin bakin shi.
Kwanciyar rigingine yay kanshi yana kallon white rufin pop ɗin falon nashi while hannunshi guda yay matashi dashi, ɗayan kuma ya rufe idanunshi dashi.
Yay kusan minti talatin ahaka, kafin yaji daddaɗar muryarta wadda aka haɗata da iyayi akai mata kwas-kwas ta doki cikin dodon kunnenshi.
"Assalamu Alaika habibina na barka kai ɗaya afuwan".
Tafaɗa tana haɗe hannayenta duka biyun waje ɗaya, abinda yasa adukkan lamuranta take aro muguwar nutsuwa idan agabanshi ne sabida tasan shiɗin oga cin ubaka ne, bayason baragada abu kaɗan zaka masa ya kai maka hannu.
Ɗago da mayun idanunshi yay waɗanda suke saka marar jin magana saurin nutsuwa.
Ya zuba matasu, wanda sauran kaɗan ta shiɗe sabida zautuwa.
Can cikin ƙasan maƙoshin sa ya furta.
"Jeki sallah".
Kana ya mayarda idanun nashi ruf ya rufe kamar bashi yay maganar ba.
Jikinta har yana rawa wajan nufar hanyar bedroom ɗinta sam kaifin idanunshi ya mantar ta cewar tayi sallar harseda takai ga shiga cikin room ɗin nata sannan, ta tuna ganin sallayar datai

sallar a shinfiɗe bata ninke ba.
Sintiri ta somayi acikin katafaren ɗakin nata wanda aka narka dukiya cikinsa.
Har wajan mintuna biyar tana faman saƙa da warwara acikin zuciyarta na yadda zata siye zuciyar Aliyu, batare data bar ƙofar wata ƴa mace ta shigo cikinta ba.
Sannan kuma tanason ta jawo hankalinshi zuwa gareta domin har yanzu bin umarnin ammi kaɗai, take gani acikin idanunshi amman bata ganin ƙwayar soyayyarta ko guda acikin idanun nashi, tofa sedai da gaske domin ta jawo hankalinshi gareta babban burinta yau ai second round ko Allah zesa ya bata kulawa kamar yadda ya kamata.
Jin kamar ƙaurin miyarta yasa tai saurin fita aguje, batabi ta cikin falon ba, setabi ta gefen kujerun har ta isa kicin ɗin nata cikin zafin nama ta sauke miyar, tata wadda ta wadata kayan lambu da nama acikinta, farar shinkafar data fara gamawa wadda ta adanata acikin katon flaks mai kyau ita ta ɗauko ta aza bisa babban farantin jera kayan abinci sannan ta ɗauko karami nanma ta zuba miyar, plate na cin abinci ta ɗiba guda biyu se saving spoon tare da spoon guda biyu se glass cup guda biyu duk haka ta jerasu akan babban farantin, ta nufi cikin falon bakinta ɗauke da sallama, akan center carfet ɗin falon, ta soma ajewa, kana ta mike a nitse zuwa daining area ta ɗauko ledar shinfiɗawa a saman carfet wadda akecin abinci akanta ta soma bazawa tsakiyar falon a hankali ta gama ta soma kwaso flaks da sauran kayan abincin ta jeresu reras tai decorating ɗinsu gwanin sha'awa.
Tsira mishi idanu tai aranta tana ayyana.
Ali xaki nawa ga tsoro ga ban tsoro nagama girkinnan amman na rasa yadda xanyi.
Gyaran murya tai! cike da salo takai hannunta dai dai saman yatsarsa guda tajashi daɗan ƙarfi, duk abinda take yana kallonta ta witsiyar idanunshi yana kuma mamakin yadda batada kawaici wajan miji.
"Habibi wake up food is ready!!." tafaɗa cike da salo.
Gyarawa yay yaɗan ɗago kaɗan yana ayyana ze saita mata burki.
Ɗago mata jajayen idanunshi yay yana kallonta dasu waɗanda suka gama cika da xallar gajiya tare da bacci.
"Barni dan Allah bacci zanyi".
Da sauri taga ya koma ya kwanta.
"H........., bai barta takaiba yaɗan ɗago da hargagi.
"I said leave m......,Bata gamajin hargagin nashiba ta miƙe tai ɗaki jikinta na shacking, tana ayyana tsananin masifarshi wataran.
Tsaki yaja da ƙarfi aranshi yana cewa....
Yarinya se jaraba jibeta kamar tsinke amman jitake kamar ta cinyeni, bazanma ci abincin nakiba bare ki lalubeni ki kuma min illah cikin dare( hoho Aliyu ɗan duniya kunjifa takuma masa illah cikin dare bama yay mata ba! Umm khadija anemi maganin sanyi domin ki rama abinda Aliyu yace ).
Mirginawa yay baijima ba barci mai nauyi ya kwashe sa.
Bar farkaba se ana kokarin kiran sallar la'asar wannan al'adarshi ce duk yadda yakai ga bacci ana kiran sallah seya tashi.
Bakinshi ɗauke da salatin annabi muhammad (s.a.w)ya farka, sauko da kafafuwanshi yay dayakejin sun ƙage sabida yaywa kujerar tsaho, baibi takan wayoyinshi ba, room ɗinshi ya koma still watsa ruwa yay as usual, Ali kamar agwagwa yake dason wanka,Wannan karon

dakakken light blue ɗin yadin wagambari ya saka ɗinki half body, yaywa kanshi ɓarin ƙamshi ɗangaske, hular tangaran ya kafa akanshi mai kalar ruwan sararin samaniya itama seyay amfani da agogon zallar fata mai kusan shigen kalar kayan jikin nashi haka xalika takalmin dayasa ma kusan hakan, bakaramin mugun kyau guy ɗin yayba da gaske shigar ta amsheshi kamar wanda zashi gaisuwar surukanshi haka ya fita yana baza uban ƙamshi.
Yadda yabar komai na falon haka ya dawo ya tararsu wayoyinshi ya kwasa tare da car key ɗinshi, harya nufi sauka seya tuna, da sauri ya nufi hanyar room ɗinta.
Cikin nutsuwa, ya tura ƙofar bakinshi ɗauke da sallama.
Zaune take saman sopa tai tagumi abin duniya duk yagama yi mata yawa jin sallamarshi yasa ta miƙe a matukar tsorace.
Kokawa take da numfashinta sabida yadda yake mata barazanar ɗaukewa sakamakon tozali datai da gwarzon mijin nata wanda ya haɗa uban kyau mai cike da tsantsar kamala da haiba jitake kamar taje ta rungumeshi.
Jitake kamar ta dauwama ahaka tana kallonshi sakato tai da baki kamar wata sakarai tana kallonshi.
"Kin wani tsareni da ido kamar zaki cinyeni ni zan fita".
Yafaɗa a dake dominshi bai san lallashi ba kodan bai taɓa soyayyaba ne oho? shi ƙarewama ƴanmatan dake sonshi suke lallashin nashi.
Itako acikin ranta cewa take.......
Indama zan sami damar lashekan aida aikine mai sauƙi.
Amman afili seta ƙwaɓe fuska kamar zatai kuka tawani marai raice mai.
"Nayi maka abinci bakaci ba, Sannan kuma a ƙa'ida washe garin tariya ango ai bai fita".
Ɗage mata girarshi yay ta ƙasa kaɗan wadda ta saka khadija jada baya kaɗan tana ayyana you will kill me da wannan kallon naka.
"Hmmm inna zauna mizaki min tell me mizaki min Deejah?".
Yafaɗa dawani irin salo na yaudara yana ƙoƙarin cilla mata kaifafan idanunshi cikin nata wanda dasu yake gano weak ɗinta akanshi.
Wani irin armashi garsashi taji acikin dukkan sassan jikinta bata taɓa jin wanda ya kira sunanta da daɗi kamarsa ba wayyooo!! ze kasheni daso.
Tafaɗa aranta.
Amman a bayyane setace.
"Nidai...nidai...kaci abincin to".
tafaɗa rabe.
Murmushin dabai shirya ba yay mata yana noticing ɗin mood ɗin  datake ciki.
Ya hango tanada muguwar jaraba yarinyar domin ga ƙwayar idanunta nan harta harba sedai baya tunanin tana cikin jerin mata masu juriya domin daga jiya yaga zahiri.
"Bazanci abincinki ba, sabida yau ko break banyi ba nafita, so kuma bancin abinci kai tsaye dole sena ɗansha ruwan zafi, amman fa na yaba abincin naki dan naita haɗiyar miyau ɗazu sedai dole zanje wajan ammi tabani ruwan zafi nasha ko hanjina ya warware ni zan fita zanzo miki da kazarki ta jiya da ban kawo ba, ai min afuwa".
Yafaɗa direct sabida shi mutum ne sak! wanda bai rufa rufa ko gulma, sabida baya son barin abu cikin ranshi ko kaɗan.
Adashe yabarta harya fice bata zaunaba sema shaƙar mayen ƙamshinsa na gado datake.

Komawa tai ta zauna tana dafe saitin zuciyarta tare da matse cinyoyinta sabida azababben feeling ɗinshi datakeji dole yau yasan yaze kumayi da ita domin ai ita shuka seda ban ruwa.......
Wajan ammi yaje amman kafin nan seda ya leƙa part ɗin umman khadija ya gaisarta, tare da karɓar accnt number ɗinta yay mata transper ɗin kuɗi masu kauri akan ta sallami ƴan biki aikuwa umma baki har kunne ta baje tana godiya, aranta tana yanzu muka fara tatsarka tai tunanin duk daɗin ƴartane yasa yay mata wannan kyautar sedai daman can Ali mutum ne mai kyauta dason kyautatawa amman rashin zaman guri ɗaya yasa umman bata fahimci hakaba, kuma babban dalilin dayasa shi yi mata hakan sabida bin umarnin iyayenshi shikuma yaga baya iya tashi batare dayay mata ihsani ba shine yasa yay mata wannan kyautar amman ita umma ai ta girmama abin harda yiwa ant ruma waya bayan ta bata labari ta kira khadija wadda itama abin ya daure mata kanta, duk da tasan kyauta halinshi ce amman tai mamakin daya baiwa ummanta kuɗi kodai ya soma sonta ne? da wannan farin cikin ta ware taci tasha ta cigaba da sabgar tarbar angon nata a karo na biyu........daga wajan umman khadija masallaci ya koma yay sallar la'asar bayan yay amfani da famfon bakin masallacin yay alwala yana idarwa yay part ɗin iyayenshi.
Lokacin dayaje part ɗin ammi babu kowa cikin falon nata, dan haka seya wuce falon abba zama yay suka gaisa da abba, cikin hikima abba ke kara nusar dashi hakurin zaman aure tare da kyautatawa iyali hadɗi da fita haƙƙinsu sosai jikin Aliyu ya kuma yin sanyi duk da yana da ilimin hakan akanshi amman yadda mahaifin nashi yake kuma tunasar dashi yasa yakuma jin soyuwar mahaifin nashi acikin ranshi, Ahaka ammi tazo ta samesu itama zama tai suka gaisa dik da yunwar dake cinshi amman tsabar zurfin cikin tsiya ya hana yacewa ammi ta bashi abinci.
Seda ta haɗowa abba tea mai kayan kamshi sannan abban ya umarceta akan ta haɗowa Aliyun.
Aikuwa babu musu ya amsa bai dire cup ɗinba seda ya shanye tass gumi ya keto mishi hamdala yaywa ubangiji, sannan ya mayar da hankalinshi ga tv inda ake watso labarai a tashar cnn.
Suna hirarsu da iyayenshi suna kallonsu cikin hikima ammi take kara nausarshi tare da nuna mishi mahimmancin auren dayay.
Har akai magariba yana tare dasu kafin su miƙe da abba suka fita, zuwa masallaci sabida shi yana da alwalarshi abbane kawai yay suka shiga cikin masallacin.
Bayan an idar da sallah suka fito tare da abba yana adai dai parking space yake cewa abba ze fita yaje ya dawo addu'a abba yay mishi ya wuce.
Yana ƙoƙarin shiga cikin motar sega usman ya fito daga wajan part ɗinshi, da sauri ya karaso bai tsaya wata wataba ya bude ɗayan side ɗin ya faɗa yana cewa.
"My man kai ga kanga kuwa wannan sheƙi haka kodai kodai".
Haɗe rai yay yana tada motar.
"Malam nifa nisa nai dalla fitarmin a mota karka cikani da surutu"
Yafaɗa yana fisgar motar.
"Eh! nima fitar zan ɗanyi amman tunda na sami driver kawai sena huta driving na shigo taka marar kunya ai yanxu dai dai kake damu tunda kaji abinda mukaji".
Yafaɗa yana dariya.
Tsaki Aliyu yaja yana danna horn.

Cikin azama suka bude musu gate ɗin ya fita daga harabar gidan tare da hawa titi.
"Malam ina ka nufa? ni nasarawa magaji rumfa kai a ina zan sauke ka?".
Yafaɗa idanunshi tsaye bisa kwalta.
"Ni sharaɗa zaka saukeni zanje duba ƴan biyune sabida kwana biyu babu dambu madam ta riƙe wuta".
Tsaki! yaja tare da ƙarawa motar gudu...........
***********
Da sallama mama ta shiga cikin gidan nata ƴan biyu suna tsakar.........

*ANZO WAJAN DASU O'O SUKE SO*
_NAGAJI WALLAHI_
*NOTE EDITING AFUWAN*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*58*

Azaune a saman tabarma sune suke amsa mata sallamar gefe guda kuma suna yi mata sannu da zuwa.
Cikin kulawa take amsa musu tare da tube mayafin jikinta ta ratayeshi a saman igiyar tsakar gidan, sannan ta zauna agefen arfa wadda tana ganin mama ta zauna ta haye saman cinyarta tana shagwaɓar auta.
"Mama ina Bebi ko bata biki ba?".
Cewar hassana wadda ta miƙe domin zubowa mama tuwon daren dasuka gama tun ɗazu domin su tunima sunci nasu daga na mama sena Bebi da shahid wanda yake wajan gawayin shi.
"Tana gidan iya wai zata wajan mutuniyarta sadiya suyi magana akan ankon mauludi, tama gama abinta bana banida kuɗin anko  injima da hidimar saukarta mana".
Tuwon hassana ta kawo mata gabanta ta dire mata sannan ta koma ta ɗebo ruwa a kofi ta aje

matashi.
"Aikuwa dai mama dan saukar naji ance kuɗin allon nasuma yafi namu lokacin da mukai tsada fa".
Inji hussaina, wadda take riƙe da tourch light a hannunta tana haskawa mama tuwon gabanta wanda zata zuba miya cikinsa.
Sallama sukaji daga ƙofar gida,kafin kuma wani yaro ya leƙo da kansa.
"Assalamu Alaikum, wai ana  kiran Balki inji mijinta".
Yaron ya faɗa yana ƙoƙarin juya kanshi ya fita.
"Kaje kace ai babu balki agidan nan matar aure".
Cewar mama wadda ta dakata da cin tuwon nata.
Komawa yaron yay minti uku ya dawo.
"Wai inji khaleepha mai shanawa, ɗan gidan mai gwall yace kota fito koya shigo da kanshi ai matarshi ce".
Cikin tsananin takaici hussaina marar haƙuri tace.
"Kace masa ko ubansa isa ya sake ya shigo mana gida semun karyashi bare kuma shi, duk talaucinmu munsan darajar kammu".
Jinjina  kai mama tai kurum zuciyarta tana suya tabbas setai da gaske domin taga lamarin yana son zarmewa.
Komawa yaron yay ya sanarwa khaleepha wanda yake fake jikin black CRV ɗinshi wadda taci uban tind babu abinda ke tashi daga jikinshi se uban ƙaurin hayaƙin sigari dana giya wanda daga ganima daga tazubar ɗinshi ya nufo nan.
Tsaki yaja da ƙarfi, shi kanshi bawai son auren nan da dakus ɗinshi ze masa yake ba, sedai ga yadda yaga yarinyar last time zasu fita ita da yayinta yaji yana mugun sha'awarta yana son yaji kalan nata baiwar wannan dalilin nema yasa yay bincike akanta harya gane ƴar ƙanin yaron mahaifinshi ce tasi'u wanda yasan samun ta baze masa wuyaba tunda talakawa ne, baiyi ƙasa a gwiwaba ya sanar da dakus ɗinshi daman abinka da mai neman kukan da aka jefeshi da kashin awaki  dama khaleepha ya dameshi da kawo mata da shaye shayen kayan maye,ai tuni haji isa ya kirawo yaron shi tasi'u ya shigar da maganar ɗanshi abin sonshi cikin rawar jiki tasi'un yay na'am daman tunda yaga yarinyar ta tsaye mishi aranshi ya ɗagu daman ya samu su haɗata da ko wanine anan ƴan kusan sabida kyan yarinyar kar ya fisgi hankalin wani mai nerar yazo ya aureta uwarta,ta huta.
Tsakin ya kuma ja akaro na biyu ransa idan yay dubu ya ɓaci sintiri yake famanyi a kofar gidan jiyake kamar ya faɗa ciki bayajin yau ze iya bacci idan bai taɓa nonon yarinyar nan ba, sabida yadda zubin halittar ta ya tsaya mishi arai yana ƙoƙarin fiddo da wayarshi dan ya kira tasi'u yagaya mishi halin da ake ciki idan da halima ai ɗaurin auren nan gobe ko jibi danya nuna ƙarfin kuɗinsu babu abinda baze iya karɓo musu ba.
Hasken wata shegiyar haɗaɗɗiyar mota yagani wadda taiwa tasa gudun wuce sa'a a kuɗi yaga ta haske masa fuska kuma abin takaicin motar tana kallon saitin tasa ta riga ta bake wajan ga kuma lungun daman bawani mai girma ba.
Takaici biyune ya hade mishi sema ya kasa kiran wayar yana son yaga wani ɗan rainin wayon ne yazo ya tokareshi haka kamar hanyar ta ubanshi ce.
Cikin jin haushi Ali ya dubi usman "Na baka minti, Biyar Allah ka ƙara zan saita layi dan kasan inada abinyi" shiko usman tsabar mamakin brain ɗin Ali yake shifa koyasha giyar wake baze iya

kawo kanshi layin ba bare gidan amman tsabar fasaha da riƙe abu akai irin na Aliyu batare da tambaya ko shakkuba ya kawo su layin wanda tsabar ƙwarewama baibi dasu ta wancan layin na farko dasuka kasa shiga da mota ba, wannan karon ta bayan layin ya shiga inda suka samu babbar hanya har kofar gidan ya sami ƙarasawa da motar, sedai CRV ɗin da suka gani a ƙofar gidan yasa basu ƙarasa dab da gidan ba seyay parking daga ɗan gefe kaɗan, amman yarasa mai yasa Aliyun ya haske Crv ɗin?.
Fitowa usman yay yana cewa.
"Afuwan ango yanzu zan leƙa na fito".
Tsaki! Ali yaja yana mamakin shishshigi irin na usman yanzufa gidan yakeson shiga sekace na ubanshi bai kashe motar ba sema ƙara hasken fitilar motar tashi dayay tare da tsirawa waje ɗaya idanunshi.
Usman sallama yay a bakin soron gidan tare da ambatar sunan hassana.
Dayake babu wata tazara da tsakar gidan yasa mama jin sallamar dan haka ta ɗan ɗaga murya tana cewa.
"Waye?"
Batare data bar wani ya fita ba sabida tsaro, daman duk suna cikin damuwar lamarin wancan shaiɗanin yaron.
"Nine mama ɗanki usman mai dambu".
Yafaɗa cike da barkwanci.
Faɗaɗa far'arta tayi tana cewa.
"To hassana maza shinfiɗa masa sallaya acan shigo mana kaida gidanku".
Tafaɗa tana jan mayafinta wanda ta ciresa ɗazu ta rufe jikinta tsaff.
Sallama usman yay tare da shigowa ciki.
Zama yay akan sallayar yana gaida mama.
suma ƴan biyu dasu ihsan suka gaidashi tare da miƙewa suka bar wajan.
"Mama lafiya kwana biyu ƙannena basa fitowa, nima dayake na kwana biyu banje ba sabida anyi bikin wannan ƙanin nawa wanda mukazo dashi kwanaki, toseda na koma jiya malam salihu kecewa basa zuwa to Allah sadai ba laifi mukai ba?".
Yafaɗa cikin nutsuwa.
"Lahh ɗana wallahi babu komai kasan garin damuna se ahankali, amman insha Allah zasu dawo ne".
Sannan ta numfasa kana ta ɗora da cewa.......
"Allah sarki ashe biki kukai? to Allah yasanya alkairi aikuwa na shaidashi wannan marar maganar ko dakuka zo kwanakin baya?".
Dariya usman yay "Eh! fa shine to mama kinsan sha'anin biki duk gajiya ta hanamu, fita office ni se jiya na koma ma".
Murmushi mama tai tana yaba karamcin usman tare da saukin kanshi.
"Aikuwa dai abubuwan biki se hakuri yawa garesu, hassana! zoki kawo mishi tuwo"!
"lahh wallahi mama yau cikina a koshe yake amman watarana naci insha Allahu".
Hira suka cigaba dayi.da usman akan tsadar rayuwa da ake ciki wanda mama ta sake sosai dashi kamar sun jima jitai  hirar usman ta wanke mata damuwar wancan mara kunyar yaron, su hassana suna daga ɗaki suna sauraran hirar sunata mamakin shakuwar mama da usman ɗin suma.......

Bebi tunda ta shiga gidan iya suka ƙule a ɗaki suna hira ita da sadiya seda aka soma labaran ƙarfe taran dare sannan iya ta kwaɗa musu kira.
"Bebi zoki wuce gida kinsan mamanki bata son fitar dare".
Tura baki Bebi tai gaba.
"Iya ni kibarni na kwana wallahi gidanmu sauro".
Dariyar sakarcin Bebin iya take.
"Maza xona sakaki a hanya ki karasa dan bana son wannan shirman naki".
Kamar zasuyi kuka! iya ta saka Bebi gaba seda suka rakata har bakin layin sannan sukai sallama iya da sadiya suka koma ita kuma Bebin tacigaba da tunkarar gida.
Gabanta ne taji ya faɗi lokacin dataga hasken fitilar mota ya haske hanyar datake harya bata damar kallon gabanta bata kuma kaɗuwa ba seda taga wata bakar ƙatuwar mota still a dab da gidansu.
Tana kokarin hawa dakalin kofar gidan nasu taga mutum kamar bugagge akanta.
Ɗago kanta tai tana ambatar sunan Allah a zuciyarta.
"Malam lafiya zakawani zo katsayamin kamar ka bugu?"
Tafaɗa cikin fitsara.
Tare da saka hannunta ta kare idanunta sabida hasken ɗayar motar dake oposite ɗinsu ya kuma ƙaruwa.
Sautin dariya taji kafin taga ya dawo gabanta ya bake hanyarta ta shiga gida se asannan hasken daya haskashi yabata damar ganin koshi ɗin waye.
Ɗan gajere ne marar jiki farine tas idan bata manta ba taɓa ganin wannan mutumin lokacin da zasu fita itada da ƴan biyu abakin wani shago yana zaune yana shan sigari ƙwarai ta taɓa.ganinshi.
"Balkisu zinariyata haba nima mijin se ammin tsiwa to angonki ne na jibi ko gata, naxo zance ne muƙarasa mota" yafaɗa yana kokarin kai hannu saman nata.
Jada baya tai sabida ƙaurin daya bugeta wanda ta tabbata na kayan mayene.
"Wallahi tallahi ka kuskura ka taɓamin hannu sena baka mamaki banza gaja kawai".
Tafaɗa tana hararashi kamar idanunta zasu faɗo ƙasa.
Dariyar basawa yay.
"Ke dakata mahaukaciya nixaki mannawa hauka kinsan waye ni kuwa to in bakida labarina kije ki tambaya waye mai shanawa nine wanda idan akacewa mutum yaje ya gani to ni ze gani tantirancina ya wuce tunanin karamin kanki wawiya kawai"!!
Murmushi Bebi tayi tana masa kallon wanda ya sami matsalar ƙwaƙwalwa.
"Ayyah kace bariki ce da kanta agabana to Allah yay min tsari da shaiɗanin mutum irinka"
Tafaɗa babu tsoro atare da ita tana jada baya sabida tunkarar ta dayay.
"Zaki gane baki da wayo yayin da jibi ko gata na turmushe ki na goge bakin tsiwa inma bakida masaniya kije ki tambayi kawunanki waye ya bada sadakin ki yarinya zan nuna miki karshen iskanci".
Gabantane ya faɗi har tsoronta ya bayyana hankalinta ya tashi nan da nan in kuwa har aka aura mata wannan tabbas angama da rayuwarta waye bai san iskancin shiba seda yafaɗi sunanshi tama kuma shaidashi dama akanta ɗazu wannan baffan nata yazo gidansu.......
Jikinta na rawa take kokarin shiga gida domin ta ƙarajin komai sabida ɗazu sama sama taji maganar dan tana tsaka da zazzaɓi.

Caraf taji hannunshi saman nata yana kokarin haɗata da jikinshi cizo ta gantsara mashi agigice ta juya da gudu amai makon ta koma gida tsabar ruduwa seta koma bayan layinsu cikin wata kwana ta raɓe tana kuka!
Duk abinda suke Aliyu yana kallon su kamar a tv sedai baijin abinda suke faɗa amman ga yadda yake hango waccan marar kunyar yaga kamar fitsara takewa gayen, bai kaɗu da lamarin ba seda yaga gayen yanason rungumeta wanda tsabar kaɗuwa yasa shi balle marufin motar batare daya shirya ba ya fito tare da nufar wajan dasuke.
Yana zuwa tana guduwa wannan gayen kawai yagani wanda yay mishi kama da ƙazami.
A ƙyamace Aliyu ke kallon khaleepha kamar yaga kashi.
"Ƙaddara ƙanwarka akazo yiwa wannan iskanci xaka yarda nace zaka yarda dan ubanka"!!
Khaleepha yaji murya dakakkiya ta doki kunnenshi.
Kafin ya ɗago kanshi ya zuba su akan tsayayyen namiji ɗan gayu wanda babu wargi atare dashi,Cikin tsoro da kuri khaleepha yake cewa.
"To kaikuma waye kuma.mai ya ruwanka da matata itafa zan aura nan da ƴan kwanaki ina ruwan.......,Bai ji karashen maganar ba ya kwaɓe bakin khaleepha da gefen hannunshi.
"Ko mijinta ne kai zan iya hukunta ka sabida su mata killacesu akace ayi ba watsasu ba bare kuma.kai daga duk inda ka fito.kai ba ɗan kirki bane wawa kawai ubanka ne ze aura maka ita dalla ja gwangwanin motarka kabarmin nan kona saka hukuma ta kama min kai"
Aliyu ya faɗa ranshi na suya.
"Zan tafi amman kasani in ka hanani taɓata anan wallahi baka iska ka hanani auranta cikin satin nan ba domin tuni sadakina ya riga komai isa gidansu".
Yafaɗa da sauri ya faɗa mota yaja a guje jikinshi na rawa kar wannan mai kama da samudawan ya zaneshi.
Dariyar rainin hankali Aliyu ya saki tare da kaiwa iska naushi yana mamakin wautar wasu iyayen da basa tsayawa wajan binciken suwa ƴaƴansu zasu aura, sunfi daraja kuɗi akan cancanta, wannan yaron daga duk inda ya fito ɗan mai kuɗine amman sangartacce marar tarbiya, to ita kuwa tayaya babar waɗannan yaran xata haɗa ƴarta da wannan yaron marar tarbiya kuma inba mantawa yayba yaji kwanakin baya tace yaran marayu ne.....
Mai makon ta tsaya ta zaɓa musu majazen ƙwarai shine zata haɗa ƴarta da wannan shikam dan dai baya da son shiga hurumin daba nasa bane amman tabbas daseya magantu akan wannan lamarin dan yana tausayawa duk wadda xa,a haɗa aure da wancan ɗan ƙwayar.
Hanyar databi ya tsirawa ido............
Yana ayyana tsabar duhun hanyar tare da ƙanƙantar ta domin garin babu wuta shikanshi dalilin dayasa ya kunna fitilar motarshi kenan.
Cikin nutsuwa yake taka kafafunshi harya karasa cikin lungun mai uban kwatoci.
Raɓe yaganta ajikin bango tana..............

*IDAN NAGA RUWAN COMMENT*

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_Bakina yagaza furta irin godiyata agareku masoyana sedai naita binku da ɗinbin addu,a tare da fatan alkairi a kullum ina kuma gaya muku inhar kukaga banyi update ba, to kufara min uzuri kafin komai mussamman yanzu da lafiya tai ƙaranci anata fama da zazzaɓin maleria, tare da mura nima jiya nayi zazzaɓi amman yanzu kam Alhamdulillahi naɗan ji dama-dama, shine nace to bara na baku koba yawa, Godiya mai tarin yawa ga ƴan COMMENTS BOX ɗina inajin daɗin yadda kuke nuna goyon bayanku akan wannan littafi, Godiya mai tarin yawa ga masu tayani SHARE zuwa sauran wasu group's ɗin tabbas na shaida soyyyarku gareni Nagode! nagode!! Allah ya saka da alkairi amin ONE LOVE_

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*59*

Tana faman kuka! kamar wadda ranta ze fita.
Yajima yana tsaye batare daya ƙarasa gab da itaba kuma bai mata magana ba domin yana tunanin ma bata ji takun ƙarasowar shiba.
Kallonta yake tundaga sama har ƙasa tacikin hasken farin watan daya haska masa ita.
Gyaran! Murya yay kaɗan yana naɗe hannayenshi a saman kirjinshi tare da kafeta da idanunshi masu mugun dafin hukunta marar jin magana.
Cike da zallar tsoro firgici Bebi ta juyo sanin hatsarin lungun domin bama abinshi da daddare sabida ƙwacen da akeyi acikinshi baya da haka har shaye shaye maza ke zama suyi acikinsa itama yau gudun khaleepha ne yasa ta gwammace ta shigo cikin layin akan tabar shi yacimma burinshi akanta.
Sedai kuma duk da hakan akwai ɗunbin tsoro da firgici mai yawa acikin ranta wanda ya bawa jikinta damar rawa kota ina kamar mazari.
Jada baya ta somayi kaɗan-kaɗan duk tunaninta khaleephane sabida duhun datake ciki bai bata damar ganin kowaye ba, Sedai ga yadda taga tsayin na gaban nata yakuma firgita ta domin ko kusa khaleepha bai kai wannan na gaban nata ba, Jin ƙamshin sassanyen turarenshi datayi ya kuma bata tabbacin bashi bane kuma ba, ƴan shaye-shayen da suke zama bane.
Ɗaga idanunta tai still taga har yanzu bai matsaba kuma bai ƙaraso inda take ba.
Tsugunnawa tai awajan tare da cusa kanta a tsakankanin cinyoyinta tana ambatar sunan ubangijinta, Kukan ma yatsaya mata cak! sabida tsoro domin batai tunanin bil adam bane sabida tsananin ruɗin data shiga.
Ganin zata ɓata mishi lokacine yasa yaja ƙafarshi da ƙyar sabida ƙyamar kwatami, agabanta ya

tsaya tare da ɗan rage tsayinshi kaɗan ya rissuna yana binta da idanunshi.
Jin mayen ƙamshin takumayi yana tunkarota kafin ta ɗaga kanta daga cikin cinyoyinta ta zuba idanunta akanshi yana rissune gabanta yaɗan ranƙwafo da kanshi gareta kaɗan.
Bushashshen miyau ta haɗiye mai zafin gaske tanajin wani mugun fitsarin tsoro ya taho mata.
Sam bata gane fuskarshi ba sabida duhu atunaninta wani ɓata garin ne yabiyo ta yay mata illah!.

Cikin dauriya take jada bayan a yadda take,Gam! taji anriƙe mata tsintsiyar hannunta,Wanda hakan yabawa fitsarin datake maƙo damar zubowa babu shiri baki ta ɓare mai zata zunduma ihu! yay saurin saka tattausan hannunshi ya danne matashi cakk, ya ɗagata yabar wajan da ita.
Wutsil wutsil take tana ƙoƙarin ƙwace kanta amman bai direta ba se a bakin layinsu alokacinne hasken farin wata yabata damar kallonshi a tsorace, take tasoma jada baya tana mamakin tayaya yazo nan?.
Babu mai bata amsa se mayun kaifafan idanunshi dasuke mata yawo akaf ilahirin jikinta.
Cak ta tsaya ta kasa jan ƙafafunta ta tafi sabida yadda sukai mata nauyin ja.
"Malama tafi kiban wuri konai ƙwallo dake kowama yaganki a wannan shigar ai baze gaza yin lalata dake ba"!
Kallon kanta tai se lokacin ta tuna da shigar datai a ɗazun har hassana tana mata magana akan tazo ta saka hijabi taƙi.
Jitai ta muzanta da wannan kalamin nashi.
"Nace ki wuce kibani wuri, ai wancan wawan ne dai-dai dake tunda baki da kamun kai yarinya kamarki kin fito da wannan tsakar daren".
Ya kuma faɗi adake.
Yana ɗan jan tsaki! sabida yaga har tara ta gota ga usman shuru.

Tura baki tai gaba tana tuna rashin kirkin daya karta mata kwanakin baya shine yanzun ma yakeson karta matashi, gashi tanajin tsoron karta tanka mishi ya duketa a banza.
"Nifa ba wani wuri naje ba Ehe! dan kar aje aimin kallon ƴar iska daga gidan iya nake kuma idan ƙarya nake kaje ka tambayi mama! bakuma wani abunne yasa na gaya maka hakan ba sedan kar wataran ka ganni kaimin wani irin kallo".
Tafaɗi maganar da sauri sabida tsoron karya masgeta.
Tunda ta soma magana yakafe bakinta da ido yana kallo first in history mace tagaya mishi magana a dake batare datai shayi ba, ko manyan mata suna rissuna mai bare wannan dayake zaton inda yay auren wuri dafa tuni ya haifi kamarta.
"Shigar jikin kifa itama mamar tasani tabarki?".
Shikanshi bai san yay wannan katoɓarar ba seda yay maganar sannan ya tuna yay taɓargaza, amman Bebi dayake akwai ƙuriciya yasa bata wani fahimta ba.
"To ina ruwan......., Baiji abinda zatace ba ya kwaɓe bakinta da bayan hannunshi yana mamakin tsiwar yarinyar.
Dira ƙafafunta ta soma a wajan tana dafe bakinta da hannunta.
"Nifa marainiyace kuma bani da lafiya ɗazu har asibiti aka kaini amman shine zakazo kana duka

na, kai kullum na haɗu dakai sekaimin mugunta jiyafa haka kaitamin masifa ka ɗaukoni a motarka yayan babana yaga nafito daga motar ya biyoni yana cemin karuwa harya zagi mama, daga nan kuma yakawon wannan na ɗazun yace se anɗaura mana aure, kuma Allah ze sakamin tunda ni marainiyace.......".

*NAKASA WALLAHI ZAZZAƁI WALLAHI ALLAH BANA JIN DAƊI KUYI HAƘURI SE GOBE*

_Albishirinku masu son littattafaina Document da page toga dama ta samu gareku ga duk mai son karanta books ɗina page ko documment kamarsu *ƊAN MAJALISSA* *RABON WANI* *KOBA SO* *HASKE* *DA IZZATA* duka akan farashi mai rahusa guda 5 ɗin a naira 1000, in kuma ɗaya kakeso a naira 300, maiso seya neman ta wannan number 08142105218 sena jiku masoya suma dukansu akwai daɗi da ratsa zuciya_

*AUREN BARE !!*🌹
{ _HOT LOVE_ }

NA
*AUTAR MANYA*

_HOME OF QAULITIES WRT ASS..._

*60*

Durƙushewa tayi a wajan tana masa kuka! kamar ranta ze fita zuciyarta tana mata zafi jitake kamar ta mutu,Dawani irin yanayi na tsantsar sanyin jiki ya bita shima yay tsugunnon a gabanta yanajin wani irin mugun sanyi na ratsa jikinshi, kalaman rarrashi yakeson arowa amman yakasa kalma ɗaya data faɗi ita ta sanyaya mishi jikinshi, datace yaja mata yayan babanta yana kiranta da karuwa har ya kawo mata mijin aure, shi mutum ne mai tausayawa ɗiya mace yana da mugun rauni akan su musamman idan yaga mace tana kuka yanajin zuciyarsa na mishi suya.
"Jiya kuma? jiya da yaushe na kawoki gida?".
Yafaɗi maganar a rarrabe, jin sautin muryarshi adai dai saitin kunnuwanta yasa tai maza ta ɗago se asannan ta manta cewar bafa jiya bane tun wancan satinne data raka hussaina talle

kamfani, tsabar ruɗune yasa tace mishi jiya wanda su kansu sun jima basuje tallen ba.
Ɗan jan jikinta tayi ta matsa daga saitinshi tana kokarin miƙewa domin bazata iya tsayawa a yadda suke ɗin ba.
"Jeki gida! Yanzu yaushe ne bikin sukace?".
Yafaɗi maganar yana miƙewa tare da zuba hannunshi acikin aljihun wondonshi.
"Nima ban saniba amman ɗazu yacemin ko gobe ko ranar friday mai zuwa wai don ya nunamin ƙarfin ikon kuɗinsu, amman mama taje gidan baba malam ɗazu sunyi magana".
Tafaɗa tana miƙewa tsaye.
"Waye haka?"
Yafaɗa yana kallonta.
"Shine kakanmu a bayan layinmu yake".
Shafa gemunshi yay yana kuma jefa mata wata tambayar.
"Ke kina son auren?".
Zaro ido tai waje tare da cewa........
"Tabb wallahi bana sonshi sabida kowa yasan ba ɗan arziki bane kuma mama bayanzu xatamin aure ba, nifa ban isa  aure ba".
Dariya yay marar sauti wadda ita bata ganta ba.
"Nidai yanxu nina ja wannan aure ni kike xargi kikace nina ja maki?"
Tura bakinta tai gaba..........
"Da ina xamana lafiya babu wanda yazomin dawani maganar aure seda akaga ka saukeni a motanka" tafaɗa tana share hawayenta.
"Jeki gida nagode".
Yafaɗa yana barin wajan.
Da sauri tai cikin gida gabanta yana faɗuwa, da usman taci karo ze fita suna sallama da mama, da sauri ta gaisarshi sannan ta wuce ɗaki tana jiran faɗan mama akan daɗewarta.
*****************
Usman ne ya fito bayan sunyi sallama da mama sannan ya ƙarasa gaban motar ya bude ya shiga ya zauna.
A zatonshi Aliyu ze mishi faɗa amman seyaga bai mishi ba sema tada motar dayay tare dayin revars yabar layin titin kabuga ya ɗauka domin isa murtala suya domin ya siyowa madam khadija kaza.
"Kaga najima ko kai hakuri hirace taɗauki daɗi".
cewar usman yana kallon wayarshi ganin time yay karfe goma saura.
"No babu matsala, ina son neman shawararka amman dan Allah bana son shirmenka magana zamuyi serious".
Murmushi usman yay tare da cewa ina jinka.
Babu wani ɓoye-ɓoye Aliyu ya fara yiwa usman bayani hankalinshi yana kan kwalta.
"Kasan wannan yarinyar ƴar gidan daka fito yanzu ba ƴan biyun ba".
Da mamaki usman yace.
"Ok Bebi naji suna kiranta kasan sunan ammi gareta".
"Koma miye sunanta nidai mafita nike nema sabida banson na mutu da haƙƙin wani akaina"...........tass yagama kwashe duk abinda ya faru dashi da yarinyar tundaga haɗuwarshi da ita a kamfaninsu har zuwa yau datake gaya mishi za,a mata auren dole.

"But ni abinda yake damuna yadda ta ɗoramin laifin danna ɗaukota a motana ne ya haifar da haka, se abu na biyu yaron dasuke son bata baya da kirki, abu na uku ina tunanin basa shiri da dangin mahaifin nasu shine yasa sukeson yi mata wannan auren domin su tozarta mahaifiyar yaran".
Yafaɗa yana ɗan huci! kaɗan tare da dafe sitiyarin motar tashi.
Cikin tsananin mamaki usman yake duban Aliyu lallai Ali ba karamin zurfin ciki gareshi ba tayaya duk akai wannan bidirin bai sanar da usman ɗin ba?
Yaso yay mishi cari amman gudun zuciyarshi yasa ya mayar da hankalinshi gareshi domin yasan yana fara dariya maganar xata watse dan baze kuma tanka mishi ba.
"Shawara ta gareka shine ka AURE TA"
Cikin wani irin ƙarfi yaja burki ya dakatar da driving ɗin yana kallon usman.
"What in aureta fa kace usman are you in sense?"
Murmushi usman yay.
"Wannan shine only solution da xaka fidda yarinyar daga cikin sarƙar datake shirin shiga rayuwarta sannan zaka ceci maraicinta".
Lumshe mayun idanunshi yay yana jan huci mai zafi yana dafe kanshi tare da bude idanun tar ya zubawa usman su, wanda shi kansa usman seda ya firgita da ganin yadda idanun Aliyun suka sauya launi.
"In auri yarinyar da zan iya haifarta sabida ƙarancin shekarunta? in auri yarinyar da babu abinda ta sani se cin abinci ƙilanma raino kawai zanyi ina nidai ka sauya wani abun sabida kasan wannan baze yuwu ba, dani naso kawai na maka uban yaron a kotu idan yaso kotu ta hana auren faƙat".
Dariya usman ya gintse tare da kallon Aliyun.
"Cewa kai zaka iya haifarta sabida karancin shekarunta, ai ba haifar tata kaiba ko? sannan raino ai anfison waɗannan sabida sune masu sugar, kawai dai kai tunani amman nidai a shawarce kai wannan yaƙin ka taimakesu dan Allah ka aureta, koba ka sonta kai yaƙi da zuciyarka gaba xatai maka rana".
Kallon kaci kai yay wa usman.
"Yaufa kwana na ɗaya dayin aure? sannan na ƙara? tayaya zan fiskanci abba akan ina son *AUREN BARE* Wanda kasan haka baya cikin tsarin familyn mai atamfa?".
Dum! dum!! gaban usman ya faɗi shifa yama manta da wannan tsarin na zuri'arsu seda Aliyun ya faɗi yazun.
"Eh! Aurenka da ita shine mafita amman babbar matsalar itaɗin BARE CE! amman ban tunanin abba zeƙi yarda sedai matsalarmu Alhaji babba domin ka tunamin lokacin da ya umar yaso auro wannan ƴar legos ɗin alhaji fa cewa yay sedai ya umar ya bar musu gidan indai baze auri jininshi ba".
"Mafita ta gaba duk da ban tsoron yin auren domin ba haram bane".
Murmushi usman yay.
"Ka auretan ko Allah xesa ka fara rusa wannan shegiyar al'adar da wannan tsohon ya kafa mana ƙiri-ƙiri muna ganin mata muna son aurowa amman a takura mana seta family kai ɗaya zaka iya rusa wannan shirin nasu ZAKIN AMMI".
Murmushi Aliyun yay a ƙasan ranshi tare da tuno abubuwan da suka shude aranshi.
"Ok toyaya lamarin ze kasance kasan kona sha giyan wake bazan tunkari abba da wannan

ɗanyen aikin ba".
Dariya usman yay kana ya jawo kunnen Aliyun yay mishi raɗa, ɗan ware ido Aliyun yay tare da girgiza kanshi kana ya tada mota suka wuce suna tafe suna hirarsu harya ƙarasa wajan siyo kazan ya futa ya siyo komai tare da nufar mota suka tafi gida lokacin da sukaje gida ƙarfe shaɗayan dare sallama sukai da usman shiya wuce part ɗinshi.shima Aliyun mota ya kashe ya kwashi kayanshi daya siyo yay nasa sashin.
Lokacin dayaje khadija tai bacci abinda ya siyo mata ya aje mata a saman madubi kana yay nasa ɗakin ya tube kayanshi ya shiga wanka yana fitowa ya sauya kayan bacci ya haye gadonshi ya kwanta yana tunanin maganar usman tabbas akwai aiki gabanshi sabida su abba basa ƙetare maganar alhaji babba wanda yanajin a wannan karon shi ze soma watsi da maganar shawarar usman ce take.masa yawo azuciyarshi ahaka bacci ya kwashe sa.
********
Tun kafin mama tashigo Bebi tai baccin ƙarya wanda kiran duniya mama tai mata amman taƙi tashi harya zarce xuwa na gaske, washe gari tun asubahi Bebi tayi wankan tsarki tai sallar ta, kana ta koma gado ta naɗe ta cigaba  da sharar baccinta.
*********
Ƙarfe bakwai na  safiya tayiwa malam a ƙofar gidan marigayi alhaji mai katifa amininshi ɗan gidan rabi'u  yagani zefita ya kirashi yace yay mishi sallama da iyayenshi.
Mintuna biyar Rabi'u Tasi'u Sani suka fito ganin baba lado (malam) yasa suka ɗanyi jim sabida basa kaunarshi sakamakon yadda yaja ɗan uwansu babansu bebi ajikinshi.
A ɗage suka gaishe shi tare da kallonshi "Muna sauraranka malam".
cewar sani wanda yake kallon malam.lado.
"Dama maganar auren nan da kuka zo yiwa wannan yarinyar shin kunyi binciken halaiyar yaron da sauran abubuwan da shari'a ta umarta a yi ayayin da ake neman aure?".
Dariya suka saki mai tattare da ranin hankali.
"Malam lado daman mutum da kayanshi har wani daga can ya isa yazo yay masa ƙarfa ƙarfa akanshi? shin ina ruwanka kana bare ina ruwanka da shiga tsakanin jini da jini?, To bari kaji wannan yaro ubansa uban gidanana ne kuma nina jagoranci auren dan haka babu fashi"!!
Cewar tasi'u.
"Eh muda kayanmu yau ko gobe ko jibi xamu daura a huta da wannan jaraba".
Cewar sani.
"Allah sarki au ashe fa malam musa ɗan uwankune ai ban saniba, ku dan Allah inba jahilci irin nakuba duk irin ƙiyayyar da kuka nuna mishi har kunada damar yiwa ɗanshi aure to bari kuji ni ɗinnan ni zan ɗaurawa kowacce a ƴaƴan musa aure kuma wannan auren nina gaya.muku baze yuwu ba gaba ɗayanku na isheku muxuba dani daku".
Yafaɗi hakan tare da barin wajan da sauri yana huci.
Jikinsu ne yay sanyi suna tunanin yaya xasuyi cikin haka kiran haji isa ya shigo wayar tasi'u da rawar jiki.ya ɗaga yana faman kirari.
Umarni ya bashi akan anjima.ze aiko da akwatunan lefe gobe za,a ɗaura auren sabida khaleepha ya bukaci haka.
Ajiyar zuciya tasiu ya saki yana ayyana faɗuwa tazo dai dai da zama tare dayin na'am da maganar kana ya kashe wayar yana duban ƴan uwanshi.
"Kurabu da wannan tsohon damu yake xancen inya san wata ai bai san wata ba gobe ma

daganan zamu ɗaura auren muga ta tsiya sedai kawai yaje ya ɗauki abarshi".
Dariya sukai kana suka watse akan gobe zasuyi fin karfi.
********
Kai tsaye malam lado gidan mama yaje lokacin suna karin kumallo shinfiɗa tai masa ya zauna anan yake wassafa mata komai.
Cikin tsoro mama tace"karfa suje su mana ƙafa ma'ana suyi ɗaurin auren nidai dan Allah malam ko wani ne ka samu ka haɗata dashi insha Allahu kafin suyi mai yuwuwa".
Jimm yay yana nazari secan yace.
"Karki damu ai ALLAH ya fisu".
Sallamar yaroce ta katse musu maganar.
"Assalamu alaikum.wai usman yana sallama agidan".
Cewar yaron.
Jimmm mama tai kana tace.
"Kace masa ya shigo"
Sallama usman yay tare da neman guri ya zauna cikin ladabi ya gaisar da malam shuru wajan yay daga mama se usman tare da malam a tsakar gidan domin ƴan biyu suna ɗaki kuma sun kunna redion data hana suji abinda ke wakana.
"Mama nida babban yayanmu ne munzo neman alfarma in bazaki damu ba sabida jiya naji komai daga bakin wannan ƙanin nawa akan auren bebi dazakuyi mama in babu damuwa muna son ayau a ɗaura auren da Aliyu ga yayanmu can a mota yaxo da sadaki sedai angon baizo ba muke wakiltarshi mu ƴaƴan alhaji idiriss mai atamfa ne.mama kowa yasan sunan mahaifinmu koda zakuyi bincike".
Malam ne ya zubawa usman idanu yana kabbara ga sarki Allah, mama kam tsabar mamakin wannan lamarin ya hanata magana.
"To babu laifi domin a shari'ar aure daman shedu da waliyai akafi so to muna godiya ga Allah dayasa kuɗin kuka kasance shaƙiƙan shi Aliyun kuma waliyanshi domin kace harda babban yayanku babu matsala ni xan zama waliyin ita bilkisun idan yaso se aje can kofar gidana ai shela, in aka ɗaura kafin bisani daga baya yazo ya ɗauki matarshi a hannuna mun gode da wannan karamci".
Cikin sauri usman ya fita ya sanar da ya abbakar wanda ke cikin motarshi malam ne ya fito suka wuce can kofar gidanshi atare.
Sosai malam lado yay shela harda mai unguwa da manyan dattijai na cikin anguwar yaya nura da ya aminu ma seda suka zo duk mamaki ya ishesu lokacin dasukaji sakon kiran malam, amman ƙarancin lokaci yasa basuyi binciken komai ba.
Ƙarfe tara da rabin safiyar lahadi 1/3/ ɗunbin jama'a suka shaida ɗaurin auren ALIYU IDRIS MAI ATAMFA da BILKISU MUSA MAI KAFITA! cikin sadaki mai daraja wanda ya abbakar babban yayan Aliyu ya miƙa kuma shiyay wakilcin ango ya tsaya a matsayin mahaifin ango, inda usman kuma yazama shaidar ango malam lado kuma yazama waliyin amarya tare da sauran shedun dasuka tsaya wajan ɗaurin auren harda su mai unguwa da sauran jama'ar unguwa.
Bayan shafa addu'oin dasuka fito daga bakin mai anguwa taro ya watse su ya abbakar sukaiwa malam lado sallama suka wuce da ɗunbin farinciki hakanan shima yay gidanshi da sadakin bebi a hannunshi.

*TAMMAT BIHAMDIHI*

*NAKAWO ƘARSHEN PART ONE CIKIN LITTAFINA PART TWO BAYA DA YAWA SEDAI AKWAI RIKITA RIKITA* 💃💃💃 *WADDA TAFI TA PART ONE*

*SHIN YAYA WANNAN AUREN ZE KASANCE* ?
*INA TARIHIN ALIYU* ?
_HANNUNA YA GAZA GAYA MUKU RIKICIN CIKIN WANNAN LABARIN WANDA KE GABA KUDAI MUJE ZUWA* 💃💃💃💃

*PART 2*

NA KUƊINE

*61*

Cikin sauri ya aminu yabi malam lado cikin gidanshi da ɗan gudunshi, dakatawa malam yay ganin aminu a bayanshi yana haki.
"Aminu lafiya naga kana bina da ɗan gudu koko wani abunne?".
Rissunar da kai ƙasa yay  kana yace.
"Malam munji zancen aurene sama taka shine mukeson jin mike faruwa wallahi bamu da wani labari akan lamarin".
Cikin nutsuwa malam ya dubi Aminu sannan yace.
"Maza aminu kiramin ɗan uwan naka kuma kam kuna da hakki yakamata a sanar daku wannan curarren lamarin, Cikin sauri ya aminu ya fita segasu da nura lokacin har malam ya shiga gidanshi ya bawa baba sadakin ta rike mai kana ya ɗauko abin zama ya shinfiɗa masu a soro. Zama sukai dukkansu.

Sannan malam ya dubesu.
Tass ya kwashe dukkan abinda ya faru ya sanar musu tare da ɗora musu da cewar ai yanzu aikin gama ya gama tunda an riga an ɗaurawa bebi aure sayi da wani kuma.
Sosai wannan lamari ya bawa su ya aminu mamaki amman basu wani ji abin sosai ba sabida daman sun kwana da sanin halin dangin mahaifin su bebin mutane ne masu tsabar son kansu da yawa.
"Kuma dai yakamata kuyi abin da yadace akan maganarku".
Cewar malam yana kallonsu.
Sunkuyar da kai sukai sannan ya aminu ya fara magana dayake shine babba.
"Malam ginin muke son karasawa insha Allahu konan da karshen wannan shekarar ne se ayi kafin nan aikinmu ya samu".
Murmushi malam ya faɗaɗa kana yace

"Masha Allahu naji daɗin hakan sosai Allah ya kaimu lokacin amin".
mikewa sukai suna masa sallama tare da ficewa daga gidan.
Tabarmar ya naɗe tare da shiga cikin gidanshi yana wassafawa baba abinda ya faru.
wata buɗa baba ta saki tana cewa.
"Aidaman inxaka gina ramin mugunta tofa ka ginashi iya tsahonka ALLAH mungode maka daman indai jinin ka a arziki ike wallahi sekayi Allah daɗa suttura".
Tattaunawa sukeyi ita da malam akan lamarin auren har zuwa wani lokaci.
Malam ɗin ya mike ya saɓi babbar rigarshi tare da karɓar kuɗin yana cewa baba bara yaje can gidan maman ƴan biyun.
Lokacin da malam ya shiga gidan mama iya tana zaune akan tabarma tanawa mama faɗan akan me zata ɓoye mata komai ashema basu zama ɗaya ba se yanxu aminu ke gaya mata abinda ke faruwa.
Haƙuri mama ke bawa iya harga Allah itama tasan bata kyauta mata ba ayadda suke amman tsabar ruɗun dasuka shigane yasa batabi takan iyan ba.
Sallamar malam ita ta katse musu maganar tasu.
Faɗaɗa far'a mama tayi itama kuma iyan haka suna yiwa malam barka da shigowa cikin axama mama ta ɗauko mishi sallaya ta shinfiɗa masa.
Gaisawa sukai cikin mutuntuka sannan ya dubi mama.
"To Aishatu kiyiwa Allah godiya an ɗaurawa balki aure yanzu dan haka maza kiramin ita".
Cikin jin daɗi mama ta miƙe ta shiga cikin ɗakinta.
Lokaci ɗaya suka fito da bebi wadda take can karshen gado tana bacci.
Ganin malam yasa ta watstsake tare da tsugunnawa a gefe guda tana gaidashi, se alokacin ma ta lura da iya itama gaisar da ita tayi sannan ta sunkuyar da kanta a ƙasa daman yau ɗin tanajin duk jikinta babu daɗi.
"Balkisu ni wanene a wajanki?".
Malam ya tambayeta cikin tsanaki.
Jimm tayi tana ayyana wannan tambayar tashi acikin ranta kafin taji muryar mama tana cewa.
"Wainikam bada bebi ake magana ba".
Cikin sanyin jiki tace.
"Kakanmu ne kai"

Murmushi malam yay tare da kallon mama.
"Waccan fa?".
Bin idanun malam Bebi tayi kana tace.
"Mahaifiyar mu mana".
"Masha Allahu balkisu nasan yanzu kin wuce yarinya karama kina da hankali kina da nutsuwa kinsan ciwon kanki kuma kinsan inda ke maki ciwo, idan har nida ita mun isa dake kuma muna da mahimmanci wajanki to ki bamu haɗin kai akan hukuncin da muka zartar akanki".
Dum! dum!!
Cikin tsoro take Addu'ar Allah yasa ba haɗin auren ta da khaleepha akai ba.
Hawaye ne ke kokarin zuba mata amman seta kanne tare da kallonshi.
"Malam babu abinda mama xata cemin nayi naƙiyi indai bai saɓa addini naba, malam koma maye nasan bazaku cutar dani ba tumma kafin naji na amince".
Cikin tsabar mamaki mama take kallon Bebi ta yadda tai maganar ka rantse wata mai hankalin kirkince.
shiko malam murmushi yay kana yace mata.
"Masha ALLAHU balkisu munji daɗi Allah yay miki albarka, a sakamakon auren da waɗancan keson yi maki muka duba tsabb muka gano shi kanshi yaron ba ɗan mafita bane gefe ɗaya akwai karancin tarbiya awajanshi yasa muka yanke shawarar haɗaki da wani dafatan kin fahimmata?".
Cikin faɗuwar gaba ta ɗaga ido tana kallon malam.
Bakinta yana rawa amman takasa faɗin komai illa binshi kawai datakeyi da idanunta.
"Mun ɗaura miki aure da ɗan mafita ɗan arxiki kuma insha Allahu baxakiyi nadama ba Balkisu ga sadakin ki yau nina ɗaura miki aure da saka hannun mahaifiyarki".
Cikin rudewa take share hawayenta bakinta ya gaza furta kowacce kalma malam mama iya babu wanda yace gada wanda aka ɗaura auren sedai sun bita d idanunsu suna kallon yadda take kuka kamar ranta ze fita.
"Balkisu ko baki na'am ba mu warware?".
Cewar malam.
"A,a malam karku warware koma waye shi naji xan zauna dashi akan na zauna da khaleepha nagode da karamcinka nagode nago......
Bata karasaba ta mike bata bi takan sadakin ba tai ɗaki tana kuka kamar babu gobe.
Murmushi malam yay tare da mikewa batare daya dauki sadakin ba.
"A,a malam ka rike a hannunka har zuwa lokacin da komai ze warware mungode Allah ya basu zaman lafiya amin".

Cewar mama tana kallon malam.
"To ba matsala Allah rufa asiri  zuwa gobe seta tawo nan wajena in yaso shi mijin nata ya karbeta a hannuna koya kuka ga?".
Iya ce tayi magana anan wajan.
"Hakan yafi malam komai kai dai daine babu abinda xamu ce maka se godiya mungode Allah ƙara girma".
Fita yay.yana musu sallama.
Sosai iya da mama suke maida zance akan lamarin auren har zuwa lokacin da rana tayi kana

sukai sallama iya ta wuce gida.
Ƴan biyu suna ɗaki dama a tsakar gidan daga mama se iya dan haka iya na tafiya mama ta mike tayi cikin ɗakin...

Su usman kuwa daga wajan ɗaurin auren...........

*LITTAFIN KUƊI*

*PART*

NA KUƊINE

*62*

Su usman kuwa daga wajan ɗaurin aure kai tsaye gida sukai sabida ranar sunday ne babu aiki, suna tafe ya abbakar yana jajanta abin yana kuma daɗa gargaɗin usman akan komai ze biyo baya kada ya sake ya ambaci sunanshi.
Dariya usman ɗin ya saki kana yace.
"Haba magajin abba kaima kasan babu kai acikin wannan badaƙalar ai ka gama mana komai ALLAH dai ya raya zuri'a amin".
Cigaba yayi da cewa..
"Amman gaskiya dattijon akwai karamci Aliyu ya ɗauko ƴar gidan masu karamci Allah dai yasa komai yazo cikin sauƙi".
Usman ne yace.
"Insha Allahu, muna fatan haka yaya".
Suna tafe suna tattaunawa har suka karasa gida, lokacin wajan 12 na rana ya abbakar part ɗinshi ya nufa bayan ya kashe motar shima usman nasa part ɗin yay domin yay break fast.

Nasan fans zaku so jin tarihin Aliyu wanda ban riga dana feɗeshi a part one ba amman yanzu insha Allah zakuji.
************

Mai atamfa family.
Asalin tarihin shi kansa mai atamfar kakan Aliyu kenan mahaifin Alhaji idiris mai atamfa abban Aliyu, sunan shi  Marigayi Alhaji Ali mai atamfa haifaffen garin kano ne shi cikin wata ƙaramar hukuma wai ita ɗan batta.
Alhaji Ali ɗane ga sarkin kasuwar garin ɗan batta waishi malam usman, shi kanshi Alhaji Ali ya gaji kasuwanci ne wajan mahaifinshi marigayi malam usman ɗin, tun yana yaro malam usman ke tafiya dashi kasuwa wajan sayar da kayan sakawar dayake kasuwanci, wanda malam usman bai saida komi se atamfa acikin kasuwar.
Marigayi Alhaji Ali shi kaɗai mahaifinshi malam usman ya haifa kamar yadda shima malam usman ɗin ya taso baida ƴan uwa na ciki ɗaya sedai ƴaƴan dangi.
Gatan duniya Malam usman ya nunawa Ali shida matarshi hajjo..
Lokacin da Ali ya taso, yazama saurayi se malam usman ya ɗauki ƴar gidan ƙanin shi wanda mahaifansu suke ciki ɗaya ya bashi yace ya aura mai suna salma, tunda shi Ali bai sami yin karatun boko ba, sedai harkar kasuwanci daya saka gabanshi kamar yadda yaga mahaifinshi yana yi.
Batare da musu ba Ali ya amshi auren salma hannu biyu cikin ladabi da biyyya, hakan bakaramin daɗi yaywa mahaifanshi ba cikin kankanin lokaci aka saka ranar biki, wanda iyayen Ali sukai rawar gani wajan nunawa ɗan nasu gata.
saka ranar aure da wata biyu.
Allah yaywa Malam usman rasuwa batare daya ga auren ɗan nashi ba, zokuga tashin hankali wajan Ali kamar zebi uban nan nashi haka yayta kuka sabida sun shaƙu, ganin babu ran mahaifinshi yasa ya mayar da hankalinshi baki ɗaya akan harkar kasuwancin mahaifin nashi harma yaso yafishi yawan jama'a.
Bayan rasuwar, malam usman da wata ɗaya aka ɗaura auren Ali da salma wadda ta kasance ƴar uwarshi ce ita ta jini.
Gida guda suke zaune da hajjo iya ladabi da biyayya salma tanayi wa uwar mijin nata.
Aurensu da shekara ɗaya Allah ya azurta salma da haihuwa ta haifi ɗanta namiji mai kyau dashi, ranar suna yaro yaci suna Ayuba, tun daga nan kuma se haihuwa ta buɗewa salma atakaice seda salma ta haifi ƴaƴa shida maza biyar mace ɗaya.
Ayuba, Salmanu, Idiris, Yusufa, Shu'aibu, karimatu.
Lokacin da aka haifi karima ne Allah yaywa hajjo rasuwa gidan seyaywa salma faɗi sam bata jin dadin zaman musamman idan yaranta suna makaranta sabida haihuwar tata akufi akufi ce shiyasa yaran suka taso kusan kansu ɗaya.
Ganin haka yasa Alhaji Ali ya tattara nasa ya nasa, ya baro ɗan batta ya dawo nan cikin kano da zama inda ya sai gida a wata anguwa wai ita  yakasai, anan suka cigaba da zama har xuwa sanda komai ya dai daita gareshi ya sayi shago anan cikin kasuwar kantin kwari yacigaba da sabgarshi ta sayar da atamfofin shi.
Ya rigada yaywa kansa alkawarin bawa yaranshi karatu mai inganci sabida shi bai samu yayi ba wannan dalilin yasa baya tafiya da ɗansa ko ɗaya kasuwa suna makaranta suna karatun su.
In akai hutu yakan tarkatasu sutafi can ɗan battan wajan dangisu suyi hutunsu acan su dawo suma kuma ƴan uwan nacan ɗin sukan tawo nan yakasan suyi kwanakin su sukoma gida wannan dalilin yajawo shakuwa mai yawan gaske a tsakanin Ali ( baffa )da danginshi  nacan haka xalika itama salma wadda ƴaƴanta ke ce mata (  inna ) tana kwatanta janyo nata ƴan uwan

ajikinta sosai sabida ita suna da yawa bakamar Ali dayake shi kaɗai ba.
Rayuwa tana tafiya shekaru naja, lokacin Ayuba shida salmanu sun kammala karatunsu na secondry, Seya samar musu makarantar ABU zariya, suka cigaba da karatunsu acan wanda kowa da fannin daya karanta, Ayuba accounting yake karanta shikuma salmanu yake karantar mass com, gidan ya rage daga idiris se ƙannenshi idiris yana ƙyalla idanu yaga babu ƴan uwanshi seya soma bin ubanshi kasuwa tun inna tana faɗa harta gaji wataranma a bakin shagon ze raɓe, Alhaji Ali na korarshi amman kamar cigam seya xauna.
Abokin Alhaji Ali ne yake ce masa kaga tunda ɗannan naka yanason harkar kasuwancin nan kabarshi ko naira hamsin kana bashi babu mamaki akwai abinda Allah ya boye akan harkar tashi.
Fafur baffa yaƙi yace shifa baze yarda idi ya xauna babu karatuba yanzu zamani ya sauya rayuwa idan babu ilimi fanko ce suma dan dai sunzo acan dane amman inda yanzune babu abinda ze saka yaki makaranta koda kuwa a boye ne seya jeta.
Babu yadda abokin baffa baida shiba amman yaki yarda.
Da ƙyar abokin nashi ya shawo kanshi akan shi ya yarda yana zuwa shagonsa in antashi daga makaranta seyana bashi ɗari biyu, dayake abokin baffan yana da yara a shagonshi
Dan dai babu yadda zeyine yasa ya amince wa abokin nashi.
Tun daga wannan lokacin idi ke zuwa shagon abokin baffanshi yana miƙa kaya ana bashi kudinshi yana tarawa, ranar asabar da lahadi da wuri yake zuwa ranar makaranta kuwa baya zuwa se antaso ahaka har ya kammala secondry lokacin, su ayuba sukuma sun shiga level 2 suma in sukazo hutu sukan bi baffa can kasuwar amman basa mayar da hankalinsu akan haka hartaja baffa yace sudaina zuwar masa shago.
Ganin Idi ya gama makaranta yasa abokin baffa ya kuma kara masa kudin biya sabida ya kara shekaru da hankali shikuma baffa lokacin yana cuku cukun samarwa idin makarantar gaba da sakandire sabida yafi masa son karatun fiye da komai, lokacin Allah bai ze samu jami'a ba shi se baffa ya samar mishi poly, inda yake karantar bussiness accounting, cikin haka shima mai binshi yusufa ya sami gurbin karatu anan poly ɗin amman shi yana karantar hausa islamic ne.
Shekarar su ayuba huɗu a makaranta sukai passing out suka tafi service, ayayin da baffa ya samarwa kowannen su macen aure kuma dukkansu sun kanace ƴaƴan ƙanin shine da iyayensu suke ciki guda, bayan dawowarsu daga service baffa ya bawa kowanne gida, tare da damƙawa kowa matarshi ahannu, bayan fitowar result Allah ya taimaki shi ayuba ya sami ikin banki shikuma salmanu ya sami aikin gidan redio amman ba anan ba acan jahar bauci, dole tasaka baffa ya saka haya a gidan salmanu ya tarkata masa matarshi suka wuce wadda ita da matar ayuba suke ciki guda kuma duka ƴan uwan inna da baffa ne.
Shikuma ayuba ya zauna anan gidan da mahaifinshi ya bashi tare da matarshi.
Adaddafe idi ya gama poly bai tsaya karbar kwalinshi ba ya bazama kasuwa cikin yardar Allah ya haɗu da ƴan chaina waɗanda suke bashi kaya yana sayar masu ya ɗora nashi................

*PART* 2

NA KUƊINE

*63*

Cikin hukuncin ubangiji idi ya soma karɓar kayan chaina yana rabawa ƴan kasuwa yana ɗora nashi, a shekarar ne kuma Allah ya azurta ayuba da samun ɗa namiji wanda yaci suna muhammadu, haihuwar matar ayuba da sheka matar salmanu itama ta haifi ɗiya mace, wadda taci suna salma.
Ganin haka yasa baffa ya kuma tafiya ɗanbatta ya aurowa idiris ƴar ƙanwar salma matarsa ( inna ) mai suna Bilkisu, shikuma yusufa ƴar abokin mahaifinshi malam muntari, mai suna ruƙayya, gida guda ya saya musu kowanne da sashensa, bilkisu mace ce mai matuƙar hakuri da kauda kai, saɓanin ruƙayya wadda tunda aka aurota take takalar bilkisu da faɗa, in inna tai magana setace ai dayake ita bare ce shiyasa zasu nuna mata bambanci.
Shekaru biyu bayan auren idiris da ƙaninshi yusuf wanda shi yusuf ɗin bayan ya gama makaranta seya sami koyarwa anan wata primary, se kuma ƙaninsu shu'aibu tare da karima, shima dai shu'aibun ƴar cikin dangi ya aura mai suna hanne, ita kuma karima ta auri ƙanin bilkisu mai suna shamsuddeeni, hankalin baffa ya kwanta sabida kowanne acikin ƴaƴan nashi ya sami madafa.
Sedai abinda ze baka mamaki duk cikinsu Allah yafi ɗaukaka idiris sabida bayan aurenshi da bilkisu se samunshi ya ninka nada domin harya kai ga buɗe runfar anan kasuwa inda ya ɗora shu'aibu a wajan.
Shekarar su uku da aure matar idiris bilkisu tana da ƴaƴa biyu duka maza ita kuma matar shu'aibu tana da ƴa ɗaya, Sukuma su ayuba suna da ƴaƴa uku uku kuma ikon Allah ayuba duka yaranshi uku mazane shikuma salmanu mata.
Itama matar idiris duka mazane biyun, abubakar da umar, ita kuma matar yusufa, tana da rumassa'u.
Su abubakar nada shekaru shida aduniya ɗaukaka ta ƙara xuwarwa idiris domin tuni idanunshi ya buɗe akan harkar kasuwancin shi wanda harya soma tunanin ginin kamfani anan anguwar sharaɗa.
Kuma a shekarunne, yakai.iyayenshi tare da yayyenshi ƙasa mai tsarki domin sauke farali wanda baffa har kuka yay da hakan ada yanaƙin ɗan nashi a kasuwa, ashe anan ɗaukakarshi take.
Lokacin da bilkisu take ɗauke da cikin ɗana uku lokacinne ya sai ƙaton fili anan anguwar yahaya gusau, wanda ya bada order ginin gida mai part bakwai ciff, sannan ya kuma siyan wani ƙaton daban wanda yace in Allah ya raya ƴaƴansu kowa ya yanka ya gina wanda aka kareshi batare da angina shiba, part ɗin iyayenshi part ɗin shi, dana yayinshi harma dana mijin ƙanwarshi karima wanda a yanzu yake kasuwa tare da shu'aibu anan shagon idiris ɗin.

Cikin ƙanƙanin lokaci aka kammala ginin tare da sabon kamfanin atamfar daya buɗe anan sharaɗan wanda zena sifirinta daga ƙasar waje zuwa nan yana bawa ƴan kasuwa sari, Komawarsu yahaya gusau tare da ƴan uwanshi ta kawo sauyi da dama, haɗin kai ne ya wanxu a tsakaninsu mai mugun ƙarfi domin su idiris basa ƙetare maganar yayansu ayuba wanda yanxu yara kece masa ( alhaji babba ) lokacin da bilkisu ta haifi ɗanta namiji na uku se aka saka masa usman sunan kakansu idi kenan, alokacinne kuma rashin lafiya ta kama Baffa wanda bai wani ɗauki lokaci mai tsayi ba Allah yay mashi rasuwa wadda ta girgiza ilahirin zuri'arshi dama sauran alumma, Tunda baffa ya rasu itama inna lafiya tai mata ƙaranci adaddafe seda tai shekara ɗaya tana fama da lalura kafin kuma itama Allah ya ɗauki ranta gidan seya zama dagasu sesu da yaransu babu uwa babu uba,idiris ya mayar da hankalinshi akan kamfaninshi wanda  daga kano har legos yana fita, ya tura kaya, Alokacin babu irin ƙiyayyar da rukayya matar yusufa bata nunawa bilkisu duk da dai yanxu ba part ɗinsu ɗaya ba amman bakin ciki yasa rukayya taji bata kaunar balkisu sabida yadda tafita ƴaƴa tafita da miji duk da ba miji guda suke aure ba, amman kullum burin rukayya ta zuga yusufa mijinta akan ƴan uwanshi amman dayake shi yusuf baida matsala sam baya kama maganarta
Bayan haihuwar usman da shekara uku balkisu ta kuma haihuwa ɗa namiji kyakykyawan gaske sedai shi bakar fatane kamar mahaifinshi haihuwar data zamarwa idiris farar haihuwa domin ribar daya daya samu a kamfaninshi tafi  ta ko yaushe wadda ta haifafa mashi fara sabon gini wani kamfanin na atamfa anan anguwar mundaɗu, Ranar suna yaron yaci sunan mahaifin idiri ALIYU, son duniya idiris ( abba ) ya ɗauka ya ɗorawa Aliyu domin ko bacci zeyi sedashi a kirjinshi yadda Aliyu ya saba da abbanshi bai saba da mahaifiyarshi ba daga abba se usman kaɗai Aliyu ke sakewa aduniya  amman kosu abubakar baya sakewa dasu sosai.
Aliyu yana da shekaru biyu, aduniya abubuwa nacigaba suka kuma samun abba, alokacinne alhaji babba ya kira ƙaninshi salmanu( abban bauchi ) wanda shi baya zama anan garin sabida aikinshi yana bauchi amman inyay hutu yakan zo da iyalinshi nan kano gidan da abba ya gina musu suyi hutunsu a part ɗinsu sutafi.
Zama sukai tare da ƴan uwanshi ayuba ( alhaji babba ) salmanu ( abban bauchi ) idiris ( abba ) yusufa  ( baba yusufa ) shu'aibu ( baba shu'aibu ) se kanwarsu karimatu ( anty karima ) addu,oi sukaiwa mahaifansu sannan Alhaji babba yay gyaran murya sannan ya soma yi masu bayanin abinda yasa ya tarasu.
Ya kirasu ne akan yana tayasu murna na samun rufin asiri tare da iyalai masu albarka domin alokacin alhaji babba yana da ƴaƴa biyar uku maxa biyu mata abban baucima biyar duka mata, se abba yana da huɗu maza baba yusufa ɗaya mace, se baba shu'aibu yana ƴan biyu duka mata , se karima datake da maza biyu, Cikin nutsuwa ya shigar musu da ƙudurinsa na cewar. kakansu marigayi malam usman shi kaɗai mahaifanshi suka haifa yazo shima ya haifi mahaifinsu shi ɗaya shikuma mahaifinsu yazo ya haifesu su shida cikin hukuncin Allah suyanzu gashinan ƴaƴansu sunkai kusan 30 dan yanason su ringa ƙulla alaƙar Auratayya a tsananin ƴaƴan nasu kamar yadda mahaifinsu baffa yay ya dinga ɗauko ƴan uwanshi na ɗanbatta yana aura musu inka cire rukayya matar yusufa wadda ita kaɗaice bare, domin itan ƴar abokin mahaifinsu ce.
Kowa yay na'am kuma yay murna da hakan domin ta hakan ma zumuncinsu ze kara ƙarko.
Anyi taro lafiya angama lafiya wanda aka yanke hukuncin haɗa ɗan gidan alhaji babba mai suna muhammadu da ƴar gidan abban bauchi salma, anan aka yanke maganar za,a na ɗaukar

mace ɗaya daga wannan ɓangaren namiji ɗaya ana haɗasu aure sannan alhaji babba ya nuna baya son ɗaya daga cikin ƴaƴan nasu ya AURO BARE! gwara kowanne ya duba anan cikin gida ya aura, da haka aka tashi ataron dayake su abba basa musa maganar alhaji babba kamar yadda mahaifinsu ya basu wasiyya wannan dalilin yasa kowa ya amsa mata dato.
Tundaga wannan lokacin zuri'ar MARIGAYI ALHAJI ALI MAI ATAMFA! suka soma auratayya a tsakaninsu, kuma abba shiyake gina masu sashe acikin wannan ƙaton filin daya aje na cikin gidan, a shekaru biyar seda akai auren mutum huɗu ƴaƴan alhaji babba maxa biyu mata na abban bauci kuma duk suna cikin gidan sedai kuma yawancinsu suna aikin gwammanatine, domin lokacin alhaji babba ma yay ritaya awajan aikinshi.
Seda Aliyu ya shekara goma sannan balkisu ( ammi ) ta sami ciki watan cikinta tara ta haifi ɗiya mace nusaiba, wanda a shekarunne kuma aliyu ya shiga secondry sukuma su abubukar sun kammala jami'a har abba ya ɗebesu zuwa kamfaninshi sabida business suka karanta.
Aliyu ya taso dason kasuwanci kamar abbanshi dominshi haryafi abbanshi son neman kudi.
Wannan dalilin yasa yana gama secondry abba ya fitar dasu UK shida usman domin su karanci, Business, bayan tafiyarsu ammi ta haifi Amina daga amina se ƴan biyu, daga nan kuma haihuwa ta tsayawa ammi, wanda alokacin da ammi ta haifi amina kusan atare suka haihu da rukayya wadda itama ta haifi mace wadda taci suna khadija ammi tana da ƴaƴa8 ita kuma rukayya ( umma ) take da ƴaƴa biyu ruma da khadija.
Bayan tafiyarsu abubuwa sun faru daga ciki kuwa harda auren su, abubakar wanda abubakar ya auri ƴar gidan alhaji babba, shikuma umar lokacin abba ya buɗe kamfani a legos tose ya tura umar can anan ya gamu da wadda yaso aura amman dayazo gida da maganar se alhaji babba yace masa sedai yabar musu gida domin su baza suyiwa kowa a ƴaƴansu AUREN BARE ba, bakaramin damuwa umar yay ba daga karshe aka bashi ƴar abban bauchi humaira wadda take sa'arsu amina da khadija ya aura ya wuce da ita legos ɗin.
Nusaiba kanwar Aliyu itama ɗan gidan anty karima mujahid ta aura,duk dai ƴaƴan gidan kowanne inya taso baya rasa wanda za,a haɗasu aure.
Lokacin dasu Aliyu suka dawo daga kasar waje, Abba yaso yi musu aure amman Aliyu yaƙi, se usman ne aka haɗashi da zainab ƴar gidan baba shu'aibu kuma itama ɗin sa'arsu amina ce dai, Aliyu kuwa baki ɗaya ya mayar da hankalinshi ne akan harkarsu ta kasuwanci wanda a wannan lokacin yana legos wajan umar suna gudanar da kasuwancin tare a kamfanin abba nacan, ganin ƙwazon yaron yasa abba ya dawo dashi kano, cikin haka suka kuma gina wani sabon kamfanin na nan kusa da anguwarsu Bebi wanda abba ya damƙawa Aliyu matsayin MD na nan ɗin sabida ƙwazon shi wanda haryafi ƴan uwanshi ƙwazo da gudanar da aiki yadda ya kamata.
Cikin Haka Allah yaywa yusufa rasuwa, bayan ƴar rashin lafiyar dayay zokuga kuka wajan umman su khadija tun daganan komai nasu ya koma kan abba, hatta khadija dasu amina take tafiya makaranta wadda tun ranar dataga Ali taji tana masa mugun so, tunda ita bata sanshi ba seda ya dawo daga waje.
Amman yadda taga baya kulata baya wasa da ita yasa takejin mugun tsoronshi.
Faɗan duniya alhaji babba yayi akan ALIYU yaki aure sabida lokacin har ƙannenshi maza na familyn wasu sunyi aure amman shi in aka kirashi seyace akara masa lokaci.

*PART* 2

NAKUƊINE

64

Sosai abin yake damun su abba ganin yadda Aliyu yay buris da zancen aure, kuma basu kaɗai ba hatta ƴan uwanshi abin yana damunsu domin a yanzu haka nusaiba mai binshi tana da yara uku! ya abbakar ƴaƴa huɗu, ya umar kuwa yana da ɗaya, yanzu kuma matarshi tana da wani cikin ga kuma usman shima matarshi tana ɗauke da cikin fari danma batai haihuwar wuriba domin yanzu haka kusan shekarunsu biyar da aure amman se yanxu akai cikin fari, Amina ansaka mata rana, tare da ɗan gidan abban bauchi, yanzu haka kuma aminar nurse ce, tana aikin asibiti.
Ƴan biyu suna lavel 2 a university, kuma suma duk da mazajensu a hannu kuma suma ɗindai ƴaƴan cikin familyn ne.
Ruma yayar khadija ita kaɗai ke aure a kaduna tana auren ɗan ƙanwar ummansu wanda umman ta kawo mata tace ta aura ganin jinin ummanne yasa su alhaji babba suka amince a shekara guda akai bikinsu da nusaiba mai bin Aliyu ita ruman tana nan kaduna yanzu yaranta huɗu.
Rayuwar Aliyu ƙalilan ce acikin gidansu sabida tunda ya dawo bai zama kullum yana hanya fita ƙasashen waje domin kawo samfir in kuwa yana kasar nan tofa yana cikin kasuwa suna harka da ƴan kasuwa sabida suna rabawa ƴan kasuwa kaya su haɗa masu kudinsu sannan ƴan kasuwan na zuwa wajansu, sari amman basa harkar komai se atamfa.

Khadija tun tana ɓoye damuwarta akan Aliyu hartazo ta soma bayyana fili domin juyin duniya anyi da ita akan ta fidda miji taƙi haka xalika a family in ankawo mata setace bata so seta saka kuka! su alhaji babba da abba suna tausayin khadija fiye da xato sabida maraicinta.
Dan haka basa takura mata karatun ma dasu amina suka fara da ƴaƴan alhaji babba su hidaya amman tsabar tunani harya kai ga sun fice sun barta da gyara exams.
Wannan abin takaicin ya dami umman khadija rannan dai ta sakata gaba har seda ta gaya mata abinda ke ranta.
Da kirsa da komai seda umma ta cusa khadija wajan ammi harta kai ga tana kwana tare dasu ƴan biyu, umma ta ɗauki ƙudirin setayi mai yuwuwar ƴarta ta auri Aliyu, sabida tun rasuwar yusufa taso abba ya aureta amman abin yaƙi ( kuji fa ) wai sabida suma su dandali arziki( hmmm banda wanda kuke ci mutum kenan)dan haka taci alwashin cusa wa ɗansa khadija

wanda daman tun kafin khadija tazo mata da maganar take saka abin aranta.
Rawar kai kala kala babu wanda khadija bataiwa Aliyu amman shikam bata ko gabanshi.
Harkar gabanshi kawai yake domin yanzu kulada harkar dukiyar mahaifinsu itace akan gaba, ga hidimar gida domin alhaji babba yay ritaya haka xalika abban bauchi shima haka duka iyayen nasu basa fita abbansu ne kaɗai yake tafiya legos ko waje domin shigo da kaya shima kuma yakan jima bai fitan ba domin yabarwa Ali wannan jigilar.
Duk da yaransu alhaji babba kowa yana aikinshi na gwamnati domin baifi mutum biyar ne a karkashin kamfanin abba ba, amman hakan bai saka abba yafasa dasa su Ali direwa kowani part kayan abincin wata ba, haka xalika sutturu karatun yara zuba mai a motocin daya zube duka abba ya dauke musu, sannan kuma babu wanda bai ɗauka yakai saudiya sauke farali ba.
Su kansu ƴaƴan abba su ya abbakar sunada mugun kuɗi, sosai, ba kamar Aliyu a kaf cikinsu sabida shi bai laru da aikin ƙarƙashin kamfanin mahaifinsu  kaɗaiba, sabida a kullum yana ayyana kuɗin bana sabane shi ɗaya, wannan dalilin yasa ya raba ƙafa yana lura da kamfanin mahaifinshi a matsayin amana da biyayya gefe ɗaya kuma shima yana lura  da harkokinshi na kasuwanci wanda ya haɗa da kawo motoci, tare da atamfofi yana bawa manyan ƴan kasuwa wanda ko iya wannan ribar tashi kaɗai zata iya riƙe gidansu,kuma Allah yasaka masa nasibi a harkokinshi domin gidajen kansama daya gina ya bada haya sunada yawa banda kaddarori tare da ƙaton ginin kamfanin sayar da atamfofi dayake ginawa anan Tokarawa!wanda shi kansa abba daya ga ganin seda ya sarawa ɗan nashi.
Yanxu haka rabinshi yana harkar kulada kaddarar abbansu rabi kuma yana zuwa tokara domin ganin ginin kamfaninshi na ƙashin kanshi wanda ze dinga sauke dillar atamfofi lesuna shaddodi harma da takalma danshi yace baxe tsaya a atamfa kaɗai ba.
Iya tsaruwa kamfanin ya tsaru sabida ɓangaren atamfofi daban! na shadda daban! na lesuna daban! na takalma da mayafai daban! domin bakaramin kudi yake narkawa ba.
Kuma babu ko silan abba ciki da iya tsantsar guminshi dayake business ɗinshi yake gina kayanshi yakai su ya abbakar sun gani dasu alhaji babba wanda suka dawo gida suna santin wurin tare da jinjinawa Aliyun.
Ranar dasu ammi da umma da su hajiya matan alhaji sukaje ganin a daren umma batai bacci ba dan kuwa seda ta dangana da wajan Alhaji babba karya ta lafta masa akan cewar khadija bata cin abinci bata shan ruwa akan soyayyar Aliyu.
Babu kunya bare tsoron Allah haka taita lafta karya harda kukan kada su bari khadija ta rasa ranta su taimaka mata su biyu ta haifa ga khadija marainiyace.
Rarrashinta Alhajin yay kana ya hau faɗan akanme khadija xata kashe kanta ita da ɗan uwanta cewa umma yay ta tashi taje ciki zasu tattauna akan maganar da ƴan uwanshi.
Washe gari alhaji ya kirasu abba ya gaya masu a ranar abba ya kirawo Aliyu tare da khadija ya gabatarwa da Aliyu khadija a matsayin matar dasuka zaɓa masa.
Kamar ze kuka haka ya amsawa abban tare da tashi yabar wajan itako khadija ranar batai bacci ba sabida farin ciki.
Tuni magana ta karade family wanda wasu daga cikin ƴanmatan famiyn suke cewa inama sune sukai dace haka.
Wasuko tausayi take basu sabida sun san baida wasa.
Tundaga lokacin yawanci khadija take zama a falon ammi tare da bin ammi kicin ta tayata aiki wanda ta sami wannan karatun daga wajan ummanta.

Sosai ammi take yabon khadija shiko gogan ko dariyarsa bata taɓa gani ba tunda shi daban bamai yawan far'a bane wannan se usman shine mai yawan far'a da sakin fuska........................

*NAKUƊINE*

*PART* 2

NAKUƊINE

*65*

ALIYU IDRISS MAI ATAMFA shine cikakken suna shi, ɗane na uku a wajan Alhaji idriss mai atamfa, yana da kimanin shekaru talatin da bakwai ciff a duniya, ya sami saukar karatun alqur'ani mai girma tun yana da shekaru goma a duniya, hakanan yay haddarshi yana da shekaru sha ɗaya a duniya, ya sami karatun addinin islama cikakke ya karanta manyan littattafan addini, a ɓangaren karatun boko yana da matsayin masters wanda ya sami iliminshi akan harkar kasuwanci business accounting, tun bayan dasuka kammala secondry ɗinsu mahaifinsu ya ɗebe su shida ɗan uwanshi usman ya fitar dasu ƙasar uk anan wata jami'a dake ƙasar suka sami damar yin karatun su tundaga matakin digree har zuwa masterring, batare dasun kuma dawo gida ba koda da hutu, har seda suka kammala karatunsu sannan suka dawo ƙasarsu ta gado cike da ɗunbin nasarori, daga nan ne kuma kowa ya kama aiki ganga ganga a karkashin kamfanin mahaifinsu.
Har zuwa wannan lokacin da shi ALIYU yakai ga soma gina kamfaninshi na ƙashin kanshi banda wasu sabgoginshi dayake na harkar kasuwancin shi da jarinshi.
ALIYU mutum ne mai riƙo da addininshi domin baya wasa da ibada hatta azumin nafila ko wanne baya wuceshi hakanan yana da miskilanci na gaske baida sakin fuska sosai, gefe ɗaya kuma harkar gabanshi kaɗai yake baida saka idanu akan lamarin wani, Dogone sosai mai suffar ƙarfafan maza baƙine shi amman irin kalar nan mai ƙyalli, yana da manyan idanu masu firgita

marar jin magana mai ɗauke da dogon hanci wanda bai cika siranta ba, sedai yana da tsaho da ɗan fadī kaɗan, bakinshi madai daici haƙoran ciki farare ne tass ajajjere dasu, yana da wani ƙaton tabon abin sallah a saman goshinsa wanda har wani turzawa yayi yay wani irin kurji-kurji yana saɓa, gashin girarshi mai gazar gazar ne, wanda ya cure a saman doguwar fuskarshi mai ɗauke da wani irin haɗaɗɗen saje wanda ya haɗe da gemun daya bari a fuskar tashi.
Baya barin suma a kanshi duk da yana da yalwarta amman bai barinta sedai yay askin saisaye batare daya bar suma akanshi ba, haka nan Aliyu mutum ne mai tsananin tsaftar gaske ko kaɗan baison ganda bare ƙazanta haka xalika baya son sanyin jiki komai nashi da zafi-zafi yakeyi da ƙarfinshi da lafiyarshi, domin ko shiryawa ze baya wuce mintuna goma ya gama, ya fice yana da mugun zafin nama, yana da rashin son magana sedai inka taɓoshi akwai zafin rai da zuciya tare da taurin kai, wannan dalilin yasa ƙannenshi suke mugun shakkarshi hakanan kuma ma'aikatan su suna ganin girmanshi sabida iya mu'amalarshi da jama'a sam baya nuna girman kai ko izza baya nuna cewar shi mai kuɗine a kullum yana nuna cewar shidasu ɗayane, suna matukar jin daɗin tafiya da shi sedai yawan rashin maganarshi kaɗai ke haɗasu dashi amman iya adalci da tausayi yana dashi.
Yana da biyayya sosai domin duk abinda ammi da abba suke so yakan hana kanshi farin ciki domin ya samarwa mahaifanshi yakan aje lokacinshi mai mahimmanci akan ya kyautatawa mahaifanshi, wannan dalilin yasa suma mahaifan nashi ke ƙoƙarin ganin sun kyautata mashi.
Aliyu yana cikin  jerin mazaje masu mugun ƙarfin sha'awa tsananin zurfin cikin shi ke sakawa bai nuna halin dayake ciki illah mutum ɗaya dr mijin kanwarshi nusaiba, wanda suka taso a tare ɗan wajan alhaji babba shine kaɗai yasan halin da abokin nashi ke ciki shima kuma dalilin yana karɓar magani wajan shine.
Duk halin daze shiga a ɗakinshi shi kaɗai yake gama murƙususun shi na azaba batare da wani ya sani ba, sedai ƙwayar idanunshi ta nuna wadda kusan kullum take a lumshe wadda gazar gazar ɗin gashi suka rufeta ruff gwanin sha'awa don kafin kaganshi ya buɗe ƙwayar idanunshi tarr akan mutum da wahala inko yay hakan sedai inyana cikin ɓacin rai wanda inya kalleka da ita seka kusan fitsari dan firgici! sabida yadda Allah ya bashi wani irin ƙwarjini da haiba, ma'abocin son ƙamshine wannan dalilin yasa kamshin ya sami wuri ajikinshi ya kama kullum yazo waje zakaji kamshi wataran ma kafin yazo wajan kamshinsa ze fara maka sallama.
Yana da kyakykyawar mu'amala a tsakanin shi da ƴan uwanshi, sedai inda ammi ke fama dashi rashin shiga cikin jama'a sosai sau tari yakan zauna ne a ɗakinshi yay ayyukan gabanshi koya ɗauki carbinshi na yatsun hannunshi yayta tasbihi ga ubangiji yakance hakan yafi masa yayta zuba surutun da baida amfani.

Yana da tsari a rayuwarshi wanda komai nashi a tsare yake tun yana karami yake da nutsuwa wadda tabi jikinshi har zuwa girmanshi, wannan dalilin yasa baya shiri da mutum mai rawar kai sabida shi mutum ne nitsatstse sau tari sukan yi faɗa da usman akan surutunshi.

Akaf ƴan uwanshi yafi shiri da usman sun shaku komai nasu ɗaya hakanan Aliyu da usman sukanyi sirrinsu batare da kowa yajiba.
Aliyu yana son usman sosai hakanan shima usman ɗin nason Aliyu wani zubinma har ƴan biyun ammi ake ce masu.

Ko kaɗan baya son khadija har cikin ranshi amman yadda mahaifanshi suka bashi umarni akan ya aureta yasa bai masu musu ba.
Sabida a tsarinshi baison karamar mace yafison babba wadda ta mallaki hankalin kanta, duk da khadija ba yarinya bace kuma tana da hankalinta amman shi baison mace irinta ko kaɗan bata burgeshi, sabida khadija akwai iyayin tsiya tare da shige masa shikuma mutum ne wanda baida son zaƙewa a rayuwa.

Khadija doguwa ce amman bacan ba farace tass wadda harta ɗan fara ɗashewa batada wani jikin kirki domin yanayinta kamar ta tsinke, tana da rashin magana, dan baza,a sakata ajerin masu son mutane ba don ko a makaranta batada kwashe-kwashen kawaye ita dai barta da iyayinta.
Tana da mugun kishi akan abinda takeso wannan dalilin yasa bata yarda da wata tazo gidansu bare suyi katari da Aliyu.
Tana da tsafta hakanan batada son jiki domin tasami ƙwarewa akan girke girke kala kala tare da kyaran jiki da gayu sabida umman ta gaskiya tanada tsafta.
Tana son Ali sosai wanda har bata iya ɓoye sonshi a ko ina.
Sedai gefe guda harda kwaɗayin abinda Aliyun ya mallaka domin arayuwarta tanada son fantamawa tafison taga tafi kowa acikin familyn su tafison tashiga jerin matan dasuka amsa sunansu mata tafison taga ta mallaki manyan kaddarori waɗanda zata shiga cikin jerin mata first class masu kuɗi da jin daɗin rayuwa, wannan dalilin yasa ta rike wuta harseda burinta ya cika akan Aliyu taga ta mallakeshi a matsayin mijinta gashi kuma burin nata ya cika na mallakar Aliyun bara muga kozatai nasarar mallakar zuciyar tasa..

Kunji tarihin ALIYU yanzu kunsan waye shi da kuma zuri'arsu.

*DAWOWA LABARI*

*PART* 2

NAKUƊINE

*66*

_CIGABAN LABARI_

Aliyu bai san bidirin dasu usman sukai ba hasalima bai san komai akan faruwar lamarin auren ba.
Shidai jiya sun rabu da usman akan cewar zega mai yuwuwar samawa yarinyar gurbin makarantar kwana mai tsada yasan intai nisa da gida babu mai takurata bare ai mata wannan auren.
Abinda kuma usman ya raɗa mashi jiya a mota shine xasu san yadda sukai ta dawo wajan ammi da zama inyaso in ta dawo hutu tai zamanta a wajan ammi da wannan dabarar suka rabu da usman ( lallai akwai ƙura ! )
Bai tashi a baccin shi ba se wajan 12 Na rana salatine ɗauke acikin bakinshi yana miƙe ƙafafunshi waɗanda ya saukesu daga saman gadonshi, jikinshi sanye da guntu wando kasancewarshi bamai kwanciya da kayaba, koda ya zira kayan bacci tofa cikin dare seya tubesu kuma baya son rufa yafi bukatar ya kwanta a haka.
Rabonshi da bacci tun karfe huɗun asubahi daya tashi yay nafila, ya wuce masallaci bai shigoba se shiddan safiya wajan motsa jiki yaje yay morning training bai shigoba gida ba se wajan 8 ruwa kurum ya watsawa jikinshi ya kuma kwanciya shine bai tashiba se yanzu.
Gaban kofar bathroom ɗinshi yaje ya ɗauko katon towel mai kalar dark blue daurashi yay a west ɗinshi bayan ya zame guntun wandon dake jikinshi cikin bathroom ɗin ya shiga yay brush tare da watsa ruwa ajikinshi.
Yafito dukkan ilahirin jikinshi yana ɗigar da ruwa.
ƙaramin towel ya ɗauka ya tsane ruwan jikinshi tare da nufar gaban AC controll ɗin ɗakin ya ƙaro ƙarfinta janyo stool yay ya zauna gaban mirrow yana shafa cream a skin ɗinshi cikin sauri.
Ɓarin body spray, yaywa kanshi sosai yabi kowani saƙo da lungu na jikinshi ya goga turarenshi na arabian uod, sannan ya gyara kwantaccen sajenshi mai haɗe da gemunshi, tashi yayi ya nufi gaban close set ɗinshi.
Ɗanyen farin boyel mai yankan gidan sugar ya ɗauka wanda akai mashi ɗinki da golden ɗin zare dogayen kayane har ƙasa, shirya kanshi yay cikinsu still ya kuma yima kanshi barin turare.
Phone ɗinshi dake yashe bisa saman bedside ya ɗauka tun jiya bai kunnata ba yanzun ma kuma baida niyya kunnawa sabida baya son yawan damu yanajin dukkan jikinshi ya gaji babu abinda yake bukata se hutu, sakamakon yawan zirga zirgar dayake yi bai samun xama shikam kusan kullum yana kasuwa ko yana wani uzirin a office.
Taka ƙafafunshi yay a saman lallausan chanies carpet ɗin dake malale a center'n ɗakinshi handle ɗin kofar ya bude ya fita falo.
Tundaga bakin room ɗinshi wani irin daddaɗan kamshi ne ke mashi well come! mamakine ya

kamashi lokacin da idanunshi sukai arba da ƙayataccen tiren sliver a tsakiyar table ɗin dake falon, an jere falasai a samanshi gawata ledanan irin ta rafin an rufe tiren  da ita da alamun kayan break fast aka jere a kan tire ɗin.
Zama yay akan one seater tare da kallon tvn dake kunne ana wani indiyan film mai kyau.
Kimanin mintuna biyar yayi yana kallon film ɗin yana kuma jin dadinshi sabida shiba ma'abokin kallace kallace bane ba amman wannan film ɗin yay  masa kyau tare da daɗi sabida soyewar da ake cikinshi.
Baƙon sassanyen kamshine yake kusantoshi rintse idanunshi yay yana kuma kwantar da kanshi a gefen hannun kujerar harta karaso gabanshi.
"Assalamu Alaika"!
Tafaɗa tana tsugunnawa gabanshi.
Can cikin makoshin sa yace mata.
"Amin wa'alaikissalam".
Domin seda tai da gaske taji abinda yace ɗin.
"Yaya barka da safiya fatan ka tashi lafiya naga hidima jiya nagode Allah ya ƙara buɗi da ɗaukaka amin".
Da sauri ya wara idanunshi yana kallonta.
Sanye take cikin atamfar holland ja wadda akai mata ɗinki rafa na riga da zani setai wani irin firit acikin kayan sabida batada ƙiba.
Dariyace taso kamashi ganin yadda tai kamar kace mata kett ta arce gawani irin burum datai acikin riga da xani domin ko kaɗan basu amsheta ba, dogayen riguna sunfi mata kyau.
Amman sanin zataga kamar yay mata cin fuskane seya kanne ya basar tare da barin dariyar can kasan ranshi.
"Yaya the break fast is ready"!
Tafaɗa tana nuna mashi da ɗayan hannunta.
"Tun ɗazu nai niyyar tashinka naga time yana wucewa amman sanin kayi zirga zirga kaji wahala yasa na barka kasami hutu".
Tafaɗa tana miƙewa daga gabanshi wajan kayan karin taje ta soma sauko dasu kasan carfet.
"Yaya abinda yasa ban kaisu daining ba sabida nasan sekafi jin daɗin yin break a kasa nima banciba kai nake jira".
Mamaki take bashi na wannan rawar kan datake mashi.
Amman bai magana ba, sedai can cikin ransa yaji dadin yadda tai mashin danshi yana son a girmamashi a riritashi aji dashi a waje musamman wajan matarsa ta sunna.
Yanajin yadda ta karramashi inya ƙi cin abinci kamar ya zuba mata kasa a idanunta ne.
Dan haka cikin nutsuwa ya taso daga kan kujerar tare da komowa kasa ya zauna gabanta yana facing ɗinta yana ganin yadda take sarving break ɗin acikin plate cikin nutsuwa tare da tsantsenin tsafta.
Kallon yatsun hannunta yake ta kasan idanunshi wanda yake hango zallar tsaftar khadija a cikinsu sabida yadda suke a yanke ƙar-ƙar dasu, aransa yakejin kodan tsaftar dake gareta ze iya cin abinda ta bashi.
plate biyu tai na soyayyen dankalin turawa tare da miyar source ɗin hanta agefensu kamshinsu ne ya cika masa hanci.
Tura mai nashi tayi gabanshi tare da ɗauko cokali mai yatsu ta saka aciki.

"No ki fara bani black tea nasha"!
yafaɗa kamar an tilasa mashi.
Cikin jin daɗi ta amsa masa tare da janyo tea flaks ɗin dake gefenta.
Ta ɗauki white tea cup  ta bude flaks ɗin ta fara zuba mashi ruwan tea ɗin data masa hadin su na'a na'a dasu kanun fari, tun tana zubawa kamshin kayan hadin yagama cika falon harta kammala ta saka tea spoon ciki tare da miko mai gabanshi.
Dayake da sugar take dafa shayi domun yafi ji tare da kara lafiya.
Mamakin yadda ta iya sarfa girki yake cikin ranshi tare da tsaftar ta amman bai ce komai ba seya karba tare da ajewa gabanshi.
"Nagode!"
Yafaɗa tare da yin bisimillah ya fara shan tea ɗin wanda bakaramin daɗi yay mashi ba............

*NA KUƊINE*

*PART* 2

NAKUƊINE

*67*

Babu abinda kakeji acikin ƙayataccen falon nasu, face ƙarar na'urar sanyaya ɗaki tare kuma da ƙarar cokalin da khadija ke ɗiban dankalin turawan dayake cikin plate ɗin gabanta tana ci ahankali ciki nutsuwa tare da tsantsar iyayi.
Yana shan tea ɗin yana lumshe idanunshi yana jin daɗin yadda kayan kamshin cikinshi ke ratsa mishi maƙogoronshi yana jin daɗinshi sosai musamman yadda kamshin ke dukan hancinshi.
Harya kammala ya dire cup ɗin idanun khadija yana bisa kanshi hamdala tayi ga sarki Allah sannan ta miƙo mashi dankalin data zuba mishi cikin plate wanda yace bazeci ba seyasha tea tukunna.
Ɗan ƙyafe bakinshi yayi kaɗan batare daya kalli plate ɗin ba, sabida yadda yaji cikinshi ya ƙoshi.
"Yaya kaci wannan ɗin".
Muryarta ta dokin kunnenshi, ɗan juyowa yay kaɗan.

"Am ok"
Abinda ya faɗi kenan yana juya kanshi yana kallon side ɗin Tv.
"Please yaya kaɗan ci koyaya danfa kai na tashi tun six nayi maka break fast mai ƙayatarwa haba mana my cwt man dan Allah kaci".
Tafaɗi maganar cikin sigar shagwaɓa.
Bayanson hayaniya hakanan kuma bayason watsa mata ƙasa bisa idanunta sabida shi mutum ne dayasan ƙimar ɗan adam sam baison yay mata abinda bazata ji daɗi ba, musamman yanzu datake ƙarƙashinsa, duk da bai sonta ko kaɗan amman bai tunanin ze iya cutar da ita ko ƙuntata mata domin shi lamarin aure na Allah ne.
Jan plate ɗin yay gabanshi sannan ya tanƙwashe ƙafafunshi abisa ƙa'idar tarbiyar cin abinci. Batare daya ɗauki spoon ba, ya ɗanja hannun rigarshi sannan ya saka hannunshi na dama yay bisimillah sannan ya soma cin abincin, Cike da nutsuwa.
Ta cikin ƙasan idanunta take kallon yadda yake cin abincin nashi cikin nutsuwa yanayi kamar baison cin abincin wanda hakan kamar acikin tsarinshi yake.
Yakai kusan mintuna biyar yana cin abincin amman kuma baifi loma uku ba, sannan ya ɗan janye plate ɗin daga gabanshi, ya miƙe tare da shiga cikin kicin ɗin dake falon, ya wanke hannunshi, ya ɗauki tiesue ɗin dake saman frij ya goge hannunshi da bakinshi ya jefa a dustbin ɗin dake gefen frij amman bawai irin wanda ake zuba shara bane ba, wanda ake ɗan zuba tarkacen dattin dake falo ne, sannan ya karasa saman seater ya zauna ya ɗauki remote control, yana serching channel, tashar saudi ya kamo tare da ɗan kwantar da kanshi yana kallonshi.
Itama khadijan miƙewa tai daga wajan cikin nutsuwa ta kwashe kwanukan tanajin ranta yay mata sanyi ganin yadda yaci abincin nata, kaiwa kicin tayi sannan ta koma ta ɗauko kayan gyaran waje ta gyare wajan tas duk daba datti yay ba sabida cin abincin nasu cikin nutsuwa sukai, sannan ta ɗauko room freshner ta fesa, wanda nan da nan ƙamshi mai sanyi ya ƙara cika falon, Seda ta tabbatar da tsaftar wajan sannan tazo kusada shi ta zauna daga saman ɗayan seater ɗin dake kusa dashi.
Itama tana kallon amman rabin hankalinta yana wajanshi tana kuma sake tsinkewa da lamarinshi na rashin maganarshi ace mutum kamar bebe.
"Ɗaukomin wayata acan".
Ya nuna mata can wajan center carpet inda sukai break fast.
Cikin sauri taje ta ɗauko mishi ita sannan ta miko mashi cikin nutsuwa.
Amsa yay yana kunnata.
Yana ƙoƙarin ɗorata a gefenshi yasomajin ringing! Cikin nutsuwa ya duba saman screen ɗin wayar sunan usman ne ya fito ɓaro ɓaro.
Mr Man.
Serving ɗin dayay ma usman kenan acikin wayar tashi, Cikin ɗan sakin fuska ya ɗauki wayar yana karawa a kunnenshi.
"Hellow kai wai wani irin mutum ne anata kiran wayarka tun safe akashe ina ka shigane?".
Murmushi yay na gefen baki wanda ke ƙara mishi tsabar kyau sannan yace.
"Bashinka naci koko a haya nake kabani notice".
Yafaɗa yana sakin ƙayataccen murmushi yana ɗan shafo gemunshi.
"Ban saniba ɗan rainin wayo dalla malam ina son ganinka in kana kusa mu haɗu a parking space".

"Bafa zan fito ba ko gidan baƙonka ne, ina cikin falona a zaune ka shigo mana".
Wata dariya usman yay harda ƙyaƙya tawa.
"Kaga farin shiga ungozo mar wake, seka gayawa wanda baida falon, Angon kwana biyu".
Ƙitt ya kashe wayar.
Murmushi yayi tare da miƙewa takalminshi ya zira a ƙafafunshi sannan ya ɗan tsaya gabanta.
"Zan ɗan fita sena dawo".
Tashi tayi cikin sauri, few mint ta ɗauko turare a ɗakinta, gabanshi ta tsaya a tsorace ta fesa mashi kaɗan a gaban rigarshi ta gaba.
"Allah ya tsare min mijina ya kareka daga dukkan sharri, ya hana idanunka kallon kowacce mace inba niba My nawa ni kaɗai".
Shikam dariyama tabashi ya raɓeta ya wuce yana yaba yadda take riritashi kamar ƙwai.
Sauka yay ƙasa tare da bude kofar falonshi ya fita harabar gidan.
Gate ɗin gidan ya buɗe ya fita part ɗin ammi ya nufa kanshi tsaye, a babban falo ya zauna a saman seater yana kallon tashar aljazeera.
Jin shurun yay yawa ya miƙe tare da buɗe kofar falon ya fita sabida yasan ƙilan ko bata tashi daga baccin data koma bane ba, sabida yau sunday babu aiki kowa yana gida shiyasa ko ina tsitt a gidan da alamun kowa yana hutawa ne.
A parking space ya tsaya tare da fiddo da wayarshi ya niman layin usman, cikin sauri usman ɗin ya ɗauki wayar bayan ya miƙe daga kishingiɗan dayake.
"Ganifa kona koma ban gankaba".
"A,a kajirani dan Allah yanzu xan bullo".
Katse wayar yayi yana ɗora hannunshi akan kirjinshi tare da ɗan kurawa gate ɗin usman idanu,mintuna kusan goma sega usman ya ɓullo, cikin mamaki Aliyu kebin usman da kallo ganin yadda yake sakin far'a fiye da wadda yasansa da ita.
Musabaha sukai sannan usman ɗin ya kalli Aliyu.
"Yaya maganarmu ta jiya a ina muka tsaya?"
Jimm yayi Da alamun ya manta sannan ya kalli usman ɗin.
"Ban fahimceka ba wace magana ce?".
Cikin ɗan zafin rai usman yace.
"Maganar ubanka banza marar mutunci to maganar ƴar mutane daka saka a tension".
Tsaki yaja ɗan kaɗan
"Lallai shehu kaci tuwo akaina yanzu akan maganar can kake zagina tnx".
Yafaɗa yana ɗan haɗe ranshi kaɗan.
"Kaga ba wannan ba yanzu kai mikake gani akan lamarin?".
Shafa gemunshi yay.
"Na ware kuɗin dazan bawa mamanta takaita bording school sabida no need mu ɗauko ƴar mutane batare da wani ƙwaƙwkwaran hujjaba domin nasan maman tata ma bazata bamu ba".
Dariyar baka da wayo usman yay mashi.
"Ƙurun ƙus! inji tatsuniyar gizo da ƙoƙi".
Inji usman sannan ya dubeshi.
"Kaga dan ALLAH ɗauko kuɗin semuje da wuri mukaiwa maman tata kawai, kaga zuwa gobe monday se a sama mata makarantar".
Zaro idanunshi yay.

"To sarkin azarbabi tayaya zamuje gidan mutane da wanna ranar dake kawo kai nikam bazan fita ba gaskiya".
Murmushi  yadda ze mar ram yay usman sannan yace.
"Ok zuwa dare insha Allahu semuje can gidan pls dan Allah karka ɓatamin lokaci".
Ɗan nazarinshi yake sannan yace.
"Wai nikam kodai da wadda ka haskone agidan kakeso irin wannan rawar ƙafa haka, kamar kai abin yashafa naga kawani damen wallahi inda nasan akan wannan shirmen nakane da babu abinda ze saka na fito da wannan ranar".
Gaban usman ne ya faɗi yana gudun kada shirinshi ya watse, amman daya tuna yadda ze masa zarge yasa yaɗan saki fuskarshi.
"Cool down karka damu koni ka bawa kuɗin sena kai musu can ɗin babu matsala, ai amman da amutunce kazo mukai masu tare kadama kuma ka kaiwa mamanta kudin muje gidan wannan kakan nata semu kai mashi tare da damƙa masa komai daga karshe muyi mashi bayanin yadda ze sakata a makarantar kwanan batare da kowa yajiba bare a damesu".
Kallon kana shirme yaywa usman amman bai ce komai ba.
"Nidai ga abinda nai niyya kaga ni se anjima" yafaɗa yana barin wajan.
Gumi ke tsirgawa usman kota ina.
Abinda yasa bai gayawa Aliyu haƙiƙanin gaskiyar lamarin ba sabida gudun rikicinsa ze iya tarwatsa wannan lamarin tunkafin abu yay nisa yafison ya ribace shi suje gaban malam, tare sannan malam ɗin ya damƙawa Alin amanar bebi daga nan kuma yasan komai zezo masa cikin sauki amman a haka akwai rikici idan yace ze gaya masa kai tsaye dan haka shima nufar part ɗinshi yay yana ayyana insha Allah ayau zasuje gaban malam maɗaurin auren bebi inda yuwuwa su tawo da ita yau in kuma Alin bai yarda ba abarta har zuwa wani lokacin kafin suga abinda Allah ze xartar.

Mama tana shiga ɗakin taga bebi ta kifa kanta tana kuka!
Ƴan biyu duk sun xagayeta suma gwanin tausayi sabida sunajin duk abinda ya faru.
Cikin rarrashi mama taje gabanta.
"Bebi maye na kukan tunda ALLAH ya ƙetarar dake auren wancan yaron, ina ba godiya xakiba da Allah ya kawo maki sauyi tare da fatarwa kanki Alkairi".
Ɗagowa tayi tana kallon mama.
"Mama banfa sanshi ba, kenan auren dole kukai min sabida bakwa sona?"
Shafa kanta mama tayi.
"Koma waye zaki ganshi kuma a sannu zaki bam bance komai".
Kukan ta cigaba dayi.
"Mama nida ko miyar kuka ban iyaba sannan kumin aure".
Duk da mama tana cikin damuwa amman seda ta dara da shirmen bebi tana raya Allah yasa Aliyu ya iya da shirmen ƴar tata.

Can kuwa gidansu tasi'u matansu ne suka shirya tsakar gida tare da shinfiɗa manyan tabarmai na karɓar baƙi ƴan kawo lefen da za,a ɗaura auren gobe, ƙarfe ukun yammacin ranar............

*Afa shirya daren nan yaya Aliyu zeji maganar ɗaurin auren da usman yay masa jagaba ayi? wanda shi bai san dashiba? hohoho harna hasko madam bebi tai ido biyu da gadanga a wannan dare a matsayin mijinta*..............................

SU TASI'U KUNA RUWA FA

*PART* 2

NAKUƊINE

*71*

"Ni zaka mayar mahaukaci,ina maka magana kaimin banza sabida ka ɗaukeni ban san minakeyi bako?".
Aliyu ya dubi usman wanda hankalinshi ke kan driving yake gaya mishi hakan.
"To yaya kakeson nace maka? cewafa kayi na taka ƙulli yau kuwa zakaga na taka ƙulli ganin idanunka".
Usman ya faɗa yana dariya,Tsaki yaɗanja kaɗan tare da fiddo da wayarshi yana neman layin Alhaji aminu abokin business ɗinshi, ringing ɗaya Alhaji aminun ya ɗauki wayar Gaisawa sukai ya soma yi mashi bayani akan harkokinsu wanda har suka ƙarasa unguwar su Bebi bai daina wayarba har seda usman ya shiga cikin layin sannan ya kashe motar ya zubawa Aliyun idanu tare da jiran ya gama wayar su shiga cikin gidan.
Sun kai kimanin mintuna goma acikin motar usman yana faman jiranshi agogon dake hannunshi ya kalla tara saura na dare.
Alokacin shikuma ya kammala wayar yana ajeta cikin aljihun wondonshi sannan ya dubi usman ɗin.
"Kaje ka fito ina nan ni kasan babu inda zan bika".

Haɗe hannaye usman yayi kamar ze zuba ihu sannan ya dubi Aliyun.
"Haba angon dija kaiwa girman Allah kazo muje kaga inna ga idanunka bazan zauna kamar rannan ba musamman in kana zabgomin harara da idanunka".
Shi dariyama usman ɗin ya bashi amman dayake wanda ya rigaka kwana tofa seya rigaka wayo seda usman yasan yadda yayi ya ribace shi ya fito yana mita suka ƙarasa ƙofar gidan agarin saurima seda Aliyu ya ƙume da ƙofar gidan, yana ayyana insha Allah ze taimaka masu a gyara musu gidan dan ƙofar kaɗai ma se taima mutum illah.
Daga bakin ƙofa usman yaɗan dakata tare da ɗaga murya kaɗan yay sallama.
Mama dake saurararan malam wanda ke mata bayani akan mahaifinsu Aliyu, ita tai saurin amsa sallamar kuma atake anan taji sanyi ya ratsa mata zuciyarta sabida tun ɗazu acikin zuciyarta zulumin yadda mijin Bebi yay biris da zuwan take.
Cikin sauri ta ɗauko babbar tabarma ta baje a tsakar gidan akusa da malam sannan ta gyara mayafinta wanda ya kuma haskata sannan ya fito mata da ainihin kyawunta na hausa fulanin Usul.
Usman ke gaba Aliyu na bayanshi, Cikin nutsuwa suka ƙarasa cikin gidan zama sukai akan tabarma da mama ta shinfiɗa musu.
Cikin Ikunya usman ya gaisar da malam tare da mama, Shiko Aliyu ko ajikinshi cikin sakin jiki ya gaisar dasu duka biyun yana duban malam.
"Niko baba kamar naso gane fuskar nan wallahi?"
Cewar Aliyu yana ɗan nazarin inda yasan malam lado.
Shima malam se a sannan ya dubi Aliyu da kyau sannan yace.
"Lah kar dai wannan yaron ne wanda kataɓa kawoni gida kwanakin baya bani da lafiya ina titi ka ganni a zaune ka tsaya ka ɗaukoni harka bani kuɗi aiko na ganeka ɗan kirki".
Murmushi Aliyu yay.
"Allah sarki baba nine naso sake komowa na ganka kuma senai tafiya Allah bai nufa ba se yau".
Yafaɗa yana kallon malam.
"Masha Allah hakan ma nagode sosai in wanine ma ai baze kalleka ba".
Sannan ya juya yana kallon mama wadda kanta ke sunkuye.
"Wato Aishatu na jima banga yaron arziki mai tausayi irin wannan bawan ALLAH ba, kwanakin baya naje kasuwa wajan wani abokinmu, zan masa ta,aziya wallahi bayan na dawo se ciwon kai da kumallo ya kamani a hanya sena zauna bakin wata bishiya ina dafe kaina, sabida juwar data kamani kawai senaga wannan yaro akaina yay min sallama cikin nutsuwa , yana tambayata baba mai yake damunka haka, sena ɗago nace masa kaina ke ciwo da kuma juwa wallahi aisha bakiga yadda ɗannan ya damuba da kanshi ya ɗagoni ya sakani amotarshi yacemin ze kaini asibiti a dubani abani magani nace masa yabari innaje gida inada maganina, kinsan seda ya kawoni har bakin layin gidana sannan ya ɗauki dubu ashirin ya bani, wato Aisha wannan yaro ɗan arzikine, amman yanzu na daina mamakin alkairinsa tunda bai ɗauka abanza ba jinin alhaji idirisa ai dole ya gaji alkairi".
Yafaɗa yana kallon Aliyun da yabawa.
Shiko ko ɗago kanshi bai ba amman yana mamakin yadda har yau mutumin bai manta yadda akaiba lokacin shima ya dawo daga office ne lamarin ya faru, shaff ya kuma mance, da batun seda yaga fuskar tsohon sannan ya shaida shi kuma abin ya faɗo masa.
"Wallahi kam baba maganarka haka take Allah bamu dacewa kawai".

Cewar usman yana kallon malam danshi bai mamaki ba sabida kowa a gidansu yasan Aliyu akwai tausayi duk zafinshi yana da mugun tausayi aranshi.
"Masha Allah baba gwara da Allah yasa muka sameka anan ɗin kaga base munje can ba gashi na kawo maka baba seka damƙa masa amana".
Dariya malam yay yana kallon usman tare da cewa.
"Aiko ni ko birnin sin wannan yaro ze tafi da balki wallahi ban damu ba sabida tun kafin nasan shine na yaba bare kuma da Allah ya haɗani dashi na ganeshi kasan wannan shi ake kira da ka gina alkairi a baya domin ka girbi abinka agaba".
"To malam Aliyu ya kamata ka ɗago ka fuskance ni sosai tare da kunnen basira".
Cewar malam yana kallon fuskar Ali.wadda take can gefe guda.
Cikin nutsuwa kamala haiba Aliyu ya juyo yana kallon malam kacokan ya basa dukkan nutsuwar shi, aranshi yana mamakin komai ya kawo hakan oho?.
"Da farko dai Malam Aliyu ni dakaina da kuma wannan baiwar Allah".
Ya nuna mama da hannunshi.
Sannan ya cigaba.
"Muna miƙo buhun godiya wajanka da kuma yi maka addu,ar mai yawa mai albarka, yadda kai mana Allah yay maka yadda ka taimaki maraici ka rufa masa asiri kaima Allah ya duba bayanka kada ya wofantar dasu, naji abin alkairi a wajan ɗan uwanka abubakar da kuma usman mungode mungode"!!
Zaro manyan idanunshi waje yay waɗanda suka ƙara haska masa kyawunshi.
*WANNAN LITTAFI NA KUƊINE KADA KI KARANTA BAKI BIYABA NAIRA 200 BABU YAWA IN KINA BUƘATARSA TUN TUƁI WANNAN LAMBAR KAI TSAYE 08142105218*
Tare da kuma matukar mamakin mai yay masu haka suke masa godiyar data saka jikinshi yay sanyi.
"Aliyu ga amanar bilkisu nan mun baka har abada babu janyewa mun baka bilkisu kamar yadda ka buƙata kuma mun cika maka kudirinka na ɗaura muku aure ayau kamar yadda ka bukata harka turo mana usmanu da abubakar sabida haka yanzu muna jiran ta bakinka domin bama fatan balki ta kuma kwanar mana agida se agidan mijinta"
Cikin sauri usman ya tari numfashin malam.
"Ai malam wannan lamarin yay mana daɗi sosai Allah dai ya ƙara girma dayake shima ɗin yau kwananshi uku da yin auren farko amman duk da haka babu damuwa insha Allah zamu san abinyi sabida hakama bama bukatar komai naku Bebi kawai muke buƙata".
Wannan kalamin  na usman sune suka saka Ali ya farga ga batun nasu.
Innalillahi wa'inna'ilaihirraju'un hasbinallahu wani'imal'wakil!
Tabbas inba ƙarya kunnenshi yay mashiba usman yazo tare da abubakar yayansu sun karɓa masa auren wannan yarinya batare da saninshi ba.
Gumine ya soma fito masa ta saman goshinsa batare daya shiryaba.
Maganar mama ita takuma katse masa tunaninshi.
"Ni mahaifiyar Bebi ce nasan komai daga cikin halinta ina rokonka daka riken bebi amana intai ba dai dai ba ka hukunta min ita inda hali ka sakata a makaranta domin ta sami zurfin ilimi ko ze saka ta daina wannan shirmen nata nagode nagode................

Tofa akwai ƙura agaba

*PART* 2

NAKUƊINE

*68*

Ilahirin matan su tasi'u sun halarci zaman karɓar lefen har faɗa ake a tsakanin matan wannan tana cewa in aka kawo a ɗakinta za,a aje wannan nacewa in aka kawo a ɗakinta za,a aje sabida baƙin ƙudirin dasuka saka aransu na in aka aje a ɗakin kowacce zata saci wanda ranta keso.
Matar tasi'u ce ta miƙe tare da kallon sauran matan.
"Waini wannan maganganun da kuke duk kunsan na banxane sabida wannan dai aure mijina shine sanadin sa dan haka ko wacce taja gefe babu wadda zamu aje komai a ɗakinta".
Tafaɗa tana girgiza kamar wata ƙaura, shewarsu ce ta karaɗe tsakar gidan kafin ƙanwarsu tasiu mai suna suwaiba ta janyo matar tasiun tana mata magana.
"Haba keko lantana wannan fiffiƙa da kike duk bai daceba yanzu a misali kina cikin wannan faɗan matan dazasu kawo lefen su shigo dan Allah bakin bamu kunya ba".
Wata harara lantanar ta watsowa suwaiba tana cewa.
"Kinga nifa bazaki min ƙasa da muryar munafurciba duka ay gayyar mun santa kowa soyake arzikin yaje ɗakinsa dan haka ni banƙi suzo su ganni anan ba maye to abinda lefen rabewa zamuyi agidan".
Dariya duka sauran matan sukai tare da buɗa sannan kuma wajan ya kaure  da cece kuce sabida suwaiba tace lantana tayi mata rashin kunya.
Sosai wajan ya hargitse da faɗace faɗace har seda rabi'u ya fito daga majalissar dasuka dasa ta zaman jiran karɓar lefe ya shigo gidan ya tsawatar masu.
Tare da rufe suwaiba da faɗa yana cewa ina ruwanta da matansu, tana babba ai seta kama girmanta.
Ataƙaice dai suwaiba harda kukanta awajan tana cewa ai sun firfita matansu akanta, da ƙyar ƴarta dasuka zo tare ta rarrasheta sannan tai shuru shikuma rabiun ya fita ya barsu.
Ni kaina abinda na fahimta su kansu a junansu su tasiun babu shiri sosai a tsakaninsu kawai ta ciki na cikine.

Ƙarfe ukun ranar manyan santala santalan motoci masu kyau da tsari har guda uku sukai dafifi a ƙogar gidan marigayi alhaji muhammadu mai katifa.
Cikin rawar jiki tasi'u ya sheƙa a guje gaban baƙar siyanar farko ya buɗe yana zabgawa wata gajerar mace baƙa kirari tare da fadanci irin na masu maula.
Cikin yauki da gwalli wannan matar ke umartar shi daya kirawo yara su kwaso akwatunan, kafin wasu mata suma guda biyu suka fito daga bayan motar.
Ragowar matan cikin sauran motocin suma suka fito tare da xuwa gaban wannan matar suka tsaya cikin rawar jiki tasiu ya kirawo sauran ƴan uwanshi cike da ƙawa zuci suka buɗe boot ɗin motar suka soma fito da akwatuna masu kyau har guda goma sha biyu.
Banda manyan jakunkuna na gana masgo, guda uku da sauri suke shigar da kayan cikin gida har suka gama abinda ze baka mamaki yadda waɗannan matan suka tsaya ƙyam a wajan batare dasun shiga cikin gidan ba a ƙyamace wannan bakar matar tace
"Base mun shiga ba wannan zuwan ma dan Alhaji ya takuramu ne, mun saka biki nan da gobe ina amaryar zamu tafi can da ita sabida gyaran jiki?"
Wani gumine ke ratsowa tasiu sannan ya aro jarumtar cewa.
"A,a ai tana can wajan uwarta dama se goben zamu ɗauko muku ita".
Batare data kula da maganarshi ba taja tsaki kaɗan tare da faɗawa mota sauran ma suka mara mata baya haka ta badesu da ƙura tabar wajan.
Jan ajiyar zuciya yay mai ƙarfi tare da baza rigarshi yayi cikin gida, daman bai bada damar taɓa akwatunan ba harse da ya shigo gidan hakanan sauran suma suka shigo cikin gidan, zama tasi,u yay agefen akwatunan tare da fito da wayarshi waya sukai ta mintuna goma kafin ya miƙe ya fita waje.
Se gashi nan tare da wani magidancin mutum, buɗe masa akwatunan yay yana ɗaga masa kayan dasuka kusan zauta jama'ar wajan seda mutumin ya gama ɗaga dukkan kayan sannan yaɗan jawo tasiu suka fita waje.
"Kayan sunmin daman kasan akwai wanda ya bani order haɗa mashi lefe nan da sati biyu".
Cikin murna tasi'un yace.
"To yanzu yaya kenan kuɗinsu xasu kama sabida nagaya maka ni kudin nakeso ko?".
Murmushi mutumin yay tare da cewa.
"No karka damu kayan sunmin kuma zaka  sami alkairi mai yawa sabida kayan masu kyau ne".Batare da ɓata lokaciba sukai cinikin kayan lefen cikin farashi mai tsada wanda harya  saka tasi'u suman wucin gadi.
"Yanzu naxo da motana xan ɗibi kayan inya so gobe wajan yamma sekazo shagona nan inda ka ganni seka amshi kudin naka ko?".
Cikin zumuɗi tasi'un yace.
"To!to babu matsala muje semu taimaka maka da ɗauko ragowar".
Cikin jin daɗi mutumin ya shiga gidan yana marawa tasiu baya, su rabiu suna zaune sukaga anan fitar da akwatun suna tsoron suyi magana tasiu yaƙi rabon kuɗi dasu.
Har suka gama kwashe kayan sannan, sukai sallama da mutumin yaja motarshi yabar gidan.
Seda ya shigo yana share zufa sannan sani ya dubeshi.
"Ni naga ankwashe kayan nan ina zaka kaisu?".
Murmushin mugunta yay sannan ya dubesu.
"Dukkan abinda ze kawo mana ɓaraka bana sonshi dan haka na kirawo maƙocin gidan da

aishan take akan yazo ya ɗauki kayan nan ya kai masu can kunga gobe ƴan ɗauri aure kowa zega lefen nan daganan semu kwashe kayanmu kunga mun fita ko awajan alhajin ne koya kukaga?".
Dariya matarshi ta sheka sannan ta rangaɗa buɗa.
"Kai lallai banyi auren banza ba nagode Allah daya bani makirin miji tabbas wannan shawara taka haka take baban ladi da larai".
Ragowar matan ma da mazan dariya sukaitayi suna yaba wayon tasi'u tare da dubararsa suna kuma ɗaukin ganin gobe kodan yadda zasuyi babakere da wannan dukiya da aka sheƙo masu ta banza.
Kallon marasa wayo sakarkarun banza yake masu yana danne abinda ke ranshi ya tsallake yabar tsakar gidan yana saƙa mugun nufin dake ranshi.
Ni zasu ɗauka wawa naje nayo farauta sannan muyi raba dai dai to baku isaba waɗannan kaya sun tafi har abada, nidai fatana kawai mu haɗu gabaki ɗayanmu mu ɗaura wannan aure daganan kuma watan rashin mutuncina ze motsa akanku, sabida amfaninku ya kare gareni, shiyasa wancan ma kudin farkon na raba komai gida biyu na danne rabin na barmaku rabin mahaukatan banza da wofi, nan kwanaki uwata data rasu rasa wanda ze sai mana kokon zaman makoki akai acikinku ko kun xata ni wawa ne.
Yana tafe yana faɗin wannan maganar a ranshi harya karasa wajan mai tsiren dayake zama lokaci zuwa.lokaci ya zaro gudar dubu sabuwa dal wadda ya zare acikin kuɗin daya danne irin wanda ake sakowa asaman kayan lefe batare daya bari sauran sun ganiba tsirenshi aka yanka masa yaja gefe yana cin abinshi hankali kwance.

****************

Yau kam babu uwar da aka tsinana agidansu bebi sabida yadda ta ɗagawa kowa hankali hatta shahid dake wajan gawayinshi seda Tasa ihsan ta kira mata shi yana zuwa ta dubeshi.
"Shahid ka yafemin kaga yadda rayuwata zata koma ko? na tashi bada shirin aure ba yau an ɗaura min aure zanje nai zaman da bani da masaniyyar yadda zan kasance ko zaku sake ganina a raye ko rasuwa zanyi oho?".
Tafaɗa tana kwanciya a saman cinyar hussaina wadda itama kukan take.
Kai jama'a nimafa kaina seda nayi kukan sabida su bebi yadda suka taso bacci tare komansu tare bada ban auren ko mutuwa ba meze rabasu da junansu musamman ita da bata san waye mijin nataba batasan yaya zata tarki zaman auren ba infact ma bebi yarinya ce batada wani ilimi akan rayuwar aure ga auren nata yazo mata a kurewar lokaci batare da mama tai tunanin sanar da ita komai ba ya ALLAH ka bawa ALIYU ikon riƙe marainiyarka da amana amin, wannan itace addu,ar daya kamata muyiwa bebi kenan.
Cikin sanyin jiki shahid ke dubanta yana ayyana wannan lamari mai sarƙaƙiya shi kansa da mama ta gaya masa maganar auren bebi seda jikinshi yay sanyi.
"Ki kwantar da hankalinki ai xamuke zuwa sannan kuma bazaki mutuba insha ALLAHU ina miki fatan alkairi acikim zama aurenki shikuma ALLAH ya bashi ikon riƙeki da amana amin".
Yafaɗa yana share hawayenshi.
"Kaima haka zakace shahid yanzu shikenan na daina ganinka nadaina faɗa dakai nadaina cinye maka indomin ka"!!

Se ta kuma fashewa da wani irin kuka daya saka mama ta tsaya cak da haɗa mata kayan datakeyi a cikin jakarta.
Tasowa tai tana rarrashinta da ƙyar ta samu tai shuru sannan hassana ta fita dan ɗora girki ganin magariba ta ƙarato.
Ana idar da sallah mama tasa bebi ta shiga wanka..................

*PART* 2

NAKUƊINE

*69*

Da kuka da gaddama mama ta samu bebi ta yarda ta shiga wankan domin seda ta haɗa mata da jan idanu sannan ta shiga tana dira ƙafafunta a ƙasa kamar wata ƙaramar yarinya.
Bata wani jimaba ta fito ƙafafunta ma basusan mai tai ba, mama tana tsakar gida agaban murhu tana firfita gawayin data ɗiba ciki ta zuba acikin kaskon turaren wuta, itace ta ɗauko ta dubi Bebi da mamaki kafin ta ɗaga murya ta kira "Hassana! zo maza ki ganemin kafafun ƴar nan ni kada tace ban gani ba sosai gwarake ƴar zamani ce baki tsufaba" cewar mama tana makawa bebi harara.
Cikin dariya hassana ta fito daga ɗaki jikinta sanye da hijabin sallah tana cewa.
"Kai mama dan Allah in wani yaji base yazata ke tsohuwa bace duka dukafa mune na farko kuma.mudin nawa muke?" da sauri mama ta kwaɗo mata ɗan maficin dake hannunta cikin wasa da barkwanci tana ce mata.
"Ke banson shirme mukam ai shekaru sunja sekuma fatan cikawa da imani".
Murmushi hassana tayi tana furta amin sannan tabi kafafun bebi da kallo tana ƙunshe dariyarta.
"Haba hajiya bilkisu mai gadon zinare in bada ban abinki ba tayaya wannan kafa taga ruwa nima dai mama banga komai a wannan ƙafarba".
Tafaɗa tana ƙara bin ƙafafun bebin da kallo.
"Karki ɓatamin rai maza ki koma kije ki dirjen ƙafafun nan banson shirmen banza da wofi".
Tura baki tai ta kuma danna shi gaba kamar zata taɓo ƙofar gidan sannan ta dubi mama
Tare da zubo da hawaye sannan ta shiga banɗakin aikuwa ta bugo ƙofar da ƙarfi kamar zata ɓallata.
Watsa ruwa tai tare da saɓawa soson data haɗa da sabulu ta wanke ƙafar, tare da watso ruwa samanta sannan ta fito gaban rijiya taje ta ɗibi ruwa tai alwala batabi takan kowaba ta saka doguwar rigar da ko arzikin bra da pant babu haka ta zir ƙaton hijabi ta tayar da sallar tana

idawa ta soma azkar har akai sallan isha tana kan darduma.
Tana sakawa da kwancewar ƴan gidansu sun tsaneta gwarama ta tafi gidan mijin ko yankata ze ta zauna sabida yadda suka shareta sukai zamansu a tsakar gida.
Daga can tsakar gidan kuwa mama ta ƴan biyune zaune da arfa da ihsan da shahid sun zagaye kwanon gyaɗa suna ɓareta suna cin kayarsu, sabida mama taga take taken Bebi inta cika shiga harkarta damula komai zatayi wanda daman koda batai wannan auren bama ai aure yazama dole su kansu ƴan biyun nan da watanni ne sun tafi gidajen su, dan haka ta tattare kan ƴaƴanta suka barowa bebin ɗakin ita ɗaya suka baje a tsakar gida suna sharafin gabansu.
Wanda wannan shariyar ta kusan saka bebi bindigar zuci.
Sallamar malam lado itace ta katsewa mama labarin datake bawa ƴaƴan nata sannan ta amsa cikin sakin fuska tana ture gyaɗar gabanta.
Cikin sauri shahid ya samasa tabarma daga gefen ɗakin mama sannan suka gaisar da malam ɗin suka tattara suka bar wajan suka shiga ɗaki dukkansu sabida a tarbiyar data basu bazama agabanta in tai baƙo ko wani irine kuwa baƙon.
"Malam ina wuni ina gajiya yaya hidima kuma angode ALLAH ya ƙara girma amin".
Tafaɗa tana ɗan gyara mayafin dake jikinta.
"Alhamdulillahi mijin nata basu ƙaraso ba, naji shurune nima yasa nace bara na shigo sabida, halin rayuwa ALLAH yasa dai lafiya danni bana ƙaunar gobe waɗancan azzaluman su tarar da ita a gabanmu sabida zasu iya yin komai domin ganin sun hana tariyarta".
Gaban mama ne ya tsinke ya faɗi nan da nan wata zufa take kara kaini bisa goshinta shaff ta manta da wannan cakwakiyar seda malam ɗin ya sanar mata dan har tana cewa bebi bazata tare ba setayi ɗan taronta ko iya yinin uwane, bayan haka kuma tana son amsar adashinta taɗan saiwa bebi kayan ɗaki dana tsakar gida sabida babu lefe kuma itama komai yazo mata a kure bare tai shirinta irin na uwa mace.
"Basu zoba malam amman meze hana mu kaita ko gidansu iya ne in yaso duk sanda yazo semu ɗauko ta ni wannan masifa dame tai kama"!
Murmushi malam yay irin nasu na manya sannan ya dubi mama yace.
"Haba Aishatu ai zancen masifa ya kare sedai duk wanda ya ɗauko da zafi ta faɗa masa, itadai yarinya ALLAH ya rufa mata asiri".
Yan nisa da maganar sannan ya cigaba da cewa...........................
"Abu nagaba kuma shine dagani harke a yanxu alhakin haƙƙin bilkisu ya sauka daga kammu yana hannun shi mijin nata dan haka bazamu zartar da komaiba harse munji daga bakin shi mijin nata sannan semuji abinda yake da akwai, amman ni a tunanina mu miƙa yarinyar nan gaban mijinta yafi inyaso komi ze faru daga baya semuji".
Ɗan nazarin maganar malam mama tayi sannan ta ɗora da cewa.
"Hakan yafi ai duk abinda kace babu fashi malam ina laifinka daka tsaya mana kafa tuna wannan gidan damuke ciki kai kabamu me muka haɗa dakai inba mutuncinba tabbas kaimana abinda ALLAH ne kaɗai ze biyaka badai mutumba, haka zalika iyalanka suma sunyi mana domin komai na rayuwa baya faruwa seda sanadi tare da sila, yau inda rahinatu ɗiyarka ta farko batazomin da maganar cinikin kamfaniba da tayaya wannan yaro zega bebi aikwa kaga komai ya faru damu na alkairi kaine sanadi malam ni mutum ce wadda tasan alkairi komai kankantar sa hakanan komai girmansa wallahi yadda mahaifinsu ze zartar da komai akansu batare danai musuba tofa kaima ɗin hakane dan haka waɗannan yara nawa jikokin kane halak malak malam

se yadda kace kuma nagode da yadda ka nunamin akan yaran nan ALLAH yasa ta dalilinsu a rayuwa ka huta kaji daɗi fiye da wanda kake ciki yanzu".
Murmushi malam yay tare da furta.
"Amin Aishatu!Ai kinsan rayuwar duniya inji ɗan hausa yace inkaji wane ba banza ba, in bai sha wuyar dare ba tofa yasha ta rana! dan haka kowa kagani da arziƙinshi, sefa yasha wahala kafin ya sami arzkin, shi kansa mahaifin yaron daya auri balkin ai ɗan ƙauye ne!a ɗanbatta yake bakiga gwaramar dayasha ba kafin yazama hakan, wallahi bantaba ganin mutum irinshi ba yasan darajar ɗan adam akwai alkairi inkinga yadda yake taimako agarin nan se ALLAH shiyasa nai farin ciki da balki ta auri ɗansa na cikinsa ko badan arzkinsuba wallahi iya karamcinsu ma da tarbiyrsu abinso ne".
Cikin mamaki mama ta dubi malam tana tambayarshi daman yasan gidansu Usman?.
Sosai malam ya gyara zama yana fayyace mata kyawun hali irin na mahaifin Aliyu.

Aliyu tunda ya shiga ɗakinshi bai fitoba seda akai sallar azahar yay sallah sannan ya wuce part ɗin ammi anan ya sami nusaiba tana parking kaya yau zata koma abuja, sallama sukai ya wuce ɗakinshi na sama, wanda iya kayanshi kawai ya ɗauka amman yadda ɗakin yake haka yake ba,a sauya komaiba, Coffee ya haɗa tare da fitowa falonshi ya xauna yana kallo yana kurɓar abinshi.
Har xuwa sallar la'asar sannan ya sauko kasa lokacin ya sami ganin ammi suka gaisa da ita sannan ya wuce wajan abba suka gaisa suka wuce masallaci tare, atare sukai sallah suka fito, sannan shi ya wuce part ɗinshi.
Lokacin daya shiga cikin falonshi na sama, ya tarar da daining table shaƙe da manyan fulasai har wata fulawa aka saka ta decoration.
A tsakiyarsu sannan ga wani sassanyan kamshi dake dukan hancinshi bude kofar room ɗinshi yay ya shiga ya watsa ruwa duk yanajin kansa a takure sabida ya saba ayyukanshi a office wannan dalilin yasa hutun dayake yanzu bai masa daɗi, shirya kanshi yay cikin milk jallabiya mai dogon hannu, amman daga ciki ya saka black jeans, ya fesa turare ajikinshi ya taje sajenshi da gemunshi, sannan ya fito falo, wanda yay dai dai da lokacin da madam khadija ta fito daga nata ɗakin.
Jikinta sanye cikin wani ƙaton wando tare da amrless wandon jane amrless ɗin kuma baƙa, seta ɗora wata irin hula akanta wadda ta bawa dogon gashinta damar ɗamewa dayake dija tana da gashi babu laifi.
Cikin ɗanjin haushin daɗewarshi kaɗan take masa barka da zuwa batare da ɗaukiba.
Sannan ta nufi gaban daining tana faɗin.
"Gafa abincinka tun ɗazu nake jiranka shuru wai yo ina katafi?".
Shareta yay kamar wata uwarshi tana tuhumarshi amman seya basar yana rabeta ya wuce saman seater ya zauna.
Cikin sanyin jiki ta buɗe fulas ɗin ta ɗebo sakwarar data sha wuyar haɗata wadda tai masifar murzuwa tai daɗi ta zubo guda ɗaya tare da zuba miyar agushin datayi ta manja wadda taji bushashshen kifi, da ganda ta zuba masa gefen sakwarar, wadda miyar take ɗaukar kamshin kayan haɗin dataji.

Lemon kwakwa wanda yaji madara da kwakwa ta zubo masa, a glass cup tare da ɗauko plate ɗin sakwarar ta nufo gabanshi dasu ta aje agabansa tare da komawa ta ɗauko cokali mai yatsu ta saka aciki tare da kallonshi wanda yake rike da wayarshi yana latsawa.
"Na haɗa maka abincin".
"Nagode"
Yafaɗa yana saukowa daga saman kujerar ya zauna ya tanƙwashe ƙafafunshi ya janyo plate ɗin gabanshi.
Aranshi yana ayyana.
Baya son khadija ko kaɗan amman kyautatawarta gareshi yasa ya soma jin tausayinta acikin ranshi yanajin ze dinga bata farinciki kodan yadda itama take kokarin ganin ta kula dashi.
Bisimillah! yay tare da daukar cokalin ya soma kai abincin cikin bakinsa ya yaba da tsaftar khadija wannan dalilin yasa yaji bayada haufin cin dukkan abinda ta sarrafa sabida khadija irin mutanan nan ne masu tsabtar gaske ƴar gayuce ta gasken gaske.
Baƙaramin daɗi sakwarar tayi mashi ba haka nan ya cinyeta tass lokacin daya ɗauki lemon kwakwar yasha jiyay kamar ya sautu dan garɗi da daɗi amman dayake gogan boss ne yasa ya kanne.
Amman ya dubeta tare da ce mata.
"Nagode na yaba tabbas kin kware wajan iya girki nagode".
Wani farin ciki taji aranta wanda ya wanke laifinsa wanda take gani na daɗewar dayayi  dakuma wanda yay mata na halin ko in kula tabbas kowa yana son yabo musamman macen data kyautatawa mijinta tofa tanajin dadi matuka gaya inya yabeta, rashin yabo kwa kan saka tsana da ƙosawa acikin kowani abu.
Lumshe idanunta tai ta budesu tarr akanshi tare da cewa.
"Hakika naji dadin yadda mijina ya yabi girkina tabbas na shaida kai mutum ne nagari mai adalci yadda baka sona baka kaunata, inda wanine da dawannan damar ze musgunamin azamantake war auranmu  yakuma gasani, amman kai dayake kana  da adalci bakaimin hakaba, duk da bana hango soyayyata a idanunka amman ina hango tsantsar adalci acikinsu nagodewa Allah daya azurtani da mijin ƙwarai ina rokonsa daya saka soyayyata azuciyarka yakuma sa dagani bazaka kuma kallon wata mace da sunan aure ba"!
Kallon kasan idanu yay mata tare da jan kanshi gefe yana mamakin zafin kishinta akanshi.
Kwashe kwanukan tayi daga wajan ta tsaftace gun sannan tai cikin ɗakinta sabida tana tunanin baya da yawan son magana kota zauna wajanshi zata wahalane kawai amman baze tankata ba.
Tashi yay tsam ya bita cikin ɗakin.
tana gaban madubi a tsaye tana kallon kanta
Ya shigo a bayanta ya tsaya ya dafa gadon bayan nata.
"Dija miyasa dana kusance a first night ɗinmu naji zafi sannan kuma ragowar kinfini saninsu tunda ke mace ce?".
Yafaɗa yana kallonta ta cikin madubin.
Idanunta ne ya ciko da ƙwalla.
"Idan na cigaba da kallonki ahaka zan iya cutar dake sabida bansan irin halittar bukatarki ba nikuma ga yanayin dana keji in ina having sex dake"
"Yaya badagani bane ba, wallahi amman insha Allah zanyi kokarin ganin na kauda matsalar"!.

"Dagani ne kenan?"
Yafaɗa idanunshi cikin nata.
"A,a kaga baki ɗayanmu a wannan karon mukai yin farko to anty tace dole zamuji zafi kafin kuma muzama ƴan gari".
"How muzam ƴan gari dija najifa ana faɗin irin runbun daɗin da ake shiga in ana having sex toni miyasa banjiba se tsabar azaba da zafi daya addaben ina rokonki akan kije ki nemi maganin sanyi sabida nayi serching akan abinda yake kawowa ma'aurata irin wannan matsalolin, niba azzalumin mutum bane bansan irin bukatarkiba dan haka bazan kalleki hakaba inƙi biya maki bukatunkiba sabida banason jefaki cikin wani hali, sabida haka xan miki transper na kuɗi masu yawa akan kinemi maganin matsalarki tunda ance na ku mata kunfimu sanin kan komai hakan yay maki?".
Yafaɗa yana riko west dinta.
wani zullo tai tare da kwanto mishi tana yaba halinshi na ƙwarai dan in wanine bafa ze lura da wannan matsalolin nataba sema dai yay amfani dasu domin munana mata.
"Nagode da fahimta kuma zan nema ALLAH ya saka maka da aljanna amin".
Kiss ya manna mata a gadon bayanta sannan yabar dakin da sauri.
Tsalle tai ta faɗa saman gado tana ɗaukar wayarta domin kiran yaya ruma......................

*PART* 2

NAKUƊINE

*70*

Ringing!  ɗaya anty ruma ta ɗauka tana faman yiwa khadija kirari.
"A,a kaga manya-manya maganin ƙananun ƙwari hajiya dije ikon ALLAH mata agidan Alhaji Ali mai atamfa da girman kujerarki ƙanwata shalelena ke ɗaya tilo abar son ruma da umma".
Tafaɗa tana gyara zamanta domin jin batu.
Cikin wani irin girman kai tare da izza mai ƙarfi khadija ta lumshe idanunta ta buɗesu cikin tsananin son mijinta sannan tace.
"Kai my aunty duk wannan kirarin ni ɗaya wallahi kyasaka kaina ya zautu amman naji daɗi dan haka wallahi kincin kyauta anty ki turomin account ɗinki na baki ko ƴar 100k ce sabida oga ya kunce aljihu".
Cikin mamaki tare da murna anty ruma tace.
"What kina nufin Aliyu ya soma yi maki tunbuɗin daloli ne dahar kikai min wannan unexpected

na wannan kyauta mai tsoka?"
Gyara kwanciyar ta tai tare da kama pillow ta rungume tanajin feeling yana taso mata.
"Yes am telling the trues aunty ruma na rantse shiya ce na bashi accnt ɗina yay min transper na kuɗi sabida wannan matsalar damuka tauna dake last wayarmu kin ganeta?".
Jimm anty ruma tai kafin kuma tace.
"Yes na gane mana, yanzu ke mekike gani? duk da hakafa inaganin ya soma sonki sabida kyautar dayama umma kema kuma gata yawan kudin daya baki wallahi yafi karfin magani inaganin harda gifts na first night ɗinku".
Murmushi khadija tayi.
"Nidai anty ba wannnan ba wallahi wannan guy ɗin yanada son jikinshi sosai kinga fa yagama gayamin wai yaji zafi rannan that means fa baze kuma kusantata ba, nikuma kinsan ALLAH yanzu haka a buƙace nike banjin zan kai dare banji yay min check up ba".
Wata irin dariya anty ruma ta kece da ita har tana yada ɗiyarta.
"Kai wannan yarinya jarabar wa kika kwaso haka danmu kam bamu da wannan jaraban, ok karki damu ai harkace ta kuɗi tunda kinada farcen susa ai magana ta ƙare dan haka zan nemi numbern ƴar maraɗi!insha ALLAH indai akan sanyine magana ta mutu sedai a tara wani jikon".
Dariya taɗanyi sannan tace.
"Anty bana ma fatan wani jikon insha Allah narabu dashi har abada sabida nagane illar sanyi yana kawo naƙasu sosai wajan auratayya, musamman gamu ƴan matan da muke gigin aure semuyita bankawa kammu maganin mata batare da mun waiwayi na infection ba".
Gyara xama ruma tai daga nata ɓarin sannan tace.
"Au kese yanzu kika san haka ai muddin mace tana da sanyi tofa ta kade wajan mijinta, sabida har fason gaba sanyi yana kawowa banda ƙaiƙayi tare da kawo fitar farin ruwa, wannan dalilin zakiga namiji yana saurin gamsuwar dole a yayin auratayya macen kuma taji gabanta yana xafi kamar barkwano, kuma zata bushe ta ƙame batare da wani show ya fita ajikinta ba dan haka dole na mike na nema miki na sanyin nan sabida ki sami fadar gaban goshi wajan oga".
Jikin dija yayi mugun sanyi ƙalau sabida ba tun yau takejin wannan sing ɗinba amman tai burus da lamarin ashe ze kaita jin takaici gaba gashinan tunmma kafin aje ko ina mijinta ya fara complain.
"Anty pls ki tai makamin wallahi ina cikin matsala sabida ina hango wutar jaraba a idanun Hydar tabbas idan nai sake tofa wankin hula zekaini ga dare domin mijina daga jiya na bam-bance cewar shiɗin mabukaci ne kuma akan wannan sabgar ze iya losing komai domin yaji daɗi kingakwa in idanunshi ya bude ze iya kwasomin wata a matsayin amarya".
Dariya anty ruma tai.
"Maganarki dutse kanwata karkiga kina da tsafta kin iya girki wallahi namiji ze iya auro ƙazama matuƙar head quater ɗinta da gyara sedai kiji ihunsu a ɗaki keda kike tsaftar anbarki da kayarki, namiji babu ruwanshi da kyan fuska ko wani abu matukar yana samun gamsuwa wajan harka baya da matsala, wani xakiga koda ya auro mai kyau ɗin matukar yajita ƙamas wallahi seya auro wata in kuma ka hanashi karin auren tofa tabbas zaki samu kishiyar waje".
Gumine ya tsirgowa khadija cikin sauri tacewa anty ruma.
"Banjin Aliyu ze iya zama da ƙazamar mace muddin rai sedai ko inshi ze dinga hidim tamata, mubar wannan maganar mukoma ta.magani yaushe zan samu zan maki transper now".
"Zaki samu next week, eh nima ban goyi bayan ƙazanta ba but amman ina gaya maki

mahimmancin ni'imar jikin mace ne yakan saka namiji zautuwa duk girman kanshi da izzarshi, amman ina ƙazanta tayi, yadda kike da tsaftar nan da iya girkin nan wallahi kika haɗa ni'imar jikinki sekin sace zuciyar Aliyu, dan haka karki damu insha Allah nan da next week zan yi kokarin ganin maganin yazo hannunki amman ki turo kuɗinki mai kauri sabida kinsan harkar magani baka san yadda za,a ƙa'ide maka ba".
"Okey anty babu matsala yanxu zan miki transper ɗin nagode Allah ƙara girma Allah bar mana zumuncin mu amin".
Murmushi anty ruma tayi daga nata ɓangaren sannan tace.
"Koda kudina ne ai xan miki kanwata Allah dai yay mana jagora amin".
Suka katse wayar bayan sunyi sallama da junansu khadija ta koma tai lamo tana nazarin maganar anty ruma.

Cikin ƙayataccen room ɗinshi ya shiga system ɗinshi  ya ɗauko ya zauna akan sopa ya ɗorata akan cinyarshi yana duba aikin kamfaninshi na tokarawa, wanda insha Allah next mounth yake tunanin buɗeshi yanzu abubuwan dasuka rage mashi kaɗanne amman kafin nan yana son fita waje sabida shigo da wasu kayan, dan haka yake son komai ya kammala cikin next week insha Allah, ranar friday ma yakeson shiga can ɗin inyaso inya gama komai se yay zancen viza maganar dasuka gama yi da abbanshi ɗazu kenan.
Har aka kira magariba yana zaune, seda aka kusan tayarwa sannan ya aje system ɗin bayan ya kasheta ya shiga bathroom ya dauro alwala ya ɗauki wayarshi ya fice daga ɗakin.
Seda ya karasa room ɗin dija yace mata ta tashi tai sallah sannan ya fita, wannan karonma ta bishi ta fesa masa turare sannan tai mashi adawo lafiya kana ta koma ɗakinta.
Masallaci ya nufa wanda cikin lokaci ƙalilan aka tayar da sallar, suna idarwa ya zauna cikin masallacin ya gabatar da azkar ɗinshi sannan ya soma lazimi.
Har akayi sallar isha'i yana zaune seda aka kira sallah aka idar sannan ya fito.
Kusan atare suka jero shida ya abbakar a harabar gidan suka tsaya suna hirarrakinsu akan maganar sabon kamfanin da Aliyun yakeson buɗewa.
Cikin barkwanci ya abbakar yake cewa Aliyun.
"A,a kaifa ƙaninnan nawa duniyar tai maka kyau ga amarya ga sabon kamfani sauran sabuwar mota, koda yake kai yanzu aiko jirgi zaka iya siya ba mota ba kana lokaci kaninmu".
Yafaɗa yana dukan gefen kafaɗunshi.
Cikin mamaki ya dubi ya abbakar yana yamutse fuska amarya kuma?yana mamakin jin hakan seda ya tuna da batun dija sannan ya saki murmushi batare dayace komaiba.
Wayarshi dake cikin jeans ɗinshi ita ta soma ringing lokacin kusan takwas takusama.
Da sauri ya fito da ita lokacin ne kuma ya abbakar yay mashi sallama ya wuce nashi part ɗin.
Ganin usman ke mashi wayarsa yasa ya ɗanja tsuka kaɗan yana karawa a kunnenshi.
"Ango kana ina haka?".
Yafaɗa daga cikin wayar cike da zolaya.
"Kai ni banson wannan suna faɗi matsalarka malam"
Dariya usman yay yana ayyana nai maka tarko dan ubanka amman a fili seyace.
"Ina tambayarka kana ina haka?"
"Ina compound amman inka kara minti ɗaya baka karasoba zan koma gida sabida ina da uzirin dake gabana".

Tun kafin ya katse wayar yaga usman agabanshi kamarma wanda yayi gudu".
Murmushi ya saki yana miƙawa usman ɗin hannu sukai musabaha sannan yace mai.
"Lafiya kira da wannan tsakar daren" yana ɗage girarshi ta ƙasa.
Dariya usman yay ƴar kaɗan sannan yace.
"Nazo kamin rakiya dan darajar Allah kada kacemin A,a kaji ɗan ƙanina".
Yafaɗi yana haɗe hannayenshi alamun roƙo.
Shafa sumar kanshi yay wadda bata cika yawaba tare da kallon usman.
"Amman gaskiya banson mujima kamar rannan sabida kaga yanayin garin ana walƙiya kuma kasan bana son dukan ruwa zazzaɓi kesani".
Murmushi usman yay yana kaɗa keyn motar hannunshi sannan ya kalli Aliyun.
"Karka damu amman pls ka sauya kayan jikinka kasaka manya dan ALLAH".
Wani wawan kallo yay mashi.
"Kasan girman Allah bafa zan sauyaba sabida ba zance zaniba kuma ba surukai zanje ganiba in shigata batai maka ba sedai ka hakura da rakiyar tawa kai tafiyarka".
Cikin sauri usman yace.
"Wane mutum naƙi kabini maza muje hakan ai jallabiya cema".
Bai maganaba se jan kafafunshi dayay suka nufi parking space.
Wata white honda accourd 016, mai black tinted windows,suka nufa usman ya shiga driver site shikuma Aliyu ya shiga emty site na kusa da driver cikin sauri usman ya fisgi motar ya nufi gate yana danna uban horn.
"Kaga malam akan gidan masu dambu wallahi baxaka zubar daniba in kasan wannan ɗanyen gudun zakai sena sauka haba wannan gida in zakaje kullum jikinka yana rawa kamar ka taka ƙulli a ƙofar gidan".
Usman yana jinshi yana kunshe dariya yasan duk sanadin zamewa yake nema shiyasa yay mashi tsitt yabarshi akan insun je can ɗin ayita ta ƙare.............

*TOFA ANZO WAJAN! INNAGA RUWAN COMMENTS ZANYI KOKARIN BAYARDA 71 AKAN KARI INSHA ALLAH*

💃💃💃💃💃 Haɗuwar gadanga da bebi!   #team dija how market😛😛😜

*PART* 2

NAKUƊINE

*71*

"Ni zaka mayar mahaukaci,ina maka magana kaimin banza sabida ka ɗaukeni ban san minakeyi bako?".
Aliyu ya dubi usman wanda hankalinshi ke kan driving yake gaya mishi hakan.
"To yaya kakeson nace maka? cewafa kayi na taka ƙulli yau kuwa zakaga na taka ƙulli ganin idanunka".
Usman ya faɗa yana dariya,Tsaki yaɗanja kaɗan tare da fiddo da wayarshi yana neman layin Alhaji aminu abokin business ɗinshi, ringing ɗaya Alhaji aminun ya ɗauki wayar Gaisawa sukai ya soma yi mashi bayani akan harkokinsu wanda har suka ƙarasa unguwar su Bebi bai daina wayarba har seda usman ya shiga cikin layin sannan ya kashe motar ya zubawa Aliyun idanu tare da jiran ya gama wayar su shiga cikin gidan.
Sun kai kimanin mintuna goma acikin motar usman yana faman jiranshi agogon dake hannunshi ya kalla tara saura na dare.
Alokacin shikuma ya kammala wayar yana ajeta cikin aljihun wondonshi sannan ya dubi usman ɗin.
"Kaje ka fito ina nan ni kasan babu inda zan bika".
Haɗe hannaye usman yayi kamar ze zuba ihu sannan ya dubi Aliyun.
"Haba angon dija kaiwa girman Allah kazo muje kaga inna ga idanunka bazan zauna kamar rannan ba musamman in kana zabgomin harara da idanunka".
Shi dariyama usman ɗin ya bashi amman dayake wanda ya rigaka kwana tofa seya rigaka wayo seda usman yasan yadda yayi ya ribace shi ya fito yana mita suka ƙarasa ƙofar gidan agarin saurima seda Aliyu ya ƙume da ƙofar gidan, yana ayyana insha Allah ze taimaka masu a gyara musu gidan dan ƙofar kaɗai ma se taima mutum illah.
Daga bakin ƙofa usman yaɗan dakata tare da ɗaga murya kaɗan yay sallama.
Mama dake sauraran malam wanda ke mata bayani akan mahaifinsu Aliyu, ita tai saurin amsa sallamar kuma atake anan taji sanyi ya ratsa mata zuciyarta sabida tun ɗazu acikin zuciyarta zulumin yadda mijin Bebi yay biris da zuwan take.
Cikin sauri ta ɗauko babbar tabarma ta baje a tsakar gidan akusa da malam sannan ta gyara mayafinta wanda ya kuma haskata sannan ya fito mata da ainihin kyawunta na hausa fulanin Usul.
Usman ke gaba Aliyu na bayanshi, Cikin nutsuwa suka ƙarasa cikin gidan zama sukai akan tabarma da mama ta shinfiɗa musu.
Cikin Ikunya usman ya gaisar da malam tare da mama, Shiko Aliyu ko ajikinshi cikin sakin jiki ya gaisar dasu duka biyun yana duban malam.
"Niko baba kamar naso gane fuskar nan wallahi?"
Cewar Aliyu yana ɗan nazarin inda yasan malam lado.
Shima malam se a sannan ya dubi Aliyu da kyau sannan yace.

"Lah kar dai wannan yaron ne wanda kataɓa kawoni gida kwanakin baya bani da lafiya ina titi ka ganni a zaune ka tsaya ka ɗaukoni harka bani kuɗi aiko na ganeka ɗan kirki".
Murmushi Aliyu yay.
"Allah sarki baba nine naso sake komowa na ganka kuma senai tafiya Allah bai nufa ba se yau".
Yafaɗa yana kallon malam.
"Masha Allah hakan ma nagode sosai in wanine ma ai baze kalleka ba".
Sannan ya juya yana kallon mama wadda kanta ke sunkuye.
"Wato Aishatu na jima banga yaron arziƙi mai tausayi irin wannan bawan ALLAH ba, kwanakin baya naje kasuwa wajan wani abokinmu, zan masa ta,aziya wallahi bayan na dawo se ciwon kai da kumallo ya kamani a hanya sena zauna bakin wata bishiya ina dafe kaina, sabida juwar data kamani kawai senaga wannan yaro akaina yay min sallama cikin nutsuwa , yana tambayata baba mai yake damunka haka, sena ɗago nace masa kaina ke ciwo da kuma juwa wallahi aisha bakiga yadda ɗannan ya damuba da kanshi ya ɗagoni ya sakani amotarshi yacemin ze kaini asibiti a dubani abani magani nace masa yabari innaje gida inada maganina, kinsan seda ya kawoni har bakin layin gidana sannan ya ɗauki dubu ashirin ya bani, wato Aisha wannan yaro ɗan arzikine, amman yanzu na daina mamakin alkairinsa tunda bai ɗauka abanza ba jinin alhaji idirisa ai dole ya gaji alkairi".
Yafaɗa yana kallon Aliyun da yabawa.
Shiko ko ɗago kanshi bai ba amman yana mamakin yadda har yau mutumin bai manta yadda akaiba lokacin shima ya dawo daga office ne lamarin ya faru, shaff ya kuma mance, da batun seda yaga fuskar tsohon sannan ya shaida shi kuma abin ya faɗo masa.
"Wallahi kam baba maganarka haka take Allah bamu dacewa kawai".
Cewar usman yana kallon malam danshi bai mamaki ba sabida kowa a gidansu yasan Aliyu akwai tausayi duk zafinshi yana da mugun tausayi aranshi.
"Masha Allah baba gwara da Allah yasa muka sameka anan ɗin kaga base munje can ba gashi na kawo maka baba seka damƙa masa amana".
Dariya malam yay yana kallon usman tare da cewa.
"Aiko ni ko birnin sin wannan yaro ze tafi da balki wallahi ban damu ba sabida tun kafin nasan shine na yaba bare kuma da Allah ya haɗani dashi na ganeshi kasan wannan shi ake kira da ka gina alkairi a baya domin ka girbi abinka agaba".
"To malam Aliyu ya kamata ka ɗago ka fuskance ni sosai tare da kunnen basira".
Cewar malam yana kallon fuskar Ali.wadda take can gefe guda.
Cikin nutsuwa kamala haiba Aliyu ya juyo yana kallon malam kacokan ya basa dukkan nutsuwar shi, aranshi yana mamakin komai ya kawo hakan oho?.
"Da farko dai Malam Aliyu ni dakaina da kuma wannan baiwar Allah".
Ya nuna mama da hannunshi.
Sannan ya cigaba.
"Muna miƙo buhun godiya wajanka da kuma yi maka addu,ar mai yawa mai albarka, yadda kai mana Allah yay maka yadda ka taimaki maraici ka rufa masa asiri kaima Allah ya duba bayanka kada ya wofantar dasu, naji abin alkairi a wajan ɗan uwanka abubakar da kuma usman mungode mungode"!!
Zaro manyan idanunshi waje yay waɗanda suka ƙara haska masa kyawunshi.
*WANNAN LITTAFI NA KUƊINE KADA KI KARANTA BAKI BIYABA NAIRA 200 BABU YAWA

IN KINA BUƘATARSA TUN TUƁI WANNAN LAMBAR KAI TSAYE 08142105218*
Tare da kuma matukar mamakin mai yay masu haka suke masa godiyar data saka jikinshi yay sanyi.
"Aliyu ga amanar bilkisu nan mun baka har abada babu janyewa mun baka bilkisu kamar yadda ka buƙata kuma mun cika maka kudirinka na ɗaura muku aure ayau kamar yadda ka bukata harka turo mana usmanu da abubakar sabida haka yanzu muna jiran ta bakinka domin bama fatan balki ta kuma kwanar mana agida se agidan mijinta"
Cikin sauri usman ya tari numfashin malam.
"Ai malam wannan lamarin yay mana daɗi sosai Allah dai ya ƙara girma dayake shima ɗin yau kwananshi uku da yin auren farko amman duk da haka babu damuwa insha Allah zamu san abinyi sabida hakama bama bukatar komai naku Bebi kawai muke buƙata".
Wannan kalamin  na usman sune suka saka Ali ya farga ga batun nasu.
Innalillahi wa'inna'ilaihirraju'un hasbinallahu wani'imal'wakil!
Tabbas inba ƙarya kunnenshi yay mashiba usman yazo tare da abubakar yayansu sun karɓa masa auren wannan yarinya batare da saninshi ba.
Gumine ya soma fito masa ta saman goshinsa batare daya shiryaba.
Maganar mama ita takuma katse masa tunaninshi.
"Ni mahaifiyar Bebi ce nasan komai daga cikin halinta ina rokonka daka riken bebi amana intai ba dai dai ba ka hukunta min ita inda hali ka sakata a makaranta domin ta sami zurfin ilimi ko ze saka ta daina wannan shirmen nata nagode nagode................

Tofa akwai ƙura agaba

*PART* 2

NAKUƊINE

*72*

Har mama ta kammala maganarta kansa yana sunkuye babu abinda ke ɗiga daga saman goshinsa face gumi wanda yake faman gudu kamar famfo idanunshi ya kaɗa yayi jajur jijiyar dake saman kanshi ta tashi tai wani irin firfitowa tai ruɗu-ruɗu.

Iya ƙololuwar tashin hankali ya shigeshi a wannan lokaci wannan shi ake kira ga ƙoshi ga kwanan yunwa m'ana shine.
Da farko ganin girma da darajar waɗannan bayin ALLAH na gabanshi bayajin ze iya mayar da kyautar da suka bashi wadda tun kafin su sanshi su san asalinshi suka ɗauki ƴa guda suka bashi wannan karamcin da sukai masa tabbas, baici ace ya watsa masu ƙasa a idanunsu ba.
Abu na biyu kuma shine, usman dayay mashi shigar sauri tabbas inda yanada dama a yanzu wadda ta wuce kunyar waɗannan bayin Allah nagabanshi dase yayiwa usman bazata domin bafa ze amshi auren ba sedai shi yasan yadda zeyi da ita sedai kuma tsananin kunyar waɗannan mutane na gabanshi yasa bayajin ze iya mayar da kyautar da ALLLAH ya bashi domin bai san ribar dazeci gaba ba.
Abu nagaba fargabar mahaifanshi musamman abba wanda baya kauce maganar alhaji babba, yasan a wannan karon zasu ɓata da abbanshi abinda bayaso kenan arayuwa yana mugun son mahaifanshi baya son ganin ɓacin ransu musamman akanshi.
Yasan abba ze masa faɗa ze fushi dashi a familynsu za,ayi rikici da gutsiri tsoma musamman akan yadda yaywa dija kishiya a kwana uku da aure yasan ko abbanshi ma zece dan yaga dija marainiyace yasa yay mata hakan,  sannan kuma daɗin tashin hankalin ta yaya zewa abba bayanin ya nemi aure batare daya sanar masa ba? batare daya sanarwa da kowa ba? yasan abba baze karɓi uzirin cewa usman shiya amsar masa auren ba tabbas laifin akanshi abba ze ɗora.
Wata zufar ya kuma sharcewa yana fidda huci sama-sama.
"Malam Aliyu bakace komiba muna jira daga bakinka ga dare yana kumayi?".
Cewar malam.
Maganar tsohonce ta katse shi, inda zasu lura dashi sanda ya ɗago zasuga yadda idanunshi ya kaɗa, duk da duhun tsakar gidan amman hasken farin wata yana haskasu.
Bai iya cewa komaiba sedai ilahirin maƙoshinsa ya bushe ƙamas domin babu alamun miyau acikin bakinshi.
"Malam inta shirya kawai zamu wuce da ita sabida dare yana yi".
Cewar usman cikin sauri.
Tayaya zasu bashi ƴarsu babu ɗan rakiya kamar yadda ake kai amarya a al'adance, babu kayan ɗaki babu taron biki, sannan batare dasun haɗata da kowa ba.
Yake faɗi cikin ranshi amman bara yaga gudun ruwansu.
"To usman Bebi fa kasan marainiyace ban sai mata komi na aure ba sabida bata isa ba, bayan haka ban sanar da wasu daga cikin ƴan uwana ba bare arakata ɗakinta, bakwa ganin hakan kamar ze xama ba dai dai ba garemu? bakwa ganin hakan kamar ze jawo mata raini wajan jama'ar gidanku, bawai ina nufin mahaifanku ba, nasan dai baza,a rasa jama'aba kunga za,a iya cewa kamar batada galihune yasa aka kawota haka".
"Mama karda ki damu ni usman nai maki alkawarin zanyiwa bebi komai wanda akewa amare insha Allahu mudai fatanmu kubamu bebi yau maganar yan zuwa ganinta kuma nida kaina zanzo na ɗaukeku kuga ɗakinta insha Allahu".
Saka mayafinta tai ta share fuskarta tana kallon yanayin Aliyu wanda jikinshi yayi sanyi ƙalau.
Ta cikin ƙwayar idanunshi yake kallon mama shima yana ayyana kardai matar nan kuka take? sekuma jikinshi ya kuma yin sanyi tausayin matar ya kamashi.
Can cikin ƙasan maƙoshinsa ya tattara dukkan kalamanshi da sukai saura.

Cikin gajiyawa da maganarsu yace.
"Hajiya ki daina kuka addu'a zaki mata akan Allah ya bata rinjaye akan komai, sannan ki mata fatan alkairi niba mutumin banza bane bawai yabon kaiba zan riƙe maki ita kamar ƙannena su hassana dan Allah hajiya ki daina kukan yana taɓamin zuciya senaga kamar kina tantama ne akammu, Kina zuwa unguwar yahya gusau ko yaro kika tambaya gidan Alhaji Idriss Mai atamfa!zai kaiki in kika tambayi Aliyu! kowa ya sanni nine ɗanshi na huɗu karki damu hajiya nagode da wannan karamcin naku nikuma Allah yasa kada na baku kunya amin".
Cikin tsananin mamaki usman ke kallonshi amman seya danne shima karba yay yana kuma yiwa mama bayani cikin kwantar da hankali.
Shima malam nasiha yakewa mama mai ratsa jiki.
"Haba Aishatu maye kuma na kukan! ai godiya xakiwa Allah daya kawoki wannan rana ba kuka ba haba aishatu addu,a xaki masu insha Allah komai ze tafi cikin farin ciki da albarka".
Share hawayen ta kumayi sannan ta ɗago tana kallon Aliyu still.
"Aliyu ina kuma damƙa maka amanar Bebi dan Allah ka kulamin da bebi ina son bebi ta shiga raina wallahi ba da ban waɗannan azzaluman dangin mahaifin nasuba, da babu abinda ze saka naiwa bebi aure yanzu sabida akwai tarin kuruciya da wauta atare da ita yana da kyau ta sami wayewa awasu abubuwan na aure waɗanda indai ba Allah ne ya baka hakuri da juriyaba bazaka iya da bebi ba, dan Allah kai hakuri da duk abinda zatai maka in na faɗane kai mata in bakaji daɗin abinba kaɗau mataki ko ka gayamin wallahi har nan zanzo na zaneta".
Ta ƙarasa fadi tana hawaye sannan ta miƙe zuwa ɗaki batare data tsaya jin mi zece ba.
Kanshi dake barazanar tarwatse mashi ya dafe yana ayyana inda shima ze sami damar kukan dayi zeyi! kodan ya sami salama acikin zuciyarsa yana ganin ita mama kukanta na daɗine tunda gidan miji xata kai ƴarta shiko.kalaman daze fuskanci mahaifanshi kaɗai yake haɗawa dan yadda mama ta bashi tausayi ta kuma kashe masa jiki bayajin ko ana muzuru ana shawo ze iya sakar mata ƴarta domin yasan tabbas alhaji babba ze iya cewa ya saketa ɗin.
"Kaga halin mata ko Malam Aliyu wai yanzu aishatu daya dace ta rarrashi ƴarta amman ita take wannan kukan kumafa ɗazu da baku zoba bakaga yadda ta ɗaga hankalinta ba gani take kamar za,a shanya mata ƴane amman yanzu kunga kuma seda kuka zo ɗin xata hau kuka oh Allah kyautawa mata".
Murmushi usman yay sannan yace.
"Malam kasan ɗa da mahaifi se Allah musamman bebi abarson kowa yarinyar tana da shiga zuciyar mutum nima haka kawai nakejinta kamar ƙanwata ta jini".
Yafaɗa yana kallon Aliyu wanda ya sunkuyar dakai amman aranshi cewa yake.
kasan da haka mai yasa baka kwasaba seni zaka ƙaƙa bawa ita.
Amman a zahiri baice komai ba seyay kamar ma bayajin me suke faɗi ɗin.

Lokacin da mama ta shiga ɗaki duk ƴaƴan nata sunyi barci se redio dake famanyi Bebi tana daga saitin siff ta makure waje ɗaya ta cure da hijabi kamar maijin sanyi, kallon tausayi dana bankwana mama tai mata sannan ta sunkuya tana tashinta a hankali tana share hawayen dake zubo mata dayake bata fiye magagi ba caraf ta miƙe tana kallon mama.

"Fita tsakar gida jirani".
maman ta gaya mata a hankali gudun kar sauran su farka su haɗu su saka mata kuka!.
Ba musu ta murje idanunta tare da bin umarnin mama, ita kuma maman ta ɗauko jakar kayan bebi data haɗa mata ta biyo bayanta.
Tana rabe a bakin kofa taji takun mama a bayanta.
da sauri ta fito tsakar gidan baki ɗaya ganin malam a xaune da baƙi yasa taja da baya tare da rissunawa tana gaisar da malam.
Se lokacin ta shaida su waye, gabanta ne ya faɗi!
amman sanin babu angon nata cikinsu yasa ta soma mamakin miya kawosu da wannan daren amman setai gumm, da bakinta seda mama tace mata.
"bakiga baƙi bane ba bebi?".
"Ya usman ina yini" tana faɗin haka taja bakinta tai gumm gabanta yana faɗuwa.
"Shifa ɗayan baki sanshi ba koko bazaki gaisarshi ba?"
"An wuni lafiya" tafaɗa tana turo baki gaba usman ne ya amsa a sake shiko gogan takaicine ya dirar masa yana ayyana xakici ubankine.
"To usman ga amanar bebi nan ga kuma kayanta"
"Ke bebi ka Aliyu nan ɗan uwan usman kuma mijinki banson shirme da sakarci kinji ko ki.masa biyayya banda ƙazanta banda rashin kunya ragowar bayani xan turo hassana ko hussaina Allah yay maki albarka yasa nan gidan zamankine amin".
Malam ma fatan alkairi yay mata kana yaywa mama sallama ya tafi sabida dare yayi.
Shiko usman kayan bebi da mama ta kawo ya ɗauka yabi malam waje.
Mama kuwa cikin sauri tayi cikin ɗakinta sabida batason ganin fitar bebi.
ita ko bebi ganin mama tayi ɗaki yasa itama ta dawo daga hutun wucin gadin data tafi domin komai nata ya tsaya cak.
Dama shine angon nata? mutumin dayake mata faɗa yake kokarin dukanta mutum mai zafin rai,tunda take bata taɓa ganin mutum mai ɗaure fuska irinshi ba itafa inta ganshi faɗuwar gaba da tsoro har kusan fitsari suke sakata tayaya xata xauna da mutumin da tsayinshi ma kaɗai cika mata waje yake.
Kuka! ne mai ƙarfi ya taho mata cikin firgici tsoro zulumi take kokarin fito da kukan.
Sedai jin tattausan hannunshi mai ƙamshi datai a.................

*Alhamdulillahi nacika alƙawarin dana ɗaukar muku wanda rashin caji yasa ban cika da wuriba amman gashi nan nayi dik da ba,a kan kari nai ba waɗanda suke kai zasu gani waɗanda basa kai sedai in ALLAH ya kaimu gobe sa gani nagode* !

*PART* 2

NAKUƊINE

*73*

Jin tattausan hannunshi mai azababban ƙamshi datayi a saman bakinta shiya kuma ƙarawa jikinta rawa da kyarma akan wanda yake tun fitowarta.
Kafin taji dirin tsaiwarshi a bayanta hannunshi guda ɗaya ya saka ya riƙo tsakiyar ƙugunta irin riƙon nan na tsauri tare da jiyo da ita saitinshi tana fuskantarshi.
Wata azababbiyar faɗuwar gaba mai cike da firgici zulumi tsoro sune sukai mata dirar mikiya fiye dana da, Rintse idanunta tayi tana addu'a cikin ranta inda xaka kula lokacin zakaga kirjinta yana tsalle kamar ze faso ya fito waje sabida tsabar kaɗuwar datayi
Kallonta yake sosai ta cikin hasken farin watan daya haska tsakar gidan, batare daya ɗauke idanunshi daga kanta ba.
Yace mata.
"zomu wuce".
Still hannunshi na riƙe da ƙugun nata, yana cigaba da kallonta se yanzu yake ƙara ganin ƙarancin shekarunta sosai.
Zumɓuro bakinta tayi gaba kamar yadda ta saba yima mama shagwaɓa duk da yadda takejin tsoronshi amman bai hanata turo bakin gaba ba, tana dira ƙafafunta ƙasa.
"Ni bazan bika ba dan Allah ka barni da mamammu".
Shiiiiiiiiiiiii yace mata da bakinshi tare da jan hannunta da ƙarfi ya fitar da ita har zuwa soro.
Abakin ƙofar waje ta kuma takurewa tare da tsayawa waje ɗaya alamun bazata bishi ba.
"Karki ɓatamin lokaci wallahi in baki shige mun tafiba ranki ze ɓaci,Wayace ki zaɓi aurena shasha sha kawai".
Hawayene ya zubo mata cike da tsoro ta bi bayanshi tana ayyana shikenan tayi bankwana da gidansu tayi bankwana da mamanta da ƴan biyunta, abakin kofar gida ta kifa kanta tana cigaba da kukan datake yi.
Ganin yayi tafiyarshi ya barta a wajan yasa tabi bayanshi salo salo kamar wadda ƙwai ya fashewa acikinta,tana ayyana Allah sarki sadiya ko sallama basuyi ba.
Lokacin data ƙarasa gaban mota usman yana wajan driver yama tada motar su kawai yake jira, azuciye Aliyu ya buɗe motar ya shige yabarta awajan cikin sakin fuska usman ya leƙo da kanshi.
"Ƙanwata buɗe gidan baya mu wuce kinji daina kuka zan ɗauko mama na kawo maki ita har gida".
Cike da sauri ta balle marufin ta shiga tana gyara hijabinta, domin batada zaɓin daya wuce haka sabida tariga tasan ƙaddarar aurenta ce tazo mata da hakan, duk da karancin shekarunta amman tasan kaddara kuma tana yarda da ita sabida gwajin imanin bayi ce.
Cikin nutsuwa yay revars tare da jan motar ya fita daga cikin layin da ita,lokacin gari yay tsit sabida taran darema ta wuce gakuma walƙiya da akeyi sosai iska mai ƙura tana kaɗawa alamun hadarin garin gab yake da zubar da ruwa, kasancewar garin yanayin damuna ne.
Tafiyar mintuna goma daga layinsu bebi zuwa kan titi usman yay, lokacin da motar xata bar layin seda bebi tai kuka harda shashsheƙa,tana jin missing ɗin anguwarsu har wajan gawayin shahid

ta kalla tana share hawayenta.
"Yanzu kai abinda kaimin tsakanin ka da girman ALLAH kayimin adalci kenan?".
Aliyu ya faɗa cikin ƙasa da murya wadd ta shaƙe kamar zeyi kuka!.
Cikin sauri usman ya kunna redion motar sabida bayason Bebi taji abinda zasu faɗi.
Ware redion yay da ƙarfi yana tukinshi batare daya tankawa Aliyun ba.
"Adalcin kenan kuma bana shakka sabida alkairi na ƙulla ba sharri ba, sannan kuma da sannu zakazo min da buhun godiya nan bada jimawa ba".
Cikin ƙufula ya kuma duban usman a karo na biyu.
"Daman haka zakace man, sabida kai kasan baka cikin case tayaya zan dubi abba nace masa nayi aure bai sani ba? tayaya zan fuskanci ammi, dan Allah kai akaran kanka kayimin adalci kenan kariga ka sakani acikin sarƙa wadda batada mabuɗi".
Dariya usman yay har yana dukan sitiyarin motar shi sannan ya kalli Aliyu wanda yake faman sababi yana jin ransa yakai ƙololuwar ƙarshe a ɓaci sannan yace.
"Karka damu mai afkuwa ta riga ta afku sedai muyi maku fatan addu'a ALLAH ya kawo ƙazantar ɗaki, haba ƙanina ka tambayeni shawara tare da hanyar warwareta nikuma naga wannan auren shi kaɗaine masalaha sabida ceton maraici kagafa in suka mata auren nan sun cuceta kuma kanada kamasho tunda kaine sila, Yanxu ko daka aureta ai magana ta ƙare, nina san abba yasan ciwon haihuwa baze taɓa cewa ka rabu da ita ba koda yay faɗan ma na lokacine amman ze huce, amman duk da haka yanzu zamu soma kaita wajan ammi semuji mizata ce".
Tunma kafin usman ya idda numfashinsa Aliyu ya kuma cafke maganar usman cikin hargagi da masifar dake ranshi wadda yake dannewa.
"Miya ruwanka dani, danna zo maka da shawara ina ruwanka da haɗani aure da ita ina ruwanka da shiga hurumina wallahi nai dana sanin gaya maka halin danake ciki kuma wallahi bada ban ƙimar wancan dattijon ba wallahi dase na saketa sedai kai ka aureta".
Ta inda yake shiga bata nan yake fitaba baƙaramin tsoro hakan ya bawa usman ba baitaɓa tunanin ƙanin nashi nada faɗa irin hakaba har suka ƙarasa gida yana masifa kamar ze ari baki.
Harda cewa usman ya cuce shi yaje ya auro masa ƴar cikinshi ko uban me ze ɗauka ajikinta oho yarinyar da ko wankan tsarki ƙilanma bata iya ba masifa tijara babu irin wadda baiyi a motarnan ba wanda har tsoro seda ya tsirgawa usman.
Inda Allah ma ya taimaka sun kunna redio yana da tabbacin bebin bazataji maganar dasuke ba ammn yasan inda taji abinda ALIN ke faɗa seta fishi shiga halin tsorata da zulumi.
Bai bar usman ya ƙarasa parking ba ya ɓalle marufin motar ya fice azuciye.
Cikin rawar jiki shima usman ɗin ya balle nasa side ɗin yabishi seda usman ya haɗa da gudu sabida Aliyu badai sauriba, yana ayyana yau na ɗebo ruwan dafa kaina
Hannu ya saka ya janyo kafaɗun Aliyu wanda harya kusan kaiwa ƙofar part ɗinshi.
Yadda kalar idanunshi suka sauya launin kala yay matuƙar razana usman sabida sunyi wani irin girma tare da ja kamar gauta wanda ko ba,a faɗa maka ba kasan yana cikin tsananin damuwa da fushi.
Sanin kanshine in Aliyu na cikin fushi ko ammi bata kulashi harse ya sauka, dan haka cikin sanyin jiki usman ya saki kafaɗun sa tare da komawa wajan motar ya rabu dashi har zuwa gobe.
Tsaki yaja da ƙarfi tare da banko gate ɗinshi ya shige batare dako ya juya wajan usman ɗin ba.
Yana son ko a iya wannan daren ne ya nunawa usman kuskurenshi na wannan shiga hanci da

ƙudundunen daya masa wanda baƙaramin haushi usman ɗin ya bashi ba.
Haka ya ƙarasa cikin part ɗinshi azuciye kota kan ɗakin dija bai biba ya haura ɗakinshi ya faɗa saman gadonshi yana dafe kanshi dake barazanar tarwatse mashi bai shirya haɗa maganar daze fuskanci ammi ba, yana son dogon tunani da nazari kafin ya ƙaddamar da komai, zumbur ya miƙe zuwa gaban frij ɗin dake manne cikin ɗakin nashi budewa yay tare da ɗaukar gorar ruwan faro mai sanyi ya kafa a makoshinsa wanda ya bushe ƙaraf babu ko alamun miyau acikinshi seda ya shanye tass ya wurgar da gorar ya kuma ɗaukar wata ya shanye tass sannan ya mike yana rangaji kamar ɗan maye ya kuma faɗawa gadonshi ya shiga duniyar tunanin mafita?

Ƙarar! Buɗe ƙofarshi ita ta dawo da bebi daga duniyar tunanin data faɗa cike da fargaba ta juya tana kallon saitinshi ta cikin glass ɗin motar taga yadda yake faman sauri kamar wanda kashi ya matseshi kunsan yadda mutum yakeji idan kashi ya matseshi duk izzarsa duk yanganrshi matukar kashi ya kamashi tofa seya saka gudu ko sauri tunanin hakan yasa Bebi tai masa uziri tare da mayar da kanta kasa batare dataji fitar usman ba.
Har sanda usman ya dawo bata sani ba seda taji alamun ya bude ɓarin ta sannan ta ɗago a tsorace tare da zuba masa manyan dara daran idanunta waɗanda in suna halin tsoro suke ƙara firfitowa.
"Ƙanwata taso mu shiga ciki".
Yafaɗa tare da ɗan matsawa baya domin ya bata guri ta fito.
Tattare hijab ɗinta tayi tana ayyana karamcin usman, sannan ta fito waje tana kallon harabar gidan wanda tsoronta ya kuma ninkuwa, inba idanunta ne yay mata karyaba tasan dare yayi domin kusan goman dare amman yaya akai wannan gidan shi yake kamar da rana sabida hasken manyan fitilu, jibi harabar gida kamar girman anguwarsu.
Bai tsaya ɗauko mata kayanta daya aje a boot ba sabida daren dayayi, Cikin nutsuwa ya dubeta.
'Zamuje wajan matata ki kwana kafin gobe mijinki ya ɗaukeki, dafatan babu wata damuwa?".
Ya kalleta.
Girgiza kanta tayi alamun babu, tana satar kallon tsarin gidan yadda motoci ke zube a harabar gidan kamar ba gobe lallai waɗannan sunfi karfin ta.
"To ƙanwata muje ciki ko?"
Yafaɗa yana wucewa gaba cikin nutsuwa tabi bayanshi har tana haɗawa da tuntube bata taɓa ganin girman gida da kyau da tsari kamar wannan ba( niko nace bebi bakiga komai ba, gidan Alhaji mai atamfa ai ba baya ba wai danma a iya harabar gidan kikene kike faɗar haka )Gaban gate ɗinshi na part ɗinshi ya dakata yana buɗewa seda ya tura gate ɗin sannan ya juyo ya dubeta.
"Bisimillah mu shiga ko".
Yafaɗa yana shiga ciki itama tabi bayansa.
Tundaga farkon part ɗin usman tasoma ganin wasu irin fulawowi masu fisgar hankali tare da wasu irin fitilu masu haske gaban wata irin ƙofa mai kyau ya tsaya tare da danna wani abu nan da nan kofar ta bude ya danna kanshi ciki, itama tabi bayansa.
Suman tsaye tai sabida jinta cikin wata irin ni'ima sassanya mai kamshi ƙafafunta ta nutsa cikin, lallausan carfet ɗin falon tana kallon tsarin yadda aka haɗe falon da wasu irin zafafa kujeru ga

wata katuwar tv tana aikinta, faɗin tsarin haɗuwar falon ɓata bakine amman dai an tsarashi cikin ilimi tare da wayewa da kyau.
"Muje mana".
Taji muryarshi firgigit! ta ɗago tana kallonshi, sannan ta bi bayanshi cikin falon suka shiga yace mata ta zauna yana zuwa minti biyu.
Wata kwana taga ya nufa tare da buɗe kofa ya shige ciki.
Lokacin ta mayar da ajiyar zuciya tacigaba da bawa idanunta hakkinsu oh lallai gobe insu hassana sukazo akwai labari dama da irin waɗannan gidajen aduniya itafa inba a tvn gidan iyaba bata ganin irin waɗannan falukan, tsuru taiwa Tv duk tsoro ya cikata gani take kamar mutanan ciki zasu faso su watso waje sabida tsabar girmansu.
Shiko usman bedroom ɗin Zee ya shiga harta soma barci ya tasota tare da ce mata ta fito falo akwai baƙuwar Aliyu amman gobe zata koma wajan ammi yauma dai dan dare yayine.
Da har zata fara mita amman jin ya ambaci Ali yasa tasan abin bana wasa bane ba,setai zaton ko abokiyar cinikinshi ce tai dare shine ya haɗota da usman tunda tasan shi ba son jama'a yacika ba.
Ajiyar zuciya ta mayar tare da saukowa daga saman gadon ta ɗauko hijab tabi bayanshi.
"Amman shi mai yasa baze kaita part ɗinshi ba senamu?".
Tafaɗa tana kallon mijin nata.
"Kinga bana son wannan maganar nida Aliyu duka ɗayane in kuma bazaki bata ɗakin ba semugani".
"Ni bance ba muje kaga karka ɗagan murya da tsohon daren nan kaje ka gaya masa ya ƙara girman harara fiye da tada da".
ƙunshe dariya usman yay sanin zee daman ba shiri suka cikayi da Aliyu ba duk da kasancewarta ƴar ƙanin ammi uwa ɗaya uba ɗaya, amma sam basa shiri domin Ali yace zee ta cika tsiwa da yawa.
Har suka ƙarasa falon bebi tana ta kallon ta sabida daman ita batada baƙunta.
Sallama zee tayi cikin nutsuwa tana dafe tirtsetsen cikinta daya tsufa.
Cikin sauri Bebi ta ɗago tana ƙarewa matar gabanta kallo wadda batafi sa'arsu hassana ba, sedai tafi ƴan biyu jiki da kalar hutu, farace tarr kuma babu laifi tanada kyanta.
Amsa mata sallamar tayi itama tana zamowa daga saman kujerar tare da cewa.
"Ina yini?".
Cikin sakin fuska zee ta ɗan sunkuyo ta riko hannun Bebi.
"Lafiya kalau kanwata zona nuna maki bedroom ɗin dazaki kwanta dare yayi".
Tafaɗa mata cikin kulawa.
"To seda safe Aliyu ze shigo gobe insha ALLAH".
Usman ya faɗa mata yana juyawa ya bar wajan.
Amsa masa tai da "To"
Sannan tabi zeee wadda hannunta ke rike dana bebin.
Wata kwanar suka nufa,  gaban wata kofar ɗaki zee ta tsaya ta bude sannan suka shiga cikinshi babu laifi yana da kyan tsari, da gado da madubi, da kuma wata kofa sakin hannunta zee tayi tana yabon kyan bebi tare da kallon ƙanƙantar yarinyar.
"Ga ɗakinan ga gado da toilet bara na kawo maki abinci".
"A,a na ƙoshi nagode".

Tafaɗa muryarta na rawa.
Juyowa zeee tayi tare dayin jimm alamun bataji daɗi ba amman setace.
"To babu matsala ai da safe kina nan kyaci seda safe"
"Nagode".
Tafaɗa tana zama gefen gadon har zee ta fice daga cikin ɗakin..............

*PART* 2

NAKUƊINE

*74*

Da baya taja ta zauna a gefen gadon tana dafe saitin kanta wani irin sihirtaccen tsorone yake ratsa ilahirin jikinta tunda take arayuwarta ta duniya bata taɓa jin makamancin tsoro kamar na wannan datake cikin kaɗaici haka.
Ta taso tare da mahaifiyarta da ƴan uwanta tunda suke basu taɓa raba makwanciba a iya wayonta, ko anguwar kwana mama bata zuwa kullum suna tare haka zalika suma bata barin suyi nisan anguwar da zasu kwana, to inama suke zuwa bayan dangin mahaifinsu sun juya musu baya duk irin yawansu, dangin mama kuma ƙalilan ne waɗanda suke zaune anan anguwar ƴan kusan suma kuma bawai shine dasu ba wannan dalilin yasa haɗuwarma take wahala amman duk da haka mama takan sakasu agaba da sallah takaisu suga danginta duk da batada uwa bata da uba kuma iyayenta ita ɗaya suka haifa sedai akwai ƴaƴan ƴan uwanta wannan yasa take ziyartarsu lokaci zuwa lokaci batare datayi gigin bita cikin gida ba ma'ana gidansu kawu tasi'u wanda in bazata manta ba kwanakin baya da babarsu kawu tasi'un ta rasu da mama taje gaisuwa da ɓacin rai ta dawo shiyasa ma yanzu dataji ɗayar tana ciwon ɓarin jiki koda wasa bata je dubiya ba.
Yau gata a ƙaton gida ƙaton ɗaki wanda ya cika da kayan alatun more rayuwa amman babu kowa nata tsananin kaɗaici tare da tsoro da zulumin kewar ƴan gidansu ita ta kuma kamata.
Zamewa tayi daga kan gadon ta zauna a ƙasan tiles sanyinshi na ratsata, hawayene masu zafi da raɗaɗi suke sauka daga kuncinta.
Babu tunanin datake face na ahalinta yanzu tasan ƴan biyu sun can tare da mama suna baccinsu ita ko tsananin kaɗaici ya dameta.
Sam tunanin Aliyu ko nawani sharetan dayay bai dameta ba sabida batada wannan hangen a ranta auren ma bata kawoshi a wannan lokacin ba amman cikin hukuncin ubangiji segashi yazo mata itafa abinda ke damunta ɗayane tsananin kewar gida tare da tsoro.

Wani mugun fitsarine ya kamata amman yadda takejin tsoron ɗakin yahanata nufar bathroom tayi bitsarib duk da taganshi acikin ɗakin amman bata tunanin iya tashi daga inda take.
Ahaka bacci ɓarawo ya saceta batare data hau saman gadon ba bare kuma ta sami zarafin fitsari kowani abu.

Cikin tunani zee ta ƙarasa cikin ɗaki zama tayi abakin gado tana jiran usman wanda ke cikin bathroom yana wanka, mintuna kusan goma ya ɗiba kafin ya fito yana tsane jikinshi, seda ta bari ya kammmala komai cikin tsanaki sannan ta dubeshi a yayin dayake zama a gefenta.
"Yaya nidai inada magana dakai fatan zaka bani amsa mai kyau".
Mirginawa yay saman pilown dake gefenta sannan ya dubeta.
"Ina jinki amman son samu ki barni wallahi nagaji baccine akaina".
Murmushi tayi tare da shafo saman kanshi da hannunta.
"Yaya dan ALLAH da gaske waccen bakuwar ALIYU ce? naga sam batai wayewar business ba bare ace abokiyar kasuwancin sace pls dan girman Allah kaimin bayanin dazan gamsu".
Tafaɗa cikin kwantar da murya.
Janyota yayi zuwa saman ruwan cikinshi.
"Yes my zee baƙuwar Aliyu ce da gaske amman wannan bakuwar bata tafiya bace ta xamace domin tuni ya aureta".
Zumbur! Zeee ta mike tare da furta.
"What! kana nufin waccan yarinyar matar Aliyu ce da gaske?".
Da kallon mamaki usman yabita sannan yace.
"Eh mana matarshi ce ta sunnan ko kina mamakine?".
Yafaɗa yana janyota zuwa jikinshi tare da kai hannunshi saman ruwan cikinta.
"Haba yaya zaki saka nai asarar bebina kina wannan mikewa haka ai seki taromin aiki".
Zamewa tayi tare da kallonshi.
"Tayaya ya aureta bayan yasan zuri'armu ba'a AUREN BARE! gaskiya abin da mamaki ace kwananshi huɗu da aure yaje ya auro wata daban wadda bana tunanin su ammi ma sunada masaniya akan auren".
Haɗe ranshi yayi tamau kamar ba usman ba sannan ya mike ya zauna yana kallonta.
"Zee tuhumar auren sunna kike koko  wata manuface aranki ina ruwanki da auren sa?".
Yafaɗa yana tsare girar sama data ƙasa.
"Babu ruwana da aurenshi amman maganar daka faɗi ce batada tushe balle makama in Ali bai auro wata ya kawoba kai zaka iya auro wata ka kawomin nan batare dana saniba tunda halinku na maza babu wanda bai fita ba".
Dariya zee tabasa daman wannan zargin natane yasa tai wannan mikewar zumburr lallai mata se abarsu amman seya basar tare da kallonta.
"Kinsan dai maganar irin haka bata taɓa haɗani dake ba why note zaki nemi musanta maganata alhalin kuma nasan yes da gaske nake maki".
Zama ta komo tai gefenshi tana kallonshi.
"Da gaske kake dan Allah in har kai ka aurota dan Allah ka gayamin danna san Aliyu baze zauna da waccan ƴar yarinyar ba sabida sanin son girmanshi duk da tanada kyau amman dai wallahi ina tam tamar yadda akai auren".

Riko hannunta yay tare da bata hankalinshi gaba ɗaya.
Zayyane mata yadda akai auren yay batare daya ɓoye mata komaiba hatta haɗuwarsu da su bebi seda ya faɗa sannan ya zuba mata idanu yana kallon re action ɗinta.
jikinta yay matukar yin sanyi cikin sanyin jiki ta dubeshi.
"To amman fa abin da ban tsoro sabida akwai rikici agaba wallahi dan kuwa inhar alhaji yaji akwai case amman dik da haka bana goyon bayan ya saki marainiyar ALLAH wallahi harnaji ta kwanta min araina".
Dariya ya saki yana cewa.
"Da har anhau kishi amman da akaji ba matata bace ba an saki nizo mu kwanta ma zanta gobe shima mai amaryar baccinsa yake sabida haka komi ta famjama fanjam gobe ayita ta kare dan wallahi kafarshi kafarta dan ba auren jingina xaiyiba".
Ranta wasai tabi bayan mijin nata suka kwanta suna barwa gobe komai in ALLAH ya kaimu.

*NOTE*

_Assalamu Alaikum barkammu da dare dan Allah inkunjini shuru kucigaba da uzurina kamar yadda kuka saba wallahi se addu'a kwana biyunnan banjin  daɗin jikina kunsam yanayin garin yadda ko ina ake fama da maleria kusan kowani gidama se ansami mai zazzaɓin nan sedai fatan Allah ya warware mana, tonima gani inafama da ɗan rashin jin daɗi kwana biyun nan kokari kawai nake wallahi wannan ma bana tunanin yakai one read more nadai yine danna cika alkawari dan Allah kuyi hakuri insha Allah gobe zanyi da yawa kuma ina muku ma albishir da cewa auren bare ya kusan zuwa makara fatan Allah yasa mugama lafiya cikin farin ciki da kwanciyar hankali amin summa amin nagode_

*PART* 2

NAKUƊINE

*75*

Aliyu ya jima yana tunanin mafita akan wannan cakuɗaɗɗan lamarin daya kunno mishi ɗago ƙwayar idanunshi yay ya zubasu akan agogon bangon dake manne a bangon ɗakin nashi ganin kusan 12 na dare yasashi miƙewa a center ɗakin ya tsaya tare da tube jallabiyar jikinshi ya rage dagashi se singlet tare da wandon jeans ɗin daya saka daga cikin jallabiyar.
Shafo kwantacciyar sumar dake saman kirjinshi yay tare da shafo shafaffan cikinshi wanda yay wani irin shafewa tamkar ba,a saka masa lomar abinci.
Yana kokarin nufar ƙofar bathroom ɗinshi yaji alamun ana murɗa handle ɗin kofar room ɗin nashi cakk ya tsaya tare da ɗora hannunshi bisa kirjinshi ya zubawa kofar idanu, Cikin siririyar muryarta wadda ta karo mata yanga da gwalli take rangaɗa sallama cikin ɗakin.
Can cikin  makoshin sa yake amsa sallamar amman ƙasan ranshi mamaki ne fall.
Bayyanarta cikin ɗakin shiyafi basa mamaki musamman yadda tai shigar jikinta mai tsananin fisgar hankali da tunanin mutum mai lafiya, Gabanshi ta tsaya tana rau-rau da ƙwayar idanunta kamar wadda zatayi kuka kafin cikin shagwaɓa ta soma magana.
"Yaya sannu da zuwa dan Allah a ina ka tsaya yau?"
Haɗe ranshi yay tare daɗan jan tsuka kaɗan ya raɓeta ya wuce cikin bathroom tare da bugo kofa yanajin takaicin wannan shige masan datakeyi.
A maimakon ta fita seta gyara zama tana kara zame yar rigar dake jikinta ta bacci wadda batada maraba da fanɗarinka tsirara wadda ta baiwa ƴan matasan kirjinta bayyana fili, ya kusan minti talatin a bayin kafin ya fito jikinshi ɗaure da tawul yana ɗigar da ruwa sam bai yi xaton tana ɗakinba shi mutum ne mai alkunya baya kaunar bayyana tsiraicinshi agaban kowa wannan halinshine tun yana yaro domin ammi ko wanka zata masa sedai ta saka masa ɗan wando inba hakaba kuwa yayita kuka kenan yana angane masa abinshi, Cikin hargagi kaɗan ya daka mata tsawa tare da bata umarnin ta fitar mai aɗaki.
Jiki babu laka taja kafafunta tabar ɗakin tana haɗiyar miyau domin surar jikinshi bakaramin nutsar da ita tayi ba a kogin sha'awar shi.
Gaban kofar yaje ya zira mata key ya dawo gaban gado ya zauna ya dafe kanshi sam a halin yanzu bayada feeling bare ya samu damar yin sex sabida halin dayake ciki na wannan tension ɗin da usman ya sakashi yasan bai yiwa dija adalciba domin a yanzu tanada hakki akanshi bayaga nan kuma baisan irin nata karfin sha'awarba sedai kuma a yadda yake koda tsirara zata mai tofa baze taɓa jin komaiba sabida in rai na ɓace feeling gudawa yake.
Ganin dare yana kuma ja yasaka ya nufi gaban jerin kayanshi ya ɗauki jallabiya milk colour tare da ɗan guntun wando ya zira ya kuma komawa cikin toilet ya ɗauro alwala ya shinfiɗa darduma, yahau ya soma gabatar da sallolin nafila wadda a dukkan sujjadar ƙarshe seya jinkirta yana kaiwa ALLAH kukanshi akan wannan abun daya faɗo masa sama taka yana kuma jaddada neman zaɓin alkairin ALLAH acikin wannan lamari tare dayiwa ubangiji kirari da sunayensa kyawawa.
Har kusan karfe ukun dare yana saman sallaya bayan ya idar ya soma lazimun la'ilaha'illah'anta'subuhanaka'inni'kuntu'minazzalimin'!akan ALLAH ya fitar dashi daga cikin wannan matsala sabida wannan addu'a ta inganta ga bayi musamman waɗanda suke cikin damuwa in suna karantawa  bazasu gusheba face ALLAH ya kawo musu mafita acikin dukkan matsalolinsu kuma ya fitar dasu daga cikinta.

Bayan ya kammala yay istigifari da hailala tare da salatin annabi s.a.w sannan ya shafa ya naɗe abin sallan ya koma saman gado ya kwanta akan hannunshi na dama bayan ya tofa addu'oinshi na kwanciya daya saba gabatarwa.
Babu jimawa bacci mai daɗi ya saceshi kuma babu laifi yaji kaso mafi yawa nadaga cikin damuwarshi ya fita yaji sakayau aranshi.
Wanda har yakusan makara a sallar asubahi inda Allah ya soshi yanada agogon dake buga alarm wanda seda ya buga wajan sau uku sannan ya buɗe idanunshi waɗanda suka cika da bacci yana karanto addu'ar tashi daga bacci sannan ya miƙe ya nufi toilet seda ya watsa ruwa a jikinshi sannan ya ɗaura alwala ya fito agurguje ya sake sauya kaya wannan karon brown ɗin jallabiya ya saka tare da fesa turare mai kamshi wanda indai ze fita sallar asubahi yake amfani dashi.
Cikin sauri ya kashe ƙwan ɗakin ya fita a falo ya dakata yaɗan leƙa ɗakin dija ya buga mata seda yaji alamun tashinta sannan ya wuce masallacin cikin sauri.
Yana zuwa ana ƙoƙarin tada jam'i wanda yau alhaji babbane ma yake jan limancin sahu yabi aka tayar da sallar har aka idar bayan an sallame yaja baya tare da soma laziminshi wanda yawanci daman inya fita sallar asubahi baya komawa bacci harse ya kammala lazuminshi tare da azkar yay walha in yanada office ya fita in yana gida yaje ya kwanta abinshi, se wajan bakwai saura ya kammala sannan ya fito aikuwa harabar gidan babu kowa sabida safiyace hatta securties ɗin gidan suna can ɗakunansu sabida yadda aka tashi da yanayin sanyi.
Harya yakai kofar part ɗin mahaifanshi maganar mama ta faɗo mishi aranshi.
"Ka kulamin da bebi ina sonta marainiyace ga amanar ƴata na baka karka cutarmin da ita"!.
Cak ya dakata yana sosa saman kanshi abin duniya ya haɗu yay mashi yawa.
Umarnin zuciyarshi yabi kai tsaye ya karya kwana ya fasa nufar sashen iyayenshi seyay na usman, abakin gate ɗin ya tsaya yana wasi wasi kafin yay ta maza ya tura ya shiga ciki, seda ya danna knowking kusan sau uku  kafin azo a buɗe mishi usman ne ya buɗe kofar tare daɗan bawa Aliyu hanya ya wuce cikin falon tsananin mamaki ya kama usman ba ɗan kaɗan ba domin sam baiyi tunanin ganinshi a wannan lokacin ba.
Gaisawa sukai ta hanyar musabaha yana xama akan ɗaya daga cikin kujerun falon, tunda usman yay aure yaune zuwanshi na biyu ɓangaren usman ɗin.
"Ina wannan yarinyar take?"
Ya faɗa yana kallon usman wanda yake kokarin xama shima a kan kujerar dake fuskantar ta Aliyun.
"Tana ɗakin dana sa aka kaita tun jiya bana zaton kota tashima amman kaje ka dubata man kaida matarka ga ɗakin can".
Usman ya faɗa yana mikewa ya nufi ɗakinshi yabar Aliyun a dashe a falon.
Miƙewa yayi tare dabin direction ɗin da usman yay mashi gaban kofar ɗakin data kwana yaje ya tsaya yana turawa ya buɗe ɗakin alamun bata saka key ba.
Sallama yayi a ƙasan bakinshi shuru yaji laluba makunnin ƙwan ɗakin yayi tare da kunnawa ya tsaya yana kallonta a kwance a kasan tiles tana baccinta masha Allah.
Tsira mata manyan idanunshi yay yana kallonta kafin ya ƙarasa gabanta ya tsugunna yana kiran sunanta.
"Ke!ke!! ke!!"
amman shuru kamar bata raye, jan ɗan yatsanta yayi guda na ƙafa wanda har wani tarar jini

yay sabida janshi, wata irin birgima tayi tare da miƙa ta hantsila saman kafafunshi ta saka hannunta guda a ƙugunshi tacigaba da baccinta.
Wata iriyar ɓoyayyar kasalace ta rufe masa jikinshi wadda baitaɓa jin kamancin irinta ba.
Zama yayi daɓas a saman tiles ɗin tare da saka hannunshi guda ya ƙara jawota jikinshi sosai ya bata masauki mai kyau, yana mai tsira mata idanunshi yaga alamun sam bata ƙoshi da baccin ba kuma aranshi baya son tashinta sedai kuma dole ta tashi ɗin tunda sallah tana kanta.
Lalubar cikin kunnenta yay tare da buɗewa yaɗan ja hijabin cikin kunnen nata ya tura harshensa yana ɗan hura mata iskar dake cikin bakinshi kaɗan batare daya furta komaiba se iya wannan sakon dayake aika mata dashi.
Jin sauyin kamshi acikin kunnenta yasa ta soma buɗe idanunta tana kuma jin saukar iska cikin kunnenta, zumbur ta miƙe jinta asaman cinyar mutum kafin ta buɗe idanunta tarwai tana kallon ɗakin.
Zare bakinshi yay a kunnenta yaɗan tureta kaɗan yana kallonta fuska ɗaure.
"Tashi kije kiyo alwala oya banson jira".
Jin tattausar muryarshi cikin dodon kunnenta ya bata tabbacin masifaffe yazo kenan.
Bata tsaya tunani akan lamarin komaiba ta mike jikinta yana rawa tabar saman cinyar tashi tana maibin umarninshi sabida sanin halin faɗanshi bakaramin kokari tayiba kafin ta iya haɗa ruwa tai tsarki tayo alwala ta fito.
Darduma ta tarar ya shinfiɗa mata shikuma yana zaune a gefen gado ya zuba tagumi yana kallon kofar bayin.
Harta hau saman dardumar bai ɗauke idanunshi akanta ba, haka ta tayar da sallar cikin nutsuwa ta idar tana addu'a ta shafa.
Sannan ta juyo gareshi.
"Barka da safiya".
Tafaɗa tana yin kasa da kanta.
Bai amsa mata ba illah tashi tsaye dayay.
"Muje ciki amman bakida kayan dazaki sauya?".
Yafaɗa yana kallon yadda take ƙunshe jiki acikin hijabin daya ɗan soma datti sabida farine.
Girgiza kanta tai tare da yin ƙasa dashi alamun batada.
"Bana son magana daka malama kimin magana yadda nai miki".
"Eh babu anan suna motar uncle usman".
Tafaɗa cikin rawar murya domin itafa a tsorace take dan wallahi inda zata sami hanya sedai aga wayam tayi wajan mama.
"Okey muje ko".
Yafaɗa yana ratseta ya wuce.
Amaimakon ta bishi seta tsaya tana kallon kanta ke yanzu bebi ahaka zaki bishi dubeki kamar ba ƴar mama ba kaca kaca dake ko bra babu ajikinki.
Harya kai falo yaga bata biyoshi ba a zuciye ya koma ɗakin.
"Malama waini akanki xan ƙare dalla fito mu wuce wajan ammi".
Rau-rau tai mar da idanu zatayi masa kuka!.
"Nidai Allah bazan fita ahaka ba jiba fa kamar wata bakauya ka ɗaukomin kayana a wannan motar ta jiya"
Tsayawa yay yana kallonta kamar wani dolo yana hango tsabar kuruciya a tare da ita.

Tsaki yaɗanja sannan ya fita a ɗakin da ƙyar ya sami mai gadi ya bashi makullin motar yaje ya ɗauko mata jakar kayan nata wanda shi badan wani abu yake yin haka ba kawai baison ta ɓata masa lokacinshine.
Har lokacin falon babu kowa da alamun usman yana can suna baccinsune harara ya ɓalɓawa wajan ɗakin usman yana ayyana ɗan iska kai kana can hankali kwance ni kabarni da raino.
Kofar ɗakin ya tura ya shiga tan nan yadda ya barta a tsaye.
Aje mata jakar yay agabanta tare da zaman jiranta a gefen gado.
Amai makon ta ɗauki kayan taje bayi ta kintsa ai ina bebi akwai hauka seta tsugunna gaban jakar seda taiwa komai filla filla babu bra ko ɗaya bare kuma pant wanda tasan mantuwa mama tayi.
doguwar rigar atamfa ja ta ɗauka sannan ta ɗauki zani falle guda ta nufi gaban madubin ɗakin tube hijabin jikinta tayi sannan ta ɗaga rigar jikinta ta ɗaura wannan zanin na hannunta.
Duk abinda take yana kallonta sedai ya zuba mata idanu ne kawai yana kallon kalar nata shirmen yarinyar yaga alama batada kunyar tsiraici agaban uban kowa aikwa da matsala.
Juyowa tayi ganin idanunshi akanta yasa gabanta ya faɗi.
Tasan babu kyau mace ta bayyana jikinta agaban namiji amman ai wannan mijinta ne kuma mama tace mata dan miji yaga jikinka ba haram bane ba.
Gabanshi tazo ta tsaya.
"Zaka zugemin ziff ɗina sannan kuma mama bata sakomin bra ba kuma bani da pant".
Tsira mata idanu yay kurum yana ayyana Aliyu kaga ta kanka.
Batare daya ce mata komaiba ya mike ya karbi rigar hannunta.
Ya xage mata ziff ɗin sannan ya mika mata ta amsa agabanshi ta ɗaga hannu ta zira rigar sannan ta juyo masa farin bayanta tass tana cewa ya zage mata ziff ɗin se asannan ya fahimci abinda take nufi.
Ɗora hannunshi yay saman bayanta ya zuge mata ziff ɗin garin sauri har yana haɗawa da fatar wajan wadda ta sakata saurin zabura ta daka tsalle da ihun zafi ta rungumeshi.
Dan itafa tafa manta da wanda take tare sabida zafin dataji.
Murza kanta take a saman kirjinshi tana furta.
"Dafa zafi kaimin wallahi bazan yarda ba Allah kuwan........tanayi tana kukan data jima tanayi na kewar mamanta.
Wayyo bebi kin kashe Aliyu wani irin yanayi yakejin kansa aciki mai wuyar misaltuwa................

*Afuwan babu editing wallahi*

*PART* 2

NAKUƊINE

*76*

Tsintar kanshi yay da ɗora hannunshi a tsakiyar bayanta ya zage ziff ɗin yayi ƙasa dashi, faffaɗan hannunshi mai uban laushi da ƙamshi ya ɗora a saman fatar bayan nata yana ɗan shafa mata shi a hankali kamar wanda ke tsoron wani abu karya taɓa mata bayan, Babu abinda kakeji acikin ɗakin face sautin ajiyar zuciyarsu wanda ya haɗe waje ɗaya tsintar kanta tayi dajin daɗin abinda yake mata ɗin wanda yau shine karonta na farko arayuwarta da wani ɗa namiji ya ɗora hannu ajikinta, ajiyar zuciya ta sauke masa mai ƙarfi tana ƙoƙarin zubewa awajan kamar wadda batada laka ajikinta.
Ya kuma kamota da ragowar ƙarfinshi tare da manneta da jikinshi lalubar kunnenta yake da harshenshi cikin dabara ya ɗora harshen nashi a saman fatar kunenta yaɗan cija kaɗan sannan ya mayar da bakinshi gaba ɗaya cikin ramin yana hura mata iskar cikin bakin nashi.
Sauran kaɗan ta saki kara sabida azababben daɗin dataji adukkan sassan jikinta tsigar jikinta ce ta miƙe gaba ɗaya har wani irin luuuu takeji kamar zata shiɗe daman su dawwama yana mata wannan tafiyar tsutsar mai daɗi.
Tuna wacece ita da halin da suke ciki yasa zumbur ya zare bakinsa tare da sakinta yana jada baya yana haɗe ranshi yana kuma gyra gaban rigarshi, Bebi data faɗa duniyar sama jannati tuni hankalinta ya dawo jikinta jada baya tayi tare da haɗe ranta tamau tanason saka kuka domin itafa abin bai isheta ba.
"Wuce muje kuma wallahi kika ƙara matsoni sena bugeki".
Yafaɗa cikin rabewar murya kamar mai shaƙuwa.
Harya kai bakin kofa still batai ko motsiba.
Seya fasa fita ya juyo yana kallon yadda ta haɗe ranta.
"Wuce mana kinafa ɓatamin lokaci".
Amai makon tabishi seta soma dira ƙafafunta a ƙasa.
"Nifa Allah bai isheni ba, wannam  ai saka raine bantaɓa jin wannan abinba seyau".
Gira ya ɗage yana nazarin maganarta.
"Wani abune kinga wallahi zan bugeki inbaki fitoba konan ɗin ɗakin kine".
Kuka ta saka masa mai karfi.
"Wannan iskar fa tabakinka daka zuba akunnena ita nakeso dan Allah wallahi daɗi nakeji".
Tafaɗa hankalinta kwance.
Riƙe haɓa yay yau yaga takanshi matanshi jarababbune wannan kam hartafi khadija.
Sabida yasami kanta yace.
"To bara mudawo zan saka miki"
Yafaɗi hakan cikin mamakin kanshi na yadda yake biye mata abin yana basa mamaki over.
Hijab ta ɗauka baƙi acikin kayanta, ta saka sa har ƙasa sannan tabi bayanshi har lokacin su usman basu farkaba.

yana gaba tana baya suka fita a falon tana kuma kallon kyau da tsarin gidan tana hango sojoji masu tsaro suna shawagi ta fella aguje ta isa gareshi ta raɓe tana binshi sabida tsoron dataji.
Har suka ƙarasa part ɗinsu ammi tundaga farkon gate ɗinsu ammi take kalle-kalle harsuka ƙarasa ƙofar falon musamman yadda ma'aikata ke faman share-sharen wajan filawas ɗin dake compund ɗin gidan.
Gaban ƙatuwar ƙofar falon suka tsaya ya danna belt cikin mintuna uku wata ƴar aiki tazo ta buɗe musu ganin Aliyu yasa taja da baya ta russuna tana gaisar dashi.
Aciki ya amsa mata sannan ya wuce bebi tana take masa baya, shagala tayi da kallon yadda aka narka dukiya acikin mahaukacin falon mai masifar faɗi da tsaho wanda seda ya lashe kujeru kusan saiti huɗu.
Aran take ayyana sukuwa waɗannan bayin Allah wani irin kuɗi garesu ko wani falo inta gani setaga da wanda yaci ubanai jiba na jiya wanda taga ashe batai kallo ba ga wanda yaci mai uwa a haɗuwa.
Har yakai bakin ƙaramin falon ammi tana tsaye tana kalle-kalle seda yaɗanyi gyaran murya sannan ta taho da sauri gabanshi ya shige ciki ta bisa darkarewa tai abakin kofar falon tana kallon falon mai kyau sedai baida wani girma sosai.
Ganin ya tsaya agaban tv yana kallon ta yasa ta taho da sassarfa ta zube a ƙasan carpet ɗin sabida cikinta ta somajin yunwa.
ƙure tv tai da idanu tana kallo har batasan sanda ya fita daga falon ba ya wuce bedroom ɗin ammi.
tana zaune tana lazumi yayi sallama cikin nutsuwa.
da far'a da kulawa ta amsa mar tare da matsa mashi gefenta ya zauna.
Sunkuyar da kanshi yayi adake ya kalleta yana gaisarta anutse.
ta amsa tana masa ya kwanan dija.
"Lafiya lau! ammi nayi maki laifi amman dan Allah ina son kafin na gaya maki komaye kifara min uzuri sannan kimin fahimta mai kyau sabida ni ɗan adam ne babu wanda baya kuskure"
Murmushi tayi irin nasu na manya sannan ta dubesa.
"Nayi maka babana Allah yasa naji alkairi".
Gyara zamanshi yayi agabanta yana mai fuskantarta batare da tsoro ko shakkaba ya soma labarta mata tun farkon haɗuwarshi da bebi har zuwa jiya da usman ya kaisa ya ɗaukota a matsayin matarshi.
Tsananin mamaki ya hana ammi furta ko kalma guda sedai bata tari numfashinsa ba har yagama ya rufe mata da cewar yaya abbakar da usman sune sukai wakilcin auren mashi shima kuma kanshi bai san da haɗin ba.
Tajima tana nanata maganar tana saki ajiyar zuciya kafin ta fuskance shi.
"Naji komai babana Allah yasa haka yazama alkairi agareku ni bazanja da ikon Allah ba sabida ban san maiya ɓoye da hakan ba,sedai banji daɗin yadda lamarin ya faru ba, sabida kafini sanin waye mahaifinka suwaye ahalinka masu tsauri da mugun son kansu to son kansu zance mana sabida wannan al'ada tasu ta rashin AUREN BARE wadda tana mugun takura kowa na cikin gidan nan".
Gyara xama yakumayi yana nazarin maganganun ammi.
"Abbanka baze damu dayin auren kaba sedai kasan yadda ranshi ze ɓaci inyaji kai aure babu saninmu sannan kuma alhaji babba shine matsalarmu, amman inaganin zanyi kasada guda

ɗaya kafin zuwa wani lokaci mugama tsara yadda zaka tunkari mahaifinka da maganar.........inaganin zaka fitar da yarinyar nan daga gidan nan katafi da ita can *Tokarawa* unguwar da sabon kamfaninka yake tunda naji kace ka gina gidan ma'aikata inaganin ka ɗauki flate guda ku zauna da ita kafin zuwa wani lokacin sedai koda wasa kada ka sanar da kowa wannan sirrin mubari iya nida kai da usman dashi yayan naku zan kirasu muji yadda lamarin ze tafi sabida nasan rashin adalcin alhaji babba tsaff ze iya sakawa ubanka yace seka saketa wanda nikuma tsananin tausayin yarinyar baze barni naga ɓaraka tasamu ba".
Tafaɗi maganar cikin nutsuwa.
Cikin ɗumbin mamaki ya ɗago yana kallon ammi
kamar zeyi kuka! yake kallonta
"Haba ammi sokike na mutu, ammi kinsan yadda anguwar take, wallahi akwai tsadar rayuwa sosai a anguwar sannan kuma tayi ciki da yawa akwai mugun nisa kafin nazo nan,but sannan kuma in zanzo wajan khadija shima ze zama akwai rashin tsaro awurinta".
Kallonshi take tsaff harya gama maganarshi.
"In zaka taho wajan khadija seka sama mata wadda zatana tayata kwana tunda kace akwai waɗanda ka zuba haya a ragowar flate ɗin kafin ka soma aiki da ma'aikatan zasu zauna cikinshi, nidai wannan ce kaɗai masalaha inba hakaba zan zuba maka ido kaida ubanka ba ruwana".
Jinshi yake cikin ɓacin rai tunda yake baitaɓa zuwa wani wuri wanda ya keɓanta da ƴan uwanshiba se akanta hatta waje dasuka fita karatu shida usman ne a office yana tare da usman a legos yana tare da ya umar amman dalilinta ammi zatace yabar gida.
"Ammi amman yaya zanyi kinsan dole zan raba kwana fa?".
"Kai kaci gidanku sekace wani yaro kowacce cikinsu zaka kasa fahimtar da itane ni muje naga ƴar tawa karka ɓatamin rai".
Dariya ya gintse ya tashi suka fita zuwa falon..........

*PART*  2

NAKUƊINE

*77*

Tashi yayi jikinshi duk a mace yabi bayan ammi suka fita zuwa falon, Zaune suka tadda Bebi a

ƙasan carpet ta zubawa Tv idanu tana kallo ko ƙiftawa batayi.
Dakatawa ammi tayi tana kallon yarinyar wadda sam ita bata san da wanzuwarsu acikin falon ba, tana mamakin yadda akai Aliyu ya auro wannan ƴar mitsilar yarinyar domin ko sa'ar ƴan biyunta batai ba, amman ba,a mamaki da ikon Allah wannan dalilin yasa ta ƙarasa cikin falon Aliyu na bayanta.
Sallamar Ammice ta dawo da bebi daga duniyar kallon datake famanyi ɗago kanta tayi bakinta yana amsa sallamar da matar da ke neman wajan zama takeyi.
Kallon dattijuwar matar bebi take wadda bazata gaza shekaru sittin ba domin ta girmi mamanta nesa ba kusaba sam bebi bata kawo ammi maman Aliyu bace sabida ko a farcen susa basuyi kama ba sabida ammi farace jajur marar girman jiki domin duka duka batada wata ƙibar kirki sedai tanada cikar haiba da kamala wadda kana kallonta kasan mace ce na gartacciya mai yawan ibada tare da tsabta.
Saɓanin shi Aliyu dayake gabjejen mutum dogo kakkaura mai ƙiba da tsaho tare da cikar zati ingarman namiji majiyin ƙarfi baƙine shi amman bazaka sakashi ajerin munana ba domin ko ammi bazata nuna masa kyau ba sedai ta nuna masa jar fata, idanunshi kaɗai masu kyaune bare gashin girar shi daya cure ya cakuɗe ya haɗe dana idanunshi suka bada samfir mai kyau gawani irin gemu na ustazai wanda ya ƙara haska masa fuskar tare da saje mai ƙayatarwa.
Zama ammi tayi tana mai kallon bebi cikin kulawa.
Shima ƙarasowa yayi kusada ammi ya zauna yana ɗaukar remote, Cikin nutsuwa bebi kejan jikinta harta ƙaraso gaban ammi sannan taɗanyi ƙasa da kanta.
"Umma ina kwana fatan antashi lafiya?".
Tafaɗa kanta a sunkuye sabida yadda ta tsinci kanta dajin nauyin matar.
Cikin murmushi ammi ta saka hannu ta ɗago kan bebi tare da cewa.
"Lafiya ƙalau amman niba umma bace sunana ammi kamar yadda ƴan uwanki suke gayamin kinji ƴar autata"
Tafaɗa tana kallon fuskar Bebi sannan ta ɗora da cewa.
"Yaya sunanki autata?".
Bebi tsintar kanta tayi dajin daɗi yadda matar ta karramata tajata ajikinta batare data nuna mata wani abun ba.
Sannan ta ɗago sosai.
"Sunana Bilkisu, sedai ƴan gidanmu suna cemin Bebi".
Karaf ya ɗago yana kallonta ashe sunan amminsa ke gareta.
Far'ar ammi ce ta ƙaru.
"Lah....lah ashe takwara tace kai amman nagode da wannan suna bilkisu mai gadon zinare matar Aliyu".
Ammi tafaɗa cike da tsokana tana dariya kaɗan-kaɗan.
Sunkuyar da kanta tayi tana mamakin yadda ammi take janta ajiki.
"Masha Allah bilkisu ga ɗana nan nima nabaki amana kamar yadda mamanki tabawa Aliyu amanarki dan Allah nima ina roƙonki daki masa biyayya kamar yadda na umarceshi akan ya kwatanta adalci akanki, ku zauna lafiya komai yace karki musu kinganni nan nida mahaifinshi shekarunmu 45 da aure tun ina shekara 15 aka auran shi kinga yanzu inada shekara 60 aduniya, bantaɓa yaji ba haka xalika bai taɓa shikana ba yanxu haka ƴaƴana 8 ciff babban su yanada yara 3 mata ɗaya kuma shi kansa ya shekara kusan 41 aduniya amman bamu da

matsalar komai nida abbansu dan Allah kema kiyi koyi da mai sunan taki kinji autata matar ɗan autana a maza".
Ammi tafaɗa tana janyota jikinta.
Cikin sanyin murya bebi ta dubi ammi tare da cewa.
"Insha Allahu nagode"
sakin hannunta ammi tayi tare da tashi tayi cikin wani lungu falon yay saura dagashi se ita.
matsawa tayi jikin kujera ta raɓe sabida yadda taga ya haɗe ranshi tamau yana kallon tv kamar baisan da biladam a falon ba.
har ammi ta dawo falon bayanta ƴan aikine mutum biyu kowanne hannunshi ɗauke da tiren sliver,agaban bebi suka aje tiren sannan suka gaisar da Aliyu kana suka juya suka bar falon.
Zama ammi tayi tana kallon bebi.
"Auta ga abinci nan kici ki ƙoshi in kin gama ina ɗakina kizo ki sameni, kaikuma kaje kai parking komai zuwa 12 Zaku wuce".
Tana gama faɗin haka ta miƙe tayi cikin ɗakinta.
Zumɓura baki yayi gaba tare da takewa ammin baya yabita ɗakin kamar jela.
Ita bebi ma dariya ya bata jiba kamar wani ɗan yaro yabi ammi yana tura baki lallaima wannan man ɗin.
Jawo tiren abincin tayi tana buɗe fulasan kai.
ɗayan farfesun farin kifine ɗayan kuma soyayyar doyace fara tas babu ƙwai se ɗayan kuma farfesun kayan cikin ragone.
Babban fulas ɗin tean ta buɗe shikuma kunun gyaɗane wanda yay fari tarr alamun anzuba madara aciki se cokula da plate tare da kofi.
Ƙwalla ce mai zafi ta zubo mata sannan ta dubi farfesun.
"Allah sarki mama dasu hassana da arfa da shahid inama zakuzo damunci tare ALLAH sarki mama koyau me zataci oho wallahi inda babu masu tsaron gidannan dase na boye wani na gudu nakai masu suma sunci sunji daɗi".
Tafaɗa tana maijin kewar mahaifiyarta da ƴan uwanta.
"Hmm koda yake mama ta hanemu da ɗaukar abinda ba namu ba nidai tunda iyani suka bawa naci kawai  inyaso sena basu labari in sunzo, kona tambayi Boss nace masa ya tambayi ammin ta bani na kaiwa mama oh! koda yake babu kyaufa roƙo ba ɗabi'a bace mai kyau sannan kuma babu kyau ɗaukar kayan miji kayi kyauta dasu musamman in bai sani ba wannan ba ɗabi'a bace mai kyau ina dai fatan Allah kabani sana'a mai kyau wadda zan tallafi ƴan gidanmu amin".
Tafaɗa tana mayar da ƙwallarta wadda ta haɗe da miyan ƙwaɗayi domin tuni miyan mutuniyar ya tsinke sabida ganin hadaya agabanta.
Ƙamshin farfesun shiya hanata magana lokacin da Aliyu yazo ze gifta ta gabanta ya fita daga falon.
"Ni zan koma ki tabbatar kinyi wanka kafin na dawo kiyi brush kafin kici abincin".
Yafaɗa yana kokarin fita.
Wani irin wullll tai da idanu kamar na farar kura tana kallonshi batare datayi magana ba still hankalinta yana kan fulas ɗin dake gabanta.
Dariya yarinyar ta bashi harya fita yana yinta daga gani yarinyar kurace za'ai daru da ita wajan cin nama.
Mayar da ajiyar zuciya tayi tana shakar kamshinsa tare da maida kallonta ga fulas ɗin gabanta.

Hannu na rawa ta ɗauki plate guda ta kusan juye rabin doyar sannan ta kwaɓe farfesun kifin kaff akai tana cewa.
"Tabb loma ba in carry yaushe gamon ƙauna ai wallahi Allah bantaɓa cin irin wannan farin kifin ba gwara naci na donge".
A bayyane take faɗin hakan.
Sannan ta janyo kofi ta zubo kunun gyaɗar cikin fulas wanda yaji suga ta ɗaga kofin ta kurɓa tare da zaro idanu.
"Kai lah ashe da madara aciki ina tsoron haɗa madara da kifi kar cikina yay ciwo".
sekuma tayi dariya kamar sakarai.
"In zakasha giya shata dubu inji bahaushe bara na aje wannan kunun agefe gwara naci kifin na haƙura da shan kunun duk da farin kifine babu ƙarni amman dai sabida tsaro gwara na hakura".
Ta janyo plate ɗin tareyin bisimillah ko cokalin bata saka ba tafara cin abincin kunnenta yana tsalle kamar ze faɗi.
Gyara xama tayi tana ci tana kallo wayyo ran bebi ze fita dama akwai abu mai daɗi kamar wannan na gaban nata.............

***********************

Bacci ɓarawo shiya sace mama a wannan dare cike da tunanin bebi aranta tana kuma yi mata addu,a tare da fatan zaman lafiya.
washe gari tunda asubahi............

*manage bana da caji yau*

*PART* 2

NAKUƊINE

*78*

Mama ta tashi su hassana akan suyi sallah sannan su fara haramar ɗora abin karin kumallon safiya sabida har zuwa wannan lokaci basu koma kamfani ba, Sanin halin Bebi na rashin tashi

akan kari yasa duka ƴan uwan nata basu wani damu da tashin nata ba kowa ya miƙe yaje yay alwala suka dawo ɗaki sukai sallah.
Seda gari yaɗan soma shaa alamun haske sannan hussaina ta duba makwancin bebi taga wayam kallon mama tayi cikin mamaki tare da cewa.
"Mama ina bebi ne banganta a makwancin taba?"
Seda mama ta shafa addu'arta sannan ta dubi hussainar kana tace mata.
"Ai bebi tayi kwanan gidan mijinta kudai kubita da addu'a kawai".
Gaba ɗaya ɗakin shuru ya ɗauka kowa yana jimanta rabuwa da bebi domin hassana har hawaye seda ya zubo mata.
"Amman mama mai yasa baki tashe mu mun rakata ba naga ai ana rakiya gidan amarya".
Inji hassana wadda take share hawayenta sabida Allah ya zuba mata ƙaunar Bebi akaf ƴan uwanta tana mugun son Bebi.
"Abinne yazo mana a gajarce amman usman yace zezo ya kaiku".
Cikin mamaki duka suke kallon mama kafin hussaina tace.
"Mama wai waye mijin Bebin munji kince ya usman?".
Murmushi mama tayi sannan tace.
"Ƙanin usman wanda sukazo rannan sunanshi Aliyu amman fa naji ance yana da mata kuma baiyi sati guda da auren ba"
Cikin tsoro hussaina tace.
"Tabb yasin nasanshi kice ZAKI bebi ta aura lallai wannan kuwa ze saita ta wallahi mama ranar dana ganshi kamar zanyi fitsari wannan aiya kusan haifar kamar bebi amman kuma ya aureta tabb wallahi mama nayi mamaki sabida gidansu fa suna da kuɗi Allah ya basu zaman lafiya ashe dai rabon mama tazama surukar mai atamfa ne yakaimu kamfani lallai na yarda komai silane tabbas rabon auren bebi ya kaimu talle kamfani'
Tafaɗa tana murmushin murnar ƴar uwarsu ta sami gidan hutu.
Gyara zama mama tayi tana kallon ƴaƴan nata sannan ta soma magana kamar haka......
"Ai daman komai kuka gani baya faruwa seda abu uku! na farko lokaci na biyu rabo! na uku kuma shine sila tabbas Allah ya rubuta Bebi zata auri wannan yaro sedai kuma ta silar tallen kune auren ze haɗu kuduba fa kuga yadda bebi taƙi tallen kamfanin tun farko ashe duk wannan zamiyar datake rabon auren ta yana can.............
Sannan kuma abu nagaba shine komai da kuka gani a rayuwa Allah ne ke tsarawa ta yuwu ta silar Bebi muji daɗi arayuwa ta yuwu ta silar Bebi muji takaici arayuwa, tunda na haifeta nake fama da ita itace ɗaukomin magana a waje tsokana faɗace-faɗace itace ƙin zuwa makaranta itace aljanu itace rashin son aiki, amman duka na hakura nacigaba dayi mata addu'a batare danayi fushi da itaba batare dana wareta cikinku ba, toga karshe dai jiba kuga yadda Allah ya nuna ikonsa akanta babu mamaki  a farkon rayuwarta Allah ya nufa zansha wuyarta daga ƙarshenta kuma naji daɗi ajikinta, wannan dalilin yasa nake kira ga duk wata uwa data zauna ta fuskanci lamarin ƴaƴanta tai iya yinta wajan gwada musu dai-dai tare da binsu da addu'a domin uwa ita makarantar farkoce, ina roƙon Allah yasa yadda nagama da ita lafiya kuma Allah ya rabani daku lafiya Amin".
Jikinsu ne duka yayi sanyi ƙalau dajin wa'azani mama tabbas maganar mama gaskiyace sannan kuma bawai dan mahaifiyarsu bace tabbas da wuya ka sami mahaifiya kamar mama wadda zata zauna ta jajurce wajan kula da tarbiyar ƴaƴa mata har guda biyar cinsu shansu

sutturarsu karatunsu uwa uba kuma basu tarbiya tabbas inda wata uwarce dafa tasami damar buɗe hannun jarine da ƴaƴan nata, amman ita ta zaɓi zaman basu tarbiya kula dasu batare data dubi wannan ba.
"Allah ya saka miki da alkairi mama haƙiƙa kincika uwa tagari Allah yabaki ikon cinye jarrabawar daya ɗora miki domin riƙonmu tabbas jarabawace agareki".
Cewar hassana tana goge hawayen tausayin mahaifiyar tasu tanajin tsananin kaunar mama acikin zuciyarta.
"Amin ya Allah hassana, sannan abu nagaba inason sanar muku da cewar kuma maganar auranku tana tasowa duk da nasan baku riga kun wayu da mazajen nakuba amman tun kafin rasuwar abbanku yabada wasiyar ke hassana a bawa Nuraddeen ke kekuma hussaina abawa Al-ameen. ƴaƴan wajan babanku ado sabida haka jiya malam ya tadarmin da maganar dan haka nan da karshen shekara za'ayi bikin kafin nan su yayyan naku sun kammala gininsu dasuye anan anguwar gaidar ƴankusa tunda kunga daman shi nura naji ance likita ya karanta kuma takaddar aikinshi ta fito, shikuma aminu lauya ya karanta kuma duka alhamdulillahi jiya iya datazo akan maganar auren bebi take cemin dukansu sun sami aikin gwamnati yanzu abinda ya rage musu ƙarasa gininsu da kuma haɗa lefe sannan kuma tacemin sunce anemi izinina zasu soma zuwa taɗi wajanku".
Tsitt ɗakin yay sabida yadda ƴan biyu sukai ƙasa da kansu alamun jin kunya yin duniya mama tayi maganar amman basu iya tanka mata ba( hmm kenan ƴan biyu sunfi Bebi kunya ohhhh! ).
"In baza kuyi magana ba kunga tashina arfa ihsan kuzo ku miƙa markaɗan koko kunji kukuma in kungama gulmar kwa saman wannan sunne kan bani zakuwa ba kuje kuyiwa iya ja'iran kawai".
ta miƙe ta saka ƴaƴanta agaba sukabar ƴan biyu a ɗaki suna faman sunne kai ƙasa.
seda suka tabbata mama tabar ɗakin sannan hassana ta mike tai tsalle akan katifa.
"Wayyo! Allah nagode maka daka bani zaɓin raina kinsan Allah hussaina batun yau nakeson ya nura ba sabida shuru-shurunsa yana burgeni kinsan kwanaki dazemin allura daya matso gabana jinai kamar kada murabu".
Dariya hussaina tayi sannan ta dubi hassanar.
"Tabb ni ai kawai jin mama nake kenifa tuni ya Al-ameen yagama fayyacen komai kinsan Allah ko ranar da bebi tai iskar nan ma seda ya kirani waje mukai hira kinsan shifa daman barrister ne akwai surutu bai wani tsaya kwana kwana ba yagama fayyacen komai wai sabida kar ai masa shigar sauri nima ina sonshi wallahi ko banza mahaifi ƴaƴa farare kinga mu farare su yaya ma haka wayyo bebi itace mai miji baƙi".
Hussaina takai maganar cikin farin ciki.
Tashi zaune hassana tayi.
"Wallahi hussaina baki san kyau ba ai Bebi fa duka tafimu more miji sabida mijinta top class ne babu ƙarya ai ita tagama dace amman muma ɗin babu abinda zamuce da Allah se godiya amman ina gargadinki da kicire mijin Bebi a lissafinmu sabida yay mana gudun wuce sa'a daga mu har mazajan damuka aura kinji ko".
Dariya hussaina tayi kana tace.
"To mu madai mungode Allah kuma muna kuma godiya gareshi tashi muje muyi abin kari madam danni yau gidan Bebi zan wuni dan senaje na kashe kwarkwatar idanuna".
Kamar wasu ƙawaye suka jera daman su kansu ɗaya kuma komai nasu ɗaya hatta kama sedai hassana taɗanfi hussaina kama da Bebi domin hassana suna mugun kama da Bebi sosai

inkaga bebi sekace hassana ce sakuwarta kasancewar Bebin duka tafisu girman jiki.
Ita kanta mama tayi mamakin yadda suka jima a ɗakin sannan kuma tayi mamakin yadda suke wani nan nan da juna yau ta fuskanci bayyanar maganar aurensu tayi musu daɗi amman tsabar alkunya yasa basu nuna mataba sedai tagani a aikace domin hatta tafiyar aikinsu nayau yasha bam-bam da sauran ranaku domin tuni suka tace gasarar koko suka haɗa wuta nan danan suka haɗa koko da ɗumaman tuwon karin kumallon safiya.
Tabarma suka baza a tsakar gida suka zubowa mama nata nasu kuma suka zuba a katon tire na shahid daban a wani ɗan farantin roba sannan suka zagaye waje ɗaya sunacin tuwon da kokon amman gefe guda hirar bebi suke.
Ihsan mai bin bebi itace tace.
"Mama ƙilafa bebi tana can tanacin farfesu yanzu".
Dariya mama tayi tace.
"Ba mamaki amman fa harna hango bakin mutuniyar".
Dariya suka kwashe da ita.
Shahid ne ya dubesu.
"Ai wallahi idona idon storen gidan Bebi senaje na ɗebo adadin idomie ɗina data cimin domin bafa zan bari ba".
Mama garin dariya seda ta kusan ƙwarewa.
"Kaikuma haka ake girman ai babu kyau ɗiban kayan miji nidai bada yawuna ba kaje dai kaci iya cinka amman banda guzuri ni ba'a gidana ba ko ita ta ɗebo ta kawon nikuma zan kira Aliyu na gaya masa nakuma ce yazo ya kwashe kayansa".
Cikin dariya tai wannan furuci mai kama da wa'azi ga ƴaƴan nata.
"Nama fa hana ana cin abinci ana magana nima kuma nazo na biye muku kuyi muci mugama muga kuma mezamuyi".
Cikin nutsuwa suka cigaba dacin abincinsu batare da wani ya kuma yin wani furuciba.
*******************
*CIKIN GIDA ƳAN KUSA*

Kimanin karfe shidan safiya kawu rabi'u Kawu tasi'u da sauran ƴan uwan mahaifinsu Bebi suka hallara a ƙofar gida suna tsara maganar yadda zata kaya da ɗaurin aure shawara suke akan yadda lamarin ze kasance wasu suna ganin kawai a ɗaura anan ɗin wasu kuma suna ganin atafi can ƙofar gidan mama a ɗaura auren domin tuni alhaji mai gwall yace zasu zone da misalin karfe taran safiya.
Kawu sani shiya dubi kawu tasi'u tare da cewa.
"Uban ango uban amarya ina kake ganin ya dace a ɗaura auren sabida kaine silar kafuwar auren nan?"
kawu tasi'u wanda yake dogon tunani akan jin shurun mutumin jiya mai tafiya da lefe shiya dubesu fuskarsa cikin damuwa sannan yace.....................

*PART* 2

NAKUƊINE

*79*

"Ina ganin kawai atafi can gidan uwarta a ɗaura mata auren domin mu baza,a barmu da yin tuwon ɗaurin aure ba gwara kawai in munje an ɗauro auren mu zame mu barsu acan su ƙarata".
Cewar kawu tasi'u kenan wanda ya faɗi maganar cikin ƙwarewa da mugunta.
Dariya sauran sukai sannan  kawu rabi'u ya miƙe yana kaɗe babbar rigarshi.
"Hakan yafi kaga daganan seka ɗauko mana lefe mu rabe tunda mekuma yay saura an rigada an ɗaura".
Cikin kawu tasi'u ne ya bada sautin ƙuuuuuuu! sannan ya fakaici idanun ƴan uwan nashi ya watsa masu harara amman a bayyane se cewa yay.
"To!to babu komai Allah ya kaimu lokacin kumiyi mu tashi muje muyi wanka mu shirya kada suzo suna jiranmu kunsan manyan mutane basa son jira".
Kowa yay na'am da maganarshi dan haka duka suka miƙe tare da.shiga cikin gidan kowa yay nashi shashen domin yin shirin fita ɗaurin aure.
Ko a ɗaki kawu tasi'u yana zaune bakin gadon ƙarfen matarshi hannunshi ɗauke da man shawafa na mai gurguwa yana lakatowa yana mitstsikawa a fatar ƙafarshi matarshi wadda ke zaune daga gefenshi ita ta dubeshi.
"Amman baban ladi abin nan naka akwai lauje cikin naɗi acikinsa tsakani da Allah ga ƴaƴanka ƴammata a zaune babu manemi faccaloli suna mana habaici amman ka tsallakesu katafi can wajan ƴaƴan mamaci ka ɗauki ƴa guda acikinsu ka kaita gidan maiƙo kai ƴaƴanka ko oho kenan kafison sune akan naka koko wata sabuwar ƙaunace ta motsa? ko kuma ita aishan ka leƙa kagani kakeso shine kake ɗan biki?".
Dariya ya kece da ita kamar wani taɓaɓɓe seda ya kusan mintuna talatin yana faman yin dariyar kafin ya ɗago ya dubeta sannan ya aje man a gefenshi.
"Haba babar ladi ina son ki ƙara fahimtar waye mijinki, ke kintaɓa ganin inda kaƙi ɗanka ka kama na gaibu? to bara na feɗe miki biri har bindinsa".
Ya faɗa mata hakan tare da mikewa tsaye ya ɗauki sabuwar shadda fara ƙarr ya soma sakawa cikin sauri seda ya kammala sannan ya dubeta wadda ta haɗe rai tana jiran kota kwana.
"Wannan aure dazamu haɗa waccan ƴar iskar da wannan gantalallen yaron to ba dan Allah bane ba, wato kinsan Alhaji mai gwall da mugun sangarta ƴaƴa mu kammu hakuri muke da zama a ƙarƙashinsa sabida halin ƴaƴansa, to hakance tasaka garin sangarta ƴaƴansa yaje ya

lalata ɗansa khaleefa wanda yaron bakiga ashararancin dayake agariba kowa fa kuka yake da ɗan ɗanda bai ganin darajar manya bai ganin darajar kowa akanme zan ɗauki ƴata ta cikina na bashi ɗanda kullum yake cikin maye ubansa na kuma ɗaure masa gindi naje wataran ya kashen ƴata, to bama tawan yagani ba waccan matsiyaciyar ya gani yace yana so Allah cikin ikonsa akai arashi ƴar tazo a ƴar musa namu kinga ai faɗuwa tazo dai dai daxama shine na shiga na fita na ƙulla auren domin a dabgi arziki dani to kinji yadda ta kaya".
Dariya matar tashi ta saki sannan ta dubi mijin nata.
"Yanzu naji batu ashe dai duk gayyar tsiyarce kaida ci arziki baban ladi amman su ladi se gani daga nesa kai amman aisha anyi sokuwar mace yoni inda nice ai baku isaba, kai yanzu dan Allah bakaji kunyar aisha ba dakaje a matsayin ɗan uwan uban ƴaƴanta kun manta irin cin kashin da kukai mata amman ita harta tsaya ta saurareku wallahi inda nice seka tawo da makahon idanu".
Haɗe ranshi yayi"kefa haka halinki yake jarabar masifar tsiya to seme nace seme mudai mune tilashin ƴaƴan kota ƙi kota so dan haka yanzuma muna gama wannan zamu ƙara famjamawa mu ɗaukowa sauran wasu ƴan ƙwayar mu game mu huta".
Murmushi kurum tayi batace masa komaiba amman  har cikin ranta ta jinjinawa aisha duk da bata son maman su bebi ko kaɗan amman setaji ta bata tausayi sabida yadda taga maxajen nasu na shirin ƙara jefa rayuwar ƴaƴan nata cikin gadar xare.
Harya fita baice da ita komai ba sabida haushin data bashi na yadda taji tausayin maman biyu, bayan ya manta su daman mata ababan raunine da wuya mace taga ƴar uwarta mace acikin wani yanayi bata taimaketa ba wannan abun yana matukar wahala kasancewar mata akwai tausayi da rauni koda baka bawa wanda kagani cikin wani hali agajiba tofa acikin ranka zakaji raunin hakan tare da zafi.
Abakin kofar gidan duka suka taru tare da sauran maƙota daƴan tsirarun dangi dasuka gayyata domin halartar ɗaurin auren.

Ƙarfe tara saura suka nufi sharaɗa can anguwarsu bebi lokacin tawagar Alhaji mai gwall tuni itama tayi gaba domin Khaleepha ya riga yasan gidansu bebi shiyasa basu sha wahalar gane gidan ba, Kusan a tare suka haɗu a ƙofar gidansu Bebin wanda har yawan mutanan wajan yaywa kofar gidan kaɗan.
Ƙarfe tara da rabi duk waɗanda suka kama zasu haɗu a wajan ɗaurin aure sun haɗu dan tsabar isa harda tabarmai suka taho dasu aka shinfiɗa a ƙofar gidan.
Cikin sauri shahid ya shiga gida yake shaidawa mama halin da ake ciki awaje domin shiya ɗauka ma rasuwa akai sabida baida masinyar komai.
Murmushi mama tayi sannan tace.
"Mugunta fitsarin faƙo maza jeka kira malam tare da mai unguwa dan Allah banda sanya ka faɗa masa halin da ake ciki sabida kada a ɗaura aure akan aure".
Shahida bai jira mama ta ƙarasaba ya danna kai aguje ya tafi wajan malam lokacin dayaje ma tuni maganar ta isa kunnen malam ɗin zaman jiran mai unguwa ma yake yazo su nufi wajansu kawu tasi'un shahid baiko zauna ba mai unguwa yazo suka rankaya atare cikin sauri zuwa wajan ɗaurin auren.
Mama tana daga cikin gida tanajin ana addu'ar fara ɗaurin aure babu abinda take se hamdala

ga Allah wato cin zarafin dasukai niyyar mata kenan Allah ya tsallakar da ita.
Lokacin dasu malam suka ƙarasa wajan lokacin ne kuma yay dai dai da sanda limamin dasu alhaji mai gwall suka tawo dashi ya miƙe tsaye yana ambatar sunan tasi'u akan ya fito wajan wakilcin auren ɗiyarshi.
Jiki na rawa kawu tasi'u ya mike zuwa wajan domin shine waliyin bebi.
Cikin nutsuwa mai unguwa yay sallama a tsakiyar wajan.
Sabida shurun da wajan ya ɗauka sakamakon gabatowar ɗaurin auren yasa kowa yaji sallamar mai unguwa.

"Yawwa ina son na sanar da dukkan al'ummar dake wajan nan cewar, su dakata da wannan ɗaurin aure domin ko anyishi bai halatta ba".
Cikin hargagin masifa kawu tasi'u ya mike tsaye.
"Sabida mai bai halattuba munafuki nace sabida me sabida kai ubanmu ne bamu nemi izinin kaba kaga kada  kaga kaifa mai unguwane bazaka nuna mana halin iko muda ƴarmu ba ehe".
Murmushi mai unguwa yayi tare da karɓar loudspeaker dake hannun liman wadda akazo da ita irin mai amfani da batir ɗinnan ce sabida kowa yaji komai.
"Ba dan ni mai unguwa bane ba yasa nace aure bai ɗauru ba sedan musulunci yadda yay mana nuni da hani da ɗaura aure akan aure bi ma'ana ita wannan yarinya bilkisu yau take kwana ɗaya tal agidan mijinta na sunna wanda nima na kasance ɗaya daga cikin waɗanda suka zama shaidun ɗaura wannan aure wanda kuma ba kowane ya kasance mijin nataba se ALIYU IDRISS MAI ATAMFA:MD MANAGER NA MAI ATAMFA TEXTILES! Wanda nasan in wani bai sanshi a wajannan ba tofa wani ya sanshi".
Mai unguwa yana gama faɗin haka ya juya zebar wajan.
"Ƙarya kake nina fi kowa sanin suwaye familyn mai atamfa ko ƴaƴan manyan masu kuɗi alhaji idi baya barin ƴaƴansa su aura sabida basa AUREN BARE azuri'arsu bare kuma wannan kucakar ƴar matsiyata kawai inzaku fito mana da yarinya ku fito mana da ita wannan shine magana sabida ni ɗinnan abokin cinikin alhaji idine babu yadda za'ai ɗan sa baba Ali yay aure mukasa sani wallahi ƙarya ne duk da kwanakin nan inna kira layin haji idi bana samu amman nasan kota egmail ɗinsa ze turo mana".
Mai unguwa yaji saukar muryar wani kakkauran dattijon mutum baki yana faɗin wannan magana a zuciye.
"Iya gaskiyar lamarin kenan amman inzaku ɗaura ku ɗaura ammanfa kusani kun ɗaura banza domin angaya muku gaskiya malam zomu wuce duk wanda yake da tamtama acikin wannan lamari seyaje ya tambayi shi ALIYUN".

Yana gama faɗin hakan yaja hannun malam suka bar wajan.
Cikin sauri wannan mutumin ya lalubo lambar wayar Alhaji idiris ya soma kira amsar ɗayace wayar tana kashe dafe kanshi yayi tare da kiran md ɗin abba nacan abuja shima wayarshi akashe take bashida number kowa a ƴaƴan abba kuma sunɗan jima basu haɗuba dan haka yaja tsuka tare da kallon alhaji mai gwall wanda ranshi yay ƙololuwar ɓaci.
"Yallaɓai wannan magana fa zata iya xama gaske kasan alhaji idi akwai tausayi a shawarce kawai a janye wannan magana sabida kaima sanin kanka ɗan alhaji idi kaɗai baka isa kaja dashi ba bare kuma shiɗin kansa dan haka kasan yadda zakai da lamarin nan danni tunda naji

an ambaci mai atamfa jikina yay sanyi alhaji".
Cikin tsabar takaicin yadda aka kunyatashi ya juyo ga wannan mutumin.
"Wato alhaji isyaku na rantse da Allah bantaɓa jin takaici irin wannnan ba tabbas wannan bawan Allah ya yaudaren sabida tsabar son abin duniyarsa inaga yaje ya bawa mai atamfa yarinyar sabida yafini kuɗi".
Cikin lokaci kaɗan magana tacika unguwa tuni mutane sukaita darewa suna watsewa.
Ƴan tsiraru suka rage se khaleepha dake faman danna ashar kamar ze doki kawu tasi'u.
Cikin zafin zuciya alhaji mai gwall ya dubi tasi'u wanda gumi ke faman keto masa kamar an masa wanka da ruwan ɗumi.
"Wallahi bakaci banza ba kai gaba ɗayanku ma zakusan kunyi dani sabida haka ina son ka tattaron komai nawa daka san kaci hatta lefene na jiya da aka kawo ka mikomin sannan zan dokaku ƙara a kotu wallahi bazan yarda ba".
Cikin sauri Rabi'u ya riƙe babbar rigar alhaji mai gwall yana masa magiya.
"Tabbas munsan mun tozartaka alhaji agaban mutananka ƴan uwanka abokanka dan Allah kai haƙuri muma bamu san da wannan magaba seda mukazo amman acikin ƴaƴan tasi'u akwai manyan ƴammata da basuyi aure ba meze hana a bashi ɗaya tunda duk suna nan gundum gundum babu aure dan Allah ka duba lamarin".
Cikin firgicin maganar Rabi'u Tasi'un ya rarrafo.
"Kaimin rai alhaji kada ka haɗa auren ƴata mai mutuncin da wancan......seyay shuru sabida ya tuna katoɓarar dazeyi.
Murmushi Alhaji mai gwall yay.
"Oh wato duk abinda nake maka kallona kake shasha wato ɗan nawane ɗan iska malam liman dawo ga sabon ɗaurin aure nan wallahi seka ɗaura auren ƴarka da khaleepha ka zaɓi ɗaya kokuma na makaka a kotu ka biyani duk abinda kaci'.
Wannan shine ga ƙoshi ga kwanan yuwan mugunta fitsarin faƙo inji bahaushe kawu tasi'u yayi gudun gara ya tarar da zago domin bashida kuɗin biyan alhaji kuma baya son ƴarsa ta faɗa hannun khaleepha sabida yafi kowa sanin illar yaron.
Yanaji yana kuma gani shedu suka shaida ɗaurin auren ƴarsa ladi da khaleepha a kuma ƙofar gidansu Bebi wanda kafin ma a gama ɗaurin auren zuciyar kawu tasi'u tai wani irin zafi kansa ya ɗau ciwo ana gama ɗaura auren yana zube a wajan sumamme
Cikin ko in kula alhaji mai gwall ya tsallakeshi ya wuce yana bada order aje can gidan tasi'un a ɗauko musu amarya sesu Rabi'une suka tarairayeshi suka ɗauko ɗan sahu suka sakashi aciki sukai gida cike da mutuwar jiki.
*Koba ba'a mutuba tofa akwai hisabi tun a duniya wanda yake aikata ba dai daiba yana da kyau ya gyara tun aduniya kafin ya rasu sabida ita duniya darasi gareta wannan ya kasance iznah ga masu hali irin na su kawu tasi'u tabbas wanda Allah ya kare babu wanda ya isa ya cutar kazama mai sanya Allah cikin lamuranka domin shine maji roƙo mai ƙarfin mulkin da babu irinshi ko alhaji mai gwall bai shari'a dasu tasi'u ba wannan haɗin auren da ƴar tasi'u kaɗai ya isa yazama darasi garesu duk yadda tasi'u yay gudun yarsa ga wannan aure seda ya faru ta hanya mai sauki wadda da yay niyyar cutar da marainiyar Allah ne lallai Allah mai ikone mabuwayine kuma mamallakin komai da kowa tabbas shi alkairi ɗanƙone hakannan sharri ɗan aikene babu wanda ze alkairi ya tafi a banza babu kuma wanda ze sharri ya xauna lafiya dukkanin waɗannan biyun kana girbansune ko a duniya ko a lahira Allah kasa mudace amin*!

Cikin lokaci kaɗan labarin wannan lamari ya cika anguwa motoci kimanin guda uku alhaji mai gwall ya tura can gidansu tasi'un wanda sam matansu basuda masaniyar hakan se ganin motoci sukai a kofar gidansu.............
# *Autar Manya*

*PART* 2

NAKUƊINE

*80*

Abakin ƙofar gidansu kawu tasi'u motocin suka dakata cikin sauri drivern alhaji mai gwall wanda daman shi tuni yasan gidan sabida dashi aka kawo lefe sannan kuma shi alhaji mai gwall ya turo suzo su ɗauki amarya ya buɗe marufin motar daya tuƙo tare da fitowa daga cikinta ya nufi kofar gidan tare da bubbuga ƙofa yana maka sallama.

Cikin tsananin mamaki matar kawu Rabi'u ta turo yaronta ya duba mai doka musu ƙofarsu sabida sune a sashen farkon gidan shiyasa komai akai a ƙofar gida suke faraji.
Yaron ne ya dawo mata da cewa wai ga baƙi nan zasu ɗauki amarya, Cikin tsananin mamaki tai ɗan ƙuri da idanu alamun tana tunanin wani abu kafin ta miƙe ta shiga cikin gida tana maka buɗa.

"Ayyiri!yiri!! matan gida ku fito anfa ɗaura munci lefe kunga ƴan wahala sun tawo mana nan ɗaukar amarya muda inzasu kashemu bamusan kalar amaryar ba kai maza ɗalha jekace musu babu amarya anan tana can gidan tsohuwarta koya kukace jama'a?".
Cikin sauri tare da zafin zalama babar ladi matar kawu tasi'u ta tashi tsaye wadda zaninta har kuncewa yake sabida garin sauri ta tsaida ɗalhatu tare da kallon sauran matan.

"Yaya zakuce haka bayan kuka sani koda uban angon akazo yanzu dan Allah idan muka leƙa da kammu kukasan garar daza'a ƙara ninko mana kai ɗalhatu zauna ni bara na leƙa kuma kada wadda taganni da ƴan canjina tace na ƴammata".
Tafaɗa tana yayar zani akan igiya ta yafa a saman ka kamar tsohuwar mahaukaciya haka ta danna kanta waje matar kawu sani tana take mata baya.

Wajan drivern Alhaji mai gwall ta ƙarasa tana wani rawar jiki kamar sabuwar kamun hauka.
"Ranka shi daɗe ai banan bane gidansu yarinyar amman in bazaku ganeba koni kuka biya aisena rakaku".

Tafaɗa cikin zaro idanu tana kallon dalla dallan motocin dake fake a ƙofar gidan nasu aranta take ayyana wannan aure akwai kyawun maciji bada ban hatsarin wannan yaroba ai damu zamu danna kai koda tsiya koda tsiya-tsiya semun shiga amman wannan ɗa tunda naga malam yay gudun haɗa iri dashi tabbas na shaida baƙaramin *Tantiri bane ba waɗanda basa jin magana ko guda*!

Maganar drivern alhaji mai gwall ce ta dawo da ita daga duniyar tunanin data faɗa"Hajiya ai nan gidan aka turomun koba nan ƴar gidan malam tasi'u take ba naji ance ko maryam amman dai ladi naji ance ai da ita aka ɗaura *auren* " yafaɗa cikin tabbatuwa da maganar daya faɗi ɗin.

Zanin datake riƙewa shiya sunce cikin tsananin tsoro ta dubeshi.

"Kai sokon ƙauye dakata babu wata ladi da aka ɗaurawa aure da watsats tsan ɗanku sedai ko balki kuje can ku ƙarata".

Tafaɗa cike tsoron gudun kada wannan lamarin ya tabbatu,Murmushi drivern ya saki tare da kallon sauran na cikin motar waɗanda suke yaran alhaji yanawa ɗaya daga ciki magana.

"Eh tabbas da ladi aka ɗaura aure bada balkiba sakamakon yadda mijinki yay munafurci wa alhaji shiyasa ɗaurin auren ya koma kan ɗiyarki ita waccan ai tun jiya tana gidan nata mijin".

Cewar wani ɗan siririn mutum ɗaya daga cikin yaran alhajin daya turo yake shaidawa babar ladi haka, wata zabura tai mai kama data mahaukata tare da faɗuwa ƙasa daɓas kamar zautacciya.

"wallahi baku isaba babu shegen daya isa ya tafarmin da ƴata wallahi bazan bawa waccan ɗan iskan yaro ƴataba sedai duk abinda za'ai ayi yau ɗinnan amman ni wallahi bazan bada ƴata ba"

Tafaɗi maganar tana kurma ihun daya jawo hankalin sauran matan gidan dukansu suka fito kowa yana tambayar ba'asin meke faruwa drivern Alhaji mai gwall ne ya dubi matan wajan waɗanda suke tambayar ba'asi cikin nutsuwa ya wassafa musu dukkan abinda ya faru a wajan ɗaurin aure daga ƙarshe ya ƙarasa da cewar dan Allah suyi sauri su kawo masa amarya suna ɓata masa lokaci Alhaji yanata waya.

Cikin wannan ƙadamin su kawu rabi'u suka sauko daga cikin adai daita sahu wadda suka ɗoro kawu tasi'u cikinta wanda yake faman surutai kamar wanda ya sami taɓin hankali

"Wallahi bazan basu ladi ba! wallahi bazan basu ladi ba sedai su kasheni sedai suyi dukkan abinda zasuyi"!! Abinda yake faɗi kenan tun bayan dasuka daukoshi a mota bayan ya farfaɗo daga gajeren suman wucin gadin daya yi awajan ɗaurin aure.

Kawu Rabi'u da kawu Sani sune suka riƙoshi shikuma kawu salisu ya sallami mai ɗan sahun daya kawosu sannan suka ƙaraso ƙofar gida anan suka kuma cin karo da tashin hankalin dayafi na wajan ɗaurin auren domin tuni jama'a sun fara taruwa wajan kallon yadda matar kawu tasi'u take zunduma ashariya tana bataga ɗan kan uban daya isa ya ɗaukar mata ƴaba koda kotu ze kawo ba ƴansanda ba babu wanda ya isa ya ɗaukar mata yarinya abawa ɗan giya shi alhaji mai gwall ɗin dan ubansa mai yasa bai tsaya ya bawa ɗansa tarbiya mai kyau ba? ai gashinan ya zama mujiya acikin al'umma ire-iren waɗannan maganganu taketa saki wanda har su tasi'un suka karaso wajan bata dainaba mutan gida masu dariya sunayi masu bata baki sunayi.

Zuwansu kawu tasi'un ne yasa tayi shuru tana aika masa da harara wanda ya watstsake tunda yaga motoci fake a ƙofar gidansu.

Kallon drivern alhaji mai gwall yayi tare da riƙe ƙugunshi.

"Kaima mallam iro dakai za'aci mutuncina? dakai za'a shiga rigar darajata a ƙeta min kana kallo za'a ɗaura auren wancan tsinannan yaron da ƴata ta sunna ka bari?"
Cewar kawu tasi'u wanda ya faɗi maganar a gaggauce alamun kamar baya cikin nutsuwarshi.
Murmushi mallam iro yayi sannan ya kalleshi

"Haba mallam tasi'u kamanta lokacin da kake shigewa falon alhaji kaci kasha kana ɓuɗa hanci kai gaka sirikinsa kana mana kallon hadarin kaji koko wannan kayan abincin da aka kawo maka da kayan lefe banda kuɗin da kaci ka tuna damu? base kallon banzan da kake mana ba kai kaga sirikinshi ai gaya nan yanzu ka zama tabbataccen suruki toni shawarata anan wallahi ka tattauro baƙauyar ƴarka kabamu mu wuce da ita sannan kajawa wannan mahaukaciyar matar taka kunne akan alhaji da ɗansa domin wallahi ruwa ba sa'an kwando bane ba, kasan ko wannan ɗan tsakurin gidan da kuke ciki bai isa ya biya alhaji irin dukiyar daka ci masaba sabida haka masalaha ta xama lafiya itace ka tarkata ka bada wannan ƴa kaga ko iya haka kaje kaita neman gafarar Allah akan laifukan ka domin wannan kaɗai isharace Allah ya nuna maka".
Mallam iro ya faɗi maganar yana kallon mutan wajan waɗanda wasu tuni suka soma yada maganganu akan irin halin mallam tasi'u na son abin duniyar jaraba.

Jin an ambaci sayar da gidansu na gado wanda shi kaɗai ya rage musu yasa tuni kawu sani wanda bai fiye magana a lamarin ba yaja matarshi gefe suka ɗan zanta ta shige gida mintuna uku segata da wata budurwa baƙa ƙirin kamar wadda ta fito daga kwatami ta mikowa kawu tasi'u ita gabanshi.
Kawu rabi'une yace.

"Ke ladi maza shige mota kutafi Allah ya baku zaman lafiya kaima tasi'u tunda an riga an ɗaura auren nan kuma ni nai wakilcin komai na auren ai tazama matarshi dan haka kuyi mata addu'a kawai".
Sum sum ladi dataga motoci masu kyau ta rude ta shige bayan mota tana raba idanunta waje kamar wadda akaiwa bushara da hajji.
Tuni driver ya shiga motar yajata da ƙarfi yabar kofar gidan wanda kusan atare babar ladi da kawu tasi'u sukabi bayan motar suna haɗe baki wajan sakin kuka!

Ganin se ƙurar motocin kaɗai a wajan yasa kawu tasi'u ya juyo yana dannawa ƴan uwansa ashar yana haɗasu da jafa'i kala-kala shikuma daga bayanshi matarshi tana sauke mata nata bala'in tana ai dukshi yaja mata.

Rabi'une yay dariya tare da kallonshi.

"Haba tasi'u ai kowa ya ɗebo da zafi bakinshi kana nufin kura da shan duka gardi da ƙwace kuɗi kenan kagama cin arziƙinka muna kallo seɗan abinda ka sammana sannan kuma taka ta shafemu ina sam baze yuwuba duk irin yadda kake cin mutuncin tsire da kaza a titi yana zuwa kunnen mu dan haka kaida ka ɗauko ka kashe da kanka".
Yana gama faɗin haka yasa matansa da ƴaƴansa gaba sukai gida haka sauran ƴan uwan duka sukai gida suka bar kawu tasi'u da matarshi da ɗayar ƴar tasu suna faman koke koke a ƙofar gida.

" *kasan girman Allah bazan yarda ba kaje can wajan wanda ka kaiwa lefen jiya ka amso na haɗa da gonata ta gado mu sayar mu biyasu kuɗinsu mu ɗauko ƴarmmu* "
Cewar babar ladi wadda ta saka haɓar zaninta ta face hanci tare da hawayen takaici.

Cikin sauri kawu tasi'u ya saka hannu cikin aljihun wandonshi ya zaro

wayarshi lambar wannan mutumin na jiya ya kira wanda yazo jiya ya ɗauki kayan lefe akan ze kawo masa kuɗin amman tun jiya shuru kuma ya kira layin mutumin bai samu ba yaje shagonsa tun ajiyan yagani a rufe dan haka yanzuma seya kuma kira amsar dai ɗayace is swich off!! Wayar ya doka da ƙasa yana furta kalmar "innalillahi wa'inna'ilaihirraju'un"!!!...............
*Muje zuwa*.......................

*Sharaɗa*
Ai tawagar ƴan ɗaurin aure na tafiya maƙota sukace salamu alaikum gidan mama banda jaje babu abinda akewa mama wasu kuma nata mamakin tayaya duka wannan lamarin ya faru mama bata sanar da kowa ba, haka itama iya ta shigo tare da sadiya wadda tun jiya take kuka wai anyi bikin Bebi bata saniba haka iya ta zauna agidan mama har yamma suna mayar da magana mama kam babu abinda bakinta yake se kabbara da hamdala ranta fess sabida tanada labarin dukkan abinda ya faru *wannan shi ake kira da ƙaiƙayi koma kan masheƙiya* sunyi abun ya koma kansu dayake bata da laifi ƴaƴanta ma haka da *Sannu dukkansu zasu girbe abinda suka shuka* har dare iya tana gidan mama sabida yadda gidan yake faman karɓar baƙi ƴan jaje wasu kuma ƴan Allah sanya alkairin auren bebi.

*Yahya gusau mai atamfa esstate*

Tuni bebi ta kusan kammale farfesun dake gabanta hartana shirin zubo na kayan cikin ragon...........
# *Autar Manya*

*81*

Gefe guda kuma ta tsirawa tv idanu tana kallon labaran safiya wanda ake haskawa a tashar Cnn, tana kallonta tana aika farfesun dake gabanta cikin bakinta hankalinta kwance ita sam bata san wainar da ake soyawa a gidansu ba.
Tana kammale na gabanta ta jawo kular farfesun kayan cikin waɗanda su ta ɗibi marar yawa sauran ta tura bayanta tace anjima zata ci, cokali ta saka tacigaba da ɗiban romon da ɗan kayan cikin tana kaiwa cikin bakinta tana ci tana lumshe idanunta.
Cikin lokaci ƙalilan tagama cinyewa sannan ta miƙe ta gyara inda ta ɓata kana ta koma waje ɗaya ta zauna bayan ta kammale dukkan kulolin waje ɗaya.
Jin cikinta take kamar ze fashe banda ƙamshin kayan haɗin farfesun babu abinda hannunta keyi, can cikin zuciyarta kuwa mamakin tarin dukiya da wadatar wannan gida take jiba gida kamar baza,a mutu ba daman da irin waɗannan manyan gidajen a duniya? lallai inda ranka zakasha kallo ba ɗan kaɗanba, zamanta da kamar mintuna goma bayan kammala cin abincin nata ammi ta kuma dawowa falon.
Cikin nutsuwa ta dubi Bebi tare da ce mata.
"Autata har kin kammala cin abincin kenan?"

Tafaɗa mata cike da tattali.
Waya kunyace ta rufe bebi sabida ko kusa batai tunanin ammi na iya dawowa a wannan lokacin ba kuma ai da kunya aga ta cinye rabi daga cikin kayan karin da aka kawo mata.
Amman ga mamakinta setaga ita ammin ma sam hankalinta baya kan kulolin yana ga wajanta wadda take tambayarta.
"Eh ammi na kammala nagode Allah ya ƙara girma da ɗaukaka amin".
Cikin tsananin jin daɗin yadda yarinyar tayi mata addu'a ammi tace.
"Amin autata nagode to maza taso kije kiyi wanka kinsan babana akwai cida zuci kar yazo yaga bakiyi wanka ba yahau sababi".
Tafaɗa tare da tashi tsaye ta nufi hanyar bedroom ɗinta.
Cikin sanyin jiki Bebi tabi bayanta salo salo tana ƙarewa hanyar wajan kallo tana ƙiyasta yadda aka kar kuɗi  a wajan, kana tana mamakin ko ammi batada yara ne taji gidan tsitt.

Ƙafafunta ta ɗora akan wani lallausan carpet wanda ke maka wellcome a bakin bedroom ɗin ammi wanda ya sami damar isa har cikin bedroom ɗin tsananin laushinsa yasa Bebi shagala batare datayi yunƙurin ɗaga ƙafafunta ba.
Har ammi ta ƙarasa cikin room ɗin kafin Bebi tayi ta maza ta kuma saka ɗayan ƙafar ta cigaba da tafiya cike da tsananin mamaki wato su masu kuɗi komai nasu yana da matuƙar bam-banci danamu.
Acikin katafaren bedroom ɗin ammi Bebi ta yada zango wanda ko iya nan ammi ta karrama Bebi kuma tabbas ita kanta ta yarda da gaske Aliyu ɗan gatane na gasken gaske a wajan mahaifiyar tasa duba da yadda ammin take nan-nan da ita tare da tattali da lallashinta kamar ƙwai daga ƙarshema take kiranta da *Autar ta* a tsakiyar room ɗin ta dakata tana kare masa kallo babban ɗakine sosai wanda ya sami damar lamushe ƙaton royal bed mai uban girma tare da babbar wadrov duka masu kalar golden se ƙaton dressing mirrow tare da wata kujera doguwa daga gefe se sallaya tare da hijabi na sallah a nannaɗe daga can ƙuryar ɗakin se wata golden ɗin kofa wadda take a rufe daga hannun hagu.
A saman wannan sopa ɗin ammi ta zauna sannan ta kalli Bebi a tsanake.
"Buɗe wannan ƙofar ki shiga zakiga tawul a saman ƙofar ciki kar ki shiga ta farkon ki shiga ta biyu akwai ruwan wanka na haɗa miki sekiyi wanka in kingama ga kayanan a gefen gado ki saka".
Ta faɗa mata cikin bada umarni kana ta mike ta nufi wata ƙofar daban ba wadda suka shigoba wadda se lokacin Bebi ta lura da ashe kofofin ukune a cikin ɗakin kenan ba iya wannan bane kaɗai akwai wasu aciki lallai inta nutsu seta leƙa tagani.
Gaban madubin ta nufa tafara tube kayanta tana kallon kanta amadubin tana ɗan xaro idanu kaɗan kamar wata yarinya.
Tana gama tube kayan ta ɗauki hijabinta ta ɗaura a ƙugunta tare da ɗaure kanta da ɗan kwali kana ta nufi cikin kofar ta murɗa ta shige abinta.
Yadda ammin tace da ita hakan ta aiwatar wani farin tawul ta ɗaura wanda daga ganima sabone kuma babu laifi ya rufe mata cinyoyinta, tana shiga cikin bathroom ɗin ta tarar an haɗa mata ruwa a tap na wanka wanda tunda ta shiga taji mugun ƙamshin turaren wanka ya cika mata hancinta.
Cire tawul ɗin tayi tare da farayin wankan cikin tsananin jin daɗin ruwan duba da yadda yake bin

fatarta  yana wani irin sulɓi yana gudu, ga kuma sabulun wanka na ruwa wanda taita makashi a sumar kanta tana wankewa domin ita ta ɗauka shampo ne na wanke kai daman ƴar kalabace hassana tai mata wadda tuni ta tuje amman dayake Bebi batada wani gashin kirki yasa bata dameta ba.
Bebi wadda ko a gida bata haura mintuna biyar a bayi amman yau bebi kusan awarta guda tana cuɗe jikinta abinka da farar fata tuni fatar ta kuma haske takuma yin kyau gwanin sha'awa domin har ɗaukar idanu takeyi.
Tashi tayi tsaye bayan ta gama wankan ɗan kallon kirjinta tayi sosai suka bata tsoro sabida yadda sukai wani irin cukowa kamar da gayya sunyi wani irin kyau,Tura bakinta tayi gaba kamar agaban wani tare da ɗaura tawul ɗin kana tace.
"Ni wannan nonon kafa ishen kullum kaita cukowa kamar wata uwar garke".
Tafaɗi hakan tana goge kanta da hijabin data cire kana ta fito waje ɗauke da ƴan kayanta a hannu.
Abakin ƙofar ta dakata seda ta ɗaura ɗankwalin a saman jikinta ta kare kanta yadda ba mai ganin kirjinta sannan ta fita zuwa cikin ɗakin.
Kamar kwa tana da masaniya domin da ammi taci karo a zaune gabanta wani irin kaskone wanda aka haɗa masa gaushi yana ta faman ci se wata jarka dake gefenta.
"Yauwa autata kin kammala wankan to maza zona haɗaki kafin ya ƙaraso zoki tsugunna akan kaskon nan amman kafin nan zona fara baki zuma kisha wallahi ta nusaiba ce ma ta manceta Allah yayi rabonki ce zuma ce mai kyau sabida tana gyara kuma akwai sinadaren maganin sanyi acikinta".
Ita dai bebi bata fahimci abinda ammi take nufi ba sabida ƙarancin shekaru wadda ita kuma ammi ta faɗa mata hakanne domin yanzu ta shiga sahun manya bayan haka kuma ta ƙara gogewa wajan gyara jikinta.
Gaban ammi ta ƙarasa bayan ta aje hijabinta a gefen kayanta data cire lokacin dazata shiga wanka ɗazu.
Cikin sauri ammi ta saka hannu ta ɗauko pillow daga saman sopa ta aje mata a ƙasan ta zauna sannan ta miƙa mata jarkar.
"Amsa maza shanye".
Karɓa tayi tana bisimillah! tare da kaiwa cikin bakinta.
Jin wani irin ɗan bauri da garɗi da dabino da kwakwa da tarkacen kayayyakin zaƙi yasa Bebi iyayen ƙwaɗayi aka gyara zama har tana lumshe idanunta seda ta shanye tas duk yawan zumar kana ta mikawa ammi jarkar.
"Yawwa autata nagode to zo matso da jikinki kinajina ko ki ware ƙafafunki sosai yadda hayaƙin ze shiga jikinki maza amshi ki zuba ina zuwa".
Ta miƙa mata wani ɗan ƙullin turare ɗan mitsil, tare da turo mata gaushin gabanta wanda tuni cinyar Bebi ta ɗauki zafin azaba.
Amman tsabar ganin girman ammi wadda ta cika idanunta yasa ta ware kafar sosai sabida lokacin ammi ta miƙe tabar wajan.
Sosai ta buɗe cinyoyin ta saka kaskon a tsakiyarsu sannan ta kunce turaren dake cikin wani irin leda mai ƙyalli ta zuba ciki aikwa nan da nan ƙamshi na azaba ya cika hancinta.
Daɗa turawa tayi cikin cinyar tata hayaƙin na shiga jikinta har wani zufa ya haɗa sabida azaba, amman haka Bebi ke ƙara ƙaƙaba turaren wanda har fatar cinyarta ta soma ɗaukar zafi alamun

zata ƙone( kai bebi wauta zata saka Ali jinya)

Cikin sauri Aliyu ya haura samansa bayan ya shiga part ɗinshi lokacin wajan karfe takwass na safiya, falon sama babu kowa alamun matar gidan bata rigada ta tashi daga bacci ba, Bedroom ɗinshi ya buɗe ya shiga domin yay wanka...............
#Autar Manya.

*Afuwan* !
*Afuwan* !!
*Afuwan* !!!
*Wallahi bani da caji awayata nima banso na tsaya anan ba amman Allah ya kaimu next*

*82*

*wannan na gobe ne insha Allah sabida gobe bazan samu damar yi muku typing ba sabida haka ga shinan a taɓa babu yawa nagode*

Tuɓe kayanshi yayi cikin sauri ya ɗaura white towel a west ɗinshi ya faɗa cikin bathroom ɗinshi cikin mintuna ƙalilan ya haɗa ruwan zafi acikin tap wanda ya wadatu da kayan ƙamshi na wanka, yajima yana cuɗe jikinshi kafin ya kammala wankan ya naɗo kanshi cikin towel ya fito zuwa cikin room ɗinshi.
Seda ya goge jikinshi tsabb da ƙaramin towel sannan ya ƙarasa gaban dresing mirrow ya ɗauki lotion ya shafa sama-sama a saman fatarshi ya ɗauki turare mai daɗin ƙamshi ya fesa ajikinshi seda yayma kanshi ɓarin turare mai kwantar da hankali sannan ya taje gemunshi mai bawa mata tsoro.
Baya da yawan wannan ƙaƙale ƙaƙalen na maza daman shi tin fil azal bai daɗewa ashiri, dan haka cikin mintuna kaɗan ya gama kammala gyara kanshi kana ya koma gaban jerin kayanshi.
Wani black jeans ya ɗauka wanda yaɗan ɗameshi kamar trouxer ya haɗeshi da white shirt mai hannu iya gwiwar seda ya shirya cikinsu tare da ƙara gyara kanshi sosai kana ya kuma komawa gaban mirrow yayma kanshi ɓarin turare still, sannan ya kwashi wayoyinshi da car key yabar ɗakin tare da ƙamshin sa.
Wayyo zokuga Aliyu yadda yay wani irin kyau seya fito kamar ɗan saurayi mai kimanin shekaru 30 sabida kyan dayay sabida ƙananun kaya suna haska guy ɗin ba kaɗan ba saidai shi a tsarinshi yafi son manyan kaya.
Yana fitowa falo ya hangi giftawar madam dija tana kaiwa da komowa a tsakanin daining area da kuma kicin, taci gayunta cikin ƙananun kaya masi bin jiki su kwanta luff.

Ɗaga kanshi yay ya kalli agogon dake bangon ɗakin, ƙarfe tara da kusan rabi, zama yay saman one seater tare da ɗaukar remote yana sauya channel.
Har dija ta kammala setting daining sannan ta karaso wurinshi ta rissuna.
"Good morning my hony ".
Ɗan kallonta yay ta ƙasan idanunshi sannan yace.
"Morning dear"
kamar an mishi dole.
Wani sassanyan daɗi taji adukkan ilahirin sassan jikinta lumshe idanunta tayi kana ta waresu bisa kanshi sannan tace.
"Wow amman naji daɗin wannan suna cwt ga abincinka a daining kona kawosa nan?".
Tafaɗi tana wani yin fari da idanunta tana juyasu kamar da gayya.
Lumshe mayun idanunshi yay batare dayace mata komaiba sedai ya fesar da wata irin sassanyar iska ta cikin bakinshi.
Hannunta wanda yaji jan lallin bikinsu ta zube bisa saman cinyarshi kafin ta sami nasarar ɗora ɗayan cikin nashi tana matsawa sannu a hankali tana wani irin lumshe idanu kamar maijin bacci.
Sosai yaji shakkar hakan aranshi yana mamakin ƙarfin halin yarinyar.
"Dija mi kikeso dani ne nifa bana break da sassafiya haka kamar wani gara dan Allah kibarni na huta".
Yafaɗa yana zare hannunshi daga cikin nata.
Jada baya tayi kaɗan tana ƙwaɓe face ɗinta zata masa kuka!.
"Amman dai yaya kasan yadda nakeji dakai acikin zuciyata danme zakana katseni aduk sanda zan raɓeka why inda kace zan maka fyaɗe ai yanzu ina matsayin matarka ne kuma inada cikakkiyar lafiyar dazan buƙaci mijina".
Kalamanta su suka hargitsa masa lissafin dake kansa, tabbas baya son yazama daga cikin maza masu tauyewa iyalansu hakkinsu amman kuma shi gaskiya zafin dayaji rannan yake tsoro sabida shi Allah yayoshi cikin mutane masu gudun abinda ze taɓa lafiyarsu.
Amman ganin yadda taja baya tana kuka kamar wadda akama rasuwa yasa yaɗan sassautawa zuciyarsa ya saka hannunshi ya ɗaukota kamar wata ƴar beby dayake khadija batada wani girman kirki ya ɗorata a saman cinyarshi.
Tsira mata narkakkun idanunshi yayi masu tsananin dafin zafin so agareta yana kallonta yana noticing ɗin mood ɗinta.
"Dija ya kikeso nayi dake ya maganarmu ta jiya?".
Yafaɗa yana ɗora gemunshi adai dai gefen wuyanta yana son yaɗan rage mata zafi koda kaɗan ne.
Ƙoƙarin magana takeyi amman jin tsinin gashin gemunshi yahanata tayi maganar sema wani irin nishi dataja tana ƙara kwanciya a cinyar tasa.
"Ina magana kinmin shuru".
Yafaɗa mata yana shin shina mata cikin kurmin wuyanta da hancinsa baki ɗaya ya gama kashe mata jiki tun a iya nan kaɗai.
"Naiwa anty ruma magana tace ba damuwa zuwa next week in sha Allah".
Tafaɗa murya a shaƙe kamar zatai kuka sabida duniyar daɗin datakejin kanta cikinta.
"Okey kice next week zamu angwance"

Yafaɗa cikin son basar da abin domin koda wasa baya zaton a yadda take ɗinnan ze ƙara gigin kai jikinshi gareta gwara in Allah yasa ta samu gyara to komai ze koma dai dai ta yadda shi bai cutu ba itama kuma bata cutu ba.
Kwantar da kanta tayi cikin kirjinshi ita ɗaya keta faman cusa kanta cikin kirjin nashi amman shikam kallonshi ma yake batare dayaji wani feeling akan abinda take masan ba.
Cikin son dakatar da ita a fitinar datake son kunnowa kanta yace mata.
"Goma tayi tashi ki kawon black tea kaɗai".
Kamar karta mike haka takeji amman hakanma tagode cikin sauri ta mike ta nufi gaban daining inda shikuma yabi cilai cilai ɗin ƙafafunta da kallo yana ayyana sirantar ta kamar wadda batacin abinci acikinta.
Harta kawo masa yana nazarin tsarin ta wanda sam batada wani na jan hankali ajikinta inka cire iyayin tsiyan dake gareta.
Karɓa yay tare da furta.
"Thanks".
Kana ya ɗora agefen shi kan wani ɗan madai daicin table sabida akwai zafi cikin tea ɗin.
Ƙoƙarin sake hayewa saman cinyar tashi kum takeyi.
a nan kam haɗe rai yay tamau ta yadda batada space ɗin yin hakan kana ya mayar da kanshi ga tv, Itama anata ɓangaren ganin ya koma mata Aliyun shi sakk nada seta kama kanta ta zauna waje ɗaya tana kallon tv ɗin kamar yadda taga ya mayar da hankalinshi ga tv.
Ɗaukar cup ɗin yay tare da kaiwa bakinshi yanayin bisimillah.
Cikin tsanaki yake kurɓar shayin wanda yakejin daɗinsa domin ta ƙayatashi da kayan ƙamshi masu daɗi da ƙayatarwa kota nan yana jinjinawa dija domin koda girki kaɗai zata iya siye wanda take tare dashi.

Sun jima cikin shuru harya kammala da kansa ya tashi yakai cup ɗin kicin ya ɗauraye ya kife sannan ya dawo ya zauna ya kalleta.
"Nagode ni zan ɗan fita ƙilan na dawo yau ko zuwa dare ƙilan kuma nakai gobe sabida haka duk abinda kike ciki ki sanar dani a waya banson yawan surutu pls ki zamanki anan banson ko part ɗin ammi kije da sunan kiran ƴan kwana domin akwai securties agidan wadatattu  sannan kiyi  addu'a Allah ne mai tsare kowa".
Yana gama faɗin haka ya miƙe tare da xube hannayenshi acikin aljihunshi yana kokarin saka kai ya fita daga falon.
"Allah ya tsaremin kai aduk inda kake amin amman ina zakaje har kwana?".
Basar da tambayar yay sabida bai shirya gaya mata sabon aurenshi ba sabida yadda ammi ta tsara dan yasan yana gaya mata seta gayawa umman ta ita kuma umma ta gayawa su alhaji daganan kuma abba yaji, sannan kuma bayajin ze iya yi mata ƙarya domin ba halinshi bane.
"Amin".
Yafaɗa bai bata sauran amsar tambayar ba yasaka kanshi yabar falon se karar rufo kofarshi taji, Tattare wajan tayi sannan tai cikin ɗakinta tanajin kewarsa amman sanin yadda sana'arshi ta business take na yawan tafiye tafiye yasa taji ɗan dama aranta.

Kai tsaye part ɗin ammi ya nufa har lokacin babu alamun mutanen gidan sun tashi sallama yay a falon ya tarar da ammi zaune tana amsa masa.

Zama yay a gefenta.
"Ammi har yau ƴaƴanki basu tashi a bacci ba?".
Murmushi tayi kana tace.
"To babana ai yau basu da morning lecture kasan yau monday se wajan 1:00pm suke fita ita kuma amina ta kwana ciwon ciki itama bataje office ba wai zata huta shiyasa na barsu".
Sosa kanshi yay da keyn mota.
"Ammi da kamata yay su tashi suyi aikace aikacen gida wallahi mace setana miƙewa domin su ƙware karsuyi ƙazanta gidan mazajensu kinsan Allah yarinyar nan khadija na jinjina mata sabida tsaftarta hakannan naji ina ganin ƙimarta".
Murmushi ammi tayi tana kallonsa tana kuma gasgata maganarsa tabbas dukkan maganganunshi daya furta suna kan tubalin gaskiya mace duk yadda takai da girma da soyuwa a zuciyar mijinta wallahi in bata tsafta dole ze fara hangen wata daga karshe kuma yaji ta fitar mashi aransa idan kuwa baya sonta intana tsafta tana gyarawa tofa wataran za,a wayi gari aji tayi wuff da zuciyar mijin nata sabida babu wanda baison kyautatawa tare da kulawa wanda tsafta duk tana cikin waɗannan rikunonin.
"Babana ai tunda muka tashi da asubahi wallahi basu komaba seda suka haɗa break ɗinda amaryarka taci ɗazu sannan suka gyara part ɗin abbanku sannan suka koma bacci waɗannan masu aikin daka gani munzo dasu ɗazu girkin ma'aikata sukeyi banamu ba".
Se lokacin ya saki ranshi.
"Ammi harnaji daɗi dan banson naga ana kawo mana complain na ƙannenmu suna ƙazanta agidan mazajensu wallahi ammi banson mace ƙazama mai son jiki".
Yakai maganar har iya gaskiyarshi.
"To babana kai sa'ar khadija itama bilkisu ina maka albishiri da insha Allah tana da tsafta kuma zata maka biyayya kaidai fatana kazama jajurtaccen namiji wajan bawa iyalanka kulawa da adalci".
Murmusawa yayi yana shafa kansa da keyn motarshi.
"Amin ya Allah, ammi tana ina mu wuce kinsan fa se nama karɓi makullin key ɗinmu a wajan wani yarona acan ɗin".
Waigawa tai bata ga fitowar bebin ba.
"Jeka bedroom tana ciki tayi wanka ko tana jiranka ne".
Tashi yay tare da nufar bedroom ɗin cikin sauri.
Sabida yafison suyi sutafi kada lokaci ya ƙure.
Zaune take abakin gadon ammi ta ware ƙafafunta a dai dai saitin fanka kamar wadda akama kaciya tana faman haɗa zufa batare data saka komai ajikinta ba, baki ɗaya fuskarta ta gama jiƙewa da ruwan hawaye dana majinar kukan zafin wuta...............
# *Autar Manya*

Wata irin azaba takeji acikin dukkan cinyoyinta sabida wutar turaren data gama ratsa mata jiki,wanda hakan ne ya kuma bawa fatar wajan damar ƙara yin wani irin jajur kamar jini ze zuba ajikinta.
Gaba ɗaya fuskarta tagama jiƙewa da ruwan hawaye dana majina se faman tura baki take gaba, tana kuma gunjin kukan da sautinshi baya fita sosai, sabida azabar datake ji acikin jikinta,wannan shine ma dalilin daya sa ta zauna a gefen gadon ta ware ƙafafun nata tare da ɗan zame tawul ɗin jikin nata tana karɓar sanyin iskar fanka dana Ac'n dake ratsa mata jikinta ko ta sami salama da irin yadda takeji ɗin.
Cikin nutsuwa ya murɗa handle ɗin ƙofar room ɗin, tare dayin sallama ƙasa-ƙasa wadda ko ita dake cikin ɗakinma bataji sallamar tashiba sabida yadda yay amfani da ƙaramin sautin muryarshi wurin fitar da ita.
Daga bakin ƙofar ya tsaya tare da zube hannayenshi acikin aljihun jeans ɗin dake jikinshi tsananin ɓacin rai yaji acikin zuciyarshi.
Tayaya shi yana can yana sauri domin su wuce sabida baya son abba ya tashi ya tarar da shi acikin gidan amman dan tsabar rainin shine tawani zube anan ko shiryawa batayi ba.
Tsaki yaja kaɗan yana mai tako ƙafafunshi izuwa gareta, Yana zuba mata kaifafan idanunshi masu cike da haiba gami da kwarjini, Tsabb ya kare mata kallo acikin daƙiƙun da basu gaza biyar ba.sannan kuma yagama fahimtar halin datake ciki amman a irin miskilancin sa seya basar kawai yana mai tsayawa agabanta ya tsareta da idanunshi yana kallon fuskarta.
Wani irin faɗuwar gaba taji acikin kirjinta sakamakon tsayawarsa agabanta wanda har hakan yasa ta kasa ɗagowa gareshi kuma ta kasa motsi sema wani ruwan hawayen dake kara kaini bisa saman fuskar tata.
"Baki shirya ba?".
Taji saukar sassanyar muryarshi tana mata amo! acikin dodon kunnenta.
Daka ta amsa masa, ma'ana ta ɗaga masa kanta sama tana taɓe bakinta irin yadda yara ƙananu keyi in suna cikin rashin jin daɗin yanayi.
"Bana hanaki amsa min magana daka ba? kinason tun yanzu nasoma tsinin baki akanki ko?".
Yafaɗa cikin kwantar da murya sabida yaga take-taken yarinyar baya son ya fiye ɗaga murya akanta domin ya fahimci irin yaran nan ne masu mugun saka mutane yawan magana tare da basu ciwon kai.
"Ammi ce tabani turare nayi shine na ƙone anan sena zauna fanka tana huramin".
Yaji muryarta cikin rawa tana wassafo masa waɗannan bayanai kamar a cikin tsoron furucin.
"Ikon Allah to garin yaya kika ƙone ina wutar ba,a wannan abun naku na turare take ba?".
Yajefa mata tambayar cikin tuhuma
"Anan take man niba cemin tai na turara sosai ba".
Shi dariyama yarinyar ta bashi amman seya basar.
"Dayake ke shasha,shace yasa kika tura cikin ƙafafun naki ko?"
Mtssss! "Allah ya sawwaƙe ki maza ki shirya na baki five minutes ina falon ammi wallahi na kuma dawowa naganki haka sena bugeki".
Yafaɗa yana ƙoƙarin juyawa
"Nifa wallahi zafi suke man toba bani akai ba nikuma zance mata baniyi ne wallahi bazan iya

tashi bani".
Tafaɗa cikin sangartar data sabayi agidansu.
Juyowa yay tare da sakin baki yana kallon yadda take fici-fici da idanu tana murzasu kamar wata yarinya tsintar kansa yay da kureta da idanunshi yana kallonta seyaji yanayinta ya sakashi nishaɗi arayuwa  yana son mace wadda ta iya shagwaɓa sabida shi feeling ɗinsa yafi karkata ga nan ɗin bare ita wannan da salon yay masifar bi da ita ya karɓeta ba kaɗan ba domin zata iya sakawa ya lalace mata anan yana kallonta.
Ahankali da wani irin sanyin jiki ya komo gabanta ya tsugunna adai dai saitin yatsun ƙafafunta tare da ƙuresu da idanu yana kallon tsarinsu acike suke musamman ta wajan agerarta wanda yana da tabbacin tana daga cikin mata masu ni'ima tare da yawan buƙatuwa.
Itako ganinshi gurbane gabanta yakuma dagula mata lissafin dake cikin ƙwaƙwalwar kanta wani irin ƙullewa cikinta yay domin atunaninta ma dukanta zeyi shiyasa ta rintse idanunta gam-gam tana jiran taji saukar duka ajikinta.
Hannunshi guda ya ɗora akan ƙafar tata dai dai wajan ƙwaurinta batare dayay gigin ɗaga idanun nashi ba, sekuma can yaɗan ɗago kanshi tare da jefa idanun nashi asaman ƙwaurin nata yana son ganin ƙunar data ce tayi amman bai gani ba, wannan dalilin ne yakuma bashi damar kai ƙwayar idanunshi saman cinyarta wadda take jajur kamar ka taɓa jini ya fita.
Kusan a tare laushin cinyar da kuma azababban ƙamshin mayen turaren da ammi tace tayi suka bugi zuciyarsa hancinsa dakuma hannunshi daya ɗaga ya ɗora a saman lallausar cikakkar cinyar tata.
*AUREN BARE PART 2 NA KUƊINE IN KINA BUƘATA KI TUNTUƁI WAGGA NUMBER 08142105218*
Cikin furgici ta ɗago idanunta dake rintse ta zuba akan hannunshi dake saman cinyarta wanda yake cike dawani irin kwantaccen gashi wanda harya kusan xagaye yatsun hannun nashi se manyan zubban azurfa farare guda biyu, tare da wani irin agogon bakar fata dake ɗaure bisa tsintsiyar hannun nashi.
Mayar da idanunta tayi ta rintse tana jiran taji kome ze mata a wajan.
Cikin wani irin dagulallan lissafin dabe taɓa ƙirga irinshi ba yake yawo da hannunshi bisa saman cinyar tata tare da ware faffaɗan tafin hannunshi adai dai saitin dayaga shatin jan tabon wutar.
Cikin wata irin cakuɗaɗɗiyar murya wadda tagama cika da zallar shauƙi ya furta mata.
"Rufe idanunki sosai zanyi maki addu'a a wajan Plsss".
Yafaɗa a rarrabe yana jan ajiyar zuciya mai zafi.
Cikin tsananin tsoro ta kuma rufe idanun nata gam tana sauraran addu'ar tasa gareta.
Bakinshi ya ɗora a tsakiyar cinyar tata tare da saka hannunshi guda yaɗanja tawul ɗin wanda yakuma basa damar ganin manyan cinyoyin nata waɗanda suke free babu komai jikinsu.
Jikinshine ya ɗauki wani irin zafi kamar gaushin wuta tare da wata irin tsuma kamar maijin zazzaɓi, kwantar da kansa yay duka a saman cinyar tata yana mayar da numfashi jin mararshi tayi wani irin ɗaurewa gam kamar zata rabe biyu, wanda tsananin zafin da jikinshi yaɗauka ne yaha naashi aiwatar da abinda ke zuciyarsa illah kwantar da kansa kurum dayay a saman cinyarta yana murza kansa a cinyar kamar yaro ƙarami.
Furzar mata da wata irin zazzafar iskar bakinshi yake wadda ita kanta tanajin hucin zafin fitar iskar bakin nashi sedai tsananin tsoro yahanata ta ɗago bare ta buɗe idanunta taga halin dayake ciki..................

*ƊAN MAJALISSA*
*RABON WANI*
*H A S K E*
*DA IZZATA*
*KOBA  SO*

_Kai dagajin sunan kasan seda aka zauna aka baje basira wajan tsarasu kedai/kadai hanzarta ka sayi dukkan waɗannan daɗaɗan littattafan cikin farashi mai sauƙi wanda a yanzu suka haɗe complt document, idan ɗaya kikeso naira 300 idan kuma dukkan biyar ɗin kike so naira 1000, kedai hanzarta neman wannan numbern domin kibiya ki samesu a ɓagas 08142105218_

*84*

Azabar tsoronshi ne yake ratsa ilahirin dukkan sassan jikinta wanda shiya hana ta  ɗagowa bare ta duba shi sema wani irin rawar jiki data kuma tsintar kanta acikinshi, ruwan hawaye kamar famfo shike ƙara gudu a saman fuskarta, Sosai zafin numfashin sa yake ratsa ilahirin fatar jikinta,Wata irin nutsuwa yakeji acikin jikinshi ayayin dayake kuma mannewa da jikinta kamar mayen ƙarfe sabida ta hakane kaɗai ze samu salama a irin yanayin dayake ciki wanda ko kaɗan bai son ya fiye zaƙewa sabida gudun abin kunya kada ammi tazo ta tararsu a haka.
Acikin zuciyarta take mamakin wannan addu'a tasa mai tsayice lallai ta ƙone dayawa tunda taga har yanzu bai ɗagoba, gakuma tsoron faɗanshi ya hanata ta ɗago bare ta buɗe idanun nata taga halin dayake ciki.
Gaba ɗaya tattarota yayi ya zubeta acikin jikinshi hannunshi na rawa ya riƙo west ɗinta irin riƙon tsaurin nan sosai kamar ze ɓalle matashi.
Rintse idanunta take tana cije bakinta sabida tsananin zafin azabar da ƙugun nata ke mata gakuma tsoronshi baze barta tai ihu ba, wani irin sassanyan ƙamshin turarenshi ke faman kai komo acikin hancinta wanda bada ban zafin da ƙugun nata ke mata ba, da zata iya cewa bata taɓajin daɗin turare kamar wannan nashi ɗinba.
Rungumeta yayi acikin jikinshi inda shikuma ya zube daɓas ya zauna yana mai ƙara riƙeta sosai ajikinshi yanajin ta hakanne kaɗai ze sami sukuni acikin gangar jikinshi sabida yadda sirrinshi ke faman dokawa kamar zata ɓalle ta fita daga jikinshi a iya tasowarshi tunda ya mallaki hankalin kanshi bai taɓa jin yanayin sa yay mugun taduwa kamar wannan ba.
Tarairayota yay zuwa jikinshi sosai tare da kwantar da kanta a saman cinyarshi inda ya baiwa tawul din dake jikinta damar ƙarasa fita baki ɗaya cikin wani irin yanayi ya birkita ta ya janyo cinyarta mai ƙunar ya ɗora bakinshi adai dai saitin dayaga turuwar jan, yana mai hura mata sassanyar iskar cikin bakinsa kaɗan kaɗan, yana ɗan shafo wajan da ɗayan hannunshi ahankali

ahankali, tsabar kaɗuwa da wannan baƙon lamarin ya sanya Bebi ƙara gudun kukanta tanajin tsananin fargaba acikin zuciyarta wannan dalilin yasa hannunta yana rawa ta janyo tawul ɗinta ta rufe jikinta har zuwa wajan kansa inda ya ɗora bakin nashi akai.
Cikin wata irin kasalalliyar murya wadda tagama nisa cikin shauki ya furta.
"Kiyi haƙuri na kusan ƙarashe miki pls ɗan ƙara buɗan wajan".
Batare dayasan hakan ya fitaba yake kuma tallafar ƙafarta yana kuma cusa kansa a wajan ƙunar yana mamula yana hurawa kamar ze cinye mata cinya.
"Dan Allah ka bari hakannan nadaina jin zafin dan Allah kabarni haka".
Tafaɗa tana kukan da sautinshi ya fito fili.
Ɗagota yay gaba ɗaya ya ɗora a kirjinshi tare da ɗora lip' ɗinshi adaidai saman goshinta ya summaba ya kuma gangarowa dai dai saman tsinin hancinta ya summaba ya kuma gangarowa dashi tsakiyar lip's ɗinta yaɗan tsotsa kaɗan kafin ya zura harshen nasa gaba ɗaya cikin labban nata ya haɗe dana tan ya gamesu waje ɗaya ya soma tsotsa kamar ya sami alewa mai tsananin daɗi.
Hannunshi ya ɗora atsakiyar gadon bayanta wanda yake wayam ba riga yana shafa dai dai kurmin wajan har zuwa ƙarshen gadon bayanta. cikin mayata da kwaɗayi, baki ɗaya yagama shagala da abinda yake matan tunda yake baitaɓa haɗa baki da ɗiya mace ba, ko dija ranar farkonsu bai gigin kissing ɗinta ba, shiyasa yau dayaji shi a irin wannan yanayi se notikan dake kansa suke kokarin suncewa, bare kuma mai gayya mai aiki hajiya Bebi wadda gaba ɗaya takejinta a wani irin yanayi numfashinta yana up and down kamar ze fice ajikinta idan banda tsananin rawa babu abinda jikinta ke mata, yajima yana juya harshensa cikin nata bakin kafin yaji yes ya ɗan sami nutsuwa kaɗan.
Turata yay tayi baya inda ya sami damar ɗora kanshi a tsakiyar kirjinta yana sakin ajiyar zuciya kamar ƙaramin yaro, yanajin yadda zuciyarta take dokawa tana bugawa kamar zata faso, jinshi cikin wani yanayi mai daɗin gaske, baiƙi ya zauna tsayin rayuwarshi ahakan ba domin hakan ze ƙara masa farin ciki ɗan gaske.
Tsahon mintuna goma suna manne da junansu kafin daga baya ya zareta daga jikinshi ya ɗago jajayen idanunshi  waɗanda sukai kamar gaushin wuta ya zuba matasu yana kallon yadda tai ƙasa da kanta taƙi ɗagowa sam, tana faman haɗe hannayenta waje ɗaya kamar mai neman gafara, tsirawa kirjinta idanu yay yana kallonsu waɗanda suke a bayyane cikin idanunshi, har wani luuuuu yakeji a gaɓoɓinshi sabida tsabar kaɗuwar dayay da halittar tata tabbas babu makusa a wajan.
Ƙara kai kanshi yay wajan ya mannawa guda kiss cikin sauri ya miƙe jikinshi na rawa yabar ɗakin batare daya shirya hakan ba.

Baya tayi ta kwanta a gefen carpet ɗin ɗakin tana mayar da azababbiyar ajiyar zuciya mai tsananin ƙarfi hawayen idanunta ne yaƙara gudu, tunda take bata taɓa jin yanayi kamar wannanba, bata taɓa jin abu makamancin wanda yay mata a yanzun ba, tome hakan yake nufi? zafin da ƙwaƙwalwarta tayi yahanata lissafa yanayin datake jiki.
Face tsintar kanta datayi cikin wata irin nutsuwa tare da sanyin jiki, a matuƙar wahale ta miƙe gaban madubin ɗakin taje ta tsaya ta yagi tissue'n data gani a gefen madubin kusa da kayan kwalliya, ta goge hawayen daya ɓata mata fuskarta, sannan ta ɗauki mai ta shafa gaban gadon ta koma tare da ɗaga kayan da ammin tace ta aje mata, doguwar rigar after dress ce sedai ita

gabanta a rufe ike sannan kuma tana da kauri jikinta tamkar karen muski, jace mai adon duwatsu masu ruwan gwal, agabansu, se mayafinta madai-daici shima ja, se kayan undies waɗanda suke acikin ledarsu daga gani sabbine.
Sakasu tai ajikinta kamar angwada da ita, cif da cif kayan sukai mata warware doguwar rigar tai ta saka acikin jikinta.
Gaban madubi ta ƙarasa tare da mayafin a hannunta.
"Masha Allah tabarakallah amman nayi kyau".
Tafaɗa tana kallon kanta wato rigar tai mata mugun kyau ba ɗan kaɗan ba, daga sama tai wani irin tattara ta kame kirjin nata tai ɗam, daga ƙasa kuma taɗan saki tawajan cikinta sedai daga baya ta kame hips ɗinta tai ɗam-ɗam domin hatta shatin pant ɗinta seda ya bayyana.
Mayafin ta ɗauka ta yafa a saman kanta tare da ɗaukar turare ta fesa amman ɗan kaɗan.
Kana taja kafafunta ta nufi kofar fita hannunta ɗaya yana kan cikinta sabida tun ɗazu da tasha wannan zumar takejin cikinta yana ɗan kartawa kaɗan kaɗan kamar ciwon mara nason kamata, sekuma jikinta datake jin abu naɗan zubo mata kaɗan daga ciki.
Kama handle ɗin kofar tayi ta buɗe ta fita zuwa falon.
Yana daga xaune daga kujerar datai saitin Tv ammi kuma tana daga wadda take kallon kofar ɗakin data fito ɗin.
Ya zubawa Tv idanu amman a cikin zuciyarsa ba Tv ɗin bace wani tunanin yake daban, musamman a ɗazun daya fito a matuƙar wahale sabida yadda sirrinshi ke ƙoƙarin tona asirinshi inda Allah ma ya rufa masa asiri ammi bata falon lokacin tana can wai kicin tana haɗawa abba break, wannan damar ta kaɗaicin daya samu ita ta ƙara bashi damar  zubewa gaban ɗan frij ɗin dake falon hannunshi na rawa ya buɗesa ya ɗauki gorar faro mai sanyi ya kafa a bakinshi yana sha yana ɗan danna ƙasan mararshi da tafin hannunshi har yaɗan sami nutsuwa sannan ya dai daita kansa ya koma saman kujera ya zauna to ahakan ammi tazo ta sameshi koda ta tambayeshi ina Bilkisun seya ɗan shafa kansa kaɗan irin na halin ko in kula ɗinnan sannan yace.
"Inaga kotana ƙarasa shirin ne"
Yafaɗi hakan batare da sakin fuska ba domin bai son ta gano halin dayake ciki shiyasa ya rufe idanunshi kamar mai bacci tare da fuskantar Tv, wanda a hakan Bebi ta shigo falon ta samesu.
"Kai masha Allahu autata kinyi kyau masha Allah kamar a sureki a gudu a,a wallahi na ɗauka kayan nan bazasu maki ba sabida ana hussaina na ɗaukar maki ashe dai autar tawa tana da girma kai masha Allah".
Tacan ƙasan idanunshi yake ɗan satar kallonta kaɗan aranshi yana ayyana ai ammi ma ke a iya riga kikaga girman nata, amman a fili seyay kamar bai san ta fito daga ɗakin ba.
Raɓewa tayi daga gefen kujera tana sunƙe kanta a ƙasa tana wasa da yatsun hannunta
"Maza zona miki hoto autata kinyi kyau zan turawa su nusaiba su ga matar Baba Ali kafin suzo zo"
Ammi ta faɗa tana fito dawata azababbiyar waya mai shegen kyau wadda kyanta ya bayyana tsadar kuɗinta ƙarara.
Takowa take zuwa gaban Ammi wadda duk taku ɗaya se kirjinta da hips ɗinta sun kaɗa kamar da gayya, Yana ankare da hakan tsaf, kuma duk takun dazatai ɗin yana dai dai da takun sautin bugun zuciyarsa ne, cikin jarumta ya miƙe batare daya saki fuskarshi ba.
Gabanta yaje ya tsaya wanda yay mata shamaki da isa gaban ammi

"Ke jeki ɗauko hijabinki wanda kika cire wani wawan ne ze fita dake da wannan shigar".
Yafaɗa tare dayin kicin-kicin da fuska wadda tasa cikin sauri Bebi ta juya hartana haɗawa da tuntuɓe tayi ɗakin ammin.
Lashe gefen bakinshi yay kamar wani maye tare da bin bayanta da wani munafukin kallon ƙulla yana mai tura hannayenshi cikin aljihun wandonshi ya fito da waya yana dubawa a basance gudun kada ammi ta gano halin daya faɗa.
Harta fito bai bar wajan ba yana kallon yadda ta sinƙe cikin hijabin ɗazun wanda hakan yaji yafiye masa sau dubu.
Juyowa yay gaban ammi yaɗan rissuna gabanta.
"Ammi zamu wuce in abba ya fito kice masa na tafi TOKARAWA".
Bebi ma tsugunnawa tayi gaban ammi kamar yadda yay tana mai sada kanta a ƙasa.
"Allah yay muku albarka Allah yasa albarka a zamanku Allah ya tsareku yabaku ikon faranta ma juna, inka samu shigowa zan baka kaya ka tafi mata dasu tunda kaga bamuyi lefe ba, kafin muga zuwa lokacin bikin amina sena haɗa da kayan lefenta a ordern nusaiba".
Tafaɗa tana janyo wata ƴar jaka a gefenta rafar kuɗine ƴan dubu dubu kimani guda uku.
Ta miƙawa Bebi cikin hannunta.
"Niga tawa ƴar gudun mawar babu yawa ki sayi koda katin wayane".
Hannun Bebi yayi kaɗan da riƙe irin waɗannan manyan kuɗaɗan dan haka se hannun ya soma rawa.
Cikin azama ya kwashe kuɗin a hannunshi tare da kallon ammi
"Nagode ammi Allah ya ƙara buɗi"
yafaɗa yana mai tashi tare da kuɗin a hannunshi.
Itama Bebin godiya taiwa ammi kana ta miƙe harya fita daga falon da sauri tabi bayansa tana juyawa tana kallon ammi mace mai dattako tare da sanin darajar ɗan adam kenan.
Har ta fita zuwa harabar gidan tare da nufar inda taga ya miƙa..........................

*ƊAN MAJALISSA*
*H A S K E*
*RABON WANI*
KOBA SO*
*DA IZZATA*

_Kowannensu akan farashin 300 waɗanda suke documents complt, gabaki ɗayansu kuma naira 1000, maiso seya nemi,08142105218, haka nan mai son wannan littafin shima dai seya nemi wannan numbern ta sama domin ya saya_

*Assalamu Alaikum ina miƙo saƙon ban haƙuri zuwa ga ɗunbin masoyana masu bibiyar wannan littafin na yadda kuka jini kwana biyu shuru abinne ya haɗemin mun ɗan shiga hidima ne amman yanzu alhamdulillahi na kammala komai sabida haka zamu ɗora daga inda muka tsaya waɗanda suka kirani domin suji lafiya da waɗanda sukai min magana ta watsapp inbox duka nagani kuma nagode da yadda kukai min uziri Allah ya saka muku da ɗunbin alkairinsa amin summa amin nagode*

Gaba ɗaya hannayenta suna naɗe acikin hijabin daya umarceta ta saka tun a cikin falon Ammi.
Tana tafiyane cikin mutuwar jiki kamar wadda ƙwai ya fashe mata acikin jikin nata, ba kuma wani abunne ya saka mata wannan yanayin ba face wannan zumar da ammi ta bata ɗazu ta sha wanda tun a ɗakin takejin baƙon yanayi acikin jikin nata amman bai tasiri kamar na yanzu ba.
Gefe ɗaya kuma tsananin mamakin girman gidan tare da haɗuwarshi sun kuma kamata ashe jiya bataga komai ba domin a dare suka shigo ko ina ma'aikatane cikin blue ɗin uniform sunata faman kaiwa da komowa domin ganin sun tsaftace gidan daga yawan dattin bushashshun ganyen bishiyun dasuke faɗowa gefe ɗaya kuma ga masu faman baiwa fulawowi ruwa ga masu wankin motoci daga can tsakiyar wasu rumfuna, har harɗewa take sabida fargaba, ahaka ta ƙarasa tsakiyar farfajiyar gidan sama ko ƙasa bata ganshi ba, waige take tana raba idanu acikin jerin manyan tsala tsalan motocin dake harabar wajan amman sam bata ganshi ba.
Aranta take ta mamakin yanayin saurin sa domin ace daga wannan ƴar tafiyar harta nemesa ta rasa sekace ƙiftawar idanu.
Tsayawa tayi kamar wata doluwa tana ta zare idanu tunani take kamar ta juya ta koma wajan Ammi amman tuna yawan faɗanshi gareta yasa ta tsaya tana jiran tsammanin ganin shi.
Wata azababbiyar farar mota wadda taci baƙin glass ce ke faman doko mata horn wadda take daga can opposite da gaban gate, Cikin sassarfa Bebi ta waiga tana kallon motar jikinta na tsananin rawa take taku har zuwa gaban motar wanda taga murfin gefen da drivern motar ke ciki a buɗe ɗan zira kanta cikin motar tayi cikin sauri kuma ta ɗago sabida haɗuwar datayi da kaifafan idanunshi waɗanda suke tsaye suna kallonta, jan murfin motar tayi ta shiga ciki ta zauna sanyi Ac gami da ƙamshin turarensa dana motar sukaima hancinta sallama.
Tsintar kanta tayi da jingina da seat ɗin kujerar cikin motar tare da lumshe idanunta tana jan ajiyar zuciya sabida mutuwar da jikinta ya kumayi.
"Malama ki rufo mana motar mu wuce kin wani tsaya kinata kalle-kalle kamar wata sokuwa tun ɗazu ina jiranki"
Yafaɗa cikin ɗan zafin rai kaɗan, ko cikanka bata ce masa ba, sabida tafiya duniyar tunanin datayi, wanda hankalinta ma baya garesa.
Tsakinsa ne yajawo hankalinta gurinsa tsintar idanunshi tayi yana maka mata ƙatuwar harara kafin ya haye kanta a sukwane yajanyo murfin motar da ƙarfi kamar ze ciresa har yana haɗewa da hijabinta.
"Dan tsabar iskanci ina miki magana kinmin banza sabida kin mayar dani sa'anki to wallahi karkiga nasha miki baki ɗazu kiga damar rainani ina gaya miki wahala zakisha".
Ta tsinci muryarshi acikin kunnenta.

Mamakin yawan faɗanshi take ji acikin zuciyarta maye na wannan masifar dan kawai bataji abinda yace ba.
Shuru tayi masa aguje yaja motar kamar ze tashi sama, sabida takaicin wawan data mayar dashi lallai yazama dole ya taka mata burki domin shi ba sauna bane ba.
Wani mahaukacin horn ya danna a gaban gate ɗin wanda seda ya cika ilahirin gidan da gudu masu tsaron gate ɗin suka antayo suka wangale masa shi suna ɗaga masa hannun dabai da niyyar mayar musu.
Aguje ya saka kan motar ya nufi waje yana faman sake ɗaure ranshi tamau kamar wani kumurcin zaki.
Tsorone fall a zuciyar Bebi addu'a take Allah yasa kada ya zubar dasu ya cuceta abanza yabar mamanta da jinya gefe ɗaya kuma tsoronshi ne  fall acikin ranta na yadda taga kamar ma harararta ikeyi.
Tsitt ko ina acikin unguwar yake babu sautin komai bare ka saka ran zakaji maganar ɗan adam, saɓanin unguwarsu da tun asubahi ma zakaji mutane nata kaiwa da komowarsu amman ita wannan unguwar dayake ta masu hannu da shunice jiba bakajin komai acikinta.
Tafiya mai ɗan tsayi yayi kafin yahau babban titi alokacinne kuma ya saka hannu ya kunna redion cikin motar yana sauraran labaran safiya.
Ƙasa tayi da kanta tana sauraran redion itama bakuma tayi gigin ɗagowa ba.
Tafiya suke kamar ta kurame sabida yadda kowa yay shuru gwarama shi tanajin sa'i da lokaci yana ɗaga waya wadda kuma bata gane komai a maganganun nashi sabida yadda muryarshi tai ƙasa sannan kuma yawancin ma da yaren harshen turanci yake maganar tashi.
Cikin haka bacci ya kwasheta wanda batayi tsammaninshi ba.
A tsakiyar cinyoyinta ta cusa kanta tanayin baccinta cike da fargaba.
Shiko baima bi takanta ba, kawai tuƙinshi yake ya matsu ya ƙarasa da ita ya kuma juyowa ya komo gida sabida baya son abba ya tashi basu haɗuba domin wajan gobe yaji abban na maganar ze koma legos, gakuma maganar dazasuyi ta fitarshi waje wadda yasan in abban ya riga ya koma tofa da wuya ya dawo yanzu dole ze ɗan jima acan legos ɗin.
Wannan dalilin yasa yake sauri yaje ya kaita ya koma gida inyaso in sunyi maganarsu da abban still ya kuma dawowa nan ɗin domin yaga mai ze saya mata na abubuwan buƙatar gida.
Tafiyar kusan awa guda  damma da go slow a hanya ita takaisu cikin unguwar tokarawa can wajan ƴan kaba.
Wadda take shaƙe da manya manya kamfanin nika gefe guda kuma akwai yawan manyan motocin ɗibar kayan kamfani acikin unguwar wadda yawancinta ƙabilu sunfi zama acikinta sekuma masu abincin saidawa sabida yawan masana'antun  dake unguwar.
Titin cikin unguwar ya shiga tare da miƙa cikinsa sosai yake tafiya hannunshi ɗaya na riƙe da sitiyarin motar ɗayan kuma yana duba wayarshi cikin lokaci kaɗan ya soma magana.
"Hellow goma yaya akai? nacefa gani nan cikin unguwar ina zan ganka na karɓi keyn part ɗin?".
Cikin sauri tare da ladabi  yusuf goma wanda ya kasance yaron Aliyu ne tunba yanzuba kuma shiya wakilta anan domin ya kula masa da sabon kamfanin nasa na nan ɗin domin goma yana da amana.
yace.
"Oga ai inama gida sekun ƙaraso kawai Allah ya kawoku lafiya".
Katse wayar Aliyu yay tare da maida hankalinshi ga tuƙinshi.

Dayake goman shima yana cikin nan gidan da Bebi zata tare ɗin shida matarshi da yaranshi, kuma bama shi kaɗai ba akwai mutane wajan biyar agidan waɗanda kuma duk yaranshi ne da suke lura da gyare gyaren kamfanin nashi na nan ɗin waɗanda ya zaɓa ya kuma bawa kowanne acikinsu part guda shida iyalinshi sabida gidan kamar irin gidane na haya haka tsarinshi yake ƙaton gate ne se ƙofa ƙofa wadda kana shiga kowacce akwai tsakar gida da toilet tare da ciki da falo se kicin haka kowanne part yake agidan waɗanda biyar daga ciki akwai mutane ragowar ukune babu kowa cikinsu yanzu kuma Bebi zata zauna a ɗaya ragowar na kusa da ita guda biyune su kuma babu kowa cikinsu.
Gaban farin gate ɗin gidan ya tsaya wanda ƙarar sautin horn ɗinshi ne ya tashi Bebi ta ɗaga jan idanunta daya cika da bacci tana faman kalle-kalle unguwar kamar sabuwar anguwa domin babu wasu gidajen kirki a wajan daya tsaya ɗin.
Kashe motar yayi tare da buɗe murfin ya fita waje, wanda itama cikin sauri ta bude nata tare da fita wajan itama tana kuma kallon unguwar kamar za,a sace mutum.
Gaban wannan farin gate taga ya nufa batare daya kulata ba, itama bin bayanshi tayi cikin sauri harda ɗan gudunta.
Buɗewa yayi ya shiga ciki wanda harabar gidan take ba komai se ƴan ciyayi da tafasa,wayarshi ya ɗaya tare da kira.
"Goma ina waje".
Yafaɗa tare da kashe wayar.
Ba'a jimaba wani magidancin mutum wanda ze kusan sa'a dashi ya fito daga wani ɗan lungu hannunshi ɗauke da makullaye masu yawa.
Cikin sauri ya karaso gabanshi suka gaisa sannan ya bashi.
"Oga ga wannan amman sedai abuɗe wancan na farko ɗin sabida wannan na gabanmu kwanaki ankashe maciji acikinsa baya da kyau gaskiya".
Yafaɗa yana nuna ɗayan ƙofar ta farko wadda kusan a tare da nunin hannunshi nashi suka tafi da yadda cikin Bebi ya bada sautin ƙuwwwww. na tsoron bala'i daya kamata...................

*BARKA! BARKA!! DA RANAR TAKUTAHA TA ANNABI S.A.W INA YIWA ƳAN UWANA MUSULMI BAKI ƊAYA MURNAR ZAGAYOWAR WANNAN RANA ALLAH YA ƘARAWA ANNABI DARAJA AMIN BARKA BARKA BARKA ƳAN UWANA MUSULMI* 😍😍💃

*86*

Nan da nan idanunta suka cika da mugun tsoro sedai kuma babu damar tayi magana sabida

dodon nata yana wajan amman a  zahiri inda dafa hali daseta turje taƙi shiga cikin gidan sabida furucin dataji wanda ya kira da goma yayi yanzun.
Ɗan jimm yay kaɗan yana kuma nazarin gidan sosai yake mamakin yadda ze iya kwanan cikinsa idan hakan ta kama, lallai rayuwa babu tabbas duba wai shine ze zaman gidan nan wanda bai kai part ɗinsa na gida girma ba, shi seyau ma yake kuma ƙarewa gidan kallo sabida tunda ya ginasa baifi sau ɗaya yazoba shima kuma lokacin yana hidimar ginin kamfanin shine shine ya biyo yaga gidan sabida ya riga da ya gama bawa masu kwangilar ginin gidan komai.
To sekuma yau da wannan ƙaddarar Auren ta kawoshi yay zaman wucin gadi kafin suga kuma mai Allah ze musu nan gaba.
"Amman goma tayaya macizai suke shigowa nan ɗin hakan ai kamar da akwai matsala?".
Sosa kai goma yay kana yace.
"Wallahi oga duk haka aketa fama kasan in akace maka waje da ƙarancin mutane baya ga nan kuma waɗannan ciyayin na nan suke kawo su".
Yafaɗa cikin ladabi da biyayya.
"Okey yanzu dai kanemo masu cire ciyayi sannan ai feshin maganin sauro sekuma a samo mutane dazasu zauna a waɗannan ragowar biyun kaga kunyi ciki da ita kuma yarinya ce kaganta zataji tsoron zama ita kaɗai anan side ɗin, inda hali ma asa ma mata mai tayata hira".
Yakai maganar yana kallon Bebi wadda tai ƙasa da kanta tana nanata.
"Kuma yarinya ce kaganta"!
Acikin ranta tana mamakinsa wani zubin idan yay magana kamar da biyu.
Dariya goma yay kana yace.
"Babu matsala oga ai tunda madam ɗinka ce babu komai akwai yarinyata ta farko sunanta mufida zata dinga zuwa suna hira shekararta sha huɗu ai ta isa base an kirawo kowa ba,sannan ta ɗan dinga shiga suna hira da matar gidan nawa".
Murmushi yayi kaɗan tare daɗan sosa  kanshi da keyn mota.
"No ita ɗiyan taka dai ta shigo amman bani son yawan fice fice tai zamanta a wajanta nagode".
Yafaɗa babu kunya bare kara.
"Okey to shikenan babu matsala oga ai kawuce komai wajanmu alkairin dakake mana.......".
"Is ok goma muje ko? dafatan an ɗan gyara nan ɗin?".
Ya dakatar da goma akan maganar dayake son yayi kana yaja ƙafafunshi suka nufi gaban ƙofar part ɗin wadda take ta zallar baƙin ƙarfe.
Da azama goman ya saka keyn ya buɗe ƙofar goman shiya soma shiga kafin Aliyu yabi masa baya se Bebi wadda take sauri kamar wani abun ze kamata sabida itafa tunda taji an ambaci maciji shikenan fa sinadarin tsoronta ya ƙaru fiye dana da.
Sallama goma yay a ɗan ƙaramin tsakar gida, tare da tsayawa yana yiwa Aliyu magana.
"Oga ga wannan"
Ya miƙa masa wani extra key daban sannan yace.
"Wannan key ɗin room&parloun, ne amman kasan babu wadatattun ɗakuna ina ganin ɗaki ɗayane se falo ga toilet kuma anan tsakar gida se kicin, kasan tsarin gidajen arean nan se ahankali".
Karɓar keyn yay tare da cewa.
"Nifa goma nayi mamakin tsarin ginin gaskiya yayi ƙunci ahaka Allah ya kyauta".
Dariya goma yay.

"Ai oga shiyasa lokacin da ake ginin naso kana zuwa sabida kozaka sauya fasali rashin zuwanka yasa sukai maka ginin gidajen haya se haƙuri fa duk haka muke fama musamman kai oga daka saba rayuwar sakewa nan ɗin ze maka zafi".
Dariya yayi a wannan karon wadda ta saka Bebi ta saki baki tana kallonshi ashe haka dariya take mugun yi mashi kyau, sannan yace.
"Toya za,ai Goma damafa in baka mutu ba ai baka gama ganin rayuwa ba hakanma ai mungode Allah".
"Hakane oga yanzu bara na koma sabida na samo masu aikin ciyayin akwai ruwa a toilet cikin famfo ga kuma na tsakar gida, sedai wataran idan ya ƙare se an fita ɗiba, sannan duka nasa an gyara cikin room ɗin nepa kuma babu matsala muna samu sosai".
Goma yakai maganar yana ɗan sada kanshi a ƙasa.
"Okey nagode goma am pls nace zan maka transper yanzu dan Allah kaje store kai mata ɗan shopping ka haɗo da ƙaramin gas komai dai na buƙata sabida ni zan koma can gidane abba yana jirana".
"Angama oga babu matsala ni zan juya Allah ya tsare mana kai".
Murmushi yayi tare da ce masa.
"Nagode se anjima".
Harya juya sekuma ya juyo ya kalli Bebi.
"Madam se anjima"
Cikin siririyar muryarta mai kama data yara tace masa.
"Nagode amman ka turomin mufidan".
Faɗaɗa far'arshi yayi tare da cewa
"Angama madam insha Allahu".
Kana ya juya ya fita cikin nutsuwarsa wadda Aliyu yake dubawa akullum shine ma yasa ya aminta dashi sabida goma irin mutanan nan ne masu gudun duniya yana da matuƙar kirki sosai kuma shima ɗan ɗambattane domin ga gidan mahaifinshi ga gidan marigayi Alhaji Ali kakansu Aliyu kenan.
Gaban ƙofar yaje ya zira keyn ya buɗe ta sannan ya tako gabanta.
"Kishiga ciki bara naje mota na ɗauko miki jakar kayanki".
Ya faɗa mata idanunshi na yawo a saman fuskarta.
Sunkuyar da kanta tayi ƙasa tana wasa da yatsun hannunta batare datace masa komai ba.
Juyawa yayi ya fita daga gidan tana jin sautin tura ƙofarshi aikwa a 360 tabi bayanshi sabida bazata iya zama ita kaɗai ba.
Daga bakin gate ta tsaya tana hango sanda ya buɗe boot yana fito da kayan nata harya gama ya rufe sannan ya turo gate ɗin ya shigo.
Kusan cin karo yayi da ita wadda take kokarin juyawa ta bishi.
Haɗe ranshi yay tamau tare da raɓeta ya wuce.
Bin bayansa tayi har suka koma cikin part ɗin nasu.
Wannan ƙofar ɗakin daya buɗe ɗazu ita ya shige itama tabi bayanshi madaidaicin falone wanda babu komai acikinsa se doguwar kujera wadda daga ganima sabuwa ce domin ga ledarta nan, se ƙaton carpet ɗin da aka shinfiɗa acikin falon se fankar sama sabuwa dall se labulan daya ke a ƙofar ɗakin dana window da kuma ƙofar bedroom ɗin, wuce nan yay ya shiga cikin room ɗin itama ta bishi abaya, nan ɗinma carpet ne aka shinfiɗa acikinsa se ƙatuwar katifa sabuwa

wadda aka shinfiɗa katon bedshit se ƙaton bargon rufa a gefenta daban tare da pilow guda biyu da aka jera a gefen katifar bayan nan ko sip babu bare kuma madubi nan ɗinma akwai fankar sama acikinsa, aje jakunkunan hannun nashi yayi agefen katifar sannan ya zauna shima daga gefen yana mai sunkuyar da kansa ƙasa alamun gajiya sun bayyana ƙarara a saman fuskarshi.
Takowa tayi sannu a hankali itama ta zauna a ƙasan carpet ɗin dab da ƙafafunshi seta ɗora kanta a saman katifar sabida itama ta gaji kuma lokacin 12 na rana ma ta kusa sabida haka itafa cikinta ma yasoma kiran chiroma.
Tsitt ɗakin yayi bakajin sautin komai sena fankar dake famanyi sakamakon wutar nepar dasuka kawo yanzu.
Ɗago da kanshi yayi tare da zuba mata idanu yana kallonta.
"Kinga dai yadda tsarin gidan yake kuma ni ba mazauni bane ba, sabida yanayin aikina ki dinga rife ƙofarki inna zo zanna saka extra key ina buɗe wa sannan kuma bana son fita kinsan Allah ko nan gidan goma nazo na tadda kin shiga sena ɓata miki rai duk abinda kike so kidinga gayamin, zan sai miki waya ki dinga kiran mamanki tare da ammi sannan nima zan sa miki numberta".
Yafaɗa yana son ya tashi tsaye.
Cikin aro jarumta Bebi ta saka hannu ta dafe saman cinyarshi sannan ta dubeshi.
"Nifa baxan iya zama anan ba salon macijin yazo ya saremin jikina".
Tafaɗa tana kuma raɓa jikinta sosai ajikinshi alamun tsoro sun nuna atare da ita.
Zame hannunta yayi daga jikinshi sannan ya zamo daga saman katifar shima ya zauna saman carpet ɗin ya jeru da ita.
Tsintar kanshi yayi da kamo hannunta guda ɗaya, wasa yake da yatsun hannayen nata sannan taji muryarshi acikin dodon kunnenta.
"To yanzu idan ban tafi ba, da yaya zanna samo miki abinci kina ci?".
Yafaɗa mata hakan muryarshi da zubin rarrashi.
"Neman abincifa zan tafi".
Ta kuma jin maganarshi ahankali kamar da wasu awajan.
"Nifa bacewa nayi karka tafi ba, amman kanafa ji ance maka akwai maciji agidan sannan kuma ni seka barni ni ɗaya?".
Ta faɗa tana turo bakinta gaba kamar zata tsinkoshi.
Kallon yarinta yake mata jiba yadda take acting kamar wata yarinyar goye tsintar kansa yayi dajin dukkan zafin ɗazu ya gushe agareshi sabida yadda take fici-fici da idanun rigima tsira mata idanu yay tare da saka hannu ya tallafi kumatunshi dasu alamun tagumi batare daya tanka mata ba.
"Sabida haka sedai na shiga gidan wancan Baban mufidan koka kiramin ita kaga har yanzu bai turo ta ba kuma ina jin yunwa sosai".
Takai maganar tana turbune fuska alamun zata yi mashi kuka!.
Can cikin ƙasan maƙoshi muryarshi cike da zallar gajiya taji yace.
"Pls kada kimin kuka malama me zakici yanzu?". yafaɗa yana sakin hannunt.

Mayar da ƙwallar datake ƙoƙarin zubo mata tayi kana tace.
"Shinkafa da salak da nama".
Murmushi yayi irin na gefen baki sannan ya dubeta da ƙasan idanu.

"Tofa harda salak da nama?".
Yafaɗa yana ɗage mata girar sa guda.
Tura kanta tayi a tsakanin cinyoyinta tana dariya ƙasa ƙasa sabida yadda yay acting ɗin nasa harda kwaikwayon muryarta.
"Hmm sarkin rigima kenan wai kece autane wajan mama?".
Taji sautin muryarshi kamar an jefo ta cikin dodon kunnenta.
Ɗago kanta tayi tare da kallonshi ganin yadda yay mata ƙuri da ido yana kallonta yasa taɗan kauda kanta gefe ƙaɗan sannan tace.
"Taɓɓijan akwaifa ihsan da arfa autar mama kenan".
Tafaɗa tana dariyar da tunda ya ɗaukota jiya batayi ba seyau dataji ya ambaci sunan mamanta.
"To sewa kuma?".
Ya kuma tambayarta idanunshi still cikin nata damma tana kauda kanta ne.
"Kaga daga hassana da hussaina se shahid ɗan rainin hankali" tafaɗi hakan tana harara da ido kamar shahid ɗin yana gabanta.
Sannan ta cigaba.
"Se Bebi se ihsan se arfa"
Murmushi yayi aransa yana nanata kuruciyarta
"Wacece Beby kuma?"
Taji maganarshi akanta.
Wurr tayi da idanunta kaɗan alamun irin mamakin nan sannan tace.
"Gata agabanka kwa tana maka magana bafa Beby ba, Bebi ake cewa se an ɗaure sunan naji kai kana faɗin Beby kamar ta wasan ƴar tsana"
Tsintar kanshi yayi dayin ƴar dariya kaɗan yanajin yarinyar tana burgeshi idan tana magana sabida komai faɗinshi take direct ba kwana kwana dominshi yafi son mutum simple ya tsani mutum mai nuƙu nuƙu sabida yawancinsu munafukai ne acewarshi, ita kwa wannan daga gani zatai sauƙin kai tare da saurin sabo yana tunanin ta hakan kaɗai ze kuma janyota jikinshi harya bata dukkan wata dokar daya dace ya gindaya mata batare daya takurata ba.
"To nima nace BEBI" yawani ja sunan kamar shiya soma raɗa mata shi.
Dariya tayi kaɗan tana mamakin dama yanada surutu haka? ( hmm nima dai Bebi yau nasha mamakin wai Aliyu ne ke zuba surutun nan har yana dariya anya kwa Ali hmm bara dai nai shuru).
Shurune ya kuma biyo baya kafin taga ga muskuta kaɗan ya zaro wayarshi yana dannata, minti ɗaya taga ya kara wayar.
"Hellow goma kana daga ina ne?". bataji mai yace masa ba tadai ji shiɗin yana cewa"ok da Allah ka biya kayomin take away guda biyu sannan ka siyo kaji masu yawa pls inda halima katawo mana da ɗan ƙaramin frij" jimm yay kana taji yace "ok nagode" sannan ya katse wayar kallon agogon hannunshi taga yayi setaga ya zaro ido kaɗan.
"Lahh lokacin sallah yayi"
Seya miƙe.
"Ki tashi kiyi sallah nima zanje na dawo amman zuwa anjima goma ze kawo saƙo bance ki fita ba ki zauna a ɗaki inya gama shigo da kayan seki fita ki ɗebe dafatan kin fahimce ni sena dawo".
Itama tashi tsayen tayi tana kallon yadda ya kere mata a tsaho nesa ba kusaba aranta tana

yaba kyawun halittar da Allah ya bashi.
Idanunta zube a bayansa tace.
"Katu romin mufidan, to kazauna muyi sallar mana anan".
Se lokacin ya juyo gareta sabida da ya kalli hanyar ƙofane ma'ana ya juya mata baya.
Saurin juya kanta tayi ta daina kallon bayansa seta kalli ƙasan carpet tana wasa da yatsunta.
"Ni ai tunda nake bantaɓa missing jam'iba ko ciwo nake sena fita nabi, sabida haka akanki bazan fasa ba".
Taji maganarshi acikin kunnenta.
Turo bakin ta kumayi gaba.
"To naji mufidan fa?".
Taku yake har yaje bakin kofa bayada niyyar tanka mata secan taji yace.
"Bazata zoba koda ita aka kawoki"
Yana faɗin haka taga ya buɗe kofar ya fice batare data ɗara daga inda take ba tafara dira ƙafafunta aƙasa kamar wata yarinya ƙarama................

*87*

Da baya ta koma ta zauna daɓar a bakin katifa tare da saka hannu ta cire hijabin jikinta sekuma ta mike tsaye taje ta ƙaro ƙarfin fanka, saman dai katifar ta kuma zama tare da kwanciya fuskarta tana kallon rufin silin ɗin ɗakin dariya take a wannan karon kamar wata yarinya ta soma magana a bayyane.
"Allah sarki mama nayi kewarki, hassana hussaina kuzo muyi hira".
Sekuma hawaye, shaaaa ya biyo fuskar tata kamar wata sokuwa.
Buga ƙofar falon taji anayi cikin azama ta miƙe tare da saka tafukan hannayenta ta goge hawayen fuskarta sannan ta fita zuwa falon.
Ƙofar ta buɗe tare da zira kanta ta leƙa ganin yara mata guda biyu yasa ta ce musu.
"Ku shigo mana kwa tsaya a waje kamar wasu baƙi".
Duk da bata san kosu ɗin suwaye ba amman sabida yadda ta saba da social interresting da jama'a yasa ta faɗa musu hakan.
Babbar wadda bazata gaza shekaru goma sha huɗu a duniya ba baƙa ce babu laifi tana da kyawunta dai dai misali ita ta soma shigowa cikin nutsuwa sannan ƙaramar wadda bazata gaza shekaru goma ba itama ta shigo suka tsugunna a ƙasan carpet cikin nutsuwa babbar tace.
"Anty ina wuni umma ce tace muzo mu tayaki zama,sannan kuma tace agaishe mata dake".
Wani daɗine ya kama bebi wai yau ita ake cewa anty! wayyo zuciyarta ai nan da nan ta hau washe musu baki.
"Lah kune su mufida? naganeki ai kefa yaya sunanki ita mufida na shaidata ta yadda naji babanku yana kwanta tamin ita ɗazu"
Murmushi ita mufidan tayi kana tace.
"Eh nice wannan kuma aymana".

Ta nuna ƙanwar tata da hannunta na hagun.
"Hmm ku zauna sosai nanma fa kamar ɗakin umma ne bara nayo alwala nai sallah karku tafi kunji".
Tafaɗa tanajin daɗin ganin nasu datayi.
Zamansu suka gyara a nutse suna kallonta.
Harta koma cikin ɗaki ta tube hijabinta sannan ta kuma fitowa waje, fita tayi tsakar gida ta tsaya abakin famfon zatayi alwala.
Cikin haka taji alamun ana buɗe ƙofar gidan kafinma ta yunƙura harya shigo cikin gidan bakinsa ɗauke da sallama, kallo ɗaya yayi mata yana ƙoƙarin saka kanshi ya shiga ɗakin yace.
"Me kikeyi har nayo sallah ke bakiyi taki ba?".
Yafaɗa yana ɗage labulan ɗakin.
"Kaifa kace bazaka dawo ba".
Tafaɗa tana ƙoƙarin kunna famfon dake liƙe da ƙofar bayin.
"Dan nace bazan dawo ba shine yahanaki sallah akan lokacinta?" yafaɗa ransa aɗan ɓace kaɗan sannan ya ɗora da cewa......
"Kada ki yarda na kuma kamaki da rashin yin sallah akan lokacinta inba haka ba ranki xeyi mugun ɓaci nagaya maki"
Yafaɗa da sauri kuma duk wannan maganar dayake muryarsa bata tashi sosai yinta yake kamar maiyin raɗa.sabida shi magana da ƙarfi bata daga cikin ɗabi'arshi.
"Naji kayi haƙuri bazan kuma ba".
Tafaɗi hakan sabida gudun jan zance domin ta fuskanci shi abu kaɗan yana fusata shi.
Buɗe labulan ya ƙarasa batare daya tanka mata ba.
Sannan ya shiga cikin ɗakin tare dayin sallama, Cikin sauri su mufida suka amsa masa tare da gaisar dashi babu yabo babu fallasa ya amsa musu kana ya shige uwar ɗaka.
Suma da sauri suka fita daga ɗakin suna kokarin barin part ɗinma baki ɗayansa.
"A,a mufi se ina haka?".
Tafaɗa ɗanƙwalinta riƙe a hannu tana yarfe ruwan dake fuskarta.
"Zamu koma gida se in Uncle ya fita zamu dawo".
Murmushi tayi aranta tana cewa kuma kunyi gamo da bajimar fuskarsa kenan amman a fili setace musu.
"To nagode ku gaisarmin da umma kafin na shigo".
Tafaɗa kamar wata babbar mace,kana ta shige ɗakin.
Direct itama uwar ɗakan ta shige tare da tsayawa akanshi wanda yake kwance kansa na kallon rufin silin ɗin ɗakin.
"Ina sallaya?"
Tafaɗa masa gatsal.
Bai mata magana ba illa tsitt dayay mata kamar tana magana da dutse.
"Ina abin sallah zanyi sallah kaji?".
Batare daya ɗagoba yace.
"Ya tafi koyo sallama".
Kunyace ta rufeta salo salo ta koma tayo masa sallama sannan ta tsaya daga gefe tare da kallon carpet ɗin ganin sa a tsabtace yasa ta tada sallar ta cike da nutsuwa.
Wayarsa ke ringing! ita ya ɗauka sukayi magana da wani abokin cinikinshi, wanda har bebin ta

idar da sallar ma bai gama ba.
Gajiyace fall jikinta ga yunwa raɓashi tayi ta kwanta abinta.
Amman ta bashi baya duk da yadda jikinta ke rawan tsoro amman dai ta dake tai ta maza.
Can kuma setaji alamun ya ƙare wayar.
Domin taji yayi shuru.
"Kinajin yunwa ko?"
Ɗaga masa kai tai sama duk da ta bashi baya.
"Nifa ba,a juyamin baya kinji ko".
Turo mai baki tai kamar yana kallo.
"Toni banason haɗa idanu dakai".
"Sabida ga dodo?".
Dariya tayi kaɗan.
"Kawai dai harararkace bana so".
Ga mamakinta setaji yace.
"Bazanyi hararanba"
Mamakine ya kamata amman se bata musa masa ba seta juyo gareshi.
Amman bata iya haɗa idanunta danasa ba setai ƙasa dana tan ta rintsesu gam tana sakin numfashi sama sama.
Tanajin yadda kaifafan idanunshi ke yawo a saman fuskarta kamar yana kallonta.
Ƙara rintse nata idanun tayi tanajin bugun zuciyarta na ƙarfi fiye da zato.
Shikam tsirawa beby face ɗinta idanu yay kurum yana mata kallon ƙuruciya aransa yana tausayawa maraicinta.
Matsota yayi sosai wanda lokacinne yayi dai dai da sanda iska irin mai ƙurarnan ta soma tashi domin gashinan an ɗauke nepa hakanan windows suna kaɗawa alamun hadari na faman haɗowa sosai.
Hannunshi na rawa ya ɗora a saman ƙuguntа, turesa tayi da sauri.
"Baka bani abinci ba sannan ni kazo kaimin irin na ɗakin ammi".
Tafaɗa da suffar wauta.
Dariyar gefen baki yayi.
"Babufa wani abunda xan maki malama kalloni".
Yafaɗa yana ɗora hannunshi a saman fuskarta.
Sake matsota yayi sosai jikinta na tsananin rawa tama kasa dubanshi tsabar tsoronshi ya ɗarsu acikin zuciyarta.
Girarta ya taɓa yana ɗan jan gashinta dayay cunkus wurin.
Atare suka sauke ajiyar zuciya, shi yanajin daɗin yadda ya raɓeta ita kuma tanajin jan gashin girar tata kamar tafiyar tsutsa.
"Naɗan sha kaɗan? amman pls kada kimin kuka!
yafaɗa yana fito da harshensa kamar wani tsohon maye.
Tura mai baki tayi gaba.
"Nifa nakasa fahimta".
"Zaki fahimta ne"
Yafaɗa yana ɗora harshen nasa a saman hancinta ya lashe matashi kamar maye.
Idanunshi dasukai jajur ya zuba a saman fuskarta zuciyarsa tana bugawa da ƙarfi tare da

azalzalashi  akan biyan buƙatar ƙwaɗayin abinda take muradi.
Dukda yana ganin hakan zubar ƙimarsane wajan wadda yake kira da yarinya amman yaya ze iya sam ba,a filako a wajan feeling.
Saka tafukan hannayenshi duka biyun yayi.
Ya tallafo fuskarta ya ƙara yi mata rumfa da faffaɗan kirjinshi mai ƙamshi, ya haɗe da nata kirjin kana ya lalubo ɗan mitsitsin laɓɓanta ya kama danasa laɓɓan ya haɗe batare da miskilaba ya zira mata harshensa acikin bakinta yana tsotsa kamar alewa lumshe idanunshi yayi yana shafo sumar kanta.
Wani irin baƙon lamari Bebi keji acikin dukkan gaɓoɓin jikinta daman tun ɗazu datasha zumar ammi ta rasa meke mata daɗi katari da lallausan laɓɓan nasa yasa taji wani irin armashi da mugun daɗi na ratsa mata ilahirin dukkan sassan jikinta.
Hannunta takai saman west ɗinshi ta rungumo tana mai biye masa wajan mayar masa da martanin kissing ɗin nasa,amman in romantical style suke gudanar da hakan.
Kusan mintuna  masu yawa suka ɗiba bakinsu sarƙe dana juna kuma bayan wannan kissing babu wani abunda ya shiga tsakaninsu.
Ahankali ya zare bakinsa anata idanunshi lumshe yake furta.
"Ina son bakinki zakina bani insha kullum plsssssssss"
yawani ja maganar yana kuma rungumota

jikinsa.
Bugun ƙofar gidan ne yasa yay saurin zareta daga jikinsa tare da miƙe ya gyara kansa kana ya fita yana furta.
"Waye?"
Idanunshi duk sun firfito sunyi jajur................

#kyan alƙawari yasa nayi muku wannan sabida ba kyau saɓa alƙawari amman wallahi banajin daɗi se hakuri#

*Mai son littattafaina complt documents dana gama*
*RABON WANI*
*H  A S K E*
*KOBA SO*
*ƊAN MAJALISSA*
*DA IZZATA*

*Dukka akan farashin naira 1000, seya neman ta numbern nan 08142105218, suna nan complt a haɗe karatu kaɗai ya rage maka*

*88*

Kallo ɗaya zakama idanunshi kasan cewar sun hau saman network, seda yaɗan kuma gyara kansa sannan ya fita tsakar gidan ya kunna famfo ya wanke idanunshi sannan ya nufi can ainihin ƙofar part ɗin nasu ya buɗe, Goma ne ke tsaye bakin ƙofar hannunshi ɗauke da ledoji manya wasu kuma a ƙasa a zube.
Faɗaɗa far'arshi yayi tare da fita gaba ɗaya.
"A,a goma harka dawo kenan sannu fa angode".
Yafaɗa yana ɗan ɗago ledojin dake ƙasan.
"Wallahi oga na dawo ga kayan nan seka duba daga ciki abinda babu sekamin waya, kayan miyane senaje ƴan kaba, sannan akwai extra canjinka fa".
Ɗiban lodojin yay guda uku yakai tsakar gida sannan ya dawo ya karɓi na hannun goman kana yace.
"Okey ka zauna ka huta ba matsala zan taho dasu inna fita ai kamayi ƙoƙari nagode".
Murmushi goma yayi tare da cewa.
"Wallahi oga sena ƙarasa ladana gwarama ka barni zan haɗo muku ma harda kayan fruit insha Allah, frij ɗin kuma anjima zan kawoshi bayan an gama chakking ɗinsa".
"To shikenan nagode goma ka riƙe sauran canjin mana ka saiwa yara sweet"
Zaro idanu goma yayi sannan yace masa.
"Haba oga canjin ai ba ƙanana bane bare susha alewa dasu wallahi sunada yawa bara nai maka sending ɗinsu yanzu".
Ɗaure rai yay sosai tare da tura kofar ya shige.
"Ka zubarsu idan baka buƙata".
Goma yaji muryarshi cikin kunnenshi sanin halin kirkinsa da alkairin sa yasa goma juyawa yana kuma yi masa fatan alkairi tare da ɗunbin nasara a rayuwarsa.
Da kansa ya dinga ɗiban ledojin yana shigarwa falo harya kammala sannan ya wuce can cikin ɗakin.
Yadda ya barta haka yazo ya sameta tayi wani ɗai ɗai a saman katifar hannunta dafe da saman cikinta idanunta a rufe ruff.
Tsira mata idanun wucin gadi yay kana yace mata.
"Ga abincin an kawo ki zuba kici, Seki buɗe ledojin dake falon abinda babu kimin magana se a kawo ai kin iya abinci ko?".
Shuru tayi masa duk da tana jinsa amman tsabar yadda jikinta yake amace ta kasa tanka masa.
Wajan sau uku yana mata magana amman ko motsin kirki tagaza yi kuma itama ba laifinta bane laifin gangar jikinta ne datake ayyana mata  jin daɗin abinda yay mata aɗazun wanda harya sakata jin wannan baƙon lamarin datake ciki a yanzu.
Takowa yayi har gabanta ya raɓa ya zauna gefen katifar.
Can cikin ƙasan muryarshi yake kiran sunanta.
Ko amafarki baze iya kiran sunan mahaifiyarsa gatsal ba, wannan dalilin yasa yaji ze iya karanta sunanta wadda take a matsayin takwarar sunan mahaifiyarshi shikam bebi yay masa wani daban wannan dalilin yasa ya soma kiranta da.
"Ummi! ummi!! tashi mana ko kinyi bacci?".
Cikin wata iriyar birkitacciyar murya marar fitar amo! taji yana kiranta da Ummi kamar da wata

manufa acikin faɗin ummin, sarai kuma ta gane da itan yake amman setai ɗuff addu'a ɗaya take Allah yasa ya tabata kotaji salama acikin azababban feeling ɗin da gangar jikinta keji.
Kamar yasan ƙudirin dake ranta, Hannunshi ya miƙa ya sauke mata hannunta dake saman cikinta, mirginawa yay ya haye saman ruwan cikinta ya kwanta flate kansa yana saman fuskarta hancinshi yana saman nata bakinsa yana saman nata hannunshi yasa ya zagayeta.
Zaro idanu take sabida yadda ya zube mata dukkan nauyin jikinsa gashi babu damar yin ihu! sabida yadda ya tokare mata bakinta da nasa.
Gaba ɗaya numfashinta yay wani irin sauyawa sabida azabar nauyinshi zuciyarta na lugude kamar zata tsinko ta fito.
Ɗan zamewa yayi kaɗan yadda bazataji nauyin nashi sosai ba ya ɗora hannunshi a saitin zuciyarta yanajin yadda take faman duka kamar zata faso.
Hawayene ya soma fitowa daga cikin idanunta waɗanda suke a lumshe, sosai take zubda hawayen zafin da kirjinta ke mata sabida bakaramin zafi tajiba a ɗazun daya haye mata cikin nata.
Miƙewa yay zaune yana mata dariya.
"Raguwa kawai taso kije kici abinci".
Ya miƙe tsayema gaba ɗaya.
"Ni zaki saka na ɓata kayana kuma bani da wasu anan"
Tashi tayi tana tura baki gaba tana share hawayenta.
Dukda bai nuna yana sonta ba kuma bai furta mata hakan da bakinshi ba, amman hakika abinda yake mata yana matukar sakata jin daɗin dayasa harta soma jin yana burgeta ba kaɗan ba.
Gaba yayi zuwa falo itama mara mishi baya tayi kamar wadda ƙwai ya fashewa aranta take raya daman haka auren keda daɗi amman ta zauna tana kuka! ai wallahi inda tasan haka yake da tuni tace mama tayi mata.
Ahaka ta karasa falon yana daga saman sopa a zaune yawani haɗe rai kamar bashi ba.
Zama tayi agaban kayan ta soma buɗe komai daki daki.
Ledar farko wani irin kwaline cikinta mai ɗauke da ɗan ƙaramin gas, na girki ajewa tayi bayan ta fito dashi waje, ledar datake ta biyu kuma tarkacen kwalayen su taliyane indomie da sauransu ɗayar kuma ɗan madai daicin bugunne na shinkafa tare da ledojin semo acikinsu,abinka da kayan store wai duk girman kayan nan se an zirasu a leda, ɗayar kuma kayan tea ne cikinta ɗayar kuma su maine da kayan ɗanɗano atakaice dai babu abinda ba,a siyo ba na kayan masarufi.
Seda ta gama fidda komai dake ledar, sannnan ta janyo karamar wadda take ɗauke da abincin dayace ya siyo musu tare da wadda ke gefenta ita kuma kajine gasassu cikinta.
Tashi tayi tsaye tana rage kayan tana fita dasu.
Tana shiga kicin ɗin datai mamakin ƙanƙantarsa wanda kuma harda lokoki acikinsa tare da tukwane guda biyu sabbi da plate's ajere da spoons dadai kayan kicin amman bawai masu yawa ba kuma daga gani sabbine wanda take tunanin duk.wannan shirya gidan nasu aikin gomane daya wakilta kafin suzo.
Komai seta ta jera a muhallinsa bugun shinkafar nema dataje zata ɗauka sabida karamine seya hanata ya ɗauka da kansa ya kawo mata ya aje sannan ya koma.ɗaki.
Plate ta ɗauka da cokali taje ta wankosu a famfo sannan ta koma ta ɗauki kofin data gani kusa

da saitin jerin filetan wajan, shima ta wanke tare da cikashi da ruwa ta nufi ɗakin bakinta ɗauke da sallama.
Ƙoƙarin zama take ta zuba abincin taji muryarshi.
"In kika tafi can wajan kofar fita akwai abin zuba datti ki ɗauki tsintsiya ki gyara wajan mana inkin gama seki ci abincin a nutse a tsabtace ai yafi"
Yafaɗa yana mai ɗaga wayarshi dake ƙara tare da furta.
"Hellow usman ya ake ciki?".
Bata gamajin abinda yake faɗi ba ta ta fita daga ɗakin, seda ta tsaya a gaban famfo tasha ruwa ta ɗan huta sannan ta nufi wajan ɗaukar tsintsiyar tanajin dik ta gaji( hmm Aliyu baka san madam ɗin taka madam ƴar madara bace ba inaga bata son aiki fa)
Lokacin data dawo ya gama wayar yawani kwanta a saman sopar idanunshi rufe harara ta ɓalla masa ta wannan sakata aikin dayay kana ta zauna ta soma sharar.
"La'ila haba ummi shara a zaune kamar wata raguwa ko dai yunwar ce ta saka haka kinsanfa ni bana son ganda"
Ko kallo bai isheta ba ta kare sharar tare da fita ta zubar ta dawo ta zauna tana faman huci.
Ledar abincin ta jawo zata zuba.
"No ke baki san akwai bacteria, ba yakamata kije ki wanko plate ɗin kafin ki zuba abincin aciki sabida gudun ƙwayar cuta".
A wannan karon jitayi kamar ta kurma masa ihu amman tsoro baze barta ba.
Tashi tayi fuww taje ta wanko ta dawo ta xauna ta soma bude abincin tana zuwaba.
Tanaji yana tambayarta meye babu akayan abincin tayi masa banza sabida haushin aikin dayake sakata.
Aɗan zaman da sukai ta fahimci tsananin tsabtarshi tare da tsantsenin shi uwa uba kuma taga baida son jiki saɓanin ita da inda ze mata wanka ma sotake.
"Ummi"
Taji ya faɗi wannan sunan daya raɗa mata yau.
"Ummm".
Ta faɗa lokacin datake kai loma abakinta fuskarta a ɗaure.
"Ni bazaki min tayi ba, kofa break fast banyi ba".
Haushine yazo mata wuya jiba yadda yake wani abu kamar karamin yaro zesha mama.
"Ai ɗauri biyune abincin".
Ta bashi amsa kai tsaye wadda take da manufa biyu.
Murmushi kawai yay kana ya koma ya kwantar da kansa, lallai samun mace kamar khadija se antona se yanzuma tunaninta ya faɗo mashi aransa.
Idan itace bazata taɓa cin abinci gabanshi ta hana shiba idanma baici ba setai kokarin yi mashi kuka! amman ita wannan kanta ɗaya ta sani.
Tunanin halin khadija ya faɗa ita ko Bebi abincinta takeci hankali kwance ta gama ta ɗauko kaza guda wadda ke cikin leda.
Ta soma yaga tana ci tana lumshe idanu sam ta manta dashi awajan seda ta gama cin abincinta tsaf sannan  ta shanye  ruwan dake kofin gabanta sabida babu pure water agidan kana taja ƙafafu ta naɗe batare data ɗauke plate ɗinba.
"Madam a ɗauke kwanukan mana, kefa banason son jiki wallahi akan wannan halin zamu soma faɗa da wuri".

Taji muryarshi akanta.
Banza tai masa ta ɗebe kayan takai kicin ta dawo.
"Jeki wankosu mana ki kife tunda ba yawa,Kuma naga akwai omo akayan daya siyo".
Kamar kububuwa haka ta koma ta wanke plate ɗin amai makon ta koma ɗakin setai zamanta aka dakalin famfon batare data koma cikin ɗakin ba.
Shiko abbane yay mashi waya cikin sauri ya ɗaga wayar sukai maganar dazasuyi kana ya miƙe, ya fito hannumshi riƙe da key.
Tana ganin ze ɗaga labule ya fito ta miƙe tsaye.
Kallonta yay kaɗan ya kauda kanshi.
"Zani gida amman ƙilan zan dawo anjima pls ki samu kiyi wanka kafin na dawo akwai kayan brush a toilet sekiyi"
Juya masa baya tayi.
"Bazaka ci abincin ba?".
Murmushi yayi tare da shafa sumar kanshi.
"Bantaɓa cin abincin waje ba zanje ammi tamin nata naci tunda ke nasan bazaki min ba".
Dariya tai kaɗan tana rufe idanunta.
"To adawo lafiya Allah ya tsare inkaga yaya usman kace nace ya gaisarmin dasu ƴan biyuna inya gansu a kamfani".
Tafaɗa muryarta tana rawa kaɗan alamun xatai halin.
Tausayi yaji ta basa amman bai nuna mata ba.
"Zan gaya masa insha Allahu kona zo dasu nan?".
Girgiza kanta tayi.
"Karka gayawa mama amman dan bazata bari suzo yauba nasani".
Dariya yayi.
"Bama yanzu ba senan gaba zasu zo kedai kiyi wanka kafin na dawo".
"Nifa bana wanka biyu sabida murace dani kamar kaza".
Dariya yayi sosai dajin maganar tata.
"Drama gel! karkiyi wallahi na dawo da kaina zan miki a tsakar gidan nan"
ai da gudu ta faila tayi ɗaki tana sheƙa masa dariya.
Shima dariya yake harya fice yaywa goma waya akan ya tura mata su mufida shikuma ya wuce yanajin zuciyarsa fresh.
Direct motarshi ya buɗe ya shiga tare dayin revars yabar layin................

*Mai son littattafaina dana kammala complt documents  akan farashin naira dubu ɗaya ( 1000) waɗanda suke guda biyar ciff seya nemi 08142105218*

*RABON WANI*

*H A S K E*

*KOBA SO*

*ƊAN MAJALISSA*

*DA IZZATA*

_Gaba ɗayansu babu na yadawa siyan nagari mayar da kuɗi gida_ 😍

*89*

Driving yake cikin nutsuwa fuskarshi ɗauke da matsanancin farinciki wanda shi kanshi ya kasa gane kona miye ahaka harya ƙarasa fita daga cikin unguwar kanshi tsaye babban titi yahau wanda ya bashi damar ɗaukar hanyar sa ta gidansu.
Tafiyar mintuna masu yawa ya shafe yanayi asaman kwalta har Allah ya bashi sa,a ya shiga cikin unguwarsu lokacin gari yaɗanyi rana saɓanin ɗazu da hadari ya haɗo kamar za,a sheƙa ruwa.
Lokacin daya isa bakin gate ɗinsu har ansoma yin kiran sallah acikin waɗansu masallatan, a nutse yake rage gudun motar tashi wadda take tafiya a slow harya zo daf da gate ɗin kana ya danna horn.
Cikin nutsuwa ba kamar ɗazu da zasu fita ba.
Cikin azama masu gadin gidan suka sheƙo aguje domin zuwa su buɗe mishi gate ɗin.
Seda suka ɗan leƙo da kansu suka tabbatar da shiɗinne kafin sukazo suka bude mishi suna masu ɗaga mai hannu.
Cikin nutsuwa yake jan kan motar harya idda shiga tafkeken ma'adanin motocin gidan nasu kana ya gyara parking ɗinshi tare da dai-daita motar sa'annan ya kasheta ya fito waje yana shaƙar iskar harabar gidan nasu tare da kamshin furran dake harabar wajan.
Jan ƙafafun shi yayi zuwa ainihin part ɗinshi seda ya kama kofar datake maƙale da gate ɗin sannan ya tuna cewar ya gayawa dija baze dawo yau ba, amman kuma dole ce ta sakashi dawowar tunda kiran abbanshi ne, buɗe kofar yayi kana ya zura kafafunshi cikin part ɗin nashi tare da ƙarasawa ya buɗe kofar falon ƙasa ya wuceshi kana ya haye samanshi, Buɗe ƙofar falon samanshi yay ya shiga bakinsa dauke da sallama, khadija ce ta amsa masa sallamar tana zaune a falon tana kallo jikinta sanye cikin vest da threequater vest ɗin jace shikuma wandon baki kanta babu kallabi se dogon kitson datai wanda ya zubo mata har wajan kirjinta waɗanda a kwana biyun nan suka ɗan tasa kaɗan.
"Lah yaya dama xaka dawo amman baka gayamin ba dana maka girki duk na ɗauka se goben".
Ta faɗi hakan bayan ta tashi tsaye tare da nufarshi ta karɓi keyn dake hannunsa.
Murmushi yayi mata kaɗan wanda ya tsinci kansa acikinsa yau tun tashin sa kana ya dubeta cikin tsantsar kulawar da bata taɓa samunta a wurinshi ba.
"Na dawo dija abba ke nema na yasa na dawo amman ƙilan na koma anjima ko gobe".
Yana faɗin hakan ya nufin hanyar bedroom ɗinshi.
Da sauri itama tabi mashi baya tana masa magana akan yadda tai farin ciki da dawowar nashi.
Se yau ta ƙarewa bedroom ɗin nashi kallo wanda babu wasu tarkacen kaya acikinsa komai tsaf,

Bata tsaya ɓata lokacinta a kallon tsarin ɗakin nashi ba ta wuce  cikin kofar data gani a gefe wadda take tunanin bathroom ne ruwa ta soma haɗa masa mai ɗan dalam dalam kana ta fito lokacin yana kokarin sanya rigar wanka.
"Yaya na haɗa maka ruwan wanka"
Juyowa yay tare da zuba mata idanu.
"Nagode dija".
Murmushi tayi tare da cewa.
"Ba naje na sama maka abu marar nauyi domin nasan tundaga tean safiya da ƙyar idan kaci wani abun"
Bata jira cewarshi ba ta fice a ɗakin murmushi yayi kana ya faɗa cikin bayin wankan kusan awa guda yay tare da ɗauro alwala ya fito duka jikinshi yana ɗigar da ruwan damshin wankan.
Gaban mirrow ɗinshi yaje ya tsaya yana goge ruwan dake jikinshi tare da shafa cream sama sama turaruka masu daɗin kamshi yayma kanshi ɓari sannan ya nufi gaban kayanshi ya shirya kanshi cikin wata ɗanyar dark blue gezner wadda aka mata ɗinki half body wanda ya fito da tsantsar baiwar cikar halittar da Allah yayi mishi seda ya kuma watsawa jikinshi wasu turarukan sannan ya ɗauki agogonsa fari na rolex ya saka,a tsintsiyar hannunshi takalmin fata ya saka wanda yay marching da kayan jikinshi hakan nan hular dayay amfani da ita ta tangaran itama mai shigece da kayan na jikinshi.
Masha Allah! Anan ya fito a ainihin Aliyun shi kuma a ainihin shigar al'adarshi ta yaren hausa fulanin usul.
Gemunshi yaɗan janyo kaɗan yana shafawa kana ya fita daga ɗakin yana barin kamshinsa acikinsa.
Gaba ɗaya falon nashi ya ɗauki mugun daddaɗan kamshin girkin da dija keyi zama yay akan ɗaya daga cikin royal chair din dake falon yana mai ɗaukar remote ya tsaida tv ɗin dakeyi sabida kiran sallar da ake yi a masallacin cikin gidan nasu.
Yana zaune bini bini ze ɗago hannunshi ya duba agogo sabida bai son abba yay sallah ya dawo basu haɗu ba.
A haka ta shigo falon hannunta ɗauke da plate wanda ta zubo ƴar jallof ɗin cous-cous ɗin data yi mai wanda tai decoreting ɗinshi da kayan vegitables masu ƙayatarwa, da ɗayan hannun ta janyo table ɗin dake tsakiyar falon ta aje mai plate ɗin akai sannan ta tura mai gabanshi tana mai cewa.
"Ga abincin nan ina zuwa".
Kallon abincin yayi sau ɗaya ko kaɗan baya son cous cous amman sabida bai son yaga ya jisgata yasa ya ɗanja spoon ɗin tare da faɗaɗa shi sabida yaɗan huce.
Babu laifi ya daina wannan tururin dan haka yay Bisimillah.
Kana ya ɗauki spoon ɗin ya soma ɗiban shi kaɗan yana kaiwa bakinshi kuma girkin yayi daɗi sedai baya son cous cous shiyasa lomarshi ɗaya ya ture duk da tsananin yunwar da yake ji.
Tawowa tayi hannunta ɗauke da wani ɗan medium jug se cup guda gabanshi ta aje a gefen plate ɗin tare da tsiyayo mai lemon kwakwar data haɗa yanzu seda ta cika tamm sannan ta tura mai gabanshi sannan ta nemi guri ta zauna tana kallonshi tana yaba kyawun dayayi tare da jin kishin wannan kwalliyar kada mace ta gansa a waje.
"Sannu nagode".
Yafaɗi tare da ɗaukar cup ɗin data haɗa mai lemon kwakwar ya kafa a bakinshi yana mai jin

daɗi sabida garɗi da daɗin lemon a zuciyarshi.
Seda ya shanye gaba ɗaya sannan ya miƙe yana mai ɗaukar phone ɗinshi.
"Kije ɗakina ki ɗaukon keyn mota".
Taji  maganarshi cikin sauri taje ta ɗauko mai ta kawo masa.
"Zan fita any way dai zamuyi waya".
Yana faɗi mata haka yabar falon sejin ƙarar fitarshi tayi.
Tattare wurin tayi ta shiga sabgarta tana jin ranta sakayau na yadda yau ta sami kansa.
Seda yaje masallaci sukai sallah sannan suka jero tare da usman wanda ke faman yi mai tsiya bai tankashi ba har sukaje part ɗin abba a falonsa suka haɗu anan suka zauna sukai maganar da zasuyi sannan ya wuce mota.
Bai sami zarafin leƙa ammi ba sabida akwai inda ze biya.
Koda ya fita daga gida kai tsaye harba hancin motarshi yayi zuwa unguwar sharaɗa.
Abakin layin gidansu Bebi yaja ya tsaya seda ya kintsa komai sannan ya fito daga motar ya shiga cikin layin da ƙafafunshi.
A ƙofar gidansu Bebi ya tsaya yana faman leken kozaiga ɗan aike cikin haka shahid yazo ze shiga a mamakin Aliyu seyaga yaron ya tsaya tare da rissunawa yana gaisarshi.
Tsira mai idanu yay yana hango tsabar kamar yaron da Bebi hatta haskensu kusan kai ɗayane.
"Dan Allah ƙanina kacewa mama ga ɗanta yazo".
Zaro idanu shahid yay kamar yadda bebi keyi kana ya juya batare daya ce komai sedai iya acting ɗinshi kaɗai ya fahimtar da Aliyu cewar yaji mamakin furucinsa ne.
Mintuna biyu shahid ya leƙo "wai tace ace ka shigo".
Cikin kamala yaja katon bugun da aka lulluɓe soron ya shiga yana mai sallama kana ya bayyana a tsakar gidan.
Mama wadda take zaune akan kujerar tsugunno iya kuma tana kan tabarma ƴan biyu suna ɗaki suna faman shirin zuwa gidan bebi harma da sadiya.Ita ta amsa sallamar duk azatonta usman ne ma amman ganin Aliyu yasa ta gyara mayafinta sosai tare da sunkuyar da kanta ƙasa bakuma tayi masa magana ba se iyace tai saurin gyara mai tabarmar ya zauna.
Muryarshi mai sanyi ita ta karade kunnuwansu, yana gaisar dasu.
Seda ya soma gaisar da iya sannan yace.
"Umma barka da yamma ya gida?".
Ta cikin mayafi mama ke amsa masa sabida itafa Allah ya zuba mata jin kunyar surukai kosu ya aminu ma tunda taji kanun maganarsu da ƴan biyu yanzu bata sakewa da su ko kaɗan.
Mama tasan Aliyu iya kuma bata san shine mijin Bebi ba sedai tayi mamakin ganin yadda mama ta koma tsit dan haka iya ta kada baki tace.
"Mamam ƴan biyu yanaji kinyi bako kuma kin  masa shuru kodai surukin namune?".
Se lokacin taɗan ɗago kaɗan.
Batacewa iya komai seta soma cewa.
"Hassana! hassana zo mana".
Sannan ta ɗan dubi Aliyu wanda tsabar mamaki ya kamashi tace.
"Toya gidan naku dafatan dai bata maka wannan shirmen nata ko, Allah ya saka maka da alkairi angode".
Tafaɗi maganar a rarrabe.
Atare su hassana suka fito dukkansu har sadiya.

hussaina ce ta sanshi dan haka cikin sakin fuska tace
"Lahhh umma fa Ya Aliyu ne mijin Bebi wallahi shine ina yini?".
Tafaɗa cikin far'arta.
Ba yabo ba fallasa yace
"Lafiya"
Haka hassana da sadiya wadda ta saki bakin mamakin haɗuwar mijin kawarta ta suka gaisar shi.
Se lokacin shahid shima ya fahimta aikwa cikin sauri ya xare jikinsa mintuna biyu sega shi ya dawo hannunshi ɗauke da bakar leda ya mikawa hassana.
Ta karɓa lemo ne da ruwa ta juyo a saman tire ta kawo masa kana suka bar wajan suka koma cikin ɗaki.
"Haba maman biyu base kice min surukin namu bane ko yau karar akansa ta motsane bafa shi bane na farko".
Iya ta faɗa tana dariya.
"To dafatan dai Bebi tana lafiya? domin yanzu da ake shirin tura ƴan uwanta su gano mana ita"

Iya ke tambayarshi hakan.
Ɗago kansa yayi.
"Lafiyanta kalau ai bama gidane ita tacan ɗayan anguwar da gidana ke can insha Allah inna sami time senazo na kaisu can ɗin".
Yafaɗa yana kallon umma wadda take kauda kai gefe.
Shi dariya abin fa ya bashi ammi ko kaɗan bata kunyar surukanta wadda a haifema ta kusan haifar kamar maman amman ita jiba tama kasa kallonshi lallai yau yana ganin ikon Allah.
"To madallah Allah ya tayaka riko mungode sosai dan Allah kadinga hakuri da ita fa wallahi Bebi yarinya ce duka yanzu take ata sha bakwai se hakuri".
Murmushi yayi.
"Babu komai insha Allah, umma ni zan koma bakida saƙo?"
Ɗagowa tayi sannan tace.
"Kace ina gaisar da ita kuma ta kula sosai, amman bara na zubo mata dambu akai mata".
Sauya yanayin fuskarshi yayi wadda ta nuna alamun rashin jin daɗi nan take.
"Umma har yau suna fita tallen ne?"
"A,a basa xuwa ɗazu dai na saka akayi na dare"
Mayar da ajiyar zuciya yayi sannan yace
"Umma dan girman Allah kada su ƙara fita talle dan Allah umma, koda ban aureta ba tabbas inna sanku xan iya hana su fita talle to bare kuma yanzu da aure ya haɗani daku,insha Allahu da anjima zan aiko yarona yazo ya kawo muku saƙo sannan zan saka ai ma mai wannan gidan na gefenku magana naga ba mutane cikinshi se a haɗa a rushe da wannan a gyara muku pls umma karkimin fassara ta daban koda ba auratayya zan iya tallafar marayun Allah dan Allah karki musamin nagode"
Yafaɗa yana mai kafeta da idanu yana hango tsantsar kamanninta da ƴarta sedai ita mama akwai hakuri.
Kasa masa magana tayi seta miƙe tayi cikin kicin ta zubo mai dambun a ƙaton fulas ta kawo gabansa anan ta tarar da iya tana faman mai.godiya kamar zata ari baki.

Jin godiyar ike har ranshi dan haka da sauri ya mike tare da daukar fulas yana zira hannunshi cikin aljihunsa.
"Umma na tafi a turomin shahid ina waje".
Ya faɗi hakan sabida jin yadda bebi take ambatar sunan shahid shine yasa kai tsaye ya gane yaron
"Mun gode Allah ya tsareka Allah ya ƙara buɗi Allah ya rabaka da iyaye lafiya".
Mama ta faɗa tare da shiga ɗaki sannan ta tura mai shahid ɗin.
Fita yay ransa sanyi kalau sabida addu'ar da sukai mai yaji daɗinta ba kaɗan ba.
"Masha Allah maman ƴan biyu arzikin ya soma sallama lallai ɗan mutum mai rana komai tsiya haifi ka yar yara ku fito yau alkawairin Allah ya cika bilkisu ta haifu domin yau dai ga arzikinta ya fara doko sallama a gidan nan".
Muryar iya kenan wadda take faman zuba buɗa kamar zata zuƙo hancinta.............
AFUWAN NA YAU BA EDITINTG

*90*

Da sauri su hassana suka fito tsakar gidan kusan atare suka furta.
"Iya meya faru?"
Kafin kuma su nemi guri kusa da iyan suka zauna suna sauraronta.
"Hmm ƴaƴan nan ba dole kuji ina buɗa ba wannan yaro anyi yaron arziki lallai Aishatu kinci wuyar Bebi a yarintarta ashe ga ranar daɗinta nan kowa zeji".
Anan ta fayyace musu dukkan abinda Aliyu ya cewa mama wanda kusan atare suka soma kabbara da hamdala ga sarki Allah.
Sumi-sumi mama ta fito daga cikin ɗaki tana share hawayen farin cikin dake saukar mata zama tayi a gefen iya tana mai cewa.
"Ashe dai iya nima zan ɗanɗani daɗin hutu aduniya?".
Da sauri iya ta dubeta.
"Haba maman ƴan biyu sekace keba musulmaba? kintaɓa jin inda bawa yake yanke rahama a rayuwarsa? yoko Aljanna bawa baya fitar da rai da samunta bare kuma duniya, sabida haka ki ƙaddara daman can Allah ya tsara ta jikin ƴarki zaki sami jin daɗi da hutu ƴar takinma wadda kika fi cin wuyarta todai kinga yadda Allah ke juya lamuransa ko?".
Share hawayenta tayi tare da cewa.......
"Hakane iya amman wallahi nidai shekarun baya da suka wuce naci wuya kinsan girman Allah wani zubinfa abincin namu baya isarmu ni zan sha ruwa na hakura na basu sukuma waɗannan su hakura subaiwa ƙannan amman fa Bebi sabida jarabarta bafa zata bar ma kowa ba yadda arfa zata lamushe itama hakan takeyi wallahi iya saukinmu fa ɗaya lokacin da muka soma yin

dambun nan ashema acikinsa silar firarmu daga wannan matsatsin take".
Tafaɗa tana murmushin jin sanyi acikin ranta.
"Hakane daman Allah ya tabbatar mana da alkairinsa amin amman daman ai bayan wuya se daɗi insha Allahu shekara mai zuwa sekinje hajji a dalilin haihuwa".
Dariya suka kwashe da ita gabaki ɗayansu.
Nan da nan kuma hira ta kuma ɓarkewa cike dajin daɗi.

Shahid na fita ya hangi Aliyu harya kusan fita daga layin seda ya haɗa daɗan gudu sannan ya cimmai, Agaban motar Aliyu ya tsaya batare daya shiga ba sannan ya kalli shahid wanda ke kokarin russuna mai.
"A,a abokina baseka rissunamin ba, zaka iya bina kasuwar sunga, muje mu dawo kona haɗaka da mai napep zaka iya dawowa gida da kanka?"
Shikam dariyama maganar ta basa ina ne baya zuwa amman seya kame sannan yace mai.
"Ina zuwa har gaba da nan mama tana aikana dan haka babu matsala, amman dan Allah ka kaini nagano Bebi kafin nan".
Dariyar gefen baki yay yana mamakin yadda yaran suke son junansu sannan ya dubeshi.
"Ai ba,a kusa nake ba kafaɗi aiken naka zan gaya mata insha Allah, amman na sami lokaci duk zanzo na kaiku kuga gidan nata".
Dariya shahid yayi.
"Damafa ni zuwa zanyi naci ladan gaben idomie ɗina dataci min domin wallahi sena kwaɗeta".
Kama baki Aliyu yayi cike da mamaki ah lallai dole waccan yarinyar tai shirme yanzu wannan yayanta ne ke faɗin wannan kuruciyar kiri-kiri.
"To ai yanzu bazaka iya dukanta ba kamanta yanxu tanada aure, In indomie ce zan biyaka katan nawa kakeso abokina?".
Dariya shahid yay batare dayace komai ba, Aliyu ya bude mai mota suka shiga yaja suka nufi hanyar kasuwar sunga wadda ake sayar da kayan masarufi acikinta.
*************
Tunda Aliyu ya fita Bebi data shiga ɗaki tana masa dariya akan yace ze mata wanka bata kuma fitowa ba anan bacci ya kamata, daman kuma ga iskar gari wadda ake yawaita yinta kwanaki biyun nan sabida ƙarshen damuna dayazo sanyi yana kawo kanshi.
Ba ita ta shiba seda taji bugun gidan yayi yawa.
Tashi tayi tana zare idanunta waɗanda sukayi jajur dasu, sannan ta miƙe miyau fall bakinta seda taje ta zubda sannan ta wanke fuskarta, kana ta nufi wajan bugun buɗewa tayi tare da raɓewa,gefe tana kallon wata bakar mace wadda bazata gaza shekaru 30 ba marar jiki doguwa amman gani ɗaya zaka mata kasan cewar ta haɗa jini da ƴan mai duguri domin ga zanenta nan na kanuri ya fito a saman goshinta, ƴar gayuce ajin farko domin babu abinda jikinta keyi se faman zuba uban ƙamshi mai kwanciya a zuciya, se su mufida a bayanta.
Hannunsu ɗauke da ledoji masu zane waɗanda alamun kayan miyane a hannun nasu.
Da far'a take cewa.
"Au mufida se yanzu kuka shigo min kun barni gida ni ɗaya?".
Tafaɗi hakan kamar ta jima da sanin yaran.
Gaba tayi suka bita abaya seda suka shiga tsakar gida sannan suka gaisa a mutunce da wannan matar kana tace mata.

"Ai su aymana suntafi islamiya ne yanzu suka shigo, Nice mamarsu sunana Nafisa amman ana cemin umman mufida, ni kaɗaice yaren hausa a gidannan ragowar dukkansu ƙabilune ma'aikatan kamfanin mijinki hausawan suna ɗayan gidan nashi na bayan layin nan".
Washe baki Bebi tayi tare da cewa.
"Kai amman naji daɗin kasan cewarmu anty nafisa Allah ya haɗa kammu amin".
Gaba tayi suka bita zuwa falon.
"Yawwa Anty Bebi ga wannan saƙon inji babansu yace ogane yace akawo kayan miyane amman bara na saka mufida ta gyara miki idan babu damuwa zan tafi dashi can naga da yawa senai miki dubara na dafa miki su yadda bazasu lalace ba".
Kallonsu tayi da murmushi.
"To anty nafisa nagode amman ku zauna mana naga kun tsaya kamar ba gida ba".
Dariya umman mufida tayi.
"Haba amarya magariba ta gabato naga ko gyaran gidan yamma ma bakiyi ba hala baccin gajiya kikene nasan ansha mota".
Hamma tayi kana ta fice waje tana ce musu tana zuwa.
Alwala tayo tazo ta tayar da sallar la'asar tana idarwa ta janyo ɗayan ledar abincin.
Babu yadda batai dasu ba akan suzo suci amman fafur sukaƙi sema faɗan da umman mufidan keyi na damme bata aiko an karɓa mata burabusko ba amman anjima zata aiko mata da abincin dare.
Godiya tai mata nan da nan taji ta aminta da umman mufida mace mai tsafta da gayu jitai ta ɗauketa kamar mama sabida yadda taga tana mata kamar ƴar uwarta ta jini( Allah ka haɗamu da mutane nagari masu halin girma masu sonmu domin Allah Allahumma Amin ) Harta gama cin abinci umman mufida tana zaune ba dai tai wata magana ba amman tana nazarin yarinyar wadda tashi ɗaya taji Bebin ta shiga ranta jinta take kamar ƴar uwarta ta jini, nan da nan taji aranta ta samu ƙanwa a kano tunda dai ita,ba ƴar garin bace kuma bata da kowa anan ɗin, Tunanin yanayin Bebin ne yaɗan bata mamaki taga yarinyar ƙaramace sannan kuma daga gani bata san komai na game da aure ba se tsabar wauta da zumuɗi kuma idan bazata mance ba kwanakin baya taji baban mufida yana ce mata oga yay aure ya auri cousins ɗinsa ba dai ta da masaniyar komai bayan wannan dan haka tasha alwashin koyar da Bebi wasu abubuwan kafin Allah ya rabasu domin tasan zaman nasu baze daɗe agidan ba kamar yadda mijinta ya gaya mata, ta ɗauki alwashin bawa bebi training na musamman akan rayuwar aure da tsafta da gyaran jiki kai harma da girki domin ɗa na kowane itama bata san mai mufidatan zata zama gaba ba.
Kallonta umman mufidan tayi cike da kulawa.
"Anty bebi yaushe angon naki ze dawo?"
Ɓata fuska tayi.
"Haba anty nafisa dan Allah kidaina cemin anty nifa wallahi ƴarkice kicemin Bebina kawai"
Tafaɗa tana rufe idanunta.
"To naji Bebi" umman mufida ta faɗi tana dariya.
"Yace ko anjima ko yaushe ma oho mishi".
Tafaɗa tana tura bakinta gaba wanda ya ƙara fiddo mata da tsantsar kuruciyarta.
"A,a Bebi, mufida kutashi anan kuje gida ku gyaramin kayan miyar nan akai markaɗe".
Tafaɗa tana mai basu umarni, wanda ba musu suka miƙe suka fita daga ɗakin.

Kamo hannun Bebi tayi ta riƙe da kyau tana fuskantar ta.
"Haba Bebi mijin kine fa ta yaya zakice bakisan ranar dawowarshi ba, bakida wayane?".
Tura bakinta tayi.
"Eh bani da ita"
"Shekarunki nawa Bebi?"
"Sha bakwai"
Ta bata amsa.
"Masha Allah Bebi nasan kinyi karatun addinin ko? kinsan haƙƙin mace akan mijinta kamar yadda namijin shima keda hakki akan mace wanda ya haɗa da, kulawa kyautatawa bin umarninshi sauke haƙƙin aure da sauransu, domin shi aure bautar Allah ne wanda se mun haɗa da hakuri a yayin zamanshi.................yanxu kin shiga sahun manya komai na hakkin aure ya wajabtu akanki tsafta kulawa kyautatawa da sauransu".................Sosai ta zauna ta fayyace mata komai na dangane da aure ta jaddada mata tsafta tafi sau uku tare da gyaran jiki dana muhalli, gami da iya girki.
Nan da nan jikin Bebi yayi sanyi har tanajin karayar zuciya.
"Ko kina son ya ƙaro miki amarya wadda zata na basa kulawa?"
Amamakinta setaga Bebi ta girgiza kai ma'ana bata so har tana haɗe ranta.
"To ki rage son jiki ki dage wajan kyautata masa kinji ko?"
Ɗaga kanta tayi sama alamun yarda da maganar umman mufidan.
"Yanxu tashi muje kicin ki duba aga mai za,a dafa masa".
Anan wajan dariya tayi kana tace mata.
"Kai anty nifa ba wani iya girki nayi ba amman dai na iya taliya"
Dariya anty nafisan tayi atare suka jera suka fita tsakar gidan da taimakon anty nafisa aka haɗa gas ɗin wanda daman an riga an zuba gas ɗin acikinsa.
Kunna mata tayi ta taimaka mata da ɗan blanding ɗin kayan miya, batai gigin taɓa mata girkin ba amman ta tsaya akanta tana nuna mata yadda zatai harta haɗa jallof ɗin taliya wadda aka baza mata kayan ƙamshi tare da na ɗanɗano ga uban kifi, Bebi tana zuba taliyar cikin fulas tana haɗiyar miyaun ƙwaɗayi harta gama, anan umman mufidan ta kuma ce mata tazo su haɗa mai lemon abarba tofa mai hali baya fasa halinsa seta tura baki gaba ta soma dira ƙafa kamar a gaban mama.
( *Wayyo Hannuna wallahi kamar ya cire dan Allah karku fitarmin da page ɗinnan bani da lafiya haka nake daurewa domin na kyautata muku dan Allah kuji tausayin marainiyar Allah* )
"Nifa wallahi anty nafisa na gaji duk uban wannan kifin shi kaɗai aka jibgawa komai shi komai shi nifa bazan haɗa mai wani lemo ba yaci haka".
Dariya anty nafisa tayi tana mata kallon ƙuruciya.
"To ina zuwa fitar da wannan kular anan sena gyara miki kicin ɗin, kaita can falonki naga shi base an share ba".
Ɗauka tayi fuska fall murna ta fice harda gudunta takai ta aje, cikin mintuna kaɗan maman mufida ta gyara kicin ɗin.
Kana tai saurin komawa gidanta ta ɗaukowa Bebin turarukansu na can ƙasar maiduguri masu sirrika na musamman.
A falon ta tarar da ita batada alamun ko motsi.
"Ah bebi tashi maza ki shiga wanka ga wannan turaren ki zuba a rikita oganmu sabida oga ya

gama mana komai Allah ya gani komai zamu mai baxamu biyashi ba".
Da taimakon maman mufidan ta shiga wanka tana fitowa ta kuma bata wata humra ƴar ƙarama tace mata ta shafa a ko'ina na jikinta, bayan ta shafa tace mata taje ɗaki ta shirya.
Wasu shegun ƙoɗaɗɗun kayanta na gida ta saka wanda seda umman mufida tai mata da gaske sannan ta koma ta ɗauko jakar kayan ta dire mata tana tura baki gaba.
Da kanta ta zaɓa mata wasu shegun riga da wando jajaye waɗanda jikinsu yake na karen miski.
Dama kayan a gumama ta taɓa siyosu lokacin an kwance a bayan layinsu to mama seta hanata sasu sabida yadda suka kame mata jikinta, shine ta ɓoye kayanta cikin ƙasan jakarta se yanzu da umman mufida ta ɗauko matasu.
"Ungo waɗannan ke waya gaya miki ana saka manyan kaya da daddare maza amsa kiyi ki shirya na gudu kar oga yazo ya ganni".
Dariya tayi tare da amsa haɗi da jakar tayi cikin ɗakinta.
Sabida  tsabar yadda kayan suka amsheta basu bata damar saka bra ba domin bata da muhalli a wajan sabida yadda kayan sukai mugun matseta wandon kwa da ƙyar ya shigeta sabida yadda hips ɗinta suka wani baje acikinsa daga baya kuma mazaunanta sukai wani irin tasawa daga saman rigar kwa baki ɗaya na shanunta sunyi wani irin ɓullutsowa kamar mai juna biyu.
Kallon kanta take sosai da hasken windon ɗakin seda ta sami mayafi ta yafa sannan ta iya fita.
"Wow ƴata amman fa kinyi kyau masha Allah yau akwai drama keda oga ungo wannan shafa a kunnen ki da tsakiyar kirjinki, da kowani saƙo na jikinki"
Ɗakin ta koma ta shafa azababban turaren wanda ya cika ɗakin gaba ɗaya.
"Yau ƴata bara na koma gida tunda komai ya kammala idan yaso gobe zan shigo na kuma gwada miki wasu abubuwan dan Allah kar aiwa oga musu"
Ɗaga kai tai tare dayi mata sallama ita dai ta bitane amman bata gane ko musun mai take nufi bama.
Umman mufida na fita itama ta koma ɗaki taɗan karkaɗe katifar ta gyaro ɗakin sannan ta sako hijabi tare da fita ta ɗauro alwala ta dawo ta xauna tana karanta azkar.
Amman tsorone fall ranta ga babu nepa ga kuma duhun magariba yasoma ƙaratowa.
Raɓewa tayi a saman sopa tana addu'a tare da neman tsarin Allah akan dukkan sharri gaba ɗaya mugun tsoro ya gama.cikata ga babu fitila gidan ga su mufida shuru.............

Basu sukaje kasuwar ba se wajan gaf da magariba sanin zezo yasa mai shagon da sukai magana dashi a waya ya dakata, Atare suka fito da shahid suka shiga cikin shagon da kayan masarufi ke jibge a bakinsa kamar zasuyi magana sabida yawa.....................
*ASHA WEEK END DA WANNAN*

Shiya soma shiga cikin shagon kafin shahid ya bi masa baya,Bakinsa ɗauke da sallama, da sauri mai shagon ya taso gami da basa kujerar ƙarfe ta zama, yana faman dashare mai haƙora.
"Ah yau muna da babban baƙo Alhaji Ali Mai atamfa,ne a shagon namu kai maza kuje ku siyo masu kayan sanyaya maƙoshi".
Mutumin da baze gasa shekarun Aliyun ba ke faɗin hakan wanda shine ma mallakin wannan shagon se yaransa dake ciki suna faman haɗa ledoji masu uban yawa.
Murmushi Aliyu ya saki yana mai ɗaga mai hannu.
"Haba mai shinkafa nifa ba baƙo bane wallahi ahanya nake ma, yawwa kayan abinci nakeso komai da komai seka saman mota ƙarama da zata ɗauka dan Allah kai sauri sekai min total na kuɗin kaimin msg ta watsapp zan maka sending ɗinsu ta account".
Yafaɗa yana mai duba agogon dake ɗaure bisa tsintsiyar hannunshi.
Cikin mintuna da bazasu gaza talatin ba mai shinkafa yadda naji Aliyun ya ambaci sunanshi ya shiga wani ɗaki wanda nake tunanin kamar store ne ya kira wani daga cikin yaransa suka soma fito da buhunan kayan abinci hatta su semo ba,a bari ba katan na indomie shinkafa taliya cous-cous da dukkan wasu kayan sarrafawa domin aci, Shidai shahid sakin baki yayi yana kallon ikon Allah lallai inda ake arziƙi ba,a tsiya, zama da mutumin arziki kuma akwai daɗi a rayuwa, wata ƙwallace tazo mai wadda bai bar kowa ya ganiba ya share kayarsa.
Cikin ƙanƙanin lokaci suka kammala dukkan haɗa kayan abincin daya buƙata aka samo irin ƙurƙurar motar nan ta ɗaukar kaya seda mai shinkafa ya zuba kayan ya biya drivern sannan ya dawo shagon.
Ya miƙawa Aliyu bill ɗin kuɗin dukka acikin wata ƴar takarda.
Sannan sukai musabaha kana ya bar shagon yana ce mai.
"Zakaga saƙo anjima insha Allah nagode"
Yafaɗa kana ya fita wajan motarsa ya koma inda ya adanata, ya buɗe irin ɗan akwatin nan na ajiyan cikin mota rafar ƴan dubu ɗaya ya fiddo dasu ya bawa shahid.
"Amsa ka kaiwa umma sekuyi cefane kaje ka zauna kusa da drivern waccan motar kuje gida tare, insha Allah wani satin kaima zanyi kokarin ganin na sama maka school kabar yawon nan na anguwa".
Dariya shahid yay "lah wallahi ban yawon unguwa gawayi nike saidawa fa tunda nai neco".
Murmushi yayi
"To masha Allah, shahid naji daɗin yadda kake neman na kanka baka tsaya ɗaukar na wani ko maula domin abaka ba, sabida dukkan waɗannan suna kawowa mutum ƙasƙanci da raini ka zauna ka nemi guminka  komai wuya kaji ƙanina nima ɗinnan daka ganni babu irin wuyar da mahaifinmu bai shaba kafin yazama haka harmu ma mu gajeshi ka ganni nan sena wuni tunanina yaɗauki zafi a office sabida tsabar lissafin shigar kayanmu da fitarsu da sarosu, kada ka yarda ka ɗauki na wani koka zauna cikin abokai marasa aikinyi sabida zama da mutanan banza shike kawo tunanin banza harma a aikata aikin banza kaji ko ƙanina".
Sosai shahid yaji daɗin nasihar da Aliyu yay masa sabida tunda yake baitaɓa zama da wanda ya zauna yay masa faɗa kamar haka ba.
"Nagode yaya Aliyu insha Allahu zanyi aiki da nasihar ka"
Buɗe motarshi yake ƙoƙarin yi sannan ya juyo.
"Zan duba takaddun naka zaka koma school insha Allahu tun yanzu zan sama maka aiki acikin kamfaninmu koda a ƙaramin section ne inyaso ranar da bakada lecture sekai tafiyar ka can

kuma duk wata zamuna baka salary".
Yafaɗa yana shigewa motarshi.
Shahid jiyai kamar ya zuba ruwa a ƙasa yasha sabida murna, dan haka da sauri ya juya motar kayan abincin nasu ya shiga nan da nan drivern ya kama hanyar kwatancen da shahid ɗin keyi masa suka ɗauki hnyar sharaɗa ɗoɗar mota fall kaya.
Kai tsaye motar su shahid a bakin layin gidansu ta dakata da taimakon matasan bakin layin aka soma fito da kayan ana, shigar dasu tsakar gidan mama waɗanda nan da nan mama da ƴan biyu sukai cirko cirko suna bin kayan da kallo cike da mamaki, sabida lokacin iya da sadiya sun tafi gida saka makon magaribar da aka soma kira.
Seda suka kammala aje komai hatta jaekokin mai, seda suka ajiye sannan mama ta shiga ɗakinta ta ɗauko gudar dubunta datai ragowa tai zuciyar dogarai ta bawa matansa tana musu godiya, shahid kam komawa yayi yaywa mai motar godiya sa'annan ya dawo gida.
"Masha Allah, Allah muna godiya gareka".
Cewar mama cike da farin ciki suke ɗiban kayan abincin suna shigar dasu ɗaki suka jera su a can karshen ɗaki sannan shahid ya zaro kuɗin da Aliyu ya basa ya miƙawa mama yana mata bayanin dukkan yadda sukai da Aliyun a kasuwa.
Mama dan murna kuka ta saka haka nan ƴan biyu suna yiwa Aliyu fatan nasara a rayuwarsa shiya soma taimaka musu acikin rayuwarsu tabbas Allah baze bar duk wanda ya share hawayen maraya ba, sakamakonsa babbane a wajan ubangiji,sallah sukai tare da saka Aliyu acikin addu'arsu sannan sukaiwa ƴar uwarsu fatan zaman lafiya agidanta.
"Shahid amsa wannan dubun kaje ka siyo mana kifi, hassana kunna gawayi ki ɗora mana dafa dukan taliya mai daddawa da kifi muma muci daɗinmu Allah ka ƙarawa annabi s.a.w daraja amin".
Sosai su arfa suka saka dariya suka miƙe ita da ihsan suna tsalle.
Mamace ta share hawayenta tana kallon ƴaƴan nata kana tace.
"Tabbas  ayau Allah kaɗai yasan ɗunbin ladan da wannan bawan Allah ya samu dukkan wanda ya saka ɗan uwansa musulmi cikin farin ciki yana da lada bare, kuma acikin zuciyar maraya wanda Allah kaɗai yasan adadin ladan daze bashi, ya Allah ina roƙonka daka sakawa da dukkan mai kyautatawa maraya da gidan aljanna firdausi amin".
Dukkansu suka amsa mata da amin, sannan hassana ta mike domin ƙaddamar da umarnin da mahaifiyar tasu ta bata shi kuma shahid ya fita.
"Hussaina muje cikin ɗaki na fitarwa da iya da gidan malam suma kayan abincin da kuɗin ki miƙa musu suma su dandali arziƙi"
Tashi sukai suka shiga cikin ɗaki.
********
Bai jima da barin kasuwarba yaji ana kiraye kirayen sallah sabida haka cikin sauri yay parking ya tsaya a wani masallacin gefen titi alwala ya ɗaura a bakin famfo kana ya shiga yabi sahun jam'i, seda ya gama lazuminshi kana ya fita zuwa mota seda ya biya ta magaji rumfa ya siyo musu wani nama wanda ake masa laƙani da suya, tare da kayan sanyi danginsu lemo da sauransu sannan ya zuba acikin mota ya kama hanyar tokarawa lokacin wajan ƙarfe takwas na dare.
Babu abinda yake buƙata a wannan lokacin kamar yajishi cikin ruwan ɗumi yasha yay wanka dashi, tafiyace mai azabar nisa yayita wadda bata kaishi can ɗinba se wajan taran dare, da

kansa ya sauka  daga cikin motar ya buɗe gate ɗin.
Cikin sauri goma dayaji ƙarar buɗe gate ya fito daga nasa part ɗin tare da hasko wajan da tourch light sabida lokacin basu rufe gidanma saka makon ragowar jama'ar gidan basu gama shigowa ba.
"Au oga ashe kaine barka da shigowa yaya dare?".
"Ina zuwa goma just give  me a two minutes"
Yafaɗa yana komawa da baya yaje ya shigo da motar ya gyara mata zama a driving in ɗin gidan kana ya kasheta ya fito hannunshi dauke da kular dambun mama da kuma babbar ledar dayay musu siyayya a magaji rumfa.
Ƙarasowa yay gaban goma ya basa hannu suka gaisa.
"Ka gannifa goma se yanzu na sami damar shigowa, amman yanaga gidan babu wutar lantarki?".
Sosai kai goma yayi.
"Wallahi oga basu bamu nepa yau ba, amman gobe zan saka a kawo mana gen kodan madam amman mukam bama kunnawa sabida ana samun nepa sosai".
Murmushi kawai yay kana yace.
"A daure a haɗa kam komai ka sanar min,ya maganar kayan nan daza'a kawo mana Jibi? amman zuwa gobe zamuyi magana".
Murmushi shima goma yayi sannan yace mai.
"Allah ya kaimu lafiya oga ai babu matsala na rigama na tura musu samfir ɗin da muke so da kuma adadin dilar amman kayan naji yace ta cikin jirgin ruwa zasu zo mana".
"Okey babu matsala Allah ya shigo mana dasu lafiya kasan na narka dukiyata cikifa".
"Amin oga Allah ya tashemu lafiya".
Sukai sallama kowa ya nufi nasa part ɗin.
Key ya saka ya buɗe kofar gidan, wanda seda ya haska da fitilar wayarshi kafin ya sami zarafin ganin hanyarshi sabida tsabar duhun dake da akwai a gidan.
Kafin kuma ya juya ya rufo gidan da key ya xare ya shiga cikin tsakar gidan wanda babu komai na sauti dake tashi face na kukan ƙwaron nan gyare.
Da taimakon fitilar wayarshi ya haska kofar ɗakin ya buɗe labule ya shiga bakinsa dauke da sallama seda ya aje kayan hannunshi duka a waje ɗaya sannan ya saka hasken wayarshi yana, haska ko ina bai ganta ba,seda ya haska can saman sopa sannan ya hango ta kwance da alamun tayi bacci duk ta cure cikin hijabi kana kallonta kasan acikin alhinin tsoro tai wannan bacci.
Cikin yanayin tausaya mata ya ƙarasa gabanta ya saka hannu yaja yatsarta na ƙafa.
Aikwa da sauri tai wata irin hantsilowa wadda bata dire a ko ina ba se a saman faffaɗan kirjinshi daddagewa tayi zata zunduma mai ihu fahimtar hakan yasa ya yarda wayarshi mai uban tsada a ƙasan carpet kana ya riƙota sosai bisa jikinshi.
Ya matseta acikin kirjinta yana faman hura mata iskar cikin bakinshi.
"Shiiiiii matsoraciya nine Aliyu"
Yafaɗa yana daɗa matseta ajikinsa.
Zamewa tayi daga riƙon dayay mata sabida aciki take dashi
"To naji nika saken mana".
Tafaɗa tana fincike jikinta.

Ɗaukar wayarshi yayi tare da ɗorata a saman sopa wadda ta bawa ɗakin damar karaɗewa da haske.
Cikin miskilancin sa ya shareta gami da wucewa cikin ɗakin batare daya kuma tanka mata ba.
Komawa tai saman sopa ta harɗe tana huro mai hanci.
Mintuna kusan biyar ya ɗauka a ɗakin kafin ya fito jikinsa sanye da ɗan guntun wando, Taɓɓ abinda baita ɓayi ba kenan a gaban wani.
Wuceta yayi ya fita toilet yaje babu tsoro aranshi ya sakarma kansa ruwan ɗumi sannan ya ɗauro alwala ya fito.
Tsuka yaja sabida babu extra kayansa agidan dole tasa ya mayar da kayansa dayazo dasu.
Falon ya dawo hannunshi ɗauke da darduma ya shinfiɗa wanda adai dai nan akwa kawo nepa haske da iskar fanka suka haska falon tarwai.
Babu alamun sassauci a saman fuskarsa ya dubeta.
"Kinyi sallah, idan bakiyi ba jeki ɗauro alwala sena jamu jam'i nima banyi ba nai missing ɗinta"
Se lokacin ta ɗago da kanta ta dubeshi sabida da tunda taga ya fito da wannan shegen wando tai ƙasa da kanta ganin ya sako kayan mutane yasa ta dubeshi sosai aranta tana yaba kyawun halittarshi babu abinda yake fisgar hankalinta gareshi face tafkeken tabon abin sallar dake saman goshinsa wanda yay baƙiƙƙirin yay siɗik.
"Idan kin gama karemin kallon kije ki alwala domin kinyi dogon bacci nasan bakida alwala yanzu".
Tura mai bakinta tai gaba.
"Wallahi ni bazan fita ba wani abun ya saran a waje"
Kallonta yay yana mai hawa saman dardumar daya shinfiɗa musu.
"Niba uwa ce ta haifan ba kenan kece ƴa ko, niba yanzu kikaga naje nai wanka ba mai ya cini, malama ki tashi kije kiyi alwala kizo muyi sallah"
Gani yadda ya zaro mata fitinannun idanunsa masu saka yara jin magana yasa ta mike har jikinta yana rawa ta fita se lokacin ta saki ajiyar zuciya sabida ganin ashe da akwai haske a tsakar gidan na farin ƙwan lantarki.
Bayin ta shiga ta kama ruwa kana tai brush sannan ta ɗauro alwala.
Lokacin data shiga ɗakin harya miƙe tsaye dan haka bayanshi tabi sabida daman da hijabinta ajikinta, sallar isha'i yajasu bayan sun ida ya kuma miƙewa anan wata nafilar ya kuma jansu raka'a biyu.
Bayan sun idar ya juyo gabanta ya dafa kanta sosai taji yana karanto addu'oi waɗanda yaja manyan lokuta yana yinsu, ya gama ya saki kan nata kana suka shafa atare.
"Allah yay miki albarka, Allah yasawa zaman aurena dake albarka, Allah yasa kizaman mace tagari mahaɗin cigaban arzikina, Allah ya bamu zuri'a masu albarka Allahumma Amin"
Yafaɗa yana mai tashi daga saman sallayar ya shige ɗaki, ninke abin sallar tai ta aje batare data tuɓe hijabinta ba, ta koma can ƙasan carpet ta zauna.
Jim kaɗan ya dawo falon hannunshi riƙe da wayarshi jikinshi babu riga gaba ɗaya zubin tsarin baiwar halittarshi a bayyane take, saka makon babu komai ajikin nashi se wannan guntun wandon na ɗazu manyan ƙirarshi ta cikakken ɗa namiji a bayyane take babu abinda ya kuma fisgar hankalinta gareshi face kwantacciyar sumar data lulluɓe masa kirjinsa har zuwa wajan ƙasan mararshi daga sama kuma ta zagaye nippy ɗinshi waɗanda suka tasa sukai wani irin cikowa a ƙoshe.

Ƙasa tai da kanta har sanda ya tako ya zauna a gefenta ya miƙe ƙafafunsa.
"Babu Tv bare kiyi kallo kona baki wayata amman fa ni bana aje komai a wayata seki shiga youtube kiyi kallo ze rage miki zaman sabida ni zanyi aiki da system ɗina amman kafin nan zanci abinci tukunna"
Cikin mutuwar jiki ta miƙe taje gaban kayan abincin ta ɗebo masa duka tazo gabanshi ta aje.
Ta miƙe taje kicin ta wanko plate da spoon ta aje mai, ta kuma fita taje kicin ɗin still karamin frij ɗin da goma ya shigo musu dashi ɗazu ta bude ta ɗauko drinks tazo mai dasu da kanta ta zuba mai taliyar a plate tana mai cewa.
"Ga abincin ka kaci"
"Nagode bana cin abinci da zafi ina zuwa".
Ya koma ɗaki ya ɗauko rigar shaddarshi ya zira kana ya fita motarshi yaje ya ɗauko system ɗinshi kana ya dawo ya kuma rufe gidan.
Yadda ya barta haka yazo ya sameta seda ya kuma rage rigarshi sannan ya dawo ya zauna.
Ɗaukar spoon ɗin dake cikin taliyar yay kana ya saka system ɗinshi a saman cinyarshi yana operating ɗinta cike da nutsuwa.
"Ɗauko kular can da ledar can seki duba akwai dambu ciki inza kici"
Da azama ta mike taje gaban ledar ta ɗaukosu duka tazo ta aje daman yunwar takeji ga abincin iya cikinsa akai masa.
Fita tayi ta ɗauko plate tazo ta zuba sannan ta buɗe ledar data gani ta fitar da komai na ciki wanda zata adana takai kicin cikin frij kamar yadda maman mufida tai mata lecture ɗazu sannan tazo ta kasa musu ɗayan ƙullin nama ta zuba masa itama ta zuba.
Lomar farko na dambu ya bata tabbacin na mamanta ne amman rashin sakin fuskar da bai mata ba yasa taja bakinta tai gumm tana zuba lomarta.
"Bana cin abu mai nauyi da daddare koze kai safiya seki ɗumama min kasona kinsan ina matukar son dambu".
Bata tanka masa ba tacigaba da tura zallar tsokar namanta cikin bakinta tana wani irin lumshe idanu.
Mayar da hankalinshi yayi bisa kan taliyar tare dayin bisimillah ya soma ci anutse kuma babu laifi yaji matuƙar daɗin girkin hadɗi da mamakin daman haka ta iya haɗa girki dama kamar kuma tasan yana matukar mugun son taliya acikin dukkan kayan abinci.
Bakajin komai acikin falon se ƙarar cokulansu harta kammale dambunta ta haɗe kayan takai kicin nasa kuma ta tura cikin frij sannan ta wanko bakinta ta dawo ɗakin.
Har lokacin yanacin taliyar wadda ko rabi bai kai ba.
"Pls kozaki dafa min black tea amman da sugar ɗinshi zakimin one cup"
Bata musa mai ba ta miƙe.
"Ummeee zonan"
Taji ya kirata
Dawowa tai gabansa ta zauna.
Haɗe ranshi yay tamau ya dubeta
"Daga yau kana na kuma miki magana kimin shuru domin mu wannan a tarbiyar gidanmu raini ne ga mutum"
Jikinta ne yay sanyi sabida ta fuskanci kamar magana ya dunƙule ya jefa mata.
"Kayi hakuri bazan kuma ba"

Tafaɗa muryarta tana rawa kamar zatai mai kuka!
"Yafi miki, domin ni ba sakaran miji bane bazan ɗauki rashin daraja ba, and kuma ki tafi da taliyarki ki rufeta da safe a bawa wani domin ni ba,a zubda abinci agidana danni ba almubazzari bane"
Kallonshi tayi cikin wani irin yanayi marar misaltuwa.
Ta kafe mai idanu kurr tana kallonshi.
"Bazaka ci abincin ba sabida na ɓata maka rai, amman kasan shayi kaɗai baze ƙosar da kaiba,ko naman ma baka ciba nidai dan Allah idan dan nice yasa kaƙi cin abincinka kaiwa girman Allah kaci wallahi bazan kuma maka laifi ba domin yunwar dare illah ce"
Kallonta yay kaɗan hankalinsa yana kan system ɗinshi.
"Cikinki ko cikina?"
Kuka! ta samai kamar wata karamar yarinya.
"Amman dai ammi ta bani amanarka nidai kacinye abincin nan".
Maganarta ta jefashi cikin rabewar tunani ƙwaƙwalwar kanshi ta shiga serching idan ya fuskanta dai dai kenan Wannan yarinyar tafi damuwa dashi akan dija.
Yakan ɓata lokaci agidansa batare daya ci abincin da dija taimai mai yawa ba, amma daya miƙe domin fita bazata ko damu da rashin cin abincin dabai ba, bakuma zata nuna ɓacin ranta akai ba sedai ta tattare ta fitar da kayanta ɓacin ranta a rashin bata kulawar kwanciya kawai yake ganinshi wanda ya fuskanci ita dai burinta acita shine matsalarta, Numfasawa yay ya dubeta har lokacin tana faman kukan baici abinci ba.
Sassauta muryarshi yayi tai ƙasa sosai cike da rarrashinta yace.
"Kimin shuru zanci amman bar tea ɗin"
Goge hawayenta tai ta koma ta zauna tana kallon yadda yakecin abincin da zafi zafinsa.
Wayarshi dake gefenshi ita ta soma ƙara alamun kira.
Ɗauka yay duk hankalinshi yana kan system ɗinshi da kuma abincin gabanshi daya kusan cinyewa.
Ɗagawa yay ya kara a kunnenshi.
"Hellow dija"
Da sauri Bebi ta ɗago ta zuba mai idanu kirjinta yana bada sautin dum!dum!!dumm!!! wanda ta rasa gane dalilin hakan.
"Sorry dare yayi se gobe, Okey take care Bye"
Ya katse wayar yana mai ɗagowa yana kallonta.
Ƙatuwar harara ta zabga mai tare da tashi fuww tabar mai wajan tai ɗaki tare da kife kanta a katifa tana kuka! sabida Bebi tana ɗaya daga cikin jerin mata masu ɗan banzan kishi ayau ta soma zama dashi amman ayau ɗin takejin kishin dukkan wata macen dazata raɓesa da sunan so duk da ita batai tabbacin zuciyarta kota aminta dashi ɗin ba amman dai taji tana masa wani irin mahaukacin kishi.
Ko talle ta fitarwa mama ada bata kwantai sabida tana kishin taga wasu sun sayar su nasu yana ƙasa, haka nan  makaranta bata yarda wata ta fita setai iya kokarin ganin taci gaba kamar kowa tana da matukar kishin kanta kuma tasan darajar kanta agabanta ya zauna yana ambatar wata dija.
Cikin sauri shima ya kashe system ɗin ya ɗauke plate ɗin yakai kicin sannan yay brush tare da komawa ya kashe wutar falon yay cikin bedroom ɗin yana ƙunshe dariya wato tun ba,aje ko

inaba yarinyar can ta soma kishin sa lallai akwai jan aiki agabanshi.
Hayewa yay saman katifar tare da birkitota zuwa jikinsa cikin sauri ya tube mata hijabin.
Haɗe ranshi yayi tare da ce mata.
"Tashi kije ki kashe mana ƙwai"
Tashi tayi tana share hawayen ta, kana ta nufi gaban makashin ƙwan ɗakin.
Tsirawa bayan ta idanu yay yana haɗiyar miyau gaba ɗaya tsigar jikinsa ta mike matse ƙafafunshi yake yana janyo numfashi da ƙyar lallai Allah ya zuba sura anan gaba ɗaya ta gama kunce masa notikan kanshi ashe haka tai wannan mugun kyau ɗin amman tawani saka mai hijabi lallai yarinyar nan akwaita, daman su waɗannan kayan daɗin ba,a shekaru suke ba a halitta suke domin ga dija nan bata da komai.
Bai jira ta ƙaraso ba yasaka hannu ya janyota ta faɗo mai saman ruwan cikinsa ya bata maxauni a saman kirjinsa ya kwantar ta hannunshi duka ya zuba a tudun mazaunanta yana matsasu yana wani irin miƙa, cikin zafin nama yake sabule mata kayan jikinta katari da cikakkun na shanunta ya kuma sumar dashi na wucin gadi kafin ya kamasu a rikice yana sarrafasu cikin haɗama, gaba ɗaya ya gama dagula mata lissafi da birkitaccen salonsa mai tsayawa acikin rai, ta riga ta sakar masa ragamarta sabida azababban shauƙin daɗin data nutsa ciki.
Bakinta ya lalubo ya haɗe dana sa hannunshi yana zube a kirjinta yana cigaba da yamutsa matasu, wani ɗan zafi-zafi takeji kasancewarta farin shiga a harkar,Shikam gaba ɗaya ya shiga ruɗu yariga da ya fita acikin hayyacinshi babu abinda ke fita a ɗakin se nishinsu zare bakinshi yay ya mayarshi saman wuyanta yana bata sumba ta musamman daga nan ya gangaro har saman kirjinta ya ɗauke hannunsa akansu ya maye gurbi da bakinsa yana wasa da nippy ɗinta waɗanda basu gama tasawa ba, a wannan karon Bebi kuka ta saka masa tana masa wata irin miƙar daɗi ajikinsa sakamakon bakon yanayin datakejin kanta cikinshi, Rumfa yay mata da faffaɗan kirjinshi kamar ba Aliyu uban miskilanciba haka ya ware girmanshi akan ƴar yarinya yana zuba romancing adukkan sassan jikinta, gaba ɗayansu sun fita daga hayyacinsu, kowanne kokari yake ya faranta ran ɗan uwanshi musamman Shida yafi birkita'ta da salonshi,Seda ya kaita maƙurar karshen daɗi a fagen kogin soyayyarshi mai tsayawa arai wanda yay mata sarƙa da ita wadda ya jiyar da ita daɗin manta kanki sannan ya ɗagota ya ɗorata a ƙasanshi idanunshi a lumshe yana kallon nata idanun waɗanda suka jiƙe da ruwan hawaye bakinsa yakai tare da fito da harshenshi yana shanye hawayen nata, kafin ya soma kissing wuyanta yana laso fatar kunnenta harya gangara saman bakinta ya kafe nasa acikinsa.
Sannu a hankali ya saka hannunshi ya ɗago mata west ɗinta addu'ar saduwa da iyali ya soma karantawa a nutse wanda ganin haka yasa na tattare takarduna domin anty ruƙayya akawu ta hanani gano muku sirrin mai girma Aliyu mijin Bebi.
Bankoma ɗakinsu ba seda aka kira sallar asubahi.
Wanda kallo ɗaya naiwa Aliyu nasan yaci kukan daɗi ajiyan harya gaji domin ga idanunshi nan sunyi wani jajur sun kumbura, Zaune yake agefenta magana yake mata ƙasa ƙasa ita kuma ta kife kanta tana masa kuka kamar ƴar Beby naga ya ɗagata ya nufi tsakar gida da ita, haɗa musu ruwan ɗumi yayi yay mata gashi sosai sannan ya naɗota ya dawo falo ya ajeta ahankali.
Ya koma ɗakin ya ɗauko Bedshit ya fita mintuna kaɗan ya tsabtace ko ina sannan ya kuma haɗa mata ruwan wankan tsarki, wanda da taimakonshi tayi wankan domin jiyan bai je mata da sauƙiba seda ya fitar mata da dukkan wani nauyin dake mararshi na tsayin shekaru sannan ya barta shiyasa yake yaba ƙwazon yarinyar domin juriyar datai mai ko babbar mace bazata mai

hakan ba, sosai ya jinjina mata sabida tagama jiyar dashi dukka wani dadi a aure, yaji ni'ima wadda bai samu a darenshi na farko ba, da taimakonshi ta saka kayanta ya mayarta saman katifa ya kwantar sabida yaji jikinta akwai zafi.
Se lokacin shima ya sami damar gyara nasa jikin sannan yay alwala yay nafila kafin ashiga masallaci adaddafe ya idar da sallar ya tube kayanshi ya kwanta.
Yana mai rungometa sabida zazzafan zazzaɓin daya rufeshi ruff.
Itako Bebi tun daren jiya data tantance shinkafa ƴar hausa da ƴar gwamnati jikinta yagama sanyi gaba ɗaya wata nutsuwa ce take shigarta tabbas iya wuya jiya tasha daman haka auren yake lallai mata na kokari hatta miyaun bakinta seda ya ƙafe kuka kam tayi sa har babu hawaye a idanunta.
Tanajinsa yana mata kuka shima amman dan azaba bai ɗaga mata ƙafaba  haka yayta budirinshi a jikinta shiyasa ko yanzu ma dataji yazo ya rungumeta tsorone ya cikata domin ita kaɗai tasan abinda takeji a ƙasanta, ganin yana fitar da numfashi ya bata tabbacin yay bacci dan haka itama ta juya tana rintse idanun azaba babu jimawa baccin itama yay gaba da ita.
***********
Tunda aka ɗauki ladi a motar gidansu khalifa take raba idanu tana zuba murna yaushe tana ganin wannan daɗin da daular zata tsaya biyewa mahaifanta sumata saki na dafe(kuji fa) ahaka motocin suka ɗauki hanyar gidan Alhaji mai gwall kai tsaye ɗauke da amarya ladi a bayan mota.................

*92*

*wayyo masoyi dadi wai wasu cewa suke karna gama book ɗinnan sabida daɗinsa amman naji daɗin wannan kalami naku sabida soyayyata ce tasa kuke faɗin haka, to ina  mai muku albishir da cewa wanda zezo gaba seyafi wannan dadi da izinin Allahu, fatana Allah ya bani ikon kammala wannan book cikin amincinsa da yardarsa amin summa amin*

Lokacin da drivern gidan alhaji mai gwall ya shigar da hancin motarshi cikin katafaren gidan ladi seda ta kusan zautuwa sabida tsabar yadda taga gidan yay mugun tafiya da tunaninta setace ma tunda tazo duniya bata, taɓa ganin gida mai mugun kyawu kamarshi ba.
Harar gefenta tayi tamkar wani na ganinta kana ta furta.
"Tabbijan daman Irin wannan gidan zan shigo amman su baba suke min buƙulu, Ai wallahi ninaga gida bazan tafi ko ina ba".
Tafaɗa tana shafo glass ɗin window ɗin motar tana wani da share bakinta kamar sakarya.
Har drivern yay parking ladi bata saniba tana can tana faman surutai ita kaɗai kamar sabuwar kammun ciwon sanyi.
"To malama munfa iso sabida haka seki sauko na nuna maki ɓarin da zaki shiga"
Dambe ta somayi da marufin motar tana kiciniyar budewa ganin zata masu ɓarna yasa drivern

ya buɗe mata marufin side ɗin nata kana ya bata hanya.
Da taimakon drivern Alhajin ta sami damar gane ɓangaren mutan gidan dazata je.
Sallama tayi a babban falon wanda yake dauke da dukkan ilahirin mutan gidan domin hatta ango khaleepha ma ba,a barsa a baya ba.
Bayyanarta a tsakiyar falon yasa khaleepha ya daka mata tsawa!
"Ke wawuya ubanwa ya shigo dake cikin wannan falon? ba'a gaya miki iya ma mallakan gidan ne kaɗai keda ikon shigowa cikinshi ba?".
Yafaɗa yana mai tsareta da fitinannun idanunshi waɗanda suka juye da tsabar tsagerancin ranshin ta ido.
Jikinta ne ya hau dukan tara! tara!! nan da nan ƴar nutsuwar dake gareta ta gudu kokarin fita take daga falon amman ga mamakinta iyayen shi babu wanda ya tanka ta.
Seda takai har bakin falon tana kokarin fita ta kumajin dirin amon! muryarshi acikin dodon kunnenta.
"Ke! Zonan"
Jiki na faman rawa ta nufesu ta zauna zaman ƴan bori agabansu sabida tsabar tsoron daya mamayeta.
"Uban ya kawoki nan? ba,a ce muku kuna zama a wajanku na masu aiki ba shegiya da fuskarki kamar anyi ɓarin garin tuwon doya zaki zomana nan salon ki tayar mana da zuciya?".
Raba idanuwanta ta somayi tana kukan zuci tana jinjina rashin mutuncinsa aranta tana jin ciwon yadda mahaifansa sukai burus dashi yana faman cin mutuncinta.
"Idan na kuma maki magana senaci......"
Bata bari ya ƙarasa ba ta soma magana.
"Dama....dama....nice wadda babana ya ɗaura mana aure..."
Takai tana sada kanta a ƙasa.
"What! ya miƙe yana huci,"haba dakus ta yaya xaku auromin wannan kidahumar yarinyar idan har domin ka hucemin zuciyata ka auromin ita wallahi baxan zauna da itaba"
Yafaɗa yana kokarin taɓe bakinshi kamar ƙaramin yaro.
Kamosa mahaifin nashi yayi ya kwantarshi saman kafaɗunshi.
"Haba my happiness ka kwantar da hankalinka sabida kasan tashin hankalinka nawa ne duk duniya kai ɗaya na mallaka namiji babu abinda zaka nema na gaza yi maka shi sabida haka yanzu ka saketa seka zaɓomin duk wadda kakeso nikuma zan aura maka ita kaji nawan"
Yafaɗa cikin rarrashi haka nan sauran ƙannenshi na falon da mahaifiyarshi suka amshe suna basa baki.
"Ni ai dakus tunda ka rabani da larabawana kayarda suka aurar ta wallahi abba nagama soyayya dan haka wannan ma senai mata kaca kaca sannan na saketa domin bazan zauna da itaba"
Yana gama faɗin haka yaja ladi kamar kayan wanki yay wata hanya da ita kuma babu wanda yace masa tak.
Babu sallah bare addu'a bare asaka ran ɗan wasan ma'aurata haka ya afka mata kamar dabba, yahau yin yadda yaso da ita.
Sosai ya gwadawa ladi rashin imanin da dukkan mai hankali da tunani yagani baze ƙi magana ba, seda ya farkata ya watsata yay mata cin kaci uwar mai ƙarya sannan ya tsallake yabarta ko hannu bata iya ɗagawa, abunda yaywa ladi ko fyaɗe albarka haka gadon yagama jikewa da

ruwan jini kamar an yanka dabba.
Ya nufi ɗayan ɗakin ya wanke jikinshi tass ya gyara kansa kamar babu gobe bai kuma ƙarabi takan ladi ba ya ɗauki makullin motarshi ya wuce club rai fess.
Babu wanda ya ƙara bi takan ladi agidan har aka kwana aka wuni seda masu gyaran part ɗin sukaje gyarawa sannan sukaga ladi kamar gawa da gudu sukaje suka sanar da hajiya matar gidan.
Amman ga mamakinsu setace aje a sanar da driver ya ɗauketa ya kaita gidan ubanta.
Babu tausayin na ƙasa bare imani babu tunanin komai haka aka naɗe ladi cikin bayan mota aka wuce da gida gidansu sabida su gidansu khalifa suna gadarar da sunada kudi ko kashe mutum sukai sun kashe banza tunda ayanzu kudi sune gaba da ƴanci.
Lokacin da motar tai parking a ƙofar gidan duk su kawu rabi'u suna waje a zazzaune ganin tsaleliyar mota fake a kofar gidan yasa dukkansu suka tashi tsaye cike da ƙwaɗayi sukai wajan motar.
Drivern shiya fito ya samesu ya ƙaddamar musu da abinda ke akwai cikin ruɗu sukai bayan motar suka bude ganin halinda ladi take ciki yayi mugun ɗagansu hankali domin kuwa acikinsu harda masu kuka musamman ƴan ɗakinsu tasi'u, haɗakar ɗaukarta sukai sukayi cikin gida da ita ganin haka yasa sauran matasan ƴaƴansu da suka rage wajan suka sakawa motar dutsina kafin kwabo sunyi uwar watsi da glasan windown motar.
Cikin tsoron cin mutuncin khalifa drivern ya ɗaga waya yake sanar da alhaji halin da ake ciki.
"What? suka fasan mota sun san irin kudin dana kashe kafin a siyeta lallai yau senaci uwar duk wani dake cikin gidan sena nuna musu tazarar datake tsakanin talaka da mai kuɗi yau zan nuna musu izzar kuɗi kai zaman ka anan ina zuwa".
Drivern zama yayi a gefe ya haɗa tagumi komai ya tsaya mai cakk yana kallon ƙudurirar Allah.

A tsakar gida suka direta kawu tasi'u kwa komai daman tsaya mai yay cak yazama baya iya taɓuka komai se binsu da idanu jiya aka fita da yarinyar nan lafiyar Allah amman jibi cin zarafin da sukai mata kana aka bita da saki har uku rak!
Babar ladi kwa zaman ƴan bori tayi tare da sauran matan suna faman koke-koke seda inna suwaiba kanwarsu tasi'un tace.
"Tunda tana da rai baici ku zauna kuna koke kokeba mu dauketa mukaita asibiti ai mata ɗinki amman wannan ɗa anyi tsinan ne matsiyaci baƙin kadara" ta faɗa tana face majina.

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payement domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*
***************
Jin ƙarar jiniyar motar ƴan sanda data cika layin ita ta saka mutan gidan dake ɗimauce wa, ahaukace ƴan sandan da alhaji mai gwall yayo haya akan suzo su kwashe mazan gidan wai akan sun fasa masa mota suka diro suka fito da taimakon drivern suka sami damar kiran su kawu tasi'u daga cikin gidan wanda zuwa lokacin mutan anguwar har sun soma fitowa suna kallo ikon Allah duka da kulki suka dinga dukan su kawu tasi'u kamar ɓarayi suka sakasu a mota suka wuce dasu hatta samarin gidan basu bari ba matan kaɗai aka bari suna sabon kukan bakin cikin kame mazajen sun da akai.
Lallai yau sunga ƙarshen kaskanci aiwa ƴarsu wannan cin zarafi sannan azo a kwashesu agidajen su kamar awakai lallai mai kuɗi se abarshi.
Da ƙyar inna suwaiba ta sami napep yazo aka tarairayi ladi aka sakata sukai asibiti koda sukaje asibitin ma kin amsar su akai wai seda ɗan sanda seda aka kai ruwa rana sannan aka ɗauki ladi aka nufi emergency word  da ita.
Inna suwaiba kuka da sauran matan da suka rakosu can kwa gida an bar wasu suna kukan ɗiban mazajensu da akai.
Tabbas duk rashin tausayin ka idan ka dubi mutan gidan nan aranar seka koka sabida ishara Allah ya nuna musu ta xahiri domin kamar yadda su kawu tasi'u suka taɓa yima baban bebi korar tujara agidan yau to haka ƴan sandan nan sukai musu kamun tujara kamar na ƴan fashi. Kuma kaf makota an rasa wanda ze bisu can wajan ƴan sanda sabida halinsu na tsiya da rashin son zaman lafiya da maƙotansu.
A can caji office ɗin kwa sosai aka bawa su kawu tasi'u kashi aka zanesu sosai domin magana alhaji ya sauya akan wai tare drivern sa sukai zasu karɓe masa mota akan ya hanasu sukai masa taron dangi suka fashe motar kana ya ɗora musu da maƙudan kuɗi sabida haka da kotu ma za,a kai maganar amman se alhajin ya hana sabida yana gudun kada magana tai nisa human right ta shiga asoma bincike daga karshe reshe ya juye da mujiya,dan haka ya bawa

ƴan sandan umarni sukaiwa su baba tasi'u shegen duka kana suka korosu tsakar dare haka kowannen su yazo gida jiki fashe.
Shikam baba tasi'u yay nadamar kwaɗayinshi ba kaɗan ba lallai kwaɗayi mabuɗin wahala inji bahaushe sannan kuma ita magunta fitsarin faƙo ce shiyasa idan zaka gina ramin mugunta to ka gina dai dai tsayinka.
Adaren ya koma asibiti duk jikinshi a fashe sukwa su rabi'u kin binsa sukai sema la'antar sa dasuke famanyi domin sun san bada ban shiba da babu abinda ze saka su daku.

Acan asibiti kwa wata nurse ce ta fito da farar takarda ta mikowa babar ladi.
"Zaki sayo mata allura ta dubu ashirin wadda za,a kashe zafin wurin kafin ai mata ɗinki domin idan ba,a mata ba zata kamu ne da cutar yoyon fitsari sabida anyi mata fyaɗen bana wasa ba"
Hawaye ta share kana ta amshi takardar daman da kuɗinta na adashi a ƙugunta dan haka taje ta siyo ta kawo.
Dayake asibitin kudine nan da nan aka soma gabatar da ɗinkin ladi wanda seda aka share manyan awowi anayi domin har kawu tasi'u yazo ba,a fito da itaba.
Se wajan 12 na dare sannan likitan ya fito nurses suna bayansa.
seda yaje office sannan ya aika aka kira mai baba tasi'u wanda cikin sauri ya nufi office ɗin.
Likitan ya basa wajan zama sannan suka gaisa.
"Malam kaine mahaifin waccan baiwar Allah'n ko? ok daman abinda yasa na kiraka shine, a tsarin asibitin nan bama karɓar mutum seme file anan amman ganin yadda matarka ke kuka da kuma halin da ƴarka ke ciki yasa muka amsheta, sabida haka ga takarda nan zakai mana bill na naira dubu ɗari uku da hamsin, kuɗin file kuɗin gado da magunguna tare da allurai"
ya mika masa takardar yana mai umartarsa da ze iya tafiya
Tashi yay ya fita jiki babu laka wani tashin hankali na fisgarshi ina yaga waɗannan maƙudan kuɗin? ta ina ze soma.
"Innalillahi wa'inna ilaihirraju'un, ni tasi'u ina zan sami waɗannan kudin nashiga uku".
Yafaɗa yana mai zubewa a wajan yana sakin kuka!.
***************
Sunjima suna barci wanda harya kaisu ga makara a sallar asubahi ita Bebi gajiya Aliyu kuma zazzaɓi..........

*93*

Bakinshi ɗauke da salati ya soma buɗe manyan idanunshi ganin hasken rana ata windown ɗakinsu yasa ya miƙe a firgice.
"A'uzubillahi minash shaiɗanirrajim"!
Yafaɗa da sauri tare da zareta ajikinshi miƙa ya kumayi da sauri kana ya miƙe tsaye duk da bayajin daɗi sosai amman hakan bai hanashi fita da sauri zuwa tsakar gida ba, kama ruwa yayi tare da ɗauro alwala kana ya dawo falon, kayanshi na jiya ya ɗauka ya mayar tare da tayar da

sallah yana mai nadamar makarar dayay a sallar asubahin yau abinda bai taɓa faruwa dashi ba tunda yake a duniya.
*****************

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*# *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*
**********************
Koda ya idar da sallar ya jima yana lazimin istigifari neman gafarar ubangijinmu kafin ya soma karatun azkar yana gamawa, ya mike daga saman abin sallar'n yana mai cije bakinsa alamun bayajin daɗin jikin nashi sosai.
Wayarshi ya kunna tare da shiga inbox ya rubutawa goma msg, akan yaje ya siyo masa jallabiyar's and boxer's sabida shi baze iya mayar da kayan jikinshi ya fita ba sabida tun jiya suke abinda bai taɓa faruwa dashi ba kenan ko yanzu ma daya saka dan dai sabida baya da wasune amman da bayajin ze iya mayar dasu.
Da ƙyar yaja ƙafafunshi ya koma cikin ɗakin still tana kwancen dai kamar yadda ya barta.
Hayewa yayi saman katifar tare da kanainayota jikinshi ya ɗorata a saman cinyarshi.
Baccinta take sosai fuskarta tayi wani irin jajur idanunta ya kumfura na alamun kuka! juyawa

tayi tare da saƙalo wuyanshi da hannunta tana tura mai baki batare data sani ba.
Murmushi ya tsinci kanshi dayi, yana mai gyara mata kwanciyar datai a cikin jikin nashi.
A fili yake furta maganar dake ranshi wadda baya zaton zataji sabida baccin ta dake faman yi.
"Ina matuƙar sonki nana bilkisu, kin sace zuciyata tun daren dana ganki agidanku na kasa nutsuwa na kasa zama akanki, bayan na fidda rai da sake ganinki kwatsam Allah ya kuma haɗani dake a kamfani wanda ranar dana ganki a wajan talle seda nai kukan da tunda ammi ta haifeni ban taɓa yinshi ba, tabbas ina matuƙar sonki Ummeenah Nuriynah fulanitah, tabbas na yarda dik abinda yake rabonka seka sameshi komai nisan dayay maka, bayan na fidda rai da samunki se Allah ya dubani ya kawon ke cikin sauki dukkan abinda naiwa usman tsabar murna ce amman banajin nayi baƙincin aurenki Sugar nah zumanah, Allah ya barmin ke yasa a daren jiya nai ajiya a mararki, ina sonki banajin da abinda ze iya rabani dake har ƙarshen numfashina akanki nabar dukkan Ahalina nazo nan domin na rayu dake farincikina"
Yafaɗa muryarshi na rawa idanunshi na cikowa da zazzafan hawayen ƙaunarta.
Ɗagota yayi tare da kwantar ta sosai ajikinshi kamar mai tsoron wani abun karya taɓa mai ita, ya soma ƙasa da kanshi harya kaisa dai dai saman fuskarta.
Sassanyar iskar cikin bakinshi ya soma hura mata acikin fuskar tata yana mai ziro harshenshi yana lasar tsakiyar idanunta.
Cikin wata iriyar kasalalliyar murya ya soma mata magana ƙasa ƙasa.
"Ummeenahhhh ki tashi kiyi sallah mun makara".
Cikin barcinta taji kamar ana mata magana akant.
Turo bakinta tayi gaba tana ƙoƙarin juya mai baya.
Hannunshi yasa ya tallafo mazaunanta yana matsasu da wani irin salo yana wani irin lumshe idanu yana jinsa kamar ya koma second round.
Zumbur Bebi ta miƙe jin ana taɓa mata bayanta.
Tashi tayi daga jikinshi tana mai ƙwaɓe fuskarta alamun zatayi mai kuka!
Matsota yayi kamar ze shige mata jikinta.
"Menene kuma?"
Yafaɗa da wata irin murya mai saka mabuƙaci tsuma.
"Bakai bane naji kana min irin abun jiya kallafa zafi nakeji sosai ko tausayamin bazakai ba"
Tafaɗa tana mai ƙoƙarin zubda hawayen shagwaɓa.
Kamota yayi gaba ɗaya ya rungumota yana mai shafo tsakiyar bayanta da lallausan hannunshi.
"Shiiiii bazanyi ba muje kiyi sallah"
Ɗan zamo kanta tai daga kirjinshi.
"Kallafa kayan daka samin ahaka zan fita kana ganin jikina?"
Bakinsa ya zira a cikin kunnenta yana mai tura harshenshi acikin ramin kunnen nata.
Yaɗan tsotsa kaɗan, cikin wani irin salo kana yace.
"Miye dan naga kaddarata a haka so kike naga ta wani wannan rigar mai tai a haka?"
Yafaɗa yana mai kallon rigar daya saka mata dayay mata wanka ɗazu rigar ta bacci ce doguwa amman bata bar komai ba, domin babu abinda ba,a gani ajikin Bebin musamman yadda bata saka komai ta ciki ba.
Ɗagata yayi kamar jinjira ya kaita tsakar gida anan ya sauketa lokacin wajan karfe 8:00am,
Dafa bango tayi tare da zira takalmi ta shiga cikin toilet ɗin inda shikuma ya nufi cikin ɗaki sabida yaji wayarshi tana ringing, ganin goma ke kiranshi yasa ya saka rigar shaddar jiya ya fita

daga gidan.
Awaje suka haɗu da goma bayan sun gaisa ya miko mashi babbar leda daya siyo mai kayan daya bukata amsa yayi tare dayi mai godiya kana ya koma gida ya rufo abinshi.
A falo ya aje ledar ya tube rigar ya rage dagashi se guntun wando ya kuma komawa bakin bayin jiyake kamar ya danna kanshi ciki.
Ita ko Beby tana daga cikin bayin tana kuka sabida lokacin data tsugunna zatai  tsarki jitai kamar an mata tsarki da ruwan barkono haka ƙasanta ke mata zafi.
Adaddafe ta tari ruwan ɗumi kamar yadda mama kece musu suna tsarki da ruwan ɗumi agida.
Ta zuba a ɗan bawon data gani a bayin seda ta cikashi taff sannan ta daddafe ta shiga ciki ta zauna tana mai sakin ƙaramar ƙara.
Jin zugin yana raguwa ruwan na salamcewa yasa ta kuma tarar wani ta ƙara shiga.
A wannan karon taji duk cinyoyinta dasuka ƙage sun warware sannan taji daɗin jikinta ba kamar da farko ba, wanka tayi da ruwan ɗumin sannan ta mayar da rigar kana tai alwala tafito tana cije baki.
Dashi taci karo abakin bayin yana leƙe harara ta banka mai batare data bari ya ganiba tana kokarin juyawa ta shiga ɗakin yay saurin ɗagata da kansa ya kaita ɗakin ya shinfiɗa mata sallaya ya ɗauko mata hijabi.
Ta saka ta tayar da sallar.
Da sauri ya fita kicin da kansa ya kunna gas.
Ya ɗora ruwan tea tunda ya iya wannan, daya kammala ya zuba a tea flaks, sannan ya dauki ƙwai ya fasa dafe kanshi yayi yana tunanin yaya zeyi ya soya domin bai iyaba.
Tunani ne ya faɗo masa da sauri ya koma ɗaki ya ɗauko wayarshi ya shiga cikin internet yay serching abunda yake son sani cikin mintuna ɗaya suka watso masa, yadda zeyi da sauri ya dire wayar ya soma kaɗa kwan ya ɗora kasko ya zuba mai ko albasa bai sakaba dan rashin sani tare da sauri kuma.
Man yay zafi ya zuba ƙwan, seda ƙwan yay jajur kamar ze ƙone sannan ya juya ya zuba a plate haka yayta fasa ƙwan yana soyawa har wajan guda biyar wai acewarsa yaga tana da cin abinci da yawa.
Se wajan 9 ya kammala duk ya haɗa gumi seda ya gyara kicin ɗin tsaf domin wajan shara daman bayajin ta sabida ya iyata sabida tsabar tsaftarshi shiyasa ya ƙware anan.
Sannan ya haɗa komai a saman tire ya shiga ɗakin ya aje ya koma ya ɗauko ragowar naman jiya a frij tare da kofinan shayi da cokali, lokacin daya koma tana zaune a darduma tana shafa azkar ɗin datayi.
Aje sauran kayan yayi yana share zufa kamar wanda yay aikin shekaru dubu baki ɗaya hannunshi ma zafi yake mai sabida wankin bedshit dayay da kuma wannan aikin, dariya ta ƙunshe tana mai kallonshi ƙasa ƙasa.
Wuceta yay ya nufi ɗakin ya fito da sauri kuma ya koma tiolet yay wanka yay brush sannan ya dawo ya ɗauki ledar kayan da goma ya kawo mai kallon yadda yake yawo tuɓi tuɓi tayi tana mamakin rashin kunyarshi.
Shirya kansa yayi cikin white jallabiya tare da feshe jikinshi da turare wanda duk acikin sautin kayan da goma ya siyo masa ne.
Sannan ya fito falon yana zuba ƙamshi zama yayi a ƙasan carpet yana mai fuskantar ta fuskarshi kamar koyaushe a ɗaure, wadda bata bayyana sirrin zuciyarshi.

Ɗagowa tayi tare da matsowa kaɗan gabanshi.
"Ina kwana"
Tafaɗa tanayin ƙasa da kanta.
Murmushi ya sauke mai sauti kana yace mata.
"Lafiya ƙalau ƴar albarka yaya gajiyar aikin lada?"
Yafaɗa idanunshi yana yawo ajikinta.
Ƙasa tayi da kanta tana maijin wata iriyar kunyarshi bakuma ta iya ce masa komiba.
"Dan Allah ki sauke wannan hijabin haba kamar gidan nida mutum dubune kin wani ƙunshemin jiki a wannan hijabin".
Yafaɗa yana mai ƙureta da idanunshi.
Hannu ta saka ta sauke hijabin tana mai ƙin kallonshi.
Wani irin yammmmm,zuuuttt yaji acikin ilahirin halittar dake aiki a sassan jikinshi tsigar jikinshi tai wani irin miƙewa haka zalika yawun bakinshi ya ƙame ya bushe ƙamas sabida tsabar yadda manyan halittun kirjin Bebi suka tokare mai idanu suka tsaya masa a ransa.
Ƙure wajan yayi da idanunshi atake anan idanunshi ya kaɗa yay wani irin jajur jikinshi ya soma mazari zazzaɓin ɗazu na neman dawo mai.
"Kici abincin mana"
Yafaɗa ararrabe sabida yadda bakinshi ke rawa.
Matsowa tayi sosai gaban abincin wanda ya bawa albarkatun dake manne da kirjinta damar kaɗawa kamar da gayya.
Wata irin miƙa Aliyu ya kumayi yana mai matse jikinshi sosai kamar mai jin sanyi.
Tea ta zuba a kofi mai yawa wanda daman da sugar ya dafashi sannan ta tura mai gabanshi.
Kamo hannunta yayi yana messeging ɗinshi tare da ɗaukar cup ɗin ya manna mata abakinta yana bata tean yana matsa hannunta yan wasa da tsakiyar tafin hannun nata.
Seda ta janje kanta sannan ya kafa nashi bakin a saman cup ɗin kuma adai dai saitin inda ta cire bakin nata yana sha yana lashe bakinshi.
Seda ya kammala sannan ya janyo plate ɗin ƙwan ze bata ta juya kanta gefe.
"Nafa ƙoshi bakina babu ɗanɗano"
Tafaɗa tana tura mai bakinta gaba.
"Oh bara naiwa ammi waya tai maki farfesu nasan zakisha"
Yafaɗa yana ƙoƙarin ɗaukar waya,aikwa cikin sauri  tai maza ta haye saman cinyarshi tana rera mai kukan shagwaɓa.
"Nidai kada ka kirata salon ta gane abinda mukayi dan Allah kabari"
Tafaɗa tana ƙoƙarin amar wayar daga hannunshi.
Wannan hawan cinyar nashi datayi shiya ƙara dulmiyashi cikin kogin buƙatuwa.
Da rawar jiki ya saɓeta sukai ɗaki ya kwantar ta saman katifa.
Rigarshi ya zame, jikinsa na wata irin rawa.
Ganin ze mata irin na jiya yasa idanunta raina fata nan da nan jikinta yahau rawa tuno wannan baƙar azabar dataji jiya.
Kafin ta dawo daga duniyar tunanin data faɗa, harya hayo saman cikinta ya mata rumfa da faffaɗan kirjinsa yana faman zuba mata zazzafan hucinshi gaba ɗaya ya gama zube mata nauyin jikinshi a yunwace ya kaiwa manyan albarkatun kirjinta wata irin damƙa yana sarrafasu cike da ƙwarewa tare da shauƙinsu bakinsa ya haɗe da nata yana aika mata da wani irin tsotsa

na musamman yana mai cigaba da yawo da hannunshi ajikin dukkan inda yasan ze kunnota, bakinsa ya mayar saman kirjinta kafin ya sami zarafin ɗora idanunsa cikin nata ya saka hannunshi ya tallafo mata jikinta ya haɗe jikinsa da nata numfashinsu na gamewa waje ɗaya hakanan fatar jikinsu tana gamuwa waje ɗaya, kafin ya sami zarafin saita hanyarshi harya sami nasarar jefa ƙwallonshi araga a wannan karon ma taji masifar zafi kamar na farko shiko anasa ɓarin barin duniyar tamu yayi seda yay nutso a kogin tafkin daɗi sannan ya dawo dai dai.
Baƙaramin budirinshi ya kuma sha tare da ita ba seda yaji dakansa ya sami wata irin nutsuwar da bai taɓa xato ba sannan ya ɗagata ya kaita bayi da kansa ya mata wanka shima kuma agabanta ya tube yay nasa wankan inda bebi tayita satan kallon halittarshi wadda atake anan ta shiga tsoron yadda taga girmanta amman kuma ahaka ta shigeta lallai tai ƙoƙari   ganin yana ƙoƙarin jiyowa yasa tai ƙasa da kanta tana sunke kai.
Tarar musu na wankan tsarki yayi suka tsarkake kansu sannan ya ɗagota ya naɗesu da sabbin tawul ɗin da goma ya haɗo masa dasu a kayan ɗazu sannan ya kawota falo ya kwantar, a saman sopa juyawar daze ya kuma hango na shanunta daya fito ta gefen tawul.
Seda ya dawo da baya ya kamo ɗaya ya tsotsa kaɗan yaɗan ciji nippy ɗin kafin yay maza ya saki ya nufi cikin room ɗin ya shiryo itama ya ɗauko mata kayanta na sakawa nashan iska yazo ya shiryata kana ya ɗauketa suka koma ɗaki ya haɗe jikinsu waje ɗaya yaja musu bargo.
Ranar da gaske Aliyu ya nunawa Bebi  zallar so ya nuna mata daga ita wata mace batada space acikin zuciyarshi domin sallah kaɗai yake barinta tayi bayan nan baya barinta tai komai shiyake mata, haka ya lalace ajikinta wunin ranar yana faman jagulata gaba ɗaya jikinta ciwo yake mata ko abinci ma a ɗaki yake bata domin goma ya aika yay musu take away,bini bini ze kaiwa kirjinta hannu ko baki haka zatai ta faman matsar hawaye haka zebi hawayen ya lashe kuma dan jaraba itama yana soma mata salonshi zata bi yarima tasha kiɗi seya gama tahau kuka.
Kashe wayarshi yayi ya cigaba da bata duk wata kulawa ta ma'aurata.
aranar seda bebi ta gane bata da wayo hakanan da daddare ya kuma binta ya ƙara da safema haka.
Tun abin yana mata daɗi harya fara fitar mata akanta amman dayake ya ƙware wajan iya romancing anan yake kasheta harta biye mai.
Ya sauke duk wannan miskilancin da zafin ran lallaɓata yake yana ririta kayarshi kamar ƙwai.
Tsayin  sati ɗaya ciff Aliyu ya ɗauka  agidan Bebi yana faman dagulata yana kashe arna abinsa yana waya da ammi da khadija amman shikam abba daman baima je sunyi sallama ba haka ya ƙaraci faɗanshi seya ce masa yayi hakuri aikin sabon kamfanin nashine ya haɗa mai xafi.
Khadijama cikin complain take kullum amman sabida daɗin baki irin nashi seya ce mata tai hakuri yana nan tafe.
Tsakaninshi da usman kwa se tsokana da shaƙiyanci domin kyautar maƙudan kudi yay ma usman ta accnt yana mai binsa da godiya haka nan kullum seya kira mama ya gaisarta sabida tunima an fashe gidan an haɗe da wanda ya sai musun ana faman gyaran gidan kamar za,a sauya shi baki ɗaya hakanan shahid ya soma zuwa bayero tuni ya daina saida gawayi tun washe garin ranar da sukai magana da Aliyu ya daina saida gawayin ya sama masa gurbin karatu a jami'a sabida kuɗi da hanya yasa nan da nan shahid ɗin ya sami addimistion ya soma fita school.
Sabida daman takardunshi sunyi kyau kuma jamb ɗinshi batai expire ba kuma ya sami point ɗin

da ake nema kawai rashin kuɗine daman yasa bai soma zuwaba yanzu kwa Allah ya kawo masa ɗauki dan haka ya mike kafa ya mayar da hankalinshi.
Gidan mama ba wata matsala zasuci zasu sha zasu bawa wani ma gefe ɗaya ga gyaran gida ana ta musu.
Sosai Bebi take ganin zallar gata wajan Aliyu yay mata mugun sabo da jikinshi baya barinta tai komai se tsabar bukatarsa dayake sauke mata koda yaushe.
Gaba ɗaya daga ita harshi sunyi wani fresh sunyi kyau, ita kanta bebi yanzu Aliyu ya sami gurbi na musamman a ranta sabida yadda yake faranta mata ko yaushe bata jin zata iya kwana ɗaya batajishi ajikinta ba sabida yadda ya horata da jarabarshi.
Yau tunda ya tashi yake shirya kansa sabida yau kwananshi takwas a gidan sannan kuma gobe monday ze koma office kafin agama na nan ya dawo gaba ɗaya.
Tunda Bebi taji yana waya da ammi akan ze koma gida take faman haɗe ranta gaba ɗaya taƙima sakar mai fuska.
Tun daran jiya yake rarrashinta amman taki daɗin azanci.
Yagama shirinsa cikin ɗanyar farar shadda tass wadda aka mata ɗinki da farin zare sabida tuni daman ya bawa goma order ɗinkunan kayanshi na nan waɗanda akayo kusan set 40 haka nan itama Bebi an karo mata kayan sosai nata na gida kuma.an fitar dasu an bawa matar goma.
Babu abinda yake se faman zuba uban kamshi gabanta yazo ya tsugunna yana kallonta.
Shi kansa yanajin wani irin kewarta a ransa yanajin kamar yayta kukan missing ɗinta.
Magana yakeson yay mata amman ya kasa itako ƙeya ta juya mai tana taɓe bakin kuka...........

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*94*

*BAZAN GAJI DA GODIYA BA, GA MASOYANA  ƘASHIN BAYAN NASARATA TA YADDA NAGA SUNA TURURUWAR BIYAN KUƊIN SABON BOOK ƊINA MAI SUNA ZUMA
A BAKI TABBAS NA SHAIDA ƘAUNAR KU GARENI ALLAHU YA BANI IKON FARAN TA MUKU YASA MU GAMA LAFIYA AMIN*

"Au ƙeya ma zaki juyamin madam?"
Yafaɗa muryarshi tana wani irin rawa kamar ze mata kuka!
Tashi tsaye yayi tare da zube hannayenshi cikin aljihun wandonshi kana ya bar mata wajan cikin bedroom ya koma ya tube kayan jikinshi.
Yay saura dagashi se singlet da gajeren wando duk kirarshi ta cikakken namiji ta bayyana a fili, ya dawo falon ya sameta a yadda take ɗagata yay cakk kamar wata jaririya ya nufi ɗaki da ita.
Kwantar ta yayi asaman katifar yana mai tsira mata kaifafan idanuwanshi masu rikita ta
Matsota yayi zuwa jikinshi ɗumin jikinsu ya haɗu waje ɗaya fuskarshi ya matsa gab da ta'ta kana ya ɗora bakinshi a saman goshinta yaɗan sumbata kaɗan.
Cikin wata irin kasalalliyar murya marar Amo! yasoma yi mata magana.
"Ammina tana missing ɗina tun jiya take min waya akan na dawo gida domin akwai nauyi akaina, keda nake zaton zaki kwantarmin da hankalina har ki bani goyon bayan tafiya, tun jiya kinmin banza ɗan murmushin da kike man kin daina nazo zan tafi kinjuya min ƙeya,to na fasa tafiyar zan zauna dake zan rayu dake zan mutu dake ko acikin aljanna ina fatan rabbi ya haɗani dake"
Yakai maganar muryarshi tana wata irin karkarwa sabida ɗimuwa da azabtuwar soyayyar da ruhinshi da gangar jikinshi ke karɓa akanta.
Wani irin tausayinshi ne ya kamata tasan haƙƙin uwa akan ɗanta ita kanta juriya take na rashin mama dan haka bazata so ta rabashi da mahaifiyarshi ba, bazata so akanta ya nesanta da ahalinshi ba, tabbas Ammi tana da matuƙar daraja a wurinta dan haka bazata so ran ammi ya ɓaci ba.

Muryarta tana wani irin karkarwa kamar zata mai kuka tace.
"Nifa kawai kewarka nake,ni bazan hanaka zuwa wurin ammi ba, amman kasan kaima ai mun saba"
Tafaɗa tana ɗora hannunta a saman gemunshi taɗan ja kaɗan tare da jan gashin girarshi mai uban yawa.
Murmushi ya sauke mai ƙayatarwa sannan ya matsota sosai kamar zasu zama abu guda.
"Ummeenah mun saba ko? yes da gaske mun saba amman nima yaya zanyi haka zanyi manage har na dawo , kema kina kewata? kema kina jin bugun zuciya akaina? kema kina sona kamar yadda nake sonki?"
Yafaɗa yana saka hannunshi a ƙasan ƙuguntayana messeging wurin a hankali kamar mai tsoro.
Wani irin yammm taji aduk kan sassan jikinta zuciyarta tai wani irin rauni haka nan kirjinta yana tsalle kamar ze doko.
Tayaya ma zatace bata son mijinta bayan tarin kyautatawar shi gareta to inama takai matsayin da zata ƙishi mutumin da bai taɓa ƙyamarta ba, baitaɓa kinta aranshi ba duk da bata da masaniyar matsayinta a wurinshi amman tasan cewar tana da babban muhalli atare dashi.
Akanshi ta soma sanin ɗa namiji akansa ta soma sauyawa daga Bebi ta koma wata mace daban mai daraja  mai ƙima ya ɗauketa batare daya duba matsayinta ba yasota akanta ya nesanta kanshi da uwar daular dasuke da ita ya kawota nan suna rayuwa to mai zata biyashi dashi...
Ɗago kanta tayi tana zubar da hawaye.
"Wallahi ina sonka ina ƙaunar ka ina kishinka,bazan taɓa daina sonka ba domin sonka a jinina yake kaika fara koyamin so akanka nasan so akanka nasan ciwon kaina, akanka na gyara halaiyyata ta son jiki da yawan bacci sabida kai mutum ne mai tsafta na kula idan na zauna a haka zaka iya gujemin, tabbas akanka na gane lafazin mamata akaina datake cemin Bebi Allah ya haɗaki da miji mai tsafta wanda kike masifar so anan zaki sauya halinki ada na ɗauki maganar da wasa amman zamana dakai nagane muddin kana son mutum tose ka kiyaye abinda yakeso da kuma wanda baya so domin neman zaman lafiya, fatana yanzu na kuma ƙwarewa a harkar girki domin na mallaki zuciyarka gaba ɗaya"
Tafaɗa tana kwantar da kanta acikin yalwataccen kirjinshi mai kamshi wani irin farinciki Aliyu yaji wanda tunda yake baitaɓa cin karo da kamarshi ba.
Tabbas kaso asoka shine so yadda bai sha wahala wajan nuna mata soyayyaba haka itama bata sha wahalar nuna mai tata ba, arayuwa shi mutum ne wanda yasan darajar kansa yasan ciwon kansa baya wahalar da zuciyarshi akan abunda yasan baze samuba, kuma baya kara wajan abinda zuciyarshi ke muradi duk miskilancin shi yasan darajar soyayya baitaɓa cin karo da soyayyar wata budurwa ba face Bebi yafara sonta tunda ya ganta, haka ya dage da addu'a da sallolin nafila se gashi Allah yasa komai yazo mai cikin sauki.
Goga mata sumar dake kwance a gefen fuskarshi yayi ahankali.
"Ina sonki my sugar zan shayar dake madarar ƙaunata ina sonki ina sonki I love you nana bilkisuuuuu"
"I love you Bebyn haidar"
Yafaɗa yana cigaba da goga mata sumar dake fuskarshi yana shafa mata gemunshin shi, kansa ya ɗora a samanta ya soma lashe fuskarta da harshensa yana tsotsar saman hancinta kamar

ya sami lolipop, Hannunshi ya zube saman kirjinta yana matsa mata su cikin ƙwarewa kafin ya fito dasu yana sarrafawa cikin nutsuwa, gaba ɗaya yagama ruɗa mata sassan jikinta da salonshi tun tana basarwa itama harta zo tana maida masa da martani tana masa wasa da dukkan inda tasan zata kunno shi wani irin nishi yake kafin ya sami damar haɗesu su zama abu ɗaya, sosai ya mantar da ita komai ya nuna mata one love.
Seda ya nuna mata ƙololuwar ƙauna  yanuna mata ita ɗince dashi, ya kaita birnin taraiyar daɗi ya nuna mata zallar soyayyar da duk macen da mijinta kesonta ke nuna mata sannan ya tattareta ya rungumeta bayan nutsuwa ta samesu bayan ya tabbatar daya bata zumar da bazata gushe mata ba, kowannensu yaji ya sami nutsuwa.
Haɗota yay kamar yarinyar goye ya nufi bayi da ita, da kansa yay mata wanka suka tsaftace jikinsu dan tsabar sangarta ma cemai tai bazata iya mikewa ba haka ya goyota ya kaita ɗaki ya shiryata da taimakonta ya shafa mai wanda anan ma suka kusan komawa ruwa,da kanta ta shiryashi cikin ɗanyen boyal milk wanda yay mashi mugun kyau turare ta besa mai tana tura bakin kishi gaba sabida yadda yay wani irin mugun kyau tare da kwarjini da haiba.
"Nidai Allah ka sauya kaya salon mata su kalleka a waje, sunganni ƴar ƙarama su maka wayo suce suna sonka"
Tafaɗa tana dira ƙafafunta a ƙasan carpet irin yadda yara sukeyi in suka so suyi shagwaɓa.

*****************
*ZUMA A BAKI...!*🌹
{  Painful love Story  }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*
******************
Kamota yayi ya haɗe da jikinshi yana goga mata sajenshi na fuska.
"Wallahi Beby kinfi min mata ɗari, kina bani zumar danake manta kaina babu macen data isa ta kallan tace tana sona seke beby na haba ƙaramar ƙasa mai albarkatun man fetur"
Yafaɗa yana tsotsar mata ƙasan lip's ɗinta danasa lip's ɗin.
Sosai yasha wahalar shawo kanta kafin ta daina mai rigima, hijabi ta saka suka fita daga gidan da kuka suka rabu ya shiga mota shima yana share hawayen love.
Seda taci kukanta a ɗaki ta ƙoshi kana ta kamo kayanshi daya cire ta rungume gashi yaƙi bata waya bare ta kirasa.
Ahaka bacci ya kwasheta wanda rabi tunanin shine.
******
Akasalane yake driving komai ya tsaya mai cak a ranshi.........

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{  Painful love Story  }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*95*

Da wani irin mutuwar jiki yake driving ɗin shi kaɗai yasan yadda zuciyarshi take tsananin jin kewar yarinyar da gaske tana da mugun shiga can cikin ran ɗan adam yana jin yana mata wani irin azababban so na fitar hankali, bayajin ze iya rintsawa batare da itaba.
Ya jima yana driving kafin ya isa gida, dayake khadija tasan da zuwan nashi tuni ta kammale komai na gida gashi kuma alhamdulillahi ɗan satin dayay bai nan ta samu damar gyara jikinta sosai da magungunan da anty ruma ta kawo mata.
Kai tsaye wajan ammi ya nufa ya tadda ita a falo tana zaune waya a hannunta ganinsa yasa ta aje wayar fuska ba sukuni take amsa mai gaisuwar daya ke mata.
Kafin ta haɗe rai tahau surfa masa masifa kamar zata ari baki.
"Sannu baba nace sannunka da shuka yanzu kai haka adalcin naka ike? kawai katafi masha Allah kabarmu da matarka baka ko leƙo mana ba?"
Tafaɗa tana mita sosai.
Seda ya jira ta gama faɗanta sannan ya kwantar dakai kamar ƙaramin yaro yana bata Haƙuri.
"Ammina kiyi hakuri, wallahi mai sunaki ce batada lafiya shine na zauna sabida babu wani kusa da ita"
Yafaɗi hakan domin yasan ta hakanne kaɗai zata rabu dashi.
Sosai ammi ta washe haƙoranta.
"Masha Allah baba amman dai kunje asibiti ko?"
Sosa kanshi yayi.
"Ban kaitaba amman inna koma zamuje"
Murmushin ta kumayi, sannan ta dubeshi.
"To inka huta kaje kaiwa ɗan uwanka barka zainab ta sami Aliyu jiya ta haihu ganin dare yasa ba,a gaya maka ba ubansa yay maka takwara, Sannan ankawo lefen su amina fa harda ƴan biyu abbanku yace sun gama school gwara an haɗa dasu tunda sunada mazajensu a hannu an saka rana nan da two weeks"
Ƙayataccen murmushi ya saki yana furta.
"Kai dik dai ammi masha ALLAH, Allah ya raya takwarana amman ni usman bai faɗamin ba?"
Murmushi ammi tai.
"Ance maka dare ne yayi shima fa yayanku umar fa humaira ta haifi mace yau kwana biyar kasan suna can legos ɗin duk se biki zasu tawo"
A wannan karon kabbara yake bakinshi ɗauke da far'a sosai yake jan addu'a a bayyane ammi tana amsa mai kana ya mike.

"Ammi banaje na gano my boy, wallahi sena ganshi zan wuce kafin na kawo ragon suna takwara ai ba wasa ba"
Yafaɗa yana nufar hanyar fita.
Da fatan alkairi ta bisa tana yabon haɗinkan zuri'arta sosai take kuma godiya ga Allah akan hakan.
A bakin part ɗin ammi ya tsaya yay wa ya umar waya yay mashi barka harda ɗan mitarshi akan yadda bai gaya masa ba hakuri ya bashi sannan sukai sallama ya tafi, bayan yay masa transper kuɗi wai a saiwa takwarar ammi pampers.
Cike da annashuwa ya isa part ɗin usman duk yan uwansu suna zazzaune a falo ana yiwa yaron wanka sosai suke kwasarshi yana wani basarwa dayake duk abokanan wasane yasa suke mashi hakan.
Bayan angamawa yaron wanka aka naɗoshi a tawul aka mikawa Aliyu shi, addu'a yay masa sannan ya mike suka jero da usman.
"Man kai kaga yadda kai wani fresh so masha Allah, amarya ta amsheka"
Usman yafaɗa yana dariya.
Shima ƴar dariyar yay kaɗan sannan yace mai.
"Bazaka gane ba amman dai nina san yanzu nayi aure fa, Alhaji kaikaga yadda ake tattalina"
Yafaɗa yana shafo gemunshi.
"Dama ai irin waɗannan sunfi daɗi yar shila malam amman da ana baka kana ƙin amsa"
Murmushi yay mai kana yace.
"Bazaka gane irin son da nakewa beby ba wallahi usman ka gama min komai a rayuwata Allah kaima ya faranta maka kamar yadda ka faranta min"
Sosai usman yake dariya ganin yadda ƙanin nashi ya zarme da yawa tab daman akwai ranar da Aliyu ze iya sauke jida kanshi yace yana son mace lallai so ba wasa bane ba.
Ganin usman ze mayar dashi sauna yasa ya wuce part ɗinshi shima bakinsa kunshe da dariyar yabar usman dashe a wurin yana dariyar ƙeta.
Sosai ya sami tarba a wajan madam dija kuma shima ɗin bai mata irin Wannan shariyar da yake mata daba sabida yana son ya kwatanta adalci gudun fushin ubangiji.
Da taimakonta yayi wanka ta tayashi ya kintsa, se wani maƙele mai take ajiki shikuma yana wani basarwa abinci ta haɗa masa mai rai da lafiya, kaɗan yaci ganin tana wani irin mirmir da idanu ya gane mai take nufi ɗaukarta yay cak ya nufi ɗakinsa da ita sosai ya ruɗa mata jikinta da salonshi kafin ya kama hanyar dayafi kauri.
Babu laifi baiji wannan azabar dayaji kwanaki ba sedai ko kaɗan bai sami ɗanɗanon daya samu wurin bebi ba domin ita bebi kusan haukacewa yake inya tare da ita.
Bai wani jimaba ya rabu da ita ya mike yaje ya tsarkake jikinsa yazo ya shirya kanshi cikin wani marun boyel mai manyan zane, yana fesa turare ya dubi dija datake kwance kamar gawa bama ta da niyar tashi.
"Dija ki tashi mana ki tsaftace jikinki"
Taji amon! muryarshi acikin kunnenta da ƙyar ta mike tana ware ƙafafu ta fita daga ɗakin tanajin kamar an mata shegen duka domin ta gurzu.
Dariya yay afili kana ya furta.
"Tabb lallai kinada aiki banyi good 30 mnt ajikinki ba kike wannan gandar, lallai dija raguwace, waccan yarinyar semu wuni muna abu ɗaya bata taɓa gajiya ba sedai intaji yunwa taci abinci

mu koma, amman ke daga sau ɗaya se ragwanci tabb,itako umminah ka daɗi ga dauriya wayyo i miss"
yafaɗa yana dafe jikinshi da hannunshi, a gaggauce ya shirya ya nufi masallaci sukai sallar azahar sannan ya ɗauki mota ya nufi gidan mama sabida tunda yaje sau ɗayama bai koma ba.
Sosai yay mamakin yadda aka ƙere gidan bayan haka kuma masu aikin sunyi mugun sauri.
Harda ɗan gate a kofar gidan ga wani uban fanti mai azabar kyau da aka yima gidan.
Parking ya gyara yana neman wanda ze aika.
Kamar daga sama sega shahid akan lifan dinsa da Aliyun ya sai masa sabida zuwa makaranta.
Yana washe baki ya ƙaraso gabansa ya rissuna yana gaisar da shi.
"Yaya Aliyu barka da rana, yanaga ka tsaya a waje yakamata ka shiga ciki aikaima ɗan gidane"
Murmushi yayima shahid sannan yace.
"Kai dai shiga kacewa mama ina waje"
"Tom bara na sanar da ita daman lefensu hassana aka kawo fa ɗazu, ansaka biki nan da sati uku"
Murmushi ya kuma sauke masa.
"Kai shahid da sauri haka za,a ɗebewa mama ƴaƴanta?"
"Wallahi yaya da ai shekara aka saka to kuma su yaya nuran sesuka ce tunda sun gama gininsu kuma sun sami aiki su kawai suna so ai da wuri"
Zaro idanu Aliyu yayi kaɗan wanda yake kara masa kyau kana yace.
"To Allah ya nuna mana lokacin Amin"
Shahid seda ya sanar da mama wadda tahau shi da faɗa damme baze ce ya shigoba sebarsa a waje.
"Mama fa seda na gaya mai shikuma yace nadai sanar dake"
Sannan ya fita wajan suka tawo tare da Aliyun
Sosai gidan ya burgeshi babu dai wani girman kirki sabida wanda aka siya ɗinma bawani babba bane sedai tsarin fasalin gidan ya ƙayatar kana shiga tsakar gidane da bayi.
Se ƙofar falon mama da aka zuba mata kujeru ma dai daita da ƴar tv ta bango harda ƙaramin frij, se kicin acikin falon se ɗakuna guda uku na shahid ɗaya na mama ɗaya na su hassana kuma duka da toilet cikinsu,se ƙaramin store sosai aka ƙayata gidan kamar ba shiba, kuma badaga wajan kowa wannan sauyin yake ba sedaga wajan Aliyu domin shiya wakilta wani yaronshi akan komai na gidan hatta saitin kayan ɗaki na kicin dana sakawa duk an kawo musu sabbi domin ɗakin mama gadone da sif da madubi hakama sauran ɗakunan su shahid ɗin bakaramin kuɗi fa gidan ya lashe ba, amman shi baiji komai ba sabida bebi ta bashi abinda yafi wannan daraja.
Sallama yayi cikin nutsuwa ya shiga falon iskar fanka tanata kaɗawa.
Mama wadda take zaune saman kujera tai saurin amsa masa tana gyara zaman hijabinta yatsunta jajur da lalle.
A ƙasan center carpet ya zauna yana gaisar da ita.
Tana amsa masa itama cikin kunya sannan ta mike taje frij ta ɗauko mai pure water ta zuba a plate ta kawo mai kicin ta wuce ta zubo masa alkubus da miya acikin kwanuka wadda miyar tasha naman kaji sabida yadda Aliyu ke sakawa a kawo musu kayan bukata akai akai.
Gabansa ta aje sannan ta wuce ɗaki.
ta ɗauko carbinta ta dawo ta zauna.

"Mama yaya gida yasu ihsan? mama kozaki bamu arfa ne na kai mata sabida gidan yay mata faɗi ba kowa ni kuma na tawo nan"
Yakai maganar kansa a sunkuye.
"Kadai ci abincin tukunna bara na baka waje"
Tafaɗa cikin kulawa ta mike ta nufi ɗakinta.
Janyo plate yayi ya zuba alkubus ɗin guda biyu ya zuba miya bai saka nama ba.
Bisimillah yayi ya soma ci ai ina tuni Aliyu ya manta a ina yake sabida azabar daɗin da abincin yayi masa, seda yaci sosai yasha ruwa sannan yay hamdala kana ya koma gefe ɗaya yana jin cikinshi ya cika damm.
Zamansa da mintuna biyar su hassana sukai sallama falon jikinsu sanye da hijabi har ƙasa,daga ganima daga unguwa suke.
Ganinshi yasa suka tsugunna suka gaishe shi sannan suka wuce ɗakin mama da kallo ya bisu yana yaba nutsuwar yaran.
Arfa ya janyo da hannunshi yarinya ƙarama mai mugun kyau tana matukar kama da bebi.
"Ajinki nawa a makaranta?"
Basa amsa tayi da cewa.
"Primary one ita kuma ihsan three"
Sabida su daman tun asali a wata private school mama ta sakasu mai saukin kudi.
"A islamiyya kuma munkai izifi sha biyar"
Zaro idanu yay yana cewa.
"Kai masha Allah"
"Su yaya Bebi kuma sauka zasuyi fa aka mata aure anma kusa shine da aka mata aure tai ta yiwa mama kuka"
Tafaɗa da suffar yarinta.
"Suma su anty hassana ma aure za,a musu sunata yiwa mama kuka, kuma yanzu mama bata saida dambu kullum inaji tana yiwa wani yaya Aliyu addu'a intayi sallah muma tace kuma muyi masa waishi ya mayar mana da gidanmu sabo yake aiko mana da abinci"
Tafaɗa batare data san cewar shiɗin bane.
Dariya yakewa yarinyar sabida yaga irin yaran nan ne masu faɗi ba,a tambayekuba.
Cikin haka mama ta dawo falon
"Aliyu harka gama ka haɗu da arfa sarkin surutu ko?"
Tafaɗa tana zama a saman kujera.
"Lahh mama daman shine kikace muna masa addu'a yanzu nake gaya masa ankawo lefen su anty hassana, lah mama daman shine yayanmu mai kyau"
Ta faɗa tana naɗewa jikin Aliyu.
Da sauri hassana ta fito ta maketa aikawa ta saka kuka tayi ɗaki aguje.
"Haba da baki duketa ba yarinya ce ai"
Ya faɗawa hassana wadda ta saki murmushi ta koma ɗaki.
"Haka suke fama dasu damma dodon tasu bata nan aisu hassana basa duka Bebi ce mai azabar saurin hannu"
Dariya ya saki kaɗan.
"Mama yanzu bebi tana dukansu?"
Gyara zama mama tayi.

"Ai Aliyu bebi ko ƙoface ta bugeta wallahi seta koma ta rama sedai fa hannunta ya fashe kaga tana ƙarama intai faɗa aka duketa kwana take kuka! ai duk yarana Aliyu babu mai rashin haƙuri kamar bebi, nasha wahala akan bebi Aliyu gashi ta soma ciwo babu mai rintsawa duk yarana bebi tafi shiga ran jama'a sedai fa tafi kowa rashin ji"
Dariya yake sosai yana hango yadda take masifar jin tsoronsa amman ashe agida ba kanwar lasa bace.
"Ai Aliyu bazan iya baku arfa ba wallahi matarka seta sumar min daƴa daman sunata murna ta tafi, Bebi akwai saurin hannu babu ƙaddarar da zata saka na baku autata wallahi"
Marai raicewa yayi yana faman magiya amman mama taƙi fafur sabida sanin halin ƴar tata.
Kallonshi mama tayi cikin nutsuwa.
"Aliyu nagode nagode Allah ya saka maka da aljanna ka sauya rayuwarmu daga ƙunci ta koma farin ciki ka gyara mana gida ka bamu kayan abinci kai mana ɗinkunan suttura, wai ashe har malam ma seda ka aika masa da kuɗi da kayan abinci duka dai nagode Allah ya biyaka"
Sosai ta bashi kunya sukewa wanima bare surukansa,.
"Mama babu komai fa wannan ba wani abu bane ai anzama ɗaya, insha Allahu zan aiko a ɗebi amaran ma akaisu ceɗi su zaɓi kayan ɗakuna ashe an kawo lefe"
"A,a Aliyu haba ɗawainiyar da kai mana ma ta isa abin ai seyay yawa"
Tafaɗa muryarta tana rawa.
"Wallahi mama bata isa ba nifa karki damu bawai kuba ko wani kuka kawo zan masa mama sabida ina son Bebi, sosai, ai kun gama min karshen karamci da kuka bani ƴa guda baku duba cewar koni wanene ba wallahi nagode kuma xan riƙeta bisa amana insha Allah"
Kunyace ta kama mama lallai yaran zamani se abarsu yanzu agabanta yake furta mata yana son ƴarta, shiko ko ajikinshi haka ya cigaba da janta da hira har yake gaya mata matar usman ta haihu,
****************
Bai iya komawa wurin babar ladiba kai tsaye gida ya wuce yayi kwanan zulumi washe garima haka ya koma shagon wannan mutumin mai kayan lefe anan yakejin labari wai ashe mutumin ɗan damfarane wai sunje sunyiwa wani mutumi irin yadda sukai masa ashe mutumumin ɗan sandane shine ya baza jami'ai har aka ganosu ashe grp ne guda dasu na irin wannan damfarar suke karɓar hayar shago a kasuwa insun yi sesu gudu se wannan lokacin dubun su ta cika. Aka kamesu aka haɗa da masu basu hayar shagunan yanxu haka suna gidan horo na musamman.
Awajan kawu tasi'u ya zauna yana kuka wiwi gadai karshen wannan mutumin yadda ya koma yasan shikam kayan lefen nan nasa sun dulmiya.
A daddafe ya koma gida nan ɗinma ya tarar da ƴan uwanshi cirko cirko duk jiki a sanyaye.
Ga ƴaƴa sunci duka wajan ƴan sanda.
"Tasi'u ina ganin lokaci yayi da zamu saduda fa lokaci yayi da zamu aje maka man yaƙinmufa shekaru suna ƙara ja iyayenmu sun rasu mun cutar da ɗan uwanmu akan gadon damu bai mana ƙarkoba tunda musa yabar gidan nan muke ganin bala'i da masifa wani cigaba muka samu a rayuwarmu? to nidai na gaya muku yanzu xan tashi naje wajan aisha ta yafemin ƴaƴanta ma haka ko Allah ya duben ya yafen laifukana".
Kawu sani yafaɗa yana kuka kamar ranshi ze fita.
Atake anan kowa yay na'am da hakan shawara suka yanke akan su fara tunkarar gidan malam

lado tukunna.
Aikuwa nan da nan suka haɗu cif tare da ƴaƴansu maza sukayi sharaɗa gidan malam lado sukaje yana soro yana karatu se ganinsu yay akansa kamar an korosu.
"A,a tasi'u salisu Rabi'u sani! zuwa kukai ku kasheni kome?"
Yafaɗa a rikice.
Jikinsu a matuƙar sanyi suka zauna a gefen tabarma.
"Malam ba wannan ya kawomu ba, munzone akan mu baka hakuri sannan kai mana jagora wajan aisha wallahi bala'i yayi mana yawa"
Dariya malam yayi.
"Kodai kunzo cin arziki kunji labarin yanzu aisha ta wuce raini ai kaɗan kuka gani azzaluman Allah kuma jira sakamakon ku"
Rantse rantse suka hau masa akan su wallahi basuma san da sauyin da mama ta samuba.
Ganin yadda sukai namada ne sosai yasa jikin malam yayi sanyi.
Da kansa ya aika aka kirawo su yaya aminu da sukazo ya zauna yayi musu bayanin komai.
Dayake ƴan bokone tuni, suka nuna murnarsu suka kuma yi na'am da tuban da kawunan amaren nasu sukai dan haka sukai musu jagora zuwa gidan mama.
Tun a bakin gidan su kawu tasi'u suka soma xare idanu katari da shegiyar motar Aliyu a kofar gidan ya kuma basu tsoro.
Malam shiya soma shiga sannan sauran suka bisu.
Mama tana zaune suna hira da Aliyu taga shigowarsu malam da sauri ta sauko kasa ta basa kujera ya zauna.
Su nurane suka karaso suma tare dasu kawu.
Gaisawa sukai da Aliyu inda mama ta sha jinin jikinta takuma haɗe ranta tamau ko gaisuwar dasu nura ke mata a ciki ta amsa falonne yayi shuru.
gyaran murya malam yayi.
"Aisha ni waye wajanki?"
Yafaɗa yana kallonta.
"Kai ubane na ƙwarai wanda ya tallafi  rayuwar marayan Allah"
"Da kyau kiramin ƴaƴanki"
Tashi tayi ta kirawo su hassana bebi ce kaɗai babu.
Aliyu ya mike zebar falon malam ya dakatar dashi.
"Zauna mana Aliyu ai kazama ɗan gida kaima ma haɗu mu bawa babar taka baki"
Zama yayi yana murmushi.
"Aisha nazo na baki hakuri ga iyayen ƴaƴanki sun gane kurensu sunzo akan su baki hakuri kucigaba da zumuncinku, kamar yadda zumunci yake daman jijiyane daga Allah wanda ya sadashi Allah ze sadashi da rahama, wanda kuma ya yankeshi Allah ze yanke masa rahama, kin dai gani da idanunki yadda Allah ya nuna musu ko?"
Kuka mama tasa awajan.
"malam da ciwo fa malam kaga cin zarafin da sukai mana nida abbansu bada ban kaiba ina zamuje a kano malam a shagofa muke kwana nida ƴaƴana"
Tafaɗa tana kuka.
Aikwa nan da nan ƴan biyuma suka hau kukan kamar rasuwar abbansu ce ta dawo sabuwa.
"Naji aisha Allah ma ana masa laifi ya yafe bare kuma mu ƴan adam ina haɗaki da girman Allah

akan kiyi hakuri ki bar maganar, kinga ga surukanki nan a wajan bai dace kina kuka ba"
Malam ya faɗa mata hakan cikin kwantar da murya.
Suma su kawu tasi'un kuka suka saka.
"Tabbas mun cutar da musa amman aisha muna rokonki da kiyi mana afuwa ki bamu damar gyara zumuncin mu"
Ɗago kanta tayi.
"Na yafe muku, nidai sauran ƴaƴanku gasu nan, suma ƴan biyu atake anan suka yafewa dangin mahaifin nasu nan kuma hira ta barke cike da nishaɗi sunayi suna kuma bata hakuri kamar zasu ari baki.
Wayar kawu tasi'u ce tahau ringing yana ɗagawa ya dire yana furta.
"Innalillahi wa'innah ilaihir raju'un ganinan"
Yafaɗa a firgice
Gaba ɗaya tambayarsa aka hau yi mai ya faru.
Da kuka yake shaidawa malam abinda ya faru da ladi da khalifa.
Zaro idanu Aliyu yayi yana jin jina rashin imanin khaleefa shiko nura tashi yayi tsaye.
"Kawu ina ganin zan shigar da ƙara kotunmu dan wannan bai isa ya taka doka mun barsa ba sunana barrister nuraddeen adam rimin gado sabida haka zan tsaya maka insha Allah harse na kwatar maka hakkin yarka nike neman auren hussaina ga kuma ɗan uwana Dr aminullah adam rimin gado shikuma shike neman auren hassana, se wannan Md Aliyu idiriss mai atamfa nasan kunsanshi shine mijin bebi na gabatar muku da kammu amatsayin surukanku dasuka auri ƴaƴan ƙaninku dan nasan baku sammu ba"
Sosai su kawu suka rude da lafazin nura.
"ni ina aiki anan kotun dake court road,a matsayin lauya, se yayana yana aiki a asibitin malam aminu kano, ƙwararren likitan matane, wannan kuma nasan kuna da sanin ɗane wajan Alhaji idriss mai atamfa textiles kuma shine director manager na kamfanin mai atamfa wanda ke sharaɗa kamfani nasan dai ko baku sanshi ba kunsan sunanshi a redio"
Ya nura ya faɗa yana mai fiddo da wayarshi.
Rudewa su kawu sukai tsoron Allah ya kuma kamasu lallai baka raina mutum domin baka san mai Allah ze masa ba, jiba aisha bata da ƴaƴa maza manya amman Allah ya bawa ƴaƴanta mata maxaje na nuna sa'a lallai ka tsayama ka bawa ɗanka tarbiyar ƙwarai jarine yanzu inda ta saka ƴaƴan a gurbatacciyar rayuwa da bazasu taɓa xama haka ba.
"Aisha mungode da samun uwa kamarmi kin jajurce wajan bawa ƴaƴan ɗan uwanmu tarbiya wadda tasa har Allah ya basu mazan ƙwarai madallah da samun uwa marar son abin duniya kamarki"
Suka faɗa a tare.
"Ni yanzu zan koma asibiti wajan ladi sabida yanzu ance ana bukatar jini da allurai wai tana ta wani abu kamar jijjiga"
Mikewa sukai mama ta bisu tana musu sallama tana kuma jin tausayinsu sabida yadda duniya ta murxasu.
Cikin sauri Aliyu ya bisu yaran sune suka tafi gida sukuma ya ɗaukesu a mota suka nufi asibitin harda ya aminu ma.
Transper suka ɗauka zuwa wani asibitin daban wanda Aliyu ne yay bill kuɗi har wanan dubu ɗari ukun ta jiya seda ya biya.

Asibitin kudi mai kyau aka mayar wanda nan da nan Aliyu ya sakar musu kudi aka soma bata taimako fiye da wanda aka bata abaya.
Bai baro asibitin ba seda ya biya kudin komai kana ya cikasu da kuɗi yanajin idan yay musu kamar mahaifin bebi yayma ne.
Fitowa yay kawu tasi'u da rabi'u suka biyoshi suna faman masa godiya hatta babar ladi seda tai kukan daɗi.
"Kaga ikon Allah ko tasi'u? suda muka walalanta ashe ajikinsu zamu huta"
Rabi'u yafaɗa yana murmushi.
Sosai suka saduda da lamarin rayuwa kuma sukai nadamar abinda sukai abaya.
Mama da daddare sukazo harda abincinta koda taga ladi seda tai kuka su inna suwaiba kamar zasu lashe mama har wajan taran dare suna can  seda ya nura yakai iya sannan suka tawo tare.
Shiko Aliyu tea kawai yasha yay sallah ya nutse agado gobe yana da office gashi kuma yana son su haɗu da nura akan zancen case ɗin khalifa domin uban yaron yana da kuɗi dole se Aliyu ya haɗa nura da manyan lauyoyi kafin a tunkari abin yana son a nunawa alhaji mai gwall cewar basuji buluss ba.
haka ya kwanta da gajiya da tunanin bebi aransa.
Washe garima mama ce ta aika shahid ya kai musu kayan karin kumallo A asibitin sabida ladi zata ɗauki wajan wata ɗaya a sibitin ana bata treatment.
Wajan 10 Aliyu suka haɗu da nura sukai abinda zasuyi kana suka shigar da karar khalifa na yadda yaywa ladi, sannan ya haɗa nura da manyan lauyoyin daya cikasu da mahaukatan kudi akan case ɗin.
Office ya wuce.
Ranar ma baije gidan bebi ba sabida gajiya bai kuma kirata wayaba ya bari gobe inyaje yama kaita ta dubo ladi.
A kotu an gama komai ranar monday za,a soma zama, amman kafin nan anbawa maga takarda takardar sammaci gidan Alhaji mai gwall..............

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{  Painful love Story  }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga

shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*96*

Alhaji mai gwall tare da iyalinshi zaune a falo suna hira, hankalinsu kwance kayan marmarine agabansu sunaci cikin nishaɗi da farin ciki da kwanciyar hankali.
Khalifa yana saman cinyar mamansa tana shafa kansa cikin kulawa shikuma alhajin yana ɓare apple yana saka mai a bakinshi.
Sam sun manta ma da lamarin wata ladi bare suyi maganar yaya ta kwana koko a wani hali take ciki? su kawai hankalinsu yana ga sabgar gabansu
Sallamar mai gadi ce tasa suka tsagaita da hirar tasu cikin ƙyamar talaka, ƙanwar khalifa take daka wa mai gadin tsawa.
"Kai miye zaka wani shigo mana falo kana wata sallama kamar mahaukaci kacikawa mutane kunne?"
Jikinshi yana rawa ya rissuna.
"Afuwan hajiya ƙarama ga wannan takardar wani yarone yace abawa alhaji"
Amsa tai a wulakance kana ta koma ciki daga tsaye ta mikawa alhajin sannan ta koma saman seater ta kwanta.
A fili alhaji yake karanta takardar.
_Kotun shari'ar musulunci dake zaune akan hanyar zaria road tana miko takardar sammaci ga, Khalipha Alhaji mai gwall, abisa yadda yay watsi da daraja da ƙimar aure bayan rattaba saki har biyu kai tsaye ga matarsa hakan bai masa ba kai tsaye ya afka mata kamar fyaɗe batare da sanin ƙimar ɗan adam ba, sabida haka wannan kotu mai adalci tana neman khaleepha shida mahaifinsu ranar litinin mai zuwa da misalin karfe taran safiya_
Wata dariya khalifa ya saki ta keta shima alhajin haka yayta dariyar harda kifawa.
Bayan sun gama jin komai daga wajan alhajin.

"Hoho talaka bawan Allah ni yau talakan dake kasana ze shigar ƙara tabb lallai sun taro faɗa dani"
Alhaji ya faɗa yana fiddo wayarshi lowyern shi ya kira yana dariya yake sanar dashi.
Shima lowyern alhajin dariya yake kana yace mai subar mai komai ze bincika case  ɗin.
Katse wayar yayi yana mai cewa inama ai shari'ar gobe domin ze gwada musu karfin kuɗine, khalifa kam dariya yake domin ya riga ya saba lalata ƴan aikin gidansu ma koda kwanaki uwar wata yarinya daga cikin masu aikin nasu yayma ƴarta ciki data kaisu ƙara a ranar aka kori case ɗin sabida sunyi toshiya da kuɗi.
Dan haka wannan bai ɗaukeshi abakin komaiba domin yasan tunda sunada kudi sun gama komai kilama reshe ya juye da mujiya.

A ɓangaren ladi kuwa sosai take samun kulawa sabida yadda Aliyu ya saki kuɗi komai yana tafiya mata cikin sauki hatta ɗinkin ma da aka mata yanzu ya fara cirewa, haka zalika matsalar abinci ma basu da ita sabida yadda Aliyu yasa aka kai masu kayan abincin can gidan su na ƴan kusan sannan yayma samarin gidan alƙawarin aiki a kamfaninshi na tokarawa da zarar an fara aiki.
Ranar dasu kawu tasi'u suke jin maganar kotu da kuma wannan aikin daya samarwa ƴaƴansu har kuka sukai suna cewa.
"Da ɗa da dukiya ba,a musu mugunta domin baka san wanda zaka mora ba ada sun ƙyamaci ƴaƴan ɗan uwansu ashe ajikinsu zasu huta rayuwa kenan"
Kamar zasu ari bakin godiya wajan Aliyu ranar har seda yaji babu daɗi sannan yay masu sallama ya tafi gida ranar ma baijewa bebi ba sabida gajiya ko khadijama bata ganshi ba ya kulle kansane a ɗaki yana faman tura sakonni na ordern kayanshi na kamfani dayake son yaje ya tawo dasu nan da wata biyu.
Ya kai wajan karfe biyun dare yana abu ɗaya kafin ya kashe system ɗin ya kwanta.
Wa shegari ranar talata nanma sun sami baƙi daga kamfaninsu bai shigo gidaba se dare.
Zama yay a gefen gado yana cire safar kafarshi sannan ya tube suite ɗin jikinshi.
Wayarshi ya zaro ya lalubo numbern goma ringing ɗaya goma ya ɗaga bayan sun gaisa yake cemai yana son ya bawa mufida waya ta kaiwa Bebi.
Cikin bin umarni goma ya bawa mufida wayar ta kai mata.
Tana kwance saman sopa tana faman baccin daya zame mata jiki tunda ya tafi bata da aiki sena bacci umman mufida ke aiko mata da abinci da daddare kuma su mufida suzo su tayata kwana.
Sallama mufida  tai sannan taɗan bugi kafarta.
"Anty ki tashi ga waya inji abbanmu"
Cikin magagi ta amsa tana yamutsa fuska.
Mufida juyawa tai aikwa nan wayar ta hau ringing.
Seda ta fita waje ta zubda miyaun daya cika mata baki sannan ta ɗaga.
"Assalamu Alaikum"
Tafaɗa cikin muryarta mai alamun bacci.
Lumshe ido yay yana shafa sajenshi.
"Amin wa'alaikissalam matar haidar"

Gabanta ne ya fadi jin muryarshi kaɗai ya hargitsa mata lissafinta.
"Umm kamanta dani ko?"
Zaro idanunshi yay waje kamar tana gabanshi.
"Bebyna ashe zan manta kaina, hope kina lafiya dai?"
Tura mai baki tai kamar  yana gabanta.
"Amman yau kwana uku, bana tare dakai ko waya bakai ba?".
Rarrashinta ya somayi cikin so da kauna nan da nan ta soma dariya tana tambayarshi yaushe ze dawo.
"Mekika tanadar min na dawowar?"
Cikin sakarci tace mai.
"Tabb nifa wallahi tunda katafi bana girki"
Gabansa ne ya fadi cikin sauri kuma yace mata.
"Subuhannallahi meyasa?"
"Ni wallahi bana son warin gas ɗin ranar da katafi na kunna zan ɗora tea kasan har amai nayifa shine umman mufida ta hanani girkin, ita take kawon kumani bana son komai inba tuwonta ba, se kuma kaina yayta min ciwo da zazzaɓi naita amai da safiya da magariba naita bacci wallahi wani bin mafa akan sallaya nake baccin"
Lumshe idanunshi yayi luff yana shafa kwantaccen gashin kirjinshi laso ƙasan laɓɓansa yake waɗanda suka ɗan bushe kaɗan.
Kobai karatun likitaba yasan abinda take nufi.
"Alhamdulillahi kina son mu sami boy mai sunan abbanki?"
Yafaɗa cikin raɗa
"A,a"
Ta bashi amsa kanta tsaye.
Gabansa ne ya fadi cikin sauri ya buɗe idanunshi
"Sabida me kika cemin haka?"
Ya tambayeta.
"Sabida bana son haihuwa gaskiya haka kawai salon in anganni da ciki asan abinda muke dakai a ɗaki, ni wallahi bazakaja aitamin kallon.............".
Dariya yake harda riƙe ciki ƙuruciya tuburan lallai maza suna morewa in suka auri yarinya karama domin anan zasu san takan wauta da kuruciya
"Asan me madam?"
Yafaɗa yana kunshe dariyarsa.
"Asan abinda kakemin mana, kai yanzu bazakaji kunyar ammin kaba?"
Dariya yay kaɗan wadda inba itanba babu maijin irin dariyar dayake.
"Kunya a raya sunna? aure fa sunnace mu tayaya akai aka samemu? haba amaryarta ki daina faɗin haka plssssss"
Tura mai baki tai gaba.
"Nifa wallahi bazan iya wankin kayan kashiba sannan yaro yayta shamin nono haka kawai nifa bana so"
Nutsuwarsa ya gyara.
"Nidai nasan nai ajiya amararki sabida haka ki kulamin da kanki sosai kafin nazo, semuje asibiti, in banda abinki nimafa nasha bare bebyna daman ai dammu akayi shi nida yarana kaɗai"

Dariya tayi har tana rufe idanunta.
Sosai ta sake suna hira batare daya fahimtar da ita abinda yake hasashe ba sedai koda wasa bai nuna mata tana da shigar cikiba sabida yaga take takenta na kuruciya acewarsa kartai masa wasa da kaddara.
Seda ta soma hamma sannan ya katse wayar anan wayar ta kwana wajanta seda safe mufida ta tafi da wayar wajan abban nata.
Shiko a daren kwanan sallah yay yana addu'ar Allah yasa hasashen shi yazama gaskiya.
Bebi nada cikinshi lallai Allah mai yadda yasone da bawansa wato dai aurenshi ma harda rabon haihuwa shiyasa Allah ya kawo auren gab babu jan lokaci.
Duk da bashida tabbas amman da safe kowa agidan ya shaida farin cikinshi sabida yadda ya dinga rabon kuɗi  ga ma'aikatansa hatta khadija ranar taga gata da safe.
Haka nan ko a office sosai ya sake yake harkoki da jama'a haka nan lina wannan tsohuwar budurwar tasa datake sonshi ita kanta dataje office ɗinsa yau ɗin taga sauyi anan take bashi card ɗin bikinta tana yi mai bayanin ta karbi musulunci dan haka aure zatai zata auri musulmi ɗan nan ma'aikatar.
Sosai yayta farin ciki harya sa ta kira angon nata yay musu kyautar maƙudan kudi sannan ya masu fatan alkairi suka tafi.
Koda ya tashi daga office daman kamar akan ƙaya yake kai tsaye gidan bebi yayi bayan ya gayawa khadija cewar yana da uzurin daze kaishi safiya bai dawo ba.................

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{  Painful love Story  }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payement domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*97*

Tafiya ce mai tsayi daga kamfaninsu zuwa unguwar da bebi take.
Seda ya tsaya a kasuwar ƴan kaba ya sayo mata kayan fruit, sannan ya nufi gida a bakin hanyar da zata sadashi da layin gidan yay parking ya nufi wani sabon gurin daya gani wanda ake gashin kifi, wajan da layi seda yaɗan jinkirta kafin azo kanshi leda biyu yay musu tare da drinks masu sanyi sannan ya nufi mota ya zube su a bayan motarshi sannan ya nufi layin gidan nashi
Gate ya buɗe ya shigar da motar sannan ya kasheta ya ɗebi ledojin hannunshi ya nufi gaban ƙofar part ɗin bebi, spare keyn dake hannunshi yay amfani dashi ya buɗe kofar bakinshi ɗauke da sallama ya nufi cikin gidan.
Lokacin wajan karfe biyar ɗin yamma, sosai yay mamakin yadda gidan yake tsaf ko ina ƙal ƙal, ga bakin famfo nan kamar ma ba,a amfani dashi.
Sallama yaketa faman yi yaji shuru kai tsaye kofar falon ya nufa nan ma seda yay sallama tare da buɗe labulan.
Wutar nepa ta haske falon ga fanka tana kaɗawa a hankali, tana kwance a ƙasan carpet ta cure hannunta a tsakanin cinyarta  zube ledojin dake hannunshi yayi da sarsarfa ya nufi gabanta ya zauna daɓas yana mai saka hannunshi ya tattarota gaba ɗaya ya ɗorata a saman cinyarshi yana mai tsirata da idanunshi jiyake yana matukar missing ɗinta tamkar yay shekara dubu bai gantaba.
Juya kanta tayi tana mai gyara kwanciyarta batare data san da zuwanshi ba.
"Ummee! ummee!! nadawo fa"
Yafaɗa yana hura mata iskar dake cikin bakinshi.
Lumshe idanunta tayi tare dajan numfashi kaɗan a hankali ta buɗe idanunta tarwai a saman fuskarshi, janye jikinta tayi wanda yake zafi zau kamar wuta.
Cikin sanyin jiki ta mike ta nufi tsakar gida.
Yawu ta zubda tana mai wanko bakinta sannan ta dawo ɗakin.
"Sannu da zuwa ina yini?"
Tafaɗa tana mai zama daga ɗan nesa dashi.
Kafa mata narkakkun mayun mayunwatan idanuwanshi yayi yana nazarinta gaba ɗaya tai wani irin duhu ta rame a mai makon taɗan ciko irin na masu ciki a,a ita se uban duhun datayi da

kuma rama.
"Zonan"
Yafaɗa mata fuskarshi ɗauke da damuwa.
Da jan jiki ta iskeshi gab dashi ta matsa kamar zata hau saman jikinshi.
Hannunshi mai cike da gargasa kota ina ya saka ya janyota ta faɗa samanshi ya saka ɗayan ya taɓa saman wuyanta.
"Meke damunki naji zazzaɓi ajikinki?"
Yafaɗa cikin matsananciyar damuwa.
Ɗan xamewa tayi daga jikinshi tana yamutsa fuskarta sam bata son warin turaren nan.
Da sauri ta mike aguje tai tsakar gida tunma a bakin kofa take kakarin amai tana mai saka hannu tana dafe maƙoshinta.
Da ƙyar ta karasa gaban rariya ta dinga sheƙa amai wanda babu komi cikinshi se ruwa.
Yana tsaye akanta harta gama aman da kansa ya zuba mata ruwa ta wanke fuskarta da bakinta.
Cikin lokaci kaɗan ya gyara wajan sannan ya kamata suka nufi falon ya kwantar ta saman sopa.
Idanunshi jajur da alamun damuwa atare dashi.
Yaɗan matso gabanta.
"Sannu kinji".
Yafaɗa a tausashe.
Hawayen datake dannewa ne yake zubowa.
"Nidai ka matsamin wallahi wannan turaren naka bana sonshi kamar zan mutu"
Tafaɗa tana juyawa tai ruf da ciki tare da danne hancinta da tafin hannunta.
Kamar zeyi kuka ya dubeta.
"naji amman dan Allah ki gyara wannan kwanciyar sabida gudun matsala bara na sauya kaya sena kira dector".
Yafaɗa yana mai tsayawa akanta da ƙyar ya samu ta gyara kwanciyar tata tare da toshe hancinta da ɗankwalin atamfar jikinta.
Ɗaki ya wuce ya sauyo kayan jikinshi sannan ya fito wayarsa ya ɗauka yana mai dannawa ya kirawo likitanshi bugu ɗaya ya ɗauka magana yake masa cikin harshen nasara bayan sun kammala ya katse wayar yana mai komawa gabanta.
"Sannu meke damunki yanzu?"
Cikin sauri ta mike daga kwanciyar tana mai dafe kanta.
Sannan ta zauna kasan carpet tana kallonshi
Idanunta yay wani irin ja cike da damuwa ya zauna a gabanta ya saka hannunshi ya kamo nata hannun ya tsirama faracenta idanu sunyi wani irin fari tas wanda ke nuni tana ɗauke da juna biyu.
"Wallahi nima ban saniba amman bakaji yadda nakeji ba"
Tafaɗa kamar zatai kuka!
"Look dan Allah kada kimin kuka! please yanzu dector zezo kinji"
Yafaɗa cikin kwantar da murya kamar ba Ali ba.
"Zafi nakeji bara nai wanka dan Allah kozaka cewa babansu mufida ya kawon kankara, kullum innace ina so se maman mufida tace bazan shaba wallahi ni kaɗai nasan zafin da jikina kemin kofa zazzaɓi nake bana rufa sabida zafin jiki"

Tafaɗa muryarta tana rawa.
"A,a bazaki sha sanyi ba kibari likitan dai yazo yanzu mai zakici?"
Juya mai ƙeya tai tana kallon ƙofa tanajinshi yana ɓaɓatunshi tai masa banza itafa ala dole ya bata haushi
Tashi yayi ya janyo ledojin dayazo dasu ya miko mata gabanta.
"Ki duba kozaki samu abinda zaki iyaci"
yafaɗa yana mai zama agabanta.
"Nifa na gaya maka kankara zansha da lemon fanta".
"Kamar yaya?"
Ya tambayeta.
"Ka ɗaukon kofi ka juyon lemon seka sakan kankara ciki ka ƙaran ruwa zantashan abuna har gobe"
"Gaskiya bazaki sha sanyi ba wallahi kinjima na rantse".
Yafaɗa mata fuskarshi daure.
"Tom shikenan"
Tafaɗa gwanin tausayi.
Sannan ta mike ta nufi uwar ɗaka tabarshi anan batare data bude ledojin ba.
Dafe kanshi yayi ahaka umman mufida wadda batasan da zuwanshi ba tayo sallama tana cewa.
"Haba anty bebi yau tun safe bakici komaiba kinata zama ahaka ga awarar na samo miki wallahi seda na fita wajan gari wai ko baccin nedai baki tashi ba?"
Tafaɗa tana yaye labulan ɗakin ganinshi a zaune yasa tai saurin komawa tana mai jin tsananin kunyarshi.
Tashi yayi ya nufo tsakar gidan ya ikota.
A mutunce suka gaisa.
"Kayi hakuri wallahi bansan kana gidan ba dayake ban lura da motar taka bama"
A sake yace mata.
"Lah babu komai ina laifin mai kula maka da naka nagode sosai da kokarinki tace ke kike miko mata abinci ma angode"
Murmushi umman mufida tai.
"Wallahi oga yarinyar ce take bani tausayi sabida cikin naku mai tsurfane ga laulayi mai zafin gaske bakaga yadda take fama ba, kagafa yau tun safe ko ruwa bata kai bakinta ba ta dage se tasha lemo da kankara wai na gayawa babansu ya siyo mata nikuma naki sabida kasan yadda sanyi ke lalata yaro aciki shike sakawa a haifi yaro da cutar limoniya, to shine tace awara kuma kasan babu anan wallahi seda na fita da kaina na samota ka ganta yanzu a hannuna"
ta miko masa robar awarar.
Sosai yake mata godiya sannan yace ze bawa goma sako ya bata.
"Amman in tanason awarar sena saka akawo wake ana yi mata in ba takura?"
A sake tace.
"Wani takura kuma oga bara dai mugani kasan abin masu ciki hawa da saukane in tai na'am tana ci ɗin ai seka siyo matan".
Godiya yayi mata kana ta juya ta fita daga gidan.
Shiga ɗakin yayi ya sameta kwance a saman kafita rannan a haɗe tamau jira take ace mata ket ta fashe.

A tsaye ya tsaya akanta.
"Ga saƙonki inji matar goma ki fito falo ina jiranki".
Yafaɗa yana mai komawa falon ya zauna.
Cikin sauri ta fito sanin sakon nata.
Washe bakinta take tare da zama agabansa ta amshi awarar ta budeta jikinta yana rawa ta somaci hannu baka hannu kwarya.
duk yawan awarar seda ta cinyeta tass har tana neman kari.
"Dan Allah akawon wata wallahi akwai daɗi"
Murmushin jin daɗi yayi ganin taɗanci abincin.
"Tom ga kifi nan da kayan fruit awarar kuma za,a siyo wake se ana yi miki"
Janyo ledar tayi kamar abin arziki ta bude ta kifin taɗan yagi kaɗan takai bakinta.
Wani masifaffan amai ne ya taso mata wanda kafin tai yunkurin tashi tuni yagama wankesu tas ta amayar da duk awarar dataci jan gefe tayi tana zuba uban Nishi tare da dafe kanta dake mata ciwo.
"Sannu"
Yafaɗa a kasalance da tausayawa.
Da kansa ya gyara ko ina harda fesa turaren daki sannan ya ɗagata ya kaita tsakar gida ya tube mata kayan jikinta.
Komawa ɗaki yayi ya sauyo kaya ya fito da wanda ya tube ɗin ya tari ruwa a famfo ya wanke mata jikinta, se wani kare kirjinta take da hannu haka  ya sunkuceta yakai saman kafita kana ya komo tsakar gidan omo ya zuba saman kayan nasu.
First in history Aliyu sunkuye gaban famfo yana wanki abinda ko singlet ɗinsa bai taɓa wankewa ba sabida sunada washing machine ɗinsu agida,amman yau soyayya da tausayi ya sakashi sunkuyen wankin kayan aman bebi, hannunshi na masa zafin rashin sabo amman haka ya daure ba ƙyamata haka ya wankesu tass ya shanya ya wanke tsakar gidan sannan ya nufi toilet yay wanka tare da ɗauro alwalar magariba ya nufi ɗakin.
tana zaune saman kafita ta sauya kaya zuwa doguwar riga.
Tana rike da carbinta ahannu ta kammala azkar ya shigo ɗakin ganinshi daure da tawul yasa taɗan kauda kanta sabida yadda ya cika mata ɗakin da girman jikinshi.
Gaban jerin kayansa ya nufa ya shirya cikin farar jallabiya sannan ya tako gabanta.
"Sannu gimbiya bara naje nai sallah kafin dector ya karaso kema ya kamata kiyi sallah kafin na dawo".
Murmushi tai kaɗan tana kallonshi.
"Hmm bara naje na
 wanke kayan can ai naji daɗin jikina wallahi ba kamar ɗazuba"
Dariya yay kaɗan.
"Sedai ki wankeni amman na kammala wanke kayan ay"
zaro idanu tayi waje can kuma setai rau rau da idanu.
"Haba ka dawo ko abinci ban baka ba ban kai maka ruwan wanka ba sannan na haɗaka da aikin da baka da ƙwarewa akansa ai da tausayi ma wallahi nidai kadama ka wanke barshi xan wanke abina".
Tsira mata idanu yay yana kallonta.
"Nafa wanke karki damu ni ay kin biyani bazaki gane komai ba sena dawo xaki bani abincinki

mai daɗi Allah yasa na wannan karon yafi na ko yaushe"
Da sauri ya fita jin ana kokarin data sallah, itama a hankali ta mike ta fita tayo alwala ta dawo ta tayar da sallah.
Tana zaune saman sallaya suka shigo bayansa wani mutum ne dogo siriri Allah yasa da hijab jikinta shima ganinta shirye yasa ya mayar da ajiyar zuciya daman baima kawo tana falon ba shiyasa suka shigo da dector ɗin.
A mutunce suka gaisa da likitan har yana tsokanar Aliyun, sannan ya fara fiddo da kayan aikinshi.
Gwaje-gwaje yay mata sannan ya bata wata kwalba yace taje tayo fitsari yanzu ta kawo masa.
A kunyace ta amsa shiko Aliyu ko ajikinsa sema hirarsu dasuke shida likitan.
Bayan ta kawo masa xama tayi agefe guda tana kallon yadda yake zuba fatsarin awani dogon abu, mintuna kusan goma ya kammala komai cike da ƙwarewa akan aikinshi ya dubi Aliyu.
"congratulation mr Aliyu madam fa tana ɗauke da juna biyu na tsayin kwanaki goma"
Cikin farin ciki Aliyu ya mikawa dectorn hannu suka kuma musaba sannan yace.
"Masha Allah dector kenan kwana ɗaya ne abin ya samu sabida yaufa kwananmu sha biyu da aure".
Murmushi likitan yay.
"A daren farko ma ana iya samufa bare washe gari lallai kai gwarzone Allah ya inganta ga magunguna zan haɗa muku na karin jini sannan kana kula da ita sosai wannan zafin jikin kuma karka damu zata dena soon insha Allah".
"Nagode amman tana amai fa"
"Okey shima in tana shan wancan jan maganin dana baku zeɗanyi sauki kasan shi wannan daman ko wacce mace tana yinsa inta da ciki marasayin basu da yawa"
"Ok nagode"
Haɗa kayansa yayi likitan kana ya dubi Bebi wadda take kunshe fuska.
"To madam Allah ya raya semun zo suna"
"Dariya Aliyu yayi kaidai yau dr kana ta babbar kyauta wallahi muje mota"
Fita sukai atare.
Da sauri bebi tayi daki tana dariya wai yau ita take da ciki  oh daman haka mama tai ta fama lokacin datake da cikinsu katifa ta faɗa.
"Naiwa ƴata wanka na saka mata pampars taimin kuka nai mata rawa"
Tafaɗa a fili tana dariya.
Sallamar dr yay da kudi masu yawa kana ya dawo ya tarar da ita tana dariya a ɗaki ita kaɗai zubewa yay agabanta.
"Kema kina murna xaki haihu kenan?"
Ya faɗa yana ɗage mata gira ɗaya.
Bata ce mai komai ba ta rufe fuskarta tana dariya.
Wayarshi ya  dauka ya soma neman layin ammi.
Bugu ɗaya ta ɗauka bayan sun gaisa ya soma ratta ba mata bayani.
"Ammi fa yau bazan dawo gida sabida Mai sunanki batada lafiya dr kuma yace ciki gareta ai mana addu'a ammi"
Sosai ammi tahau murna tana hamdala nan tace ya bawa bebi waya amman fafur bebi taki amsa haka ammi tai masu fatan alkairi ta katse wayar usman ya kira ya shaidawa aifa nan

usman yayta murna yana masa tsiya wai yacika haɗama.
Numbern mama ya kira wadda yacewa usman ɗin ya tura masa to bayan ya turo masane ya soma kira.
mama duk suna asibiti wajan ladi hassana  ta miko mata wayar amsa tai tare dayin sallama bayan ta ɗaga.
Jin muryar Aliyu yana gaisarta yasa ta saki fuska a nutse suke gaisawar.
Jimm yay kafin kuma yace mata.
"Mama ai mana addu'a dan Allah"
Murmushi mama tayi sannan tace.
"To Allah ya dafa maka adukkan lamuranka"
"Amin mama sedai fa mama kinyi jika wai bebi tana ɗauke da juna biyu ɗazu dr ke shedamin gatama zakuyi magana"
Yafaɗa batare dayaji kunyar hakanba sabida yadda yake ɗaukin cikin.
Kunyace ta rufe mama amman jin muyar bebi yasata dole tai magana.
"mama kun manta dani ko? ina nan bani da lafiya akawon ihsan mama"
Murmushi mama tai irin nasu na manya sannan tace.
"to naji uwar ƴan raki haka kike masa wannan sangartar halan? to dai ki kula da kanki da wayonki na samu cikin arfa sabida haka ki kula da kanki Allah raba lafiya amin".
Murmushi bebi tayi"mama anty hassana fa?"
"Gata"

Mama ta mikawa hassana wayar wadda ta amsa tana murna.
Nanfa hira ta barke har hassanar ta bawa sauran suka gaisa sannan suka katse wayar kamar kada su rabu.
"Oh ni aishatu yaran yanzu babu kunya wai mijin bebi ne kecemin batada lafiya tana da ciki"
Dariya babar ladi tai da inna suwaiba kanwarsu abban bebi kana sukace.
"To ai zamanin ne se a hankali yaran yanzu kamar jira suke daga an haɗu se ciki, Allah ya raba lafiya wannan aure ashe rabone yasa akayishi cikin gaggawa".
Nanfa hirar lissafin cikin ta barke.
"Aini tun yanzuma zan soma haɗa kayan yajina kafin barkono ya tashi"
Cewar inna suwaiba kanwar abbansu bebin.
Dariya hussaina tai.
"mama zata goya jika Allah mai iko"
Mako mata hannu mama tai.
"Babu ɗan dazan goya kowacce cikinku tai goyon abinta"
Sosai suka sake suna hirarsu har lokacin da suka tashi tafiya sukai sallama suka tafi, koda suka koma gida mama kamar tai tsalle dan murna lallai Allah ne abin godiya a koyaushe tana godiya ga Allah daya axurtata da ƴaƴa mata nutsatstsu waɗanda ta raina ta  basu tarbiya ingantacciya har Allah yasa yanzu zata soma amsar jika daga gurinsu.
********

Ita ko bebi tana gama waya da mama ta koma jikinshi ta kwanta tana lumshe idanunta.

Kamata yay suka koma falo tea ya haɗo mata data sha tasha magani taɗanci apple ɗin dayazo da ita, Anan sukai sallar isha'i ta koma kan cinyarshi ta kwanta hannunta ta saka tana ɗan jan gemunshi kamar yadda umman mufida ke mata lecture akan yawan wasa da sassan jikin mijinki amman inda yafi ɗaukar hankalinshi alokacin da kuke keɓance da juna,
"Kasan ɗazu banji dadin wanki dakai ba"
Yaji maganarta.
"Saboda me?"
"Sabida Allah"
Murmushi yayi amatse yake da ita amman baison ya nuna mata hakan kodan lalurar jikinta, shiyasa ma shurun tasa tai yawa.
Hamma tayi tare da mikewa ajikinshi ta bankaro mai kirjinta tare da cewa.
"Bacci nikeji wallahi"
Haɗiyar miyau yay kana yace.
"Okey" ararrabe muryarshi can kasa alamun ya soma hawa network.
Ɗaukarta yayi zuwa bedroom sauya kaya sukai ita ta saka wata half gown ta bacci shikuma ya bar only boxer'n jikinshi batare daya saka komai ba kwanciya sukai bayan ya shafe musu jikinsu da addu'ar tsari.
Ruɗa mata jiki ya somayi da salonshi tare da haɗe bakinsu waje ɗaya hannunshi zube a kirjinta yana sarrafa mata su,cikin kankanin lokaci komai yagama sauyawa soyayya mai tsayawa arai yake gwada mata sosai suka kasance tare har lokaci mai tsayi kafin ya zare jikinshi anata ya sunkuceta sukai bayi wanka sukai suka koma baccinsu.
Da asubahi ma da ƙyar ya barta yana dawowa suka koma ruwa wanda ranar ko office baije ba seda usman yay masa waya yace jinya yake, yinin ranar sallah cin abinci kaɗai ke tadasu sabida cikin bebi mai jarabar nacin mijine shiyasa baya gajiya itama kuma bata gajiya nan da nan aman ma ya tsaya hakannan zafin jikin nata ya dena kobai nemeta ba ita zata saka masa kuka ala dole seya kara abin har mama yake bashi, seda yay mata kwana biyu kamar na dija sannan ya soma kokarin komawa gida wannan karonma seda tai kuka sannan tabarshi ya tafi, koda ya koma gida shima a sukuku yake baya wani samun sukuni ga shige da ficen karar su khalipha wadda yau sauran kwana ɗaya ashiga kotu wanda ranar ta kama zagayowar girkin bebi.
Babu laifi yana bawa dija kulawa itama irin ta aurarayya, ranar daze koma gidan bebi cewa dija yay zeje legos, ze kwana biyu haka ya shirya ya nufi kotu wadda yau ɗin za,a soma gabatar da karar da karfe goman safiya gaba ɗaya kotun ta cika khalifa kaɗai ake jira domin hatta ladi ma ta sami zuwa kotun wan aka ɗaukota daga asibitin
Karfe goma saura alkali ya shigo wanda suma su kalifan suka shigo kotun shida ubansa da yan gidansu da lawyansu hakannan Ya nura tare da sauran lauyoyin da Ali ya ɗauko suma sun hallara dan haka alkali ya soma magana kamar haka.............

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*# *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*98*

"Kotu tana buƙatar ganin ladi tasi'u tare da wanda take ƙara khalifa alhaji mai gwall"
Cikin rashin sabo ladi ta nufi ɗan gaban katakon nan da waɗanda ake tuhuma ke tsayawa khalifa ma ya nufi na gefenta ya tsaya, alkaline ya dubi mai gabatar da ƙara kana ya bashi umarni akan ya karanto ƙarar.
Tiryan tiryan mai karanto kara ya karanto komai na abinda barrister nuraddin ya shigar sannan kotu ta nemi lauyan wanda ake kara koyana da abinda zece.
Cikin kasaita wani kakkauran mutum ya mike.
"Sunana barrister salim mai goro, nike kare khalifa Alhaji mai gwal abisa shaidar kwararan hujoji...........nan ya soma karanto karya da gaskiya domin ya kare khalifa daga karshe ya ɗora

da cewa sharri sukaiwa khalifan su basu san komai nakan lamarin ba.
Kana ya koma ya zauna.
Cikin tsanaki alkali ya dubi ya nura.
"Barrister nura ko kana da wata hujjar tare da shaidar gani da ido?"
Cikin nutsuwa ya nura ya mike.
"Assalamu Alaikum, sunana barrister nuraddin adam rimin gado nike shigar da karar khalifa abisa cin mutuncin wannan baiwar Allah dayay bayan ya aureta a ranar yay mata cin zarafi ajikinta kana yazo ya rattaba mata saki har biyu wanda abinda ya faru da ita seda ya saka har aka kwantar da ita a asibiti sabida haka inada shaida ƙwaƙwƙwara daga wajan nurse ɗin data dubata aranar"
Ya numfasa sannan yace.
"Ina neman kotu mai adalci data bani damar bayyana shaidar nurse tare da drivern gidan wanda agabanshi akai komai"
"Kotu tana neman nurse ɗin data ma ladi dinki tare da drivern gidan alhaji"
Cewar alkali.
Cikin nutsuwa wannan nurse ɗin data soma duba ladi ta bayyana tiryan tiryan ta bayyanawa kotu komai daya faru sosai mutan cikin kotun suka firgita da abin hakanan drivern gidan alhaji wanda su Aliyu suka shawo kansa da kyar shima ya bayyana nasa shaidar.
Nan da nan zufa ta karyowa kalifa idanunshi ya soma raina fata.
"Ko lauyan wanda ake kara yana da abinda zece?"
Girgiza kansa yayi sabida baya da abinda zece.
"Br salima baka da abinda zakace? khalifa kuma fa?"
Nan ma shuru.
Kotun ce tai tsit shikuma alkali ya sunkuyar da kansa a ƙasa yana rubutu a farar takarda.
Yana kammalawa ya ɗago.
"Abisa yadda kotu ta yanke hukuncinta cikin adalci, kotu ta yankewa khalifa hukuncin zaman gidan kaso na natsayin shekaru uku tare da horo mai tsanani Batare da bada beli ba, tunda aikine yay na ganganci, sannan ze bawa ladi tarar kuɗi naira miliyan goma"
Kana ya tashi nan fa kotu tahau tsine yan sanda ne suka sakawa khalifa ankwa aikwa nan alhaji ya zube atake anan   ya suma mahaifiyarshi kwa binsa tai tana kuka.
Dakatawa yayi yana kallon mahaifiyar tasa.
"Momcy nayi nadamar zuwa a ɗanku domin kuba mahaifan ƙwarai bane tunda baku bamu tarbiyar kwarai ba duk abinda mukeso shikuke mana ashe akwai ranar dazan girbi abinda najima ina shukawa kuma ba kowa yajamin ba face ku, momcy naji na amince zanje domin na gyara halina ko Allah ze yafan laifukana dana jima ina aikawata in baba ya farfaɗo kice masa kadama yay wahalar fito dani domin nayi nadama gwarama ya barni naje na girbi abinda na shuka acan sannan ku rokarmin ladi ta yafemin"
Ƴan sandane suka saka keyarshi a mota sukabar mamansa tana kuka!
Da taimakon ƴan sanda aka saka Alhaji mai gwall a mota aka nufi asibiti dashi domin barin jikinshi ya tabu koda aka kaisa asibitin ma taimakon gaggawa aka soma bashi sedai duk yadda akaso a dai daita lamarin Allah baiba sabida zuciyarsa ta sami bugawa tare da cutar barin jiki cikin mintuna goma Alhaji yace ga garinku nan ya rasu da tsananin takaicin halin daya jefa ɗansa ya rasu da takaicin yadda abinda yake ganin yafi karfi gashi shiyazo yafi nasa karfin.

Sosai iyalinsa suka gigice suna kuka ba khalifa ba alhaji nanfa duniya ta juya musu baya a rana ɗaya lallai Allah abin tsorone.
Haka aka naɗo gawar akayo gida da ita.
Ladi kwa gida aka wuce da ita tare dasu Aliyu sosai su kawu tasi'u kewa Aliyu da nura godiya su Ali na kokarin tafiya gida sakon rasuwar mai gwall ya samesu sosai sukaji abin tare da nema masa gafarar Allah kana sukai sallama dasu kawu suka tafi.
Itama ladi maman su bebi tabi can gidan tace ita ta koma wajan ƴan uwanta.
Daga ƴan kusa, Aliyu gidan bebi ya wuce sabida yanzu yanajin ya sami nutsuwa dayaga ya kwatarwa yarinyar can hakkinta sedai gefe ɗaya kuma tsananin tausayin kalifa ya kamasa na rashin mahaifin dayay ga kuma yadda rayuwar ta koma masa shiyasa ake son kawaita addu'a akan ƙaddararka Allah yasa tazo maka a mai kyau.
Dama tun safe umman mufida ta wankewa bebi kanta da karkashi dasu ƙwai da zuma, zaman kitso sukai inda tai mata kananun kitso mai kyau irin na ƴan maiduguri, lalli tai mata ja wanda ya haska farar fatarta.
Da taimakonta suka haɗa masa abincin gargajiya wanda suka haɗa mai burafusko da miyar taushe gyara gidan bebi tayi ta kunna turare kana ta gyara kanta cikin wasu shegun riga da wando.
Jera mai kayan tai a falo kana ta harde a saman sopa tana kallon kofa.
Aikwa tanajin budewar ɗakin tai maza ta mike ta nufeshi ta rungume shi tana furta.
"Barka da zuwa i missing you" tafaɗa tana kwanciya akirjinshi.
Shafa kanta yayi tare da ɗora bakinsa a goshinta yana sumbata.
Da taimakonta yay wanka ya shirya sannan ta haɗa mai kayan abincin yana ci yana tambayarta ya ajiyarshi kuma koda wasa bai nuna mata cewar ga lamarin dake faruwa da gidansuba domin duk hidimar dayay musu da karar kalifa da komai bai sanar da itaba haka zalika bai gaya mata shiryawarsu da dangin mahaifinsuba.
Sedai hirarshi akan bebinsa ne na ciki da kuma hirar love.
Seda ya kammala komai na game da cin abincinshi sukai sallah sannan ta haye saman cinyarshi tana nuna masa lallanta.
Hannun ya kama ya zira yatsan a bakinsa yanasha kamar alawa, zame ɗan kwalin kanta yayi yana shafo kitson nata.
Hannunshi ya saka ya zagaye ƙugunta yana hura mata hiskar bakinshi cikin kunnenta.
"Ummi kinyi kyau kamar na cinyeki nikaɗai nasan mi nakeji ajikinki pls ki karamin yawunki nasha na koshi".
yafaɗa yana mai bude bakinta ya zira harshenshi yana zuƙe miyan bakinta yana lumshe idanunshi,hannunshi ya ɗora a kirjinta yana matsa mata na shanunta dasukai wata mahaukaciyar cika kamar xasu fasa kirjin nata, lumshe idanunta tai tana jan ajiyar zuciya tana fesar da numfashi, ganin wankin hula na neman kaisu dare yasa ya sunkuceta yay bedroom da ita a haukace yake rudata da zafafan romancig ɗinshi kafin ya kama hanyarshi inda nake jiyo kukan daɗin bebi danashi.
Ranarma sunyi matukar jiyar da junan su daɗi bakaɗan ba harda asubahi suna tare kafin suyi wanka ya wuce masallaci.
****************
Legos washe garin talata Alhaji idiris mai atamfa zaune a airport na legos yana son ya dawo

kano yau sabida yadda bayajin daɗi kwana biyu  na jikin nashi cikin farin ciki Alhaji isyaku shima wanda ke kokarin zama a gefen abba ya dubeshi.
"A,a mai atamfa nake gani anan ne kamar kwa kasan ina nemanka wayarka bata shiga, nima yanzu haka kanon nayi wallahi aminina Alhaji mai gwall ne ya rasu jiya"
Cikin jimami abba kewa haji isyaku ta'aziya sannan ya karasa da cewa shima zeje kano ne unexpected sabida bayajin dadin jikinshi.
Hira suke da Alhaji isyaku kafin a soma kiran sunaye.
Sabida suna a waiting room ne.
"Niko Alhaji idiris ina son nai maka murna kuma Allah bai ba, ashe baba Ali yayi aure to Allah sanya alkairi ai munje ma kofar gidan matar tasa har ina karyata auren nasa sabida nasan zuri'arku bakwa AUREN BARE! amman yadda naji tabbacin auren ne yasa na yarda ai yarinyar nasan har mahaifanta ƴan mafuta ne"
Murmushi abba yay.
"Alhaji isyaku auren Aliyu yazone a kure kasan yar gidan kanina marigayi ya aura, amman har yanzu muna kan bakammu na rashin AUREN BARE! Aliyu ƴata ya aura ai"
Murmushi haji isyaku yayi.
"Kasan girman Allah Alhaji idiris Ali ɗanka yay aure kuma yarinyar daya aura ita ɗan gidan marigayi mai gwall yaso aura se Aliyun ka ya rigashi yanzu ma haka akan case ɗin yaron fa mai gwall ya sami heart attack"..............tiryan tiryan Alhaji isyaku ya zayyanewa abban Aliyu komai batare daya rageba hatta ƙaryata mai unguwa da haji isyaku yay seda ya gayawa abba, ( in baku manta ba alhaji isyaku shiya karyata mai unguwa lokacin daurin auren kalifa da bebi ku duba shafukan baya kuma isyaku kunsan abokin abba ne daman bashine harya kira layin abba yaki shigaba).
zuface take karyowa abba kota ina yana ina hakan ta faru?
Maganar isyakuce ta karade masa kunne.
"Yakama Alhaji fa ku daina wannan al'adar ta rashin AUREN BARE sabida ba addini bace kama godewa Allah dayasa aure yay ba karuwa ya aje ba bana gaya maka wannan maganar dankai fushi da ɗanka ba nagaya makane domin kuyi saurin gyara ɓarakarku kafin a haifi ɗan da baya da idanu"
Yana gama faɗin haka ya tashi domin an kira sunanshi, seda aka zo kan abba shima ya tashi ya shiga cikin jirgin jikinshi yay sanyi kalau.
Koda suka sauka kano ma baiwa kowa wayaba haka ya dauki napep har gida a falon alhaji babba abba ya yada zango lokacin karfe goman safiya sosai Alhaji babba yake faɗa lokacin da abba yagama shaida masa komai nan da nan aka kira meating na gaggawa iyalin mai atamfa ƙwansu da ƙwarƙwatarsu sun hallara a falon alhaji hatta khadija dasu usman wanda cikinshi ya duri ruwa.
Abba rike da waya yana kiran layin Aliyu amman anki ɗagawa secan ya ɗauka cikin ladabi yake gaida abba.
"Bana bukatar gaisuwarka Aliyu maza kazomin da wannan yarinyar daka aura yanzu ina falon alhaji"
Ƙittt ya katse wayar zuface ta soma karyowa Aliyu rana dubu ta ɓarawo..

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payment domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*# *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*99*

Rana ɗaya kuma ta mai kaya inji bahaushe, zama yayi a bakin katifa tare da saka hannunshi guda ɗaya ya dafe saman kanshi gaba ɗaya tashin hankali yagama mamaye zuciyarshi arayuwa baya son ɓacin ran mahaifinshi ko kaɗan tabbas yasan a wannan karon sesun sami gagarumar matsala da abban nashi, sharce zufar data karyo mashi yayi tare da furta.
"Innalillahi wa'inna'ilaihirrajun, ubangiji ka kawomin sassauci acin wannan cakuɗaɗɗan lamarin" yafaɗa tare da mikewa tsaye.
Ya soma shirya kanshi cikin wani brown boyel mai yankan manyan sukari tare da ɗora hula a

saman kanshi takalmi ya saka mai kalar kayan jikin nashi, turare ya fesa mai daɗin kamshi tare da ɗaukar wayarshi da makullin motarshi ya fita daga ɗakin.
Bebi tana falo a zaune tana shan tea wanda ko sugar babu acikinshi sabida yadda bakinta yake babu ɗanɗano ko guda dan ko abincima a wannan lokacin se Ali yayi mata jan ido take turawa tana kuka! wanda baya minti ɗaya kuma seya dawo tass.
Akanta ya tsaya tare da kallonta fuskarshi babu sukuni.
"Tashi ki ɗauko hijabi zamu fita"
Da kallo ta bishi tana nazarinshi amman ganin yadda ya haɗe girar sama data ƙasa babu alamun wargi yasa tai maza ta janye tea ɗin daga gabanta tana yatsine fuskarta daman tunda taga suna tare an kirashi a waya ya tashi yabar falon ya koma ɗaki tasha jinin jikinta abinda yasa bata bishi ba dan karyace tana masa bin diddigine.
"Lafiya dai ko? naganka ba kamar ɗazuba?"
Tafaɗa cikin kwantar da murya kamar yadda umman mufida ke gaya mata aduk sanda zakaiwa mijinka magana yazama ka tausasa lafazinka tare da kwantar da muryarka.
Agogon dake ɗaure bisa tsintsiyar hannunshi ya kalla.
"Kinga 1:00pm dan Allah kiyi sauri ina mota ina jiranki"
Ya fita da saurinshi.
Cikin mutuwar jiki ta mike zuwa bedroom wani coffee hijab ta ɗauka har ƙasa ta ɗora saman doguwar gown ɗin material ɗin dake jikinta tare da saka plate shoe ta fito cikin sauri tana tafiya kamar iska zata ɗebeta cikin tsanaki ta mika hannu ta bude marufin motar ta shiga wanda shi harya ma kunnata domin ita kaɗai kawai yake jira.
Revars yayi kana ya nufi wajan gate ya fita daga gidan.
Redion motar ya kunna batare daya mata magana ba, ta kula yau ƴan shariyar nashine suka motsa masa kokuma akwai abinda ke damunshi acikin zuciyarshi.
Sosai yake falfala gudu a saman kwalta har ya sami zarafin barin arean unguwar ganin ya ɗauki hanyar da gidansu yake yasa komai nata ya tsaya cak.
Har lokacin daya ƙarasa cikin unguwar tasu, abakin gate ya dakata tare da danna horn masu tsaron gate ɗin sukazo suka bude masa suna masa barka da zuwa.
A harabar wajan adana motoci ya parker motar ya kashe tare da balle murfin ya fita.
Haɓa ta riƙe tare da gyara zamanta batare datayi yunƙurin binshi ba, har ya kusan ɓacewa daga gurin ya juya yaga bata biyosa ba tsaki! yaja a fili tare da komowa kansa ya zira ta cikin glass ɗin motar.
"Kifito mana ya kike ɓata min lokacina"
Da sauri ya saka hannu ya buɗe murfin motar yana tsaye ta fito a wannan karon yaɗan sassauta saurin nasa suna jerawa tare sedai bai ce mata komaiba.
part ɗin alhaji babba ya nufa dukkan ilahirin jikinshi yayi sanyi amman dayake shiɗin namijin duniyane babu ta yadda zakai ka gane halin dayake ciki sabida ko saman fuskarshima bata nuna hakanba.
Kofar babban falon alhajin ya bude wadda daman anan ake tattauna dukkan wani important issues na cikin zuri'ar tasu.
Zare idanunshi yay lokacin dayay katari da mutanan dake falon domin babu wanda bai sami zarafin halartar wannan wuriba hatta zee datake jego seda ta amsa kira, sedai su umar da basa gari.

Sallama yayi kanshi sunkuye ya kutsa cikin falon wanda ƙannenshi suka sada kansu ƙas sauran iyayenshi kuma suka zuba masa idanu.
Bebi na biye a bayansa wadda ilahirin jikinta yake rawa musamman yadda taga idanun kowa yayo kanta caaaa akai mata da ido ana kallonta.
Abba wanda tun ɗazu ya kasa zama se faman kaiwa da komowa yake wayarshi ahannu cikin sauri ya juyo ga Aliyu dake kokarin gaisar da abban bauchi.
Tas! tas!! tas!!! falon ya ɗauki sautin tagwayen maruka uku ciff da abba ya wankewa fuskar Aliyun dasu.
Cikin wani irin yanayi bebi ta silale a jikin bango ta raɓe tana rintse idanunta sabida yadda taji marin kamar ita akaiwa.
Itako khadija tun shigowar bebi takejin gabanta na wani irin bugawa sam bataji marin mijin nata ba gaba ɗaya hankalinta da idanunta yana kan bebi tai mugun zuba mata idanu ko kiftawa batai.
Karuwarshi ko matarshi no karuwa dai domin tasan zuri'arsu basa AUREN BARE! rintse idanunta tai gam tana kiran sunayen Allah.
Kafin maganar alhaji babba ta karaɗe wurin.
"Kaimin dai-dai idiris daka mari shasha Aliyu muzaka zubarwa da ƙima muzaka tozarta muzaka kwancewa zani a kasuwa muzakaiwa abin kunya a cikin zuriya?"
Yafaɗi hakan cikin cakuɗaɗɗiyar hausar data saka kowa cikin zulumi wanda tuni zuciyar wasu ta soma raya musu Aliyu karuwa ya aje agidansa.
"Dakata Alhaji"!
Ammi ta mike a matuƙar fusata wadda tunda abba ya aurota bata taɓa yin irin wannan maganar ga dukkan ahlin nashiba.
"Ta yaya kake jefarmin ɗa da irin waɗannan munanan kalaman waɗanda suke kaman ceceniya da zaman dadiro...........,
"Bilkisu koma ki zauna kada in kuma jin maganarki in ba hakaba ranki ze mugun ɓaci"
Abba ya faɗa cikin zafin rai.
"Wallahi idris bazan komaba ta yaya kai kana gani za,a lalata auren ɗanka sabida wata banzar al'adar daba addiniba sannan kai shuru to wallahi senai magana koda zakace yau ƙarshen igiyoyin aurenmu dakai ya ƙare Aliyu auren sunna, yayi da sanin ƴan uwanshi abubakar da usman su'suka wakilci aurensa kuma abubakar shiya miƙa sadakin auren nasa sun ɓoye mukune sabida banzar ɗabi'arku ta rashin AUREN BARE! Wadda nake addu'a Allah ya rusa wannan al'adar kowa ya sami ƴancin kanshi".
"Dakata bilkisu!
Alhaji babba ya faɗa tare da mikewa.
Shiko abba ƙasa yay da kanshi yasan ran ammi ya ɓaci tunda tace abbakar kai tsaye tace idriss kai tsaye wanda bata taɓa faɗin sunanshi ba tunda ta haifeshi sabida alkunya ta ɗan fari hakanan bata taɓa faɗin sunan shi abban ba sabida alkunya itama abba take faɗa mai kamar yaranshi ammi macece mai kawaici da hakuri yadda yaji yau ta mike tana wassafa magana yasan ranta ne ya ɓaci.
"AUREN BARE Baya cikin tsarinmu dana iyayenmu sabida kina ganin kin isa kin kai kin kawo shine zaki dubi idanuna ki gayamin wadda duk ta fito abakinki ko? madallah to nagode amman ki sani wannan aure dashi da babu duk ɗayane a wajanmu sabida haka a yanzu base anjima ba

kai tsageri marar mutunci inason ka saki waccan yarinyar ka bata takardarta ga matarka nan hadiza ƴar uwarka ta jini da ita muke son ka zauna ba BARE ba! domin bazamu lamun AUREN BARE  a mai atamfa family ba"
Alhaji babba ya kare maganar yana mikawa Aliyu takarda da biro, Bebi kafe tsohon tayi da idanu tana kallonshi maganarshi ta ƙarshe tafi kalmar sakinta dayace zafi acikin zuciyarta. Lallai namiji munafuki ne au ashe daman yana da mata yake wannan rawar jikin akanta jar bura'uba! lallai ya gama da ita ƙarewa ma matar tashi ƴar uwarsa ce lallai ya cuceta!!!
Falon ne yay tsit illah sautin kukan dija dake tashi sannu a hankali tanajin duniyar tana juya mata Aliyu yayi aure? da wadda take hango tsantsar sonta a gareshi wayyo taga takanta itakam.
Haka zalika umman khadija datai zaman dirshan tana share zufa.
"Amsa nace"
Alhaji babba ya dakawa Aliyu tsawa wanda ko motsi ya kasayi illah kansa daya sunkuyar kuma har yanzu yana duƙe ne agaban abban bauchi wanda tun fara maganar baice komai ba, usman kwa ji yake kamar yaje ya naushi Alhaji haka zalika ya abbakar hankalinshi yay matukar tashi,gaba ɗaya falon tsitt ya ɗauka.
Ɗago da jajayen idanunshi yayi waɗanda suka kuma girma jijiyar kanshi ta mike tai wani irin ruɗu-ruɗu zubawa alhaji babba idanu yayi batare dayay shakkarshi ba yace.
"Alhaji kayi hakuri wallahi bazan saketa ba sabida inason matata! kuma ai AUREN BARE ba haram bane bafa zan saketa ba wallahi kozaka mutu haka nan addini ya haramta sakin mace mai juna biyu akan me zan saki matata da cikin sati biyu ajikinta?"
Yafaɗa yana mai miƙewa tsaye yana jefawa alhajin wani irin kallon raini.
Gaba ɗaya falon hayaniya ya ɗauka kowa yana na'am da maganar Alin domin daman yawanci mazan biyayya suke bawai son wannan auren haɗin suke ba.
Gyaran murya abban bauchi yay wanda daman shi baice komai ba tun farkon maganar.
"Zauna babana, ya dubi Aliyu a tsanake.
Zama yayi cikin na'am da maganar abban bauchin sabida mutum ne shi mai feɗe gaskiya wannan dalilin ne yasa ma suke yawan samun matsala da alhajin.
"Haba yaya ta yaya zaka ringa tilaswa yara Auren da basuyi niyya ba wannan fa abun ba addini bane ba yanzu hakan ku bai ishemu ishara ba? yanzu inda karuwa ya ajefa dafa haka za,a kawo mana ɗan shege mu goya amman ku duba auren nan nasa abubakar da usman su suka goya masa baya yayi akanme zakace ya saki matarsa ita khadijan da kuka liƙa masa ai ya amsa yay muku biyayya ku ba seku goya mai baya a binda yake soba kuduba isharar Allah auren da kwana goma sha biyar har Allah ya basu rabo toni dai babu ruwana sabida haka inma zaku aje wannan makaman yakin naku seku aje, kai babana tashi kaja matanka Allah ya baka ikon yin adalci sannan daga yanzuma duk mai son AUREN BARE yaje yayi matukar zeyi adalci Allah ya bashi tagari amin"
Abban bauchi ya faɗa yan mai tashi yabar wajan daman shi abinda alhajin yake yafa isheshi yana musu wata isa da gadara kamar shine ubansu ai wa ba uba bane.
Falon ne ya dauki hayaniya nan da nan kowa ya soma tofa ta bakinshi mazan familyn kwa ihu suke suna cewa.
"Well done yaya Aliyu Allah ya biyaka ka kwato mana ƴanci" haka suketa faɗa wanda hatta ƴammatan ma ba,a barsu abaya ba domin yawanci da samarinsu amman tsoro yake hanasu

kawosu gaban iyayen nasu.
Gyaran murya alhaji babba yayi.
"Tabbas maganar Abban bauchi ta sanyaya mun jikina kuma auren baba Ali yazaman ishara tabbas rabo ma kaɗai ze iya kasheni dan Allah ƴaƴan nan kumin afuwa waɗanda na tursasa sukai auren dole duka kuyi hakuri daga yau najanye wannan al'adar tawa kowa yana da damar AUREN BARE! amman nagartacciya mai tarbiya, tabbas idan har iyaye zamu dinga tilasawa yaranmu auren da basa so tofa za'a iya haifar ɗan da baida idanu, tabbas wannan ma isharace gamu iyaye mu dinga yiwa ƴaƴanmu adalci sabida tsanani tilasawa yaro yana sakawa ya bujirewa mahaifa musamman Aliyu wanda ban taɓa masa magana ya musan ba bantaɓa ganin ɗan albarka kamarshiba baya musu haka nan baya saɓa mana amman yau harni ze duba yace kozan mutu baze saki matarsa ba ya kalli idanun ubansa baiji kunya ba lallai soyayyar shi da wannan yarinya takai ta kawo wallahi inda ba'ai auren bama za,a iya haihuwa a titi, kai idriss karkai fushi da ɗanka maza kai masa afuwa Allah yay muku albarka gaba ɗaya, haka zalika kema bilkisu nasan rankine ya ɓaci har kika jefamin kalamanki na ɗazu abinda baki taɓa min ba tun aurenki agidan nan kikemin biyayya duk tursasawar dazanwa ƴaƴanki baki taɓa ɗaga ido kin dubeni ba sabida haka ban rike ki araina ba Allah ya baki hakuri yayi maki albarka keda zuri'arki Amin"
Amsawa dukkan mutan falon sukai gaba ɗaya. alhaji babba yaji jikinshi yayi sanyi, daman shi abba marinma  dayay wa ɗan nasa dan dai kar alhajin yaga kamar ya daure masa gindine amman shi tun kalaman alhaji isyaku yaji jikinshi yay sanyi tabbas yayi godiya ga Allah dayasa ba ɗan shege aka kawo masa ba.
"Zonan ƴar albarka kiyi hakuri do Allah kada ki rikeni akan nace asake ki kiyi haƙuri ɗiyata"
Alhaji yafaɗawa bebi haka yana  kallonta wadda tun ɗazu ta raɓe tana jin duk maganganun nasu bata ɗago ba sema kasa data kumayi da kanta domin ita kaɗai tasan a halin data ke ciki. Abba ne ya ɗago kansa batare dayace kamai ba.
Yadai zubawa Aliyu idanu yana kallon yadda gaba ɗaya hankalin Aliyun na kan matar tashine data sada kanta kasa taƙi kallon kowa.
Addu'a abba yayi tare da sallamar kowa ya kama gabansa amman yacewa iyalinshi su samesa a falonshi harda surukanshi kaf.
Kowa tashi yayi yana murna, ammi da kanta tazo gaban bebi ta ɗagata suka wuce can part ɗinta.
Abakin kofa dija ta tsaya tana turawa umman ta baki.
"Nace ki kwantar da hankalinki ko? wannan marar kunyar yaron tunda ya furta maganar dayaso agaban alhaji wallahi akan waccan ƴar ze iya sakinki kinafa kallo ciki gareta ke bazaki kwanto ki samuba,so kike ki ɗaga hankali mu tashi a tutar babu? akanta fa yau Alhaji ya rusa al'adar da aka gina sama da shekaru ashirin a wannan zuri'a tamu"
"Amman umma kishiya fa nidai ina son mijina ina kishinsa"
Murmushi umma tayi.
"Kamar yaya kenan ban fahimta?"
"Ina son ya Aliyu tun farko sabida Allah wallahi umma na yada makaman yaƙina na cewar dan dukiyarshi zan zauna dashi nidai kimin addu'a domin yanzu zan fuskanci ƙalubale akanshi Allah yagani inason sa dukiyarshi bata gabana nagane so yanzu na kuma gane son kuɗi"
Mamaki khadija ta bawa, umman tata wadda tsabar zafin maganar yasa umman jan tsaki tabar

mata wajan.
Part ɗin ammi dija tayi duk tanajin babu daɗi aranta.
Gaba ɗayansu ta samu a falon abba,hadda bebi datake raɓe jikin ammi taki kallon kowa ma a falon.
Gyaran murya abba yayi sannan ya dubi Aliyu.
Cikin tsanaki yagama masa nasiha tsaf sannan ya nusarshi kuskuren dayay akan maganganun shi na gaban alhaji daga karshe ya ce masa lallai koyau ko gobe yaje ya bawa alhajin hakuri.
Itama ammi nasihar yay mata tare da cewa taje ta bawa alhajin hakuri sannan yahau ya abbakar da faɗa sosai akan kuskuren da sukai shida usman itama khadija nasiha yay mata sannan ya kirawo bebi itama kamar yadda yaywa khadija nasihar zamansu lafiya haka yayi mata, daga ƙarshe yahau yima su usman tsiya harda cewa daman rana dubu ta ɓarawo rana ɗaya ta mai kaya.
Addu'a akai aka shafa daga karshe kuma aka hau hirar bikinsu amina tashi abba yayi yana duban Aliyu.
"Babana tashi muje asibiti zanga likita nifa nagodewa Allah dayasa ba ɗan shege aka kawon ba Allah yay muku albarka ya ƙara haɗa kanku ami"
Dariya suka saka gaba ɗaya sukwa ƴan biyu saka bebi agaba sukai suna damunta da surutu.
Watsewa akai daga falon dija ta kama hanyar part ɗinta tana nanata maganar abba na cewa.
"Amina dasu hassana zasuje part ɗin khadijan sauran extra room ɗin dake saman za,aiwa bebi jere zuwa anjima gobe zata koma can da zama domin yafison ya haɗe iyalanshi waje ɗaya daga yau maganar rabuwa ta kare"
Yanzu shikenan zata zauna guri ɗaya da kishiya damma Allah yaso kowa da toilet ɗinshi amman kicin a haɗe falo a haɗe damma dai kowa da falonshi a bedroom ɗinshi spare guda ɗaya, yanzu yakama su suka saka Aliyu a tsakiya kenan domin ɗakin bebi yana gefen na Aliyu na dija na ɗaya gefen shima.
Haka ta koma ɗaki duk jikinta sanyi kalau.
Ammi da kanta ta haɗawa bebi ruwan wanka tanayi ta kwanta saman gado ba jimawa bacci ya kwasheta.
Shima daya dawo daga kai abba asibiti wajan sayyyar kayan ɗaki suka wuce da amina wadda ita taiwa bebi zaɓen kayan ɗaki white colour masu kyau.
Daga nan can tokarawa ya wuce yaywa su goma bayani akan sun bar nan ɗin kayayyakin shi mai amfani ya ɗauko da nata sauran tarkacen kayan abinci kuma ya bawa su goma haka ya baro tokarawa yana kewar gidan domin anan yasan bebi a cikakkar mace anan sukai rayuwa mai tsayuwa arai tabbas wannan gida ya shiga kundun tarihinshi na rayuwar shi da bebi.
lokacin daya dawo gida part ɗinshi ya wuce anan ya tarar dasu amina da ƴan biyun ammi da sauran cousins ɗinshi sunata faman gyara ɗakin da bebi xata zauna sun jera kayan ɗaki yanzu falon suke haɗa mata sosai tsarin wajan ya burgeshi wajan khadija ya wuce wadda ta yada fushinta ta zage ta ringa basa kula ta musamman anan yay sallah yaci abinci ya kwanta saman gadonta wanda shine farko tun aurensu.
Har su amina suka gama basuga gilmawarshi ba haka nan dijan bata fito ba itama  sauka sukai suka fita lokacin magariba tayi falon ammi suka yada zango.
Lokacin bebi ta tashi tana zaune a carpet tana cin taliya.
Ammi tana zaune saman kujera tana jan carbi.

"Washh Allah ammi yunwa mun gama amman munci ubanmu"
Da mamaki ammi ta kallesu.
"A,a kar ku gayan zancen banza tun wajan 2;00pm ku tafi jere amman dija bata baku abinci ba? ina baba Alin yake naga abbanku tun ɗazu yana falon shi?"
Dariya hussaina ta saki.
"Taɓɓijan ammi tunda fa muka bar gidan nan muke aiki dasu hidaya,wallahi anty khadija bata leko ba shima yaya Aliyun daya shigo tun la'asar yace mana sannu ya shige ɗakinta har muka fito basu leƙo muba sun kulle kansu a ɗaki"
Hussaina ta faɗa cike da wauta.
Dum! dum!!dum!!! gaban Bebi yay wani irin faɗuwa wani irin zazzafan kishine..................

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payement domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_

~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

*100*

AUREN BARE

*NA*

#AUTAR MANYA

Gaba ɗaya jitayi taliyar ma ta fita daga ranta zuciyarta na wani irin tashi kamar dukkan sauran dataci zata zubo ma'ana ta amayar da ita rantane ke mata masifar ƙuna kamar ana zuba mata gaushin wuta mai zafi cikin zuciyarta.

Bata taɓa sanin ta damu dashiba tana masa wani irin mahaukacin so mai tattare da kishi mai mugun zafi da zugiba se yau, tabbas tana son mijinta tana kishin duk wata macen dazata raɓar matashi musamman ayau data sheda hakan dayay mata halaccin soyayyarshi daya ɗaga martabarta ya nuna yes ita keda muƙami mai girma a zuciyarta, ta yadda agaban dubban jama'a ya nuna yana sonta ze zauna da ita muddin rai.
Sedai kuma kash! yanzu datake jin furucin kanwarsa setaji ya fita aranta setaji tana jin matsanancin haushinsa tare da jin zafin yadda yay ɗin, duk da hakan ba haramun bane domin waccan ɗinma matarshi ce kuma tana da haƙƙi kamar yadda itama take da haƙƙinshi.
Ƙurawa Tv'n dake jikin bangon falon tai batare datasan mitake kallo ba jitake inda zata sami matsera wallahi baze shigo ya tarar da itaba domin zata wucene wurin mamanta amman sanin matakan tsaron dake cikin gidan masu kama da samudawa yasa wannan ƙudirin nata ya rushe.
Su Amina tashi sukai suna mika suka wuce bedroom ɗinsu suna masu cewa ammi.
"Ammi bara muje muyi sallah muci abinci ƙilafa se gobe dan wallahi bakiji yadda muka gajiba".
Murmushi ammi tai musu cikin kulawa tace.
"Masha Allah, sannunku Allah yay muku albarka Amin seda safen in baku fitoba".
Murmushi sukai atare kuma suka juyo ga Bebi wadda take faman tunani ita ɗaya.
"Anty Bebi se Allah ya kaimu"
Firgit! ta juyo tare da ƙaƙalo murmushi dole sabida yadda maƙoshinta yake a bushe.
"Allah ya tashemu lafiya nagode"
Tafaɗa tana mai mayar da ƙwallarta, barin falon sukai wanda yay saura daga Ammi se ita.
Waya ammi ta ɗauka, tana kiran nusaiba cikin bada umarni take cewa nusaiban tana son next week ta daure ta shigo kano domin shirye-shiryen biki sannan tazo da lefen bebi da suka haɗa.
Sosai suke tattaunawa akan maganar bikin su amina har aka tada sallar magariba.

Bebi ce ta mike ta shige ɗakin ammi, tai alwala a toilet ɗin ammi sannan ta tayar da sallah.
Bayan ta idar azkar ta zauna tayi sannan ta fito falon wanda bata sami ammi cikinsa ba.
Zama tai a ƙasa tare da rafka tagumi ta zubawa ƙofa idanu.
Anan tai sallar isha'i tana idarwa ammi ta fito daga wani lungu, zama ammi tayi cikin kulawa tana kallon Bebi kafin a nutse tace mata.
"Kin gaji da zaman kaɗaici ko auta?"
Murmushin dole tai mata.
"A,a ammi daman zanje wajan Anty zainab matar yaya usman naga boy".
Faɗaɗa far'arta ammi tayi tare da ce mata.
"Zaki gane wajan ne?".
Da sauri ta ɗaga mata kanta.
"Eh! Ammi zan gane in Allah ya yarda".
"To shikenan amman ki maza sabida mijinki nasan yana tafe".
"Insha Allahu" tafaɗa a fili amman ƙasan ranta cewa take.
Tab yayta zuwan mana ni ina ruwana dashi.
Tashi tayi ta gyara hijab ɗinta sannan taiwa ammi sallama kana ta fita daga falon.
Da sauri take nufar part ɗin usman ɗin, kamar daga sama ta hangi tsaiwarsa gaban motar da sukazo ɗazu daga gani kayansu yake ɗiba yana bawa wasu ma'aikatan gidan suna mika masa cikin part ɗinsa.
Cikin azama ta ɗauke kanta tai kamar bata ganshiba damma Allah yasa shiɗin bai gantaba.
Gate ɗin ɓangaren usman ta bude ta shiga cikin falon.
Usman zaune da jinjirin a cinyarshi zee tana gefe tana shan tea sallama tayi tare da fara gaisar da usman tana masa barka.
Sosai yake janta da wasa yana tambayarta ina Aliyun?
Basarwa tai bata basa amsa ba ta koma kusada zee ta zauna wadda take tambayarta yaya fama da jiki?
Sosai usman ya sake yana mata hira tun tana jin kunya harta sake nanfa hira ta ɗauka har zee batare data san lokaci yana jaba.
Ɗaukar yaron tayi tana yaba kyansa babu ta inda yabar usman.
"Lah yaya usman kamarku ɗaya"
Tafaɗa tana dariya.
"Yes aimu ƙarfin jini garemu kema nasan Aliyu zeyo ɗan naki"
Dariya ta saki tana kunshe fuskarta a hijabi.
"Anty zee zan tafi se gobe"
"Tsaya amarya ina zuwa"
Zee tafaɗa tana mai tashi ta shiga ɗakinta mintuna uku ta fito hannunta ɗauke da littafi guda biyu.
"Ga wannan ze rage miki kewa nasan zaki gaji da zaman kaɗaici wannan na farkon girke-girkene tare da gyaran jiki na mata,wannan kuwa littafin karatun hausa ne na soyayya da faɗakarwa na marubuciya Autar manya sunanshi HASKE na tabbata kika karanta Haske sekin nemi KOBA SO, uwarsu ubansu kuma Ɗan majalissa labarin Muhammadu Anwar Sameer( mai girma Mas ) tare da nafisa Fk, tabbas litattafan zasuyi matukar tayaki hira"
Zee ta faɗa tana mai zama akan pillown data tashi.

"Umm kudama mata hirarku kenan na littafi wai dan Allah bakwa gajiya da karatunne?"
Usman ya faɗa yana dariya.
"Haba cwt heart ka manta kwanaki yadda ka dinga cewa Auta kuwa ta fara sabon littafi zaka biya ka sai mana sabida yadda kacemin kaji daɗin RABON WANI wanda nake karanta mana kullum da daddare koka manta?"
Washe baki usman yay yana mai gyara xamanshi.
"Yes my heart ai har yau labarin ya kasa barin zuciyata shine wanda yayansa saddiq ke auranta ko? ashe shi kuma tun tana karama yake sonta amman yayansa yay masa shigar sauri, seda ta haifi tagwaye sannan Allah yaywa sadiq ɗin rasuwa shikuma ALIYUN ya aure tako? kai haryau my love na kasa manta RABON wani na Fatin inna da Aliyu cousin brother ɗinta ko?"
Yafaɗa yana dariya.
Dariyar itama zee tai.
"Ai wallahi auta babu laifi inajin dadin book's ɗinta shiyasa na matsu ta soma sabon datake mana tallenshi"
Da sauri usman ya mike.
"Wanne kenan kina nufin Auta zata kuma yi mana wani book ɗin bayan AUREN BARE?"
Murmushi zee tayi.
"Koma ka zauna oga! ai auta a shekara daman tana yin book ne guda uku to wannan shekarar ma gata tazo mana da DA IZZATA, labarin ɗiyar sarki Memah asma'u masu dukiyar gado tare da sahibinta shahararren ɗan ƙwallon ƙafar nan wato ABDUL-NASEER ALIYU ADAM DAULA! sannan tazo mana da AUREN BARE labarin Aliyu idriss mai atamfa, to yanzuma naji ana cewa, zatayi mana sabo wanda tun kafin na karanta shi naji sunansa ya burgeni bara na nuna maka tallen nashi".

*ZUMA A BAKI...!*🌹
{ Painful love Story }

_Shine sabon littafina da ze soma zuwa da zarar na kammale wannan kedai/kaidai maza ka hanzarta ka biya naka domin tun kafin na soma posting ɗinshi zan soma karɓar kuɗin masu son karantawa kai dagajin sunan kasan akwai rikita rikita wadda bazan ce komai ba amman rubutuna ze bayyana muku *Zuma A Baki* comming soon da izinin Allah ƙofa a buɗe take masu soma payment_

*ƊAN ƊANO*!
_Wannan karon tafiya nai mai mugun nisa har naje na zaƙulo muku ƙayataccen labarin masoya Biyu *Umar Muhammadu Sarkin-Gida* wanda jama'ar unguwa da abokai ke masa laƙani da ( *Cika Daji* ) Eh cika dajin ne mana sabida duk umar ba,a rago to hakance ta kasance ga shalelen inna kuma autanta wanda ya tsunduma a dafkin kogon soyayya da *Aishatul humaira* ɗiyar anty Har soyayyar tasu ta zamewa kowannen su *ZUMA A BAKI* Tabbas tunda nake rubutuna bantaɓa katari da labarin daya kwantamin ya tsayamin kamar ZUMA A BAKI ba! tabbas kodaga jin sunan kasan akwai rikita rikita kuda kawai kubiyoni nasan insha Allah bazan baku kunya ba_

*Hohoho! my fans nace muku painful wallahi da gaske wannan soyayyar mai zafice mai raɗaɗi ce duk wani masoyi yaci katari da wannan labarin nawa seya dara seya koka seya warwasa labarin ze ƙayatar ze tsaya arai ze nishaɗantar ze wa'azantar ze ilimantar kudai kubiyoni kawai*💃💃💃💃🤝

_kai ƙoƙarin ganin kayi payement domin zan soma sakin sane da zarar na kammale wagga_
~N~ *300*#  *ta wannan account numbern 0078174806 starling bank show me your evidance of payment ta wagga numbern 08142105218 love you my ƴan amana my ƴan iya wuyata*

"Ka ganshi sunanshi ZUMA A BAKI dan Allah oga sunan bai burgeka ba kuma nasan labaranta na karanta naji tabbas baxata bamu kunya ba, shiyasa zanyi maza na tura mata 300naira ɗinnan domin naji da sauƙi ma kuɗin littafin domin naga wata frnd ɗita tana cewa ita tunima ta tura mata nata kudin harta tsunduma ta a grp na ZUMA A BAKI wanda zata fara post da zarar ta kammale wannan"
Zee takai maganar tana kallonshi.
"Ah lallai cwt zamusha karatu maza sender mata 300 ta domin ta sakaki afara ZUMA A BAKI damu domin har na matsu naji labarin UMAR dan tunda naji ance CIKA DAJI nasan wannan ba ragon maza bane".
Dariya zee tai tana kallon yadda usman ke zubo zance.
"Ai daman yanzun nan zan mata transper ta hanyar data nuna mana a tallen nata domin a dama dani".
Zee ta faɗa tana kallon Bebi wadda ta mike tare da cewa.
"Kai anty zee gaskiya kin tsumani Allah ya bani waya nima na biya na karanta amman dai bara naje da waɗan nan ɗin domin yau zan karance su insha Allahu".
"Karki damu kanwata se goben kenan?"
Ɗaga mata kai tayi alamun Eh sannan ta fita daga falon tanajin kaso goma na cikin damuwar Aliyu ya fita daga ranta.

Koda taje falon Ammi zaune ta tarar dasu harda matarsa wadda suke zaune kujera guda ammi kuma tana saman ɗayar.
Rannan nashi a haɗe tamau tana sallama yana harararta a fakaice.
"Harkin dawo?"
Ammi ta faɗa mata cikin kulawa.
"Eh ammi na dawo da acan ma zan kwana wallahi sena tuna kuma karkiji shuru shiyasa na dawo ɗin"
Tafaɗi maganar da gayya tare da raɓesu ta wuce ɗakin ammi batare data yiwa kowa magana acikinsu ba...........

*101*

Sosai tabaiwa Aliyu mamakin yadda tai masa wannan shariya, zufar data karyo masa ya saka tissue ya goge duk da azabar sanyin AC'n dake ratsa ilahirin ɗakin.
Murmushi Ammi tayi sabida tagama hasashen komai ta riga data gane cewar kishine ke ɗawainiya da ita, tashi tayi ta bar musu wajan tai shigewarta ɗakin dake kusada nata.
Hamma dija tayi cikin salon kirsa ta dubesa.
"Dear ya kamata ka fito mana da amarya mu wuce naga kamar ma bata lura damu ba".
Tsaki yaɗan ja Afili.
"Rabu da ita goben kawai ta koma ta kwana anan"
Ɗan murmushin jin daɗi ta kumayi.
"Haba dear yakamata itama ta kwana a ɗakinta tunda ammi ta amince kawai tazo muje na haɗa mana dinner"
Kallonta yayi tare da yaba halinta tabbas dija mace ce mai kawaici.
Cikin jin daɗin kalamin nata ya mike da ƙarfin gwiwa ya nufi ɗakin Ammi itako dija zazzafan kishinta ta danne tare da kafe kofar daya shiga da idanunta.
Tura ɗakin yayi ciki-ciki yay mata sallama, tana zaune a gefe gado ta kafawa littafin da zee ta bata idanu sosai takejin daɗin karatun sabida yadda take fahimtar girke-girken ciki dalla-dalla.
Ƙamshin mayen turarensa shiya bata tabbacin zuwansa, amman setai kamar ma batasan Allah yay ruwan sa a gurinba.
"Madam yakamata ki daina fushi dani hakan nan domin ina azabtuwa"
Yafaɗa cikin rashin sabo da rarrashin mace.
Banza tayi dashi batare data tanka mai ba.
Riƙo hannunta yayi wanda bata rike littafin dashiba yana matsa matashi cikin wani irin salo.
Ture hannun nashi tai da ɗayan hannunta tare da juya mai baya.
Gaba ɗaya tafikan hannayenshi ya zube saman gadon bayanta yana shafowa.
Can cikin ƙasan maƙoshinsa kamar ze saka mata kuka! yace.
"Wai dan Allah mai nayi miki duk kinbi kin ɗagamin hankali ki taso mutafi part ɗinmmu"
Yafaɗa yana juyo da fuskarta saitin tasa fuskar yana mai kafeta da idanunshi dasu kai jajur sabida damuwa.
Hawaye ne yasoma zarya a saman fuskarta.
Anan nai kallon kiɗima sabida atake Aliyu yay wata irin dira a gabanta hannayenshi ya saka ya tallafo ta tare da fito da harshen shi yana lashe mata hawayen nata kamar ze tsotse dukkan fuskar gabaki ɗaya.
"Nika rabu dani kuma Allah sena gudu wurin mama tunda muka tawo kake hantara ta tunda kazo kai tafiyarka baka kuma waiwaye naba yanzu kuma kazomin da matarka dan Allah ka rabu dani da abinda nakeji a zuciyata".
Tafaɗa cikin kuka!
Dafe kanshi yayi duk jikinshi yana wani irin rawa gaba ɗaya ya gigice ya daburce.
Rungumota yayi gaba ɗaya zuwa saman faffaɗan kirjinshi hannunshi ya saka yana shafa saman gadon bayanta har zuwa mazaunanta.

Kafin ya lalubo cikin kunnenta ya soma raɗa mata kalamai masu kwantar da hankali.
"Haba sarauniyata haba masoyiyata akanki fa ina kasa bacci yanzu tsakani da Allah ke bazaki min uzuriba nazo ban sami hutu ba ina ta zirga-zirga shine naje ɗakin dija na kwanta yanzu kuma munfi awa anan muna jiranki ni banyi fushin fitar da kikai babu izinina ba seke haba tawan kada na kumaji kince zaki tafi gidan mama batare da izinina ba keda gidan mama semun je ziyara"
yafaɗa mata hakan cikin shaukin soyayyarta.
Jin zuciyarta tayi tai mata sanyi amman duk da hakan bata nuna mashi ba.
Mikewa tsaye yayi tare da zube hannayenshi acikin pocket ɗinshi yana mai zuba mata narkakkun idanunshi.
"Tashi mutafi kinsan dija ta bamu sati guda still wai muci amarcinmu a gida".
Haushine ya kuma kamata jin ya ambaci sunan matarshi amman ganin yadda duk ya lanjare mata kamar maraya yasa ta mike tana tura bakinta gaba.
"Toni kai gaba ganinan"
Tafaɗa cikin ɗaure rai.
Murmushi yayi tare dayin gaba kamar yadda tace ɗin yana jin jina rigimarta.
Seda tagama yangarta sannan ta bishi yana tsaye a falon shi kaɗai bataga matarshi ba kuma bata tambayeshi ba.
"Ina ammi nai mata sallama?"
Ɗan ranƙwabowa yayi gabanta sabida yafita tsayi nesa ba kusaba.
"Ammi tana wajan mijinta tana basa kulawa kema ya kamata kiji dani"
Yafaɗa mata hakan yana kanne mata idanunta guda ɗaya.
Bai bata izinin magana ba ya kama hannunta suka wuce.
Fita sukai daga falon duk yawani shige mata jikinta shi ko kunyar wani ya wuce ya gansu ba yay kasancewar gidan akwai wadatar haske kamar rana.
Gaban gate ɗin part ɗinshi ya karasa shiya buɗe musu gate ɗin suka shiga tana mai karanto addu'a acikin bakinta.
Sosai tsarin falon ƙasan ya burgeta wanda babu komai cikinsa se manyan saitin kujeru na royal masu kalar royal blue.
Step suka haye cikin nutsuwa ya bude kofar glass ɗin dake saman ya kama hannunta suka shiga cikin babban falon daya gama tsaruwa da wasu shegun kujeru masu azababban kyau na fitar hankali.
Ƙafafun Bebi suka nutse cikin lallausan carpet ɗin dake falon ga wani kamshi da sanyin Ac sun gama kashe mata jikinta.
Kallo ɗaya taiwa falon idanunta yasan an narka dukiya acikinsa.
Ƙofar dake gefe wadda ta kasance itace ta room ɗinta ya bude suka shiga falone a farko wanda aka jera fararen kujeru marasa girma se Tv tare da frij, da wani ɗan table a tsakiya kofar bedroom ya bude suka shiga wanda ya kasance katon gaske wanda yaji saitin kayan gado farare babu abinda yafi burgeta ga wajan face tsarin gado mai uban kyau da ɗaukar hankali kofar dake hagu itace ta bathroom ɗinta.
Sakin hannunta yayi yana mai kallonta.
"Well come to the mai atamfa estate mrs Aliyu idriss mai atamfa Allah ya albarkaci rayuwar auren mu"

Yafaɗa yana kashe mata idanu guda ɗaya zama tai a gefen gadon tana lumshe idanunta domin mugun baccin daya kama idanunta.
"Bacci kike ji? ina zuwa"
Yafaɗa yana fita daga ɗakin.
Kansa tsaye ɗakin khadija ya nufa ya sameta zaune gaban madubi ta kifa kanta alamun tunani.
Sallamarshi ita ta dawo da ita daga duniyar tunanin data afka.
Gabanta ya karasa tare da ɗagota ya manna da kirjinshi.
"Dija why kika baro falon ammi bayan kince zamuje mu tawo da Beby?'
Yafaɗa mata murya ƙasa-ƙasa.
"Dole na baro can mana sabida naga kiri kiri kana nuna ban bamci a tsakanina da ita alhalin bata fini da komi ba"
Murmushi yayi lallai mata biyu gobara, yagama da waccan ya dawowa wannan.
"Kiyi hakuri ba nufina kenan ba, amman bakiga tana da lalura ba komai sena bita asannu, yanzu dai kiyi hakuri nazo nai miki sallama ne kamar yadda kikace kin bani sati ɗaya".
Harara ta dalla mai tana jin dama batai ɓarin zancen faɗin hakan ba.
"Hmm shine yasa naga jikinka yana rawa akan ƴar cikinka?"
A wannan karon haɗe ransa yayi tamau tare da zareta ajikinshi.
"Ke khadija kada kikaga ina bin ta taki kinemi gayan magana bazan juri cin zarafi daga garekiba koma miye ai ke kika ce nai satin in kuma baki amince ba zan kwanta a ɗakin ki domin a lissafi yau kece dani"
Murmushin yake tayi.
"A,a Allah ya raka taki gona ni jini nake bana bukatarka wadda kakeso ka ɗirkawa ciki kaje taji da jarabarka ni bazan iya ba".
Tafaɗa tare da banka kofar toilet ta datsota sanin ze iya kai mata duka.
Dafe kanshi yayi cike da ɓacin rai ya nufi ɗakinsa faɗawa saman gado yayi tare da dafe saitin zuciyarshi yana mamakin yadda dija take gasa masa baƙaƙen maganganu a ɗazu, tabbas bada ban bai da tsarin dukan mace ba daseta raina kanta.
Yajima yana saƙawa da kwancewa acikin zuciyarshi kafin ya mike dukkan jikinshi a kasalance ya nufi bathroom wanka yayi tare da saka singlet and boxer ya feshe jikinshi da turare tare da fita daga ɗakin.
Ɗakin bebi ya nufa wadda ya tarar da ita,kwance saman gado da alamun baccinta yayi nisa.
Ɗagata yayi tare da kwantar da ita sosai a saman gadon, hayewa yayi gefenta ya janyota jikinshi ya rungumeta da dubara ya zare mata hijabin jikinta tai saura daga ita se doguwar rigar jikinta,bai son ya tasheta sabida yadda doctor yace ba,a tashin mace mai ciki in tana bacci, sosai ya saka ta ajikinshi ɗumin jikinta ya haɗu dana shi wanda hakan ya haifar masa da wata azababbiyar sha'awarta, hannunshi ya zira cikin rigarta ya fiddo da abinda yake muradi wasa yasoma yi dashi cikin maitarsa  kafin ya ɗora bakinshi akai yana wani irin zuƙa kamar ze cire mata shi.
Cikin baccinta taji yana ruɗa mata jikinta da salonshi, gantsaro mai tai gaba ɗaya sabida tana muradin hakan batare da bata lokaciba ya rabeta da kayan dake jikinta yasoma yi mata wasannin data kusan zautuwa.
Tunda take bata taɓajin kamar na yauba sabida yau yay mata abinda tunda mama ta haifeta bata taɓajin irin daɗinshi ba ya nuna mata yes ita mace ce mai daraja a wurinshi.

Sosai yake mika hannunshi akan dukkan inda yasan ze kunno mata wutarta, kafin ya ɗagata ya dangana bakinshi zuwa ma'aikatarta wanda atake anan ta saka wani irin ihun daya amsa ilahirin ɗakin babu abinda kakeji se nishinsu,sosai ya zage ɗamtse wajan faranta mata seda ya tabbatar daya wanke dukkan fushinta na ɗazu sannan ya sarara mata ɗaukarta yayi cak, kamar ƴar bebi ya kaita can toilet suka tsaftace jikinsu kafin ya naɗota ya dawo da ita ɗaki, kaya suka sauya kana suka koma baccinsu cike da nutsuwa.
Basu farkaba seda asubahi shiya soma tashi yaje yay wanka yay alwala tare da shinfiɗa abin sallah ya soma gabatar da nafila, lokacin daya idar ana kiran sallar assalatu, Alokacin ya tayar da ita inda shikuma ya nufi masallaci bugun duniya yayma dija domin ta bude ƙofa tai sallah yaji shuru ganin yana ɓata lokacinshine yasa ya wuce masallaci abunshi.
Ahanya suka haɗu da abba dasu usman kamar koda yaushe gaisawa sukai ya wuce part ɗin ammi har wurin shida yana wajanta.
Kafin ya mike domin yana son fita office anjima.
Bebi kuwa yana fita tai bayi alwala tayo tare da fitowa ta soma gabatar da sallah.
Bayan ta idar azkar tai tare da mikewa ta faɗa wanka, bayan ta fito kaya ta sauya masu kyau wadda tai adonta cikin doguwar rigar shadda marar nauyi.
Fita tai zuwa falo da karan bani ta nemi kicin.
Sabida yadda umman mufida kullum ke mata lecture akan tsafta kwalliya da kuma iya girki tare da kula da miji,maganar umman mufida batai tasiri a wurinta ba se yau dataga matarsa hankalinta ya kuma tashi taji zata iya bawa mijinta dukkan kulawarta matukar tana son zaman lafiya dashi seta mike ta cire dukkan gandar dake zuciyarta, ada in mama na mata faɗa seta ɗauki abin a wasa amman kam yanzu tagane cewar sefa ta mike tsaye inba hakaba duk son dayake mata ze tashi a banza ne.
Cikin nutsuwa ta kunna gas kana ta ɗora ruwan tea duk da yadda bata son warinshi amman haka ta daure ta haɗa komai na tea ɗin bayan ta gama ta fita main falo ta zauna carbi a hannunta tanaja gaba ɗaya nutsuwa ta sauka ajikinta tamkar ba bebin daba lallai zama da nitsatstse shike sakawa kaima kaji kazama nitsatstsen cikin zuciyarta take raya hakan domin zamanta da Aliyu ta ƙaru da abubuwa kala-kala na cigaban rayuwarta.
Zamanta da kamar mintuna uku taji karar bude kofa bata ɗagoba sabida taji kamar matarsa ce.
Cikin wulakanci dija take kallon yadda aka ɗora mata tukunya akan gas ɗinta kuma tasan ba kowa bace ba face amaryar Aliyu.
cike da gadara ta dawo falon tana wani bude hanci a tsaye ta tsaya akan bebi.
"Ke ƴar matsiyata ubanwa yace uwarki taƙi haɗoki da tukunya setawa zaki ɗauka angaya miki kayana na matsiyatane irin......, Ai bata barta ta karasaba cikin tashin hankalin jin wannan furuci Bebi ta mike ta kwashe dija da mari wanda hakan yay dai dai da shigowar Aliyu,cikin wani irin yanayi Dija ta ɗago a firgice zata zubawa bebi marin domin ta rama.
Cak ya rike hannunta Bebi batai aune ba taji tagwayen marukan Aliyu a fuskarta har guda biyu.
"This is the first and last dazan kuma ganin kin marar min matata duk da ina nuna miki so wallahi baki isa kin takan itaba wannan ƙanwatace ta jini and kuma matata uwar gidana sabida haka banga dalilin dazakiga fuskar marinta ba".
Yafaɗa mata cikin tsananin zafin rai.
Dafe kuncinta tai cikin mamaki take kallonshi.
Murmushin dole ta saki, tana kuma ganin yadda khadija ke mata gwalo batare data bar Aliyun

ya ganiba.
Da sauri Bebi tai ɗakinta jikinta yana matukar rawa.
Har wani jiri take gani.
Hijab ɗinta ta ɗauka ta saka tare da takalmi kana ta fito falon tarar dashi tai tsaye ya goya hannunshi a baya yana kaiwa da komowa A falon alamun komai ya tsaya mai cak!
Matarsa kwa tana saman kujera tana wani hura hanci.
Rabeshi tayi ta wuce sabida babu abinda ze saka ta zauna tanaji gwara ta koma gaban mahaifiyarta taji da abinda ke damunta.
Cikin zafin nama yasha gabanta.
"Kada ki sauka Beby wallahi ranki zeyi mugun ɓaci in kika bude kofar nan"
Yafaɗa cikin tsawar data saka hatta dija seda ta tsorata dashi.
Wawan tsaki taja tare da nufar kofar ko kallonshi batai ba.
"Wallahi sedai komai zakai kayi amman sena fita"
Tafaɗa kanta tsaye.
Hannunta yaja da ƙarfi yay bedroom ɗinshi da ita yabar dija da leken kofa datse kofar yayi tare da tsayawa a gabanta yana faman zuba uban huci, ƙam ta tsaya a gabansa gaba ɗaya hawaye ya gama jiƙa mata fuskarta.
"Kaban guri malam zan fita ai nan ɗin ba ɗakin ubana bane zan tafi na barka da uwargidanka kuma kanwarka ni bare banga amfanin zama dakai ba kamatsa min na fita" tafaɗa tana mai kai mai duka a saman kirjinshi jijjigashi take da iya karfinta amman shiko ko gezau yama zuba mata jajayen idanunshi kawai yana kallonta.
Seda ta jigata dan kanta sannan ta daina ta soma zuba uban huci!
Riko tsintsiyar hannunta yay rikon tsauri gam yana mai zuba mata zafafan idanunshi masu uban girma da kaifi waɗanda sukai wani irin jajur fuskarshi babu alamun sassauci yake kallonta.
"Bilkisuu"!
Yafaɗi sunan adake.
"Dan kinga ina sonki shine zaki nemi takamin matata? ko dija bata rigaki aurena ba ai agirme ta girmeki ni ba lusarin namiji bane bazan yarda da sakarci acikin gidana ba"
Kokarin tureshi take amman yaki bata damar hakan.
"Nida tacemin ƴar matsiyata ta zagi mahaifiyata akan na ɗora maka ruwan shayi a tukunyarta baka ɗauki mataki ba se ita dayake kanwarka ce tonima Allah yasa iyayena basu haifan ni kaɗaiba"
Tafaɗa tana murguɗa mashi bakinta gaba.
Kana ta cigaba dayi mai bayanin duk abinda ya faru cikin kuka!
Jikinshi ne yay wani irin sanyi zubewa yay a wajan ya janyota jikinshi ya rungumeta kafin ya ɗagota.
"In dai marina ze sakaki jin dadi ga fuskata kita mari har kiji zuciyarki tai sanyi pls am very sorry wallahi laifina ne da ban nemi ba'asi ba"
Yafaɗa muryarshi na rawa kamar zeyi mata kuka!
Tureshi tai tana kuka"kaima kasan bazan iya marinka ba, amman nima kabani waya na kira mama ta saimin tukunya sabida adaina min gori" tsananin tausayin maganarta yaji har ransa.
"Ummi nine mamanki nine abbanki nine yayanki nine ƙaninki sabida haka komai kikeso zanyi miki indai kicin ne da kayan kicin duk zan miki kinji kanwata".

Yafaɗa yana mai ɗagota hanyar waje suka nufa a falo suka tarar da dija tana faman kai komo.
"Dija zauna xamuyi magana"
Yafaɗa fuskarshi babu sukuni, zama tayi a gefen kujera inda ya zaunar da bebi a kusa dashi.
"Ummi ki faɗi abinda ya faru a tsakaninku keda dija har kika ɗauki hannu kika mareta?".
Batare da tsoro ko fargaba ba bebi ta mayar mai da duk yadda akai sannan ta ɗora da cewa........
"In kuma karya nake aje a duba kicin akwai tukunyar dana ɗora akan gas ɗin".
"Ke dija mai yasa kikai mata haka? bayan kinsan komai na gidan nan mallakina ne haka zalika mallakin dukkan matar dana aurone? mai yasa kina babba bazaki assasa zaman lafiya agidan nan ba?"
Sosai yake mata faɗa wanda seda ta raina kanta.
Sannan ya juya ga Bebi itama yahau yi mata nata faɗan, akan me zata mari dija mai yasa bazata bari ya dawo ta gaya masa ba? daga karshe ya ɗora da cewa.
"Dukkan ku kunyi kuskure amman ninafi ku yi domin ban tsaya naji ba'asin komi ba na ɗauki hukunci dakaina, sabida haka ina son daga yau kada wadda ta kuma tayar min da husuma ke anjima zan saka a gyara wancan extra room ɗin a maida miki dashi kicin ɗinki and store anan zakina girkin ki dan Allah ina son ku haɗe min kanku bana son tashin hankalinku pls".
Yafaɗa yana mikewa ya nufi dakinshi shirin office yayi ya fito anan ya sami dija itako Bebi tana ɗakinta tana baccin daya zame mata jiki.
Sallama yay mata ya wuce.
Acikin satin kullum Aliyu yana like da bebi kamar cimgam yasa an gyara mata kicin ɗin dayace sabida haka yanzu babu zancen shiga kicin ɗin dija.
Kowa girkinshi yakeyi.
Seda tai sati guda sannan aka raba girki inda in yay kwana biyu a ɗakinta zeje na khadija yay biyu dayake ma shi baya bin ɗaki sedai kowacce ranar girkinta taje gareshi.
Zaman gidan Aliyu ya koma kamar gasa domin ko wacce ta mike sotake taga ta ƙwaci kambun so wurin mijinta musamman a yanzu dayake kokarin nuna adalci a tsakaninsu domin duk son dayakewa Bebi baya yarda ya tauyewa dija hakkinta babu ta inba baya kyautata mata amman ita a nata ɓangaren kullum korafinta yaki yay mata ciki.
Kwanan Bebi goma agidan ta saba da mutanan gidan domin sun ƙulle ita da zee matar usman haka nan sunyi sabo dasu amina domin kusan kullum tana wajan ammi tana koyon girke girke wajanta awajan su amina ko ta iya gayu ta ƙara koyar abubuwa na kwalliya haka nan zee matar usman ita take bata kayan gyara namu na mata da abubuwan rikita oga, Alhaji babba kuwa kusan duk girkin dazatai seta zuba takai masa wanda hakan yasa yaji yana mata wani irin so wanda ko ganinta in bai ba seyayta cewa hajiya matarsa ina ƴar albarkata yau ban ganta ba.
Lokacin bikinsu hassana yayi wanda yazo kusan ɗaya dana ƙannenshi komai na hidimar da uba kewa ƴaƴa Aliyu yay musu amman abin takaici bai gayawa Bebi ko bikin ba har akai bikin aka gama bebi bata saniba.
Haka nan aka faɗa bikin amina dana su hassana wanda a daran da za,ai mothers event ammi ta mikawa Bebi nata lefen da basuyi mata ba, akwatina ne saiti biyu haka ma dija akai mata na faɗar kishiya sosai Bebi tai murna.
Tare da zee suka ɗauke kayan sukai part ɗinta dashi, abin takaici duk hidimar da akai Aliyu ya hanata ko leke wai acewarsa kada ta wahalar mai da bebinsa haka ze sakata a daki yayta

faman abu ɗaya.
Har akai biki aka gama ƴan uwa na nesa dana kusa suka tafi a wannan bikin Bebi taga nusaiba mai kama da Aliyu sak sannan suka gaisa da ya umar sabida ba'ai taro a sunan zee ba yasa basu zoba.
Tunda anty ruma tazo biki taga bebi da ciki take faman zuga khadija akan damme ita tana zaune wata zatazo ta rigata haihuwa agidan, to hakance ta saka dija tai muguwar sauyawa Aliyu komi yace mata setace bazatai ba rashin kirki kala kala take masa abin da yasa yake rabuwa da ita sabida kar ace dan yay aurene ze wulakanta tata.
BAYAN WATA BIYAR
Lokacin cikin Bebi yana wata shida sosai yay wata irin girman dayake bawa kowa tsoro alokacin ta kafa mashi rigimar seya kaita wajan mama, seda ammi tasa baki sannan ta haƙura da maganar, lokacin ma yawanci tafi zaman wajan ammi domin shi baya samun zama sabida ya riga ya bude kamfaninshi na TOKARAWA wanda tuni har an soma aiki acikinshi wanda ya ɗora goma da baban nazir a matsayin manajojinshi,wannan dalilin yasa bai fiye samun zama ba.
Matar goma ma tazo mata kusan ma tana yawan zuwa sabida tana mata kitso da kunshi, cikin wannan lokacin ne Allah yaywa Alhaji babba rasuwa mutuwar data girgiza ilahirin zuri'ar mai atamfa sosai Bebi ta dinga kuka! ranar uku mama tazo gidan tare dasu hassana da iya da sadiya da baba matar malam da wasu mata da bebi bata sansu ba, a part ɗin ammi suka zauna lokacin da bebi taga mama kuka ta saka mata sedai abinda ya bata mamaki sauyin dataga kowa yayi hatta su hassana sunyi wani irin kyau seda ammi ta basu wuri sannan mama take bata labarin duk abubuwan dasuka faru, awajan gaya mata bikinsu hassana ne tahau kukan mai yasa ba,a gaya mata ba dariya mama tai tare da ce mata ai mijinta ne yace kada agaya mata ga sadiya nan ma bikinta sauran wata ɗaya, sosai Bebi take dariya ganin yadda su hassana sukai wata kiba wadda kallo ɗaya xakai musu kasan sunada shigar ciki.
Shahid ta tambaya wanda mama tace mata ai yana ta zuwa aikinshi wajan Aliyu yana kuma zuwa makaranta, sosai bebi take mamakin zurfin cikinsa ko kaɗan bai taba gaya mata dukkan waɗannan lamura ba.
Bata tsinke da lamarin bama seda mama take bata labarin case ɗin khalifa da rasuwar mahaifinshi dakuma belinshi da Aliyu ya karbo sabida tausayin daya basa, yanzu haka wai khalifa ya shiryu daman can babansa ke ɗaure masa gindin rashin mutunci.
Kuma yanxu haka an mayar da auren shi da ladi tunda daman saki biyu yay mata kuma Aliyu ya ɗaukeshi aiki a kamfaninshi haka nan ta zayyane mata zancen shirinsu da dangin mahaifinsu tare da gabatar mata da waɗannan matan inna suwaiba kanwar abbansu dakuma matan su kawu tasi'u sosai bebi ta sake dasu tana kuma gaisarsu domin tasan baka mayar da sharri ga duk wanda yay maka shi kuma nagaba ai yayi gaba na baya se labari.
Mama ta kara mata da nasiha.
"Dan Allah bebi ki rufa mana asiri ki zauna lafiya agidan ki duk da naga sauyi sosai atare dake kuma ki kara yi masa godiya bakiga gidanmu ba yanzufa sekin ɓata in kikazo gaskiya Allah ya sakawa da wannan yaron da alkairinshi amin"
Sosai jikin bebi yakuma yin sanyi takuma jin kaunar Aliyu har ranta wanda yazama HASKE gareta yazama HASKE ga ahalinta bata da abinda zata ce masa sedai fatan addu'a da kuma fatan nasara arayuwarsu.
Har dare su mama suna gidan sosai ta sake dasu hassana sunata hirarsu,anan taji labarin

tafiyar hussaina abuja sabida transper da ya nura ya samu zuwa babbar kotun kasa dake birnin taraiya.
Har kuka bebi tai dataji irin dadin da ƴan uwanta da mahaifiyarta suke ji lallai rayuwa babu tabbas kuma dukkan tsanani yana tare da sauƙi komai nisan jifa dole ƙasa ze sauka ada sun taso a kunci amman da sannu komai ya koma tarihi.
Yanzu mama bata da wata matsala su ihsan ma suna ta makarantar su batare da wata matsala ba.
Da kansa ya zuba su mama a motarshi ya kaisu gida wanda tun a mota suka tsinke da daular da sukaga Bebi acikinta lallai Bebi ta taka ƙasa ta shiga jerin manyan mata, washe garima sega wata tawagar nan daga wajansu kawu tasi'u domin ilahirin zuri'arsu seda sukazo gaisuwa harda khalifa da ladi wanda seda ya saka aka kira mai bebi yayta mata godiya har yana ce mata ba daban Aliyu ba da sun shiga taskun rayuwa sabida bashin bankin da mahaifinshi yaci wanda hatta gidansu seda aka ɗaga aka siyar duk yana gidan yari bai saniba rayuwa taiwa mahaifiyarshi da kannenshi zafi cikin hukuncin Allah da taimakon Aliyu ya sai musu gida yay belinsa harya samu ya ɗaukeshi aiki har zuwa yanzu da komai yake warware musu,yanzu haka suna zaune gida ɗayane shida mahaifiyarshi da kannenshi da ladi matarsa inda shi kuma yake zuwa tokarawa aiki a karkashin kamfanin Aliyun.
Haka nan su kawu tasi'u suka hau neman afuwarta tare dayi mata godiya akan hidimar mijinta garesu abin har kunya ya bata haka dai aka rabu cikin jin dadi da farin ciki.
Har tsayin kwanaki bakwai ana faman karbar gaisuwa acikin gidan wanda ƴan uwan bebi sukai mata kara wajan zuwa kullum kuma da kular abinci abin mamaki kuma arana mutum kusan goma ke zuwa.
Ranar da akai bakwai da yamma shahid shima yazo sabida suna exams bai sami damar zuwa ba sosai bebi tai mamakin yadda shahid ya zama magidanci yay wani irin girma da kyau, a falonta suka zauna suna hira duk farin ciki ya cika Bebi se wajan magariba ya tafi washe garima sega hassana hussaina ihsan da arfa anan suka wuni ihsan an zama ƴan mata se wani iyayi take wai ita likita zata karanta ita tai musu girki.
Ran bebi wasai gata cikin ƴan uwanta nanfa hira ta kaure musu koda Aliyu ya dawo daga office shiya ɗaukesu ya kaisu gida ya haɗasu da shatara ta arzki.
Adaren ranar Bebi taci adonta na bam mamaki daman ranar ita ce dashi soyayya mai tsayawa arai ta nuna masa tana mai kuka akan abinda yaywa danginta daga karshe tace.
"Tabbas kacika masoyi na hakika Allah ya bani ikon faranta ranka"
"Karki damu mai sona komai nai maki ban faɗiba"
Yafaɗa yana haɗe jikinsu wuri guda aranar sunyi soyayya mai narkar da zuciya.
Tsayin kwanaki ana amsar gaisuwar alhaji babba har zuwa sanda komi ya lafa rasuwar ta xama tarihi.
Cikin wannan lokaci cikin bebi ya shiga wata na bakwai.
Alokacin kuma Allah yaywa malam shima rasuwa sakamakon mura dayay fama da ita wannan karon seda Aliyu ya kai bebi gida.
Anan gidan malam akaita amsar gaisuwa ammi tazo abba yazo da sauran ƴan uwanshi.
Ranar bakwai da yamma bebi ta koma gidansu sosai tai mamakin yadda aka ƙere musu gidan nasu abin yay matukar burgeta adaren ranar Aliyu yazo suka wuce gida.
Abin mamaki kaca kaca suka tarar da falon kamar anyi barin kayan falon wucewa ɗaki bebi tayi

Aliyu kuma ya wuce ɗakin dija, tarar da komi yay a watse kanshi tsaye sauka yayi kasa ya wuce part ɗin ummnta anan ya tarar da ita a zaune tana kuka umman ta na bata baki.
Tambayar mai yake damunta yaywa umma, amma ga mamakinsa se umma tahau tijara tana aibatashi sosai ransa ya ɓaci amman seya mike baice mata komiba ya wuce wajan abba anan yake masa bayani cewar ya dawo baiga khadija ba ya bita part ɗinsu ummanta tai masa rashin kirki.
Abbane yasa aka kira abban bauchi tare da umman khadija da ammi koda sukazo abban bauchi ya tambayi khadija shin Aliyu yana mata wani abunne.
Buɗar bakinta tace.
Ba rashin ci bana sha ita dai haihuwa takeso.
Kallonta abba yayi.
"khadija aure da haihuwa da mutuwa lokacine na Allah sabida haka ki kwantar da hankalinki in Allah ya yarda kema zaki haihu"
Amman ga mamakinsu se umman tace.
"Kaga ya idriss nagaji ya sakarmin ƴata kawai ai wadda yake so yaywa ciki amman ita gata har yau ko ɓatan wata"
Kunyace ta kama Aliyu ya sada kansa a ƙasa baice komiba.
"Abba nidai ya sakeni kawai bana bukatar xamana dashi"
"To kai Aliyu kanaji fa"
Cikin kwantar da murya yace.
"Khadija kiyi hakuri har yau aurenmu bai shekaraba kema zaki haihu insha Allahu"
Duk yadda abba yaso su fuskanci komai amman sunki hakan yasa abban bauchi ya fusata.
"wato ke khadija daman ba domin Allah kike son baba Ali ba? in bada wata manufa kike sonshiba tayaya zaki nuna ke haihuwa kike so in sonki domin Allah ne ai bazaki dage sekin haihuba wannan maganar banza ce kai baba ali saketa nace ai ba tare kukazo duniya ba Allah ya gani baka shiga hakkinta ba"
Atake anan Aliyu yay mata saki ɗaya wai kuma seta saka kuka abban bauchi tsaki yay yabar wajan shima Aliyun tashi yay duk baiji dadi ba haka yabar falon.
Koda ya koma bai gayawa bebi ba haka yasa aka gyara falon kamar da sukaci gaba da zamansu seda ta matsa masa da tambaya sannan ya zauna yay mata bayanin komi.
Har ranta bataji dadi ba amman addu'ar alkairi taiwa dijan sannan ta cigaba da harkokinta.
Soyayya mai kyau suke gudanarwa ita dashi lokacin da watan azumi yazo cikinta ya shiga wata na tara gashi zasu tafi umara shida ammi da usman harda mamanta, hakan yasa baba matar malam tazo suka zauna tare, tunda ya tafi kullum addu'arshi akan Allah ya raba bebi da cikin jikinta lafiya take.
Ranar sallah suka dawo da asuba kuma aranar nakuda ta kama bebi wadda bata wani sha wuyaba Allah ya sauketa lafiya a part ɗin ammi.
Ta haifo ɗanta namiji mai kama da Aliyu sak sedai farar fatar bebi daya ɗauko, zokuga farin ciki wajanshi kamar ze mayar da ɗan nan ciki gyarata akai kana aka wuce da ita part ɗinta anan baba tacigaba da kula da ita.
Ranar suna yaro yaci suna Musa sunan babansu bebi sosai akai shagali a wannan rana kamar babu gobe.
Washe garin sunan dija tazo ganin yaron harda ummanta cikin mutunci suka gaisa sun jima

anan kafin sutafi.
Haka baba tacigaba da kula da bebi da sahib,har tsayin kwanaki arba'in ranar kwana na arba'in da biyar bebi ta tafi gida bayan sun aje baba agidanta sun cika ta da kayan abin arziki.
Kwanan bebi biyar a wajan mama ta zaga dangi taje gidan hassana husaina tana abuja taje gidan sadiya taje gidan iya ta zaga ko ina har gidan ladi taje anan ta wunima washe gari a gidan kakan ninta na ƴan kusa ta wuni gidansu kawu tasi'u kenan wanda aka gyara gidan yazama na zamani sabida yanzu haka duk samarin gidan suna aikine a kamfanin Aliyu sosai taga gata dangin mama ma na nan ɗin ta kai musu ziyara sabida daman su tun fil azal basu wulakanta suba kuma suma sun mata godiyar hidimar da mama ke musu domin duk abinda mama ta samu bata taɓa mantawa da danginta ba suma tana musu yadda ya kamata.
Bata dawo gidaba se dare ita da ihsan duk sun gaji basu sami mama agida ba tana wajan kayanta dasuka zo sabida mama mai neman na kanta ce wannan dalilin yasa bata rabu da ƴan buga bugarta ba yanxu haka shinkafa ake kawo mata ƴar hausa take rabawa mata masu abinci da masu awo a wata su haɗa mata kudinta, sannan tana saida kayan yaji agidanta.
Bayan mama ta dawo zagewa tai tasoma gyara bebi ciki da waje na tsayin kwanaki biyu hatta fatar bebi seda ta sauya, tunda yazo ɗaukarta yake ɗaukinta dan haka koda suka koma gida sahib wajan ammi aka barsa ya dauketa se master room.
Sosai ya gigice ya susuce akanta ya shiga rudu wanda harda yi mata kyautar kujerar hajji a wannan rana sabida yajita xam zam kamar bata haihuba.
BAYAN SHEKARU BIYAR.
Abubuwa masu dadi da rashin daɗi sun faru.
Rasuwar abban Aliyu data girgiza kowa rasuwar kawu tasi'u da kawu sani rasuwa baba matar malam.Waɗannan sune abubuwa marasa dadi dasuka faru domin zaman duniya daman akwai dadi ne akwai rashinsa

Abubuwa masu daɗin sune kamar haka.
auren shahid bayan ya kammala karatunshi ya sami aikin gwamnati haihuwar su hassana da kannen Aliyu da akama aure,auren khadija da wani abokin karatun ta ƙarin haihuwar Bebi wadda yanzu haka tana da yara uku idriss( irfan ) musa ( sahib) Aisha ( noor)dakuma saka ranar auren ihsan da arfa kannen bebi waɗanda sukai candy kuma suma Allah ya kawo musu mazajen arziki.
Rayuwa mai kyau ita take wanzuwa a tsakanin Bebi da Aliyu tabbas bebi ta sami sauyin rayuwa azamanta da mijinta xama suke mai cike da faranta wa junansu rai bawata matsala a tsakaninta da ƴan uwan mijinta da mijinta dakuma danginta bare kuma usman uwa uba wanda ya zama haske gareta hatta baban nazir da matarsa da goma da matarsa bebi bata yada suba suna zumuncisu.
Yanzu haka Aliyu ya shirya musu tafiyane zuwa ƙasa mai tsarki ita dashi yara kuma an barsu wajan ammi sabida school damma little Aliyun mama zee yana zuwa wajansu yana wasa da sahib domin tsiransu ba nisa.
Ranar da suka tashi zuwa saudi bebi har kuka tai data ganta cikin jirgi zata ziyarar kabarin annabi s.a.w sabida bata taɓa xuwa ba domin duk alkawarin daya mata ada daga tafiyar tazo se ciki ya bayyana wannan karon ne Allah yasa tana da rabon zuwa ɗin koda suka sauka a madina ɗaki ya kama musu babu wata shagala dake zaunar dasu face bada himma wajan

bautar Allah maɗaukakin sarki sosai bebi ta zage tanawa abbanta addu'a tare da mamanta da suka zama silar shigowarta duniya kuma suka bata kyakykyawar kulawar data saka harta zamo kamar haka tabbas samun mahaifiya kamar mama a wannan zamanin se an tona wannan dalilin yasa bebi ta xage ta dinga musu addu'a tare da ɗaukacin musulmi baki ɗaya.
Basu suka samu nutsuwa ba seda suka gabatar da hajjinsu cikakkiya satinsu biyar a saudi suka wuce london daga nan ya wuce dasu england, anan suka baje hajar soyayyarsu kamar zasu cinye kansu inka gansu kokai waye sekai sha'awarsu domin gaba ɗayansu sunyi wani irin kyau sun murje bebi ta ƙara cika tai kiba tai kyau ta zama babbar mace
Siyayya suka jibgo mai uban yawa sukayo gida cike daso da kaunar junansu ransu tass babu wata matsala a tsakaninsu
*TAMMAT BIHAMDIHI*
Anan na kawo karshen littafin AUREN BARE ladan dana samu cikinshi Allah ka bani kuskuren danai cikinshi Allah ka yafemin.
Akwai dubba darusa acikin wannan litttafi dajan hankali gamu iyaye mata wanda dukkan wanda ya karanta littafin daga farko har karshe ze faɗaku da abinda ke cikinshi.
Fatana makaranta zakuyi amfani da abin daya dace na amfani daga cikin littafin abinda baida amfani kuma ku watsar dashi.
Ina neman yafiyar dukkan wanda naiwa ba dai dai ba acikin wannan tafiya domin ɗan adam ajizine ku yafeni.
Alhamdulillahi nagodewa Allah daya bani ikon kammala shi a ranar asabar 13/11/2021/12:13pm
Allah nagode maka Allah nagode maka.

Semun haɗu a sabon littafina da izinin Allah mai suna .

*ZUMA A BAKI*

Littafin naira.
300 ne ta wannan accnt numbern 0078174806 starling bank shedar biyanki tanan 08142105218, sena jiku masoyana kashin bayan nasarata AUTAR MANYA tana muku sonso.